ELLEN G. WHITE

BABBAN JAYAYYAR

New Covenant Publications: Hausa

Copyright © 2020. New Covenant Publications International.

An kiyaye duk haƙƙoƙi. Ba wani ɓangare na wannan littafin da za a iya sake bugawa ko watsa shi ta kowace hanya ko ta kowace hanya ba tare da takamaiman izini daga marubucin ba, sai dai a cikin taƙaitaccen magana da ke kunshe a cikin labarai masu mahimmanci da sharhi. Da fatan za a mayar da duk tambayoyin da suka dace ga mawallafin.

An kiyaye duk haƙƙoƙi. Ba wani ɓangare na wannan littafin da za a iya sake bugawa ko watsa shi ta kowace hanya ko ta kowace hanya, na lantarki ko na inji, gami da yin kwafin hoto, rikodi, ko ta hanyar adana bayanai da tsarin dawo da bayanai - sai ta mai nazari ko mai bincike wanda zai iya kawo taƙaitaccen bayanin da za a buga. a cikin mujallu, mujallu ko mujallu.

ISBN: 359-2-85933-609-1 ISBN:

359-2-85933-609-1

Kataloji a cikin Bayanan Labarai

Edita da Tsara ta: Sabon Alkawari Publications International Group

Buga a cikin United Kingdom.

Buga Farko 26 Mayu 2020

An buga ta: New Covenant Publications International Ltd.,

Kemp House, 160 City Road, London, EC1V 2NX

Ziyarci gidan yanar gizon: www.newcovenant.co.uk

An bar wannan shafin da gangan babu komai.

New Covenant Publications

International Ltd.

Littattafai na Gyaran; Sabbin Tunani

New Covenant Publications International Ltd.,
Kemp House, 160 City Road, London, EC1V 2NX

Imel: newcovenantpublicationsintl@gmail.com

Godiya

Wannan littafi sadaukarwa ce ga Allah.

Gabatarwa

New Covenant Publications International [Wallafe-wallafen sabon alkawari na duniya] yana haɗa mai karatu tare da shirin allahntaka mai ɗaure sama da ƙasa da ƙarfafa dawwama na dokar ƙauna. Tambarin, Akwatin alkawari yana wakiltar dangantakar dake tsakanin Kristi Yesu da mutanensa da kuma tsakiyar dokar Allah. Kamar yadda aka rubuta, “Amma wannan shi ne alkawarin da zan yi da mutanen Isra'ila bayan waɗancan kwanaki, ni Ubangiji na faɗa. Zan sa dokokina a cikinsu, zan rubuta su a zukatansu, zan zama Allahnsu, su kuma za su zama jama'ata.” (Irmiya 31:31-33; Ibraniyawa 8:8-10). Hakika, sabon alkawari ya nuna cewa za a sami fansa, wanda jayayya ta haihu kuma da jini ya hatimce shi.

Tsawon ƙarnuka da yawa, da yawa sun sha wahala da zalunci, ana ƙididdige su don murkushewa da ɓoye gaskiya. Musamman a zamanin duhu, wannan haske ya kasance yana adawa da shi sosai kuma ya rufe shi ta hanyar al'adun mutane da jahilcin duniya. Jama'ar sun ƙazantar da duniya da suka keta dokokin Allah, suka ta da alkawarin da ya yi don ya dawwama...

Barnar cin hanci da rashawa da karuwar munanan ayyuka sun haifar da rashin mutuntaka na diabolism. An sadaukar da rayuka da yawa, domin sun ƙi ba da ’yancin lamiri. Duk da haka, ilimin da ya ɓace ya sake farfadowa, musamman a lokacin gyarawa.

Zamanin gyarawa na karni na 16 ya kunna lokacin gaskiya, canji na asali da tashin hankali, kamar yadda aka nuna a cikin Counter-Reformation. To sai dai a cikin wannan rubutu, masu karatu sun gano muhimmancin wannan juyi guda daya ta fuskar ‘yan canji da sauran jajirtattun majagaba. Daga idanunsu, mutum zai iya fahimtar adawa mai tsanani, dalilan da ke haifar da sabani mai ban mamaki da shiga tsakani na Allah.

Taken mu: “Littattafai na Gyaran; Sabbin Tunani,” Yana ƙarfafa nau'in wallafe wallafen daban-daban, wanda aka haɗa a cikin lokaci mai mahimmanci da tasirinsa. Har ila yau, yana sake haifar da gaggawar sake fasalin mutum, sake haifuwa da canji. Kamar yadda gidan buga littattafai na Gutenberg, baya ga hukumar fassara, ke yaɗa ƙa'idodin bangaskiyar da aka gyara, kimanin shekaru 500 da suka wuce, dandamali na kan layi da kafofin watsa labarun za su yi wa'azi --- [ga mazaunan duniya, wato, ga kowace al'umma, da kabila, da harshe, da jama'a]…

Tebur Abun Ciki

Babi na 1— Tarihin Duniya Annabta 6
Babi na 2— Baftisma na Wuta da Jini 19
Babi na 3— Zamanin Duhu 25
Babi na 4— Mutane na musamman 32
Babi na 5— Tauraruwar Safe 43
Babi na 6— Sojojin Gaskiya 54
Babi na 7— Babban Rabuwa 69
Babi na 8— A Gaban Kotun Koli 84
Babi na 9—Dan Canjin Switzerland 100
Babi na 10—Ci Gaban Canji a Jamus 108
Babi na 11—Yardar ‘Ya’yan Sarkin 116
Babi na 12—Canjin Faransa 125
Babi na 13—Netherlands da Scandinavia 141
Babi na 14— ‘Yan Canjin Ingila na Baya. 146
Babi na 15—Littafi da Juyin-Danwaken Faransa 158
Babi na 16—Ubani Matafiya 172
Babi na 17—Alkawuran Dawowan Kristi 179
Babi na 18—Dan Canji America 190
Babi na 19—Haske Ta wurin Duhu 205
Babi na 20—Babban Falkaswa na Ibada 212
Babi na 21—Gargadin da Aka Ki 224
Babi na 22—Cikawar Annabci 234
Babi na 23—Menene Haikalin? 245
Babi na 24—Cikin Wuri Mafi-Tsarki 254
Babi na 25—Dokar Allah Ba Ta Sakewa 260
Babi na 26—Aikin Canji 271
Babi na 27—Falkaswa na Zamani 277
Babi na 28—Fuskantar Rahoton Rayuwa 289

Babi na 29—Mafarin Mugunta 297
Babi na 30—ƙiyayya ta Jahannama 305
Babi na 31—Miyagun Ruhohi..... 309
Babi na 32—Tarkokin Shaitan 313
Babi na 33—Babban Rudi na Farko..... 321
Babi na 34—Ko Mattatu Za Su Iya Magana da Mu?..... 333
Babi na 35—Barazana ga Yancin Lamiri..... 340
Babi na 36—Yakin da Ke Zuwa. 352
Babi na 37—Littafi, Mai-tsaro. 359
Babi na 38—Gargadi na Karshe..... 365
Babi na 39—Kwanakin Wahala 371
Babi na 40—An Tsirar da Mutanen Allah 385
Babi na 41—Mayar da Duniya Kango 396
Babi na 42—Karshen Jayayyar 402

Babi na I— Tarihin Duniya Annabta

“Yace, Da ma kin sani a chikin wannan rana, har ke ma, abin da ya tabbata ga salama! amma yanzu a boye yake a idanun ki. Gama kwanaki za su abko maki, inda makiyan ki za su gina maki ganuwa, su sa ki a tsaka, su tsare ki daga kowane sasa, su fyade ki a kasa, da yayan ki a chikin ki, ba za su bar ko dutse daya a bisa wani a chikin ki ba; da shi ke ba ki lura da kwanakin ziyartanki ba.” Luka 19:4 -44.

Daga kan dutsen Zaitun, Yesu ya dubi Urshalima. Bai ga komi ba sai abin ban sha’awa da kuma salama. Lokacin Paska ne, kuma yayan Yukubu daga dukan kasashe sun tattaru a wannan wuri don wannan babban biki na al’umma baki daya. Cikin lambuna da gonakin anab, da kuma filaye masu ni’ima cike da bukokin maniyyata, akwai tuddai da kyawawan gidajen sarauta, da kuma manyan ganuwoyin cibiyar Israila. Sai ka ce diyar Sihiyona, cikin alfarma tana cewa ne, “Ni gimbiya ce, kuma ba zan ga bakin ciki ba;” da ban-sha’awan nan nata, tana kuma gani kamar Allah yana gayon bayan ta, kamar yadda a zamanun baya mawakan sarki suka raira cewa, “Mai-kyaun tsaye ne, abin murna ga duniya duka, Dutse Sihiyona kenan. “Birnin Madaukakin Sarki.” Zabura 48:2.

A fili kuma ga kyawawan gineginen haikalin. Hasken rana ya haskaka dukan gine ginen nan, da kofar zinariyan da hasumiyar sa da kuma benen sa. A lokacin, haikalin nan abin fahariya ne ga al’ummar Yahudawa. Kowane dan kasa in ya bude shi yakan cika da murna da sha’awa! Amma wadansu ababa dabam ne suka cika tunanin Yesu a wannan lokaci. “Sa’anda ya kusa, ya hangi birni, ya yi kuka a kanta.” Luka 19:41. Cikin farin cikin da ya mamaye ko ina sabo da shigowar Sa Urshalima, yayin da ake nuna ganyen dabino, ana raira hosanna, dubbai kuma suna shelar cewa Yesu ne sarki, Mai-fansar duniya ya cika da bakincikin na ban mamaki, faraf daya. Shi Dan Allah, Dan Akawali na Israila, wanda ikon sa ya yi nasara bisa mutuwa, ya kuwa ta da matattu daga kabarbarun su, sai ga Shi ya cika da hawaye na azabar bakinciki sosai.

Hawayen Sa ba don kan Sa ba ne ko da shike ya sani sarai abin da zai faru da shi. A gaban sa yana ganin Gathsamani, inda za’a azabtar da Shi. Ga kuma kofar tumaki ta inda aka yi daruruwan shekaru ana shigowa da tumakin hadaya, ta inda kuma za a bi da Shi “kamar dan rago da aka kai wurin yanka” Ishaya 53:7. Kusa da wurin kuma akwai kalfari wuirn giciyewan. Dole mumunan duhu ya rufe hanyan da Yesu zai bi zuwa inda Ya mika ran Sa hadaya sabo da zunubi. Duk da haka ba tunanin wadannan ababa ne ya sa Shi bakinciki a wannan lokaci da ake murna ba. Ya yi kuka sabo da dubban mutanen Urshalima ne. Domin makanta da rashin tuban wadanda ya zo domin ya albarkace su, ya kuma cece su ne.

Tarihin shekaru fiye da dubu na alherin Allah da kulawan sa da nuna ma zababbun mutanen sa ya bayana ga idanun Yesu. Ya ga Dutsen Moriah inda aka daure dan alkawali mai-biyaya a a kan bagadin hadaya, alamar hadayar Dan Allah. Farawa 22:9. Can aka

tabbatar ma uban masu bangaskiya alkawalin nan mai albarka, alkawalin zuwan Masiya. Farawa 22:16-18. Can ne kuma wutar hadaya da ke hawa zuwa sama daga wurin masussukar Ornan ta kawar da takobin malakan nan mai-hallakaswa. Labarbaru 1, 21 — alamar hadaya da tsakancin Mai-Ceto a madadin mutane masu laifi. Allah ya girmama Urushalima bisa dukan duniya. Ubangiji "ya zabi Sihiyona", "ya yi marmarinta domin mazamninsa." Zabura 132:13.

Can fa tsarkakan annabawa suka rika furta sakonin su na kashedi. Can kuma priestoci suka rika mika hadayu, addu'o'in masu sujada kuma suka rika hawa zuwa gaban Allah. Can aka rika mika jinin yankakkun raguna, alamar Dan rago na Allah. Can ne Yahweh ya bayana kasancewar Sa a cikin girgijen daraja bisa dakalin jin kai. Can ne kuma tsanin nan wanda kansa ya kai har sama, ya kafu a kasa (Farawa 28:12; Yohanna 1:51) — tsanin nan da malaikun Allah suke hawa suna kuma sauka a kan sa, wanda ya bude ma duniya hanyar wuri mafi-sarki. Da al'ummar Israila ta yi ma Allah aminci, da Urushalima ta dawama har abada, zababbiya ta Allah. Irmiya 17:21-25. Amma tarihin kaunatattun nan, na ja da baya ne da tawaye. Sun ki alherin Allah, suka kuma wofinta alherai da zarafi da aka ba su.

Ko da shike Israila "suka yi ma manzanin Allah ba'a, suka rena maganatasa, suka yi ma annabawansa zunda" (Labarbaru II 36:16), duk da haka ya bayana kan Sa gare su, "Ubangiji, Allah ne chike da juyayi, mai-alheri kuma, mai-jinkirin fushi, mai-yalwar jin kai da gaskiya". (Fitowa 34:6); duk da yawan bijirewar su, cikin jin kan Sa ya ci gaba da rokon su. Cikie da kaunar da ta fi ta uba zuwa ga dan sa, Allah " ya aike gare su ta wurin manzaninsa, yana tashi da wuri yana aikassu domin yana jin juyayin mutanensa, da mazamninsa kuma" Labarbaru II, 36:15. Sa'anda lallashi da tsautawa da Allah ya aika masu da kyauta mafi-kyau da sama ke da shi, watau ya zubo masu dukan sama cikin Kyautan nan.

An aiko Dan Allah kan Sa domin shi roki kangararen birnin nan. Kristi ne ya fito da Israila, inabi mai-kyau da Masar. Zab. 8:8. Da hannun Sa ya kori kafirai daga cikin Israilan. Ya dasa ta a kan tudu mai-kyau, ya kuma kange ta. Aka aiki bayin Sa su ciyar da ita. Ya nome ta "a chikin wani tudu mai-albarka kwarai." Mai lura masa da ita ya rigaya ya kewaye ta da shimge. An rigaya an aiki ma'aikata suka tsintsinche duwatsunta. Ya ce: "Me ya rage a yi ma ganata da ban yi a chikinta ba?" Ishaya 5:1-4. Ko da shike, sa'anda ya zata za ta haifi inabi, sai ta fito da inabi mara anfani, duk da haka, ya zo wurin gonar inabin nasa da begen samun 'ya'ya, ko za a cece ta daga hallaka. Ya yi tono kewaye da inabin; ya gyara ressan ta. Bai gaji da kokarinsa na ceton inabin sa da ya dasa ba.

Ubangijin haske da daraja ya yi shekara uku yana ma'amala da mutanene Sa. Ya rika ayukan nagarta, yana warkar da dukan masu-aljannu, yana ta'anzantar da masu-bacin zuciya, yana kuma kubutar da dauraru, yana mayar da gani ga makafi, yana sa guragu su yi tafiya, kurame kuma su ji. Ya ta da matattu, yana kuma shelar bishara ga matalauta.

Ayukan 10:38; Luka 4:18, Matta 11:5. Ya kira dukan mutane cewa: “ Ku zo gare ni, dukanku da ku ke wahala, masu-nauyin kaya, ni kuwa in ba ku hutawa” Matta 11:28

Ko da shike an rama masa adalcin Sa da mugunta, kaunar Sa kuma da kiyaya (Zabura 109:5), ya ci gaba da aikin Sa na jin kai. Bai taba koran mai-neman taimako ba. Ba shi da gidan kan Sa, ga reni, ga talauci, amma ya rika biyan bukatun mutane, yana rage wahalolin su, yana kuma rokon su su karbi kyautar rai. Cikin kauna ya rika maimaita ayukan Sa na jinkai da kangararu suka ki karba. Amma Israila ta ki babban abokin ta, wanda Shi ne kadai Mai-taimakon ta. Ta ki jin rokon Sa, ta ki karban kaunar sa, ta kuma ki jin shawarar sa da kashedin Sa.

Sa’ar bege da gafara ta kusan wucewa, kokon fushin Allah ya kusan cika. Hatsarin da ya rika taruwa a zamanin ridda da tawaye yana gaf da fashewa kan masu laifi; ga shi kuma sun rigaya sun ki wanda Shi kadai ne zai iya ceton su, suka wulakanta Shi, kuma ba da jimawa ba ma za a giciye Shi. Wannan giciyewan Kristi ne kuwa zai kawo karshen mastayin Israila na zababbiyar al’ummar da Allah Ya yi mata albarka. Mutuwar mutum daya ma kawai abin bakinciki ne, amma yayin da Kristi Ya dubi Urshalima, Ya ga hallakar birni guda ne, al’umma guda wadda da ita ce zababbiya ta Allah.

Annabawa sun rika kuka sabo da riddar Israila da munanan wahalolin da suka biyo baya. Irmiya ya so da idanun sa mabulbulolin hawaye ne, da ya yi ta kuka dare da rana, domin mutanen sa da aka karkashe, da garken Ubangiji kuma da aka tafi da su kamammu. Irmiya 9:1; 13:17. Yesu fa Ya fi dukan su bakinciki, da shike yana hangan zamanai can gaba. Ya hangi malaika mai-hallakan nan da takobin da zai hallaka birnin da Yahweh Ya dade yana kasancewa ciki. Daga gefen Dutsen Zaitun, daidai wurin da daga baya Titus da dakarun sa suka kama, Yesu ya hangi wurare masu tsarki, da hawaye a idanunsa kuwa, ya ga ganuwan da magabta za su kewaye. Ya “Ji surutun mayaka suna shirin yaki. Ya ji muryoyin uwaye da yara suna kukan neman abinci a cikin birnin da magabta suka kewaye. Ya hangi gidan nan mai-tsarki, da gidajenta na sarauta suna konewa, suka kuma zama kango kawai.

Sa’anda ya dubi sararaki nan gaba, ya hangi mutanen alkawali a warwatse cikin kowace kasa. Cikin horon da zai abko ma ‘ya’yanta, Ya hangi kashin farko na azaban da za ta sha daga kokon fushin, lokacin shari’a ta karshe. Sai Ya bayana tausayin Sa da kaunar Sa cewa: “Ya Urshalima, Urshalima, wadda ki ke kisan annabawa, kina jejjefe wadanda an aiko gare ki! So nawa ina so in tattara ‘ya’yanki, kamar yadda kaza takan tattara yan tsakinta kalkashin fikafikanta, amma, baku yarda ba!” da dai ke zababbiyar al’umman nan kin san lokacin wahalarki, da ababan da suka shafi salamar ki! Na dakatar da malaikan adalchi, na gayyace ki zuwa ga tuba, amma a banza. Ba barori da wakilai da annabawa ne kadai kika ki ba, amma Mai-tsarki na Israila, Mai-fansarki ne kika ki. Idan an hallaka ki kuwa laifin ki ne. amma ba ku yarda ku zo wurin na ba, domin ku sami rai.” Matta 23:37; Yohanna 5:40

A kan Urshalima Kristi ya ga alamar duniya kangarariya cikin rashin tawaye da rashin gaskatawa; da kuma hanzari zuwa ga saduwa da horon Allah. Kaito da wahalolin fadadiyar al'umman nan ne suka tilasta Shi furta wannan kuka mai-zafi. Ya ga zunubi a bayane cikin wahala da hawaye da jinin mutane; zuciyar Sa ta motsu da tausayi. Ya yi marmarin dauke masu wannan azabar. Amma ko hannun Sa ma ba zai kawar da azabar dan Adam ba. Kalilan ne masu bidar taimakon Sa. A shirye yake Ya mutu ma domin kawo masu ceto, amma kalilan ne masu zuwa wurin Sa domin su sami rai.

Sai ga Sarkin sama yana hawaye! Dan Allah Madaukaki Ya cika da bakinciki! Dukan sama ta cika da mamaki. Wannan abu yana bayana mana matukar munin zunibi; yana nuna yadda yake da wahala ainun, har ga Mai-cikaken iko ma, Ya ceci mai-laifi daga sakamakon ketare dokar Allah. Yesu Ya hangi cewa a zamanin karshe, duniya za ta shiga irin rudun nan da ya jawo hallakawar Urshalima. Babban zunubin Yahudawa shi ne kin Kristi da suka yi; kin dokar Allah wadda ita ce tushen gwamnatin Sa a sama da duniya, shi ne zai zama babban zunubin Kirista. Za a wofinta dokokin Allah. Miliyoyin masu zunubi da bautan Shaitan da ke fuskantar mutuwa ta biyu za su ki jin kalmomin gaskiya na zamanin su. Mumunar makanta ke nan.

Kwana biyu kafin idin Paska, bayan Kristi Ya yi fitar Sa ta karshe daga haikalin, bayan Ya tsauta ma riyar shugabanin Yahudawa, Ya sake komawa Dutsen Zaitun tare da almajiran Sa, ya kuma zauna da su a gefen dutsen da ke fuskantar birnin. Sai Ya sake duban ganuwar birnin, da hasumiyoyin sa, da manyan gine ginen sa. Ya sake ganin haikalin, gwanin kyau, abin ban sha'awa.

Shekaru dubu kafin wannan lokacin, mai-zabura ya bayana alherin da Allah Ya yi ma Israila inda Ya mai da haikalin ta mazamnin Sa. Ya ce, "A chikin Salem mazamninsa yake, wurin zamansa kuma chikin Sihiyona." Ya zabi kabilar Yahuda Dutsen Sihiyona wanda yake kamna. Ya gina tsatsarkan wurinsa kamar tsawawa." Zabura 76:2; 78:68,69. An gina haikali na fari a zamanin da Israila ta fi ci gaba ne. Sarki Dawuda ya tara dukiya a yalwace don wannan ginin, tsare-tsaren ginin kuma Allah ne ya bayar. Labarbaru I, 28:12,19. Solomon, mafi-hikima cikin sarakunan Israila, shi ne ya yi ginin. Duk duniya ba a taba ganin wani gini kamar haikalin nan ba. Duk da haka Ubangiji ya sanar tawurin anabi Haggai game da haikali na biyu din, cewa: "Daukaka ta baya ta wannan gida za ta fi ta farin." "Zan raurawadda dukan dangogi; kuma muradin dukan dangogi za ya zo; zan chika wannan gida da daukaka, in ji Ubangiji mai-runduna." Haggai 2:9,7.

Bayan da Nebuchsadnezzar ya rushe haikalin, mutanen da suka dawo kangon kasarsu daga bauta sun sake gina shi, shekara dari biyar kafin haifuwar Kristi. Cikin su akwai tsofofi da suka ga darajar haikalin Solomon na da, suka kuma yi kuka sa'anda aka kafa tushen sabon ginin, cewa ba zai yi kyau kaman na farin ba. Annabin ya bayana yadda suka ji inda ya ce: "Wa ya rage daga chikinku wanda ya ga gidan nan a chikin daraja ta da? Yaya

kuke ganinsa yanzu kuma? A idanunku ba ya zama kamar babu ba?" Haggai 2:3, Ezra 3:12. Sa'an nan ne aka yi alkawalin cewa darajar sabon haikalin nan za ta fi ta farkon.

Amma haikali na biyu din bai kai na farkon kyau ba; kuma ba a tsarkake shi tawurin alamun kasancewar Allah a cikin kaman na farkon ba. Ba a nuna wani ikon Allah a bukin budewarsa ba. Ba'a ga girgijen daraja ya cika sabon haikalin ba. Wuta bai rika saukowa daga sama yana kona hadaya da ka bisa bagadinsa ba. Shekina bai sake kasancewa tsakanin cherubim na wuri mafi-tsarkin ba, sanduki da kujerar jin kai da tebur na shaida basu kasance cikinsa ba. Murya bai rika saukowa daga sama yana shaida ma priest nufin Allah ba.

Yahudawa sun kwashe daruruwan shekaru suna kokarin nunata yadda aka cika alkawalin da Allah Ya yi tawurin Haggai, a banza kuwa; amma girman kai da rashin bangaskiya sun rufe tunanin su daga ainihin ma'anar kalmomi annabin. Ba a girmama haikali na biyu din da girgijen darajar Allah ba, sai dai da zahirin kasancewar wanda cikin Sa akwai cikar Allahntaka cikin jiki — wanda Shi kansa Allah ne cikin jiki. "Marmarin dukan al'ummai" ne ya zo haikalinsa sa'anda Mutumin nan na Nazareth ya rika koyarwa da warkarwa a wuri mai-tsarkin. Ta wurin kasancewar Kristi ne kadai haikali na biyu din ya fi na farkon daraja. Amma Israila ta ki Kyautan nan na sama. Sa'anda Mai-koyarwan nan ya fita kofar zinariya ta haikalin, daraja ta rabu da haikalin har abada. Maganar Mai-ceto ta cika cewa: Ga shi, an bar maku gidan ku kango." Matta 23:38.

Almajiran sun cika da mamakin annabcin Kristi cewa za a rushe haikalin, suka so su kara fahintar maganarsa. An yi sama da shekara arba'in ana anfani da dukiya da kwarewa na fasahar gine gine domin a kara ma haikalin kyau. Sarki Hiridus ya jibga arzikin Rum da wadatar Yahudawa a wurin, har sarkin dukan duniya ma ya arzunta haikalin da kyauta iri iri. Aka yi anfani da manyan duwatsu masu daraja a ginin, har ma almajiran suka jawo hankalin Yesu akan su cewa: "Ka duba, wadanne irin duwatsu kenan, wadanne irin ginegine kuma kenan!" Markus 13:1.

Yesu ya amsa wannan da cewa: "Hakika, ina che maku, Ba za a rage wani dutse bisa wani ba, da baza a rushe ba." Matta 24:2 Almajiran sun danganta rushewar Urshalima da zuwan Kristi cikin daraja ta mutuntaka domin Ya karbi kursiyin mulkin duniya, ya kuma hori Yahudawa, ya kuma kubutar da al'ummar daga kangin bautar Romawa. Ubangiji ya rigaya ya fada masu cewa zai sake zuwa. Sabo da haka sa'anda ya ambaci hukunci da horo a kan Urushalima, tunaninsu ya je wurin wannan zuwan ne; kuma sa'anda suka taru kewaye da Mai-ceto a kan Dutsen Zaitun, suka tambaye shi: "Yaushe wadannan abu za su zama? Mi ne kuma alamar zuwanka da cikar zamani?' Matta 24:3.

Cikin jinkai aka boye ma almajiran abin da zai faru nan gaba. A lokacin, da sun gane abu biyu din nan - azaba da mutuwar Mai-fansar, da kuma rushewar birnin da haikalin - da bakinciki ya fi karfinsu. Kristi ya bayana masu jerin muhimman ababa da za su faru kafin

karshen lokaci. A lokacin ba a gane maganar sa gaba daya ba; amma za a bayana ma'anar sa yayin da mutanen sa za su bukaci umurnin da ke cikin maganan ne. Annabcin da Ya yi yana da ma'ana kashi biyu ne: yayin da ya nuna hallakawar Urshalima, ya kuma bayana ababan ban tsoro da za su faru a rana ta karshe.

Yesu ya fada ma almajiran matsalolin da za su abku ma Israila mai-ridda, musamman ma horon nan sakamakon kin Masiya da kuma giciyewarsa. Alamu za su rigayi horon. Sa'ar da ake tsoro za ta zo nan da nan, da sauri kuma. Mai-ceton kuma ya gargadi Masu bin Sa: "Sa'anda kun ga kyamar lalata, wadda aka ambace ta ta bakin annabi Daniyelu, tana tsaye a cikin tsatsarkan wuri (bari mai-karantawa shi fahimta), sa'annan wadanda ke chikin Yahudiya, su gudu zuwa duwatsu." Matta 24:15,16; Luka 21:20,21. Sa'anda za a kafa gumakan Romawa a wuri mai-tsarki wanda ya zarce ganuwar birnin, to a wannan lokacin ya kamata masu bin Kristi su gudu. Idan aka ga wannan alamar, duk mai-neman tsira sai shi hanzarta. Dole cikin hanzari a yi biyayya ga wannan kashedi ko ina a kasar Yahudiya da Urshalima kanta. Wanda ya yi sa'a yana kan bene, kada ya sauka zuwa cikin gida, ko don ceton wani abin sa mafi-tamani. Wadandan ke aiki a gonaki ko lambu ba za su dawo don daukan rigan da suka tube kafin su fara aikin gonan ba. Kada wani ya yi jinkiri ko kadan, domin kada a hada da su cikin halakar.

A zamanin mulkin Hiridus, an yi ma Urshalima adon gaske aka kuma gina mata manyan gidaje da ganuwa da mafaka da suka kara mata tsaro, wanda ya yi annabci cikin jama'a cewa za a hallaka ta, za a mai da shi mahaukaci yadda aka yi ma Nuhu a zamaninsa. Amma Kristi Ya rigaya Ya ce: "Sama da kasa za su shude, amma zantattuka na ba za su shude ba." Matta 24:35. Sabo da zunuban Urshalima, an kadara ma Urshalima fushi sosai. Urshalima da taurin kanta sun sa hallakawar ta ya zama dole.

Ubangiji, ta bakin annabi Mikah ya ce: "Ku ji wannan, ina rokonku, ku shugabannai na gidan Yakub, ku mahukunta na gidan Israila, ku da kuke kin shari'a kuna bata dukan gaskiya. Suna gina Sihiyona da jini, Urshalima kuma da sabo. Manyanta suna shari'a domin toshi, priest nata suna koyaswa domin ijara, annabawanta kuma suna duba domin kurdi; duk da wannan sai su jingina ga Ubangiji, su che, ubangiji ba shi chikinmu ba? Babu chiwuta da za ta same mu" Mikah 3:9-11

Kalmomin nan sun bayana halayen mazamnan Urshalima daidai. Yayin da suke cewa wai suna kiyaye dokokin Allah daidai, suna ketare dukan kaidodin dokokin. Sun ki jinin Kristi domin tsabtarsa da tsarkinsa sun bayana zunubansu. Suka kuma zarge shi da jawo dukan matsalolin da suka fuskanta sabo da zunabansu. Ko da shike sun san ba shi da zunubi, sun zartas da cewa dole Shi Ya mutu domin al'ummarsu ta sami zaman lafiya. Suka ce: "Idan mun bar Shi haka kurum, dukan mutane za su ba da gaskiya gare shi, Romawa kuma za su zo su amshi wurinmu duk da alummarmu." Yohanna 11:48. Wai idan aka kashe Kristi, su za su sake zama al'umma kakarfa mai-hadin kai. Sai suka goyi bayan

maganar babban priest nasu cewa zaifi kyau mutum daya ya mutu maimakon dukan al'umma ta hallaka.

Ta haka ne shugabannin Yahudawa suka gina "Sihiyona da jini, Urshalima kuma da sabo." Mikah 3:10. Amma kuma yayinda suka kashe Mai-cetonsu domin ya tsauta zunabansu, sun mai da kansu kamnatattu na Allah, suka zata kuma cewa Ubangiji zai kubutar da su daga magabtansu. Inji annabin, "Domin wannan, sabada aikinku, za a hude Sihiyona kamar gona, Urshalima kuma za ta zama tuddai, dutsen gidan Ubangiji kuma za ya zama kamar tuddan kurmi." Mikah 3:12. Kusan shekara arba'in bayan Kristi da kansa Ya yi annabcin hallakawar Urshalima, Ubangiji Ya jinkirta hallaka birnin da al'ummar. Jinkirin-fishin Allah zuwa ga masu kin bishararsa, masu kisan Dan sa kuma, abin al'ajibi ne. Misalin itace mara yayan nan ya bayana yadda Allah Ya yi da al'ummar Yahudawa ne.

An umurta cewa: "ka sare shi; don mi yake tsare kasa banza." (Luka 13:7) amma alherin Allah ya kyale shi har tsawon lokaci kadan. Cikin Yauhudawan akwai da yawa da basu san halin Kristi da aikin Sa ba tukuna. Yaran kuma basu sami zarafi ko hasken da iyayensu suka ki ba. Ta wurin wa'azin manzanin da abokansu, Allah zai ba su haske; za a yarda masu su ga yadda aka cika annabci, ba ta wurin haihuwar Kristi da rayuwarsa kadai ba, har ma tawurin mutuwarsa da tashinsa. Ba a kama yaran da zunuban iyayensu ba; amma sa'anda yaran suka ki karin hasken da aka ba su, bayan sun san hasken da aka ba iyayensu, sai suka zama masu tarayya cikin zunuban iyayensu, suka kuma cika ma'aunin zunuban su.

Jinkirin-fushin Allah zuwa Urushalima ya tabbatar da Yahudawa cikin rashin tubansu ne kawai. Cikin kiyayya da muguntar su ga almajiran Yesu, sun ki tayin karshe na jin kai ne. sai Allah ya janye kariyarsa gare su, ya kyale Shaitan da malaikunsa, sai al'ummar ta koma kalkashin mulkin shugaban da ta zaba. 'Ya'yanta sun ki alherin Kristi, wanda da zai ba su ikon magance miyagun halayyansu, sai Shaitan ya ingiza munanan halayyen nasu; suka dena yin tunani, suna bin ta zuciya da kuma fushi mara-ma'ana. A cikin iyali da cikin al'umma, cikin manya da kanana, aka iske zato da kiyashi da kiyayya da rashin jituwa da tawaye da kisan kai.

Ko in aba tsoro. Abokai da yan-uwa suka rika bashe da junansu. Iyaye da yan-uwa suka rika kashe juna. Shugabanni suka kasa yin mulkin kansu, suka zama azalumai. Yahudawa sun yarda da shaidar karya suka giciye Dan Allah, mara laifi. Yanzu kuma zarge zargen karya sun sa su cikin rashin tabbas. Ta wurin ayukansu sun dade suna cewa: "ku sa mai-tsarki na Israila shi dena shi bar mu." Ishaya 30:11. Yanzu an biya bukatar su. Tsaron Allah bai sake domin su ba. Shaitan ya zama shugaban al'ummar, manyan shugabanni na gwamnati da na addini kuma suka kasance kalkashin ikon sa.

Shugabannin bangarori masu hamayya da juna sukan hada kai su tsotse mabiyan su su kuma wulakanta su, sa'annan su kuma su karkashe juna ba tausayi. Ko tsarkin haikalin

ma bai hana su aikata muguntar su ba. Sukan kashe masu-sujada a gaban bagadi, aka kuma kazantar da haikalin da gawayen. Duk da haka cikin makantarsu da sabonsu, masu aikata muguntan nan sukan furta cikin jama'a cewa ba sa tsoron cewa za a halaka Urushalima, domin birnin Allah ne. Don kara tabbatar da ikonsu, suka ba annabawa toshi su shelata cewa mutane su jira kubutarwa da za ta zo daga wurin Allah, ko da dakarun Romawa suna kewaye da haikalin. Har karshe jama'a da yawa sun gaskata cewa Madaukaki zai sa hannu ya ba su nasara bisa magabta. Amma Israila ta rigaya ta bijire ma tsaron Allah, yanzu kuma ba ta da tsaro. Urushalima ta zama abin tausayi! Rashin jituwa ya nakasa ta, jinin yankakkun 'ya'yanta ya mamaye tituna, mayakan magabta kuma suka rushe ganuwoyin tsaron ta suna karkashe mayakanta!

Kowane annabcin da Kristi Ya yi game da rushewan Urushalima ya cika. Yahudawa sun dandana gaskiyar kashedin Sa cewa: "Da mudun nan da kuke aunawa kuma da shi za a auna maku." Matta 7:2.

Alamu da al'ajibai sun bayana, suna nuna cewa hallaka da kaito suna zuwa. Da tsakar dare, wani haske da ba a saba gani ba ya haskaka haikalin da bagadin. Da faduwar rana aka ga karusai da mayaka akan gizagizai suna shirye don yaki. Priestocin da ke aiki cikin haikalin da daren suka razana sabo da wasu surutai da basu gane ba; duniya ta girgiza, aka kuma ji muryoyi masu yawa suna cewa: "mu bar wurin nan." Babban kofar gabas din nan da mutum ashirin ba sua iya rufe ta da sauki, wadda kuma aka tokare ta da manyan karafuna da aka dasa cikin dutse a kasa, ta bude da tsakar dare, ba kuma wanda ya bude ta.

Shekara bakwai wani mutum ya rika kai da kawowa a titunan Urushalima yana shelar munanan ababan da za su abko ma birnin. Dare da rana, ya rika shela cewa: "Murya daga gabas! Murya daga yamma! Murya daga kusurwoyi hudun! Murya sabanin Urshalima da haikalin! Murya sabanin angaye da amare! Murya sabanin dukan mutane!" Sai aka kame wannan mai-shelan da ba a gane ko wane irin halitta ne shi ba, aka kulle shi a kurkuku aka kuma yi masa bulala, amma bai ce komi ba. Idan aka zage shi ko an mare shi, yakan amsa kawai: "kaito, kaiton Urshalima." "kaito, kaiton mazamna cikinta." Bai dena shelar kashedin nan ba har sai da aka kashe shi cikin yakin da ya y i annabcinsa.

Ko Kirista daya bai mutu a hallakawar Urshalima ba. Kristi ya rigaya ya ba almajiran Sa kashedi, kuma dukan wadanda suka gaskata maganarsa sun jiraci alamun da aka ce za su zo. Yesu yace: "Amma sa'anda kun ga Urshalima tana kewaye da dagar yaki, sa'annan ku sani ribdewatta ta kusa. Sa'annan wadanda ke chikin tsakiyarta su fita waje." Luka 21:20,21. Bayan da Romawa Kalkasin shugabancin Cestius suka kewaye birnin, sai haka kawai suka watsar da yakin a lokacin da ya kamata su kai hari. Israilawa suna gaf da sallama masu garin ke nan, sai janar din Romawa ya janye mayakansa, ba dalili. Amma Allah ne cikin alheri ya sa hakan ya faru domin mutanensa. An rigaya an ba Kirista alaman da aka yi masu alkawali, yanzu kuma an ba duk wanda ya yarda ya bi kashedin Mai-ceto. Aka shirya alamura ta yadda Yahudawa ko Romawa ba za su iya hana Kirista gudu ba.

Sa'anda Cestius ya janye, sai Yahudawa daga Urushalima suka bi dakarun nasa; yayin da suke fada da juna, Kirista suka sami damar ficewa daga birnin. A lokacin kuma babu magabta a kauyuka da za su tare su. Lokacin kewayewar Urushalima, Yahudawa sun tattaru a Urushalima don Idin Bukkoki, ta haka kuwa Kirista ko ina suka iya gujewa ba matsala. Ba da jinkiri ba suka gudu zuwa birnin Pella, a kasar Perea, gaba da urdun.

Dakarun Yahudawa suka tasamma Cestius da mayakansa kamar za su hallaka su gaba daya. Dakyar Romawa suka iya tserewa. Yahudawa suka koma Urushalima da ganimar nasaran yakin da suka yi. Amma nasaran nan ta jawo masu wahalu ne kawai. Ta sa sun yi ma Romawa taurin kan da ya jawo ma birnin su hallaka nan da nan.

Sa'anda Titus ya dawo ya kewaye Urushalima da mayaka, matsalolin da suka fado ma Urushalima suna da yawa. Birnin ya cika da miliyoyin Yahudawa da suka zo idin Paska. Shaguna cike da kayan masarufi da ya kamata su isa anfani har tsawon shekaru, bangarori masu-gaba da juna a cikin birnin sun rigaya sun hallaka shagunan lokacin tashe-tashen hankulan su, yanzu kuma aka dandana azabar yunwa. Aka sayar da mudun alkama kan talent guda. Yunwa ta kai inda mutane suka cinye mazagin wandonsu da takalmin su da jakar su ma. Mutane da yawa sukan fita da dare a sace, su nemi ciyayi da ganyaye a bayan ganuwar garin, ko da shike an rika kashe wandansun su da azaba mai-tsanani, wadanda suka dawo lafiya kuma akan kwace abin da suka samu dakyar din nan. Azabtarwa mafi-muni shi ne wanda masu-mulki sukan yi don kwace dan abin da mayunwata suka boye. Yawancin masu muguntan nan kuma mutane ne masu koshi da kan yi kwacen nan domin su ajiye ma kansu ne don nan gaba.

Dubbai sun mutu da yunwa da annoba. Kauna kam ta kare. Mazaje sun yi ma matan su fashi, mataye sun ma mazan su fashi. Akan ga yara suna kwace abinci daga bakunan iyayen su tsofofi. Tambayan annabi cewa: "Ya yiwu mache ta manta da danta mai-shan mama?" ya sami amsa cikin wannan birnin: "Hannuwan mata masu-tabshin rai sun dafa 'ya'yansu chikin ruwa, abinchinsu kenan a cikin hallakar diyar jama'ata." Ishaya 49:15; Makoki 4:10. An kuma cika annabcin da aka bayar karni goma sha hudu da suka gabata, cewa: "Machen kuma da ke wurinku, mai-tabshi, mai-sanyin hali, wadda ba ta da karfin rai da za ta ko sa tafin sawunta a kasa domin sanyin hali dajin tabshi, za ta dubi mijin kirjinta da mugun ido, har da danta da diyarta kuma; ….. da yayanta wadanda take haifassu; gama a boye za ta chinye su domin rashin abu duka, chikin datsewar yaki da matsi, wadanda abokin gabanka za ya matsa ka chikin kofofinka." Kubawar 28:56,57.

Shugabannin Romawan sun so su razana Yahudawa ta yadda dole za su sallamar. Fursunonin da suka yi taurin kai aka yi masu bulala da tsanantawa, aka kuma giciye su a cikin ganuwar birnin. Haka aka kashe daruruwan mutane kowace rana, aka kuma ci gaba har sai da gefen kwarin Jehoshaphat, a Kalfari kuma, an jera giciye da yawa ta yadda da kyar ma ake wucewa a tsakanin su. Ta haka aka cika la'anan nan da aka furta a gaban dakalin sharia'r Bilatus cewa: "Jininsa shi zamna a kanmu da 'ya'yanmu." Matta 27:25.

Titus ya so ya takaita yakin, ta haka kuma ya dauke ma Urushalima cikar azabarta. Tausayi ya cika shi sa'anda ya ga gawaye tuli tuli a cikin kwari. Daga kan Dutsen Zaitun kuma ya dubi haikalin nan mai-daraja, sai ya umurta cewa kada a taba ko dutse daya daga ginin. Kafin ya yi yunkurin kama haikalin sai da ya roki shugabannin Yahudawa kada su tilasta shi ya kazamtar da wuri mai-tsarkin da jini. Idan za su je a yi fadan a wani wuri dabam, Romawa ba za su bata tsarkin haikalin ba. Josephus da kansa ya roke su su sallamar domin su ceci kansu da birninsu da wurin sujadar su. Amma suka amsa masa da la'ana. Aka jejjefi mai-tsakancin nan na karshe yayin da yake rokon su. Yahudawa sun ki rokon Dan Allah, Yanzu kuma bayani da roko sun kara sa su nacewa ne cikin fadan, har karshe. Kokarin Titus domin ceton haikalin ya zama banza; wanda ya fi shi Ya rigaya Ya ce ba za a iske dutse daya a bisan wani dutsen ba.

Taurin kan shugabannin Yahudawan da, munanan laifukan da aka aikata cikin birnin, suka jawo fushin Romawan; sai kuma Titus daga baya ya kudurta kama haikalin a gurguje. Amma ya kudurta cewa ba za a hallaka haikalin ba. Amma ba a bi umurninsa ba. Bayan ya koma bukarsa da dare, Yuhudawa suka ruga daga cikin haikalin suka abka ma sojojin a waje. Cikin gwagwarmayar, wani soja ya jefa itacen wuta ta wani rami a ginin, nan da nan kuma dakunan ginin da aka yi masu ado da katako suka kama wuta. Titus ya ruga wurin tare da hafshoshinsa, ya umurci sojojin su kashe wutar. Ba a ji maganarsa ba. Cikin fushinsu, sojojin suka rika jefa wuta cikin dakunan da ke hade da haikalin, sa'an nan suka yanke dimbin mutane daga wadanda suka buya a wurin, jini ya kwarara a matakalan haikalin kamar ruwa. Dubban duban Yahudawa suka hallaka. Aka rika jin ihu cewa "Ichabod!" — darajar ta tafi.

Titus ya kasa tsayar da fushin sojoji, ya shiga da hafsoshin sa, ya dubi cikin ginin nan mai-tsarki. Darajar ginin ta ba su mamaki, kuma kafin wutar ta kai wuri mai-tsarki, ya yi yunkuri na karshe domin ya ceci haikalin, ya kuma umurci sojojin su tsayar da ci gaban wutar. Wani hafsa, Liberalis, ya yi kokarin tilastawa a yi biyaya bisa ga ikon matsayin sa; amma kiyayan da aka wa Yahudawa ya fi karfin buyayya ga sarkin Rum, ya kai ga marmarin yaki da bagen ganima. Sojojin suka ga komi kewaye da su zinariya ce da wutar ta haskaka; suka dauka cewa akwai dukiya mara iyaka a cikin haikalin. Wani soja a sace, ya tura wuta ta kofar wuri mai-tsarkin: nan da nan ginin gaba daya ya kama da wuta. Hayaki da wuta suka tilasta hafsoshin komawa, aka bar ginin ya kone "Abin bai yi kyaun gani ga Romawa ba — ga Yahudawa kuma fa?

Dukan kan tudun da birnin yake ya haskaka kamar aman wuta. Gine gine suka rika rushewa daya bayan daya, wuta kuma ta cinye su. Jinkan katako suka zama kamar harsunan wuta; bene ya zama kamar igiyar jan haske, sorayen kofofin suka rika fitar da wuta da hayaki. Tuddai da ke kusa suka haskaka; aka kuma ga mutane sun tattaru suna kallon hallakar, cikin bakinciki. Mutane suka cika kowace ganuwa da tsaunuka suna fushi da tunanin ramuwa. Ihun sojojin Romawa da kukan mutane da ke konewa sun hadu da karar

wutan da ke kona ginin, da kuma surutun katakai da ke faduwa. Kuwan duwatsu sun rika dawo da surutun mutane daga tsaunuka; mutanen da suna mutuwa da yunwa suka yi anfani da sauran karfin su don yin kukan bakinciki.

“Kisan cikin haikalin ya fi abin da ake gani a wajen muni. Maza da mata, tsofofi da yara, masu-tashin hankali da priestoci, masu-fada da masu-rokon jin kai duk an karkashe su barkatai. Wadanda aka kashe sun fi masu kashe su yawa. Dakarun suka rika tattaka tari tarin gawaye domin su ci gaba da kisa.”

Bayan hallakar haikalin, nan da nan dukan birnin ya fadi a hunnun Romawa. Shugababbin Yahudawa suka gudu daga mabuyansu; Titus kuma ya iske su, ba kowa ciki. Cikin mamaki ya ce Allah ne ya ba shi su cikin hannun sa; domin ba injin da ya isa ya rusa mabuyan nan komi karfin sa kuwa, aka kona birnin da haikalin har kasa, aka kuma kabce wurin da da haikalin ke tsaye, kamar gona. Irmiya 26:18. Daga kewayewar birnin har kisa da aka yi, sama da mutum miliyan daya sun hallaka; aka kwashe wadanda suka rage a matsayin kamammu, aka sayar da wadansu cikin bauta, wadansu kuma aka kai su Rum, aka jefa su ga namomin daji a wuraren shakatawa, wadansu kuma aka watsar da su barkatai cikin duniya.

Yahudawa sun yi ma kan su tarkoki; suka cika ma kansu kokon ramuwa. Cikin hallakan al’ummar su, da kuma wahalolin da suka bi su inda suka warwatsu, girbi suka yi na shukan da suka yi da hannunsu. In ji annabi: “Ka hallaka, ya Israila.” “gama ka fadi ta wurin sabon ka” Hosea 13:9; 14:1. An cika nuna cewa wai wahalolin su horo ne kai tsaye daga Allah. Ta haka ne babban mai-rudin nan ke so ya boye aikin sa. Tawurin bijire ma alheri da kaunar Allah, Yahudawa sun sa an janye kariyar Allah daga gare su, aka kuma bar Shaitan ya yi mulki bisan su yadda ya ga dama. Miyagun ababan da aka yi lokacin hallakar Urushalima kwatanci ne na ikon ramuwa na Shaitan a akan wadanda suka yarda da mulkinsa.

Ba za mu iya sanin bashin da Kristi ke bin mu sabo da salama da kariyan da muke moriya ba. Ikon kariyan Allah ne ke hana mutum shiga kalkashin ikon Shaitan dungum. Marasa biyayya da marasa godiya suna da dalili babba don godiya ga Allah sabo da jin kan Allah da jinkirin fushinsa yadda yake hana Shaitan anfani da ikonsa na mugunta. Amma idan mutane suka wuce iyakar hakurin Allah, akan cire wannan kariyar. Allah ba ya tsayawa kan mai-zunubi kamar mai-zartas da hukuncin laifin; amma yakan bar masu-kin jin kan Sa da kansu, su girbe abin da suka shuka. Kowane kashedi da aka bijire masa, kowace jaraba da aka yarda da ita, kowace ketarewar dokar Allah, shuka ake yi wadda kuwa za ta haifar da girbin ta. Daga bisani za a janye Ruhun Allah da aka yi ta kin Sa, daga mai-zunubin, sa’annan babu sauran ikon da zai danne miyagun halayyan mutum, ba kuma tsaro daga muguntar Shaitan da magabtakar sa. Hallakawar Urshalima kashedi ne ga dukan masu wasa da tayin alherin Allah, suna kuma bijire ma rokon da yake yi cikin jin kai. Ba a

ta ba ba da wata shaidar kiyayyar Allah ga zunubi da kuma tabbacin horo da zai abku ma mai-laifi kamar wannan ba.

Annabcin Mai-ceto game da hukumci da aka aiwatar kan Urshalima zai sake cika ta biyu wadda ta farkon ma alamar ta ce kawai. Daga abin da ya faru da Urshalima za mu iya ganin rushewar duniyar da ta bijire ma alherin Allah, ta kuma tattake dokar sa. Duniya kam ta ga munanan wahaloli cikin daruruwan shekarunta na laifuka. Abin ba dadin tunawa. Sakamakon bijire ma ikon Allah sun yi muni sossai. Amma ana nuna cewa abin da zai faru nan gaba zai fi muni. Ababan da suka faru can baya — jerin tashe tashen hankula, tarzuma, juyin juye-hali, “mayaki chikin girman yaki, da tufafi mirginannu chikin jini” (Ishaya 9:5) mene ne su in aka gwada su da ababan ban razana na ranan can sa’anda za a jenye Ruhun sassauci na Allah gaba daya daga miyagu, ta yadda ba bin da zai sassauta muradin zuciyar mutum da fushin Shaitan! Lokacin ne duniya za ta ga sakamakon mulkin Shaitan yadda ba ta taba gani ba.

Amma a wannan ranar, kamar ranar rushewar Urushalima, za a kubutar da mutanen Allah, dukan wanda za a iske sunansa cikin masu rai. Ishaya 4:3. Kristi Ya rigaya Ya bayana cewa zai sake zuwa domin Ya tattara nasa zuwa wurin kansa. “Sa’annan kuma dukan kabilun za su yi bakin chiki, za su kuwa ga Dan mutun yana zuwa a bisa giza gizai na sama tare da iko da daukaka mai-girma. Kuma za ya aike malaikunsa da babbar kara ta kafo, su kuma za su tattara zababbunsa daga kusurwoyi fudu, daga wannan iyakar sama zuwa wannan.” Matta 24:30,31. Sa’an nan wadanda sun ki biyayya da bishara za a cinye su da ruhun bakinsa a kuma hallaka su da hasken zuwansa. Tassalunikawa II, 2: 8. Kamar Israila ta da miyagu ne za su hallaka kansu ta wurin zunubinsu. Ta wurin rayuwa ta zunubi, sun ware kansu daga Allah, har mugunta ta bata yanayin su ta yadda bayanuwar darajar Sa wuta ce mai hallakaswa.

Bari mutane su yi hankali, kada su manta darasin da Kristi Ya koya masu. Yadda Ya gargadi almajiran Sa game da hallakawar Urushalima, Ya kuma ba su alama, domin su tsira daga hallakar, hakanan ne Ya gargadi duniya game da ranan hallaka na karshe, Ya kuma ba da alamun zuwan wannan ranar, domin dukan wadanda sun yarda su guji fushin da ke zuwa. Yesu ya ce: “A chikin rana da wata da tamrari za a ga alamu; a kan duniya al’ummai suna chiwon rai.” Luka 21: 25; Matta 24:29; Markus 13:24-26; Ruya 6:12-17. Wadanda sun ga alamun nan “su sani ya yi kusa, har bakin kofa.” Matta 24: 33. Ya kuma yi kashedi cewa “Ku yi tsaro fa.” Markus 13:35. Wadanda sun ji kashedi ba za a bar su cikin duhu ba, har wannan ranar ta hume su. Amma wadanda basu yi tsaro ba, “ranan nan za ta tarshe [su] kamar barawo.” Tassalunikawa I, 5:2-5.

Yadda Yahudawa basu shirya karban fadakar Mai-ceton game da Urushalima ba, haka ne duniya bata shirya karban sako na wannan lokacin ba. Ko da yaushe ne ranar Ubangiji za ta zo, za ta humi marasa imani. Sa’an da rayuwa ke gudana kamar yadda ta saba, yayin da mutane suka nutse cikin nishadi da harka, da kasuwanci, da neman kurdi, sa’an da

shugabannin addini suke daukaka ci gaban duniya da wayewar ta, mutane kuma sun shagala cikin yanayin tsaro na karya, lokacin ne, kamar yadda barawo da tsakar dare yake sata a cikin gidan da ba mai-gadi, hakanan ne hallaka faraf daya za ta abko ma marasa kula da marasa imani, “ba kwa za su tsira ba ko kadan.” Aya 3.

Babi na 2— Baftisma na Wuta da Jini

Sa'anda Yesu Ya bayana ma almajiransa abin da zai faru da Urushalima da kuma al'amura da suka shafi zuwansa na biyu, Ya kuma fada masu abin da zai faru da mutanensa da lokacin da za a dauke Shi daga wurinsu har zuwa dawowansa cikin daraja domin kubutarwarsu. Daga Zaitun, Mai-ceton Ya hangi matsalolin da za su abko ma ekklesiyar manzanin, jima kadan, idonsa kuma ya hangi munannan guguwa da za su addabi masu binsa a sararaki na biye, cike da duhu da zalunci. Cikin kalmomi kadan cike da ma'ana, Ya bayana ababan da shugabannin duniyan nan za su yi ma ekklesiyar Allah. Matta 24:9,21,22. Dole masu-bin Kristi su bi hanyan nan na kaskanci da reni da wahala da Mai-gidan Ya bi. Za a gwada ma dukan masu-bada gaskiya ga sunan Mai-fansar duniya kiyayyar da aka nuna masa su ma.

Tarihin edkklesiyar farko ya shaida cikar maganar Mai-ceton. Ikokin duniya da na lahira suka tinkari Kristi ta wurin masu-binsa. Kafirci ya ga cewa idan bishara ta yi nasara za a kawar da masujadan sa da wuraren hadayun sa; don haka kafirci ya tattaro ikokin sa domin su hallaka Kiristanci. Sai fa aka fara tsanantawa. Aka kawar da Kirista daga mallakansu, aka kuma kore su daga gidajensu. Sun "sha kokuwa mai-zafi ta wahala" Ibraniyawa 10:32. Aka "auna wadansu da ba'a da dukan bulala, i, har da sarkoki da damri." Ibraniyawa 11:36. Da yawa sun hatimce shaidarsu da jininsu. Shugabanni da bayi, mawadata da matalauta masana da jahilai duk an karkashe su ba tausayi.

Tsanantawan nan tun lokacin Nero, wajen lokacin da aka kashe Bulus, ya ci gaba har dauruwan shekaru. Aka zargi Kirista da laifuka mafi-muni, aka kuma ce su ne sanadin manyan matsaloli — yunwa da annoba a duniya. Da shi ke an ki jininsu, ko wane lokaci akwai shaidun karya a shirye domin su bashe su. Aka hukunta cewa 'yan tawaye ne su, magabtan addini, kwari kuma ga al'umma. Aka jefa da yawan su ga namomin jeji, ko uma an kone su a wuraren shakatawa. Wadansu an giciye su ne, aka kunsa wadansu cikin fatun namomin daji, sa'an nan aka jefa ma karnuka suka cinye su. Horon su ne yakan zama baban abin kallo lokacin bukukuwa. Jama'a da yawa sukan taru domin su sha kallo, suna dariyan azabarsu.

Duk inda masu bin Kristi suka nemi mafaka, akan bi su kamar namun daji ne. Sukan nemi buya a kangaye ne, inda ba mutane. "Suka sha rashi; kuntatattu ne, wulakantattu (sun fi karfin darajar duniya), suna yawo a jeji, chikin duwatsu da kogai, da kwazanzaman kasa." Ibraniyawa 11:33, 38. Koguna suka zama mabuyar dubbai. A kalkashin tuddai a bayan birnin Rum, aka tsaga dogayen ramuka masu tsawon gaske. Nan ne masu-bin Kristi suka rika bizne matattun su, kuma nan ne suka nemi mafaka idan aka zarge su, ana neman kama su. Sa'anda Mai-ba da rai zai falkas da wadanda suka yi aminci, da yawa da aka kashe su sabo da Kristi za su taso daga wadannan wuraren ne.

Cikin tsanani mafi muni wadannan shaidu na Yesu sun rike bangaskiyarsu. Ko da shi ke an hana su sakewa, aka boye su daga hasken rana, suka rika zama cikin koguna, duk da haka basu yi gunaguni ba. Da kalmomin bangaskiya da hakuri da bege suka rika karfafa juna su jimre kunci da wahala. Rashin dukiya na duniyan nan bai iya tilasta su yin musun bangaskiyarsu ga Kristi ba. Jarabobi da tsanantawa suka zama matakai da suka rika kawo su kusa da hutunsu da ladar su kuma.

Kamar bayin Allah na da, "aka kashe wadansu da duka, basu karbi pansarsu ba domin su ruski tashi mafi kyau." Ibraniyawa 11:35. Wadannan suka tuna maganar Mai-gidansu cewa idan aka tsananta masu sabo da Kristi, sai su yi murna sosai domin ladar su a sama mai-yawa ce; domin haka aka wulakanta annabawa kafin su. Suka yi farincik cewa sun isa su sha wahala sabo da bangaskiyar su, suka raira wakoki har daga cikin wuta ma. Sa'an da suka dubi sama cikin bangaskiya sai suka ga Kristi da malaiku suna kallon su daga sama, suna kuma nuna amincewa da naciyarsu. Murya ta sauko masu daga kursiyin Allah ta ce: "Ka yi aminci har mutuwa, ni ma im ba ka rawanin rai." Uya 2:10.

Shaitan ya yi kokarin hallaka ekklesiyar Allah da karfi, amma a banza. Babban jayayyan nan inda almajiran Yesu suka ba da rayukan su bai kare ba sa'an da amintattun nan suka mutu cikin famar su. Ta wurin shan kaye suka yi nasara. An kashe ma'aikatan Allah amma aikin Sa ya ci gaba. Bishara ta ci gaba da yaduwa, masu karban ta kuma suna karuwa. Ta shiga wuraren da ko gaggafar Rum ma ba za ta iya zuwa ba. Wani Kirista ya ce ma masu wulakanta su: "Kuna iya kashe mu, ku azabta mu, ku hukumta mu ma....Rashin adalcin ku shi ne shaida cewa ba mu yi laifi ba.... muguntar ku kuma ba za ta taimake ku ba." Wahalar su ma ta karfafa wadansu ne suka karbi sakon. "Kuna kashe mu, muna kara yawaita; jinin Kirista iri ne."

An kulle dubbai aka kuma kashe dubbai, amma wadansu kuma sun taso suka dauki wurin su. Wadanda aka kashe sabo da bangaskiyarsu sun zama tabbatattu na Kristi, Shi kuma Ya mai da su masu-nasara. Sun yi aikinsu, za su kuma karbi rawanin daraja sa'anda Yesu za ya zo. Wahalar Kirista ta jawo su kusa da juna, kusa da Mai-fansa kuma. Rayuwar su ta kyakyawar kwatanci, da shaidar mutuwar su, sun zama shaidar gaskiya a kullum, har inda ba a zata ba ma 'ya'yan Shaitan suka rika barin bautar sa suna zama masu-bin Kristi.

Sabo da haka Shaitan ya sake dabarar yakin sa da gwamnatin Allah ta wurin dasa tutar sa a cikin ekklesiyar Kirista. Idan har za a iya rudin masu bin Kristi su bata ma Allah zuciya, karfin su da karfin halin su da naciyar su za su lalace, zai kuma zama da sauki a kama su. Babban magabcin kuwa ya yi yunkurin anfani da dabara don samun abin da bai iya samu da karfi ba. Tsanantawa ya tsaya, a maimakon sa kuma aka kwadaita ma mutane kayan duniya. Aka sa masu bautar gumaka suka karbi wani bangaren adinin Kirista. Suka ce sun yarda Yesu Dan Allah ne kuma Ya mutu ya kuam tashi, amma basu yarda suna da zunubi ko bukatar tuba ko sakewar zuciya ba. Da shi ke sun yarda da wadansu koyaswoyin,

sai suka bidi cewa Kirista ma su yarda da wadansu koyaswoyin su, wai domin duka a hada kai a kan bangaskiya ga Kristi.

Yanzu ekklesiya ta shiga babban damuwa ken nan. Kurkuku da azaba da wuta da takobi basu yi muni kamar wannan dabarar ba. Wadansu Kirista suka tsaya da karfi suka ce ba za su sassauta addinin su ba. Wadansu kuma suka goyi bayan canja wadansu fannonin bangaskiyar, suka kuma hada kai da wadanda suka karbi wani bangaren Kiristanci, suna cewa watakila ta haka ne za su tuba. Wancan lokaci ne na bakinciki ga amintattu masu bin Kristi. Kalkashin rudu na Kiristancin karya, Shaitan ya rika shigowa cikin ekklesiya, domin shi lalata bangaskiyar su, shi kuma juya zukatan su daga maganar gaskiya.

Yawancin Kirista sun yarda daga baya suka sassauta matsayin su, aka kuwa sami wani hadin kai tsakanin Kiristanci da kafirci. Ko da shike masu bautar gumaka sun ce sun tuba, suka kuma hada kai da ekklesiya, sun ci gaba da bautar gumakan su, sai dai sun sake abin da suke masa sujada ne zuwa surar Yesu ko ta Maryamu ko tsarkaka. Bautar gumaka da aka kawo cikin ekklesiya hakanan ta ci gaba da mummunan aikinta. Koyaswoyi marasa kyau da camfe-camfe da bukukuwan gumaka suka sami shiga cikin bangaskiyar ekklesiya da sujadar ta. Sa'anda masu bin Kristi suka hada kai da masu bautar gumaka, addinin Kirista ta lalace, ekklesiya kuma ta rasa tsabtar ta da ikon ta. Amma akwai wadanda rudin nan bai batar da su ba. Suka rike amincin su ga Tushen gaskiya suka kuma yi sujada ga Allah kadai.

A kullum, masu cewa suna bin Kristi su kan kasu kashi biyu ne. Yayin da kashi daya su kan yi nazarin rayuwar Mai-ceton su kma yi kokarin gyarta kurakuransu ta yadda za su bi gurbinsa, kashi na biyu din sukan yi banza da gaskiyan da ke bayana kurakuran nasu ne. Ko lokacin da ekklesiya ta fi karfi ma ba ta kunshi amintattu ne kadai ba. Mai-cetonmu Ya koyar da cewa kada a karbi masu-zunubin ganganci cikin ekklesiya; amma kuma Ya hada masu-raunin halaye cikin mutanen Sa, Ya ba su dandanon koyaswar Sa da kwatancin Sa, domin su sami damar ganin kurakuran su su kuma gyarta su. Cikin manzani goma sha biyu din akwai mazambaci. Ba don raunin halin Yahuda ne aka karbe shi ba, sai dai duk da an san da raunin halin nasa aka dai karbe shi. Aka hada shi da almajiran domin ta wurin fadakarwa da kwatanciin Kristi, ya koyi halin Kiristanci, ta hakanan kuma ya ga kurakurnsa, ya tuba, kuma, ta wurin alherin Allah, a tsarkakae rayuwar sa cikin biyayya ga gaskiya. Amma Yahuda bai yi tafiya cikin hasken da aka ba shi ba. Ta wurin aikata zunubi ya gayyato jarabobin Shiatan. Miyagun halayyan sa suka bayana. Ya ba da zuciyar sa ga ikokin duhu, yakan ji fushi sa'an da an tsauta masa sabo da kurakuran sa, ta haka kuma har ya kai inda ya aikata babban laifin nan na bashe Mai-gidan shi. Haka dukan wadanda ke son zunubi yayin da suke boyewa a kalkashin inuwar cewa wai su masu-bi ne, sukan ki jinin wadanda ke nuna masu zunubin su. Sa'an da sun sami dama, kamar Yahuda, za su ba da wadanda cikin kauna suka nuna masu kuskuren su.

Manzanin sun sadu da wadanda cikin ekklesiya suka nuna cewa masu-bi ne su, alhali suna aikata zunubi. Hananiya da Safiratu sun yi rudi, suka nuna kamar sun ba da komi ga Allah, alhali sun ajiye ma kansu wani abu. Ruhu Mai-tsrki Ya bayana ma manzanin ainihin halin makaryatan nan, hukumcin Allah kuma ya kawar da wannan aibi daga tsabtar ekklesiya. Wannan shaida na Ruhun sani na Kristi cikin ekklesiya ya zama abin razana ga munafukai da miyagu. Ba su iya dadewa tare da wadanda ke wakiltar Kristi kullum cikin halin su da manufofin su ba; kuma yayin da jarabobi da tsanantawa suka abko ma masu bin Sa, wadanda suka kuduri aniyar barin komi sabo da gaskiya ne suka yarda su zama almajiran Sa. Sabo da haka, muddan tsanani ya ci gaba, ekklesiya ta ci gaba cikin tsabtar ta. Amma sa'an da an dena tsautawa, tubabbu marasa gaskiya ne da naciya suka rika shigowa, kofa kuwa ta budu ma Shaitan da shi ke ya sami wurin sa kafa.

Amma babu jituwa tsakanin Sarkin haske da sarkin duhu, kuma ba za a taba hada kan mabiyan su ba. Sa'an da Kirista suka yarda su hada kai da wadanda basu tuba gaba daya ba daga kafirci, sun shiga wata hanya ce da ta rika kara nisantar da su daga gaskiya. Shaitan ya yi murna cewa ya rudi mutane da yawa masu bin Kristi. Sa'an nan ya kawo dukan ikon sa a kan su; ya sa suka wulakanta wadanda suka kasance da aminci ga Allah. Ba wanda ya fi sanin yadda za a saba ma koyaswar Kirista kamar wadanda sun taba zama masu-kare ta; sai wadannan Kirista da suka yi ridda, tare da abokan su masu hadawa da kafirci, suka kallafa yakin su a kan fannonin koyaswar Kristi mafiya muhimmanci.

Sai da aka tsaya da gaske domin masu aminci su tsaya da karfi sabanin rudi da kazamtan da aka shigo da su cikin ekklesiya. Ba a karbi Littafi a matsayin ma'aunin gaskiya ba. Aka ce zancen 'yancin addini ridda ce, aka kuma ki jinin masu-karfafa batun.

Bayan an dade ana jayayya mai-tsawo, amintattun nan suka kudurta rabuwa da ekklesiyan nan mai-ridda, idan ta ki barin bautar gumaka. Suka ga cewa rabuwa ya zama dole idan har za su yi biyayya ga maganar Allah. Ba za su amince da kurakurai da ke iya jawo masu hallaka ba, har su kafa kwatancin da zai sa bangaskiyar 'ya'yansu da jikokinsu cikin hatsari ba. Don tabbatar da salama da hadin kai, sun yarda su yi duk wata yarjejjeniyar da ta je daida da aminci ga Allah; amma suka ga cewa bai kamata su rabu da aminci wai domin a sami salama ba. Idan har sai an sallamar da gaskiya da adalci domin a sami hadin kai, to sai dai a ci gaba da bambanci, ko yaki ma.

Da za a farfado da kaidodin da suka motsa amintattun nan a cikin zukatan mutanen Allah, da ekklesiya da duniya ma sun gyaru. Akwai kyaliya sosai game da koyaswoyin da suka kasance madogaran Kiristanci. Ana koyas da cewa wai ba su da muhimmanci sosai. Wannan lalacewan yana karfafa wakilan Shaitan, domin koyaswoyin karya da amintattu a zamanai da suka gabata suka sadakar da rayukan su domin su hana, sai ga shi yanzu dubban masu kiran kan su masu-bin Yesu suna girmama irin wadannan koyaswoyin.

Kiristan zamanin farko mutane ne na musamman ainun. Halin su mara-abin zargi, da bangaskiyar su mara-sanyi zargi ne kullum da ya rika hana mai-zunubi salama. Ko da shi ke ba su da yawa, kuma ba su da arziki ko matsayi ko sarauta, sun kasance abin ban razana ga miyagu, ta wurin halayen su da koyaswoyin su. Don haka miyagu suka ki jinin su kamar yadda Kayinu ya ki jinin Habila. Dalilin da ya sa Kayinu ya kashe Habila shi ne dalilin da ya sa miyagu suka karkashe mutanen Allah. Da dalili dayan ne Yahudawa suka ki giciyayyen Mai-ceeton- domin tsarki da tsabtar halinsa sun rika tsauta ma son kansu da muguntarsu kuma. Daga zamanin Kristi har zuwa yau, amintattun almajiransa suna jawo kiyayya da magabtakan masu-zunubi.

Ta yaya kenan za a ce da bishara sakon salama? Sa'an da Ishaya ya yi annabcin haihuwar Masiya, ya ba shi lakabin "sarkin salama." Sa'an da malaikun suka sanar ma makiyaya cewa an haifi Kristi, sun raira cewa: "Alhamdu ga Allah chikin mafi-daukaka, a duniya kuma salama wurin mutanen da yake murna da su sarai." Luka 2:14. Akwai kamanin sabani tsakanin annabce annabcen nan da maganar Kristi cewa: "Na zo ba domin in koro salama ba, amma takobi." Matta 10:34. Amma idan an fahimce su da kyau, bayanai din sun je daidai da juna. Bishara sakon salama ce. Kiristanci tsari ne wanda idan aka karba aka yi biyayya da shi, zai kawo salama da jituwa da farinciki ko ina a duniya. Addinin Kristi zai hada kan dukan masu karban koyaswoyin sa. Manufan Kristi shi ne sasanta mutane da Allah, da juna kuma. Amma duniya kan ta tana kalkashin Shaitan, magabcin Kristi. Bishara tana ba su kaidodin rayuwa da suka bamabnta da halayen su, suna bijire mata. Sun ki jinin tsabtar ta da ke nuna munin zunuban su, suna kuma tsananta ma wadanda su ke bayana masu sharuddan ta. Da shi ke gaskiyan da take kawowa tana jawo kiyayya ne ya sa aka ce bishara ta na kawo takobi.

Asirin da ke sa adilai su sha tsanani a hannun miyagu yana da ban mamaki kwarai ga masu kankantar bangaskiya. Wadansu ma sukan so su janye bagaskiyar su ga Allah wai don yana barin miyagun mutane su ci gaba, yayin da ake wulakanta nagargarun mutane masu halin kirki. Akan tambaya cewa: Yaya Mai-adalci da jinkai, Mai-matukar iko kuma, zai bari a yi rashin adalci a duniya? Wannan tambaya ce da ba ruwan mu da ita. Allah ya ba mu isashen shaidar kaunarsa, kuma bai kamata mu yi shakkar adalcinsa ba, da shi ke ba za mu iya gane al'amuransa ba.Yesu Ya ce ma almajiransa: "Ku tuna da maganata wadda na fada maku, Bawa ba ya fi Ubangijinsa girma ba. Idan suka yi mani tsanani, za su yi maku tsanani kuma." Yohanna 15:20. Yesu Ya wahala domin mu, fiye da yadda duk wani mai-binsa zai iya wahala ta wurin muguntar miyagu. Wadanda ake bidar su su jimre azaba da kisa suna bin sawun Dan Allah ne.

"Ubangiji ba mai-jinkiri ba ne ga zanchen alkawalinsa." Bitrus II, 3:9. Ba Ya manta 'ya'yansa, amma Ya kan bar miyagu su bayana ainihin halin su, domin kada su yaudari wadanda su ke son bin Sa. Kuma ana sa adilai cikin azaba domin a tsarkake su ne, domin

kwatancin su ya nuna muguntar marasa ibada; kuma domin naciyar su ta nuna muguntar marasa ibada da marasa ba da gaskiya.

Allah yakan bar miyagu su ci gaba, kuma su nuna magabtakar su da Shi, domin sa'anda sun cika ma'aunin zunubinsu, kowa zai ga adalcinsa da jinkansa, yayin da ake hallaka su. Ranar ramuwarsa tana gagabtowa, sa'anda dukan masu-ketare dokarsa da masu wulakanta mutanensa za su gamu da sakamakon ayukansu; sa'an da kowace mugunta ko rashin adalcin da aka yi ma amintattun Allah zai sami sakamakonsa, sai ka ce Kristi ne da kansa aka yi masa muguntar.

Akwai kuma wata muhummiyar tambaya da ya kamata ta ja hankalin ekklesiyoyi yau. Manzo Bukus ya ce: "Dukan wadanda su ke so su yi rai mai-ibada chikin Kristi Yesu za su sha tsanani." Timothawus II, 3:12. Idan haka ne, don me tsanani ya yi sanyi yanzu? Dalilin kadai shi ne cewa ekklesiya ta rungumi kaidar duniya, sabo da haka kuma ba ta tayar da sabani. Addinin zamanin mu yau ba irin mai-tsabta da tsarkin nan ne na zamanin Kristi da manzaninsa ba. Sabo da ruhun gama-hunnu da zunubi ne, domin an yi wasa da muhimman gaskiyan maganar Allah, don akwai karancin ainihin ibada a cikin ekklesiya, shi ya sa Kiristanci ke da farin jini a duniya. Bari a falkas da irin bangaskiya da ikon nan na ekklesiyar farko, za a kuwa ta da ruhun tsanantawa, za a kuma sake kunna wutar tsanani.

Babi na 3— Zamanin Duhu

Manzo Bulus cikin wasikar sa zuwa ga Tassalunikawa, ya ce za a yi babbar riddar da za ta kai ga kafawar mulikn paparuma. Ya ce rana ta Kristi ba za ta zo ba, “sai riddan ta fara zuwa, mutumen zunubi kuma ya bayanu, dan hallaka, shi wanda yana tsayayya, yana kwa daukaka kansa gaba da dukan abin da ake yi masa sujada, har yana zamne chikin haikalin Allah, yana shelar kansa shi Allah ne.” Biye da wannan kuma, manzon ya gargadi yan-uwan sa cewa “asiri na taka shari’a yana ta aikawa ko yanzu.” Tassalunikawa II, 2:3,4,7.

Kadan da kadan dai, a sace, daga baya kuma har a bayane, bayan ya kara karfi har ya mallaki zukatan mutane, “asiri na taka shari’an” ya ci gaba da aikin sa na sabo. A hankali dai har al’adun kafirai ya kawo sassauci ga ruhun saka-saka. Amma da zaran tsanantawa ya tsaya, sarakuna da fadawan su kuma suka fara shigowa addinin Kiristanci, sai ekklesiya ta watsar da tawali’un Kristi da manzanin sa, ta rungumi fadin rai da fahariyar priestoci da shugabannin kafirai, ekklesiya ta sauya sharuddan Allah da koyaswoyin mutane, da al’adun su kuma. Tuban karya da Constantine ya yi, ya jawo farinciki sosai; sai duniya, yafe da kamanin adalci, ta shiga cikin ekklesiya. Sai kuma lalacewa ya habaka. Kafirci da ake gani kamar an rigaya an murkushe shi kuma sai ya sami nasara. Ruhun kafirci ya mallaki ekklesiya. Aka shigo da koyaswoyin kafirci da al’adun sa cikin addini da sujadar wadanda ke kiran kan su masu-bin Kristi.

Garwayewar kafirci da Kiristancin nan ya kai ga tasowar “mutumen zunubi” wanda annabi ya ce yana tsayayya, yana kuma daukaka kan sa gaba da Allah. Wannan addinin babban alama ce ta ikon Shaitan da kokarin sa na neman hawa kan kursiyin domin shi yi mulkin duniya yadda ya ke so.

Shaitan ya taba so ya gama hannu da Kristi. Ya zo wurin Dan Allah a jeji inda ya jarabce Shi, sai ya nuna masa dukan mulkokin duniya da darajar su, sa’an nan ya ce zai ba da dukan su a hannun Kristi idan har Ya amince da fifikon sarkin duhu. Kristi Ya tsauta ma majarabcin, Ya kuma tilasta masa gudu daga wurin. Amma Shaitan yana yin nasara sa’anda yake jarabtar mutum da abu dayan. Don samun riba da girma na duniya aka sa ekklesiya ta nemi goyon bayan manyan mutane na duniya kuma da shike ta musunci Kristi hakanan, aka rude ta har ta yarda da shugabancin wakilin Shaitan, watau bishop na Rum.

Wata koyaswar Rum ita ce cewa wai paparuma ne shugaban ekklesiyar Kristi cikin dukan duniya, wanda ake gani, kuma wai an ba shi iko bisa bishop- bishop da pastoci da ke ko ina a duniya. Fiye da haka ma wai an ba paparuma lakabi irin na Allantaka. Ana ce da shi “Ubangiji Allah Paparuma,” an kuma ce shi mara-kuskure ne. Yana bidar ban girma daga kowane mutum. Abin da Shaitan ya bida inda ya jarabci Yesu, shi ne paparuma ke bida ta wurin ekklesiya Rum, kuma dimbin mutane suna shirye su ba shi girman.

Amma masu tsoron Allah suna amsa wannan renin yadda Kristi Ya amsa ma magabcin ne: “Ka yi sujada ga Ubangiji Allahnka, shi kadai kuma za ka bauta masa” Luka 4:8. Allah bai taba cewa Ya nada wani mutum ya zama kan ekklesiya ba. Amma Koyaswar fifikon paparuma ta saba ma koyaswar Littafi. Paparuma ba zai taba samun iko bisa ekklesiyar Kristi ba, sai dai ta wurin kwace.

Ekklesiyar Rum tana zargin sauran ekklesiyoyi da laifin ridda, cewa sun baude daga ekklesiya ta gaskiyar. Amma su Katolikawa ne suka yi wannan laifin. Su suka saukar da tutar Kristi, suka rabu da “bangaskiya wadda aka taba ba tsarkakan.” Yahuda 3.

Shaitan ya sani sarai cewa Littafi zai sa mutane su gane rudinsa, su kuma fi karfin ikonsa. Ta wurin wannan ne Mai-ceton duniya ma Ya yi nasara da shi. Ga kowane hari, Kristi Ya yi anfani da garkuwa ta gaskiya, cewa, “An rubuta.” Idan har Shaitan zai tabbatar da ikon sa a kan mutane ya kuma tabbatar da ikon paparuma, dole sai ya hana mutanen sanin Littafi. Littafi yakan daukaka Allah ya kuma sa mutane daidai matsayin su; shi ya sa dole Shaitan ya danne ya kuma boye gaskiyar Littafin. Matakin da ekklesiyar Rum ta dauka ke nan. An hana yaduwar Littafi har tsawon daruruwan shekaru. Aka kuma hana mutane karanta shi ko ajiye shi a gidajensu ma, priestoci kuma suka rika fassara Littafi ta yadda zai tabbatar da rudinsu. Ta haka aka sa kusan ko ina aka dauka cewa paparuma ne wakilin Allah a duniya, mai-iko bisa ekklesiya da kasa.

Da shi ke an kau da mai-gano kuskure, Shaitan ya yi abin da ya ga dama. Annabci ya ce mulkin paparuma “za ya nufa ya sake zamanu da shari’a kuma.” Daniel 7:25. Domin samo ma tubabbu daga kafirci wani abu a madadin bautar gumaka, ta haka kuma a karfafa jabun Kiristancin nan nasu, sai aka shigo da girmamawar sifofi cikin sujadar Kirista a hankali, a hankali. Daga baya wani kudurin majalisa ya tabbatar da wannan bautar gumakar. Don kalmasa wannan batancin, Rum ta yi yunkurin cire doka ta biyu daga dokokin Allah, ta kuma raba doka ta goma kashi biyu domin dokokin su cika goma.

Ruhun daidaitawa da kafirci ya bude hanya domin a kara rena ikon Allah. Shaitan, ta wurin lalatattun shugabannin ekklesiya, ya taba doka ta hudu kuma, ya kuma yi kokarin watsar da Assabbat din, ranar da Allah Ya albarkace ta Ya kuma tsarkake ta (Farawa 2:2,3), a maimakon ta kuma ya so ya girmama bukin da kafirai ke yi, wai bukin babban ranar rana. Da farko dai ba a bayyane aka so a yi canjin ba. A karni na fari dukan Kirista sun kiyaye Assabbat ne. Sun girmama Allah, suna kuma gaskata cewa dokar sa ba mai-sakewa ba ce; suka rika kare kaidodinta. Amma sannu a hankali, Shaitan ya yi aiki ta wurin wakilan sa don cim ma manufar sa. Domin a jawo hankulan mutane zuwa Lahadi, sai aka mai da shi bukin tunawa da tashin Kristi daga matattu. Aka rika hidimomin ibada a ranar; duk da haka an mai da ita ranar shakatawa ce, yayin da ake kiyaye Assabbat. Domin shirya hanya don aikin da ya shirya yi, Shaitan ya sa Yahudawa kafin zuwan Kristi, su jibga ma Assabbat nauyin bukatu masu-yawa ta yadda kiyaye shi ya zama abu mai-wuya. Bayan wannan sai yanzu kuma ya bata mata suna, wai ranar yahudawa ce. Yayin da yawancin Kirista suka ci

gaba da kiyaye Lahadi a matsayin bukin farin ciki, sai Shaitan ya sa suka mai da Assabbat ranar azumi, ranar bakin ciki, domin mutane su nuna kiyayyar su ga Yahudanci.

A farkon karni na hudu, sarki Constantine ya ba da umurnin da ya mai da Lahadi ranar buki ta dukan kasar Rum. Kafiran kasar sa suka tsarkake ranar ranan, Kirista kuma suka girmama ta; nufin sarkin ne ya hada kan kafirci da Kiristanci. Bishop bishop na ekklesiya ne kuwa suka shawarce shi ya yi hakanan, wadanda sabo da dogon buri da neman mulki suka ga cewa, idan kafirai da Kirista suna kiyaye rana daya, wannan zai kara sa kafirai su karbi Kiristanci da suna kawai, ta haka kuma ikon ekklesiya da darajar ta za su karu. Amma yayin da aka sa wadansu Kirista masu- tsoron Allah suka fara ji kamar Lahadi yana da tsarki kadan, duk da haka suka rike ainihin Assabbat a matsayin sa na mai-tsarki na Ubangiji, suka kiyaye shi kuma bisa ga doka ta hudu.

Mai-rudin bai kamala aikin sa ba dai. Ya kudura tattara Kiristan duniya kalkashin mulkin sa, ya kuma yi mulki ta wurin wakilan sa, paparuma, wanda ya ce shi ne wakilin Kristi. Ta wurin kafirai masu-rabin tuba da shugabannin addini masu-dogon buri, da kuma masu bi da ke kaunar duniya, ya cim ma manufar sa. An rika taronin majalisu loto loto, inda manyan shugabannin ekklesiya daga dukan duniya sukan taru. A kusan kowane taro akan kara danne Assabbat da Allah Ya kafa, yayin da ake kara daukaka Lahadi. Ta haka aka karfafa bukin kafirai a matsayin rana ta Allah, Assabbat na Littafi kuma aka ce da shi al'adar Yahudanci, masu kiyaye shi kuma aka ce la'antattu ne.

Babban mai-riddan ya daukaka kan sa "gaba da dukan abin da ake ce da shi Allah, ko abin da ake yi masa sujada." Tassalunikawa II, 2:4. Ya yi yunkurin canza dokar Allah da ke nuna ma dukan yan Adam Allahn gaskiya Mai-rai. Cikin doka ta hudu an bayana Allah a matsayin Mahalicin sammai da duniya, ta haka kuma aka bambanta shi daga dukan allolin karya. A matsayin abin tunawa da halitta ne aka tsarkake rana ta bakwai ta zama ranar hutu. An shirya ta ne ta rika tuna ma mutane cewa Allah ne tushen rayuwa wanda kuma za a yi masa sujada da bangirma. Shaitan yana kokarin juyo mutane daga biyayya ga Allah da dokar Sa; sabo da haka yana mai da hankalinsa ga yin sabani da dokan da ke nuna Allah a matsayin Sa na Mahalici.

Kiristan da suka ki ikon paparuma yanzu suna cewa tashin Kristi ran Lahadi ne ya mai da Lahadin Assabbat. Amma babu nassin da ya ce haka. Kristi ko manzanin basu ba ranan wannan darajar ba. Kiyaye Lahadi ga Kirista yana da tushe daga "asiri na taka shari'an" ne (Tassaluniawa II, 2:7) wanda ko a zamanin Bulus ma ya rigaya ya fara aikin sa. Ina ne, kuma yaushe ne Ubangiji Ya yarda da wannan kage na paparuma? Wane kyakyawan dalili za a bayar don canjin da Littafi bai goyi bayan sa ba?

Cikin karni na shida, paparuma ya rigaya ya kafu sosai. Rum ne cibiyar mulkin sa, aka kuma ce bishop na Rum ne kan dukan ekklesiya. Kafirci ya ba paparuma wuri. Dragon ya ba bisan "ikonsa da kursiyinsa da hukumchi mai-girma." Ruya 13:2. Yanzu ne kuma

farkon shekaru 1260 na danniyar paparuma da aka yi annabci cikin litattafan Daniel 7:25; Ruya 13:5-7. Aka tilasta Kirista, ko su sadakar da amincin su su yarda da shugabancin paparuma, ko kuma su karasa rayuwar su cikin kurkuku ko kuma a kashe su. Lokacin ne maganar Yesu ta cika cewa: “Amma har da iyaye, da yan-uwa, da abokai za su bashe ku: a chikin ku kuma za su kashe wadansu. Za ku zama abin ki ga dukan mutane sabili da sunana.” Luka 21:16,17. Tsanantawa ta abko ma amintattu da muni fiye da duk wanda aka taba yi, duniya kuma ta zama babbar filin daga. An yi daruruwan shekaru ekklesiyar Allah tana fakewa a boye. In ji annabin: “Machen kwa ta gudu zuwa chikin jeji, inda Allah Ya rigaya Ya shirya mata wurin da za a yi mata kiwo a chan, kwana dubu da metin da satin.” Ruya 12:6.

Hawan ekklesiyar Rum kan karagar mulki ne ya zama mafarin Zamanin Duhu. Sa’an da ikon ta ya karu, duhun yakan karu. Aka dauke bangaskiya ga Kristi aka mayar wurin paparuma. Maimakon dogara ga Dan Allah don gafarar zunubi da ceto na har abada, mutane suka dogara ga paparuma, da priestoci da ya zaba su wakilce shi. An koya masu cewa papruma ne matsakancin su a duniya, kuma wai ba mai zuwa wurin Allah sai ta wurin sa; kuma, wai shi yana matsayin Allah ne gare su sabo da haka dole a yi masa biyayya. Kauce ma umurnin sa yakan zama dalilin horo mai-tsanani kan jikuna da rayukan masu-laifin. Ta wurin wannan aka juya tunanin mutane daga Allah zuwa fadaddun mutane masu kuskure, masu mugunta, har zuwa wurin Shaitan kan sa wanda ya cika nufin sa ta wurin su. Aka boye zunubi cikin rigar adalci. Sa’an da an danne maganar Allah har mutum ya mai da kan sa madaukaki, ba abin da zai faru sai dai zamba da rudi da zunubi. Daukaka dokokin mutum da al’adun sa ya jawo rubewa da yakan faru sa’an da aka kawar da dokar Allah.

Wadannan kwanaki ne na wahala ga ekklesiyar Kristi. Amintattu kalilan ne a lokacin. Akwai dai shaidu na gaskiya, amma wani lokaci kuskure da camfi sukan so su sami fifiko, addini na gaskiya kuma yakan kusan bacewa daga duniya. Ba a ganin bishara kuma a lokacin, amma addini na karya ya dinga yaduwa, aka rika damun mutane da wahaloli.

An koya masu su dogara ga paparuma a matsayin matsakancin su, su kuma dogara ga ayukan su domin kafarar zunubi. Aka bukace su su rika tafiya mai-nisa, da ayukan neman gafara, da sujada ga tsofofi, da gina majami’u da wuraren hadaya, da biyan kurdade masu yawa a ekklesiya, wai domin a kawar da fushin Allah ko kuma a sami alherin Sa; sai ka ce Allah kamar mutane ne da zai fusata kan kananan ababa, ko kuma a kwantar Masa da zuciya ta wurin ayukan neman gafara!

Ko da shi ke zunubi ya karu ko cikin shugabannin ekklesiyar Rum ma, duk da haka farin jinin ta ya rika karuwa. Kusan karshen karni na takwas, ekklesiyar Rum ta koyar da cewa wai a sararrakin farko na ekklesiya, bishop-bishop na Rum suna da ikon da suke manna ma kansu. Don tabbatar da hakan, dole a kirkiro wata hanya, uban karya kuwa ya nuna masu yadda za su yi. Shugabannin addini suka kirkiro rubuce rubucen karya. Aka fito

da dokokin karya, wadanda ba a taba jin labarin su ba, duk da suna cewa wai paparuma ne madaukaki tun farkon zamanai. Ekklesiyar da ta ki gaskiya kuwa nan da nan ta yarda da wannan rudin.

An zalunci amintattun maginan nan kan tushen gaskiyan (Korinthiyawa I, 3:10,11), aka kuma hana su aiki yayin da koyaswar karyan ke bata masu aiki. Kamar masu gini kan ganuwar Urushalima a zamanin Nehemiah, wadansu sun kasance a shirye su ce, “karfin masu daukan kaya ya lalace, ga kwa da kasa barkatai tuli; har da mun kasa gina ganuwa.” Nehemiah 4:10. Sabo da sun gaji da tsanani, da rudi da zunubi, da kowace matsala da Shaitan ya iya kawowa don hana ci gaban aikin su, wadansu amintattun magina suka yi sanyin gwiwa; kuma domin salama da zaman lafiya sabo da dukiyar su da rayukan su, suka kauce daga tushe na gaskiyan. Wadansu da basu damu da muguntar magabtan su ba suka ce: “Kada ku ji tsoronsu, ku tuna da Ubangiji wanda shi ke mai-girma, mai-ban razana.” Nehemiah 4:14; kuma suka ci gaba da aikin, kowa da takobinsa a maran sa. Afisawa 6:17.

Ruhun nan na kiyayya da sabanin ne yakan motsa magabtan Allah kowace sara, kuma akan bukaci tsaro da aminci iri dayan daga bayin Sa. Jawaban Kristi ga almajiran farko sun shafi masu bin Sa na kowane lokaci har karshen lokaci. Ya ce: “Abin da ni ke che maku, ina che ma duka: ku yi tsaro.” Markus13:37.

Duhun ya dinga karuwa. Bautar sifofi ta yadu. Aka dinga kunna wutar kyandir a gaban sifofi, ana addu’a gare su. Al’adu mafi-muni suka yawaita. Camfi ya mallaki zukatan mutane har ma suka kasa yin tunani da kyau. Sa’an da priestoci suka zama masu son nishadi da annishuwa da toshi, dole masu-bin kwatancin su su rude cikin jahilci da lalacewa.

Wani matakin ci gaban paparuma kuma shi ne lokacin da paparuma Gregory VII ya yi shelar rashin aibin ekklesiyar Rum. Ya ce ekklesiyar bata taba kuskure ba, kuma ba za ta taba yi ba, bisa ga Littafi, in ji shi. Amma ba a ambaci inda Littafin ya ce haka ba. Paparuman ya kuma ce yana da iko ya saukar da sarakuna, kuma ba wanda ya isa ya warware duk wani umurnin da shi ya bayar, amma shi yana da iko ya warware umurnin sauran mutane.

Misalin ha’incin wannan paparuman shi ne abin da ya yi ma sarkin Jamus, Henry IV. Ya ware sarkin daga ekklesiya, sa’annan ya sauke shi daga saurautar. Don tsoron barazanar yarimomin sa, Henry ya ga wajibi ne ya nemi sulhu da Rum. Tare da matar sa da wani aminin sa, Henry ya ketare tsaunukan Alps da tsakar rani lokacin matukar sanyi, domin shi kaskantar da kan sa a gaban paparuma. Sa’an da ya haura dakin da Gregory yake hutawa, sai aka kai shi wani zaure, ba tare da dogarawan sa ba, nan ne fa, cikin sanyin rani, ba hula ko takalmi, kuma sanye da riga mara kauri, ya jira izinin ganin paparuma. Sai da ya cika kwana uku yana azumi da tuba kafin paparuma ya yafe masa. Duk da haka ma sai da ya jira izinin paparuma kafin ya koma sarautar sa. Gregory kuma ya rika fariya cewa yana da ikon ladabtar da girman kan sarakuna.

A fili, ga bambanci tsakanin girman kan paparuma da tawali'un Kristi wanda ke roko a kofar zuciya domin a ba Shi damar shiga domin ya ba da gafara da salama, wanda kuma Ya koya ma almajiran Sa cewa: "Kuma dukan wanda yake so ya zama na fari a chikinku, bawanku za ya zama." Matta 20:27.

Sararraki na biye an rika samun karin kurakuran koyaswa daga Rum. Tun kafin kafuwar mulkin paparuma ma, koyaswoyin kafiran masana sun sami tasiri cikin ekklesiya. Da yawa da suka ce sun tuba, sun ci gaba da kaidodin kafircin su, suka kuma koya ma wadansu, domin su kara tasirin su a cikin kafirai. Ta haka aka shigar da munanan kurakurai cikin addinin Kirista. Daya daga cikin su ita ce koyaswar cewa wai mutum ba ya mutuwa, kuma matacce ma ya san abin da ke faruwa. A kan wannan koyaswan ne Rum ta kafa al'adar ta na rokon tsarkaka da kuma daukaka ga Maramu. Daga nan ne ma koyaswan nan ta azabtarwa har abada ga marasa tuba ta taso.

Sa'an nan kuma aka shirya hanya don wata koyaswar kafirci kuma wadda Rum ta ba shi suna purgatory, wadda ake anfani da ita don razana jama'a. Ta wurin wannan koyaswa ana cewa wai akwai wani wurin azaba inda wadanda basu cancanci wuta a lahira har abada ba za su sha horo don zunuban su, daga nan kuma, bayan an tsarkake su, sai a shigar da su sama.

An kuma kirkiro wata koyaswar domin Rum ta yi riba daga tsoro da laifukan masu bin ta. Akan yi ma dukan wadanda suka yi ma paparuma yake-yaken sa na neman fadada mulikinsa, ko horon magabtansa, ko hallaka masu-musun daukakarsa, alkawalin gafarar zunubansu na da da na yanzu da na nan gaba. Aka kuma koyar da cewa ta wurin biya ma ekklesiya kurdi, za su ceci kansu daga zunubi, su kuma kubutar da rayukan matattun abokan su da ke fama cikin azabar wuta. Ta wannan hanya ma Rum ta cika baitulmalinta, ta kuma iya biyan bukatun ma'aikatan ta da anishuwan su.

An kuma sauya jibin Ubangiji da wata hadaya da ake ce da ita mass. Priestocin ekklesiyar katolika sun rika cewa wai ta wurin al'adar su ta mass, sukan juya gurasa da rowan anab su zama ainihin jikin Yesu da jinin Sa. Da sabo, cike da rashi kunya, suka yi ikirarin cewa suna da iko su halici Allah, Mahalicin komi. Aka bukaci Kirista, a bakin ran su, su rantse cewa sun ba da gaskiya ga koyaswan nan na ridda. Dimbin mutane da suka ki kuwa, an kone su da wuta.

A karni na goma sha uku, an kafa wani Bincike, wani tsari mafi-muni cikin dukan dabarun ekklesiyar Rum. Shaitan ya hada hannu da shugabannin ekklesiyar Rum. A majalisar su, Shaitan da malaikun sa suka mallaki tunanin miyagun mutane, a tsakanin su kuwa malaikan Allah, wanda ba su gan shi ba, ya dinga rubuta kudurorinsu, yana kuma rubuta tarihin ayukansu da idon mutum ba zai so ya gani ba. "Babila babba" kuma "tana maye da jinin tsarkaka." Guntayen gababuwan miliyoyin mutanen da aka kashe sun dinga kai kara wurin Allah domin ramuwa kan Rum.

Mulkin paparuma ya zama azalumin duniya. Sarakunan duniya kanana da manya suka rika biyayya ga dokokinsa. Ya zama kamar kadarar mutane a duniya, ko dawama ma, tana hannunsa ne. An yi daruruwan shekaru ana amincewa da dokokin Rum, ana bin al'adun ta, ana kuma yin bukukuwan ta. An rika darajanta priestocin ta, ana biyan bukatun su a yalwace. Ekkelesiyar Rum ba ta taba samun maraba, ko ban sha'awa ko iko irin na wannan lokacin ba.

Amma "tsakar ranar paparuma tsakar daren duniya ne." Kusan ma da mutane da priestoci kan su basu san Littafi ba. Kamar Farisawa na da, shaugabannin ekklesiyar paparuma suka ki jinin hasken da kan bayana zunuban su. Da shike an cire dokar Allah wanda shi ne ma'aunin adalci, suka yi mulki ba kadada, suna aikata mugunta ba sassauci. Zamba da handama da fasikanci suka dawama. Mutane basu damu su yi kowane laifi ma ba don dai su sami arziki ko matsayi. Fadar paparuma da ta kowane priest suka zama cibiyoyin shaye shaye. Wadansu paparuma-paparuma suka aikata laifukan da har shugabanni na duniya ma suka so su saukar da su sabo da munin laifukan nasu. An yi daruruwan shekaru Turai bai sami ci gaban ilimi ko wayewa ba. Kiristanci kuma ya sami nakasa na tarbiyya da na bishara.

Yanayin duniya a zamanin ikon Rum ya zama abin tsoro wanda ya cika maganar annabi Hosea daidai cewa: "Mutane na sun lalace domin rashin ilimi: tun da ka ki ilimi ni ma za ki ka.... tun da ka manta da shari'ar Allahnka, ni kuma zan manta da yayanka." "Babu gaskiya, ko jinkai, ko sanin Allah a kasar. Babu komi sai rantsuwa da cin amana, da kisa da sata, da aikin zina. Sukan pasu, jini kuma yana taba jini." Hosea 4:6,1,2.

Babi na 4— Mutanɛ na musamman

Duk da duhun da ya mamaye duniya a zamanin mulkin paparuma, ba a iya bice hasken gaskiya kwatakwata ba. A kowace sara akwai shaidu na Allah - mutane da suka ba da gaskiya cewa Kristi ne kadai Matsakanci tsakanin Allah da mutu., suka mai da Littafi kadai kaidar rayuwar su, suka kuma tsarkake Assabbat na gaskiya. Aka lakaba masu suna masu-ridda, aka zargi manufofinsu , aka bata masu suna, aka hana yaduwar rubuce rubecensu, ko kuma a canza rubucerubucen, a sake manufofinsu. Duk da haka suka jimre daga sara zuwa sara, suka rike bangaskiyarsu da tsarki, domin sararakin baya su gada.

Tarihin mutanen Allah a zamanun duhu da suka biyo bayan mulkin Rum yana rubuce a sama. Amma a duniya da wuya a same su a rubuce, Rum takan murkushe kowace alamar bambancin ra'ayi game da koyaswoyin ta da umurnin ta. Takan hallaka masu ridda har da rubuce rubucen su. Ko sau daya mutum ya nuna shakka game da sahihancin koyaswar Rum, wannan kawai yakan sa a kashe mutumin, komi girma ko kankantar sa. Rum ta yi kokarin hallaka kowace shaidar muguntar ta. Ga masu bambancin ra'ayi. Majalisun ekklesiya sukan umurta cewa a kone litattafai da rubuce rubucen da suka kunshi labarin muguntar. Kafin a kirkiro buga littattafai, littattafai ba su da yawa, kuma ba sa cikin yanayin da za su yi dadin ajiya; don haka bai zama ma Rumawan da wahala su cika nufin su ba.

Ba a bar wata ekkelesiya da ke kalkashin Rum ta dade tana morar 'yancin addinin ba. Da zaran mulkin paparuma ya sami iko, nan da nan ya mika hannuwan sa don murkushe dukan wadanda suka ki bin umurnin sa, kuma daya bayan daya ekklesiyoyin suka yarda da mulkinsa.

A Birtaniya ainihin Kiristanci ya dade da kahuwa. Sa'an nan bisharan da mutanen Birtaniyan suka karba a karni na farko ba ta lalace da riddar Rum ba. Kirista da yawa masu gudun zalunci a Ingila sun sami mafaka a Scotland; daga nan aka kai gaskiyar a Ireland, kuma a dukan kasashen nan an karbi ainihin kiristacin da farin ciki.

Sa'an da Saxons suka shiga Birtaniya da yaki, kafirci ya yi nasara. Masu nasaran suka ki karban koyaswa daga bayin su, don haka aka atilasta Kirista suka gudu zuwa duwatsu da dazuka. Duk da haka hasken da aka boye na wani lokaci ya ci gaba yana haskakawa. A Scotland bayan shekaru dari, ya haskaka da hasken da ya kai kasashe masu nisa sosai. Daga Ireland, Columba da abokan aikin sa suka taso, kuma da suka tattaro masu-bi da ke warwatse a tsibirin Iona, sai suka mai da tsibirin cibiyar aikin bishararsu. Cikin wadannan masu wa'azi akwai mai-kiyaye Assabbat na Littafi, ta haka kuma aka shiga da gaskiyan nan cikin mutanen. Aka bude makaranta a Iona, daga nan kuwa masu bishara suka dinga zuwa Scotland da Ingila da Jamus, da Switzerland, har da Italiya ma.

Amma Rum ta sa ma Birtaniya ido, ta kuma kudurta kawo ta kalkashi ikonta. Cikin karni na shida, masu wa'azin ta suka shiga tubar da kafiran Saxony. Barbarians suka karbe su da marmari, suka kuma zuga dubban mutane suka rungumi koyaswar Rum. Sa'an da aikin ya ci gaba, shugabannin ekklesiyar Rum da tubabbun su suka sadu da Kiristan nan na ainihi. Bambanci tsakanin su ya bayana. Kiristan ainihin nan masu kamewa ne, da tawali'u da ruhaniya a hali da koyaswa da tsabi'a, alhali wadacan sun nuna camfi da girman kai da bankaman nan nasu. Dan sakon Rum ya ce ma ekklesiyoyin Kiristan nan su yarda da mulki da daukakar paparuma. Kiristan Birtaniyan nan suka amsa a natse cewa suna marmari su kaunaci dukan mutane, amma paparuma bai cancanci daukaka cikin ekklesiya ba, kuma za su yi masa ban girma irin wanda ake yi ma kowane mai-bin Kristi ne kadai. Aka yi kokari akai akai domin su yi biyayya ga Rum; amma Kiristan nan talakawa masu tawali'u, da suka yi mamakin girman kan yan sakon ekklesiyar, suka nace cewa basu san wani mai-gida ba ban da Kristi. Yanzu kuma aka bayana ainihin ruhun mulkin paparuma. Sai ya ce: "Idan baza ku karbi yan-uwa da ke kawo maku slama ba za ku karbi magabta da za su kawo maku yaki. Idan ba za ku hada kai da mu wajen nuna ma Saxons hanyar rayuwa ba, za ku karbi mutuwa daga wurin su." Wannan ba barazanar banza ba ce. An yi anfani da yaki da dabara, da rudi a kan shaidun nan na addini na Littafi, har sai da aka hallaka ekklesiyoyin Birtaniya ko kuma aka tilasta su yarda da ikon paparuma.

A kasashen da Rum ba ta da hurumi, an iske rukunonin Kirista da lalatar ekklesiyar Rum bai shafe su ba, har tsawon daruruwan shekaru. Kafirci dai ya kewaye su har kurakuran sa sun shafe su; amma suka ci gaba suna daukan Littafi a matsayin ma'auni tilo na bangaskiya, suka kuma rike yawancin koyaswoyin Littafin. Kiristan nan sun gaskata dawamar dokar Allah suka kuma kiyaye Assabbat na doka ta hudu. Ekklesiyoyin da suka rike wannan bangaskiya da ayuka sun kasance a Afirka ta Tsakiya da cikin Armeniyawan Asia ne.

Amma Waldensiyawa sun yi fice wajen tsayayya da mulkin paparuma. A kasar da paparuma ya dasa kursiyin sa, nan ne karyarsa da lalacewarsa suka gamu da matukar tsayayya. Ekklesiyoyin Piedmont sun rike yancinsu har daruruwan shekaru; amma lokaci ya kai daga bisani da Rum tan nace cewa su ba da kai. Daga nan bayan sun ki na wani lokaci, shuabannin ekklesiyoyin nan suka yarda da wannan mulkin da duniya ke biyayya da shi. Amma akwai dai wadanda suka ki yarda da ikon paparuma, sun kudurta za su rike biyayar su ga Allah, su kuma kiyaye tsabtar ibadar su da saukin kan ta. Rabuwa fa ta shigo. Wadanda suka manne ma bangaskiya ta farko suka janye; wadansu suka kaura daga kasar su a Alps, suka daga tutar gaskiya a kasashen waje; wadansu suka koma cikin koguna da kewayen tsaunuka, inda suka kiyaye yancin su na sujada ga Allah. Bangaskiyan nan da Waldensiyawan nan suka rike, suka kuma koyar har daruruwan shekaru ya bambanta da koyaswoyin karyan nan na Rum. Bangaskiyar addinin su ta kafu kan rubutaciyar maganar Allah ne. Amma wadannan Kiristan a inda suka buya daga sauran duniya, suna noman inabi da rike dabbobi ne, tukuna basu sami gaskiyar, sabanin bidi'ar ekklesiyan nan mai-

ridda ba. Gaskiyar su ba sabuwa suka karba ba. Sun gaji addinin nan daga ubanin su ne. Suka yi tsayayya domin imanin ekklesiyar manzani, “imani wanda aka bayas ga tsarkaka so daya dungum” Yahuda 3. “Eklesiyar cikin jeji,” amma ba mai girman kai din nan da aka kafa a Rum ba, ita ce ainihin ekklesiyar Kristi, mai lura da muhimman gaskiya da Allah Ya ba mutanen Sa, su ba duniya.

Daya daga manyan dalilan rabuwar ekklesiyar gaskiya da Rum shi ne kiyayyar Rum ga Assabbat na Littafi. Kamar yadda annabci ya ce, mulkin paparuma ya yar da gaskiya har kasa. Aka tattake dokar Allah cikin kura, yayin da aka daukaka al’adun mutane. Tun da farko aka tilasta ekklesiyoyi da ke kalkashin paparuma su girmama Lahadi a matsayin rana mai-trsarki. Cikin yawan camfi da kuskure, yawanci, har da ainihin mutanen Allah, suka rikice ta yadda, yayin da suke kiyaye Assabbat, suka dena aiki ran Lahadi. Amma wannan bai gamsar da shugabannin ekklesiyar Rum ba. Suka umurta cewa a tsarkake Lahadi a kuma bata Assabbat; suka kuma yi soka mai-karfi game da masu-kiyaye Assabbat din. Ta wurin tserewa daga ikon Rum ne kadai aka iya yin biyayya ga dokar Allah cikin salama.

Waldensiyawa suna cikin mutanen farko a Turai da suka sami Littafi da aka juya zuwa harshensu. Daruruwan shekaru kafin zamanin gyare gyaren nan, sun mallaki Littafi rubutaciya cikin harshensu. Suka kasance da gaskiya tsaba, wannan kuma ya sa suka zama abin kiyaya da zalunci musamman. Suka sanar cewa ekklesiyar Rum ce Babila mai-riddan nan na Ruya ta Yohanna, kuma a bakin ran su suka tashi tsaye domin tsayayya da kurakuran ta. Yayin da sakamakon matsin zalunci wadansu suka sassauta imanin su, sannu a hankali kuma suka rabu da muhimman kaidodin sa, wadansu kuwa sun manne ma gaskiya. Cikin sararakin duhu da ridda akwai Waldensiyawa da suka ki daukakar Rum, suka ki bautar sifofi cewa bautar gumaka ne, suka kuma kiyaye Assabbat na gaskiya. Cikin kiyaya mafi-muni sun rike imaninsu. Ko da shi ke an zalunce su, sun tsaya da gaske ma maganar Allah da daukakar Sa.

A cikin kogunan duwatsu, Waldnesiyawa sun sami wurin buya. Nan fa aka rike hasken gaskiya cikin duhun nan da ake kira a Sararakin Tsakiya. Nan kuma shaidun gaskiya suka kwashe dubban shekaru suna rike da imanin zamanin da.

Allah Ya rigaya Ya tanada ma mutanen Sa haikali mai-daraja ainun wanda ya dace da muhimman gaskiya da ya ba su amana. Ga korarrun amintattun nan, duwatsu alamu ne na adalcin Yahweh. Suka nuna ma yayansu tsayin duwatsun nan kewaye da su suna ba su labarin Shi wanda ba Ya sakewa, wanda maganar Sa tana dawama kamar duwatsun. Allah Ya kafa duwatsun, Ya kuma tokare su da karfi; ba mai iya gusar da su sai Shi Mai-cikaken iko. Haka kuma Ya kafa dokar Sa, harsashen gwamnatinsa na sama da na duniya. Hannun mutum zai iya samun yan-uwan sa mutane ya kuma hallaka rayukan su; amma wannan hannun ba zai iya tumbuke duwatsun daga gindin su, ya jefa su cikin teku ba, kamar yadda ba za su iya canza dokar Allah ba ko daya, ko kuma su share alkawalinsa daya ga masu

aikata nufinsa ba. Cikin amincinsu ga dokar Allah, ya kamata bayin Allah su tsaya da karfi kamar tuddai da ba sa sakewa.

Duwatsun da suka kewaye garin su shaida ce kullum na ikon halita na Allah, tabbaci kuma na tsaronsa da kulawansa. Matafiyan nan suka kawunaci al'ammun nan na kasancewar Allah tare da su. Basu dinga gunaguni don wahalolin su ba; a tsakanin duwatsun nan ba basu ji kamar su kadai ne ba. Suka gode ma Allah domin Ya tanada masu mafaka daga fushi da zaluncin mutane. Sun yi murna don yancin su na sujada gare Shi. Sau da yawa idan magabtansu suka kai masu hari, duwatsun ne sukan zama kariyarsu. Daga tsaunukan nan sukan raira yabon Allah, mayakan Rum kuma basu iya tsayar da wakokin godiyarsu ba.

Ibadar masu-bin Kristi din nan mai tsabta ce, mai-sauki kuma. Sun girmama kaidodin gaskiya fiye da gidaje da filaye, abokanai, yan-uwa da su kan su ma. Suka yi kokari wajen koya ma matasa kaidodin nan. Akan koya ma yara nassosin tun suna kanana, ana kuma koya masu su daukaka dokar Allah. Littafi bai yi yawa ba a hannun mutane, don haka aka rika hadace nassosi akai kawai. Mutane da yawa sukan iya maimaita dogayen nassosin Tsohon Alkawali da na Sabon Alkawali daga kai, ba sai sun karanta ba. Aka danganta Allah da kyawawan ababan da Ya halita da kuma albarkun Sa na yau da kullum. Kananan yara suka koyi yin godiya ga Allah Mai-bayar da kowane alheri da kowane jin dadi.

Iyaye sun kaunaci yayan su da hikima ta yadda basu bata su da jin dadi ba. Gabansu akwai rayuwar tsanani da wahala, ko mutuwa ma. Aka koya masu tun suna yara su jimre wahala, su yi biyayya, amma kuma su yi tunani su kuma aikata don kansu. Tun da wuri aka koya masu daukan nauyin kansu, yin hankali da maganarsu, su kuma gane hikimar yin shuru. Idan magabtansu suka ji mumunan kalma daya kawai daga wurinsu, wannan zai iya jawo hallaka ga ran mai-maganar, har da rayukan daruruwan yan-uwan sa, gama kamar yadda dabbobi sukan yi farautar naman da za su ci, haka abokan gaban gaskiya suka rika neman wadanda suka yi yunkurin rike yancin addini.

Walsensiyawa sun sadakar da ci gaban su na duniya, sabo da gaskiya da naciya cikin hakuri kuma, suka rika fama don neman abincinsu, suka rayar da kowane wurin da za a iya noma a duwatsun; aka so kowane kwari da gefen dutse ya zama gona mai ba da anfani. Tsimi da hakuri suka kasance ilimin da yaran suka samu a matsayin abin gadon su kadai. An koya masu cewa Allah Ya shirya cewa rayuwa ta zama abin koyo ne, kuma za a iya biyan bukatunsu ta wurin aikin kansu ne da hangen gabansu, da kulawansu, da bangaskiyar kansu kuma. Koyaswan nan mai wahala ne da gajiyarwa, amma kuma mai-kyau ne, wanda mutum da ke bukata, makarantar da Allah ya tanada don koyaswar mutum da ci gabansa. Yayin da ake koya ma matasa jimre wahala, ba a manta zancen inganta tunanin su ba. Aka koya masu cewa kowace baiwarsu ta Allah ce, kuma ya kamata a inganta ta don yi masa hidima.

Ekklesiyoyin Waldensiyawan nan, cikin tsabta da saukin kansu, sun yi kama da ekklesiyar zamanin manzani. Da suka ki daukakar paparuma, sai suka rike Littafi cewa shi kadai ne kaida mara-aibi. Pasocinsu, ba kamar priestocin Rum masu son girma ba, suka bi kwatancin Mai-gidansu wanda "Ya zo ba domin a yi masa bauta ba, amma domin shi bauta ma wadansu." Suka ciyar da garken Allah, suna kai su makiyaya mai-danya da mabulbulan ruwayen maganarsa Mai-tsarki. Ba kamar masu-shagalin nan da girman kai, masu-tattaruwa a manyan majami'u ba, sun rika sujada a kalkashin inuwar duwatsun Alps, ko kuma a lokacin hadari sukan rika taruwa a kogunan duwatsun ne don jin maganar gaskiya ta bakin bayin Kristi. Ban da wa'azin bishara, pastocin sun rika ziyarar marasa lafiya, suna koyar da yara, da gargadi ga wadanda suka yi kuskure, da yin kokarin sasanta masu-sabani da juna, suna karfafa jituwa da kaunar yan-uwa. Lokacin salama sukan dogara ga baye bayen mutane ne don rayuwa; amma kamar Bulus mai-yin tentuna, kowa ya koyi sana'an da yakan dogara da ita in ta kama.

Matasa sun sami koyarwa daga pastocinsu. Yayin da aka mai da hankali ga fannonin sani iri dabam dabam, an mai da Littafi abin nazari mafi-muhummanci. Aka hadace bishara ta Matta da ta Yohanna, da kuma da yawa cikin wasikun Bulus. An kuma yi anfani da wadansu cikin matasan wajen yin kofen nassosin. Wadansu rubuce rubucen sun kunshi dukan Littafi, wadansu kuma zababbun nassosi ne kawai da akan hada da fassara ta bakin wadanda suka iya bayyana Littafin. Ta haka aka kawo tamanin gaskiya da masu neman daukaka kansu fiye da Allah suka dade suna boyewa.

Ta wurin kokari cikin hakuri, wani lokaci ma cikin duhun koguna, da hasken tocilan, aka rubuta nassosi masu-tsarki, aya bayan aya, sura bayan sura. Ta haka aikin ya ci gaba, bayyanannen nufin Allah kuma yana haskakawa kamar zinariya mara aibi; ya kara haske da karfi ma sabo da jarabawa da aka sha dominsa, wanda masu yin aikin ne kadai ke iya ganewa. Malaiku daga sama sun kewaye amintattun ma'aikatan nan.

Shaitan ya bukaci priests da shugabannin su su bizne maganar gaskiya kalkashin karmomin kuskure, da ridda, da camfi, amma ta hanya mai-ban mamaki, an kiyaye shi ban da aibi duk tsawon sararakin duhu. Ba shi da hatimin mutum, sai amincewar Allah.

Mutane ba sa gajiya da kokarin su na duhunta bayananiyar ma'anar maganar Allah, da kuma neman sa nassosi su saba ma juna, amma kamar jirgin kan teku, maganar Allah takan fi karfin kowace guguwar da ke so ta rushe ta. Yadda ma'adini yakan kasance da jerin zinariya da azurfa a boye a kalkashin kasa, domin duk mai-so dole sai ya tona da karfi, haka ne Littafi yana da tamanin gaskiya wanda ake bayana ma wanda ya nema ta wurin naciya cikin addu'a da tawali'u kadai. Allah Ya ayyana Littafi ya zama littafin koyaswa ne ga dukan yan Adam, yara da matasa da manya, a kuma yi nazarin sa kowane lokaci. Ya ba mutane maganarsa domin ta bayana Shi. Kowace sabuwar gaskiya da aka fahimta, sabuwar bayani ce ta halin Mai-ba da ita. Nazarin Littafi ne Allah Ya kadara ya zama hanyar jawo

mutane zuwa ga Mahalicinsu, a kuma ba su Karin sanin nufinsa. Hanyar sadarwan ken nan tsakanin Allah da mutum.

Yayin da Waldensiyawa suka mai da tsoron Ubangiji mafarin ilimi, basu rufe ido ga muhimmancin sanin duniya ba, sanin mutane da na ruhaniya, inganta tunani da basira kuma. Daga makarantunsu a cikin duwatsun aka tura wadansu matasa makarantu a biranen Faransa ko Italiya, inda akwai fili mai fadi don karantarwa da tunani da kulawa fiye da na Alps. Matasan da aka aika sun fuskanci jaraba, sun ga mugunta, sun sadu da wakilan Shaitan wadanda suka matsa masu su karbi ridda da rudi mafi-muni. Amma ilimin su daga yaranta irin wanda ya rigaya ya shirya su don jarabobin nan ne.

A makarantun da suka je, basu yi abokan shawara da kowa ba. An dinka masu rigunansu ta yadda za su iya boye rubutatun maganar Allah a ciki. Sun rika tafiya da maganan nan duk inda za su, ba tare da tayar da zato ba, a hankali kuma sukan ajiye wadansu rubutattun nassosin inda masu-alamar son gaskiya za su gani. Tun yarantakan su an hori matasan Waldensiyawan nan da wannan manufan ne; sun gane aikinsu,suka kuma yi shi da aminci. An sami masu-tuba zuwa imani na gaskiya a makaranun nan, kuma sau da yawa kaidodin imanin nan sukan mamaye dukan makarantar; duk da haka shugabannin ekklesiyar Rum ba su iya gane tushen kaidodin nan ba, komi binciken su.

Ruhun Kristi ruhun shelar ishara ne. Wanda ya tuba yakan fara so ya ja wadansu zuwa wurin Mai-ceton ne su ma. Irin ruhun Waldesiyawan ke nan. Sun ji a jikin su kawai cewa Allah Ya bida daga gare su abin da ya wuci kiyaye gaskiya cikin tsarkin ta kawai a cikin ekklesiyoyin su; cewa nawaya ta rataya a kan su, su haskaka haskensu ga wadanda ke duhu; ta wurin ikon maganar Allah suka so su karya bautan da Rum ta kafa. An horar da pastocin Waldeniyawan, aka kuma bukaci duk mai-son aikin pasto ya sami horaswa na mai-bishara. Kowane dayansu ya kan yi aikin shekara uku yana lura da wata ekklesiya a wani wuri a gida. Wannan aiki da ya bukaci sadakarwa, gabatarwa mai-dacewa ne zuwa rayuwar pasto a wancan zamani mawuyaci, matasan da aka shafe su pastoci su ga ba rayuwa ce ta wadata da daukaka ba, amma rayuwa ta wahala da hatsari, mai yiwuwa ma har da mutuwa. Masu bisharan suka rika tafiya su biyu biyu, yadda Yesu Ya aiki almajiransa. Akan hada kowane matashi da wani dattijo mai-kwarewa mai yi ma matashin jagoranci da horaswa, aka kuma bukaci matashin ya yi biyayya. Ba kowane lokaci ne sukan kasance tare ba, amma sukan dinga saduwa don addu'a da shawara, ta haka kuma suka rika karfafa juna cikin imanin.

Da a ce sun bayyana manufar aikinsu, lallai da an hana aikin, sabo da haka suka boye ainihin manufarsu. Kowane pasto ya iya wata sana'a ko aiki, suka kuma yi aikin su da sunan sana'a. Yawanci sukan zabi jari ne ko talla. "Suka sayar da yaduna ko kayan ado, ko dai wadansu ababa wadanda ba a cika samu ba sai a kasuwanni masu nisa, aka kuwa marabce su a matsayin yan kasuwa inda da an ki su a matsayin sun na masu-wa'azi." Kullum sukan bidi hikima daga wurin Allah, domin su iya gabatar da tamanin nan da ya fi zinariya ko lu'alu'ai. A boye sun rika tafiya da Littafi ko kuma nassosinsa, kuma sa'an da

dama ta samu, sukan jawo hankulan abokan cinikinsu ga Littafin. Sau da yawa ta wurin haka akan jawo hanlkali zuwa maganar Allah, akan kuma bar masu Littafin ko nassosin idan sun nuna suna so.

Aikin masu bisharan nan ya fara a wuraren da ke kewaye da duwatsun da suke da mazamnin su ne, amma ya yadu daga wurin. Da kafafun su ba takalma, da kuma tufafi tsofofi sabo da yawan tafiya, kaman na Mai-gidansu, suka dinga ratsawa ta manyan birane, suka shiga kasashe masu-nisa. Ko ina sun watsa irin. Ekklesiyoyi suka taso duk inda suka wuce, jinin amintattu da aka kashe kuma ya dinga ba da shaidar gaskiyar. Ranar Allah za ta bayana rayuka da yawa da amintattun nan suka jawo. A boye, shuru kuma, maganar Allah ta dinga shiga cikin Kirista, ana kuma karban ta da murna a gidaje da zukatan mutane.

Ga Waldaelsiyawan, Littafi ba labarin abin da Allah Ya yi da mutane ne a da can kawai, da bayanin aikin da ya rataya a kafadar su yanzu ba, amma ya hada har da bayanin matsaloli da daukaka na nan gaba. Sun gaskata cewa karshen komi ya kusa, kuma yayin da suke nazarin Littafi cikin addu'a da hawaye, maganar sa ta burge su sosai, suka kuma kara ganin aikin da ya rataya a kafadar su na sanar ma sauran mutane gaskiyar Littafi mai-kawo ceto. Suka ga shirin ceto a bayyane sarai cikin Littafin, suka kuma sami ta'aziya da bege da salama cikin ba da gaskiya ga Yesu. Yayin da hasken ya kara masu ganewa, ya kuma faranta masu zukata, suka yi marmarin isar da hasken nan ga wadanda ke cikin duhun kuskuren ekklesiyar paparuma.

Sun ga cewa kalkashin shugabancin paparuma mutane da yawa suna faman neman yafewa ta wurin azabtar da jikunansu, sabo da zunubin su. Da shi ke an koya masu dogara ga kyawawan ayukan su don samun ceto, sai suka rika duban kansu, suna tunanin yanayinsu na zunubi, suna ganin kansu fuska da fuska da fushin Allah, suna azabar da ruhu da jiki, duk da haka ba magani. Ta haka ne koyaswoyin Rum suka daddaura ruhaniyar mutane. Dubbai suka rabu da kasashe da yan-uwa, suka yi rayuwar su cikin kulle na covent. Ta wurin azumi akai akai da bulala na zalunci, da kwana-gani, da durkusawa na sa'o'i da yawa cikin sanyi a kan duwatsu, ta wurin tafiya mai-nisan gaske, ta wurin wahalar da jiki ta hanyar wulakanci da tsanani mai-ban tsoro, dubbai suka nemi damar samun salamar lamirinsu, amma a banza. Duk da damuwa game da zunubin su da tsoron fushin Allah, da yawa suka ci gaba da shan wahalar su, har sai da suka mutu, ba kuma wanda ya ba su bege.

Waldensiyawan su yi marmarin mika ma mutanen nan gurasar rai, su bude masu sakonin salama cikin alkawuran Allah, su kuma nuna masu cewa Kristi ne kadai begen cetonsu. Suka nuna cewa koyaswar cewa wai kyawawan ayuka za su iya yin kafara don ketarewar dokar Allah karya ce. Dogara ga kokarin mutum ya kan hana ganin kaunar Kristi mara-iyaka. Yesu Ya mutu a matsayin hadaya sabo da mutum, domin yan Adam fadaddu ba za su iya yin komi don gamsar da Allah ba. Anfanin giciyewar Mai-ceto da tashinsa su ne tushen imanin Kirista. Dogarar mutum ga Kristi tabbas ne, kuma dole mannewar sa da

Kristi ta zama kamar ta hannu ko kafa da sauran jiki, ko kuma mannewar reshe da kuringar anab.

Koyaswoyin su paparuma da priestoci sun sa mutane suka rika gani kamar halin Kristi zalunci ne da bakin ciki, hali mara-kyau. Suka nuna kamar Mai-ceton ba ya tausaya ma dan Adam, ta yadda har ya zama dole sai an nemi tsarkaka su shiga tsakani. Wadanda maganar Allah ta rigaya ta wayar masu da kai sun yi marmarin nuna ma mutanen nan cewa Yesu Mai-ceton su mai-tausayi ne da kauna, kuma yana tsaye, hannuwansa a mike, yana gayyatar kowa ya zo wurinsa da nauyin zunubinsa, da damuwarsa, da gajiyarsa. Sun yi marmarin warware matsalolin da Shaitan ya tara ma mutane domin kada su ga alkawuran har su zo kai tsaye wurin Allah, suna furta zunuban su, suna kuma samun gafara da salama.

Da marmari sosai Waldensiyawan nan masu wa'azin bishara suka bayana ma duk mai-tambaya gaskiyar bisharar. A hankali mai-wa'azin ya kan fitar da rubutacen nassin. Farin cikin shi ne ya ba da bege ga mai-lamiri wanda zunubi ya buga shi, wanda yana ganin Allah kamar mai-ramuwa ne kawai, wanda kullum yana jira ne kawai Ya zartas da hukumci. Da harshen tausayi, idon sa cike da hawaye, yawancin lokaci a durkushe ma, mai-bisharan yakan bude ma mutanen alkawuran da ke bayana begen da mai-zunubi ke da shi kadai. Ta haka hasken gaskiyan ya shiga tunanin mutane da yawa, ya kawar da girgijen duhu, har sai da ranar adalci ta haskaka da warkarwa cikin haskensa. Sau da yawa akan karanta wani fannin Littafi akai akai, mai-ji kuma ya rika cewa a sake maimaitawa, kamar yana so ya tabbatar ma kansa cewa ya ji da kyau. Musamman an rika cewa a maimaita kalmomin nan: "Jinin Yesu Dan Sa yana tsarkake mu kuma daga zunubi duka." Yohanna I, 1:7. "Kuma kamar yadda Musa ya ta da maciji bisa cikin jeji, hakanan kuma dole za a ta da Dan mutum bisa, domin dukan wanda yana ba da gaskiya shi sami rai na har abada a chikinsa." Yohanna 3:14,15.

Da yawa basu yarda da rudin Rum ba. Suka ga rashin anfanin aikin tsakanci da aka ce mutane ko malaiku ke yi a madadin mai-zunubi. Yayin da hasken gaskiya ya haskaka tunanin su, suka ta da murya da murna suka ce: "Kristi ne priest di na, jinin Sa ne hadaya ta; bagadin Sa ne wurin tuba na." Suka sallamar da kansu gaba daya ga aikin Yesu, suna maimaita kalaman nan cewa: "Ba shi kwa yiwuwa a gamshe shi sai tare da bangaskiya." Ibraniyawa 11:6. "Babu wani suna kalkasin sama, da aka bayas wurin mutane, inda ya isa mu tsira." Ayukan 4:12.

Tabbacin kaunar Mai-ceto ya zama ma wadansu wulakantattun mutanen nan da wuya su gane. Saukin da wannan ya kawo mai-yawa ne sosai, aka haska masu hasken nan mai-yawa, har suka ji kamar ana kai su sama ke nan. Suka sa hannun su cikin hannun Dutsen Sararraki. Dukan tsoron mutuwa an kawar. Yanzu ma suka so kurkuku, idan har ta wurin wannan za su daukaka sunan Mai-fansarsu.

A boye aka rika kawo maganar Allah ana karantawa, wani lokaci don mutum daya ma, wani lokaci don wata kingiyar mutane kalilan da ke begen samun haske da gaskiya. Sau da yawa akan kwana ana karatun nan sabo da mamaki da sha'awar masu ji, har ma sau da yawa akan roki mai-karatun ya dakata tukuna, har sai an gama fahimtar tarihin ceton. Sau da yawa kuma akan ji kalmomi kamar: "Ko Allah zai karbi bayaswa ta? Za ya gafara mani kuwa?" Sai a karanta amsar cewa: "Ku zo gareni dukanku da ku ke wahala, masu nauyin kaya kuma, ni kwa in ba ku hutawa." Matta 11:28.

Bangaskiya takan amice da alkawalin, akan kuma ji amsa cewa: "Ba damuwar tafiya kuma, ba tafiya mai-wahala zuwa wurare masu-tsarki. Zan iya zuwa wurin Yesu yadda ni ke, mai-zunubi, mara tsarki kuma, kuma ba zai ki addu'ar tuba ta ba. 'An gafarta zunuban ka' nawa, har nawa ma za a gafarta!"

Farin ciki yakan cika zuciya, akan kuma girmama sunan Yesu ta wurin yabo da godiya. Wadannan masu-murnan sukan koma gidajen su su bayana haske, suna ba kowa labarin abin da ya faru da su; cewa sun sami Hanyar gaskiya, mai-rai kuma. Akwai iko da ba a saba da shi ba, cikin maganar Littafi da ke zuwa kai tsaye cikin zukatan wadanda ke begen samun gasiyar. Muryan Allah ne kuma yakan taba zukatan dukan wadanda suka ji.

Dan sako na gaskiya yakan tafi abinsa; amma tawali'unsa, gaskiyarsa, himmarsa da kwazonsa sukan zama abin labari. Lokuta da dama masu jinsa ba sa tambayan inda ya fito da inda za shi. Da farko sukan cika da mamaki, daga baya kuma sukan cika da murna da godiya har ma ba sa tunanin tambayan shi ababan nan. Sa'an da suka roke shi ya bi su zuwa gidajen su, yakan amsa cewa tilas ne ya ziyarci batattun tumakin garken. Su kan tambaya, Ko shi malaika ne daga sama?

Sau da yawa ba a sake ganin dan sakon nan kuma. Ya tafi wadansu kasashe kuma, ko kuma yana fama a wani kurkuku daba a sani ba ma, ko kuma kasusuwan sa suna shudewa a wurin da ya shaida kalmomin gaskiyan. Amma ba za a iya hallaka kalmomin da ya bari a baya ba. Suna aikin su a zukatan mutane; lokacin hukumci ne kadai za a san sakamakon.

Waldensiyawa masu wa'azin nan sun kai ma mulkin Shaitan hari ne, ikokin duhu kuma suka taso suna tsaro ba barci. Shaitan ya dinga lura da kowane yunkuri na ci gaba da gaskiyar, ya kuma tsoratar da wakilansa. Shugabannin ekklesiyar Rum suka ga hadari ga ekklesiyarsu daga aikin matafiyan nan. Idan aka bar hasken gaskiya ya ci gaba da haskakawa, zai share gizagizan kuskure ya kuma rinjayi mutane. Zai kai tunanin mutane wurin Allah kadai, ya kuma rushe daukakar Rum daga bisani.

Kasancewar mutnen nan masu rike imanin ekklesiyar farko shaida ce ta riddar Rum, kuma don haka suka janyo kiyayya da zalunci mafi tsanani. Kin sallamar Littafi da suka yi ma ya zama laifin da Rum ba ta iya yafewa ba. Ta dauki kudurin shafe su daga duniya. Lokacin nan ne aka fara yake yake mafi-muni kan mutanen Allah a gidajen su cikin

duwatsu. Aka tura masu masu-bincike, sau da yawa aka rika maimaita irin abin da Kayinu ya yi ma Habila.

Akai akai aka rika lalata gonakin su, aka kawas da gidajen su da majami'un su ta yadda inda da akwai gonaki masu-albarka, da gidajen jama'a da basu yi laifi ba, masu kwazon nema, ba abin da ya rage sai hamada. Kamar yadda dabba mai-barna yakan kara hasala in ya taba jini, haka fushin 'yan paparuma ya kara tsanani sabo da wahalolin masu-wa'azin nan. Aka hori masu wa'azin imani mai-tsarkin nan har ketaren duwatsun, aka yi farautar su cikin kwari inda suka buya, cikin manyan dazuzuka da tsaunuka kuma.

Ba a iya zargin kungiyan nan da wani hali na rashin kirki ba. Ko magabtan su ma sun ce mutanen nan masu salama ne marasa hayaniya, masu imani kuma. Babban laifin su shi ne cewa basu yarda su yi sujada ga Allah bisa ga nufin paparuma ba. Sabo da laifin nan kowane wulakanci da zagi da zalunci da mutane ko aljannu ke iya kirkirowa an yi masu.

A wani lokaci, sa'an da Rum ta yi niyyar rushe kungiyan nan da ta ki jini, paparuma ya kafa dokar da ta mai da su masu ridda da ya kamata a kashe su. Ba a zarge su da zaman banza ko rashin gaskiya ko tashin hankali ba, amma aka ce suna da kamanin imani da tsarkin da ke rudin "tumakin ainihin garken." Don haka paparuma ya umurta cewa "muguwar haramtaciyar kungiyar kangararrun nan," da suka "ki rantsewa cewa sun bar akidar su, sai a murkushe su kamar macizai masu dafi." Ko paparuma ya san zai sake saduwa da kalmomin nan nasa? Ko ya san cewa an rubuta su a litattafan sama, domin a nuna masa su a ranar shari'a? "Da shi ke kuka yi wannan ga guda daya a chikin wadannan yan-uwana," in ji Yesu, "ni kuka yi ma." Matta 25:40.

Dokan nan ta kirayi sukan membobin ekklesiya su shiga yaki da masu riddar. Ladar shiga mugun aikin nan it ace an "yafe masu dukan wahaloli da horo na ekklesiya, na kan su da na duka; ta yafe ma dukan wadanda suka shiga yakin kowace rantsuwa da suka taba yi; ta halarta masu duk wata gona ko fili ko gida da suka mallaka ba bisa doka ba; ta kuma yi alkawalin yafe zunuban dukan wanda ya kashe mai-ridda. Ta soke duk wata yarjejjeniya mai-anfani ga Walddensiyawa, ta umurci masu yi masu aiki a gida su rabu da su, ta hana kowa ba su kowane irin taimako, ta kuma ba kowa dama ya kwace dukiyarsu." Wannan ya bayana ainihin ruhun da ke aiki a boye. Rurin dragon ne, ba muryar Kristi ake ji a cikin dokar ba.

Shugabannin ekklesiyar Rum ba su yarda su daidaita halayen su da babban ma'aunin dokar Allah ba, amma suka kafa ma'aunin da ya gamshe su, suka kuma so kowa ya bi su domin haka Rum ta so. Aka aikata mugunta mafi-muni. Miyagun priestoci da paparuma sun yi aikin da Shaitan ya ba su. Babu jinkai a cikin su. Ruhu dayan da ya giciye Kristi ya kuma kashe manzanin, ruhun da ya kuma motsa Nero ya saba ma amintattu a zamanin sa, shi ne ya motsa a raba duniya da kamnatattu na Allah.

Zaluncin da aka yi ma masu tsoron Allahn nan, su sun jimre cikin hakuri da naciyar da ta girmama Mai-fansarsu. Duk da yakokin da aka yi da su, da kisan wulakanci da aka yi masu, sun ci gaba da aika masu-wa'azi su baza gaskiyan. Aka yi farautar su har mutuwa; duk da haka jininsu ya yi ma irin da aka shuka ban-ruwa, kuma bai kasa ba da 'ya'ya ba. Ta hakanan Waldensiyawan suka shaida Allah, har daruruwan shekaru kafin haihuwar Luther. A warwatse cikin kasashe dabam dabam suka shuka irin Canjin nan da ya fara a lokachin Wycliffe, ya habaka a zamanin Luther, za a kuma ci gaba da shi har karshen lokaci ta hanun wadanda ke shirye ma su sha wahala "sabili da maganar Allah da shaidar Yesu." Ruya 1:9.

Babi na 5— Tauraruwar Safɛ

Kafin Lokacin Juyin juye-hali, yakan yi wuya a ga Littafi Mai-tsarki, amma Allah bai bari a hallaka maganar sa gaba daya ba. Yakan wadatar da maganar rai kamar yadda yakan bude kofofin kurkuku domin kubutar da bayinsa. A kasashen Turai, Ruhun Allah ya rika motsa mutane suka dinga neman gaskiya kamar masu neman boyayen tamani. Suka rika nazarin Littafi Mai-tsarki da marmari ainun. Sun yarda su karbi haske, ko da me zai faru da su. Ko dashike basu ga kowane abu sarai-sarai ba, aka ba su ikon fahimtar koyaswoyin gaskiya da yawa da aka dade ana boyewa. A matsayin su na aikakkun Allah, suka yi dukufa wajen warware sarkokin kuskure da na camfe camfe, suna kira ga wadanda an dade ana takura masu, cewa su tashi su kwace yancin su.

Ba don Waldensiyawa ba kam, da masana harsuna ne kadai suke da Kalmar Allah; amma lokaci ya yi da za a juya maganar Allah a kuma kai ma mutanen kasashe daban dabam cikin yarurukan su. Lokacin duhu ya fara wucewa ga duniya, alamun wayewan gari kuma sun fara bayana a kasashe daban dabam.

Cikin karni na goma sha hudu, jagoran Juyin juye-hali ya taso a Ingila. John Wycliffe ne ya fara juyin juye-hali a cikin Kiristanci ko ina, ba a Ingila kadai ba. Tawayen da ya fara yi ma Rum ne ya bude gwagarmayar da ta kai ga yantarwar mutane da ekklesiyoyin da al'ummai.

Wycliffe ya sami isashen ilimi, kuma ya mai da tsoron Ubangiji mafarin ilimi. A makaranta an san shi da son addini da kuma baiwa iri iri ga kuma yawan ilimi. Don son ilimi, ya so ya koyi kowane fannin ilimi. Ya ilimantu ta fannin nazarin ussan ilimi, da kaidodin ekklesiya, da fannin doka, musamman dokar kasarsa. Muhinmincin horaswan nan da ya samu lokacin kuruciyarsa cikin gwagarmayarsa ya bayana can gaba. Sabo da kwarewarsa game da irin tunanin zamaninsa ne ya iya bayana kurakuran zamanin, tawurin sanin dokar kasa da ta ekklesiya kuma ya iya sa hannu cikin gwagwarmayar neman 'yancin dan adam da na addini. Yayin da ya iya anfani da makamai daga Kalmar Allah, ya kuma sami horaswar makaranta, ya kuwa gane dabarun masana. Karfin iyawansa da kuma yawa da zurfin saninsa sun sa abokansa da magabtansa ma suka rika bashi girma. Mabiyansa suka ji dadin ganin cewa jagoransu yana daga cikin manyan masanan kasarsu; magabtansa kuwa basu iya rena aikinsa na neman canji ko kuma su nuna wani gazawa ko jahilci daga wurin jagoran canjin ba.

Yayin da Wycliffe ke koleji, ya shiga nazarin Littafi sosai. A wancan zamanin da ba a rigaya an juya Littafi Mai-tsarki daga harsunan asalin ba, masu ilimi ne sukan sami sanin gaskiyar. Sabo da haka ilimin Wycliffe ya shirya shi domin aikin san a neman canji. Masana suka yi nazarin Maganar Allah suka, sami gaskiyar alherinsa a bayane. Suka rika baza gaskiyan da suka samu, wanda kuwa ya kai wadansu ga Maganar Rai.

Sa’anda aka jawo hankalin Wycliffe zuwa Littafi Mai-tsarki, ya shiga bincikensa da irin kwazon da ya sa shi ya kware a ilimin da ya samu a makaranta. Kafin nan, ya dinga samun wani marmarin da ilimin sa da koyarswar ekklesiya basu iya gamsarwa ba. A cikin maganar Allah, ya sami abin da ya dade yana nema bai samu ba. Nan ne ya ga shirin ceto a bayane ga kuma Kristi kadai a matsayin Matsakancin mutane. Ya ba da kansa ga bautar Kristi, ya kuma kudurta yin shelar kowace gaskiya da ya gano.

Kamar sauran masu neman canji da suka biyo bayan sa, Wycliffe da farkon aikin sa bai san inda aikin zai kai shi ba. Bai shirya kan sa gadan-gadan don hamayya da Rum ba. Amma dole ne rikon gaskiya ya kai shi ga magabtaka da karya. Duk sa’anda ya kara gane kuskeren paparuma, ya kan kara kwazo wajen bayana koyarswar Littafin. Ya ga cewa Rum ta rabu da maganar Allah, ta rungumi ala’adun mutane ba da tsoro ba, ya zargi priestoci da yin watsi da Littafin, ya kuma bidi cewa a dawo ma mutane da Littafin, a kuma mayar da muhinmincin sa ga ekklesiya. Shi kwararren mallami ne, shahararen mai-wa’azi, kuma rayuwar sa ta yau da kullum ta je daidai da wa’azinsa. Saninsa na Littafin da karfin koyaswarsa da rayuwarsa mai-kyau da karfin halinsa, sun kawo masa bangirma da amincewar mutane. Mutane da yawa basu gamsu da addininsu ba kuma, domin sun ga zunubin da ya mamaye ekklesiyar Rum, suka cika da fushi sa’anda suka ga cewa Wycliffe yana samun karbuwa fiye da su.

Wycliffe mai-iya gane kuskure ne da sauri, ya kuma kushe kurakuran Rum ba tsoro. Yayin da yake aikin lura da ruhaniyar sarki, ya dauki mataki da karfin hali na hana sarkin Ingila biyan gandu ma paparuma, ya kuma nuna cewa ikon da paparuma ya ba kansa bisa shugabannin kasa ya saba ma hankali da Littaffin. Ababan da paparuma ya nema sun ta da haushi sosai, koyaswoyin Wycliffe kuma suka yi tasiri sosai ga manyan masanan kasar. Sarki da fadawansa suka hada kai, suka ki zancen nan na ikon paparuma bisa sarakuna da kuma cewa sarki ya rika biynasa gandu. Ta haka aka rage darajar paparuma a Ingila.

Wani abin da Wycliffe ya ki akai shi ne zancen kungiyoyin kebabbun membobin ekklesiya da al’adar yan bara da ba a yarda su mallaki dukiya ba. Masu baran nan sun mamaye Ingila, suka kaskantar da kasar suka kuma rage ci gabanta. Kwazo, ilimi, da tarbiyya duka suka sami damuwa. Rayuwar yan kungiyoyin na zaman banza da bara, ba wai ya rika tsotse dukiyar mutane kawai ba, amma ya sa aka rena masu yin aiki mai-anfani kuma. Matasa suka rasa himmar su, suka zama malalata. Ta wurin tasirin yan baran, da yawa suka shiga rayuwar kadaici da zaman zuhudu, ba aikin komi, ba da yardar iyayensu ba, ba kuma da saninsu ba, sabanin umurnin iyayen ma. Wani uban ekklesiyar Rum na zamanin da, don nuna fifikon zaman zuhudu bisa kaunar yara ga iyaye, ya ce “ ko da babanka zai kwanta a gaban kofarka, yana kuka yana makoki, mamanka kuma ta nuna jikin da ya haife ka da nonon da ya rene ka, ka tabbata ka tattake su da sawayenka, ka kuma mike kai tsaye zuwa wurin Kristi” Ta wurin wannan “mugunta na rashin mutunci,” yadda Luther ya bayana abin nan, “wanda ya fi kama da kerkeci da azalumi ne, ba Kiristi da

mutum ba," aka taurara zukatan yara sabanin iyayensu. Haka shugabanin mulkin paparuma suka yi, kamar Farisawa na da, suka wofinta dokar Allah ta wurin al'adarsu. Ta wurin wannan aka warwatsar da iyalai, aka kuma raba iyaye da yayansu, maza da mata.

Har daliban jami'o'i ma an rude su ta wurin karyan shugabannin addini, har aka sa suka shiga kungiyoyin nan. Da yawa daga baya sun tuba da daukan wannan mataki, ganin cewa sun bata rayuwarsu, suka kuma jawo ma iyayensu bakin ciki, amma da zaran sun shiga tarkon, basu iya samun yancinsu ba kuma. Iyaye da yawa don tsoron tasirin yan zuhudun, suka ki kai yaransu jami'a. Yawan dalibai da ke zuwa jami'a sai ya ragu sosai.Makarantu suka lalace, jahilci kuma ya karu.

Paparuma ya rigaya ya ba yan zuhudun nan ikon sauraron furta laifukan mutane tare da yi masu gafara. Wannan ya jawo mugunta sosai. Domin kara ma kansu riba, masu ba da gafaran sun mai da gafara araha, ta yadda kowane irin mai-laifi yakan zo wurinsu, sabo da haka kuwa munanan laiuka suka karu. Aka bar mataulata da marasa lafiya cikin wahala, alhali baye-bayen da ya kamata su magance damuwarsu, yan zuhudu sun karbe, ta wurin rokon sadaka har da barazana ma, aka zargi wadanda basu ba da sadakar ba da rashin imani. Duk da cewa sun ce su matalauta ne, wadatar yan zuhudun nan ya dinga karuwa, manyan gidajensu da kyawawan teburansu sun kara nuna talaucin al'ummar. Yayin da suke kashe lokacinsu cikin holewa da shakatawa a madadin su kan su, suka rika aikan jahilai wadanda sun iya maimaita labaru, da tatsuniya, da ba'an da suka ji ne kadai, domin a ba mutane dariya kawai. Duk da haka 'yan zuhudun sun ci gaba da rike jama'a da yawa, suka nuna masu cewa iyakar abin da addini ke bukata shi ne a yarda da daukakar paparuma, a girmama tsarkakansa, a kuma rika ba yan zuhudu kyautuka, kuma wai wannan ya isa ya samo masu wuri a sama.

Masana masu imani sun yi kokari a banza don kawo canji a kungiyoyin nan na 'yan zuhudu; amma Wycliffe, da ganewa mai-kyau, ya tinkari tushen zunubin ne, inda ya ce tsarin kansa na karya ne, kuma ya kamata a kau da shi. Aka fara shawara da bincike. Yayin da 'yan zuhudun suka shiga ko ina a kasar suna tallen gafarar paparuma, mutane da yawa suka yi shakkar yiwuwar sayen gafara da kurdi, suka tambaya ko ba wurin Allah ya kamata su bidi gafara ba, maimakon wurin paparuma. Da yawa suka yi mamakin kwadayin 'yan zuhudun, wadanda handamar su babu iyaka. "'Yan zuhudun Rum da priestocin ta", inji mutane, "suna cinye mu kamar ciwon daji. Dole Allah ya cece mu, im ba haka ba mutane za su hallaka." Domin su boye handamar su, 'yan zuhudun nan masu-bara, suka ce wai suna bin kwatancin Mai-ceto ne, cewa wai da kyautukan mutane ne aka taimaki Yesu da almajiransa.

Wannan ikirarin ya jawo masu cikas, domin ya sa mutane da yawa komawa Littafi domin su ga gaskiyan da kansu, abin da kuwa Rum bata so ba kenan. Tunanin mutane ya koma ga Tushen gaskiya, wanda shi ne ta so ta boye.

Wycliffe ya fara rubutu yana kuma wallafa majallu game da yan zuhudun, ba wai don yana neman jayayya da su ba, sai don jawo hankulan mutane ga koyaswoyin Littafin da kuma Tushen Littafin. Ya sanar da cewa ikon paparuma na yin gafara ko na cire mutum daga ekklesiya bai bambanta da na sauran priestocin ba, kuma cewa ba wanda za a iya cire shi daga ekklesiya ma ainihi, sai dai wanda ya rigaya ya kai kansa kalkashin hukuncin Allah. Babu wata hanyar sa da ta fi wannan kada mulkin paparuma wanda ya kama, ya kuma rike miliyoyin mutane.

Kuma, an sake kiran Wycliffe domin shi kare 'yancin sarkin Ingila daga fetsa da Rum ke yi masa, kuma da aka nada shi jakadan sarki, ya yi shekara biyu a Netherlands, yana shawarwari da kwamishinonin paparuma. Nan ya sami saduwa da masu aikin ekklisiya daga Faransa, da Italiya, da Spain, ya kuma samin damar duba bayan labulen, har ya sami sanin ababa da yawa da zamansa a Ingila kawai bai bar shi ya gani ba. Ya koyi ababan da za su taimake shi aiki nan gaba. Daga wakilan nan daga fadar paparuma ya gane ainihin hali da manufar mulkin ekklesiyar. Ya koma Ingila ya maimaita koyaswoyinsa na da a fili, da karin kwazo, yana cewa kiyashi, fadin rai, da rudu alloli ne na Rum.

Cikin daya daga rubuce rubucensa game da paparuma da masu tara masa dukiya y ace: "Daga kasar Rum suna janye rayuwar matalauta, da kuma dubban lambobi daga kurdin sarki duk shekara, sabo da hidimomin ekklesiya da ababan ruhaniya, wannan la'antaciyar ridda ce ta cinikin gafara. Kuma hakika ko da kasarmu tana da babban tudun zinariya, kuma ba wanda ke dibawa sai masu tattara ma priest din nan dan duninya, a hankali wata rana tudun nan zai kare dole; domin kullum yana daukan kurdi daga kasarmu, kuma ba ya mayar da komi sai la'anar Allah sabo da sayar da gafara da yake yi".

Jima kadan bayan ya koma Ingila, sarki ya nada Wycliffe shugaban Lutterworth. Wannan ya tabbatar da cewa sarki bai sami damuwa da maganarsa, kai a waye ba. Tasirin Wycliffe ya shafi ayukan fada, ya kuma taimaka wajen tsara imanin al'ummar.

Ba da jimawa ba paparuma ya fara jefa masa barazana, aka aika da dokokin har Ingila - zuwa jami'a, zuwa wurin sarki, zuwa wurin shugabannin ekklesiya kuma, duka ana umurtarsu su dauki matakan kawar da wannan mai-koyar da riddan maza maza. Kafin zuwan umurnin kuwa, bishop bishop din, cikin gaggawarsu, sun rigaya suka kira Wycliffe zuwa wurinsu don shar'anta shi. Amma biyu daga manyan yarimai mafi-iko a kasar suka bi shi zuwa wurin shari'ar; mutane kuma da suka kewaye wurin, suka kutsa ciki, wanda ya tsorata masu shari'ar har ya sa aka dakatar da shari'ar, aka bar shi ya tafi abinsa cikin salama. Jima kadan, Edward III, wanda cikin tsufarsa shugabannin ekklesiyar suka yi kokori su sa shi ya sami sabani da dan canjin, ya mutu, sai kuma wanda da yake kare Wycliffe ya zama mukaddashin sarkin kasar.

Amma isowar wasikun dokokin nan na papruma ya aza ma dukan Ingila umurni na dole cewa a kama a kuma jefa mai riddan nan cikin kurkuku. Ya bayana a fili cewa tilas

Wycliffe zai shiga hannun Rum, ba da jimawa ba. Amma Shi wanda Ya ce ma wani a zamanin da, “kada kaji tsoro…. Ni ne garkuwarka” (Farawa 15:1), ya sake mika hannunsa ya tsari bawansa. Mutuwa ta zo, ba kan mai-canjin ba, amma ga paparuma da ya umurta cewa a kashe shi. Gregory XI ya mutu, masu shari’an da suka taru don yi ma Wycliffe shari’a kuwa suka waste.

Ikon Allah ya sake ba da dama domin ci gaban canjin. Bayan mutuwar Gregory aka zabi paparuma guda biyu masu hamayya juna, kowane dayansu yana cewa ba ya kuskure, yanzu kuma suna cewa a yi masu biyaya. Kowane daya ya bukaci masu-bi su taimake shi yaki da dayan, yana bin bayan kiran nasa da la’ana mai-muni ga magabtansa, da kuma alkawuran ladar sama ga masu binsa. Wannan al’amari ya rage ikon mulkin paparuma sosai. Bangarorin biyu suna da dukan bukata don kai ma juna hari, Wycliffe kuma ya sami hutu na wani lokoci. La’ana da zagi sun rika firiya daga paparuma zuwa paparuma, aka kuwa zubar da jini sosai don kare ikirarinsu, masu sabani da juna. Laifuka da ababan ban kunya suka cika ekklesiya. Lokacin kuwa dan canjin nan, a parish nasa a Lutterworth, ya rika aiki cikin natsuwa don mai da hankulan mutane daga paparuman nan biyu zuwa wurin Yesu, Sarkin Salama.

Rabuwar, tare da rikici da lalacewan da ta jawo, sun shirya hanya domin canjin ta wurin nuna ma mutane har suka ga ainihin yadda mulkin paparuma yake. A wata majaila da Wycliffe ya buga mai-suna “On the Schism of Popes,” ya bukaci mutane su lura, su ga ko ba gaskiya ne priestocin nan biyu ke fadi game da juna, kowane dayansu yana ce da dayan dan hallaka ba? “Allah,” inji shi, “ba zai ci gaba barin magabcin ya ci gaba mulki cikin priest daya kadai a cikin su ba,…. Amma ya kawo rabuwa tsakanin su biyu din, domin mutane, a cikin sunan Kristi, su iya yin nasara bisa su biyu din cikin sauki.”

Wycliffe, kamar Mai-gidansa, ya yi shelar bishara ga matalauta. Dashike bai gamsu da yada hasken a kananan gidajensu a Lutterworth ba, ya shirya cewa za a kai bisharar ko ina a Ingila. Don cimma manufan nan, ya kafa kungiyar masu wa’azi, mutane masu-saukin kai, masu kwazo da suke kaunar gaskiya, kuma ba abin da suke so kamar watsa shi. Mutanen nan suka je ko ina, suna koyarwa a kasuwanni, a titunan manyan birane, da kuma cikin kauyuka. Suka nemi tsofofi, da marasa lafiya, da matalauta, suka kuma bude masu labari mai ba da murna, labarin alherin Allah.

A matsayinsa na shehun mallamin ilimin tauhidin Littafi a jami’ar Oxford, Wycliffe ya rika wa’azin maganar Allah a Jami’ar. Ya yi aminci wajen bayana gaskiyar ga dalibansa yadda har suka ba shi lakabin “likitan bishara”. Amma aikinsa mafi-muhimmanci shi ne juya Litaffi zuwa Turanci da ya yi. Cikin Littafinsa mai-suna “On the Truth and Meaning of Scripture,” ya nuna niyyar juya Littafi domin kowane mutum a Ingila ya karanta ayukan al’ajibin Allah cikin harshen da aka haife shi.

Amma kuma faraf daya, aikinsa ya tsaya. Ko dashike bai rigaya ya kai shekara sittin da haihuwa ba, yawan aiki, da karatu, da fitinar magabtansa, sun shafi karfinsa har suka sa shi ya tsufa. Sai wani mumunan ciwo ya kama shi. Labarin ya faranta zuciyar ‘yan zuhudu. Sun dauka cewa yanzu zai tuba sabo da muguntar da ya yi ma ekklesiya, suka je kusa da dakinsa domin su ji tubarsa. Wakilan kungiyoyi hudu na addadin, tare da jami’ar kasa su hudu, suka kewaye mutumin da suka zata zai mutu. Suku ce “kana da mutuwa a lebenka, bari kurakuranka su taba ka, ka janye a idonmu, dukan ababan da ka fada na batanci game da mu.” Dan Canji ya saurare su shuru; ya ce ma mai lura da shi ya daga shi a kan gadonsa, sa’annan ya kalle su yayin da suke jiran janyewar maganganunsa, da babban murya kuma ya ce, “Ba zan mutu ba, zan rayu, in kuma sake bayana miyagun ayukan ‘yan zuhudun.” Cikin mamaki da kunya, suka tafi a gurguje.

Maganar Wycliffe ta cika. Ya rayu domin shi ba ‘yan kasarsa makami mafi-karfi kan Rum, watau Littafin, abinda Allah Ya bayar don ‘yantarwa da wayewar mutane da kuma yi masu wa’azi. Aikin nan ya fuskanci manyan matsaloli da yawa. Wycliffe ya kamu da rashin lafya; ya san cewa shekarun aiki da sun rage masa ba yawa; ya ga hamayyan da zai fuskanta dole; amma bisa ga alkawuran maganar Allah, ya ci gaba ban da shakka. Da dukan karfin iliminsa, da kwarewarsa, Allah Ya rigaya Ya shirya shi don aikin nan mafi-girma. Yayin da addinin Kirista ke fama da rikici, Wycliffe a wurin aikinsa a Lutterworth, ya sa kai sosai cikin aikin nan da ya zaba, bai ko kula hayanniyan da ake yi ba.

A karshe an gama aikin — juyin Littafi zuwa Turanci, na farko da aka taba yi. Aka bude ma Ingila maganar Allah. Yanzu Mai-Canjin ba ya tsoron kurkuku, ko mutuwa. Ya rigaya ya ba mutanen Ingila hasken da ba za a taba kashewa ba. Ta wurin ba mutanen kasarsa Littafin, ya yi abin da zai fi tsinke sarkokin jahilci da mugunta, ya kuma yantar da kasarsa, fiye da kowace nasara da aka taba yi a filin yaki.

Da shike ba a rigaya an fara buga Littattafai na kusa ba, a hankali ne Littattafai suka yawaita. Marmarin samun Littafin ya yi yawa har mutane da yawa suka shiga yin kofen sa, amma da kyar suka iya gamsar da masu bukata. Wadansu mawadata suka so Littafin dungum. Wadansu suka sayi sashi sashi ne kadai. Wadansu lokuta iyalai da yawa ne sukan hada kurdi su sayi Littafi daya. Ta haka Littafin Wycliffe ya shiga gidajen mutane.

Motsawar tunaninsu da Littafi ya yi, ya falkar da su daga yarda kuma da koyaswoyin paparuma. Yanzu kuma Wycliffe ya koyar da kaidodin rabuwa da ekklkesiya cikin Kristi, da kuma rashin kuskuren Litaffin. Masu wa’azin da ya aika suka rika sayar da Littafi tare da rubuce rubucen Wycliffe, har kusan rabin mutanen Ingila suka karbi sabuwar ibadar.

Bayanuwar Littafin ya bata ma mahukuntan ekklesiya rai. Yanzu dole su sadu da abinda yafi Wycliffe karfi. Abin da makaman su ba za su iya yi masa kome ba. A wannan lokacin ba doka a Ingila da ta hana Littafin, domin ba a taba wallafa shi a harshen mutanen

ba. Daga baya aka yi wadannan dokokin, aka kuma aiwatar da su sosai. Kafin nan, duk da kokarin priestocin, an sami zarafin baza maganar Allah, na wani lokaci.

Kuma, shugabanin mulkin paparuma suka shirya rufe muryar Wycliffe. Aka gurbanar da shi a gaban hukumomi uku, daya bayan daya, duk a banza. Da farko wata majalisar bishops ta sanar da cewa rubuce rubucensa ridda ne, kuma da suka jawo matashin sarki Richard gefensu, suka sami dokar sarki da ta umurta jefa duk wanda aka samu da koyaswoyin nan cikin kurkuku.

Wycliffe ya daukaka kara daga Synod zuwa Majalisar kasa; gurbanar da shugabannin gaban Majalisar kasa, ya bukaci a canza munanan cin mutunchi da ekklesiya ta ba da izinin yi. Da karfi sosai ya bayana kwace da muguntar ikon paparuma. Magabtansa suka rikice. An rigaya an tilasta abokan Wycliffe da magoya bayansa suka ja da baya. Kuma aka zata cewa shi kansa, mai-canjin sabo da tsufa da kadaici da rashin abokai, zai amince da hadadden ikon ekklesiya da na shugabaninta. Amma maimakon haka, suka ga an ka da su. Majalisa da jawabin Wycliffe ya ja hankalinta, sai ta sake dokan nan na zalunci, Wycliffe ya sake samun yanchi kuma.

Sau na uku, aka kai shi gaban sharia, gaban hukuma mafi girma ta ekklesiya a kasar. Ba a tausaya ma ridda a nan. Nan aka zata Rum za ta yi nasara a kuma tsayar da aikin canji idan suka yi nasara , za a tilasta Wycliffe ya janye koyaswoyinsa, ko kuma daga kotun a kai shi inda za a kone shi kawai.

Amma Wycliffe bai janye ba; ba tsoro ya manne ma koyaswoyinsa, ya kuma rushe zarge-zargen masu cin zalin sa. Sa’anda ya manta kansa, da matsayinsa, da inda yake, sai ya kai karar masu sauraronsa gaban hukumar sama, ya kuma auna rudunsu a ma’aunin gaskiya ta har abada. Aka ji ikon Ruhu Mai tsarki a cikin dakin majalisar. Masu ji suka harbu da jifa daga wurin Allah. Suka ji kamar ba su da ikon barin wurin. Kamar kibawu daga kwarin Ubangiji, kalmomin dan canjin nan suka rika sakar zukatansu. Ya juya zargin ridda da suka yi masa a kansu. Ye ce, don me suka baza kurakuransu? Sabo da neman riba sai a yi kasuwanci da alherin Allah?

Daga baya ya ce, “Da wa, a ganinku, kuke jayayya? Da tsoho da ke bakin kabari? Babu! da gaskiya — Gaskiyar da ta fi karfinku, za ta ku ma yi nasara bisanku. Da ya fadi wannan, sai ya fita daga majalisar, ba wanda kuma ya gwada hana shi fita.

Aikin Wycliffe ya kusa cika, tutar gaskiya da ya dade yana rikewa tana gaf da faduwa daga hannunsa; amma kuma zai dai sake ba da shaida ga bishara. Za a yi shelar gaskiya daga madogarar mulkin kure. Aka yi sammacin Wycliffe gaban kotun paparuma a Rum, wadda sau da yawa ta rika zub da jinin tsarkaka. Bai kasa ganin hasarin da yake fuskanta ba, duk da haka, ba don ciwon inna ya hana shi zuwa ba, da ya je wurin tuhumar. Amma ko da shike ba a ji muryarsa a Rum ba , zai iya magana tawurin wasika, ya kuma shirya yin

hakan. Daga wurin aikinsa, Wycliffe ya rubuta ma paparuma wasika wadda tsautawa ce ga shagali da girma rai na mulkin paparuma.

Ya ce, “hakika ina murna in bude in kuma shaida ma kowane mutum imanin da ni ke rike, musamman ma ga bishop na Rum: wanda, da shike na san na kwarai ne kuma ga gaskiya ce, za ya hakikance imanin nawa, idan kuma akwai kuskure, ya gyara mani shi”

“Da farko, ina gani kamar bisharar Kristi dukan dokar Allah ne dungum…. A gani na bishop na Rum, da shike shi ne wakilin Kristi a nan duniya, shi ne dokar bisharar ta zama wajibi gare shi, fiye da dukan sauran mutane. Gama girma tsakanin almajiran Kristi, bai kunshi martaba ko daraja irin na duniya ba, amma ya kunshi bin Kristi kusa kusa daidai kuma da rayuwarsa da halayyansa ……. Kristi, a lokacin rayuwarsa a nan matalauci ne sosai, wanda yaki ya kuma yi watsi da dukan shugabanai da daraja na duniya…..

“Ba amintace da ya kamata ya bi paparuma kansa, ko kuma wani daga cikin mutane masu-tsarki, sai dai idan shi ma ya bi Ubangiji Yesu Kristi; gama Bitrus da yaran Zabadi, ta wurin bidar daraja ta duniya, sabanin bin matakai na Kristi sun yi laifi, sabo da haka kuwa bai kamata a bi su cikin kura kuran nan ba…..

“Ya kamata paparuma ya bar ma masu ikon duniya dukan mulki na duniya, ya kuma gargadi dukan ma’aikatan ekklesiyarsa su yi hakanan, gama haka ne Kristi ya yi, masamman ma manzaninsa. Sabo da haka, idan na yi kuskure game da wani abu cikin wadannan ababan, da tawali’u matuka zan mika kai na a yi mani gyara, har tawurin mutuwa ma, idan ta kama; idan kuma zan iya fama bisa ga nufin kai na dakai na, hakika zan gabatar da kai na wurin bishop na Rum; amma Ubangiji Ya ziyarce ni akasin hakan, Ya koya mani in yi biyayya ga Allah maimakon mutane.”

A karshe, ya ce: “Bari mu yi addu’a ga Allahnmu, domin Ya motsa paparumanmu Urban VI, yadda ya fara, domin shi da ma’aikatansa na bishara su bi Ubangiji Yesu Kristi cikin rayuwa da halayya; kuma su koya ma mutane da kyau, su kuma hakanan su bi su cikin sa.”

Ta haka Wycliffe ya nuna ma paparuma da manyan ma’aikatan ekklesiyarsa tawali’u da saukin kan Kristi, ya kuma nuna masu da dukan Kirista bambanci tsakanin su da Mai-gidan, wanda suka ce suna wakiltansa.

Wycliffe ya sa rai lallai ransa zai zama farashin amincinsa. Sarkin, paparuman, da bishops din, sun hada kai don tabbatar da tatikewarsa, ya kuma ga kamar cikin watanni kalilan za a kashe shi. Amma karfin halinsa bai raunana ba. Yace: “Don me kake neman rawanin mutuwa sabo da addininka da nisa? Yi shelar bisharar Kristi ga priestoci masu alfarma, mututwa don addini kuwa ba za ta wuce ka ba. Mene! Ni in rayu sa’anan in yi shuru?.... ko kadan! Bari bugun ya fada, ina jiran zuwan sa.”

Amma alherin Allah ya kuma tsare bawansa. Mutumin da duk rayuwarsa ya tsaya da gaske yana kare gaskiya, kullum cikin hadari ga ransa, ba zai fadi a hannun makiyansa ba. Wycliffe bai taba neman kare kansa ba, amma Ubangiji ne ya kasance mai-tsaron sa. Yanzu kuma da magabtansa suka ji kamar ya shiga hannunsu, hannun Allah ya cire shi daga gare su. Cikin ekklesiyarsa a Lutterworth, yayin da yana gaf da ba da jibin Ubangiji, ya fadi, gama ya harbu da ciwon shan inna, jima kadan kuma ya rasu.

Allah ya shirya ma Wycliffe aikinsa. Ya sa maganar gaskiya a bakinsa, ya kuma tsare shi domin maganan nan ya kai wurin mutane. An tsare ransa, aka kuma tsawaita aikinsa, har sai da aka kafa harsashen babban aikin nan na canji.

Wycliffe ya zo daga duhun Zamanin Duhun nan ne. ba shi da wadansu magabata da zai yi anfani da aikinsu don sifanta nashi aikin canjin. An tayar da shi kamar Yohanna mai-baptisma ne, domin shi cim ma wata manufa ta musamman, ya zama mai-gabatarwan sabon zamani. Duk da haka, cikin irin gaskiyan da ya bayana akwai daidaituwa da ‘yan canjin da suka bi bayansa basu wuce ba, wanda wadansu kuma basu kai ba, har bayan shekaru dari ma. Tushen ya yi fadi da zurfi, tsarin kuma mai-karfi ne da gaskiya kuma, ta yadda bai kamata na bayansa su sake shi ba.

Babban aikin da Wycliffe ya fara, wato yantarwar lamiri da tunani, ya kuma kubutar da al’ummai da suka dade a daure a jikin mulkin Rum, ya taso daga Littafi ne. Wannan ne mabulbulan albarkan nan, wanda kamar ruwan rai, yana gudu cikin sararaki tun karni na goma sha hudu. Wycliffe ya karbi Littafi da cikakken bangaskiya, cewa hurarren bayanin nufin Allah ne, isasshiyar kaidar bangaskiya da aikatawa. An koya mashi ya ga ekklesiyar Rum kamar iko daga Allah wanda ba ta kuskure, shi kuma yarda, ban da tambaya, da koyaswoyi da al’adun da aka kafa fiye da shekara dubu; amma ya juya daga dukan wadannan, ya saurari magana mai-tsarki na Allah. Wannan ne ikon da ya roki mutane su yarda da shi. Maimakon ekklesiya da ke magana ta wurin paparuma, ya bayana cewa muryar Allah da yake magana ta wurin maganarsa ne ke da iko. Ya kuma koyar da cewa ba wai Littafi cikakken bayanin nufin Allah ba ne kawai, amma cewa Ruhu Mai-Tsarki ne kadai mai fasarta shi, kuma ta wurin nazarin koyaswoyinsa, ya kamata kowane mutum ya koya ma kansa abin da ya kamata ya yi. Ta haka ya juya tunanin mutane daga paparuma da ekklesiyar Rum zuwa maganar Allah.

Wycliffe yana daga cikin fitattun yan Canjin. Game da yawan hikima, da kyakyawar tunani, da naciyar rikon gaskiya, da kuma karfin zuciya wajen kare ta, kadan ne daga cikin na bayansa sun kai shi. Tsabtar rai, naciyar himma wajen nazari da aiki, aminci, da kauna irin ta Kristi, da aminci cikin aikinsu, su ne halayyan yan canji na farko. Kuma duk da duhun tunani da rashin adalcin da suka mamaye zamanin nasu kenan fa.

Halin Wycliffe shaida ce ta ikon ilimantarwa da sakewa na Littafin. Littafin ne ya sa shi ya zama yadda ya zama. Kokarin gane muhimman gaskiya da aka bayana yakan ba da

sabuntawa da kuma kwazo ga kowane fannin jikin mutum. Yakan fadada tunani, ya inganta fahimi, ya kuma nunar da basira. Nazarin Littafin zai inganta kowane tunani, da buri fiye da kowane irin ilimi. Yana ba da karkon manufa, hakuri, karfin zuciya da dauriya; yana inganta hali, ya tsarkake mutum. Nazarin Littafi cikin kwazo da saduda, wanda ke sada tunanin dalibin da na Allah, zai ba duniya mutane masu tunani mai karfi da kuzari kuma, da kuma kaida mafi-kirki, fiye da wanda ya taba samuwa daga koyaswa mafi-inganci na mutane. In ji mai-zabura: “Buden zantattukanka yana ba da haske; yana ba da fahimi ga sahihai.” Zabura 119:130.

Koyaswoyin Wycliffe sun ci gaba da yaduwa na wani lokaci; mabiyansa, da ake kira Wycliffawa da Lollards, ba wai sun shiga dukan Ingila ba ne kadai, amma suka bazu zuwa wadansu kasashe, suna kai sanin bishara. Yanzu da an cire shugabansu, masu wa’azin sun yi aiki da kwazo fiye da da ma, jama’a kuma suka rika taruwa domin jin koyaswoyinsu. Wadansu fadawa, har da matar sarkin ma, suna cikin tubabbun. A wurare da yawa aka sami kyakyawan canjin halayyan mutanen, aka kuma cire alamun gumakan ekklesiyar Rum daga majami’un. Amma nan da nan guguwar zalunci ba tausayi ta abko ma wadanda suka karbi Littafin a matsayin mai-bishewarsu. Sarakunan Ingila, don neman karfafa ikon su tawurin samun goyon bayan Rum, basu yi jinkirin sadakar da ‘yan canjin ba. Lokacin ne na farko a tarihin Ingila da aka taba umurtawa a kashe almajiran bishara. Kisa ta bi bayan kisa. Masu shelar gaskiya, da aka wulakanta, sun iya kai kukansu ga Ubangijin Assabbat ne kadai. Da aka yi farantarsu a matsayin magabtan ekklesiya da masu cin amanar kasa, suka ci gaba da wa’azi a wurare na boye, suna samun mafaka a gidajen matalauta, sau dayawa ma sukan buya a koguna ko ramuka.

Duk da zafin zalunci, an ci gaba da nuna kin yarda da lalcewar imani cikin natsuwa da hakuri da naciya har tsawon daruruwan shekaru. Kiristan wancan zamanin sun mallaki karamin sanin gaskiya ne kawai; amma suka koyi yin kaunar maganar Allah da biyayya gare ta kuma, suka kuma jimre shan wahala domin ta. Kamar almajiran a zamanin manzanin, da yawa suka sadakar da mallakarsu ta duniya sabo da aikin Kristi wadanda aka yarda masu su kasance a gidajensu suka ba abokan famansu matsuguni, kuma sa’anda aka kore su su ma, sai su ma suka karbi yanayin korarrun. Dubbai kam, don tsaron fushin azalumansu, suka sayi yancinsu tawurin sadakar da imaninsu, suka fita daga kurkuku yafe da tufafin masu-tuba, don bayana janyewarsu daga imaninsu. Suna da yawa, kuma cikinsu akwai ‘yan gidajen sarauta da matalauta da suka yi ta shaida gaskiyar a cikin kurkuku, cikin azaba da wuta, ba tsoro, suna murna cewa su ma sun isa su san zumuntar wahalolinsa.

Mutanen paparuma su kasa cim ma manufarsu game da Wycliffe lokacin rayuwarsa, kuma kiyayarsu ba ta kare ba yayin da gawarsa ke kwance shuru cikin kabari. Ta wurin dokar Majalisar Constance, sama da shekara arba’in bayan mutuwarsa, aka fito da kasusuwansa, aka kone su a gaban jama’a, aka kuma zubar da tokar cikin wani rafi da ke kusa. Wani tsohon mawallafi ya ce: “Wannan rafin ya kai tokansa Avon, daga Avon zuwa

cikin Severn, daga Severn zuwa cikin kananan tekuna, daga nan kuma babban teku. Ta haka, tokan Wycliffe alama ce ta koyasuwarsa, wadda yanzu ake bazawa ko ina a duniya." Ko kadan magabtansa basu gane ma'anar aikin muguntan nan nasu ba.

Ta wurin rubuce rubucen Wycliffe ne John Huss na Bohemia ya kai ga watsar da kurakurai da yawa na ekklesiyar Rum, ya kuma shiga aikin canji. Ta haka, cikin wadannan karni biyu masu-nisa da juna, aka shuka irin gaskiya. Daga Bohemia aikin ya ci gaba zuwa wadansu kasashe. Aka jawo zukatan mutane zuwa ga maganar Allah da aka manta da ita da dadewa. Hannun Allah yana shirya hanya domin Babban Canji

Babi na 6— Sojojin Gaskiya

An shuka bishara a Bohemia tun karni na tara. An juya Littafin zuwa harshen mutanen, aka kuma rika yin sujada cikin harshen nasu. Amma yayin da ikon paparuma ke karuwa, haka kuma maganar Allah ta dinga shudewa. Gregory VII, wanda ya rigaya ya kuduri aniyar ladabtar da sarakuna, haka kuma ya shirya jefa mutane cikin bauta, kuma sabo da haka aka ba da dokar da ta hana sujada cikin jama'a da harshen Bohemianci. Paparuma ya ce: "Ya gamshi mai-cikakken iko a yi sujadarsa da yaren da ba a sani ba, yana cewa mugunta da bidi'a da yawa sun taso sabo da kin bin wannan kaidar." Sabo da haka, Rum ta umurta cewa a kashe hasken maganar Allah a kuma kulle mutane cikin duhu. Amma Mai-sama Ya tanada wadansu hanyoyi dabam domin kiyaye ekklesiyarsa. Waldensiyawa da Albigensiyawa da yawa da zalunci ya kore su daga gidajensu a Faransa da Italiya, sun zo Bohemia. Ko da shike basu iya yin koyaswa a fili ba, sun rika yin aiki a boye. Ta haka aka rike ainihin imani daga karni zuwa karni.

Kafin zamanin Huss akwai mutanen Bohemia da suka taso a fili suka nuna rashin ingancin ekklesiya da fasikancin mutanen. Aikin su ya ja hankulan mutane da yawa. Taron shuagbannin ekklesiya ya karu, aka kuma bude ma almajiran bishara zalunci. Sa'an da suka gudu zuwa dazuzuka da tsaunuka don yin sujada, sai sojoji suka rika farautar su, suka kashe da yawa cikin su. Bayan wani lokaci, sai aka umurta cewa a kone dukan wadanda suka bar sujada ta Rum, amma yayin da Kiristan suka ba da rayukan su, sun rika begen nasarar aikin su. Daya daga cikin masu-koyar da cewa ceto ta wurin Mai-ceton da aka giciye ne kadai, sa'an da yake mutuwa, ya ce: "Yanzu fushin magabtan gaskiya yana nasara kan mu, amma ba har abada ba ne, wani daga cikin talakawa zai taso; babu takobi ko iko; kuma ba za su iya nasara kan sa ba." Zamanin Luther yana da nisa a lokacin; amma wani ya rigaya ya fara tashe, wanda shaidarsa game da Rum za ta motsa al'ummai.

John Huss dan talaka ne, kuma cikin kurciyar sa mutuwar baban sa ta mayar da shi maraya. Uwar sa mai-ibada sosai ta ba ilimi da tsoron Allah muhimmanci matuka, ta so ta samo ma danta wannan gadon. Huss ya je makarantar lardin sune, daga nan ya je jami'ar Prague ta hanyar agaji. Maman shi ta je Prague din tare da shi; gwamruwan nan mai-talauci ba ta da guzuri mai-ma'ana da za ta ba danta, amma sa'an da suka kusa da babban birnin, ta durkusa a gefen saurayin nan mara uba, ta roka masa albarkar Uban su na sama. Da kadan uwan nan ta san yadda za a amsa addu'arta.

A jami'ar, nan da nan Huss ya yi fice ta wurin kwazon sa da ci gaban sa maza maza. Hakanan, rayuwarsa mara-aibi, mai-saukin kai kuma da fara'arsa suka sa kowa ya girmama shi. Shi amintacen dan ekklesiyar Rum ne mai- kwazo wajen neman albarku na ruhaniya da ta ce tana bayarwa. Bayan ya gama jami'a, sai ya zama priest, ya kuma yi fice nan da nan, sai aka hada shi da fadar sarkin. An kuma mai da shi shehun mallami, daga baya kuma ya zama shugaban jami'ar, inda shi ya yi makarantar sa. Cikin shekaru kalilan, dalibin nan

da ya yi makaranta ta wurin agaji ya zama mutumin da kasar sa ke alfahari da shi, sunan sa kuma ya zama sananne ko ina a Turai.

Amma a wani fanni dabam ne Huss ya fara aikin canji. Shekaru da dama bayan ya zama prirest, aka sa ya zama mai-wa'azin ekklesiyar Baitalahmi. Wanda ya kafa wannan majami'an ya dinga koyar da cewa da harshe mutanen wurin ne za a rika koyar da Littafin. Duk da kin hakan da Rum ta yi, ba a dena kwata kwata ba a Bohemia. Amma akwai jahilci sosai game da Littafi, kuma laifuka mafi-muni suka mamaye mutane a kowane mataki. Huss ya kushe laifukan nan, yana anfani da maganar Allah domin tabbatar da kaidodin gaskiya da tsabta da shi yake koyarwa.

Wani mutumin Prague, Jerome, wanda daga baya ya shaku da Huss sosai, ya dawo da rubuce rubucen Wycliffe daga Ingila. Sarauniyar Ingila da ta rungumi rubuce rubucen Wycliffe, gimbiyar Bohemia ce, kuma ta wurin tasirin ta ne aka baza rubuce rubucen dan Canjin ko ina a kasarta ta gado. Huss ya karanta su da maarmari; ya gaskata cewa mawallafin su Kirista ne na kwarai, kuma ya yarda da canje canjen da aka ce a yi. Kafin nan, Huss, ko da shike bai sani ba, ya rigaya ya shiga hanyar da za ta kai shi nesa daga Rum.

Kusan lokacin nan, wadansu baki biyu suka shigo daga Ingila, masana ne da suka sami hasken, suka kuma zo domin su yi shelar sa a kasan nan mai-nisa. Da shike sun fara da zargin paparuma kai tsaye, nan da nan hukumomi suka hana su yin magana; amma da shike basu yarda su bar manufar su ba, suka canja dabarun su. Da shike kwararrun masu-zane da kuma wa'azi ne su, suka shiga anfani da kwarewar su. A wani wuri da kowa zai iya gani, suka zana hotuna biyu. Daya ya nuna shigowar Kristi Urushalima "Mai-tawali'u ne, yana tafiya bisa kan jaki" (Matta 21:5), almajiran Shi kuma suna bin Shi da kodaddun riguna, ba takalma. Daya hoton kuma ya nuna jerin gwanon paparuma; paparuma yana yafe da tufafinsa masu-tsada da rawaninsa, yana bisa kan doki mai-ado sosai, a gabansa ga masu busa kaho, manyan shugabannin ekklesiya cikin ado mai-tsada kuma suna bin sa.

Wa'azin nan ya jawo hankulan koawane fanni na jama'a. Jama'a sun rika zuwa kallon zanen hotunan. Kowa ya gane sakon, da yawa kuma suka motsu da bambanci tsakanin tawali'u da saukin kan Kristi Mai-gidan, da fahariya da girman kan paparuma, mai-cewa wai shi bawan Kristi ne. An yi tashin hankali sosai a Prague, jima kadan kuma bakin suka ga cewa wajibi ne su tafi, sabo da tsaron lafiyar su. Amma ba a manta darasin da suka koyar ba. Hotunan sun sa Huss tunani sosai, suka kuma sa shi ya kara nazarin Littafi da rubuce rubucen Wycliffe da kyau. Ko da shike bai shirya karban canje canjen da Wycliffe ya shawarta ba, ya kara ganin ainihin halin paparuma, da Karin himma kuma ya kushe faharya da buri da lalacewar tsarin.

Daga Bohemia hasken ya kai Jamus, domin tashe tashen hankula a Prague sun jawo sallamar daruruwan dalibai, ‘yan Jamus. Da yawa cikinsu sun rigaya sun sami Littafin su na fari daga wurin Huss, kuma daga dawowarsu suka yi shelar bisharar a kasarsu ta gado.

An kai labarin aikin Prague din a Rum, nan da nan kuwa aka bukaci Huss ya bayana a gaban paparuma. Zuwan shi zai sa a ba da shi ga mutuwa tabbas. Sarikin Bohemia da sarauniyar, da jami’ar da masu-martaba da jami’an gwamnati, suka hada kai, suka roki paparuma cewa a bar Huss ya kasance a Bohemia, ya amsa zargin Rum ta wurin wakilinsa. Maimakon amincewa da wannan roko sai paparuma ya ci gaba, ya shar’anta Huss, ya iske shi da laifi, ya kuma ce Birnin Prague ma tana kalkashin horo, cewa ba za a yi hidimar ibada a cikinta ba kuma.

A wancan zamanin, irin hukumcin nan yakan ta da hankula ko ina. Aka tsara hidimomin da aka hana, ta yadda za a razana mutanen nan da ke ganin paparuma kamar wakilin Allah kansa, mai-rike mabudan sama da lahira, da kuma ikon jawo horo, na jiki da na ruhaniya. Akan dauka cewa an rufe kofofin sama daga kowane wurin da aka kakaba masa wannan horon; kuma har lokacin da paparuma ya ga dama ya cire takunkumin, mutanen nan ba za su iya shiga wuraren salama ba. Alamar wannan masifa ita ce dakatar da dukan hidimomin addini. Akan rufe dukan majami’u; a kan daura aure a harabar masujadar ne. Matattun da akan hana bisonsu a wurin da aka kebe, akan bizne su babu hidimomin biso, a cikin lambatu ko a daji. Ta hakanan Rum ta yi kokarin mallakan lamirin mutane.

Birnin Prague ya cika da tashin hankali. Jama’a da yawa suka zargi Huss cewa shi ne sanadin dukan matsalolin, suka kuma bidi cewa a ba da shi ga ramuwar Rum. Don kwantar da tarzumar, dan Canjin ya koma kauyen haihuwarsa. Ya rubuta ma abokansa da ya bari a Prague: “Idan na juye daga tsakanin ku, domin bin kwatancin Yesu Kristi ne, domin kada in ba masu-mugun nufi dama su ja ma kansu hukumci na har abada, kuma kada in zama ma masu-ibada sanadin bala’i da zalunci. Na janye kuma don gudun kada priestoci marasa imani su dade suna hana wa’azin maganar Allah a cikinku; amma ban yarda maku ku ki gaskiyar Allah wadda ni ke shirye in mutu sabo da shi ba.” Huss bai dena aikace aikacensa ba, amma ya dinga zagaya kauyukan kewaye yana wa’azi ga jama’a. Ta hakanan hanyoyin da paparuma ya bi don danne bisharar sun kara fadada bishra ne kuma. “Gama ba mu da iko mu yi komi sabanin gaskiya ba, sai domin gaskiya.” Korinthiyawa II, 13:8.

“Zuciyar Huss a wannan lokacin aikin nasa ya cika da tankiya mai-tsanani. Ko da shike ekklesiya ta nemi rufe shi da hare harenta, bai rabu da ikonta ba. Har wancan lokacin dai, ekklesiyar Rum ce amaryar Kristi, paparuma kuma, wakilin Allah, mataimakinsa kuma. Abin da Huss ke yaki akai shi ne yin anfani da iko yadda bai kamata ba, ba kaidar kan ta ba. Wannan ya jawo sabani sosai tsakanin ganewarsa da lamirinsa. Idan ikon nan daidai ne, mara-kuskure kuma, yadda shi ya gaskata, ta yaya shi ya ga ya kamata ya ki yin biyayya gare ta? Ya ga cewa yin biyayya zunubi ne; amma don me yin biyayya ga

ekklesiyar da ba ta kuskure zai kai ga haka? Damuwan da ya kasa magancewa kenan; shakkar da ta dinga zaluntar sa ke nan kowace sa'a. Amsar da ta fi kusa gamsar da shi, ita ce cewa abin ya faru ne kamar yadda ya faru lokacin Mai-ceton, sa'an da priestocin ekklesiya suka zama miyagu, suna anfani da ikon da doka ta ba su domin aikata ababa ba bisa doka ba. Wannan ya sa shi ya dauka a zuciyarsa cewa umurnin Littafi da aka bayar ta wurin ganewa su ne ya kamata su yi mulki bisa lamiri; watau Allah da ke magana cikin Littafi Shi ne Mai-bishewa mara- kuskure kadai, ba ekklesiya da ke Magana ta wurin priestoci ba."

Sa'an da bayan wani lokaci hayanniyar Prague ta ragu, Huss ya koma majami'arsa ta Baitalahmi, ya ci gaba da wa'azin maganar Allah da karfin himma, da karfin zuciya kuma. Magabtan sa masu kwazo ne da iko kuma, amma sarauniya da fadawa da yawa abokan sa ne, mutane da yawa kuma suka goyi bayansa. Da yawa da suka gwada koysawoyinsa marasa aibi da rayuwarsa mai-tsarki da munanan koyaswoyin da Romawan suka koyar, da fasikanci da son kurdinsu, sai suka ga cewa ya fi kyau su goyi bayansa.

Kafin nan, Huss shi kadai ne ya yi ta aikinsa, amma yanzu, Jerome, wanda a Ingila ya karbi koyaswoyin Wycliffe, shi ma ya shiga aikin Canjin. Daga nan su biyu din suka hada kai cikin rayuwarsu, kuma a mutuwa ma basu rabu ba. Jerome mai-madaukakiyar iyawa ne, ga iya magana ga sani kwarai; amma Huss ya fi shi halayya na gari. Halin shi na natsuwa ya rika rage gaggawar Jerome wanda cikin tawali'u yakan bi shawarwarinsa. Kalkashin aikinsu tare, canjin ya yadu da sauri.

Allah Ya bar haske mai-yawa ya haskaka zukatan mutanen nan zababbu, Ya bayana masu kurkuran Rum da yawa; amma basu karbi dukan hasken da aka ba duniya ba. Ta wurin bayin nan nasa, Allah Ya jawo mutane daga duhun addinin Rum; amma akwai manyan matsaloli da suka fuskanta, kuma Ya bi su daga mataki zuwa mataki yadda suka iya jimrewa. Basu shirya karban dukan hasken a lokaci daya ba. Kamar dukan hasken tsakar rana ga wadanda suka dade cikin duhu, da an nuna masu hasken gaba daya, da ya kore su. Don haka Ya bayana ma shugabanin kadan kadan, yadda mutanen za su iya karban shi. Daga karni zuwa karni wadansu amintattun ma'aikata suka bi baya don jagorantar mutane cikin hanyar canji.

Rashin jituwa ya ci gaba cikin ekklesiyar. Paparuma uku suka yi ta hamayyar neman fifiko, wannan kuwa ya cika Kiristanci da laifuka da hayanniya. Zage zage basu ishe su ba, suka hada da makamai ma. Kowane dayansu ya shiga sayen makamai da tara sojoji; dole a sami kurdi kuma ai; don haka aka shiga sayar da kyautukan ekklesiya da matsayi da albarkun ekklesiya. Prietocin ma, don kwaikwayon manyansu, suka shiga sayar da ababan nan da yakin kaskantar da abokan hamayyansu da inganta ikon kansu kuma. Da karfin zuciya Huss ya kushe ababan ban kyaman nan da aka dinga yi da sunan addini; mutanen kuma suka zargi shugabannin ekklesiyar Rum din cewa su ne sanadin wahalolin da suka mamaye Kiristanci.

Birnin Prague kuma ya shiga wata hayanniyar. Kamar zamanun baya, an zargi bawan Allah cewa: “Kai mai-wahal da Israila.” Sarakuna I, 17:18. Aka sake sa birnin cikin horo,Huss kuma ya koma kauyen haihuwarsa. Shaidar da aka rika bayarwa da mainci a majami’arsa ta Baitalahmi ta kare. Ya shiga yin magana ga dukan Kirista, kafin ya ba da ransa ya mutu a matsayin Shaidan gaskiya.

Domin magance muguntar da ke dauke hankalin Turai, aka shirya taron majalisa ta bai daya a Constance. Babban sarki Sigismund ne ya bukaci a kira taron, ta wurin daya daga cikin paparuman nan uku masu-hamayya da juna, John XXIII. Paparuma John din bai so a yi taron nan, ba, halin sa kuwa ba wanda zai so a bincika ne ba, ko da malalatan yan bisharan zamanin ne za su yi binciken. Amma bai isa ya ja da umurnin Sigismund ba.

Muhimman manufofin majalisarsu ne magance rashin-jituwa da ke cikin ekklesiya, a kuma kawar da ridda. Sabo da haka, aka kira masu-jayayyan nan da paparuma, su biyu din, su bayana a gaban majalisar, har da jagoran sabobin ra’ayoyin nan, John Huss. Mutum biyu na farkon, sabo da tsaron lafiyarsu, basu hallara da kan su ba, amma wakilan su sun hallara. Paparuma John da ake gani shi ne ya kira taron majalisar, ya hallara da shakku, yana zato cewa babban sarkin yana shirin tube shi ne, yana kuma tsoron za a abincike shi sabo da miyagun ayukansa da suka kunyatar da mulkin paparuma, da kuma laifukan da suka karfafa mulkin. Duk da haka ya shiga birnin Constance din da shagulgula sosai, tare da ma’aikatan ekklesiya da fadawa ma. Dukan ma’aikatan eklesiya da masu-martaban birnin, da ‘yan kasa da yawa, sun fita suka marabce shi. Bisa kansa akwai babban laima na zinariya da manyan majistaroti hudu suka rike. Aka rike gurasar cin jibi a gabansa, tufafi masu tsada da shugabannin ekklesiyan suka sa kuma sun ba da sha’awa.

Ana haka, wani matafiyin ma yana kusatowa Constance. Huss ya san da hadarukan da ke barazana gare shi. Ya rabu da abokansa, kaman ba zai sake saduwa da su ba, ya ci gaba da tafiyar sa da tsammanin cewa za ta kai shi ga mutuwa. Duk da haka, ya karbi takardar kariya wurin sarkin Bohemia, da wata kuma wurin babban sarki Sigismund. Yayin da yake cikin tafiyar tasa, ya yi dukan shirye shiryensa da tsammanin yiyuwar mutuwarsa.

Cikin wata wasika da ya rubuta ma abokansa a Prague, ya ce: “‘Yan-uwa na, zan tafi tare da takardar kariya daga wurin sarki, in sadu da magabta na masu-yawa, masu neman kashe ni kuma…. Daga baya na dogara ga Allah mai-cikakken iko ne, da Mai-ceto na; na gaskata zai ji addu’o’in ku na naciya, cewa zai cika baki na da dabararsa da hikimarasa, domin in yi tsayayya da su; kuma cewa zai ba ni Ruhunsa Mai-tsarki Shi karfafa ni cikin gaskiyarsa domin, da karfin zuciya, in fuskanci jarabobi da kurkuku, in ta kama ma, har da mutuwa ta azaba. Yesu Kristi ya wahala sabo da kaunatattuns; sabo da haka kuma, ko ya kamata mu yi mamakin cewa Ya bar mana kwatancinsa, domin mu ma mu jimre dukan ababa da hakuri sabo da ceton mu? Shi Allah ne, mu kuma halitattunsa ne; Shi ne Ubangiji, mu kuma bayinsa; Shi ne Mai-gidan duniya, mu kuma masu-mutuwa ne, abin tausayi, duk da haka Ya wahala! Sabo da haka don me mu ma ba za mu wahala ba, musamman ma idan

wahalar sabo da tsarkakewar mu ne? Sabo da haka kaunatattu, idan mutuwa ta za ta kara darajarsa, ku yi addu'a ta zo da sauri, cewa kuma Ya taimake ni jimre dukan masifu na da aminci. Amma idan ya fi kyau in dawo cikin ku, bari mu yi addu'a ga Allah in dawo babu aibi, watau kada in danne wasali daya na gaskiyar bisharar, domin in bar ma yan-uwa na kwatanci gwanin kyau da za su bi. Sabo da haka watakila ba za ku sake ganin fuska ta a Prague ba; amma idan nufin Allah Mai-cikakken iko ne Ya dawo da ni wurin ku, bari mu ci gaba da karin karfin zuciya cikin sanin dokarsa da kaunar ta kuma."

Cikin wata wasika kuma, zuwa ga wani priest da ya zama almajirin bishara, Huss ya yi magana da tawali'u mai-zurfi game da kurakuransa, yana zargin kansa "da jin dadin sa tufafi masu-tsada, da kuma bata sa'o'i masu anfani, yana yin ababa marasa anfani." Sa'an nan ya kara gargadin cewa: "Bari darajar Allah da ceton rayuka su cika zuciyarka, ba mallakar duniya da gidaje da filaye ba. Ka yi hankali da yi ma gidan ka ado fiye da zuciyarka; kuma fiye da komi, ka lura da gini na ruhaniya. Ka yi ibada da tawali'u game da matalauta, kuma kada ka kashe dukiyar ka ta wurin bukukuwa. Idan ba ka sake rayuwar ka, ka rabu da almubazzaranci ba, ina tsoro cewa za a hore ka sosai, kaman ni kai na…. ka san koyaswa ta, da shike ka karbi koyaswata daga kuruciyarka; don haka ba anfani in kara rubuta maka. Amma ina kira gare ka, bisa ga alherin Ubnagijinmu, kada ka yi kwaikwayo na cikin duk wani aikin banza da ka ga na fada a ciki." A bayan wasikar, ya kara da cewa: "Ina rokon ka aboki na, kada ka bude hatimin nan har sai ka sami tabbaci cewa na mutu."

Cikin tafiyarsa, Huss ya ga alamun yaduwar koyaswoyinsa ko ina da kuma goyon bayan da aikinsa ya samu. Mutanen sun rika tururuwa domin su sadu da shi, kuma a wadansu garuruwa, majistarorin suka yi masa rakiya a titunansu.

Sa'an da Huss ya kai Constance, sai aka ba shi cikakken yanci. Paparuma ya kara masa tsaro da kansa, bayan takardar kariya da babban sarki ya ba shi. Amma ta wurin ketare wadannan umurnin kariyar, ba da jimawa ba, aka kama dan Canjin, bisa ga umurnin paparuma da shugabannin ekklesiyar Rum, aka jefa shi cikin wani kurkuku mai ban kyama. Daga baya aka kai shi wani babban daki a ketaren kogin Rhine inda aka rike shi a matsayin fursuna. Daga baya ma, paparuman da cin amanarsa bata anfane shi komi ba, an kai shi kurkuku dayan. An tabbatar da laifofin sa da yawa masu-ban kyama a gaban majalisa, ban da kisan kai da sayar da ababa na ruhaniya, da zina, da "zalunci da bai kamata a ambata ba ma." Don haka majalisa da kanta ta umurta aka raba shi da rawaninsa, aka kuma jefa shi cikin kurkuku. Masu takaran zama paparuma ma an sauke su, aka zabi sabon paparuma.

Ko da shike laifofin paparuman sun fi wadanda Huss ya taba zargin priesetoci da aikatawa, ya kuma bukaci cewa a yi canji a kansu, duk da haka, majalisa dayan da ta sauke paparuman, ta ci gaba ta murkushe dan Canjin. Sa Huss a kurkuku da aka yi, ya ta da fushi sosai a Bohemia. Mutane da yawa masu-martaba da iko suka rubuta ma majilisar rashin amincewarsu da wannan rashin adalcin. Babban sarkin, wanda bai ji dadin ketarewar takardar kariyan da ya bayar ba, bai goyi bayan tuhumar Huss ba. Amma magabtan Huss

sun nace, suka dage. Suka ja hankalin babban sarkin ga zancen bambance bambance da ababan da yake tsoro da kwazon sa ga ekklesiya. Suka yi mahawara masu-tsawo sosai don nuna cewa “bai kamata a cika ma masu-ridda alkawlin da aka yi masu ba, ko ma wadanda ake zato sun yi ridda, ko da an ba su takardar kariyan da babban sarki ko sarakuna suka bayar.” Ta hakanan ne suka yi nasara.

Rashin lafiya, da zaman kurkuku sun nakasa Huss, sabo da danshi da warin kurkukun sa sun jawo masa zazzabin da ya kusan kashe shi, daga baya aka kawo shi gaban majalisar. Yana fama da sarkoki ya tsaya gaban babban sarkin, wanda da aka yi alkawalin ba Huss kariya bisa ga daraja da kyakyawan amincinsa, shi babban sarkin. Duk lokacin tuhuman nan naas mai-tsawo, Huss ya rike gaskiya, a gaban shugabannin ekklesiya da na kasa kuma ya bayana kin yarda mai-nauyi da aminci game da lalacewar shugabannin ekklesiya. Sa’an da aka bukace shi ya zaba tsakanin janye koyaswoyinsa ko mutuwa, ya gwammaci a kashe shi.

Alherin Allah ya kiyaye shi. Cikin makonin wahalan nan da suka wuce kafin hukumcin sa na karshe, salamar sama ta cikka ran sa. Ya ce ma wani abokin sa: “Ina rubuta wasikan nan a cikin kurkuku na, kuma da dauraren hannu na, ina sa ran za a aiwatar Hukumcin kisa ta gobe.… Sa’an da, tare da taimakon Yesu Kristi, za mu sake saduwa kuma cikin salaman nan mai-dadi na rayuwa mai-zuwa, za ka ji yadda Allah Ya nuna mani jinkansa, yadda Ya goyi baya na a tsakiyar jarabobi na da kunci na.”

Cikin duhun kurkukun shi, ya hangi nasarar ainihin bangaskiya. Sa’an da cikin mafalki ya koma majami’arsa a Prague inda ya yi wa’azin bishara, ya ga paparuma da bishop bishop dinsa suna shafe hotunan Kristi da shi ya zana a bangon. “Wahayin nan ya dame shi: amma washegari ya ga masu zane da penti da yawa suna mayar da hotunan nan, fiye da yawan na da, da hasken launinsu ma. Da zaran sun gama aikinsu, masu-zanen, wadanda wani babban taron jama’a ya kewaye su, suka ta da murya suka ce: “Yanzu bari su paparuman, da bishop bishop din su zo; ba za su kara shafe su kuma ba!” Sa’an da dan Canjin ke fadin mafalkin nasa, ya ce: “Na tabbata hakika, cewa ba za a taba shafe kamanin Kristi ba. Sun so da sun hallaka Shi, amma za a zana Shi sabo cikin dukan zukata, ta wurin masu-wa’azi da sun fi ni sosai.”

Karo na karshe aka kawo Huss gaban majalisar. Babban taro ne mai-ban sha’awa — babban sarki da ‘ya’yan sarkin kasar, da wakilan sarki da cardinals da bishop bishop da priestoci, da kuma babban taron jama’a da suka zo kallon al’amuran ranan. Daga dukan fannonin Kirista aka taru don shaida babban hadayan nan ta farko cikin faman nan mai-tsawo, wadda ta wurin ta za a sami yancin lamiri.

Sa’an da aka bukace shi ya fadi kudurin shi na karshe, Huss ya bayana cewa ba zai janye ba, kuma yana kallon idon sarkin nan da ba kunya aka ketare umurninsa, ya ce: “Na kudurta da yardar kai na, in bayana gaban majalisan nan, kalkashin tsaro da amincin babban

sarkin nan da ke zaune a nan.” Jikin Sigismund ya yi sanyi sa’an da idanun kowa a wannan taron suka juya kansa.

Da shike an rigaya an ba da hukiumci, sai aka fara hidimar aiwatar da horon. Bishop suka sa ma fursunan kayan priest, kuma yayin da ya karbi rigar sarautar, ya ce: “An sa ma Ubangijinmu Yesu Kristi farar riga ce, don cin mutunci, sa’an da Hiridus ya sa aka kai Shi gaban Bilatus.” Sa’an da aka sake bidar sa ya janye, ya juya ya kalli jama’a, ya ce: “Da wace fuska ke nan zan kalli sammai? Yaya zan kalli jama’a da yawa da na yi masu wa’azin tsabtar bishara? Babu; ina girmama cetonsu fiye da jikin nan mara-gata, wanda aka shirya mutuwarsa.” Aka cire rigunan, daya bayan daya, kowane bishop kuma yana tsine masa yayin da yake aikata nasa fannin hidimar. Daga baya, “suka sa masa har hular takarda da aka zana mata hotunan aljannu masu ban-tsoro, da kalman cewa ‘Babban mai-ridda’ a rubuce a gaban. ‘Da farin ciki sosai,’ in ji Huss, zan sa rawanin nan na kunya dominka, ya Yesu, Kai da Ka sa rawanin kaya sabo da ni.’”

Sa’an da aka gabatar da shi, “priestocin suka ce: ‘Yanzu mun mika ranka ga iblis.’ ‘Ni kuma, in ji Huss, yayin da ya ta da idanun sa sama, ‘na mika ruhu na cikin hannayenka, ya Ubangiji Yesu, da shi ke kai ka fanshe ni.’”

Sai aka mika shi ga hukumomin kasa, aka kai shi wurin da aka kashe shi. Babban taron jama’a suka bi, daruruwan masu rike da makamai, priestoci da bishop bishop cikin tufafin su masu-tsada, da mazauna Constance. Bayan an daure shi ga babban itacen, an kuma shirya komi don kunna wutar, sai aka sake shawartar Huss cewa ya ceci kan sa, ta wurin janye kurakuransa. “Wadanne kurakurai,” in ji Huss, “zan janye? Na san ban yi ko daya ba. Ina kira ga Allah Ya shiada cewa duk abin da na rubuta, na kuma yi wa’azin sa, da niyyar ceton rayuka ne daga zunubi da hallaka, kuma, don haka, da murna matuka za hakikance da jini na gaskiyan da na rubuta na kuma yi wa’azin ta.” Sa’an da harsunan wutan suka taso kewaye da shi, ya fara waka cewa: “Yesu, Kai dan Dawuda, yi mani jin kai,” kuma ya ci gaba hakanan har sai da muryar sa ta kare har abada. Har magabtansa ma sun yi mamakin jaruntakarsa. Wani dan papaaruma mai-matsanancin ra’ayi, game da mutuwar Huss da na Jerome wanda ya mutu jima kadan bayan Huss, ya ce: “Dukan su sun rike amincin zukatan su har sa’ar su ta karshe. Sun shirya ma wutar, sai ka ce za su bukin aure ne. Basu yi kuka domin zafi ba. Sa’an da harsunan wuta suka taso, sun fara raira wakoki ne; kuma ko zafin wutar bai hana su rairawa ba.”

Bayan da wuta ta gama cinye jikin Huss, aka tattara tokan sa da kasar wurin da tokan ya kwanta, aka jefa cikin kogin Rhine, daga nan kuma ya wuce har teku. Masu zaluntar sa sun ga kamar ta wurin yin haka sun kawar da gaskiyar da ya koyar ke nan. Basu ko yi mafalkin cewa tokan da suka zubar har zuwa teku sun zama kamar iri ne da aka watsa cikin dukan kasashen duniya ba; cewa a kasashen da ba a rigaya an sani ba ma, zai haifar da ‘ya’ya a yalwace cikin shaidu na gaskiyar. Muryar da ta yi magana a babban zauren majalisar Constance ta falkas da muryoyin da za a dinga ji cikin dukan sararraki. Huss dai

ya tafi, amma koyaswoyin gaskiyan da ya mutu sabo da su ba za su taba lalacewa ba. Kwatancin shi na bangaskiya da aminci ya karfafa jama'a da yawa su tsaya da karfi domin gaskiya, komi zalunci ko mutuwa ma. Kisan shi ya bayana ma dukan duniya zaluncin Rum irin na cin amana. Ko da shike magabtan gaskiya basu sani ba, sun kara ci gaban aikin da suka so a banza su lalatar ne.

An kuma shirya wani wurin kisa a Constance. Dole jinin shaida ya shaida gaskiya. Sa'an da Jerome ya yi ban-kwana da Huss lokacin da zai tashi zuwa majalisar, ya karfafa shi ya yi karfin zuciya da naciya, yana cewa idan ya shiga wata damuwa, shi kan shi zai gudo ya taimake shi. Da zaran ya ji cewa an sa dan Canjin cikin kurkuku, nan da nan amintacen almajirin nan ya shirya domin cika alkawalin sa. Ba tare da wani alkawalin tsaro ba, ya kama hanya, tare da wani abokin tafiya, zuwa Constance. Daga isar sa wurin, ya gane cewa ya sa kansa cikin damuwa ne kawai, ba tare da wata yiwuwar yin wani abu domin kubutar da Huss ba. Ya gudu daga wurin, amma aka kama shi a hanyar sa zuwa gida, aka dawo da shi daurarre da sarkoki, kalkashin tsaron sojoji. A bayanuwar sa ta farko a gaban majalisar, kokarin sa na amsa zarge zargen da ake yi masa ya gamu da ihu cewa, "A kai shi wuta!" A kais hi wuta!" Aka jefa shi cikin kurkuku a daure, ta yadda ya wahala kwarai, ana ciyar da shi da burodi da ruwa. Bayan wadansu watanni, azabar kurkukun Jerome ta jawo masa ciwon da ya nemi ya dauke ransa, magabtansa kuma, sabo da tsoron cewa zai iya tserewa, suka rage tsananta masa, ko da shike ya kasance a kurkukun, har shekara guda.

Huss bai mutu yadda yan paparuma suka so ba. Ketarewar alakwalin tsaron sa ya ta da guguwar fushi, kuma a matsayin hanyar da ta fi sauki, majalisar ta kudurta cewa, maimakon kona Jerome, a tilasta shi, idan ya yiwu, ya janye. Sai aka kawo shi gaban majalisar, aka kuma ba shi zabin janyewar, ko kuma ya mutu a daure a jikin itace. In da ya mutu a farkon zaman sa a kurkuku, da ya zama jinkai gare shi, idan aka gwada da munanan wahalolin da ya sha; amma yanzu da ya nakasa sabo da ciwo da wahalolin kurkuku, da kuma azabar taraddadi da rashiN sanin abin da zai faru, ga rabuwa da abokai, ga kuma bakin cikin mutuwar Huss, karfin zuciyar Jerome ya waste, ya kuwa yarda zai bi umurnin majalisar. Ya dauki alkawalin manne ma addinin Katolika, ya kuma amince da yadda majalisar ta sake koyaswoyin Wycliffe da Huss, sai dai "gaskiyar masu-tsarki" da suka koyar.

Ta wurin matakin nan, Jerome ya yi kokarin rufe muryar lamiri, ya tsere kuma daga hallakar sa. Amma cikin kadaicinsa a kurkukun, ya ga abin da ya yi, a bayane. Ya yi tunanin karfin zuciyar Huss da amincinsa, sabanin haka kuma ya yi bimbini game da musun gaskiya da shi ya yi. Ya tuna Allah, Mai-gidan da shi ya yi alkawalin bauta masa, wanda kuma Ya jimre mutuwa ta giciye dominsa. Kafin janyewarsa, ya rigaya ya sami ta'aziya cikin dukan wahalolinsa, cikin tabbacin alherin Allah; amma yanzu juyayi da shakku suka azabtar da zuciyarsa. Ya san cewa akwai wadansu janyewa dole sai ya yi kafin ya sami

salama da Rum. Matakin da yake daukawa zai karasa da ridda gaba daya ne kawai. Ya dauki kudurinsa: don gudun takaitacen lokaci na wahala, ba zai yi musun Ubangijinsa ba.

Ba da jimawa ba, an sake kai shi gaban majalisar. Masu shari'an basu gamsu da jawabinsa ba. Kishin su na jini da mutuwar Huss ta tayar, ya sa sun rika marmarin karin wadanda za a kashe. Sai ta wurin yin watsi da gaskiya kwata kwata ne Jerome zai iya ceton ransa. Amma ya rigaya ya kudurta shaida bangaskiyarsa, ya kuma bi dan-uwansa Huss zuwa wutar.

Ya fa fasa janyewan da ya yi, kuma a matsayin wanda ke fuskantar mutuwa, ya bukaci zarafin kare kansa. Sabo da tsoron sakamakon kalmominsa, shugabannin ekklesiyar suka nace lallai sai dai ya amnice ko kuma ya yi musun zarge zargen da ake tuhuman sa da su. Jerome ya ki wannan zalunci da rashin adalcin. "Kun rike ni kuka hana ni magana, kwana dari uku da arba'in, cikin kurkuku mai-bantsoro, a tsakiyar kazanta da surutu, da wani wari da rashin komi da komi; sa'an nan kun kawo ni gabanku, bayan kun saurari magabta na, sai ku ki ji na…. Idan za ku zama mutane masu hikima da gaske, haske ga duniya kuma, sai ku mai da hankali kada ku yi zunubi sabanin adalci. Ni dai kumama ne mai-mutuwa, rai na mai- kankantar muhimminci ne; kuma idan na fadakar da ku cewa kada ku ba da hukumci na rashin adalci, ina magana sabo da ku ne, fiye da sabo da ni kai na."

A karshe, an amince da rokon shi. A gaban masu shar'anta shi, Jerome ya durkusa ya yi addu'a cewa Ruhun Allah Ya bi da tunaninsa da kalmominsa, domin kada ya yi wata magana da ta saba ma gaskiya ko kuma wadda ba za ta cancanci Mai-gidan shi ba. Gare shi a ranan nan an cika alkawalin Allah ga almajiran farkon cewa: "I, kuma a gaban mahukumta da sarakuna za a kawo ku sabili da ni,…. Amma sa'an da sun bashe ku, kada hankalin ku ya tashi irin magana da za ku yi, ko kwa abin da za ku fadi. Gama ba ku ne kuna fadi ba, amma Ruhun Ubanku ne mai-fadi a chikinku." Matta 10:18-20.

Kalmomin Jerome sun jawo mamaki da sha'awa har cikin magabtansa ma. Shekara guda yana tsare a kurkuku, bai sami damar yin karatu ba, ba ya ko gani ma, cikin wahala mai-yawa da tarddadi mai-tsanani. Duk da haka ya gabatar da mahawararsa sarai sarai da karfi kuma kamar da ma ya sami damar yin nazari ne ba tare da tsangwama ba. Ya ja hankulan masu sauraron sa ga dogon jerin mutane masu-tsarki da masu-shari'a marasa adalci suka hukunta su. A cikin kowace sara akwai wadanda, yayin da suke kokarin daga mutanen lokacin su, an zarge su, aka kuma kore su, amma da ga baya kuma aka iske cewa sun cancanci girmamawa. Kristi kansa, an hukumta cewa Shi mai-laifi ne, a wani kotu na rashin adalci.

Lokacin janyewar sa, Jerome ya rigaya ya yarda cewa hukumcin da ya iske Huss da laifi daidai ne. Yanzu kuma ya bayana tubarsa, ya kuma shaida tsarkin Huss da rashin laifinsa. "Na san shi tun kuruciyarsa," ya ce: "Mutum ne cikakke mara-aibi, mai-adalci da tsarki; an hukumta shi, duk da rashin laifin shi…. Ni ma, ina shirye in mutu: ba zan ja da

baya ba daga azaban da magabta na da shaidun karya suka shirya mani, wadnada wata rana dole za su ba da lissafin karyarsu a gaban Allah babba, wanda ba abin da zai iya rudin Sa."

Cikin zargin kansa sabo da musun gaskiya da ya yi, Jerome ya ci gaba cewa: "Cikin dukan zunuban da na yi tun ina saurayi, ba wanda ya fi damu na, yana kuma jawo mani nadama da yawa kamar wanda na aikata a wannan wurin mutuwar, lokacin da na amince da mugun hukumcin da aka yi ma Wycliffe, da kuma na mai-tsarkin nan Huss, mai-gida na da aboki na kuma. Hakika! Ina furta shi daga zuciya ta, ina kuma bayanawa da kyama cewa, da ban-kunya, nay i rashin karfin zuciya sa'an da, da tsoron mutuwa na kushe koyaswoyin su. Sabo da haka ina rokon…Allah madaukaki ya yi hakuri, Ya yafe mani zunubai na, kuma musamman wannan din, wanda ya fi dukan su muni." Sai ya nuna masu-shari'an da yatsa, da karfi kuma ya ce: "Kun hukumta Wycliffe da John Huss, ba don sun raunana koyaswar ekklesiya ba, amma don kawai sun nuna rashin amaincewa da ababan fallasa da ke fitowa daga ma'aikatan ekklesiya - shagulgulansu na girman kai, da alfaharinsu, da dukan laifukansu. Ababan da suka fada, wadanda kuma ba za a iya karyatawa ba, kamar su, ni ma na yi tunani na bayana su."

Aka sa baki cikin maganarsa. Ma'aikatan ekklesiya, suna rawan jiki don fushi, suka ta da ihu cewa: "Akwai kuma bukatar wani tabbaci fiye da wannan? Da idanun mu muna ganin mai-ridda mafi-taurin kai!"

Jerome bai kula holon su ba, ya ce: "Mene! Kuna tsammanin cewa ina tsoron mutuwa? Kun rike ni har shekara guda cikin kurkuku mai-ban tsoro. Kun wulakanta ni fiye da Baturki, ko Bayahudi, ko arne, nama na kuma, zahiri ya rube, ya rabu da kasusuwa na, da rai na kuwa; kuma duk da haka, ban nuna damuwa ba, da shike makoki bai yi kyau da mutum mai-zuciya da ruhu ba; amma dole in bayana mamaki na game da wannan irin babbauci da aka yi ma Kirista."

Guguwar fushi ta sake barkewa, aka kuma ruga da Jerome zuwa kurkuku. Duk da haka, cikin taron akwai wadanda kalmominsa suka taba zukatansu sosai, suka kuma so su ceci ransa. Masu martaba na ekklesiya sun ziyarce shi, suka roke shi ya ba da kan sa ga majalisar. Aka gabatar masa da hange mafi-ban sha'awa a matsayin ladar janye jayayyar sa ga Rum. Amma, kamar Mai-gidansa sa'an da aka yi masa tayin darajar duniya, Jerome ya nace da karfin halinsa.

"Ku tabbatar mani daga Littafi Mai-tsarki cewa ina kuskure," ya ce, "ni kuwa sai in rabu da shi."

Daya daga cikin masu-jarabtar shi ya ce, "Rubuce rubuce masu-tsarki! Watau da su za a gwada kowane abu ke nan? Wa zai fahimce su, idan ba ekklesiya ce ta fassara su ba?"

“Ko al’adun mutane sun fi bisharar Mai-ceton mu cancantuwa a gaskata su?”, amsar Jerome ke nan. “Bulus bai bukaci wadanda ya rubuta masu su saurari al’adun mutane ba, amma ya ce, ‘Ku bincika Nassosin.’ ”

Aka amsa cewa: “Mai-ridda! Na tuba da na dade haka ina rokon ka. Na ga cewa Iblis ne yake zuga ka.”

Ba da jimawa ba, aka sanar da hukumci a kan shi. Aka kai shi daidai inda Huss ya sallamar da ransa. Ya tafi yana waka a hanyarsa, fuskarsa tana haskakawa da murna da salama. Ya kafa hankalinsa a kan Kristi ne, a gare shi kuwa, mutuwa ta rigaya ta rasa ban-razanar ta. Sa’an da mai-kisan, gaf da lokacin da zai kunna ma karmomin wuta, ya koma bayan sa, Jerome da karfi ya ce: “Taho gaba na kai tsaye; kunna wutar a gaban fuska ta. Da a ce ina tsoro da ba na wurin nan.”

Kalmomin shi na karshe da ya furta sa’an da harsunan wutan suka taso a kan shi, addu’a ce. Ya ce: “Ubangiji, Madaukaki Uba, ka ji tausayi na, ka gafarta mani zunubai na; gama ka san ina kaunar gaskiyar ka kullum.” Muryar sa ta tsaya, amma lebunan sa suka ci gaba da motsi cikin addu’a. Sa’an da wutar ta gama aikinta, aka tara tokansa, da kasan da tokan ya kwanta a kai, kuma kaman na Huss, aka jefa su cikin Kogin Rhine.

Hakanan ne amintattun masu-kai hasken Allah suka hallaka. Amma hasken gaskiyan da suka yi shelan ta - hasken kwatancin jarumtakarsu- ba a iya bicewa ba. Yunkurin mutane na hana wayewan garin da a lokacin ya zo ma duniya, daidai yake da yunkurin tura rana ta koma baya.

Kashe Huss da aka yi ya kunna wutar fushi da kyama a Bohemia. Dukan al’ummar ta dauka cewa shi dai kiyayyar priestoci da cin amanansa da babban sarkin ya yi ne kawai suka sa an kashe shi. An bayana cewa shi amintacen mallami ne mai-koyar da gaskiya, aka kuma zargi majalisar da ta umurta kisansa da laifin kisa. Yanzu kuma koyaswoyinsa sun kara jawo hankula fiye da can baya. Ta wurin umurnin paparuma, an kone rubuce rubucen Wycliffe. Amma wadanda suka tsira daga kunar, yanzu an fito da su daga inda aka boye su, aka yi nazarinsu tare da Littafi, ko kuma fanonin Littafin da aka iya samu, ta haka kuma aka jawo mutane da yawa suka karbi sabuwar bangaskiyar.

Masu kashe Huss basu tsaya a gefe suka kalli nasarar aikinsa ba. Paparuma da babban sarkin suka hada kai domin murkushe aikin, aka kuma tura ma Bohemia mayakan Sigismund.

Amma fa an ta da mai-kubutarwa. Ziska, wanda daga farkon yakin ya makance, duk da haka ya kasance daya daga cikin kwararrun janar janar na zamaninsa, shi ne ya jagoranci yan Bohemia. Da dangana ga taimakon Allah da kuma adalcin aikinsu, al’umman nan ta nuna ma shahararrun mayakan nan karko. Akai-akai babban sarkin yakan ta da sabobin mayaka, ya kai ma Bohemia hari, amma sai a kuma kore su a saukake. Hussiyawan sun

wuci inda za su ji tsoron mutuwa, kuma ba bin da ya iya karawa da su. Shekaru kalilan bayan farawan yakin, jarumin nan Ziska yam mutu; amma Procopius, wanda shi ma jarumin janar ne, kwararre mara-tsoro, wanda kuma a wdansu fannonin shugabanci ya fi Ziska, ya dauki matsayin sa.

Magabtan Bohemiyawa, da sanin cewa makahon mayakin ya mutu, suka dauka cewa wannan zarafi ne da za su dawo da dukan abin da suka rasa. Sai kuma paparuma ya sanar da yakin addini kan mutanen Huss, ban da haka kuma aka ta da babban fada da Bohemia, amma kuma aka sha kaye mumuna. An sake sanar da wani yakin addinin. A dukan kasashen Turai masu-bin paparuma, aka tara mayaka da kurdi da makamai don yaki. Jama'a suka rika tururuwa don shiga rundunan mayakan paparuma, da tabbacin cewa a karshe dai za a kawo karshen masu riddan nan Hussawa. Da tabbacin nasara mayakan nan suka shiga Bohemia. Mutane suka taru domin su kore su. Rundunonin biyu suka fuskanci juna ta yadda kogi ne kadai tsakanin su. "Mayakan addinin sun fi na Hussawan karfi kwarai, amma maimako su kutsa cikin kogin su ketare domin su gwabza yaki da Hussawan, sai suka tsaya shuru suna kallon mayakan." Sai kuma faraf daya, wata razana mai-ban al'ajibi ta abko ma rundunar. Ba tare da ko bugu daya ba, babban rundunan nan ta waste, kamar wani iko da ba a gani ba ne ya watsar da su. Mayakan Hussawan suka kashe magabtan da yawa sosai, suka kore su, kuma ganima da yawa ta shiga hannun masu-nasaran,don haka maimako yakin ya tsiyatar da Bohemiyawan, ya arzunta su ne kuma.

Shekaru kaklilan bayan haka, kalkashin wani sabon paparuma, an sake shirya wani yakin addinin kuma. Kamar karon farko, an sake tara mutane da dukiya daga kasashen Turai yan paparuma. An kwadaita manyan lada ma masu zuwa wannan yaki mai-yawan hatsari. Aka tabbatar ma kowane mayaki cikakkiyar gafarar zunubai mafi muni. Dukan wadanda suka mutu a yakin an yi masu alkawalin babban lada a sama, wadanda basu mutu ba kuma za su girbe daraja da arziki a filin dagan ma. Aka kuma tara mayaka da yawa; kuma sa'an da suka ketare iyakar kasar, suka shiga Bohemia. Dakarun Hussawan suka ja baya, ta hakanan kuma suka rika jan magabtan zuwa ciki-cikin kasar. Suka kuma sa su sun dauka cewa sun rigaya sun yi nasara. A karshe dai, mayakan Procopius [shugaban Hussawan] suka tsaya, suka juya kan magabtansu, suka kuma ja daga da su. Masu yakin addinin, yanzu da suka gane kuskurensu, suka kwanta a sansaninsu, suna jira a fara fada. Da aka ji holon mayakan Hussawa, tun ma ba a gan su ba, rudewa ta sake abka ma mayakan addinin. 'Ya'yan sarki da janar janar da sauran sojoji suka jefar da makamansu, suka waste barkatai. A banza wakilin paparuma, wanda ya shugabanci harin, ya yi kokarin tattaro firgitattun mayakan nasa. Duk iyakar kokarinsa, shi kan shi ma ya arce tare da sauran masu-gudun. Cikakkiyar nasara aka yi, haka kuma ganima da yawa ta sake shiga hannun masu nasarar.

Haka kuwa, mayaka da dama a kasashe mafi-karfi na Turai suka tura rundunar horarru, da kayan yakinsu, suka gudu, kuma ba wanda ya taba su, daga gaban kankanuwar

al'umma mara-karfi. Nan ga shaidar ikon Allah. An buge magabtan da razana ce wadda ta wuce ikon dan Adam. Shi wanda Ya hallaka rundunonin mayakan Fir'auna a Jan Teku, wanda Ya kori rundunonin mayakan Midian a gaban Gideon da mutanen sa dari uku, wanda cikin dare daya, Ya hallaka dakarun Assyria masu alfarma, Ya kuma mika hannunsa domin shanye ikon azalumin. "A chan fa suka ji tsoro mai-yawa, ba kwa abin tsoro ba: gama Ubangiji Ya watsadda kasusuwan wanda ya kewaye ka da sansani; ka kumyata su, domin Allah ya ki su." Zabura 53:5.

Sa'an da shugabannin yan paparuman suka kasa yin nasara ta wurin yin anfani da karfi, a karshe sai suka koma ga lallashi. Aka yi wata daidaitawa dai, wadda, yayin da ta ce ta ba Bohemiyawa yancin lamiri, a zahiri ma dai ta bashe su ne ga ikon Rum. Bohemiyawan sun rigaya sun ba da sharudda hudu don sulhuntawa da Rum, watau: yancin wa'azin Littafi; yancin dukan ekklesiya ga gurasa da ruwan anab lokacin cin jibi da kuma anfani da harshensu lokacin sujada ga Allah; raba ma'aikatan ekklesiya daga dukan makamai na gwamnati da ba na addini ba; sa'an nan game da aikata laifuka, kotunan kasa su kasnce da hurumi kan ma'aikatan ekklesiya dadai da sauran mutane. A karshe dai mahukumtan yan paparuman sun "yarda cewa a amince da sharudda hudu na Hussiyawan, amma kuma cewa yancin fassara su, watau bayana ainihin ma'anar su zahiri, ya kamata ya kasance a hannun majalisa ne, watau dai a hannun paparuma da babban sarkin." Bisa ga wannan aka shiga yarjejjeniya, Rum kuma, ta wurin rudi da yaudara, ta sami abin da ta kasa samu ta wurin fada; gama, ta wurin ba sharuddan Hussawan ma'anan da ita ta so, kamar yadda ta yi da Littafi, za ta iya canja ma'anar su don cim ma manufofinta.

Mutane da yawa a Bohemia da suka ga cewa yarjejjeniyar ta tauye hakinsu, basu yarda da ita ba. Gardama da rarrabuwa suka taso, suka kai ga tashin hankali da zub da jini tsakaninsu. Cikin hargitsin nan ne mai-martaban nan Procopius ya mutu, yancin Bohemiyawa kuma suka hallaka.

Sigismund mai-bashe da Huss da Jerome, yanzu ya zama sarkin Bohemia, kuma duk da rantsuwar sa cewa zai goyi bayan yancin Bohemiyawa, ya ci gaba ya kafa tsarin paparuma. Amma bai yi riba mai-yawa ba ta wurin ba da kan sa kalkashin Rum. Shekaru ashirin rayuwar sa tana fama da wahaloli da hatsari. An rigaya an hallaka mayakan shi, baitulmalin shi kuma an tsiyaye ta wurin yaki mai-tsawo mara-anfani. Yanzu kuma, bayan ya yi mulki na shekara daya, ya mutu, ya bar kasarsa a bakin yakin basasa, ya kuma bar ma magada suna mara-kyau.

Rigingimu da tashe tashen hankula da zub da jini sun tsawanta. Dakarun kasashen waje suka sake kai ma Bohemia hari, rashin jituwa na cikin kasar kuma ya ci gaba yana dauke hankalin al'ummar. Wadanda suka kasance da aminci ga bishara kuma an gallaza masu azaba mai-zub da jini.

Yayin da yan'uwan su na da, da suka yi yarjejjeniya da Rum suka rungumi kurakuran ta, wadanda suka rike bangaskiya ta asalin sun kafa ekklesiyar su dabam, mai-suna "Yan'uwa Masu-Hadin kai." Wannan ya jawo masu tsinewa daga dukan bangarori. Duk da haka basu raunana ba. Sa'an da aka tilasta su suka nemi mafaka a koguna da dazuka, sun ci gaba da tattaruwa suna karanta maganar Allah da hada kai cikin sujada gare Shi.

Ta wurin 'yan sako da suka aika a boye zuwa kasashe dabam dabam, sun gane cewa da can akwai "tsirarun masu rungumar gaskiya, kalilan a wannan birni, kalila a wancan, wadanda kamar su, masu shan tsanantawa ne; kuma cewa cikin duwatsun Alps din nan, akwai dadaddiyar ekklesiya da ta kafu bisa harsashen Littafi, tana kuma jayayya da lalacewar Rum, irin ta bautar gumaka. An karbi labarin nan da murna sosai; aka kuma shiga sadarwa da Kiristan Waldensiyawa."

Cikin aminci ga bisharar, Bohemiyawan sun jira har karshen daren zaluncinsu, cikin sa'a mafi-duhu, suna dai juya idanunsu zuwa sama, kamar masu-jiran safiya. "Sun kasance cikin mugun zamani ne, amma … sun tuna kalmomin da Huss ya fara fadi, Jerome kuma ya nanata, cewa sai bayan shekaru dari kafin gari ya waye. Kalmomin nan sun zama ma Hussawan kamar yadda kalmomin Yusufu suka zama ma kabilun Israila ne a kasar bauta, cewa: 'Ina mutuwa: amma hakika Allah za ya ziyarche ku, ya fishe ku.'" "Lokacin karshen karni na sha biyar ya gamu da yawaitar ekklesiyoyin Yan'uwan a hankali, hakika kuma. Ko da shike an fitine su, duk da haka sun sami Karin hutu. A farkon karni na sha shida, ekklesiyoyin su sun kai guda dari biyu a Bohemia da Moravia." "Masu daraja ne ringin nan da suka tsere ma fushin hallaka na wuta da na takobi, aka yarda masu su ga tahowar ranan nan da Huss ya ce tana zuwa."

Babi na 7— Babban Rabuwa

Na gaba cikin wadanda aka kira domin jagorantar ekklesiya daga duhun tsarin paparuma zuwa haken gaskiya mafi-tsabta shi ne Martin Luther. Ga himma, ga kwazo, ga dukufa, ba tsoro sai dai tsoran Allah, wanda ya yarda da Littafin kadai a matsayin tushen imanin addini, Luther ne mutumin zamanin sa, ta wurin sa Allah Ya yi aiki mai-yawa domin canza ekklesiya da kuma haskaka duniya.

Kamar jakadun farko na bisharar, Luther ya taso daga talauci ne. Ya yi yarantakan shi a gidan wani talakan Jamus ne. Ta wurin aikin tonon ma'adini kowace rana, baban shi ya rika biyan kurdin makarantan shi. Ya so shi ya zama lauya ne; amma Allah Ya nufa Ya mai da shi magini a babban haikalin nan da ke tasowa a hankali cikin daruruwan shekaru. Wahala da kunci da tsananin horo ne makarantar da Allah Ya shirya Luther a ciki domin babban aikin da zai yi.

Baban Luther mutum ne mai-karfin zuciya da kuzari kuma, mai-halin kirki, amintace mai-taurin zuciya, mara zagaye-zagaye kuma. Mai-aminci ne ga aikinsa, ko da me zai faru. Basirar sa ta sa bai yarda da tsarin zuhudun nan ba. Bai ji dadi ba, lokacin da Luther, ba da goyon bayansa ba, ya shiga zuhudu; kuma sai bayan shekara biyu uban ya shirya da dan nasa akan wannan, duk da haka kuma ra'ayin uban bai sake ba.

Iyayen Luther sun kula da ilimin yayansu da horarwarsu sosai. Suka koya masu sanin Allah da bin kaidodin rayuwar Kirista. Dan ya kan ji uban yana addu'a cewa dan ya tuna sunan Ubangiji, wata rana kuma ya taimaka wajen ci gaban gaskiyarsa. Iyayen suka rika goyon bayan duk wani abin da ke iganta tarbiyya ko basirar yaran. Suka yi iyakar kokarinsu don shirya yaran domin rayuwa mai-anfani da kuma son ibada. Sabo da naciyarsu da ingancin halinsu, wani lokaci tsananinsu ya kan yi yawa; amma shi dan Canjin, ko da shi ke yakan san sun yi kuskure, yakan amince da horonsu.

A makaranta inda aka kai shi tun yana karamin yaro, an rika cin zalin Luther. Talaucin iyayensa ya sa lokacin da ya je makaranta a wani gari, akwai lokacin da sai ya bi gida gida yana raira waka kafin ya sami abinci, wani lokaci kuma ya fama da yunwa. Koyaswoyin camfi na addini a zamanin suka cika shi da tsoro. Yakan kwanta da dare cike da bakin ciki, yana tunanin munanan ababan da za su faru nan gaba, da tsoro kuma yana tunanin Allah kamar azalumin Mai-sahri'a, Mara-tausayi, maimakon Uba na sama Mai-nasiha.

Duk da haka, cikin manyan matsaloli da yawa, Luther ya ci gaba da himma don samun ingantaciyar tarbiyya da basiran da yake sha'awa. Ya yi kishin samun sani, halinsa na naciya da gaskiya kuma ya sa shi marmarin neman abu na kwarai maimakon mai-kyaun gani sama-sama kawai.

Sa'an da a shekarar sa ta sha-takwas ya shiga Jami'ar Erfurt, yanayin rayuwarsa ya fi na yarantakarsa kyau. Iyayen sa ta wurin tsimi da kwazo sun iya biyan dukan bukatunsa a

lokacin. Tasirin abokai na kirki kuma ya rage masa damuwar irin koyaswan da ya samu da farko. Ya shiga nazarin muhimman mawallafan litattafai, yana sah'awar tunaninsu, yana koyo kuma daga hikimarsu. Ko a kalkashin muguntar mallamansa na farko ma ya ba da alamar yin fice, da ababa suka kara kyau kuwa, tunaninsa ya kara inganci da sauri. Iya tuna abu, hangen nesa, azanci mai-kyau da kuma aiwatar da kudurorinsa sun sa nan da nan ya yi fice cikin abokansa. Ingancin basira ya nunar da ganewarsa, ya kuma ba shi tunani da ganewan da suka shirya shi domin tankiyar rayuwarsa.

Tsoron Ubangiji ya kasance cikin zuciyar Luther ya kuma sa shi ya rike amincinsa ga manufarsa, wanda ya kai shi shiga kaskantar da kai a gaban Allah. Ya dogara ga taimako daga Allah, bai kuma fasa fara kowace rana da addu'a ba, yayin da zuciyarsa ke rokon bishewa da goyon baya kowane lokaci. Sau da yawa yakan ce: "Yin addu'a da kyau shi ne rabi mafi kyau na nazari."

Yayin da yake duba littattafai a dakin karatun jami'ar, Luther ya gano Littafin, na harshen Latin. Bai taba ganin irin littafin nan ba. Bai san akwai shi ba ma. Yakan ji ana karatu daga Bishara ko Wasiku a wurin sujada, sai ya dauka cewa Littafin kenan dukansa. Yanzu kuma ya ga dukan maganar Allah gaba dayansa. Da ban-mamaki ya bude shi, zuciyarsa tana bugawa, ya karanta ma kansa kalmomi na rai, loto loto yana cewa: "Da dai Allah zai ba ni nawa littafi irin wannan!" Malaiku na sama suna gefensa, haske daga kursiyin Allah kuma ya bayana tmanin gaskiya ga ganewarsa. Kullum yana tsoron yi ma Allah laifi, amma yanzu sanin yanayin sa na mai-zunubi ya zo masa fiye da duk yadda ya taba ji.

Marmarin samun yanci daga zunubi da samun salama da Allah ya sa shi ya shiga rayuwar zuhudu. Nan aka bukace shi ya yi ayukan kaskanci, yana kuma bara gida gida. Shekarunsa sun kai inda a kan so bangirma sosai, wadannan ayuka na kaskanci kuwa suka ci masa mutunci sosai; amma ya jimre cin mutuncin, yana gani kamar wannan wajibi ne gare shi sabo da zunubansa.

Kowane zarafi ya samu yakan shiga nazari, yana hana kan shi barci, da kyar ma yakan sami damar cin abinci. Fiye da komi, yakan ji dadin nazarin maganar Allah. Ya sami wani Littafi da aka daure da tsarka a jikin bango, kuma sau da yawa yakan je wurin. Sa'an da ya kara sanin zunubinsa, ya yi kokarin samun gafara da salama ta wurin ayukansa. Ya yi rayuwa ta fama sosai, yana azumi, yana kwana gani, ya yi ma kansa bulala ma wai domin shi danne muguntarsa ta mutumtaka, wadda kuma rayuwar zuhudu ta kasa magancewa. Bai yi shakkar yin kowace sadakar da za ta kawo masa tsabtar rai da zai sa ya sami karbuwa ga Allah ba. Daga baya ya ce: "Da ni dan zuhudu ne mai-son addini, na kuma bi kaidodin kungiya ta filla filla. Da wani dan zuhudu zai iya zuwa sama ta wurin ayukansa, da ni na samu.... Da na kara ci gaba cikin zuhudu, da na kai kai na har ga mutuwa." Ta wuin wannan rayuwar, karfin sa ya kare, ya kuma fama da tsanani, bai kuwa warke daga wannan ba har

mutuwar sa. Amma duk da famarsa, zuciyarsa bat a hu ta ba. Daga baya ma har ya kusan sallamar da komai.

Sa'anda Luther ya ga kamar ba shi da bege, Allah ya tanada masa aboki mai-taimako kuma. Mai-ibadan nan Staupitz ya bayana ma Luther maganar Allah, ya kuma bukace shi ya bar tunani game da kansa, ya dena tunanin horo mara iyaka sabo da ketarewar dokar Allaha, ya dubi Yesu Mai-ceto Mai-gafarar zunubai. "Maimakon azabtar da kan ka sabo zunubanka, ka jefa kanka cikin hannuwan Mai-fansa. Ka amince da Shi da adalcin rayuwarsa, da kafarar mutuwarsa.... saurari Dan Allah. Ya zama mutum domin ya ba ka tabbacin alherin Allah ne." "Ka yi kaunar Shi wanda Ya fara kaunarka." Kalmominsa sun yi tasiri ga tunanin Luther sosai, bayan fama da kurakurai da ya dade da su, ya iya gane gaskiyar, salama kuma ta zo zuciyarsa.

An nada Luther priest, aka kuma kira shi ya zama shehun mallami a Jami'ar Wuttenburg. Nan ya shiga nazarin Littafi cikin harsunan asali na Littafin. Ya fara koyarwa game da Littafin, ya bayana ma jama'a da yawa littafin Zabura da Wasikun, da Bishara, har suka fahimta. Abokinsa Staupitz ya roke shi ya hau bagadi, ya yi wa'azin maganar Allah. Luther ya yi jinkiri, yana ganin kansa bai isa ya yi ma mutane Magana a madadin Kristi ba. Bayan doguwar mahawara ne ya yarda da shawarar abokin. Kafin nan ya rigaya ya kware a sanin Littafin, alherin Allah kuma ya kasance a kansa. Iya maganan sa ya jawo hankulan masu jinsa, yadda ya bayana gaskiyan a fili da karfi kuma, ya sa sun fahimta suka kuma yarda, kwazonsa kuma ya taba zukatansu.

Luther dai dan ekklesiyar Rum ne, bai ko yi tunanin barin ta ba. Cikin shirin Allah sai aka sa shi ya ziyarci Rum. Ya yi tafiyarsa a kafa, ya rika kwana a mazamnan 'yan zuhudu a hanyarsa. Ya yi mamakin wadata da kyau da holewan da ya gani a wani gidan ma'aikatan ekklesiya. Sabo da makudan kurdi da suke da shi, 'yan zuhudun suka zauna a manyan gidaje, masu-kyau sosai, suna saye da tufafi mafi-tsada, suna kuma cin abinci mai-kyau sosai. Luther cikin fushi ya gwada wannan da rayuwarsa ta kunci da musun kai, da wahala. Zuciyar sa ta damu kwarai.

Daga baya ya hangi birnin daga nesa. Sai ya durkusa a kasa, da babban murya kuma ya ce, "Rum mai-tsarki, na gaishe ki!" Ya shiga birnin, ya ziyarci ekklesiyoyin, ya saurari labaru na ban mamaki ta bakin priestoci da 'yan zuhudu, ya kuma yi dukan al'adun da akan yi. Ko ina, ya ga wurare da suka cika shi da mamaki da kyama ma. Ya ga cewa akwai zunubi cikin ma'aikatan ekklesiya. Ya ji priestoci suna ba'a ta rashin kunya, ya kuma yi kyamar rashin tsabtar ransu, har a lokacin mass ma. Yayin ma'amalar sa da yan zuhudu da mutanen gari, ya sadu da barna da fasikanci. Duk inda ya je ya sadu da abin kyama ne maimakon tsarki. In ji shi, "Ba wanda zai yi zaton irin zunubi da aikin mugunta da ake yi a Rum; sai an gani an kuma ji za a gaskata. Sabo da haka sun cika cewa 'Idan akwai lahira an gina Rum a kan ta ne: rami mara-matuka ce ita, daga inda kowane irin zunubi ke fitowa.' "

Ta wurin wata doka, paparuma ya yi alkawalin wata gafara ga dukan wadanda za su hau “Matakalan Bilatus,” inda aka ce Mai-ceto mu Ya bi Ya sauko daga dakin shari’ar, wai kuma ta hanyar ban al’ajibi aka dauki matakalan daga Urushalima zuwa Rum. Wata rana Luther yana hawan matakalan nan da zuciya daya, sai faraf daya murya kamar tsawa ta ce masa: “Amma mai-adilchi da bangaskiya za ya rayu.” Romawa 1:17. Ya tashi tsaye ya bar wurin maza maza cikin kunya. Nassin nan bai taba rasa karfin ikon sa ga rayuwar Luther ba kuma. Daga lokacin ya kara ganin wautar dogara ga ayukan mutum domin samun ceto, ya kuma ga cewa tilas a ba da gaskiya kullum ga Kristi. An bude idanunsa, kuma ba za a sake rufe su ba, game da rudi na tsarin paparuma. Sa’an da ya juya fuskarsa daga Rum, ya juya zuciyarsa ma, kuma daga wannan lokacin, rabuwar ta dinga karuwa ne, har ya rabu da ekklesiyar paparuma kwatakwata.

Bayan dawowansa daga Rum, Luther ya sami digiri na likata a fannin addini a Jami’ar Wuttenburg. Yanzu yana da yancin dukufa ga Littafi fiye da duk wani lokaci da ya gabata. Ya yi alkawalin yin nazari a hankali da kuma yin wa’azin maganar Allah da aminci, ba furcin su paparuma da koyaswoyinsu ba, duk tsawon ransa kuwa. Yanzu shi ba kawai dan zuhudu ba ne ko kuma mallami, amma mai-izinin koyar da Littafi ne. Kalmomin nan sun girgiza tushen daukakar paparuma. Sun kunshi muhummin kaidar Canjin.

Luther ya ga hadarin daukaka tunanin mutane bisa maganar Allah. Ba tsoro ya soki rashin gaskiyan mallaman makaranta, ya kuma yi hamayya da ussan ilimi da tauhidin da ya dade yana tasiri kan mutane. Ya soki irin koyaswoyin, cewa ba su da anfani, kuma suna da hatsari sosai, sai ya so ya juya tunanin masu jinsa daga karyar masanan ussan ilimi da masanan tauhidi zuwa gaskiya ta har abada, wadda annabawa da manzani suka bayana.

Sakon da yakan bayar ma jama’an da suka gaskata shi yana da daraja sosai. Ba su taba jin irin koyaswan nan ba. Albishir na kaunar Mai-ceto, tabbacin gafara da salama ta wurin jinin kafararsa, sun ba su murna da bege mara karewa. A Wittenburg an kunna wani haske wanda zai kai karshen duniya, kuma zai rika kara haskakawa har karshen lokaci.

Amma haske da duhu ba za su iya daidaituwa ba. Tsakanin gaskiya da kuskure akwai sabani mara boyuwa. Goyon bayan dayan sabani ne da na biyu din. Mai-ceton mu da kansa Ya ce: “Na zo ba domin in koro salama ba, amma takobi.” Matta 11:34. Shekaru kadan kuma bayan an fara Canjin, Luther ya ce: “Allah ba Ya bishe ni, yana ingiza ni ne zuwa gaba. Yana dauke ni. Ni ba mai-gidan kai na ba ne. Ina marmarin zaman hutu; amma ana jefa ni cikin tsakiyar hargitsi da juyin dan wake.” Yanzu an kusa a roke shi ya shiga hamayyar kenan.

Ekklesiyar Rum ta yi kasuwanci da alherin Allah. Teburan masu canja kurdi (Matta 12:12) sun kasance a gefen bagadin ekklesiya, iska kuma ta cika da surutun masu saye da sayarwa. Kalkashin cewa wai ana tara kurdi don gina majami’ar Saint Peter a Rum aka rika tallan gafarar zunubi! Amma hanyar da aka dauka don cika burin Rum ta haifar da bugu

mafi saurin kisa ga ikonta da girmanta. Wannan ne ya haifar da magabcin tsarin paparuma mafi himma, mafi nasara kuma.

Hafsan da aka nada ya gudanar da jarin gafaran nan a Jamus, mai suna Tetzel, an rigaya an hukumta shi sabo da laifuka ga jama'a da kuma laifuka ga dokar Allah; amma bayan ya tsere ma horo don laifukansa, sai aka dauke shi aikin ci gaba da munanan laifofin nan na paparuma. Ba kunya ya dinga maimaita karyan, yana ba da labarun karya domin a rudi jahilai masu saukin rudi, masu camfi kuma. Da suna da maganar Allah da ba a rude su hakanan ba. Domin a rike su kalkashin ikon paparuma ne, domin a kara iko da wadatar shugabanci kansu ne aka hana su Littafin.

Yayin da Tetzel ya shiga garin, wani masinja yakan wuce gabansa yana sanarwa: "Alherin Allah da Uba Mai-trsarki yana gaban gidanku." Mutane kuma suka marabci makaryacin nan kamar Shi Allah kan Sa ne Ya sauko wurinsu daga sama. Aka kafa wannan ciniki a cikin ekklesiya, Tetzel kuma yakan hau bagadi ya sanar cewa gafaran da ake sayarwa it ace kyauta mafi girma daga Allah. Ya ce ta wurin takardun nan nasa na shaidar gafara dukan zunuban da mai saye zai so ya sake aikatawa za a gafarta masa, kuma wai ba ya bukatar tuba ma. Fiye da wannan, ya tabbatar ma masu jinsa cewa gafara tana da ikon ceto ba kan masu rai kadai ba, har da matattu; cewa da zaran kurdin ya taba gindin tasar sa, ruhun wanda aka ba da kurdin a madadinsa zai tsere daga purgatory ya je sama.

Sa'an da Simon Magus ya sayi ikon yin al'ajibai daga wurin manzanin, BItrus ya amsa masa: "Azurfarka ta lalace da kai, tun da ka aza a ran ka za ka sami kyautar Allah da kurdi." Ayuka 8:20. Amma dubbai suka karbi tayin Tetzel da suari ma. Zinariya da azurfa suka rika kwararowa cikin baitulmalinsa. Ceto da za a iya saye da kurdi ya fi saukin samu da wanda ke bukatar tuba da bangaskiya da kokarin kin zunubi da yin nasara da shi kuma cikin natsuwa.

Masana a cikin ekklesiyar Rum sun yi jayayya da koyaswan nan na sayar da gafara, kuma akwai da yawa da basu yarda da rudin nan da ya saba ma hankali da ruya ba. Ba ma'aikacin ekklesiya da ya isa ya yi jayayya da mugun cinikin nan, amma zukatan mutane sun far damuwa, da yawa kuma suka fara tambaya ko Allah ba zai iya bin wata hanya don tsarkake ekklesiyar Sa ba?

Luther, ko da shi ke dan tsarin paparuma ne, na kwarai kuwa, ya cika da kyamar sabon da masu sayar da gafaran nan suka dinga yi. Da yawa daga majami'an da yake sujada sun sayi takardun shaidar gafaran, kuma suka fara zuwa wurin paston su suna furta zunuban su, suna kuma zaton zai yafe masu, ba don sun tuba ba, amma domin sun sayi gafara. Luther ya hana yafewar, ya kuma gargade su cewa in ba sun tuba suka sake rayuwarsu ba, za su mutu cikin zunuban su. Cikin mamaki suka koma wajen Tetzel da kukan cewa mai-karban furcin zunubansu ya ki takardun shaidar gafaran da shi Tetzel ya sayar masu; wadansu ma suka ce a mayar masu da kurdinsu. Tetzel ya fusata sosai. Da la'ana iri iri,

mafi muni, ya sa aka kunna wuta a wuraren taron jama'a, sa'an nan ya sanar da cewa shi "ya karbi umurnin daga paparuma cewa ya kone dukan masu-ridda da suka yi jayayya da takardun gafararsa mai-tsarki."

Luther yanzu kuma ya shiga aikinsa na jarumin gaskiya, ba tsoro. Akan ji muryarsa daga bagadi yana kashedi da gaske. Ya bayana ma mutane munin zunubi, ya kuma koya masu cewa ba zai yiwu ma mutm, ta wurin ayukansa, ya rage munin laifin zunubinsa ko kuma ya kauce ma horon ba. Ba abin da zai iya ceton mai-zunubi sai tuba ga Allah da bangaskiya ga Kristi. Ba za a iya sayen alherin Allah ba; kyauta ce. Ya shawarci mutanen kada su sayi takardun shaidar sayen gafaran nan, amma cikin bangaskiya su dubi Mai-fansa da aka giciye. Ya ba da labarin kokarinsa a banza don samun ceto ta wurin kaskantar da kai da wahalar da kai, ya kuma tabbatar ma masu jinsa cewa ta wurin rabuwa da kansa, da kuma ba da gaskiya ga Kristi ne ya sami salama da farin ciki.

Yayin da Tetzel ya ci gaba da cinikinsa, da rashin imaninsa, Luther ya shirya jayayya mafi dacewa game da kurkuran nan. Nan da nan dama ta samu. Majami'ar Wittenburg ta mallaki sifofi da yawa da akan nuna ma mutane a wadansu ranaku masu tsarki, sa'an nan akan ba da cikakkiyar yafewar zunubi ga dukan wadan da suka zo majami'a ranan, suka kuma furta zunubansu. Don haka, wadannan ranakun mutane da yawa sukan taru a wurin. Daya daga cikin muhimman ranakun nan, watau bukin Dukan Tsarkaka ta kusato. Kwana guda kafin ranar bukin, Luther, cikin jerin mutanen da ke tafiya zuwa majami'ar, ya manna wata walka kunshe da dalilai guda tasa'in da biyar da suka nuna kurakuran koyaswar cinikin gafarar. Ya bayana cewa yana shirye ya kare dalilan nan washegari a jami'a, idan akwai wadanda ke shirye su kushe su.

Ra'ayoyin nasa sun ja hankalin duniya. An karanta su akai akai ta kowace fuska. An zaburar da jami'a da birnin kuma kwarai. Ra'ayoyin nan sun nuna cewa ba a taba ba paparuma, ko kuma wani mutum ma, ikon gafarta zunubi ko yafe horonsa ba. Tsarin gaba daya rudi ne, dabarar Shaitan don hallaka rayukan wadanda suka gaskata rudinsa. An kuma nuna a fili cewa bisharar Kristi ce tamani mafi-girma ga ekklesiya, kuma alherin Allah da aka bayana a ciki kyauta ce ga dukan mai-bidar ta tawurin tuba da bangaskiya.

Ra'ayoyin Luther sun bukaci mahawara, amma ba wanda ya isa ya ta da mahawarar. Ababan da ya fada sun yadu ko ina a Jamus cikin kwanaki kadan, kuma cikin makoni kadan suka kai duk inda Kirista suke. Manyan Romawa da suka gane suka kuma yi bakin cikin zunubin da ya mamaye ekklesiyar, amma ba su san yadda za su tsayar da shi ba, sun karanta ra'ayoyin Luther da murna sosai, suka gane muryar Allah a ciki. Sun gane cewa Allah Ya sa hannu domin Ya tsayar da ci gaban zunubin da ke bulbulowa daga Rum. 'Ya'yan sarakuna da Majistarori suka yi murna a boye cewa za a tsayar da tsarin nan da ya hana daukaka kara daga hukumcin Rum.

Amma jama'a masu kaunar zunubi sun tsorata domin an share dabarun da suka kwantar masu da rai. Ma'aikatan ekklesiyar da aka hana su goyon bayan zunubi suka kuma ga hanyar samun kurdin su za ta rufu, suka fusata, suka kuma nace za su ci gaba da ayukan su. Luther ya gamu da masu zargi da sun rigaya sun fusata. Wadansu suka ce ya yi gaggawa da rashin tunani. Wadansu suka zarge shi da ganganci, cewa ba Allah ne Ya ba shi umurni ba, amma girman rai da zafin kai ne suka tura shi. Ya amsa da cewa: "Wane ne bai san cewa duk wanda ya kawo sabon ra'ayi akan gan shi kamar mai-girman kai ne, mai-neman ta da fitina ba?... Don me aka kashe Kristi da dukan adilai da aka kashe? Domin an gan su kamar masu rena hikimar zamaninsu ne, kuma domin sun fito da sabobin ra'ayoyi ba tare da neman shawarar masanan tsofofin ra'ayoyin ba."

Ya kuma ce: "Duk abin da ni ke yi zan yi ne, ba ta wurin hikimar mutane ba, amma ta wurin bishewar Allah. Idan aikin na Allah ne, wa zai tsayar da shi? Idan ba na Allah ba ne, wa zai ci gaba da shi? Ba nufi na ba, ko nasu ko namu; amma nufinka, ya Uba Mai-tsarki, wanda ke cikin sama."

Ko da shi ke Ruhun Allah ne ya motsa Luther ya far aikinsa,ya gamu da tankiya sosai. Zarge zargen magabtansa, da karyarsu game da manufofinsa, da karyarsu game da halinsa da burinsa, sun abko masa kamar ambaliya; sun kuwa shafi aikinsa. Ya dauka cewa shugabanni na makaranta da na ekklesiya za su hada kai da shi don samun canji. Kalmomin karfafawa daga manyan mutane sun ba shi bege da murna. Sai ya ga kamar rana ta haskaka ma ekklesiya. Amma kafafawa ta koma reni da zargi. Manya da yawa na ekklesiya da na kasa sun gamsu da ra'ayoyinsa; amma suka ga karban koyaswoyin zai kunshi manyan canje canje. Wayar da kan mutane da kuma canja su zai rage ikon Rum, ya tsayar da dubban kurdade da ke shigowa baitulmalinta yanzu, ta haka kuma zai rage bushasha da almubazzaarancin shugabannin tsarin paparuma. Ban da haka, koya ma mutane yin tunani da aikatawa kamar masu hankali, suna duban Kristi kadai don cetonsu, zai hambarar da gadon sarautan paparuma, ya kuma lalata nasu ikon. Don haka suka ki sanin da Allah Ya ba su, suka kuma jera kansu don jayayya da Kristi da gaskiyar kuma a wurin yin jayayya da mutumin da ya aiko domin wayar da kansu.

Luther ya raunana sa'an da ya dubi kansa , mutum daya sabain ikoki mafi girma na duniya. Wani lokaci yakan yi shakka ko da gaske Allah ne Ya bishe shi ya ja daga da ikon ekklesiya. Ya rubuta cewa: "Wane ne ni in ja da martabar paparuma, wanda a gabansa ...sarakunan duniya da duniyar kan ta ke rawan jiki?... Ba wanda zai iya sanin wahalan da zuciya ta ta sha cikin shekaru biyu na farkon nan, da kuma irin yankan kauna da na shiga." Amma ba a bar shi ya karai gaba daya ba. Sa'an da ya rasa goyon bayan mutane, yakan dubi Allah kadai, ya gane kuma cewa zai iya dogara ga hannun nan Mai-cikaken iko.

Luther ya rubuta ma wani abokin Canjin cewa: "Ba za mu iya fahimtar Littafin ta wurin nazari ko basira ba. Wajibi ne ka fara da addu'a. Ka roki Ubangijji cikin jinkansa Ya ba ka ganewar gaskiyar maganarsa. Ba wani mai-fasarar maganar Allah kamar wanda Ya

wallafa ta, gama Shi da kan Sa Ya ce, ‘Allah zai koya ma dukansu’ kada ka yi begen komi daga aikinka, daga ganewar kanka: ka dogara ga Allah kadai, da kuma tasirin Ruhunsa. Ka gaskata wannan da shi ke maganar wanda ya gogu ne.” Wannan darasi ne mai muhummanci kwarai ga wadanda ke ji cewa Allah Ya kiraye su domin su bayyana ma wadansu muhimman gaskiya na wannan zamani. Gaskiyan nan za su ta da magabtakan Shaitan da masu kaunar tatsuniyoyin da ya kirkiro. Cikin sabani da ikokin mugunta akwai bukatar wani abu fiye da karfin basira da hikimar mutum.

Yayin da magabta suka dogara ga al’ada ko kuma furcin paparuma ko ikonsa, Luther yakan nuna masu Littafin ne kawai. Nan ne akwai zantattukan da ba za su iya kushewa ba, don haka bayin nan na camfi suka bidi jininsa, yadda Yahudawa suka bidi jinin Kristi. Suka ce: “Mai-ridda ne. Babban cin amana ne a bar kazamin mai-riddan nan da rai har tsawon sa’a guda nan gaba. Bari a kafa dakalin da za a rataya shi maza maza!” Amma fushinsu bai cinye Luther ba. Allah Yana da aiki dominsa, aka kuwa aiko malaikun sama domin su tsare shi. Amma da yawa da suka karbi hasken daga wurin Luther sun gamu da fushin Shaitan, ba tsoro suka fuskanci azaba da mutuwa.

Koyaswoyin Luther sun jawo hankulan masu tunani ko ina a Jamus. Daga wa’azin sa da rubuce rubucensa haske ya rika fitowa yana haskaka dubban mutane. Bangaskiya mai-rai ya fara daukan wurin matacen tsarin al’adun nan da ya rike ekklesiya da dadewa. Mutane suka fara shakkar camfe camfen ekklesiyar Rum. Shingen wariya sun fara watsewa. Maganar Allah da Luther ya rika gwada kowace koyaswa da ita, kamar takobi ne mai-kaifi biyu; yana yanka hanyar sa zuwa zukatan mutanen. Ko ina marmarin ci gaban ruhaniya ya fara tasowa. Ko in aka sami yunwa da kishin adalci irin da ba a taba gani ba da dadewa. Idanun mutane da aka dade ana nuna masu al’adun mutane da matsakanta na duniya, yanzu kuma sun fara juyawa cikin tuba da bangaskiya zuwa wurin Kristi, Shi wanda aka giciye.

Jawowar hankalin nan ya kara tsoratar da mahukumatan tsarin paparuma. Luther ya sami sammaci cewa ya je Rum don amsa tuhumar ridda. Umurnin ya cika abokansa da tsoro. Sun san hadarin da ke kansa a birnin nan da ya riga ya shawu da jinin amintattun Yesu. Suka ki yarda da tafiyarsa Rum, suka ce a tuhume shi a Jamus.

Daga bisani an yarda da wannan shirin, aka zabi jakadan paparuma ya ji tuhumar. Cikin umurnin da paparuma ya ba jakadan, an ce an rigaya an sanar da cewa Luther mai-ridda ne. Don haka aka umurci jakadan ya zarga ya kuma hukumta, ban da jinkiri. Idan ya nace, har kuma jakadan ya kasa kama jikin Luther din, an ba shi dama “ya hana shi zuwa ko ina a Jamus; ya kora, ya la’anta, ya kuma ware dukan wadanda suka yarda da shi.” Bayan haka, paparuma ya umurci jakadan nasa, domin dai a batar da annoban riddan, ya ware duka, komi girman su a ekklesiya ko a kasar, ban da sarkin, wadandan duk suka ki kama Luther da masu binsa, su tura su ga ramuwar Rum.

Nan ne aka bayana ainihin ruhun tsarin paparuma. Babu ko alamar Kiristanci ko kaidar adalci ma a cikin takardar umurnin. Luther yana da nisa sosai daga Rum; bai sami dammar bayana matsayinsa ba, duk da haka kafin a bincika tuhumarsa, an hukumta cewa shi mai-ridda ne, a rana dayan kuma aka tsauta masa, aka tuhume shi, aka hukumta shi, aka kuma iske shi da laifi; kuma mai-karyan kiran kansa uba mai-tsarki, makadaici, madaukaki, mai-iko, mara-kuskre, a kasa ko ekklesiya, shi ne ya yi haka.

A awannan lokaci da Luther ya bukaci goyon baya da shawarar abokan gaskiya, Allah Ya aiko Melanchthon zuwa Wittenberg. Matashi ne mai-kamewa, hikimarsa da yawan iliminsa, da iya maganansa sun hadu da tsabtar halin sa da nagartarsa, suka jawo ma Melanchthon farin jini da ban girma. Kyaun baye bayensa bai fi halinsa na tawali'u karbuwa ba. Nan da nan ya zama almajirin bisharar, kuma abokin Luther mafi aminci da mai-goyon baya mafi tamani, tawali'unsa da hankalinsa da natsuwansa suka rika jan linzamin jaruntakar Luther da karfin halinsa. Haduwarsu cikin aikin ta kara ma Canjin karfi ta kuma karfafa Luther sosai.

An zabi Augsburg ne inda za a yi shari'ar, Luther kuma ya kama hanya da kafa zuwa wurin. An ji masa tsoro sosai. An rigaya an yi barazana a fili cewa za a kama shi a kashe shi a hanya, kuma abokansa suka roke shi kada ya je. Har ma sun roke shi ya bar Augsburg na wani lokaci, ya nemi mafaka a wurin wadanda za su kare shi. Amma ya ki barin wurin da Allah Ya sa shi. Dole zai ci gaba da rikon gaskiya da aminci, komi hare haren da ke zuwa masa. Maganarsa it ace: "Ni kamar Irmiya ne, mutum mai-fama da kuma yawan hamayya; amma yayin da barazanan nan ke karuwa, haka murna ta take yawaita.... Sun rigaya sun bata daraja ta da suna na. Abu daya kawai ya rage; jikin nan nawa mara-martaba: su dauke shi; ta haka za su takaita rayuwa ta, na tsawon sa'o'i kalilan. Amma ruhu na kam, ba za su iya daukewa ba. Duk wanda ke so ya yi shelar maganar Allah ga duniya, dole ya yi tsammanin zai iya mutuwa ko wane lokaci."

Labarin isowar Luther Augsburg ya gamsar da jakadan paparuma sosai. Fitinannen mai-riddan nan da ya ja hankalin dukan duniya ya shigo kalkashin ikon Rum, jakadan kuma ya kudurta cewa ba zai tsira ba. Luther bai samo ma kansa kariya ba. Abokan shi sun gargade shi kada ya halarci wurin shari'an ba tare da tsaro ba, su kansu kuma suka so su samo masa tsaron daga wurin sarki. Jakadan ya so ya tilasta Luther ya janye ra'ayinsa, ko kuma ya sa a a kai shi Rum, domin a yi masa yadda aka yi ma Huss da Jerome. Sabo da haka ta wurin wakilan sa, ya yi kokrain sa Luther ya bayana ba tare da kariya ba, domin ya yi abin da ya ga dama da shi. Luther kuwa ya ki yin hakan. Sai da ya karbi takardar shaidar kariyar sarki kafin ya bayana a gaban jakadan paparuman.

Bisa ga al'adarsu, Romawan sun so su ja hankalin Luther ta wurin nuna kamanin tawali'u. Jakadan a cikin hirarsu, ya nuna kamanin abota sosai; amma ya bukaci Luther ya yarda da ikon ekklesiya kawai ba hamayya ko tambaya. Bai san halin mutumin da yake magana da shi ba. Cikin amsarsa Luther ya nuna ban girman sa ga ekklesiya, burin sa na

tabbatar da gaskiya, shirinsa don amsa kowace tambaya game da ababan da ya koyar, ya kuma mika koyaswoyinsa ga binciken wadansu fitattun jami'o'i. Amma kuma ya ki yarda da bukatar jakadan cewa ya janye ba tare da ya nuna masa kuskurensa ba.

Martaninsa kawai ita ce: "Ka janye, ka janye!" Luther ya nuna cewa matakin da ya dauka daidai yake da Littafi ya kuma nace cewa ba zai musunci gaskiya ba. Sa'an da jakadan ya kasa amsa maganar Luther, sai ya dinga tura masa ashar, da ba'a, da fadanci, yana surkawa da wadansu maganganu daga al'ada da furcin ubanin ekklesiya, amma bai ba Luther damar yin magana kuma ba. Da ya ga taron ba zai haifar da komi ba, a karshe Luther ya sami iznin mika amsarsa a rubuce.

Ya rubuta ma wani abokin sa cewa: "Ta wurin yin haka, wulakantace ya kan sami riba kashi biyu: na daya, watakila za a ba wadansu abin da aka rubuta din su duba; na biyu kuma mutum yakan sami damar taba lamirin wani azalumi mai-fadin rai da yawan magana, wanda da zai fi karfin ka da maganganu irin na manya kawai."

Ya gabatar da gajeruwar bayani a fili, mai-karfi kuma, na ra'ayoyinsa cike da nassosin Littafin da suka goyi bayan ra'ayoyin. Bayan ya karanta takardar bayanin, sai ya mika ma jakadan, shi kuwa ya jefa ta a gefe da reni, yana cewa tarin kalmomin banza ne kawai da ba su dace ba. Luther kuwa ya fusata, sai ya ba shi amsa daga al'adu da koyaswoyin ekklesiya, ya kuwa nuna kurakuran jakadan.

Sa'an da jakadan ya ga ba zai iya amsa koyaswar Luther ba, ya kasa kame kansa, cikin fushi kuma ya ta da murya ya ce: "Ka janye! ko kuma in aika da kai Rum, inda za ka bayana a gaban masu shari'an da aka zaba su yi shari'arka. Zan ware ka da dukan magoya bayanka, da dukan wadanda daga baya za su karbe ka, zan kuma cire su daga ekklesiya." A karshe cikin fushi ya ce: "Ka tuba, ko kuma kada ka dawo kuma."

Nan da nan Luther ya fice tare da abokansa, sa'anda ya nuna cewa ba zai taba janyewa ba. Ba abin da jakadan ya nufa kenan ba. Ya rigaya ya rudi kansa cewa ta wurin anfani da karfi zai razana Luther ya yi biyayya, yanzu kuwa da aka bar shi tare da masu goyon bayansa, ya dube su daya bayan daya, yana mamakin kasawar dabarunsa.

Kokarin Luther a wannan karo ya haifar da sakamako masu kyau. Tarin jama'a da suke wurin sun sami zarafin gwada mutum biyu din nan don kansu, ko wane irin ruhu ne suka nuna, da kuma kafri da gaskiyar matsayin da suka dauka. Bambancin ya yi yawa! Luther mai-saukin kai da tawali'u da karfi, ya tsaya cikin karfin Allah, a gefen gaskiya; wakilin paparuma kuwa, ga ji cewa shi wani abu ne, ga son duniya, ga alfarma, ga rashin kima, ba shi kuma da goyon baya daga Littafin, amma ya yi ta ihu da naciya cewa: "Ka janye ko kuwa a aika da kai Rum domin a hore ka."

Duk da cewa Luther ya rigaya ya sami kariya, yan ekklesiyar Rum din nan sun so su kama shi su sa shi a kurkuku. Abokansa suka ce masa, tun da zamansa a Augsburg din ba

anfani kuma, gara kawai ya koma Wittenberg maza maza, kuma a yi hankali sosai kada a gane abin da yake shirin yi. Sabo da haka ya bar Augsburg kafin wayewan gari, a kan doki, daga shi sai mai-nuna masa hanya wanda majistare ya ba shi. Da rashin tabbachi, a boye ya wuce ta titunan birnin cikin duhu. Magabta masu tsaro da zalunci suna shirin hallaka shi. Ko zai tsere ma tarkokin da aka shirya masa? Wannan lokaci ne na fargaba da addu'a sosai. Ya kai wata karamar kofa a ganuwar birnin. Aka bude masa, tare da mai-bishe shi, ba matsala. Da zaran sun fita sai suka kara hanzari, kuma kafin jakadan ya san cewa Luther ya gudu, ya rigaya ya wuce inda masu tsananta masa za su iya kama shi. An ka da Shaitan da 'yan sakonsa. Mutumin da suka zata yana kalkashin ikonsu ya rigaya ya tafi, ya tsere kamar tsuntsu daga tarkon mai-farauta.

Sa'an da jakadan ya sami labarin tserewar Luther, ya cika da mamaki da fushi kuma. Ya dauka zai sami lada mai yawa sabo da hikimar sa da naciyarsa wajen ladabtar da mai-damun ekklesiyan nan; amma begen sa bai yiwu ba. Ya bayana fushinsa cikin wasikarsa zuwa ga Fredrick mai-zaben Saxony, inda ya bukace shi ya tura Luther zuwa Rum, ko kuma ya kore shi daga Saxony.

Don kare kansa, Luther ya bidi jakadan ko kuma paparuma ya nuna masa kuskurensa daga Littafi, ya kuma yi alkawalin rabuwa da koyaswoyin sa idan har an nuna cewa sun saba ma maganar Allah. Ya kuma gode ma Allah cewa har shi ma an ga ya cancanta ya wahala sabo da imani.

A lokacin mai-zaben bai rigaya ya san koyaswoyin da aka canja ba, amma ya yi sha'awar gaskiya da karfi da saukin maganar Luther; kuma in ba an nuna kuskuren Luther ba, Fredrick ya kudurta zai zama mai-kare shi. Cikin amsar sa ga wasikar jakadan, ya rubuta cewa: "Da shi ke Likita Martin ya bayana gabanka a Augsburg, ya kamata ka gamsu. Ban zata za ka yi kokarin sa shi ya janye ba, sai bayan ka nuna masa kuskurensa. Ba wani masani a yankin mu da ya fada mani cewa koyaswar Luther ta saba ma imani, ko Kiristanci, ko kuma ridda ce ba.' Dan sarkin kuma ya ki tura Luther zuwa Rum, ko kuma shi kore shi daga kasarsa."

Mai-zaben ya ga cewa akwai lalacewar halayyan kirki a kasar. An bukaci babban aikin canji mai-girma. Tsarin nan mai-tsada da wuyan ganewa kuma, na horon laifi, ba zai zama da anfani ba idan mutane sun yi biyayya ga umurnin Allah da bukatun lamirin da ke da sani. Ya ga cewa Luther yana kokari ne ya cim ma wannan manufar, ya kuma yi farin ciki a boye cewa wata koyaswa mafi kyau tana shigowa ekklesiya.

Ya ga kuma a matsayin sa na shehun mallamin jami'a Luther yana nasara sosai. Shekara guda ce kadai ta wuce bayan ya manna ra'ayoyinsa a babban majami'an nan , amma yawan masu zuwa ekklesiyar Bukin Dukan Tsarkakan nan a Rum ya ragu sosai. Rum ta rasa masu sujada, da baiko kuma, amma wata kungiya ta dauki wurinsu, masu zuwa Wittenberg kenan, ba don yin sha'awar sifofin ta ba, amma dalibai masu neman sani.

Rubuce rubucen Luther sun ta da sabon marmarin Littafin, ko ina kuma ba daga Jamus kadai ba, amma daga wadansu kasashe ma dalibai suka rika tururuwa. Samarin da farkon zuwan su Wittenberg kenan suka "daga hannuwan su sama, suka yabi Allah da Ya sa hasken gaskiya ya haskaka daga birnin nan, kamar daga Sihiyona a zamanun da, daga inda kuma ya yadu zuwa kasashe mafi nisa."

Luther a lokacin nan bai gama tuba daga kurakuran tsarin paparuma ba. Amma yayin da ya gwada Littafi da dokokin paparuma da kundin tsarin mulkinsu, ya cika da mamaki. Ya ce: "Ina karanta dokokinsu paparuma, kuma...ban san ko paparuma ne ..... din nan da kansa ba ko mazon Kristi, an bata sunan Kristi aka kuma giciye Shi a cikin su." Duk da haka a wannan lokacin Luther mai-goyon bayan Ekklesiyar rum ne, kuma ba ya tunanin cewa zai taba rabuwa da ita.

Rubuce rubucen Luther da koyaswarsa sun ci gaba da yaduwa cikin Kirista. Aikin ya yadu har Switzerland da Holland. Kofen rubuce rubucensa suka kai Spain. A Ingila an karbi koyaswoyinsa kamar maganar rai. Maganar ta kai Belgium da Italiya ma. Dubbai sun rika falka daga barcinsu mai-kama da mutuwa, zuwa murna da begen rayuwa ta bangaskiya.

Rum ta kara damuwa game da hare haren Luther, kuma wadasu masu matukar gaba da shi, har da likitoci a jami'o'in Katolika, suka ce duk wanda zai kashe dan zuhudu mai-tawayen nan bai yi zunubi ba. Wata rana wani bako da ya boye karamar bindiga a kuntun sa ya je wurin Luther, ya tambaye shi don me yake tafiya shi kadai hakanan. Sai Luther ya amsa masa: "Ni ina hannun Allah ne. Shi ne karfi na da garkuwa ta. Mene ne mutum zai iya yi mani?" Da bakon ya ji wannan, sai jikin shi ya yi sanyi, ya gudu kamar yana gudun malaikun sama.

Rum ta nace sai ta hallaka Luther; amma Allah Shi ne kariyarsa. An ji koyaswoyinsa ko ina, "a kauyuka da gidajen ma'aikatan ekklesiya...a gidajen fadawa, a jami'o'i, da kuma gidajen sarakuna." Kuma manyan mutane suka rika tasowa ko ta ina suna goyon bayan kokarinsa.

Wajen wannan lokacin ne Luther, bayan ya karanta rubuce rubucen Huss, ya gane cewa babban gaskiyan nan na kubutarwa ta wurin bangaskiya wadda shi kansa ke kokarin koyarwa, Huss ma ya yarda da shi. Luther ya ce: "Ashe dukan mu, Bulus da Augustine da ni, almajiran Huss, ne amma ba mu sani ba!" ya ce: "Allah zai kama duniya da laifin cewa an yi mata wa'azin gaskiya shekaru dari da suka wuce amma aka kona gaskiyar!"

Cikin wani roko ga sarkin Jamus da fadawansa a madadin Canjin Kiristanci, Luther ya rubuta game da paparuma cewa: "Abin ban kyama ne a ga mutumin da ke kiran kansa wakilin Kristi yana nuna girma da kyau na ban mamaki wanda babu sarkin da ke da irinsa, kamanin Yesu matalauci ko Bitrus mai-tawali'u kenan? In ji su wai shi ne Ubangijin

duniya! Amma Kristi, wanda shi ya ce yana wakilta Ya ce, ‘Mulki na ba na wannan duniya ba ne. Ko mulkin wakili zai iya zarce na mai-gidansa?”

Game da jami’o’in, ya rubuta cewa: “Ina tsoro watakila jami’o’in za su zama kofofin lahira fa. In ba sun yi kokarin fassara Littafi da kyau, suna kuma zana shi cikin zukatan matasa ba. Ban shawarci wani ya sa yaran sa inda Littafi ba shi da fifiko ba. Kowace makarantar da ba a binciken maganar Allah lallai za ta lalace.”

Nan da nan aka kai sakon nan ko ina a Jumus, ya kuma yi tasiri sosai a kan mutane. Kasar gaba daya ta motsu, jama’a da yawa suka tashi suka goyi bayan canji. Magabtan Luther cike da neman ramuwa suka roki paparuma shi dauki matakai na karshe a kan Luther. Aka umurta cewa nan da nan a hana koyaswoyinsa. Aka kuma ba da masu goyon bayansa kwana shida su janye ko kuma a ware su.

Wannan ya zama babban damuwa ga Canjin. Da dadewa hukumcin warewa na Rum yana razana sarakuna; ya cika manyan kasashe da kaito da hallaka kuma. Wadanda aka ware su din akan rika kyamarsu da tsoronsu; akan raba su daga yin ma’amala da yan-uwa, a mai da su masu ketare doka da ya kamata a yi farautar su a kawar da s u. Luther ya san guguwar da ke fuskantar sa; amma ya nace, ya dogara ga Kristi shi zama taimakon sa da garkuwarsa. Da bangaskiya tare da karfin hali ya rubuta cewa: “Abin da ya kusa faruwa ban sani ba,...Bari naushin ya bugi inda ya ga dama, bana tsoro. Ko ganye ma ba ya faduwa sai da yardar Ubanmu. Ai kuwa zai fi lura da mu! Mutuwa don maganar Allah ba komai ba ne, tun da Kalman da ya zama nama Shi ma ya mutu. Idan mun mutu tare da Shi za mu rayu tare da Shi; kuma idan mun dandana abin da shi Ya dandana kafin mu, za mu kasance inda Shi yake mu kuma zauna tare da Shi har abada.”

Sa’an da umurnin paparuma ya kai wurin Luther, ya ce: “Na rena shi, na kuma yake shi, cewa rashin imani ne, karya ne kuma, ... Kristi da kansa ne ake hukumtawa a wurin.... ina farin ciki in sha wahalolin nan sabo da dalili mafi kyau. Na rigaya na fara jin karin yanci ma a cikin zuciyata; da shi ke yanzu na san cewa paparuma ne magabcin Kristi, kuma gadon sarautarsa na Shaitan kansa ne.”

Duk da haka umurnin Rum din ya yi tasiri, kurkuku, azaba da takobi makaman ta na tilasta biyayya kenan. Marasa karfin zuciya da masu camfi suka yi rawan jiki game da dokan nan na paparuma; kuma ko da shi ke ana tausaya ma Luther, da yawa sun ce ba za su sa rai cikin kasada wai sabo da canji ba. Bisa dukan alamu dai, aikin Luther ya kusan karewa.

Amma Luther bai ji tsoro ba dai. Rum ta rika tsitsine masa, duniya kuma ta na kallo, da tabbaci cewa Luther zai hallaka, ko kuma a tilasta shi ya karai. Amma da karfin gaske, ya mayar ma Rum da hukumcin nata a fili, kuma ya bayana aniyarsa ta rabuwa da Rum din har abada. A gaban taron dalibai, likitoci da ‘yan kasa, Luther ya kona umurninn paparuma, da dokokin ekklesiyar, da wadansu rubuce rubuce da suka karfafa ikon paparuman. Ya ce:

“Magabta na, ta wurin kona litattafai na, sun iya bata gaskiyan da ke cikin tunanin mutane, suka hallaka rayukansu kuma; dalilin kenan ni ma na rama ta wurin kona littattafansu. Babbar kokawa ta fara kenan. Kafin yanzu ina wasa ne kawai da papruma. Na fara aikin nan cikin sunan Allah ne; za a karasa shi ban da ni, da girman sunan Allah kuma.”

Ga zarge zargen magabtansa da suka rika yi masa ba’a game da rashin karfin famar tasa, Luther ya amsa: “Wa ya san ko Allah bai zabe ni, ya kira ni ba, kuma idan bai kamata su ji tsoron wannan ba, ta wurin rena ni su na rena Allah da kansa ne? Musa ne kadai lokacin Fitowa daga Masar; Iliya shi kadai ne a zamanin mulkin sarki Ahab; Ishaya shi kadai ne a Urushalima; Ezekiel ne kadai a Babila;... Allah bai taba zaben babban priest ko wani mai-martaba shi zama annabinsa ba; amma ya zabi mutanen da aka rena ne, har da Amos dan kiwo ma. A kowace sara tsarkaka sukan tsauta ma manya, da sarakuna da yarimai, da preistoci da masu-hikima, a bakin ransu.... Ban ce ni annabi ne ba; amma ina cewa ne ya kamata su ji tsoro domin ni kadai ne, su kuma suna da yawa. Na tabbatar da wannan, cewa maganar Allah tana tare da ni, kuma ba ta tare da su.”

Amma da wuyan gaske ne Luther ya dauki matakin karshe na rabuwa da ekklesiyar. Wajen wannan lokacin ne ya rubuta cewa: “Kowace rana ina kara jin wahalar rabuwa da tarbiyyan da mutum ya koya a kuruciyarsa. Ya zafe ni sosai, ko da shi ke ina da goyan bayan Littafi, cewa ni kadai in yi jayayya da paparuma, in kuma bayana cewa shi ne magabcin Kristi. Wadanne irin damuwoyi ne zuciyata ba ta shiga ba? Sau nawa ina ma kaina tamabayan nan da tsarin paparuma sun cika yi ma kansu, cewa: ‘Kai kadai ne mai-hikima? Watau dukan sauran mutane suna kuskure kenan? Yaya zai kasance idan ya zamana cewa kai ne mai-kuskuren, kuma kana jawo rayuka da yawa cikin kuskuren ka, har su kuma su hallaka har abada?’ Haka na dinga fada da kai na da Shaitan kuma, har sai da Kristi, ta wurin maganarsa mara kuskure, ya karfafa zuciya ta sabanin shakkun nan.”

Paparuma ya rigaya ya yi ma Luther barazana zai ware shi idan ya ki janyewa, sai kuma aka cika barazanar. Sabon umurni ya fito da ya sanar da rabuwar Luther daga ekklesiyar Rum, yana cewa Luther la’antace ne tun sama, haka ma dukan wadanda suka karbi koyaswarsa, la’antattu ne an shiga ainihin fadan ke nan.

Dukan wadanda Allah Ya ba su aikin gabatar da gaskiyar sa da ta je daidai da zamanin su sukan gamu da jayayya. A zamanin Luther akwai gaskiya ta lokacin. Gaskiya mai-muhimminci musamman ga wancan zamanin; akwai gaskiya ta yanzu domin ekklesiya ta yau. Shi wanda yake yin komi bisa ga nufinsa, Ya ga ya kamata ya sa mutane a yanayi dabam dabam, Ya kuma ba su aikin da ya dace da zamanin da su ke raye da kuma yanayin da Ya sa su a ciki. Idan suka ga muhimmincin hasken da Ya ba su, za a kara bude masu filayen gaskiya a gabansu. Amma yawanci yau ba su fi ‘yan tsarin paparuma da suka yi hamayya da Luther son gaskiya ba. Akwai son karban ra’ayoyi da al’adun mutane maimakon maganar Allah yau kamar sararakin da suka gabata. Kada masu-shelar gaskiya yau su zata za a karbe su da marmari fiye da ‘yan canji na da. Babban jayayya tsakanin

gaskiya da kuskure, tsakanin Kristi da Shaitan, zai kara zafi har zuwa karshen tarihin duniya.

Yesu Ya ce ma almairansa: “Da na duniya ne ku, da duniya ta yi kamnar nata; amma domin ku ba na duniya ba ne, amma ni na zabe ku daga chikin duniya, sabada wannan duniya tana kinku. Ku tuna da Magana wanda na fada maku, Bawa ba ya fin Ubangijinsa girma ba. Idan suka yi mani tsanani, su a yi maku tsanani kuma; idan suka kiyaye maganata, su a kiyaye taku kuma.” Yohanna 15:19, 20. Ta wancan gefen kuma Ubangijin mu Ya bayana a fili cewa: “Kaiton ku lokachin da dukan mutane za su yabe ku! gama hakanan ubanninsu suka yi ma makaryatan annabci.” Luka 6:26. Ruhun duniya yau bai fi na zamanin da can jituwa da Ruhun Kristi ba, kuma masu wa’azin maganar Allah da tsarkinta ba za a karbe su da amincewa da ta fi ta da din ba. Irin jayayyan zai iya canzawa, kiyayyar za ta zama a boye domin da zurfin wayo ake yin ta; amma magabtaka dayan ake yi, kuma za ta ci gaba har karshen lokaci.

Babi na 8— A Gaban Kotun Koli

Sabon sarki Charles V ya hau gadon sarautan Jamus ke nan, ‘yan sakon Rum kuma suka yi sauri suka je su yimasa barka, su kuma lallabe shi ya yi anfani da ikonsa ya hana Canjin. A wancan gefen kuma mai-zaben Saxony, wanda ya taimaki Charles samun rawaninsa, ya roke shi kada ya dauki wani mataki game da Luther har sai ya saurare shi. Wannan ya sa mai-zaben cikin halin rudewa da rikicewa. Babu abin da zai gamsar da ‘yan paparuman nan sai umurnin da zai sa a kashe Luther. Mai-zaben ya rigaya ya furta da karfi cewa, “Ko mai-martaba sarki, ko kuma wani mutum da bam, babu wani mutumin da ya nuna cewa an karyata rubuce rubucen Luther,” sabo da haka ya bidi “cewa a ba Likita Luther tsaro, domin ya bayana gaban hukuman nan na masana, masu ibada, masu-sahri’a marasa son kai kuma.”

Hankalin dukan mutane kuma yanzu ya koma ga majalisar kasashen Jamus da suka taru a Worms jima kadan bayan Charles ya hau gadon mulki. Akwai muhumman batutuwa da wannan majalisar za ta duba; na farko ke nan da ‘ya’yan sarautan Jamus za su fara saduwa ta shawarar majalisa da matashin sarkin nasu. Daga dukan bangarorin kasar, masu martaba na ekklesiya da na kasa, suka zo. Manyan kasa da ‘ya’yan sarauta da masu iko, masu-kishin yancin gadonsu; shugabannin ekklesiya, cike da sanin fifikonsu da ikonsu; fadawa masu-matsayin jarumtaka tare da barorinsu, rike da makaman su; da jakadu daga kasashen waje masu nisa - duka suka taru a Worms. Duk dai babban abin da ya fi daukan hankalin taron nan shi ne mai-canjin nan na Saxony, watau Luther.

Charles ya rigaya ya umurci mai-zaben ya zo majalisar tare da Luther, ya kuma tabbatar masa da tsaro, da alkawalin yin mahaware cikin sauki tare da masana, game da batutuwan da ake mahawara akai. Luther ya yi taraddadin bayanuwa gaban sarkin. Lafiyarsa a wannan lokacin ta ragu sosai; duk da haka ya rubuta ma mai-zaben cewa: “Idan ba zan iya zuwa Worms da koshin lafiya ba, zan je da rashin lafiyan nan nawa. Domin idan sarki ya kira ni, ba ni da shakka cewa kiran Allah ne da kansa. Idan suna so su yi anfani da karfi a kai na, wanda kuwa mai yiwuwa ne (domin ba don fadakarwarsu ne suka umurce ni in je ba), na bar batun a hannun Ubangiji. Har yanzu Yana da rai, Yana kuma mulki, Shi wanda Ya kiyaye samari ukun nan a cikin tanderun wuta. Idan ba zai cece ni ba, rai na ba komi ba ne. Mu dai mu kare bishara daga renin miyagu, mu kuma zub da jininmu domin bisharar, domin kada miyagun su yi nasara, ba ni ne zan zabi ko rayuwa ta ko mutuwa ta ce za ta fi kawo ceto ga duka ba.... za ku iya begen komi daga wuri na ...amma ba gudu ko janyewa ba. Ba zan iya gudu ba, balle ma janyewa.”

Sa’an da labari ya yadu a Worms cewa Luther zai bayana a gaban Majalisa, hankalin mutane ya tashi sosai. Aleander, wakilin paparuma da aka ba shi yin sahri’an, ya yi mamaki da fushi kuma. Ya ga cewa sakamakon zai bata aikin paparuma. Ta da binciken sahri’an da paparuma ya rigaya ya ba da hukumcin warewa akai zai zama reni ne ga ikon paparuma

din. Biye da haka ya ji tsoron cewa kaifin harshe da karfin mahawaran mutumin nan za su iya janye hankulan ‘ya’yan sarki daga ra’ayin paparuma. Sabo da haka, cikin hanzari, ya nuna haushin sa ga Charles game da zancen zuwan Luther Worms. Kusan lokacin nan ne aka wallafa umurnin da ya ware Luther; wannan kuwa hade da fadan da jakadan ya yi ma sarkin ya sa shi sarkin ya yarda. Ya rubuta ma mai-zaben cewa idan Luther ba zai janye ba, sai dai ya kasance a Wittenberg.

Da shi ke bai gamsu da nasaran nan tasa ba, Aleander ya yi iyakar kokarinsa ya tabbatar an hukumta Luther. Da naciyar da ta cancanci abu mafi kyau, ya jawo hankulan ‘ya’yan sarkin, da prietocin, da wadansu membobin majalisar, ya zargi Luther da “ta da hargitsi, tawaye, rashin ibada, da sabo.” Amma zafi da mumunan fushin da jakadan ya nuna a fili haka ya bayana irin ruhun da ya motsa shi. Mutane suka rika cewa: “Fushi da ramuwa ne su ke motsa shi, maimakon himma da ibada.” Yawancin yan Majalisar suka fi yarda da matsayin Luther.

Da karin himma, Aleander ya matsa ma sarkin cewa wajibi ne gare shi ya aiwatar da umurnin paparuman, amma a kalkashin dokokin Jamus ba za ya iya yin wannan ba sai da yardar ‘ya’yan sarkin; sa’an nan da matsin wakilin paparuman da ya fi karfinsa, Charles ya ce ma Luther ya gabatar da maganarsa ga Majalisar. “Ranar alfarma ce ga jakadan. Majalisar mai-girma ce: dalilin ma ya fi girma. Aleander aka zaba zai yi Magana a madadin Rum, ... uwa da uwargijiyar dukan ekklesiyoyi. Zai nuna yarimancin Bitrus a gaban taron nan na shugabannin Kirista. Yana da baiwar kaifin harshe, ya kuwa shirya ma babban zaman nan. Allah Ya shirya cewa Rum ta zo gaban taro mafi girma ta bayana kanta, ta bakin jami’inta mafi iya magana, kafin a hukumta ta.” Cikin shakka masugoyon bayan Luther suka so su ga sakamakon maganar Aleander. Mai-zaben Saxony ba ya wurin, amma bisa ga umurnin, wadansu fadawansa suka hallara domin su rubuta abin da jakadan zai fada.

Da dukan ikon sani da kaifin harshe, Aleander ya shirya rushe gaskiya. Ya dinga jefa ma Luther zagi daya bayan daya, cewa Luther magabcin ekklesiya ne da na kasa kuma, da na masu rai da matattu, masu aikin bisahara, majalisu da Kirista daya dayansu. Ya ce: “A cikin kurakuran Luther, akwai isassun dalilan kona yan ridda dubu dari.”

A karshe, ya yi kokarin nuna reni ga magoya bayan sabuwar gaskiyar. Ya ce: “Ina yan Luther din? Kungiyar mallamai masu zagi, priestoci masu-rashawa, ‘yan zuhudu marasa halin kirki, jahilan lauyoyi da fadawa marasa kunya, tare da talakawan da suka batar. Ina yawan fifikon yawan jama’ar Katolika, da fifikon iyawa, da iko! Wata doka ta bai daya daga wannan babban Majalisar za ta wayar da marasa hikima, ta gargadi marasa hankali, ta ba da tabbaci ga masu shakka, ta kuma karfafa marasa karfi.”

Da irin makaman nan ake kai ma masu shelar gaskiya hari a kowace sara. Dalilai dayan ne ake anfani da su a kan dukan wadanda suka yi shelar bayananiyar maganar Allah

sabanin sanannun kurakurai. Masu-son addini na yayi sukan ce: “wadanne ne wadannan masu wa’azin sabobin koyaswa?” “Ba su da ilimi, basu da yawa, kuma marasa wadata ne. Duk da haka suna cewa suna da gaskiya, kuma wai su ne zababbun mutanen Allah. Jahilai ne su, rudaddu kuma. Dubi yadda ekklesiyaar mu ta fi tasu yawan jama’a da tasiri kuma! Dubi yawan manyan mutane da masanan da ke cikinmu! Dubi yawan ikon da ke cikinmu!” Dalilan da ke jan hankulan duniya kenan; amma kamar yadda ba su da nasara a zamanin Luther, haka kum ba su da nasara yanzu ma.

Canji fa bai tsaya kan Luther ba yadda mutane da yawa su ke zato. Zai ci gaba har karshen tarihin duniyan nan. Luther ya yi babban aiki na bayana ma sauran mutane hasken da Allah Ya haska masa; amma bai karbi dukan hasken da ya kamata a mika ma duniya ba. Daga wancan lokacin zuwa yanzu, sabon haske yana haska Littafin kullayaumin, sabobin gaskiya kuma suna bayanuwa.

Jawabin jakadan ya yi tasiri sosai a kan Majalisar. Ba Luther awurin da zai rushe jarumin paparuman nan da gaskiyar maganar Allah mai-saukin ganewa. Ba a yi wani yunkurin kare dan Canjin ba. A fili aka nuna shirin hukumta shi da koyaswoyinsa, idan ya yiwu ma a tumbuke ridda. Rum ta sami dama mafi-kyau don kare matsayin ta. An fadi duk abin da ta iya fadi don kare kanta. Amma kamanin nasaran ne ya zama shaidar kasawarta. Daga nan za a kara ganin bambancin gaskiya da kuskure a fili, sa’an da suka ja dagar yaki a bayane, daga ranan Rum ta dena rashin tsoron da take da shi da.

Yayin da yawancin yan majalisan ke marmarin mika Luther ga ramuwar Rum, da yawa cikinsu sun gani suka kuma yi kyamar lalacewan da ke cikin ekklesiya, suka kuma so a hana wulakncin da mutanen Jamus ke sha ta dalilin lalacewa da handaman shugaabannin ekklesiya. Jakadan ya nuna kyaun mulkin paparuma sosai. Yanzu kuma Ubangiji ya motsa wani dan Majalisa ya ba da ainihin sakamakon zaluncin tsarin paparuma. Da karfi cikin martaba, sarki George na Saxony ya tashi tsaye a wannan taron, ya bayana daidai rudi da ayukan ban kyama na tsarin paparuma da munin sakamakon su kuma. A karshe ya ce:

“Wadannan ne wadansu daga cin mutuncin da ke nuna kasawar Rum. An ajiye dukan kunya a gefe, kuma manufarsu kadai it ace ...kurdi kurdi kurdi,... ta yadda masu wa’azi da ya kamata su fadi gaskiya ba abin da suke fadi sai karya, kuma ba barin su ake ba, lada ma ake ba su, da shike yawan ribar su daidai da yawan karyar su. Daga wannan mumunar mabulbulan ne mumunan ruwan nan ke kwararowa. Lalata ta sadu da son kurdi.... Abin kunyan da ma’aikatan ekklesiya ke yi ne yake jefa mutane da yawa cikin hallaka. Dole a yi canji gaba daya.”

Luther kansa ba zai iya yin sokan da ya fi wannan game da cin mutunci da tsarin paparuma ke yi ba, kuma da shi ke mai-maganan ma sanannen magabcin Luther ne, wannan ya kara ma maganar sa tasiri.

Da an bude idanun yan Majalisan, da sun ga malaikun Allah a tsakaninsu, suna aika tsirkiyoyin haske cikin duhun kuskure suna kuma bude zukata da tunani don karban gaskiya. Ikon Allahn gaskiya da hikima ne ya mallaki har magabtan Canjin ma, ta haka kuma ya shirya hanya domin babban aikin da za a yi, ba d a jimawa ba. Martin Luther ba ya wurin; amma an ji muryar Wani wanda Ya fi Luther a wannan taron.

Nan take Majalisar ta kafa komiti da zai kirga, ya jera kowane cin zarafi da paparuma ke danne mutanen Jamus da shi. Jerin nan da ya kunshi ababa dari da daya, aka ba sarki, aka kuma bukace shi ya dauki mataki nan da nan don magance cin zarafin nan. Masu rubuta takardar karar suka ce: “Ga fa babban hasarar rayukan Kirista, ga barna ga kwace sabo da ababan kunya da suka kewaye shugaban ruhaniyar Kirista! Aikin mu ne wajibi mu hana hallaka da wulakantarwar mutanenmu. Don haka cikin tawali’u amma da hanzari, mu ke rokon ka ka umurta canji na duka, ka kuma dauki nauyin aiwatar da shi.”

Yanzu kuma Majalisar ta bukaci dan Canjin ya bayana a gaban su. Duk da roko da kin yarda, da barazanar Aleander, daga baya dai sarkin ya yarda, aka kuma yi sammacin Luther ya bayana gaban Majalisar. Aka hada sammacin da takardar izinin tafiya da tabbacin tsaronsa. Aka ba wani dan sako da aka zaba ya kawo shi Worms daga Wittenberg.

Abokan Luther sun tsorata kwarai. Da sanin kiyayya da gaban da ake masa, sun ji tsoro cewa ba za a kula da takardar izinin tafiyarsa ba ma, suka kuma roke shi kada ya sa ransa cikin hatsari. Shi kuwa ya amsa: “Yan paparuma ba sa so in je Worms, hukumci na da mutuwa ta suke so. Ba komi ba ne. Kada ku yi mani addu’a, amma ku yi ma maganar Allah addu’a.... Kristi zai ba ni Ruhunsa don nasara da wadannan ‘yan sakon kuskuren. Ina rena su tun ina da rai, zan yi nasara kan su ta wurin mutuwata. Suna kai da kawowa a Worms game da tilasta ni in janye; kuma ga yadda janyewata za ta kasance: da na ce paparuma wakilin Kristi ne; yanzu ina cewa shi magabcin Ubangijinmu ne, manzon Iblis kuma.”

Luther bai yi tafiyan nan shi kadai ba. Ban da dan sakon sarkin, uku daga cikin abokansa na kusa kusa sun nace za su je tare da shi. Melanchthon ya nace zai bi su. Zuciyar sa ta hadu da ta Luther, ya kuwa so ya bi shi, in ta kama, har kurkuku ko mutuwa. Amma ba a yarda masa ba. Idan Luther ya hallaka dole begen Canjin ya rataya a kafadar abokin famarsa. Yayin da Luther ke rabuwa da Melanchthon, ya ce: “Idan ban dawo ba, kuma abokan gabana suka kashe ni, ka ci gaba da koyaswa, ka kuma tsaya da karfi cikin gaskiyar. Ka yi aiki a madadi na.... Idan ka rayu, mutuwa ta ba komi ba ne.” Dalibai da ‘yan kasa da suka taru domin su ga tafiyar Luther, sun motsu sosai. Jama’a da bishara ta taba zukatansu suka yi masa bankwana da kuka. Haka Luther da abokan tafiyarsa suka kama hanya daga Wittenberg.

Cikin tafiyar, sun ga cewa zukatan mutane sun damu da tsoron munanan ababa. A wadansu garuruwa ba a ba su girmansu ba. Sa’an da suka tsaya domin su kwana, wani

priest aboki ya nuna damuwar sa ta wurin nuna ma Luther hoton wani dan canji, mutumin Italiya da aka kashe. Washegari suka ji cewa an haramta rubuce rubucen Luther a Worms. ‘Yan sakon sarki suka rika shelar dokar sarkin, suna bidar mutane su kawo ma majistarori rubuce rubucen. Dan sakon sarki da ke tare da Luther, sabo da shakkar tsaron Luther a majalisar, da kuma zaton cewa karfin zuciyar sa ya raunana, ya tambaye shi ko yana da niyyar ci gaba. Ya amsa: “Ko da za a hana aiki na a kowane birni, zan ci gaba.”

A Erfort, an karbi Luther da daraja. Jama’a masu sha’awarsa suka kewaye shi har ya wuce ta titunan nan da ya sha bi da zabirar barar sa. Ya ziyarci dakin da ya taba zama ciki a unguwar masu zaman zuhudu, ya kuma tuna famar da ta kawo masa hasken da yanzu ya mamaye Jamus. An roke shi ya yi wa’azi. Wannan kuwa an hana shi yi, amma da sakon sarkin ya ba shi izini, sai Luther, wanda da an taba mai da shi bawan unguwar, yanzu kuma ya hau bagadin unguwar.

Ga taron jama’a ya yi anfani da kalmomin Kristi, “Salama gare ku.” Ya ce: masu bin ussan, ilimi, likitoci, da marubuta sun yi kokarin koya ma mutane hanyar samun rai madawami, kuma ba su yi nasara ba. Yanzu zan fada maku shi:... Allah Ya ta da Mutum daya daga matattu, Ubangiji Yesu Kristi, domin Ya hallaka mutuwa, Ya tumbuke zunubi, Ya kuma kulle kofofin lahira. Wannan shi ne aikin ceto. Kristi ya yi nasara! Wannan shi ne labari na farin ciki; kuma an cece mu ta wurin aikinsa, ba ta wurin aikinmu ba, ... Ubangijinmu Yesu Kristi Ya ce, “Salama gare ku; dubi hannuwana; watau kenan, Duba, Ya mutum! Ni ne, ni kadai, wanda na dauke zunubanka, na fanshe ka; yanzu kuma kana da salama, in ji Ubangiji.”

Ya ci gaba yana nuna cewa ana nuna ainihin bangaskiya ta wurin rayuwa mai-tsarki ne. “Da shi ke Allah Ya cece mu, bari mu yi ayukan mu domin su karbu gare Shi. Kana da arziki?, bari dukiyarka ta tanada domin bukatun matalauta. Kai matalauci ne? Bari hidimomin ka su zama karbabbu ga masu-arziki. Idan aikinka yana da anfani gare ka kai kadai ne, aikin da kake cewa kana yi ma Allah karya ne.”

Mautanen suka ji shi kamar ya rike su da dabo. Ya ba mayunwatan mutanen nan gurasa ta rai. Aka daga Kristi a gabansu bisan su paparuma da priestoci da sarakuna manya da kanana. Luther bai ambaci hatsarin yanayin da shi kansa yake ciki ba. Bai nemi ya sa a yi tunaninsa ko a ji tausayinsa ba. Garin tunanin Kristi, ya manta da kansa. Ya boye a bayan Mutumin Kalfari, yana kokarin nuna cewa Yesu kadai ne Mai-fansar mai-zunubi.

Yayin da Luther ya ci gaba da tafiyarsa, ko ina an so ganin shi sosai. Jama’a sukan kewaye shi, masu kaunarsa kuma suka yi masa kashedi game da manufar Romawan game da shi. Wadansu suka ce: “Za su kona ka, su mai da jikin ka toka, yadda suka yi da John Huss.” Luther ya amsa: “Ko da za su kunna wuta daga Worms zuwa Wittenberg, har harshen wutan ya kai har sama, ni zan yi tafiya cikin wutar, cikin sunan Ubangiji; zan

bayana a gabansu; zan shiga mukamukan dorinan nan, in karye hakoran sa, ina dogara ga Ubangij Yesu Kristi."

Labarin kusantowar shi Worms ya ta da rudewa sosai. Abokansa sun damu da tsaron lafiyarsa; magabtansa sun damu game da yiwuwar nasarar aikinsa. An yi kokari sosai don hana shi shiga birnin. Bisa shawarar 'yan paparuma, aka roke shi ya je gidan wani jarumi mai-goyon bayansa, inda aka ce za a magance dukan matsaloli cikin salama. Abokai sun yi kokarin nuna masa abin ban tsoro da yake fuskanta. Dukan kokarinsu ya kasa. Luther dai bai damu ba. Ya ce: "Ko da yawan aljannun da ke Worms ya kai yawan fallayen jinkan dukan dakunan da ke birnin, duk da haka zan shige shi."

Da shigowarsa Worms, jama'a da yawa suka kewaye kofofin, domin su marabce shi. Ko sarki kansa jama'a ba su taba taruwa da yawa hakanan domin su gaishe shi ba. Ya ja hanakula sosai, kuma daga cikin jama'ar aka ji wata murya mai-karfi tana wakar biso don yi ma Luther kashedin abin da zai faru da shi. Luther ya ce: "Allah zai zama Garkuwa ta," sa'an da yake saukowa daga karusarsa.

Mutanen paparuma basu gaskata cewa Luther zai dauki kasadar bayanuwa a Worms ba, zuwan sa kuwa ya cika su da mamaki. Babban sarkin nan da nan ya kirawo yan majalisarsa domin su yi sahwara kan matakin da za su dauka. Wani bishop, mai-tsananin ra'ayin paparuma, ya ce: "Mun dade muna shawara kan wannan batu. Bari mai-martaba ya gama da wannan mutumin gaba daya. Ba Sigismund ya sa an kone John Huss ba? Ba lallai ne mu bayar ko kuma mu tabbatar da kariyar mai-ridda ba." Babban sarkin kuwa ya ce: "Babu, dole ne mu cika alkawalinmu." Sabo da haka aka yarda cewa a saurari Luther.

Dukan birnin sun kosa su ga kwararren mutumin nan, jama'a da yawa kuwa suka cika masaukinsa. Luther bai gama murmurewa daga ciwonsa ba; tafiyarsa ta sati biyu kuma ta gajiyar da shi; dole ne zai shirya domin muhimman ababan da za a yi washegari, yana kuma bukatar wuri shuru da hutawa ma. Amma marmarin ganin shi ya kai inda 'yan sa'o'i kadan ne kawai ya samu ya huta kafin fadawa da jarumawa, da priestoci da 'yan kasa suka kewaye shi. Cikinsu akwai fadawa da yawa da suka dade suna rokon babban sarkin cewa a canja daga cin mutunci da eklesuya ke yi, kuma, ta bakin Luther , "dukan su an yantar da su ta wurin bishara ta." Magabta da abokai suka taru domin su ga dan zuhudun nan mara tsoro; amma ya karbe su a natse, yana amsa ma kowa da girmamawa da hikima kuma. Babu alamar kumamanci ko tsoro a jikinsa. Fuskarsa cike da alamun gajiya da ciwo ya nuna nagarta da farin cikin da ke cikinsa. Saduda da hikimar maganarsa sun ba shi ikon da ko magabtansa ma basu iya tsayayya da shi ba. Abokai da magabta suka cika da mamaki. Wadansu sun gaskata cewa akwai ikon Allah cikinsa; wadansu kuma suka ce: "Yana da aljannu," kamar yadda Farisawa suka fada game da Kristi.

Rana ta biye aka kira Luther domin ya halarci Majalisar. Aka hada shi da wani hafsan babban sarki wanda zai kai shi zauren da za a yi zaman; amma da kyar ya kai wurin.

Kowane titi ya cika da ‘yan kallo suna marmarin ganin dan zuhudun nan da ya ki ikon paparuma.

Da ya zo zai shiga wurin shari’an, wani tsohon janar wanda ya yi yake yake da yawa, ya ce masa: “Ya mai-zaman zuhhudu, yanzu za ka dauki matakin da ya fi nawa da wanda kowane kyaftin ya taba dauka cikin dukan yake yakenmu da aka fi zub da jini. Amma idan dalilin ka daidai ne, kuma ka tabbatar da shi, ci gaba cikin sunan Allah, kuma kada ka ji tsoron komi. Allah ba za ya rabu da kai ba.”

Daga bisani Luther ya bayana gaban majalisar. Babban sarkin ya zauna bisa kujerar sarautar. Manyan mutane mafi girma a kasar suka kewaye shi. Ba mutumin day a taba bayana gaban taron day a fi wanda Luther ya bayana a gaban sa, don kare bangaskiyar sa. “Wannan tuhumar ma babban nasara ce a kan tsarin paparuma. Paparuma ya rigaya ya hukumta mutumin, yanzu kuma yana tsaye a gaban wata hukuma, wannan ma kawai ya nuna cewa hukumar ta aza kan ta isa paparuma. Paparuma ya rigaya ya ware shi ya raba shi daga dukan ya Adam; duk da haka an yi sammacin sad a harshe mai- ban girma, aka karbe shi a gaban majalisa mafi mafi martaba a duniya. Paparuma ya rigaya ya hukumta masa yin shuru har abada, yanzu kuma ga shi zai yi magana a gaban dubban masu sauraron sa a natse da suka zo daga kasashen Kirista masu nisa. An yi wani babban canji kenan tawurin aikin Luther. Rum ta fara saukowa kenan daga gadon sarautan ta, kuma muryar mai-zaman zuhudun ne ta jawo wannan kaskantarar.”

A gaban wannan majalisar mai-iko da martaba, Luther dan Canji ya cika da tsoro da rudewa kuma. Da yawa cikin yarimomin, da suka gane yadda yake ji, sai suka je wurinsa, dayan su kuma ya ce masa a kunne: “Kada ka ji tsoron wadanda ke kashe jiki, amma ba za su iya kashe ruhu ba.” Wani kuma ya ce: “Sa’an da za a kai ku gaban gwamnoni da sarakuna sabili da ni, Ruhun Uban ku za ya ba ku abin da za ku fada.” Ta haka manyan mutanen duniya suka kawo kalmomin Kristi domin karfafa bawan Sa a lokacin jaraba.

An kai Luther ya zauna fuska da fuska da wurin zaman babban sarkin ne. Sai wuri ya yi shuru. Sa’an nan wani jami’in babban sarkin kasar ya tashi yana nuna yatsa ga wani tarin littattafan Luther, ya bukaci dan Canjin ya amsa tambayoyi biyu: ko ya yarda littattafansa ne, da kuma ko yana sirye ya janye ra’ayoyin da ya bayana a cikinsu. Da shi ke an rigaya an karanta sunayen littattafan, Luther ya amsa cewa game da tambaya ta farko littattafan nasa ne. Ya kuma ce: “Game da tambaya ta biyu din, da shi ke tambaya ce da ta shafi bangaskiya da ceton rayuka, wadda kuma ta safi maganar Allah, dukiya mafi daraja a sama ko duniya, zan yi rashin hankali idan na amsa ba tare da yin tunani ba. Ina iya kasa abin da ya cancanci yanayin, ko kuma fiye da abin da gaskiya ke bida, wanda zai zama zunubi bisa ga furcin Yesu cewa: ‘Amma dukan wanda za ya yi musun sani na a gaban mutane, shi zan yi musunsa a gaban Ubana wanda ke chikin sama kuma.’ [Mata 10:33.] Sabo da haka, ina rokon martabar sarautar ka, da dukan saukin kai, ka ba ni lokaci domin in amsa ba tare da ketare maganar Allah ba.”

Rokon nan na Luther hikima ce. Matakin sa ya nuna cewa ba cikin fushi ko gaggawa yake aikinsa ba. Irin natsuwa da kamewan nan wanda ba a zata za a samu wurin mai- karfin hali da rashin daidaituwan nan ya kara mashi karfi, ya kuma taimake shi daga baya ya amsa da hankali, da tabbaci, da hikima da martaba da suka ba magabtansa mamaki, ya yanke masu buri, ya kuma tsauta ma rennin su da fahariyar su.

Washegari ne ya kamata ya bayana ya ba da amsarsa ta karshe. Da farko zuciyar sa ta yi sanyi, ganin irin ikokin da suka hada kai sabanin gaskiya. Bangaskiyarsa ta raunana; tsoro da rawan jiki suka abka masa, kyama ta cika shi. Sai ya ga hatsarukan da yawa a gabansa; ya ga kamar magabtan sa suna gaf da yin nasara, ikokin duhu kuma su rinjaya. Duhu ya rufa shi Kaman zai raba shi da Allah. Ya yi marmarin tabbacin cewa Ubangijin runduna zai kasance tare da shi. Cikin bakin ciki kwarai ya jefa kansa a kasa, ya yi rub da ciki, ya kuma kai kukansa mai-zafi ga Allah wanda Shi kadai ne mai gane irin kukan nan.

Ya roka cewa: “Ya MAdaukaki, Allah na har abada, wace irin muguwar duniya kenan! Duba ga shi ta bude bakinta za ta hadiye ni, kuma dogara ta gare ka kadan ne. Idan a kan karfin duniyan nan ne kadai zan dogara, an gama komi.... sa’a ta ta karshe ta zo, an furta hukumci na.... Ya Allah, ka taimake ni da dukan hikimar duniya. Ka yi wannan kai kadai, gama akin nan ba nawa ba ne, naka ne, ba ni da abin yi a nan, ba abin mahawara da wadannan manya na duniya.... Amma aikin naka ne,... kuma aikin adalci ne, na har abada kuma. Ya Ubangiji ka taimake ni! Allah Mai-aminci Mara sakewa kuma, ba mutumin da na dogara gare shi.... Kowane abu na mutum ba shi da tabbaci; duk abin da ya fito daga mutum yana faduwa.... Kai ka zabe ni domin wannan aikin.... Ka tsaya a gefe na sabi da Kaunatacen Ka Yesu Kristi, wanda Shi ne kariya ta, garkuwa ta, da mabuya ta mai-karfi.”

Allah mai-cikakken hikima ne Ya yarda Luther ya gane hadarin da ke gabansa, domin kada ya dogara ga karfin kansa, ya yi gaggawar shiga damuwa da ganganci. Amma ba tsoron wahala kansa ko tsoron azaba ko mutuwa, wadda da alama ta kusa, suka dame shi ba. Ya iso wurin tashin hankalin, sa’an nan ya ji rashin isansa ya fuskance shi. Ta wurin kumamancinsa gaskiya za aa iya yin nasara. Ba don tsoron lafiyarsa ba, amma don nasarar bishara ne ya yi kokawa da Allah. Kamar ta Israila a kokawar daren nan a gefen rafi, haka damuwa da tashin hankalinsa suka kasance. Kamar Israila kuma, ya rinjaya tare da Allah. Cikin kumamancinsa, bangaskiyarsa ta manne ma Kristi, babban Mai-kubutarwan. Aka karfafa shi da tabbacin cewa ba zai bayana gaban majalisar shi kadai ba. Salama ta dawo zuciyarsa, ya kuma yi murna cewa an yarda mashi ya girmama maganar Allah a gaban shugabanin al’ummai.

Da wannan tunani da ya dogara ga Allah da shi, Luther ya shirya don faman da ke gabansa. Ya yi tunanin tsarin amsarsa, ya yi nazarin wadansu ababan da ya rubuta, ya kuma samo tabbaci daga Littafi da ya dace da matsayinsa. Sa’an nan, da hannunsa a kan Littafin da ke bude a hannun damansa da ya daga sama, ya yi alkawali cewa zai “kasance da aminci

ga bishara, ya kuma sanar da bangaskiyarsa kai tsaye, ko da zai hatimce shaidarsa da jininsa ne.”

Sa’an da aka sake shigo da shi cikin Majalisar, fuskarsa ba ta nuna alamar tsoro ko rudewa ba. Cikin natsuwa da salama, amma kuma cikin martaba da rashin tsoro, ya tsaya a matsayinsa na shaidan Allah cikin manyan mutanen duniya. Hafsan sarkin kuma ya yi masa tambayan nan, ko yana so ya janye koyaswoyinsa. Luther ya ba da amsarsa cikin natsuwa da murya mai-ladabi, ba fada ko haushi. Ya nuna kunya da rashin tsoro da murna da ta ba Majalisar mamaki.

Luther ya ce, “Ya sarki mai-hankali kwance, manyan ‘ya’yan sarki, masu-sarauta da alheri, na bayana a gabanku yau bisa ga umurnin da aka ba ni jiya, kuma da jin kan Allah ina rokon mai-martaba, da ku masu girma, ku saurari kariyar matsayin da na tabbata daidai ne kuma gaskiya ce. Idan, ta wurin jahilci, na ketare al’adu da kaidodin fada, ina rokonku ku yafe ni; domin ba a girmar da ni a fadar sarakuna ba, amma a ware cikin unguwar masu zaman zuhudu.”

Sa’an nan, game da tambayan, ya ce rubuce rubucensa da aka wallafa ba iri daya ba ne. A wadansu ya yi magana kan bangaskiya da kyawawan ayuka ne, kuma ko magabtansa ma sun ce suna da anfani, bayan ba su da illa. Janye wadannan zai zama rushe gaskiyan da duka aka yarda da shi. Kashi na biyu din rubuce rubuce ne da suka bayana lalacewa da kuma cin zarafin da tsarin paparuma ke yi. Janye wadannan zai karfafa zaluncin Rum, ya kuma kara bude babbar kofa ga manyan rashin ibada masu yawa. A kashi na ukun, ya zargi mutane da suka goyi bayan muguntan da ake yi ne. Game da wadannan ya yarda cewa ya yi anfani da karfin da ya wuce kadada. Bai ce ba shi da laifi ba, amma ko wadannan litattafan ma ba zai iya janyewa ba, domin yin haka zai karfafa magabtan gaskiya, sa’an nan za su yi anfani da zarafin nan su murkushe mutanen Allah da zalunci mafi muni.

“Duk da haka, ni mutum ne kawai, ba Allah ba,” Luther ya ce; “sabo da haka zan kare kai na yadda Kristi Ya yi: ‘Idan na fadi mugunta, ku ba da shaidar muguntar.... Ta wurin jinkan Allah, ina rokonku, ya sarki mai-hankali shifidadde, da ku, masu sarauta da alheri, da dukan mutane kowane iri, ku nuna daga rubuce rubucen annabawa da manzani cewa na yi kuskure. Da zaran na gamsu da wannan zan janye kowane kuskure, in kuma zama na farko da zan dauki littattafai na in jefa su cikin wuta.”

“Abin da na fada yanzun nan, ina fata ya nuna cewa a hankali na yi la’akari da hatsarin da nake jefa kai na ciki, amma maimakon karaya, ina farin ciki ganin cewa bishara yanzu, kamar da, ta zama sanadin damuwa da gardama. Wannan shi ne yanayi da kadarar maganar Allah. Yesu Ya ce, ‘Ban zo domin in kawo salama a duniya ba, sai dai takobi.’ Allah Mai-al’ajibi ne da ban tsoro cikin al’amuransa; a yi hankali kada garin neman murkushe gardama ku tsananta ma maganar Allah, har ku jawo ma kanku ambaliyar matsaloli na matsifu da hallaka ta har abada.... Zan iya ambaton misalai daga maganar Allah. Zan iya

magana game da su Fir'auna da sarakunan Babila, da na Isaraila, wadanda ayukan su na neman karfafa mulkinsu sun taimaka wajen jawo hallakarsu. 'Allah yana tura manyan tsaunuka amma su basu sani ba.' "

Luther ya yi magana da harshen Jamusanci ne; yanzu kuma aka ce ya maimaita kalmomi dayan da Helenanci. Ko da shike maganan da ya fito yi ta gajiyar da shi, ya yarda dai, ya kuma yi jawabinsa sarai, da karfi kaman na farkon. Ikon Allah ne ya bi da wannan al'amarin. Da farko kuskure da camfi sun rufe idanun mutane da yawa daga 'ya'yan sarki da yadda basu ga ma'anar maganar Luther ba; amma maimaitawar ta sa sun gane sarai abin da ya fada.

Wadanda cikin taurin kai suka rufe idanunsu daga hasken, suka kuma nace cewa ba za su karbi gaskiyar ba, sun fusata da karfin maganar Luther. Da ya gama magana, mai-magana a madadin Majalisar, cikin fushi ya ce: "Ba ka amsa tamabayar da aka yi maka ba.... Ana bukatar ka ka ba da amsa sarai gajeruwa kuma.... za ka janye ko babu?"

Luther ya amsa: "Da shike mai-martaba da ku masu girma kuna bidar amsa sarai mai sauki, gajeruwa kuma, zan ba ku, kuma ita ce: ba zan ba da bangaskiya ta ga paparuma ko majalisu ba, domin a bayane yake cewa sau da yawa sun yi kuskure, suka kuma yi sabani da juna. Sabo da haka in ba an gamsar da ni ta wurin shaidar Littafi ko fasara mafi-saukin ganewa ba, in ba an fahimtar da ni ta waurin nassosi da na ambata ba, sa'an nan kuma in ba ta wurin haka sun daura lamirina da maganar Allah ba, ba zan iya janyewa ba, kuma ba zan janye ba, domin kasada ce ga Kirista ya yi magana sabanin lamirinsa. Nan na tsaya ba zan iya yin wani abu dabam ba; bari Allah Ya taimake ni. Amin."

Hakanan adalin nan ya tsaya kan tabbatacen tushe, watau maganar Allah. Hasken sama ya haskaka fuskarsa. Girman sa da tsabtar halinsa, salamar sa da murnar zuciyarsa, sun bayana ga kowa yayin da yake ba da shaida sabanin kuskure ya kuma shaida fifikon bangaskiyan nan da ke da nasara bisa duniya.

Dukan majalisar ta yi shuru na wani lokaci sabo da mamaki. A amsar sa ta fari, Luther ya yi magana da murya mara-karfi, da ban girma kuma. 'Yan Rum din suka mai da wannan alamar cewa karfin halinsa ya fara kasawa kenan. Sun dauka cewa rokon karin lokaci da ya yi da farko hanya ce da za ta kai ga janyewarsa. Charles da kansa da ya lura cikin reni cewa da gajiya a jikin Luther, da suturar sa mara tsada, da kuma saukin jawabinsa, ya ce: "Mai zaman zuhudun nan ba zai ta ba mai da ni mai-ridda ba." Jaruntaka da naciya da ya nuna, da kuma karfi da saukin ganewar maganarsa, sun cika kowa da mamaki. Babban sarkin, cike da yabawa, ya ce: "Wannan mai-zaman zuhudun yana magana da karfin zuciya." Da yawa daga cikin yayan sarkin Jamus suka kalli wannan wakilin na kasar su da alfarma da farin ciki kuma.

An yi nasara bisa masu goyon bayan Rum; an nuna munin tasirinsu. Sun so su rike ikonsu ba ta wurin anfani da Littafin ba, amma ta wurin anfani da barazana, yadda Rum ta

saba. Kakakin Majalisan ya ce: “Idan ba ka janye ba, babban sarki da jihohin kasar za su yi shawara su ga matakin da za a dauka game da mai-ridda da ya ki tuba.”

Abokan Luther da suka saurari kariyarsa cikin farinciki, suka yi rawan jiki da jin maganan nan; amma Luther kansa, cikin kwanciyar hankali ya ce: “Bari Allah Ya zama mai-taimakona, gama bazan janye komi ba.”

Aka umurce shi ya fita daga Majalisar, yayin da ‘ya’yan sarkin suka shiga shawara. An dauka cewa babban tashin hankali ya zo. Nacewar Luther cewa ba za ya janye ba zai iya shafar tasirin ekklesiya har sararraki. Sai aka yarda cewa za a ba shi dama ta karshe domin ya janye. Aka kawo shi cikin Majalisa, kawowa na karshe. Aka sake tambayarsa ko zai janye koyaswoyinsa. Ya ce: “Ba ni da wata amsa da zan bayar, da bam da wadda na rigaya na bayar.” Ya bayana a fili cewa ba za a iya lallabar sa, ko ta wurin alkawura ko barazana, cewa shi amince da tsarin Rum ba.

Shugabannin tsarin paparuman suka fusata domin wani mai-zaman zuhudu kawai ya rena ikon nan nasu da yakan sa sarakuna da fadawa su yi rawan jiki; suka yi begen sa shi ya gane fushinsu tawurin azabtar da shi har mutuwa. Amma Luther, duk da sanin wannan hatsari, ya yi magana da dukansu da martaba, cikin kwanciyar hankali. Maganarsa babu girman kai ko fushi ko rudewa. Ya rigaya ya manta kansa, da manyan mutanen da suka kewaye shi, ya kuma ji kawai cewa yana tare da wanda Ya fi su paparuma, da priestoci da sarakuna, da manyan sarakuna. Kristi Ya rigaya Ya yi magana ta wurin jawabin Luther, da iko tare da martaban da ya kawo ma abokai da magabta ma bangirma da mamaki. Ruhun Allah Yana cikin wannan Majalisar a lokacin, Yana aiki cikin zukatan manyan kasar. Da yawa cikin ‘ya’yan sarkin sun yarda da matsayin Luther, ba tsoro. Da yawa sun amince da gaskiyar; amma ga wadasu, koyaswan da suka samu bai jima a cikinsu ba. Akwai wadansu kuma da basu bayana amincewarsu a lokacin ba, amma bayan sun bincika Littafin da kan su, daga baya suka nuna nasu goyan bayan Canjin ba da tsoro ba.

Mai-zabe Fredrick ya yi ta begen bayanuwar Luther a gaban Majalisar, kuma da marmari ya saurari jawabinsa. Da alfarma da farincki ya ga karfin hali da naciya da kwanciyar hankalin likitan, har ma da kasancewarsa a shirye ya kara kare kansa. Ya bamabanta masu jayayyar, ya kuma ga cewa an wofinta hikimar paparuma da sarakuna da prietoci ta wurin karfin gaskiya. Tsarin paparuma ya sha kaye ta yadda dukan al’ummai a dukan sararraki kuma za su sami labari.

Sa’an da jakadan ya ga sakamakon da jawabin Luther ya haifar, ya ji irin tsoron da bai taba ji ba, sabo da tsoron ikon Rum, ya kuma dauki kuduri zai yi duk abin da zai iya domin tabbatar da cewa an kawar da Luther. Da duk iya magana da kwarewar jakadanci da ya yi fice akai, ya nuna ma babban sarkin wauta da hadarin sadakar da abota da goyon bayan mulkin Rum wai don wani mai-zaman zuhudu kawai da bai isa komi ba.

Maganar sa ta yi tasiri. Bayan amsar Luther, washegari Charles ya sa aka kai ma Majalisar sako cewa shi zai ci gaba da tsarin magabatansa na tabbatarwa da kuma kare addinin Katolika. Da shike Luther ya ki janye kurakuransa, za a yi anfani da matakai mafi tsanani a kansa da riddan da yake koyarwa. “Mutum daya mai-zaman zuhudu wanda wautarsa ta batar da shi, ya ta da jayayya stakanin sa da dukan Kirista. Domin hana wannan rashin ibadar, zan sadakar da mulkoki na, da dukiya ta, da abokai na, da jiki na, da rai na, da ruhu na. Ina gaf da wofinta Luther, in hana shi jawo ma mutane rikici; zan kuma tuhume shi da masu binsa, masu ridda da laifin rena hukuma, a hukumta su da warewa, da horo da kowace hanya da za ta hallaka su. Ina kira ga dukan membobin jihohi su yi kamar amintattun Kirista.” Duk da haka babban sarki ya ce dole a cika da alakawalin nan na tsaron Luther, kuma kafin a fara tuhumarsa, dole a yarda mashi ya shiga gidan shi lafiya.

Membobin Majalisan fa suka fito da ra’ayi biyu masu sabani da juna. Yan sako kuma wakilan paparuma, suka sake cewa a yi watsi da zancen alkawalin tsaron lafiyar Luther. Suka ce, “Ya kamata Kogin Rhine ya karbi tokarsa, yadda ya karbi tokar Huss karni guda da ya wuce.” Amma ‘ya’yan sarkin Jamus, ko da shike su ma ‘yan paparuma ne, magabtan Luther kuma, suka ce ba za su yarda su jawo ma Jamus da babban sarkin su maimaicin wadannan matsalolin ba.

Amsar Charles kan sa ga mumunan ra’ayin nan it ace, “Ko da an kawar da girma da aminci daga dukan duniya, dole girma da aminci su sami mafaka a zukatan ‘ya’yan sarki.” Magabtan Luther dai suka kara matsa cewa ya yi ma Luther abin da Sigismund ya yi ma Huss, ya ba da shi a hannun ekklesiya; amma sa’an da ya tuna lokacin da Huss a gaban jama’a ya nuna ma kowa sarkokin, sa ya kuma tuna ma sarki matsalar imaninsa, Charles ya ce: “Ba zan so in yi ajiyar zuci kamar Sigismund ba.”

Amma kuma Charles ya rigaya ya ki gaskiyan da Luther ya bayana. Ya rubuta cewa: “Na dauki kuduri zan bi kwatancin ubani na.” Ya kudurta cewa ba zai kauce daga al’ada ba, ko domin ya bi hanyoyin gaskiya da adalci ma. Da shike ubaninsa sun goyi bayan tsarin paparuma, shi ma zai goyi baya, da dukan zaluncin ta da lalacewar ta. Hakanan ya ki karban duk wani haske da ya fi wanda ubaninsa suka karba, ko kuma ya yi wani abin da su basu yi ba.

Akwai mutane da yawa yanzu da ke manne ma al’adun iyayensu. Sa’an da Ubangiji ya aika masu Karin haske, sukan ki karban shi, domin da shi ke ba a ba iyayen su ba, iyayen basu karba ba. Ba a ajiye mu inda iyayen mu suke ba; sabo da haka aikinmu da bukatunmu ba daidai ne da nasu ba. Allah ba zai gamsu da cewa muna duban kwatancin ubaninmu domin mu san aikin da ya rataya a wuyanmu, maimakon binciken maganar gaskiya ma kanmu ba. Aikin da ke kanmu ya fi wanda yake kan iyayenmu. Za mu ba da lissafin hasken da suka karba, wanda aka mika mana gado, kuma za mu ba da lissafin Karin hasken da ke haskaka mu daga maganar Allah.

Game da Yahudawa marasa ba da gaskiya Kristi Ya ce: “Da ban zo na yi masu magana ba, da ba su da zunubi ba, amma yanzu ba su da hujjar zunubinsu ba.” Yohanna 15:22. Ikon Allah dayan ya yi magana ta wurin Luther zuwa ga babban sarki da yaran sarkin Jamus. Kuma yayin da hasken ya haskaka daga maganar Allah, Ruhunsa Ya yi roko na karshe ga mutane da yawa a Majalisar. Yadda Bilatus, daruruwan shekaru da suka gabata, ya bar fahariya da farin jini suka rufe zuciyarsa daga Mai-fansar duniya; yadda firgitacen Filikus ya ce ma dan sakon gaskiya: “Tafi dai yanzu, sa’an da na sami zarafi, na kirawo ka,” yadda Agaribas ya amsa, “Da kankanuwar rinjayaswa kana so ka maishe ni Christian” (Ayukan 24:25; 26:28), duk da haka suka juya ma sakon Allah baya, haka Charles V, sabo da alfarmar duniya da manufofin tafiyar da gwamnati, ya ki hasken gaskiya.

An yayata jita jitan shirye shiryen da ake yi game da Luther, wanda ya jawo rashin kwanciyar rai ko ina a birnin. Luther ya rigaya ya yi abokai da yawa wadanda, da sanin zaluncin Rum ga dukan masu jayayya da halayyanta, suka dauki kuduri cewa ba za a sadakar da shi ba. Daruruwan fadawa suka dauki alkawalin tsaron sa. Da yawa suka kushe sakon sarkin a matsayin nuna amincewa da kasancewa kalkashin ikon Rum. Aka rika manna sakoni a kofofin gidaje da gine ginen gwamnati, wadansu suna yabon Luther, wadansu kuma suna sokar sa. Waninsu ya rubuta maganar mai-hikiman nan ne, cewa: “Kaiton ki kasa, sa’an da sarkin ki yaro ne.” Mai-wa’azi 10:16. Karbuwan da aka nuna ma Luther ko ina a Jamus ya tabbatar ma babban sarkin da Majalisar cewa duk wani rashin adalci da aka nuna masa zai lalata salamar kasar da karkon gadon sarautan ma.

Fredrick na Saxony ya kame kansa, a hankali kuma ya boye son Luther da yake da shi, yana kuma tsaronsa sosai ba ja da baya, yana lura da take taken sa da na magabtansa. Amma da yawa basu boye goyon bayansu ga Luther ba. ‘Ya’yan sarki da hakimai da masu unguwa da sauran sanannun mutanen ekklesiya da na waje, sun rika ziyartarsa. Spalatin ya rubuta cewa: “Dan kankanin dakin likitan bai iya daukan dukan masu ziyartar sa ba.” Suka rika ganin sa kaman ya fi dan Adam ma. Ko wadanda basu gaskata koyaswarsa ba dole suka yi sha’awar amincin da ya sa shi ya gwammaci mutuwa maimakon ketare lamirinsa.

An yi kokari sosai a sa Luther ya sasanta da Rum. Fadawa da ‘ya’yan sarki suka ce masa idan ya nace yana gwada ra’ayin sa da na ekklesiya da na majalisu, ba da jimawa ba za a kore shi daga kasar, kuma ba zai sami kariya ba.... Luther ya amsa cewa: “Ba za a iya shelar bisharar Kristi ba tare da bata ma wani rai ba.... Don me tsoron hatsari zai raba ni da Ubangiji, kuma daga maganarsa wadda it ace kadai gaskiya? Babu, gwamma in sadakar da jiki na, da jini na, da rai na.”

An kuma sake matsa mashi ya amince da ra’ayin babban sarkin, sa’an nan ba abin da zai same shi. Ya kuwa amsa: “Na yarda da dukan zuciya ta cewa babban sarkin, da ‘ya’yan sarkin, har ma da Kirista mafi mugunta su bincika, su kuma auna rubuce rubuce na; amma bisa sharadi daya, cewa maganar Allah ta zama ma’auninsu. Mutane ba su da abin yi sai

dai biyayya ga maganar Allah. Kada ku bidi ketarewar lamiri na wanda ke daure da sarka cikin Littafi Mai-Tsarki."

Game da wata sahwarar ya ce: "Na yarda in sallamar da alkawalin tsaro na, na sa jiki na da rai na a hannun babban sarki, amma ba zan taba sallamar da maganar Allah ba!" Ya ce yana shirye ya amince da hukumcin majalisar, amma fa idan majalisar za ta yanke hukumcin bisa ga Littafi. "Game da abin da ya shafi maganar Allah da imani, kowane Kirista ya isa ya yanka hukumci daidai da paparuma, ko da majalisu miliyan guda ne suke goyon bayan paparuma din." Da abokai da magabta duka suka gane dai duk wani kokarin sasantawa ba zai yi anfani ba.

Da Luther ya yarda da abu daya, da Shaitan da rundunansa sun yi nasara. Amma naciyar sa ce ta zama hanyar yantarwar ekklesiya da farawar sabuwar sara mafi kyau. Tasirin mutum dayan nan wanda ya yi tunani don kansa game da addini ya kuma aikata, ya shafi ekklesiya da duniya, ba a zamaninsa kadai ba, amma har dukan sararraki da suka biyo baya. Naciyarsa da amincinsa za su karfafa kowa, har karshen lokaci, duk wanda zai wuce ta irin yanayin nan kuwa. Ikon Allah da martabansa sun tsaya fiye da shawarar mutane, fiye da yawan ikon nan na Shaitan ma.

Ba da jimawa ba, babban sarki ya umurci Luther ya koma gida, ya kuma san cewa za a bi wanna da hukumtawarsa maza maza. Ya fuskanci barazana, amma yayin da ya tashi daga Worms, zuciyar sa ta cika da murna da yabo. Ya ce: "Iblis kansa ne tsare dakin yakin papruma, amma Kristi Ya huda shi, aka kuma tilasta Shaitan ya yarda cewa Ubanfiji Ya fi shi."

Lokacn tafiyarsa, don dai kada a ga naciyarsa kamar tawaye ne, Luther ya rubuta ma babban sarkin cewa: "Allah wanda Shi ne Mai-karanta zukata Shi ne Shaida na, cewa ina shirye da gaske in yi biyayya gare ka mai-martaba, cikin daraja da cikin rashin daraja, cikin rai ko cikin mutuwa, kuma in ceci maganar Allah, wanda tawurin sa mutum yake rayuwa. Cikin dukan al'amuran rayuwan yanzu, aminci na ba zai raunana ba, domin a nan yin nasara ko riba ba wani abu ba ne game da ceto. Amma idan ana zancen al'amura na har abada, Allah ba Ya so mutum ya dogara ga mutum. Da shike dogara ga mutum a sha'anin ruhaniya ainihin sujada ne, kuma Mahalici ne kadai Ya cancanta a yi masa sujada."

Cikin tafiyarsa daga Worms, Luther ya sami karbuwa fiye da wanda ya samu lokacin tafiyarsa can. Manyan ma'aikatan ekklesiya suka marabci mutumin nan da ekklesiya ta ware, shugabannin gwamnati kuma suka girmama mutumin da babban sarki ya hukumta. Aka roke shi ya yi wa'azi kuma, ko da shike babban sarkin ya hana, ya sake hawa bagadi. "Ban taba yin alkawalin kulle maganar Allah ba, kuma ba zan taba yi ba."

Bai dade da barin Worms ba, 'yan paparuma suka sa babban sarkin ya ba da doka game da shi. Cikin dokar, an ce Luther "Shaitan ne da kansa cikin kamanin mutum, yafe da tufafin mai-zaman zuhudu." Aka umurta cewa da zaran alkawalin tsaron sa ya kare, sai

a dauki matakan tsayar da aikinsa. Aka hana kowane mutum yin harka da shi, ko ba shi abinci ko abin sha, ko taimaka masa ta wurin magana ko ayuka, cikin jama'a ko a boye. Aka kuma ce a kama shi duk inda yake, a mika ma hukuma. A kuma sa masu bin sa a kurkuku, a kwace dukiyarsu. A hallaka rubuce rubucensa, a karshe kuma, dukan wadanda suka ketare wannan doka suna kalkashin hukumcin dokar. Mai-zaben Saxony da 'ya'yan sarki masu goyon bayan Luther sun bar Worms jima kadan bayan tafiyar Luther, dokar babban sarkin kuma ta sami goyon bayan Majalisar. Yanzu kuma yan paparuma suka yi murna. Sun dauka cewa karshen Canjin ya tabbata.

Allah Ya rigaya Ya tanada ma bawansa hanyar tsira a wannan sa'ar hatsarin. Idon da ba ya barci ya dinga bin Luther duk inda ya je, wani mai-zuciyar gaskiya da martaba ya dauki kudurin kubutar da shi. Sanin kowa ne cewa Rum ba za ta gamsu da komi ba sai mutuwarsa; ta wurin boye shi ne kadai za a iya raba shi da bakin zaki: Allah Ya ba Fredrick na Saxony hikimar yin tsarin da ya kiyaye Luther. Da goyon bayan abokai na gaskiya aka aiwatar da manufar mai-zabe Fredrick, aka kuma boye Luther daga abokai da magabta. Cikin tafiyarsa zuwa gida aka kwace shi, aka raba shi da masu rakiyarsa, aka kuma bi da shi ta jeji maza maza zuwa babban sansanin Wartburg. Al'ajibai sun bi kwacewan nan nasa da boyewar sa, ta yadda har shi Fredrick kan sa ya dade yana tababar inda aka kaishi. Rashin sanin nan ma daidai ne, domin muddan dai mai-zaben bai san inda Luther yake ba, ba zai iya fada ma wani ba. Ya dai gamsu cewa Luther yana cikin tsaro, wannan kuma ya ishe shi.

Bazara da damina da kaka suka wuce, rani kuma ya zo, Luther dai yana tsare. Aleander da magoya bayansa suka ji dadi suna gani kamar hasken bishara ya kusan mutuwa. Amma maimakon haka, Luther ya yi ta cika fitilarsa ne daga rumbun gaskiya; haskenta kuma zai kara karfi.

A sansanin tsaron nan na Wartburg, ya ji dadin sakewarsa daga zafin yaki da hayaniyarta. Amma bai dade yana jin dadin hutun ba. Da shi ke ya saba da aiki da kuma zafin jayayya, bai iya jimre hutu ba. A wannan lokacin kadaicin, yanayin ekklesiya ya zo zuciyarsa, sai ya ta da murya ya ce: "Kash! Babu wani a wannan ranar karshe ta fushinsa, da zai tsaya kamar ganuwa a gaban Ubagiji, ya ceci Israila!" sai tunaninsa ya dawo wurinsa kuma, ya ji tsoron cewa za a zarge shi da cewa matsoraci ne shi, da shike ya gudu daga fadar. Sai ya tsauta ma kansa sabo da kiwuyarsa da son kansa. Duk da haka kowace rana ya rika yin ababan da mutum daya ba zai iya yi ba. Alkalaminsa bai taba hutawa ba. Yayin da magabtansa ke rudin kansu cewa an rufe bakinsa, sun yi mamaki suka kuma firgita ganin alamun cewa yana kan aikinsa. Rubuce rubucensa sun yadu ko ina a Jamus. Ya kuma yi ma 'yan kasarsa babban hidima ta wurin juya Sabon Alkawali zuwa harshen Jamusanci. Daga dutsensa, misalin Pathmos, ya kusa shekara guda yana shelar bishara, yana kuma tsautawa game da kura-kuran zamanin.

Amma ba domin kare Luther daga fushin magabtansa ne kadai, ko kuma domin a ba shi lokaci don yin muhumman ayukan nan ne kadai, Allah Ya janye bawan Shi daga rayuwa cikin jama'a ba. Akwai manufofin da suka fi wadnnan. A boyayyen wurin nan na kadaici, an dauke Luther daga taimako na duniya, aka boye shi daga yabo na duniya. Ta hakanan aka cece shi daga alfarma da dogara ga kansa, wanda nasara takan iya jawowa. Ta wurin wahala da kaskantarwa, an shirya shi domin ya sake tafiya kan tafarkin da an rigaya an kai shi.

Yayin da mutane ke murna cikin yancin da gaskiya ke kawo masu, sukan so su daukaka wadanda Allah Ya yi anfani da su domin su tsinke sarkokin kuskure da camfi. Shaitan yana kokarin janye tunanin mutane daga Allah, ya kai su kan mutane. Yakan sa su girmama kayan aikin, su kuma manta da Hannun da ke bi da kowane al'amari. Sau da yawa shugabannin addini da ake yaba masu ana kuma daukaka su, sukan manta dogararsu ga Allah har su dogara ga kansu. Sakamakon wannan, sukan so su mallaki zukata da lamirin mutanen da ke so su nemi bishewa daga gare su, maimakon meman bishewa daga maganar Allah. Aikin canji yakan sami koma baya sabo da irin ruhun nan. Allah Ya tsare aikin Canji daga wanan hatsarin. Ya so aikin ya sami hatimin Allah ne, ba na mutum ba. Zukatan mutane sun koma wurin Luther a matsayin mai-bayana gaskiyar; an cire shi domin dukan idanu su koma ga Tushen gaskiya na har abada.

Babi na 9—Dan Canjin Switzerland

Shirin Allah game zaben ma'aikata don kawo canji a ekklesiya daidai yake da shirinsa domin kafa ekklesiya. Babban Mallami na saman Ya tsallaka manyan mutanen duniya, masu matsayi da mawadata, wadanda suka saba karban yabo da bangirma daga mutane. Sun rika alfarma da alfahari, suna fariya da giramansu ta yadda ba za a iya sifanta su su tausaya ma yan-uwan su mutane, su kuma zama abokan aikin Mutumin Nazareth din nan mai-tawali'u ba. Ga jahilan masunta masu faman nan na Galili aka yi kira cewa: "Ku biyo ni, ni kuwa in maishe ku masuntan mutane."Matta 4:19. Almajiran nan masu tawali'u ne, masu karban koyaswa kuma. Karancin tasirin koyaswar karya ta zamaninsu a gare su ya sa Kristi Ya kara yin nasaran koyar da su da kuma horar da su don hidimarsa. Haka lokacin babban Canjin. Shugabannin Canjin masu tawali'u ne, mutanen da ba ruwan su da fahariyar matsayi da kuma tsananin ra'ayin priestanci. Shirin Allah ne Ya yi anfani da kananan kayan aiki don cim ma manyan manufofi. Ta haka ba za a daukaka mutane ba, sai dai Shi wanda Ya ke aiki ta wurinsu domin sun yarda su yi abin da ya gamshe Shi.

Makonnni kalilan bayan haifuwar Luther a dakin mai-aiki a ramin ma'adini a Saxony, aka haifi Ulric Zwingli a gidan wani mai-kiwo a cikin duwatsun Alps. Abubuwa da suka kewaye wurin zaman Zwingli a kuruciyar sa, da horonsa na farko, sun shirya shi domin aikin shi nan gaba. Da shi ke ya girma cikin wurare masu asalin kyau da muhimmanci, masu girma na ban tsoro, hankalin sa ya saba tunanin girma da iko da martabar Allah, tun yana yaro. Tarihin ayukan sa na jaruntaka a kan duwatsun garinsu sun shafi burinsa tun samartakansa. Kuma a gefen kakansa mai- ibada, ya ji labaru daga Littafin da ita ma ta tsinto daga tatsuniyoyi da al'adun ekklesiya. Da marmarin gaske ya yi ayukan ubani da annabawa, da makiyaya da suka yi kiwon garkunan su a tuddan Falesdinu, inda malaiku suka yi magana da Mutumin Kalfari kuma.

Kamar John Luther, baban Zwingli ya so ma dansa ilimi, ya kuwa tura shi makaranta tun da wuri. Tunanin shi ya girma nan da nan, tambaya kuma ta kasance, Ina za a sami mallamai masu kwarewa da za su koya masa. Yana dan shekara goma sha uku ya je Bern, inda akwai makaranta mafi inganci a Switzerland. Amma kuma a nan, wani hatsari ya taso da ya yi barazanar lalata burinsa. Ma'aikatan ekklesiya suka yi iyakar kokari su ja hankalin shi ya shiga gidan 'yan zaman zuhudu. 'Yan kungiyar zaman zuhudun Dominican da na Franciscan suka rika kishin juna game da samun farin jini. Sun yi kokarin samun wannan ta wurin adon da suka yi ma majami'unsu, da fahariyar iliminsu, da manyan sifofi masu kyau da al'ajiban da suka rika yi.

Yan Dominican na Bern sun ga cewa idan suka iya jan hankalin saurayin nan dalibi mai-baiwa, za su sami farin jini da daraja. Samartakansa da iya maganansa da iya rubutunsa kuma, da kuma baiwarsa ta iya waka da wake, za su fi dukan girman kai da fahariyarsu jan hankalin mutane zuwa hidimominsu, su kuma kara ma kungiyarsu kurdi. Ta wurin rudi da

fadanci suka yi kokarin shawo kan Zwingli ya shiga kungiyarsu. Yayin da Luther ke makaranta, ya bizne kansa cikin daki a wurin da masu zaman zuhudu suke, kuma ya bata daga sauran duniya, in ba don Allah Ya kubutar da shi ba. Ba a yarda Zwingli ya shiga wannan matsalar ba. Ta wurin ikon Allah ubansa ya sami labarin kulle-kullen ma'aikatan ekklesiyar. Ba shi da niyyar barin dansa ya bi rayuwar zaman banza da rashin anfani na masu zaman zuhudu. Ya ga cewa anfanin sa nan gaba yana cikin hatsari, sai ya umurce shi ya dawo gida ban da jinkiri.

An yi biyayya da umurnin; amma matashin bai iya gamsuwa da zaman kauyensu da dadewa ba, ya kuwa fara makarantarsa bayan wani lokaci kuma ya koma Basel, Wittenbach, mai-koyar da tsofofin yaruka na da. Yayin da yake nazarin Hellenanci da Ibrananci, ya taba samun Littafi Mi-tsarki, a haka kuma tsirkiyoyin hasken Allah suka haskaka tunanin daliban sa ta wurin koyaswarsa. Ya sanar da cewa akwai wata gaskiya da ta fi dabarun mallaman makaranta da na masu bin ussan ilimi dadewa da kuma anfani kwarai. Wannan da daddiyar gaskiyar it ace cewa mutuwar Kristi ce kadai fansar mai-zunubi. Kalmomin nan ne tsirkiyar farko da ta zo ma Zwingli, kafin wayewan gari ya zo masa.

Ba da jimawa ba aka kira Zwingli daga Basel ya shiga aikin rayuwarsa. Wurin aikinsa na farko a majami'ar Alps ne, kusa da kauyensu. Da shike an shafe shi priest, ya "dukufa da dukan ransa ga neman gaskiya ta Allah, domin ya sani sarai yawan sanin da yake bukata game da wanda aka damka masa amanar garken Kristi," in ji wani dan-uwansa dan Canji. Yayin da ya ci gaba da nazarin Littafi, bambanci tsakanin gaskiyarsu da riddar Rum ya ci gaba da kara bayanuwa gare shi. Ya ba da kansa ga Littafin a matsayin maganar Allah kadai isashiya mara kuskure. Ya ga cewa dole it ace kadai mai-fassara kanta. Bai isa ya fassara Littafi domin tabbatar da ra'ayi ko koyaswa da ya rigaya ya kulla a zuciyarsa ba, amma ya dauki kudirin koyo daga abin da Littafin ke koyarwa kai tsaye a bayyane. Ya nemi kowane taimako don samun cikakken ganewa adaidai na ma'anar ta, ya kuma roki taimakon Ruhu Mai-tsarki wanda zai bayana ma dukan wanda ya neme shi da gaske cikin addu'a kuma.

Zwingli ya ce: "Littafi ya zo daga Allah ne, ba daga mutum ba, kuma ma Allah Mai-bayanawa zai ba ka ganewa cewa maganar daga Shi Allah ne. Maganar Allah ba za ta taba faduwa ba; tana da haske, ta na koyar da kanta, ta na bayana kanta, tana haskaka rai da dukan ceto, da laheri, ta kuma ta'azantar da mutum cikin Allah, ta ba shi saukin kai, domin ya musunci kansa, ya rungumi Allah kuma." Zwingli da kansa ya tabbatar da gaskiyar kalmomin nongame da rayuwar sa ta wannan lokacin , daga baya ya rubuta cewa: "Sa'an da na fara ba da kai na gaba daya ga Littafi Mai-tsarki, bin ussan ilimi da ilimin tauhidi suka rika shawarta mani yin fada. A karshe tunani ya zo mani cewa, 'Dole ka rabu da dukan masu karya ka koyi ma'anar Allah daga maganarsa mai-sauki kadai.' Sa'an nan na fara rokon Allah haskensa, kuma Littafi ya fara kara saukin ganewa gare ni."

Bisahran da Zwingli ya yi wa'azin tab a daga Luther ya karba ba. Koyaswar Kristi ce. Zwingli y ace: "Idan Luther yana wa'azin Kristi, yana abin da ni ke yin a.wadanda ya kawo wurin Kristi sun fi wadanda ni na kawo yawa. Amma wannan ba komi ba ne. Ba zan amsa wata suna dabam da ta Kristi wanda ni sojansa ne ba, wanda Shi kadai ne kuma Sarki na. Ko kalma daya ban taba rubuta ma Luther ba, Luther kuma bai taba rubuta mani ko kalma daya ba; don me?... Domin a nuna yadda Ruhn Allah ba ya sabani da kansa da shike mu biyu din, ba tare da shawara da juna ba, muna koyar da koyaswar Kristi ba tare da wani sabani ba."

A shekara ta 1516, an gayyaci Zwingli ya je ya zama mai-wa'azi a gidan 'yan zaman zuhudu a Einsiedeln. A nan ya ga kurakuran Rum kusa kusa, ya kuma yi tasiri ga dan Canjin da aka ji har can nesa da kauyensu na Alps. Cikin manyan ababan ban sha'awa a Einsiedeln akwai sifar budurwar, wadda aka ce tana da ikon yin al'ajibai. A kofar shiga unguwar masu zaman zuhudun, aka rubuta cewa: "A nan za a iya karban cikakkiyar gafarar zunubai." Matafiya kowane lokaci suka dinga zuwa wurin budurwar; amma a babbar bukin tsarkaketa na shekara shekara, jama'a da yawa suka rika zuwa daga kowane bangaren Switzerland, har ma daga Faransa da Jamus. Zwingli da ya fusata da abin da ya gani, ya yi anfani da zarafin don shelar yanci ta wurin bishara ga bayin nan na camfi.

Ya ce: "Kada ku zata cewa Allah Yana cikin haikalin nan, fiye da yadda yake a kowane wuri a duniya. Ko da wace kasa kake, Allah Yana kusa da kai, Yana kuma jin ka.... Meme ne anfanin tarin kalmomin da muke jibga ma addu'o'in mu? Wane iko ke a hula mai-ado, ko kai da aka aske suman sa gaba daya, ko doguwar riga, ko takalma masu adon zinariya?.... Allah Yana duban zuciya ne, kuma zukatan mu suna nesa da Shi." Ya ce: "Kristi wanda aka taba ba da Shi a kan giciye, Shi ne hadaya da ta biya hakin dukan zunuban masu ba da gaskiya har abada."

Da yawa cikin masu jin sa basu so maganan nan ba. Ba su so a ce masu wai wahalar tafiyan nan ta su banza ce ba. Basu iya gane gafaran da aka ba su kyauta ta wurin Kristi ba. Sun gamsu da tsohuwar hanyan nan zuwa sama wadda Rum ta zana masu. Suka yi sanyin gwiwa game da rudewan da neman wata hanya dabamza ta kunsa. Ya fi masu sauki su dogara ga priestoci a paparuma, maimakon bidar tsabtar rai.

Amma wata kungiya ta karbi labarin fansan nan ta wurin Kristi da farin ciki. Ababan da Rum ta umurta yi basu kawo salamar zuci ba, cikin bangaskiya kuma suka karbi jinin Mai-ceton a matsayin fansar su, wadannna suka koma gidajen su suka bayana ma wadansu kuma hasken da suka samu. Ta haka aka kai gaskiyar daga unguwa zuwa unguwa, gari zuwa gari, yawan masu zuwa wajen Budurwar kuma ya ragu sosai. Bayaswa kuma ta ragu sosai, haka kuma albashin Zwingli ya ragu, da shike daga baye-bayen nan ake biyansa. Amma wannan ya ba shi farin ciki ne kadai sa'an da ya ga cewa ikon tsananin ra'ayi da camfi yana raguwa.

Shugabanninn ekklesiya basu kasa sanin aikin da Zwingli yake yi ba, amma a wannan sa'ar basu dame shi ba. Da begen komo da shi gefensu, suka yi kokarin jawo shi ta wurin yi mashi balmar baka; ana haka kuma gaskiya tana samun shiga zukatan mutane.

Aikin Zwingli a Einsieldeln ya shirya shi don babban fili, wanda zai shiga ba da jimawa ba. Bayan shekara uku a nan aka kiraye shi a zama mai-wa'azi a babban majami'ar Zurich. A lokacin, Zurich ne gari mafi muhimmanci a tarayyar Switzerland, kuma tasirin da aka kawo nan, za a ji shi ko ina. Masu bisharan da suka gayyato shi Zurick dai sun so su hana duk wani sabon abu, da sauri kuwa suka fada mashi aikin da zai yi.

Suka ce: "Za ka yi iyakan kokari ka tara kurdaden sashin, komi kankantansu. Za ka gargadi masu bi, daga bagadi da kuma wurin-furta zunubinsu, su biya dukan zakkoki da baye baye, su kuma nuna soyayyarsu ga ekklesiya ta wurin baikonsu. Za ka yi kwazo wurin kara kurdin da ke shigowa daga wurin marasa lafiya, da jama'a, a takaice dai, daga kowane fannin ekklesiya." "Game da ba da jibi, da wa'azi da kulawa da garken kuma, wadannan ma aikin mai-bisharan ne. Amma game da wadannan, kana iya samo wani a madadinka, musamman ma game da wa'azi. Kada ka ba kowa jibi, sai dai sanannu, kuma sai an bukaceka ka bayar; ba a yarda maka ka ba kowa ba tare da bambanta mutanen ba."

Zwingli ya saurari umurnin nan shuru, sa'an nan bayan ya nuna godiyarsa sabo da girmama shi da aka yi, da ba shi muhuimmin aikin nan, sai ya ci gaba ya bayana matakin da yake so ya dauka. Ya ce: "An dade ana boye ma mutane rayuwar Kristi. Zan yi wa'azi kan dukan bishara ta Matta...., bisa ga Littafin kadai, ina bayana zurfin ta, ina kuma gwada nassi da nassi, ina kuma neman fahimi ta wurin himma wajen addu'a. Ga daukakar Allah da yabon Dansa tilo, ga ainihin ceton rayuka da kuma ginuwarsu cikin imanin gaskiya ne zan kebe hidima ta." Ko da shike wadansu shugabannin ekklesiyan basu amince da shirinsa ba, suka kuma yi kokarin hana shi bin shirin, Zwingli ya tsaya da karfinsa. Ya bayana cewa ba sabon tsari yake so ya kawo ba, amma tsohon tsarin da ekklesiya ta yi anfani da shi ne a zamanai na farko masu tsarki.

Kafin nan an fara marmarin gaskiyan da ya koyar; mutanen kuma suka rika tururuwa da yawansu don sauraron wa'azinsa. Da yawa da suka dade da barin zuwa sujada suna cikin masu jinsa. Yakan fara hidima ta wurin karantawa da kuma fassara ma masu jinsa daga Bishara, game da rayuwa da koyaswa, da mutuwar Kristi. Nan ma, kamar a Einsiedeln, ya gabatar da maganar Allah a matsayin iko kadai mara aibi, mutuwar Kristi kuma a matsayin cikakkiyar hadaya ita kadai, ba wata kuma. Ya ce: "Wurin Kristi ne nike so in kai ku, wurin Kristi, ainihin tushen ceto." Mutane iri iri, daga manyan gwamnati da masana, zuwa masu aikin hannu da talakawa, suka dinga tattaruwa wajen mai-wa'azin. Da sha'awa sosai suka saurari kalmominsa. Ba kyautar ceto kadai ya bayana ba, ya kuma tsauta ma mugunta da lalacewar zamanin, ba da tsoro ba. Da yawa suka rika dawowa daga majami'ar suna yabon Allah. Suka ce: "Wannan mutumin mai-wa'azin gaskiya ne. Shi ne zai zama Musan mu, domin ya shugabanci fitowar mu daga duhun Masar din nan."

Amma ko da shike da farko an karbi aikin sa da babbar sha'awa, daga bisani jayayya ta taso. Masu zaman zuhudun suka shirya hana aikinsa da kushe koyaswoyinsa. Da yawa suka rika masa ba'a da reni; wadansu kuma suka shiga zagi da barazana. Amma Zwingli ya jumre da hakuri, yana cewa: "Idan muna so mu jawo miyagu zuwa wurin Yesu Kristi, dole mu rufe idanun mu daga abubuwa da yawa."

Wannan lokacin, wata kungiya ta shigo don kara ci gaban canjin. Aka aiki wani mai suna Lucian da wadansu rubuce rubucen Luther zuwa Zurich, ta wurin wani abokin sabuwar bisahrar a Basel, wanda ya shawrta cewa sayar da litattafan anan zai zama babban hanyar baza hasken. Ya rubuta ma Zwingli cewa: "Ka tabbatar ko wannan mutumin yana da isashen hikima da kwarewa; in haka ne, ya kai rubuce rubucen Luther daga birni zuwa birni, daga gari zuwa gari, daga kauye zuwa kauye, har ma daga gida zuwa gida, cikin mutanen Swiss, musamman ma bayanin fassara Luther din ta addu'ar Ubangiji da ya rubuta don marasa ilimin tauhidi. Kara saninsu zai jawo kin cinikinsu." Ta haka ne hasken ya sami hanyar shiga.

Lokacin da Allah ke shirin karye sarkokin jahilci da camfi, lokacin ne Shaitan yakan yi aiki da dukan ikonsa don kunsa mutane cikin duhu, kuma don kara daure sarkokinsu da karfi. Yayin da mutane ke tasowa a kasashe dabam dabam don mika ma mutane gafara da barataswa ta wurin jinin Kristi, Rum ta ci gaba da karin karfi don bude kasuwar ta ko in cikin Kirista, tana tallan gafara sabo da kurdi.

Kowane zunubi da farashisa, aka kuma ba mutane lasin na yin zunubi kyauta, muddan dai baitulmalin ekklesiya zai cika sosai. Ta haka kungiyoyi biyu din suka ci gaba, daya tana tallan gafara don kurdi, dayan kuma tana shelar gafara ta wurin Kristi, Rum tana ba da lasin na zunubi tana kuma samun kurdin shiga; yan canjin suna kushe zunubi, suna kuma nuna Kristi a matsayinsa na kafara da mai-kubutarwa.

A Jamus, an damka cinikin takardun shaidar gafara a hannun priestocin kungiyar Dominican ne, kalkashin Tetzel. A Switzerland, an ba da cinikin a hannun 'yan Franciscan ne, kalkashin shugabancin Samson, mai-zaman zuhudu, dan Italiya. Samson ya rigaya ya yi ma ekklesiya aiki mai-kyau inda ya tara makudan kurdi a Jamus da Switzerland da suka isa su cika baitulmalin paparuma. Yanzu kuma ya rika yawo a Switzerland yana jawo jama'a da yawa, yana tsotse kurdaden talakawa, yana kuma jan kyaututtuka masu tsada daga mawadata. Amma tasirin Canjin ya rigaya ya kai inda ya rage yawan kasuwancin, ko da shike bai tsayar da shi ba gaba daya. Zwingli, dai yana Einsiedeln lokacin da Samson, jima kadan bayan da ya shigo Switzerland, ya taho da kayan jarinsa a wani makusancin gari. Da aka fada ma Zwingli abin da ya kawo shi, nan da nan ya je domin ya yi jayayya da shi. Basu sadu ba, amma Zwingli ya yi nasarar fallasa karyar priest din ta yadda ya kama shi dole ya koma wani gari dabam.

A Zurich, Zwingli ya yi wa'azi da himma sabanin masu jarin gafaran nan; kuma da Samson ya kusa da wurin, wani masinja daga majalisa ya same shi da sako cewa ana bukatar shi ya wuce ne. Daga baya ta wurin dabara ya shiga garin, amma aka kore shi, ko gafara daya bai sayar ba; ba da dadewa ba kuma ya bar Switzerland. Canjin ya sami karin karfi sa'anda annoba, ko Babbar Mutuwa, da ta abka ma Switzerland; a shekara ta 1519 ta bayana. sa'anda mutane suka gamu da mai-hallakaswa, fuska da fuska, da yawa suka ji yadda gafaran da suka saya ya tabbata banza mara anfani; suka kuma yi sha'awar tabbatacen harsashe domin bangaskiyarsu.

Zwingli a Zurich ya harbu da ciwo; ya kai inda begen warkewar sa ya kare, labari kuma ya kai ko ina cewa ya mutu. Cikin wannan mawuyacin halin ma begen sa da karfi halinsa basu ragu ba. Ya rika duban giciyen Kalfari yana dogarawa ga cikakkiyar kafara ga zunubi. Sa'an da ya dawo daga kofofin mutuwa, ya yi wa'azin bishara da himma fiye da duk yadda ya taba yi; kalmominsa kuma suka fito da iko na ban mamaki. Mutanen suka marabci paston su kaunatace da farin ciki, paston da aka dawo masu da shi daga bakin mutuwa. Su kansu sun fito jinyar marasa lafiya da masu mutuwa, suka kuwa ji tamanin bishara yadda basu taba ji ba.

Zwingli ya kara fahimtar gaskiyar bisharar, ya kuma dandana a jikinsa cikakken ikonta na sabuntawa. Faduwar mutum da shirin fansa ne kawunan magana da ya mai da hankalinsa akai. Ya ce: "Cikin Adamu, dukan mu matattu ne, nutsatsu cikin lalacewa da hukumci." "Kristi.... Ya sayo mana fansa mara karshe.... Azabarsa, hadaya ce ta har abada, mai-ikon warkarwa kuma har abada; tana gamsar da adalcin Allah har abada a madadin dukan wadanda suka dogara gare ta da bangaskiya mai-karfi mara kaduwa." Duk da haka ya koyar a fili cewa mutane ba su da yancin ci gaba da zunubi wai don alherin Kristi. "Duk inda akwai bangaskiya ga Allah, akwai Allah, kuma duk inda Allah Yake, akwai himma da ke ingiza mutane su yi nagargarun ayuka."

Sha'awar saurarom wa'azin Zwingli ta kai inda har majami'ar ma takan cika da jama'a masu son sauraronsa, har ta kasa. Kadan da kadan dai ya rika bayana masu gaskiya. Ya yi hikima da bai fara da ababan da za su ba su mamaki har su ta da kiyayya ba. Aikinsa dai shi ne jawo hankalin su zuwa koyaswoyin Kristi, domin su zama masu saukin kai tawurin kaunar Kristi din, ya kuma nuna masu kwatancin Kristi; kuma yayin da za su karbi kaidodin bisharar, za a hambarar da camfe camfensu ba jinkiri.

Sannu a hankali canjin ya ci gaba a Zurich. Cikin fushi magabatansa suka tayar da jayayya. Shekara guda kafin nan, Luther, mai-zaman zuhudun Wittenberg, ya ce ya ki ma paparuma da babban sarki a Worms, yanzu kuma komi ya nuna kamar za a maimaita tsayayyan nan da koyaswar paparuma a Zurich ma. An dinga kai ma Zwingli hare hare akai akai. A cibiyoyin 'yan paparuma loto loto an dinga kai almajiran bishara wurin kisa, amma wannan bai isa ba, dole a kashe Zwingli mai koyar da ridda. Sabo da haka bishop na Constance ya tura wakilai uku zuwa majalisar Zurich, yana zargin Zwingli da koya ma

mutane su ketare dokokin ekklesiya, wannan kuwa yana barazana ga salama da oda. Ya ce idan aka kawar da ikon ekklesiya dukan duniya za ta shiga rashin zaman lafiya. Zwingli ya amsa cewa shekara hudu yana koyar da bishara a Zurich, amma Zurich din ya fi kowane gari cikin tarayar zaman lafiya. Ya ce: “Wannan bai nuna cewa Krisitanci ne ya fi tabbatar da tsaroba?”

Wakilan sun rigaya sun shawarci yan majalisar wadda suka ce cikin ta kadai ake samun ceto. Zwingli ya amsa: “Kada wannan zargi ya dame ku. Harsashen ekklesiya shi ne Dutse dayan, Kristi dayan da Ya ba Bitrus sunansa domin ya karbe Shi da aminci. A kowace al’umma duk wanda ya ba da gaskiya da dukan zuciyarsa cikin Ubangiji Yesu, za ya karbu ga Allah. Wannan a gaskiya ita ce ekklesiyar, wadda cikin ta kadai ake samun ceto.” Sakamakon wannan taron, daya daga cikin wakilan bishop din ya karbi sabuwar bangaskiyar.

Majalisar ta ki daukan mataki akan Zwingli, Rum kuma ta yi shirin sabon hari. Sa’an da aka fada masa kulle kullen magabatansa, Zwingliya ce: “Bari su zo; ina tsoron su kamar yadda dutsen gefen kogi ke tsoron igiyoyin rowan da ke kalkashin sawayensa.” Gaskiya ta ci gaba tana yaduwa. A Jamus magoya bayanta da suka damu sabo da bacewar Luther, suka ta’azantu kuma sa’an da suka ga ci gaban aikin a Switzerland.

Sa’an da Canjin ya faru a Zurich, aka fi ganin sakamakonsa a raguwar mugunta da ci gaban oda da jituwa. Zwingli ya rubuta: “Salama tana da mazauninta a garinmu, ba fada, ba riya, ba kishi, ba tashin hankali. Daga ina irin hadin kan nan zai fito in ba daga wurin Ubangiji, da koyaswar mu da ke cika mu da ‘ya’yan salama da ibada ba?”

Nasarorin Canjin sun hanzuga yan Rum, suka kara kokarin hambarar da shi. Ganin kankantar abin da zalunci ya samo game da danne aikin Luther a Jamus, suka shirya tasam ma Canjin ta wurin anfani da makaman da canji ke anfani da su. Za su yi mahawara da Zwingli, su kuma tabbatar sun yi nasara ta wurin zaben wurin mahawaran da alkalan mahawaran, su da kansu. Idan kuwa suka sami Zwingli sau daya a kalkashi ikon su, za su tabbatar cewa bai tsere masu ba. Idan aka gama da shugaban, za a iya murkushe kungiyan nan da nan. Amma fa an boye wannan shirin da kyau sosai.

An shirya za a yi mahawaran a Baden ne; amma Zwingli bai hallara ba. Majalisar Zurich da ta gane kulle kullen yan paparuma, da kuma ganin yawan kisan magoya bayan bishara da ake yi a wuraren yan paparuma, suka hana paston nasu sa kansa cikin wannan kasadar. A Zurich, yana shirye ya sadu da dukan wadanda Rum za ta aika; amma zuwa Baden, inda aka fito zub da jinin masu bi, sabo da gaskiya, zai zama zuwa wurin mutuwa kenan. Aka zabi Oecolampadius da Haller su wakilci yan Canjin, yayin da Dr. Eck tare da likitoci masana da priestoci da yawa za su wakilci Rum.

Ko da shike Zwingli bai halarci taron ba, an ji tasirinsa. ‘Yan paparuma ne suka zabi dukan sakatarorin, aka kuma hana sauran yin rubutu, wanda ya yi kuma a kashe shi. Duk

da haka Zwingli ya sami rahotun komi da aka fada a Baden kowace rana. Wani dalibi da ya kasance a wurin taron ya dinga rubuta mahawaran da aka yi kowace rana. Wadansu dalibai biyu kuma suka dauki nauyin kai ma Zwingli rahotanin nan, tare da wasikun Oecolamoadius kowace rana a Zurich. Zwingli yakan amsa tare da shawarwari. Yakan rubuta wasikun sa d a dare ne, daliban kuma sukan kai ma Oecolampadius da safe. Don kada masu tsaron birnin su gane su, daliban sukan zo da kwandunan kaji a kawunansu, akan kuma bar su su wuce ba matsala.

Ta haka Zwingli ya ci gaba da yakinsa da magabtansa. Miconius ya ce: “Ya yi aiki ta wurin bimbininsa da kwana ganinsa, da shawararin da ya rika turawa Baden, fiye da yadda ya yi ta wurin mahawara da kansa a tsakanin magabtansa.”

Magabtan, cike da begen nasara, sun zo Baden cikin tufafinsu mafi tsada, cike da ado. Sun rika shakatawa suna cin abinci iri iri masu tsada, ga ababan sha na musamman. Suka rika sauke nauyin aikinsu na ekklsiya ta wurin annashuwa. Sabanin wannan sai ga ‘yan Canji, wadanda mutane suka gan su kamar da kadan suka fi masu-bara da karancin abincin su ya sa ba sa dadewa a wurin cin abincin. Sa’an da mai-gidan dakin da Oecolampadius ke haya ya leka shi kowace rana, yakan gan shi yana nazari ne ko kuma addu’a, cikin mamaki kuwa ya ce wannan mai-riddan, ko ba komai dai yana ibada.

A wurin taron, “Eck da girman kai ya hau bagadi da aka masa ado sosai, amma Oecolampadius ya sa sutura mara tsada, aka tilasta mashi ya zauna a gaban magabcin sa kan wata yar kujerar katako mara baya.” Babban muryan nan na Eck da yawan tabbacinsa, basu taba barin shi ya karai ba. Himmar sa ta karu sabo da begen zinariya da yin suna, domin an ce ladar mai-kare bangaskiyar kurdi ne mai-yawa. Sa’an da ya rasa abin fadi na kwarai, sai ya shiga zagi har da rantsuwa.

Oecolampadius, cikin saukin kai da ganin kasawar kansa, ya yi shakkar shiga mahawarar, ya kuma shige ta da cewa: “Ban amince da wani ma’auni ba sai maganar Allah.” Ko da shike mai-hankali ne da bangirma, mutum ne shi mai kwarewa da naciya kuma. Yayin da ‘yan Rum din suka dogara ga al’adun ekklesiya, dan Canjin ya manne ma Littafi babu kaucewa. Ya ce: “Al’ada ba ta da iko a Switzerland din mu, sai dai bisa ga kundin tsarin dokokin kasar; yanzu fa, a sha’anin bangaskiya Littafi ne kundin tsarin dokokin mu.”

Bambanci tsakanin mutum biyu masu mahawaran nan ya yi tasiri. A karshe, yan paparuma sun dauka cewa sun yi nasara. Yawancin wakilan sun goyi bayan Rum, Majalisar kuwa ta furta cewa an ka da ‘yan Canjin, ta kuma ce su da shugabansu Zwingli an yanke su daga ekklesiya. Amma sakamakon taron ya nuna ko wane ne ya yi riba. Mahawarar ta haifar da kwarin gwiwa ga aikin masu kin ikon paparuma, kuma ba da jimawa ba bayan wannan, manyan biranen Bern da Basel suka bayana cewa su ‘yan Canji ne.

Babi na 10—Ci Gaban Canji a Jamus

Bacewar Luther ta jawo damuwa ko ina a Jamus. An rika jin tambayoyi game da shi ko ina. An yayata jita-jita, mutane da yawa kuma suka dauka cewa an kashe shi ne. Aka yi makoki sosai, ba sanannun abokan sa kadai ba, har da dubbai da basu bayana matsayin su game da Canjin ba. Da yawa suka rantse za su rama mutuwarsa.

Shugabannin Romawa cikin tsoro suka ga yawan munin kiyayar da ake masu. Ko da shike da farko sun yi murna cewa Luther ya mutu, nan da nan suka so su buya daga fushin mutanen. Magabtansa basu taba damuwa da manyan ayukan karfin halinsa kamar yadda suka damu da bacewarsa ba. Wadanda cikin fushinsu suka so su hallaka dan Canjin nan kuwa suka cika da tsoro yanzu da ya zama kamamme mara taimako. Wanin su ya ce: “Hanya daya tak da ta rage mana don ceton kanmu ita ce mu kunna fitillu, mu nemi Luther ko ina a duniya, mu mayar da shi ga al’ummar da ke bidar sa.” Dokar babban sarkin ta kasa aiki. Wakilan paparuma suka cika da haushi, ganin cewa dokar ba ta jawo hankula kamar yadda yanayin da Luther ke ciki ya jawo ba.

Labarin cewa yana lafiya ko da shike fursuna ne shi, ya kwantar da hankulan mutane, ya kuma kara yawan sha’awarsa da suke yi. An rika karanta rubuce rubucen sa da marmari fiye da da. Yawan masu goyon bayan mutumin nan, wanda a cikin kasada mai ban tsoro ya tsare maganar Allah, ya karu sosai. Canjin ya ci gaba da kara karfi. Irin da Luther ya shuka ya tsiro ko ina. Bacewar sa ta yi aikin da kasancewarsa da ba ta yi ba. Wadansu ma’aikata ma suka ji sabon aiki ya kama su, yanzu da babban shugabansu ba ya nan. Da sabuwar bangaskiya da kwazo kuma, suka yi iyakar kokarinsu, domin kada aikin da aka fara da kyau ya sami koma baya.

Amma Shaitan bai huta ba. Yanzu kuma ya gwada abin da yakan gwada a kowane kokari na canji: ya rudi mutane ya kuma hallaka su ta wurin rudinsu da jabu a maimakon aiki na gaskiyan. Kamar yadda aka sami Kristi na karya a karnin farko na ekklesiyar Kirista, haka annabawan karya suka taso a karni na goma sha shida.

Mutane kalilan da suka motsu ta wurin abin da ke faruwa a sha’anin addini suka ga kamar sun sami ruya ta musamman daga sama, suka kuma ce wai Allah Ya aiko su su ci gaba har karshe da Canjin da Luther ya fara da kumamanci, in ji su. Gaskiyar ita ce, sun rika warware aikin da shi ya yi ne. Suka ki babban kaidar da ta kasance harsashen Canjin, cewa maganar Allah ce kaidar gaskiya da ayuka; kuma suka sanya wannan mai bishewar da ra’ayinsu da tunanin kansu kuma. Ta wurin kawar da babban abin da ke bayana kuskure da karya aka bude ma Shaitan hanyar mallakar zukata yadda ya ga dama.

Daya daga annabawan nan ya ce wai malaika Jibrailu ne ya aiko shi. Wani dalibi da ya bi shi, ya watsar da makaranta yana cewa wai Allah da kan Shi ya ba shi hikimar bayana maganarsa. Wadansu da suka saba da tsananin ra’ayi suka hada kai da su. Aukan wadannan

mutanen sun ta da hankula sosai. Wa'azin Luther ya falkas da mutane ko ina, suka ji a jikinsu cewa canji ya zama dole, yanzu kuma annabawan karya suka rudi mutane masu ainihin gaskiya.

Shugabanin sabuwar kungiyar suka ci gaba zuwa Wittenberg. Suka dami Melanchthon da abokan aikinsa da ra'ayoyinsu. Suka ce: "Allah Ya aiko mu mu koya ma mutanen. Mun ji sahwarwari kai tsaye daga Ubangiji; mun san abin da zai faru; a takaice, mu manzani ne da annabawa, muna tare kuma da Luther."

Yan Canjin sun yi mamaki sosai. Basu taba gamuwa da irin wannan ba, kuma basu san matakin da za su dauka ba. Melanchthon ya ce: "Hakika, akwai ruhohi na musamman cikin mutanen nan; amma wadanne ruhohi?... A gefe daya, mu yi hankali da bice Ruhun Allah, a daya gefen kuma, mu yi hankali kada mu bar ruhun Shaitan ya batar da mu." Sakamakon sabuwar koyaswar ya bayana nan da nan. Ya sa mutane suka kyale Littafi, ko ma suka ajiye shi a gefe gaba daya ma. Makarantu suka shiga rudami. Dalibai suka watsar da makaranta, suka janye daga jami'ar. Mutane da suka ga kamar suna da kwarewar da za su falkas da aikin Canjin, sun kai aikin kusa da hallaka ne kawai. Masu bin Rum din suka dawo da kwarin gwiwansu, suka ce: "Fama daya na karshe kawai sa'an nan komi zai zama namu."

Luther a Wartburg, da jin abin da ya faru, ya ce: "Da ma na san Shaitan zai aiko mana wannan annobar" Ya gane ainihin halin annabawan karyan nan ya kuma ga hadarin da ke barazana ga gaskiyar. Jayayyar paparuma da ta babban sarkin basu jawo masa irin damuwa da rudewa da ya shiga a wannan lokacin ba. Daga masu cewa su abokan Canjin ne, magabtansa mafi-muni suka fito. Gaskiyan nan da ta ba shi murna da kwanciyar rai ne aka yi anfani da ita don ta da hargitsi da rudewa cikin ekklesiya.

Cikin aikin canjin nan, Ruhun Allah ne Ya dinga ingiza Luther. Bai shirya daukan matakai da ya dauka ba, ko kuma ya yi canje canjen da ya yi ba, shi dai ya kasance kayan aiki ne a hannun Iko mara iyaka. Duk da haka yakan yi rawan jiki game da sakamakon aikinsa. Ya taba cewa: "Idan an san cewa koyaswata za ta yi ma wani mutum daya rauni, komi kankantansa, wanda kuwa ba zai taba yiwuwa ba, da shike bishara ce kanta, zan gwammaci mutuwa sau goma maimakon kin janye koyaswar."

Yanzu kuma Wittenberg kansa, cibiyar Canjin, ta fada cikin tsananin ra'ayi da rashin bin doka. Wannan mumunan yanayi ba daga koyaswoyin Luther ba ne; amma ko ina Jamusawa, magabtansa sun rika tura masa laifin. Cikin bacin rai, wani lokaci yakan tambaya: "Ko wannan zai iya zama sakamakon Canjin?" idan kuma ya koma ga Allah cikin addu'a, salama takan shigo zuciyarsa. Yakan ce: "Aikin ba nawa ba ne, naka ne. Ba za ka bari ya lalace ta wurin camfi ko tsananin ra'ayi ba." Amma tunanin ci gaba da rabuwa da jayayyar har wannan tsawon lokacin a wannan yanayi ba daidai ba ne. Sai ya shirya zai koma Wittenberg.

Ba da jinkiri ba, ya kama hanyarsa mai yawan hadari. Yana dai kalkashin takunkumin kasar. Magabta suna da yanci su dauke ransa; an kuma hana abokai taimaka masa, ko kuma ba shi masauki. Gwamnatin kasar ta dauki matakai masu tsanani game da masu goyon bayansa. Amma ya ga cewa aikin bishara ya sami matsaloli, cikin sunan Ubangiji kuma ya fita ba tsoro, domin yin yaki sabo da gaskiya.

Cikin wasikarsa zuwa ga mai-zaben, inda ya fada masa niyyar sa ta barin Wartburg, Luther ya kara da cewa: “Ina shirye in sadu da rashin gamsuwar ka ya mai-girma, game da zuwa na Wittenburg, kalkashin tsaron da ya fi na yarima da na sarakuna. Ba na tunanin neman goyon bayan ka, kuma maimakon neman tsaron ka ma gara ni kai na in tsare ka. Idan na sani kai mai-girma za ka tsare ni, ba zan je Wittenburg ba ma sam. Babu takobin da zai iya ci gaba da wannan aikin. Dole Allah ne zai yi komi ba tare da taimako ko yardar mutum ba. Shi wanda Ya fi bangaskiya Shi ne Ya zai fi iya tsaro.”

Cikin wasika ta biyu da ya rubuta a hanyarsa zuwa Wittenburg, Luther ya kara da cewa: “Ina shirye in fuskanci rashin jin dadin ka, ya mai-girma, da fushin dukan duniya ma. Yan Wittenberg ba tumaki ba ne? Ba Allah ne ya ba ni amanarsu ba? Bai kamata ni, in ta kama, in ba da kai na ga mutuwa sabo da su ba? Ban da haka, ina tsoron ganin mumunar annoba a Jamus, wadda Allah zai hori al’ummarmu da ita.”

Cikin lura da bangirma, amma kuma da gaske, ya shiga aikinsa. “Ta wurin maganar za mu rushe, mu kuma hallaka abin da aka kafa da karfi. Ba zan yi anfani da karfin yaki masu camfi da rashin bangaskiya ba.... Ba wanda za a tilasta. Yanci shi ne ainihin bangaskiya.”

Jima kadan aka labarta a Wittenberg cewa Luther ya dawo kuma zai yi wa’azi. Mutane suka kwararo daga kowane gefe, majami’a kuma ta cika makil. Da ya hau bagadi, cikin hikima da natsuwa ya umurta, ya karfafa, ya kuma tsauta. Game da aikin wadansu da suka yi anfani da karfi don kawas da mass, ya ce:

“Mass mumunan abu ne, Allah ba ya son shi; ya kamata a kau da shi; kuma fata ta ce a duk duniya a sauya shi da jibi na bishara. Amma kada a raba wani da shi karfi da yaji. Dole mu bar batun a hannun Allah. Maganarsa ce za ta yi aiki ba mu ba. Don me kuwa? Domin zukatan mutane ba a hannuna su ke ba, yadda mai-yin tukwane ke rike da yumbu. Muna da yancin yin magana; ba mu da yanci game da aikatawa. Bari mu yi wa’azi, sauran na Allah ne. Idan na yi anfani da karfi mene ne riba ta? Gatsine, kwaikwayo, al’adun mutane, da riya.... Amma ba za a iske zukata na gaskiya ko ainihin bangaskiya ko kauna ba. Inda ba abu ukun nan, ba komi kenan, kuma ba zan dami kai na da wannan ba.... Allah Ya na yin abu da yawa da maganarsa fiye da abin da ni da kai da dukan duniya ke yi da karfin dukan mu. Allah Yana kama zuciya ne; kuma sa’an da aka kama zuciya, an sami komi kenan...”

“Zan yi wa’azi, da mahawara da rubutu, amma ba zan tilasta ma wani ba, da shike bangaskiya yardar rai ne. Dubi abin da na yi. Na yi jayayya da paparuma da cinikin gafara da masu goyon bayan paparuma, amma babu nuna karfi ko tashin hankali. Maganar Allah na sa a gaba; na yi wa’azi, na yi rubutu; abin da na yi kenan kadai. Duk da haka yayin da nike barci,...maganar da na yi wa’azin ta ta hambarar da paparuma, ta yadda babu yarima ko babban sarki da suka yi ma maganar wata illa sosai. Kuma ban yi komi ba, maganar kadai ta yi komi. Da na so in yi anfani da karfi watakila da dukan Jamus ta jike da jinni. Amma da mene ne sakamakon? Hasara da kango na jiki da na ruhu. Sabo da haka ne na yi shuru, na bar maganar ta shiga duniya ita kadai.”

Kowace rana, har mako guda, Luther ya ci gaba da yi ma jama’a wa’azi. Maganar Allah ta karya makarin matsanancin ra’ayi. Ikon bishara ya sa wadanda aka rude su suka dawo hanyar gaskiya. Luther bai yi marmarin saduwa da masu matsanancin ra’ayin nan da aikinsu ya haifar da masifa sosai ba. Ya san su marasa tunani mai-kyau ne, da rashin tarbiyya kuma sosai, wadanda yayin da suke cewa sun sami wayarwa daga sama, ba za su jimre jayayya mafi kankanta ko ma gargadi ko shawara mafi anfani ba. Da suka mallaka ma kan su mafificiyar daukaka, suka bukaci kowane mutum ya yarda da ikirarinsu, ban da tambaya. Amma sa’an da suka nemi yin ganawa da shi ya, yarda zai sadu da su; kuma ya tone karyarsu sosai, ta yadda nan da nan ‘yan sojan gonan suka fice daga Wittenberg.

An tsai da matsanancin ra’ayin, na wani lokaci; amma shekaru kalilan daga baya ya bullo da karin karfi da munanan sakamako kuma. Game da shugabannin masu wannan ra’ayin, Luther ya ce: “Gare ku Littafi mataciyar magana ce; dukansu kuma suka far ihu, ‘Ruhun! Ruhun!’ Amma hakika ba zan bi inda ruhun su ke kai su ba. Bari Allah cikin jinkansa Ya kiyaye ni daga ekklesiyar da babu kowa sai tsarkaka. Ina so in kasance tare da masu twali’u, marsa karfi, marasa lafiya, wadanda sun san zunubansu, suna kuma kuka ga Allah kullum daga tsakiyar zuciyarsu don samun taimakonsa da goyan bayansa.”

Thomas Munzer, mafi zafi cikin masu matsanancin ra’ayin, mutum ne mai-kwarewa sosai, wanda da ya yi anfani da kwarewarsa daidai, ya yi abu mai-kyau; amma shi bai koyi kaidodin addinin gaskiya ba tukuna. “Ya shaku da marmarin canza duniya, kuma ya manta, kamar yadda dukan masu tsananin sha’awa sukan yi, cewa ya kamata canjin ya fara daga shi kansa ne.” Ya yi burin samun matsayi da tasiri, kuma bai yarda ya zama na biyu ga ko Luther kansa ba. Ya ce ta wurin sauya ikon Littafi a maimakon ikon paparuma suna kafa wani tsarin paparuma ne dabam kawai. Ya ce shikansa an aiko shi ya fito da canji na gaskiya ne. “Wanda ke da irin wannan ruhun,” in ji Munzer, “yana da bangaskiya ta kwarai, ko da ba zai taba ganin Littafi ba duk tsawon rayuwarsa.”

Mallamai masu matsanancin ra’ayi sun bar zato ya mallake su, suka mai da kowane tunani ko tsammani kamar muryar Allah ce; sabo da haka suka kai makura sosai game da dukan al’amura. Wadansu ma sun kona Littafinsu, suna cewa: “Harafi yana kisa, amma ruhu yana bada rai.” Koyaswar Munzer ta je dadai da sha’awar al’ajibai da mutane ke da

shi, yayin da ya kuma gamsar da alfarmar su ta wurin ba ra'ayin mutum da tanninsa fifiko bisa maganar Allah. Dubbai suka karbi koyaswarsa. Jima kadan ya yi watsi da duk wani tsari ko oda cikin sujadar jama'a, ya kuma ce yin biyayya ga yarima kokari ne na bauta ma Allah da Belial tare.

Zukatan mutane da suka rigaya suka fara watsar da kangin paparuma sun kuma damu sabo da takurar mahukmta na gwamnati. Koyaswoyin Munzer na juyin dan wake da ya ce Allah ne Ya ba shi, sun sa mutane suka bijire ma kowane iko, suka dogara ga wariyarsu da tunaninsu. Munanan ayukan tawaye da tashin hankali suka fara aukuwa, har kasar Jamus ta jike da jini.

Damuwan da Luther ya fuskanta da dadewa a Erfurt ya taho masa yanzu da karin karfi, yayin da ya ga sakamakon matsanancin ra'ayi da aka zargi Canjin da yi. Mahukunta 'yan tsarin paparuma suka ce, kuma da yawa suka so su yarda, cewa gawayen da aka yi sakamakon koyaswar Luther ne. Ko da shike zargin nan ba shi da tushe ko kankani, duk da haka ya jawo ma Luther damuwa babba. Bai iya gane yadda aka daidaita aikin gaskiya da muguntar matsanancin ra'ayi ba. Ta wani bangaren kuma shugabannin tawayen sun ki jinin Luther domin, ban da jayayyar sa ga koyaswarsu, ya kuma ki amincewa da ikirarinsu cewa Allah ne Ya aiko su. Domin ramuwa su kuma suka yi sokar sa cewa sojan gona ne shi. Kaman dai ya jawo ma kansa kiyayyar mahukumta da na mutane ne.

Yan Rum din sun yi murna, suna jira su ga faduwar Canjin; suka kuma ba Luther laifi har game da kurakuran da ya yi ta kokarin gyarawa. 'Yan matsanancin ra'ayin da suka yi zargin cewa ba a yi masu adalci ba, suka yi nasarar samun goyon bayan jama'a da yawa, kuma, kamar yadda aka cika yi game da masu kuskure, sai aka kuma mai da su kamar wadanda aka wulakanta sabo da banaskiyarsu. Sabo da haka wadanda suka rika yin iyakar kokarin yin sabani da Canjin su ne aka tausaya masu, aka kuma yaba masu cewa su ne aka yi masu mugnta da danniya. Aikin Sahitan ke nan ta wurin ruhun tawaye dayan da ya fara nunawa tun a sama.

Shaitan kullum yana kokarin rudin mutane domin ya sa su kira zunubi adalci, adlci kuma zunubi. Kuma yana yin nasara! Sau da yawa akan yi ma amintattun bayin Allah horo da reni domin sun tsaya ba tsoro suna kare gaskiya! Amma a kan yabi wakilan Shaitan a kuma yi masu balmar baka ko lallaba, har ma ana ganinsu kamar wadanda aka azabtar sabo da bangaskiyarsu, alhali wadanda ya kamata a girmama a kuma karfafa sabo da amincinsu ga Allah, akan bar su su tsaya su kadai, kalkashin zato da rashin amincewa.

Jabun tsarki, da tsarkakewa ta karya suna aikin su na rudi har yanzu. Kalkashin kamani dabam dabam yana nuna ruhu dayan kamar zamanin Luther, kawar da tunanin mutane zuwa bin ra'ayin kansu da kuma yadda suke ji kawai, maimakon yin biyayya ga dokar Allah, daya daga dabarun Shaitan ne na jawo reni ma tsarki da gaskiya.

Da rashin tsoro, Luther ya kare bishara daga hare haren da suka zo daga kowane gefe. Maganar Allah ta nuna kanta makami mai-girma cikin kowace fada. Da wannan maganar ya yaki paparuma, da koyarwar sassauci ta masu-makaranta, yayin da ya tsaya da karfi kamar dutse, ya yaki matsanancin ra'ayi da ya so ya hada kai da Canjin.

Kowane daya daga cikin bangarorin nan masu sabani ya rika sake Littafin ne, yana daukaka mutum a matsayin tushen gaskiya da sani da addini. Addinin Rum da ke cewa wai ruhun paparuma ya sauko masa ne tawurin manzani, kuma ba ya sakewa har abada, yana ba da isashen zarafi ya boye kowane irin almubazzaranci da lalacewa a kalksahin tsarin sakon manzanin. Karfafawar Munzer da abokansa ta fito daga abin da zuciyarsu ta gani ne kawai, kuma tasirin ta ya kaskantar da kowane iko, na mutum da na Allah. Kiristanci na gaskiya yana karban maganar Allah a matsayin babban gidan dukiya na gaskiya da ma'aunin kowane motsuwa ko horuwa.

Da ya dawo daga Watburg, Luther ya kamala juya Sabon Alkawali, ba da jimawa ba kuma aka ba mutanen Jamus bishara cikin harshensu. An karbi wannan juyin da farinciki sosai ga masu kaunar gaskiya; amma wadanda suka zabi al'adun yan Adam da dokokin mutane, suka ki shi da reni ma.

Priestoci suka tsorata, ganin cewa yanzu kowane mutum zai iya yin mahawara ma da su game da maganar Allah, kuma ta haka za a tone jahilcinsu. Makaman tunanin su na mutumtaka sun rasa iko kan takobin Ruhu. Rum ta yi iyakar kokarinta don hana yaduwar Littafi; amma dokoki da tsinewa da azaba duk sun zama banza. Yayin da yake kara karanta Littafni, sai mutane kuma suka kara samun marmarin sanin ainihiin abin da Littafin ke koyarwa. Dukan wadanda sun iya karatu suka yi marmarin karanta maganar Allah don kansu. Sun dinga tafiya ko ina da shi, suna kara karantawa, basu gamsu ba kuwa har sai da suka hadace nassosi da yawa masu tsawo kuma. Ganin farin jinin da Sabon Alkawali ya yi, ya sa Luther nan da nan ya fara juya Tsohon Alakwali yana wallafa shi bangare bangare da zaran ya juya.

An ji dadin rubuce rubucen Luther a birni da kauye. "Abin da da abokan sa suka rubuta, wadansu suka baza. Masu zaman zuhudu da suka gane rashin cancantar takalifansu, suka kuma so sauya doguwar rayuwar kiwuya da rayuwar aiki tukuru, amma kuma ba su da sani da za su iya shelar maganar Allah, suka rika zuwa dukan lardunan, suna ziyartar kauyuka da unguwanni, inda suka sayar da littattafan Luther da abokansa. Nan da nan Jamus ta cika da masu sayarda litattafan nan."

Mawadata da matalauta, masana da jahilai, sun dinga nazarin littattafan nan da marmari sosai. Da dare mallaman makarantun kauyukan sukan karanta su ga kananan kungiyoyi a gefen wuta. Da iyakar, kokari wadansu sukan gane gaskiyar, kuma bayan sun karbi maganar da murna, su kuma sukan fada ma wadansu kyakyawar labarin.

An tabbatar da gaskiyar maganar Allah: “Buden zantattukanka yana ba da haske; yana ba da fahimi ga sahihai.” Zabura 119:130. Nazarin Littafin ya rika kawo babban canji cikin tunani da zukatan mutane. Mulkin paparuma ya rigaya ya aza ma masu binsa karkiya ta karfe da ta daure su cikin jahilci da kankantar girma. An rika bin kamanni da sifa a hankali; amma cikin dukan hidimarsu, ba su yi anfani da zuciya ta tunani kuma ba. Koyaswoyin Luther da suka bayana ainihin gaskiyar maganar Allah, da kuma ita maganar Allahn kanta da aka sa a hannun mutane marasa gata, ya falkas da kwarewarsu, ya tsarkake ya kuma girmama yanayin ruhaniyarsu, wannan kuwa ya ba da karfi da kuzari ga tunaninsu.

An rika ganin mutane kowane iri da Littafin cikin hannuwansu, suna kare koyaswoyin Canjin. ‘Yan paparuma da suka rigaya suka bar nazarin Littafin a hannun priestoci da ‘yan zaman zuhudu, yanzu kuwa suka fara kiran su priestocin su zo su karyata sabobin koyaswoyin. Amma da shike priestocin basu san maganar Allah ba, wadanda an rigaya an ce da su jahilai masu ridda suka ka da priestoci. Wani marubucin Katolika ya ce: “Abin bakinciki, ya rigaya ya ce ma mutanensa kada su sa bangaskiyarsu ga wani abu dabam da Littafin.” Jama’a sukan taru domin su ji gaskiya daga mutane masu karamin ilimi, har ma suna mahawarar maganar Allahn da masana masu iya magana. Jahilcin mutanen nan ya bayyana sa’an da aka tare hujjojinsu da koyaswoyi masu sauki na maganar Allah. Leburori da sojoji da mata, har da yara ma, suka fi priestoci da likitoci fahimtar koyaswar Littafi.

Bambanci tskanin almajiran bishara da magoya bayan camfin paparuma ya bayana cikin masana da kuma cikin marasa gata. “Sabanin tsofofin jarumawan sarautar, wadanda suka ki koyon harsuna da sanin littattafai, suna kuma koya ma kansu sani mafi inganci na da. Da shike sun mallaki tunani mai-kuzari, da ruhu mai-daukaka, da zukata marasa tsoro, matasan nan suka sami sanin nan da ya dade ba a sami mai-takara da su ba.... Sabo da haka, sa’an da wadannan matasa masu kare Canjin suka sadu da likitocin Rum a kowane taro, sukan fada masu a saukake gabagadi kuma, ta yadda jahilan nan suka ja baya, suka sha kunya, suka kuma fada cikin renin da ya cancance su.”

Sa’an da ma’aikatan Rum suka ga jama’an su suna raguwa, suka bidi taimakon majistarori kuma ta kowace hanya da suka iya bi, suka yi kokarin dawo da masu jinsu. Amma mutanen sun sami abin da ya gamsar da ruhunsu a cikin sabobin koyaswoyin, suka kuwa rabu da wadanda sun dade suna ciyar da su da buntun banza na camfi da al’adun mutane.

Sa’anda aka ta da zalunci kan masu koyar da gaskiyar, sai suka ji maganar Kristi cewa: “Amma sa’anda sun tsanance ku chikin wannan birni, ku gudu zuwa na kusa.” Matta 10 :23. Hasken ya shiga ko ina. Yayin da suke gudu, akan karbe su a wani wuri, nan kuwa sukan yi wa’azin Kristi, wani lokaci cikin majami’a, ko kuma, idan an hana su damar, a cikin gidaje ko a fili ma. Duk wirin da za a iya jin su yakan zama tsarkakakken haikali. Gaskiyar da aka yi shelar ta da karfi da tabbaci kuma hakanan, ta yadu ta yadda ba za a iya ki ba.

A banza aka nemi mahukuntan ekklesiya da na kasa su murkushe riddar. A banza suka yi anfani da kurkuku da azabtarwa da wuta da takobi kuma. Dubban masu bi suka hatimce bangaskiyarsu da jininsu, duk da haka kuma aikin ya ci gaba. Zalunci ya kara fadada gaskiyan ne ma, kuma tsanancin da Shaitan ya so ya hada da zaluncin ya kai ga kara bayana bambanci da ke tsakanin aikin Shaitan da aikin Allah ne.

Babi na II—Yardar ‘Ya’yan Sarkin

Daya daga cikin shaida mafi kyau da aka taba bayarwa game da Canjin ita ce rashin yardar Kirista ‘ya’yan sarki na Jamus da suka nuna a Majalisar Spires a 1529. Karfin hali da bangaskiya da naciyar mutanen Allahn nan ya samo ma sararakin baya yancin tunani da na lamiri. Kin yardar su ya ba ekklesiyar da aka canja din suna masu kin yarda; kaidodinta su ne “ainihin kin yardan.”

Rana mai duhu da barazana ya taho ma Canjin. Duk da dokar Worms din nan, wadda ta ce Luther mai ketare doka ne, ta kuma hana koyarwa ko yarda da koyaswarsa, yancin addini har yanzu ya ci gaba a kasar. Ikon Allah ya tsayar da ikokin da suka yi jayayya da gaskiyar. Charles V ya nace wai sai an murkushe Canjin, amma kullum ya daga hannunsa, akan tilasta shi ya fasa kai bugun. Akai akai kusantuwar hallakawar dukan wadanda suka yi jayayya da Rum ta dinga bayanuwa; amma daidai lokacin, mayakan Turkawa sukan bayana ta gabas, ko kuma sarkin Faransa, ko paparuma kansa, cike da kishi sabo da karuwan da girmar babban sarkin ke yi, ya yi yaki da shi; sabo da haka yayin da ake fama da tashe tashen hankulan al’ummai, an bar Canjin ya yi karfi, ya kuma yadu.

Amma a karshe dai, shugabannin ‘yan paparuma sun rage fadace fadacensu, domin su hada hannu su fuskanci ‘yan canjin. Majalisar Spires a 1526 ta ba kowace jiha cikakken yanci game da harkokin addini har sai gamayyar majalisun ta yi zaman ta; amma da zaran damuwar da ta sa aka ba da ‘yancin nan ta wuce, babban sarkin ya kira taron Majalisa na biyu a Sires a 1529 da manufar murkushe ridda. Aka shirya lallabar ‘ya’yan sarki, cikin salama, in ya yiwu, domin su yi jayayya da Canjin; amma idan hakan bai yiwu ba, Charles ya shirya zai yi anfani da takobi.

‘Yan paparuma fa sun ji dadin wannan. Suka taru a Spires da yawansu, a fili kuma suka bayana kiyayarsu ga yan Canjin da masu goyon bayansu. Melanchthon ya ce: “Mu ne tarkace da karmomin duniya; amma Kristi za Ya dubi mutanensa, zai kuma kiyaye su.” Aka hana ‘ya’yan sarki da suka halarci Majalisar baza bishara har a masaukinsu ma. Amma mutanen Spires sun ji kishin maganar Allah, kuma duk da hanawar, dubbai sun halarci taronni da aka rika yi a majami’ar mai-zaben Saxony.

Wannan ya zaburar da hargitsin. Aka sanar da Majalisar cewa da shike kudurin da ya ba da yancin lamiri ya haifar da hargitsi mai-yawa, babban sarki ya bukaci cewa a soke shi. Wannan abu ya ta da fushin Kirista masu baza bishara. Wanin su ya ce: “Kristi Ya sake faduwa cikin hannun Kayafa da Bilatus kuma.” Yan ekklesiyar Rum fa suka kara nuna fin karfi. Waninsu mai matsanancin ra’ayi ya ce: “Turkawa sun fi Luthawa, domin Turkawa suna kiyaye ranakun azumi, Luthawa kuma suna ketare ranakun. Idan ya zama dole mu zaba tsakanin Littafin da kurkuran ekklesiya, ya kamata mu ki Littafin.” Melanchthon ya ce: “Kowace rana a taron dukan Majalisa, Faber yakan jefa sabon dutse a kan masu shelar bishara.”

An kafa yancin addini bisa ga doka, jihohi masu baza bishara kuma sun dauki kudurin yin jayayya da ketarewar hakkokin su.luther, da shike har yanzu dai yana kalkashin takunkumin dokar Worms, baa barshi ya kasance a Spires ba; amma abokan famar sa sun cika gibin, gama Allah Ya shirya su domin su kare aikin Sa a wannan mawuyacin lokacin. Mmai-halin kirkin nan Fredrick na Saxony,wanda ya kare Luther a da, ya rigaya ya rasu; amma kanin sa John,wanda ya gaje shi, ya marabci Canjin da farin ciki,kuma ko da shike mai-son salama ne shi, ya nuna karfi da rashin tsoro kuma sosai game da duk ani day a shafi bangaskiyar.

Priestoci suka bukaci jihohin da suka karbi Canjin su amince da mulkin Rum kawai. Yan Canji kuwa suka rike yancin da aka rigaya aka bayar. Basu yarda cewa Rum ta sake jawo jihhin nana da suka karbi maganar Allah kalkashin ikon tq akuma ba.

Domin sasantawa, aka bad a shawara cewa inda yan Canjin basu rigaya sun kafu sosai ba, sai a aiwatar da dokar Worms da karfi, kuma “a wuraren da mutanen sun kauce ma canjin, da inda ba za su iyabin sa ba tare da tashin hankali ba, a takaice dai kada a yi sabon canji, kada su taba wani batu da ake musu akai , kada su kushe bukin mass, kada su yarda wani dan roman Katolika ya rungumi Luteranci.” Majalisar ta amince da wannan, priestocin paparuma kuwa suka gamsu.

Da an aiwatar da dokan nan “dab a iya fadada Canjin ba...inda ba a san shi ba tukuna, ko kumama a kafa shi kan harsashe mai-karfi, inda da ma akwai shi.” Da an hana yancin magana kenan. Da ba a yarda da tuba ba. Wadannan takunkumi da dokokin ne fa aka so abokan Canjin su amince da su nan take.begen duniya ya nuna alamar bicewa. “Sake kafawar mulkin Rum...da ya dawo da cin mutunci irin na da;” kuma da an sami dammar kamala rushewar aikin da an rigaya an girgiza shi sosai ta wurin matsanancin ra’ai da sabani.

Sa’an da masu bisharan suka taru don yin shawarwari, sun rika kallon juna da mamaki. Suka rika tambayan juna: “Me za mu yi?” manyan al’amuran da suka shafi duniya ne sun taso. Ko shugabannin Canjin za su mika wuya su karbi dokar? Yana da sauki a wanan babban hargitsin a iske cewa yan Canjin sun yi ta musu har suka daukikuduri na kuskure! Akwai kyawawan hujjoji da yawa da za su iya bayarwa donmika wuyar. An ba Lutherawa da ke yayan sarki yancin sun a addini. Aka mika kyauta dayan ga dukan mabiyan su wadanda kafin a yi dokar, sun rigaya sun karbi koyaswar Canjin. Ko bai kamata wannan ya ishe su ba? Ina yawan matsalolin da mika wuya zai hana! Ina yawan kasada da hargitsi da jayayya za ta jefa su ciki! Wa ya san zarfin da za a samu nan gaba? Bari mu rungumi salama; bari mu karbi tayin salama da Rum ke mika mana, mu kuwa rufe raunukan Jamus. Da irin ra’ayoyin nan ne yan Canjin suke iya anfani da su a matsayin hujjojin daukan matakin da lallai day a kai ga rushewar aikin su.

“Abin farin ciki, suka dubi kaidar da aka kafa wannan tsari akai, suka kuma aikata cikin bangaskiya. Mene ne kaidar? ‘Yancin Rum ne ta tilasta lamiri, ta kuma hana ‘yancin bincike. Amma ko bai kamata su kan su da masu binsu ‘yan kin yarda su mori ‘yancin addini ba?” I kam, amma a matsayin lheri, bisa ga shirin kawai, amma ba ‘yanci ba. Sauran wadanda ba a ambata cikin shirin ba, ikon nan dai zai ci gaba da mulki kansu; babu zancen lamiri a kotu; Rum ce mai-sharia mara kuskure, kuma dole a yi mata biyayya. Da an amince da shirin, da ya zama an amince kenan cewa ‘yancin addini zai kasance a Saxony ne kadai; ga sauran Kirista kuma ‘yancin bincike da amincewa da sabuwar bangaskiya, da sun zama laifuka kenan, hukumcinsu kuwa kurkuku da kisa. Su za su yarda a kange yancin addini a wuri daya? a yi shela cewa kada wani ya sake amincewa da Canjin? cewa duk inda Rum ke iko yanzu ya zama nata har abada? Da ‘yan Canjin za su iya cewa ba su da laifi akan jinin dubban mutane wadanda sabo da wannan shirin da sun rasa rayukansu a hannun paparuma? Wannan da ya zama cin amanar aikin bishara da ‘yancin Kirista a wannan lokaci na musamman. Maimakon wannan suka gwammaci “sadakar da komi har jihohinsu ma, da rawaninsu, da rayukansu.”

Yayan sarkin suka ce: “Mun ki wannan dokar. A sha’anin lamiri, masu rinjaye ba su da iko.” Wakilai suka ce: “Sabo da dokar 1526 ne kasar take morar zaman salama: soke shi zai cika Jamus da wahaloli da tsatsaguwa. Majalisar ba za ta iya yin komi ba sai dai ta kiyaye yancin addini, har sai babban majalisa ta yi zama.” Tsaron yancin addini aikin gwamanti ne, kuma iyakan ikon ta kenan game da sha’anin addini. Duk wani gwamnati da ya yi kokarin takurawa ko tabbatar da kiyaye addini ta wurin ikon ta, yana sadakar da kaidar da Krista masu baza bishara suka yi fama akai ke nan.

‘Yan paparuman sun shirya danne abin da suka kira “Karin hali na taurin kai.” Sun fara da kokarin ta da rarrabuwa tsakanin magoya bayan Canjin ne, su kuma razana dukan wadanda suka goyi bayansu a fili. Wakilan yantattun jihohin suka gurbana a gaban Majalisar domin su amsa ko za su amince da sharuddan abin da ake niyyar yi. Suka nemi a ba su lokaci, amma a banza. Sa’anda aka gana da su, kusan rabinsu suka goyi bayan ‘yan Canjin. Wadanda suka ki sadakar da ‘yancin addini da ‘yancin zabi sun san wannan matakin ware su kenan don zargi da hukumci da zalunci nan gaba. Wani wakili ya ce: “Dole mu ki maganar Allah ko kuma a kone mu.”

Sarki Ferdinand, wakilin babban sarkin kenan a Majalisar, ya ga cewa dokar za ta kawo rarrabbuwa soai, sai dai in sun lallashi ‘ya’yan sarkin suka amince da shi. Sabo da haka, ya gwada lallashi, ganin cewa gwada ma irin mutanen nan karfi zai kara taurara su ne kakwai. Ya “roki ‘ya’yan sarkin su amince da dokar, yana tabbatar masu cewa baban sarkin zai ji dadinsu sosai.” Amma amintattun nan sun yarda da ikon da ya fi na shugabannin duniya, suka kuma amsa a natse cewa: “Za mu yi biyayya da babban sarkin cikin komi da zai kara kawo salama da daukakar Allah.”

A gaban majalisar, sarkin a karshe ya sanar ma mai-zaben da abokansa cewa dokar, “ba da jimawa ba za a zana ta a matsayin dokar babban sarki,” kuma cewa “abin da ya rage masu kawai shi ne su goyi bayan masu rinjaye.” Bayan wannan magnar sai ya fita daga wurin taron, bai ba ‘yan Canjin dammar shawara ko ba da amsa ba. “A banza suka aika a roki sarkin ya dawo.” Amsar da ya bayar it ace: “An gama da zancen nan; amincewa kadai ya rage.”

Mutanen babban sarkin sun tabbatar cewa ‘ya’yan sarkin, Kiristan nan, za su manne ma Littafin, cewa ya fi koyaswoyin mutane da dokokinsu; kuma sun san cewa duk inda aka yarda da wannan kaidar, a karshe za a hambarar da tsarin paparuma. Amma kamar dubbai tun zamaninsu, “suka dubi ababan da ake gani kadai,” suka rudi kansu cewa manufar babban sarki da paparuma tana da karfi, na ‘yan Canji kuma ba ta da karfi. Da ‘yan Canjin sun dogara ga taimakon mutane ne kadai fa da sun zama marasa karfi, kamar yadda ‘yan paparuma suka dauka. Amma ko da shike ba su da yawa, kuma suna sabani da paparuma, sun kasance da karfinsu. Suka daukaka kara “daga rahotun Majalisar zuwa ga maganar Allah, kuma daga babban sarki Charles zuwa wurin Yesu Kristi, Sarkin sarakuna da Ubangijin iyayen giji.”

Da shike Ferdinand ya ki kula abababn da lamirinsu ya amince da su, ‘ya’yan sarkin suka ki kulawa da tayinsa, amma suka kai kin amincewarsu gaban Majalisar kasa baki daya ba tare da jinkiri ba. Sabo da haka aka zana wani bayani aka gabatar ma Majalisar, cewa:

“Mun nuna kin yarda, ta wurin rubutun nan, gaban Allah, Mahalicinmu, Makadaici, Mai-kiyayewa, Mai-ceto kuma, wanda kuma wata rana zai zama Mai-sahr’anta mu, da kuma gaban dukan mutane da dukan halita, cewa mu, domin mu kan mu da domin mutanenmu, bamu yarda ba, ba ma kuma kiyaye ta kowace hanya, dokar da ake so a kafa ba, cikin duk wani abin da ya saba ma Allah da maganarsa mai-tsarki, da lamirinmu da ceton rayukanmu.”

“Mene! Mu amince da dokar! Muna furta cewa Allah Madaukakai yana kira ga mutum ya san Shi, duk da haka kuma mutumin nan ba zai iya sanin Allah ba!” “Ba wata tabbataciyar koyaswa sai wadda ta je daidai da maganar Allah.... Ubangiji Ya hana koyar da wata koyaswa dabam.... Wani nassi na Littafi ne yakan fassara wani.... Wannan littafin, game da duk abin da Kirista ke bukata, yana da saukin ganewa, kuma an shirya shi domin watsar da duhu. Mu mun kudurta, da alherin Allah, za mu ci gaba da wa’azin maganarsa mai-tsarki kamar yadda take a cikin littattafai na Tsoho da Sabon Alkawali, ba tare da kara wani abu akai da zai saba masa ba. Wannan maganar ce gaskiya kadai, it ace tabbataciyar magwajin dukan koyaswa da na dukan rayuwa, kuma ba za ta taba kasawa ko kuma ta rude mu ba. Wanda ya yi gini a kan wannan harsashe zai tsaya ya yi tsayayya da dukan ikokin lahira, yayin da dukan ababan banza na mutumyaka da aka shirya masa za su fadi a gaban fuskar Allah.”

“Sabo da haka, mun ki karkiyar da aka tilasta a kanmu.” “A lokaci dayan kuma muna da tsammanin cewa mai-martaba babban sarki zai bi da mu, kamar yariman Kirista wanda ke kaunar Allah fiye da kowane abu, mun kuma bayana kanmu a shirye mu yi masa, da ya ku iyayengiji ma duka, soyayya da biyayya da suka cancanta.”

Majalisar ta sami ganewa sosai. Yawancinsu suka cika da mamaki game da karfin halin masu kin dokar. Gaba ya zama masu da kamanin hargitsi da rashin tabbaci. Suka ga kamar dole kawai tsatsaguwa da hargitsi da zub da jini za su faru. Amma ‘yan Canjin, da shike sun tabbatar cewa suna da gaskiya, sun kuma dogara ga Mai-cikakken iko, suka “cika da karfin hali da naciya.”

“Kaidodin da wannan kin yarda ya kunsa... su ne ainihin Kin yarda da ikon paparuma. Kin yardan nan yana jayayya da cin mutunci kashi biyu ne, game da sha’anin addini: na farko shi ne shisshigin majistare, na biyu kuma shi ne mulkin kama-karya na ekklesiya. Maimakon wadannan cin mutuncin, Kin yarda ya aza ikon lamiri bisa majistare, ikon maganar Allah kuma bisa ekklesiyar da ake gani. Da farko ma yana kin ikon kasa a cikin ababan ruhaniya, kuma kamar manzani da annabawa, yana cewa: ‘Dole sai mu fi biyayya ga Allah da mutane.’ A gaban renin Charles V, Kin yardan yana daukaka rawanin Yesu Kristi. Amma ya ci gaba: ya tsara kaidar cewa dole kowace koyaswar mutane ta kasance kalkashin hikimar Allah.” Masu Kin yardan sun kuma nanata ‘yancin su na furta abin da suka gaskata. Ba gaskatawa da aikatawa kadai za su yi ba, amma za su koyar da abin da maganar Allah ke koyarwa ma, suka kuma ki ‘yancin preist ko majistare ya sa baki. Kin yardan nan na Spires babbar sahida ce sabanin rashin hakuri na addini, da kuma bayana ra’ayin dukan mutane su yi sujada ga Allah bisa ga lamirinsu.

An rigaya an yi furcin. Aka rubuta shi cikin tunanin dubbai, aka kuma yi rajistansa cikin littattafai na sama, inda duk kokarin mutum ba zai iya share shi ba. Dukan yan bisharan Jamus suka rungumi Kin yardar a matsayin bayyanawar bangaskiyar Jamus. Ko ina mutane suka ga yiwuwar sabon zamani mafi-kyau a cikin wannan furcin. Wani dan sarki ya ce ma masu Kin yarda na Spires: “Bari Madaukaki, wanda Ya ba ka alheri har ka furta da karfi ba takura, kuma ba tsoro, ya kiyaye ka cikin wannan karfin Kiristan, har rana ta har abada.”

Da a ce Canjin, bayan ya fara cin nasara, ya yarda da hada kai da duniya don samun tagomashi a duniya, da ya yi ma Allah da shi canjin kan shi ma rashin aminci, ta haka kuma da ya tabbatar da rushewar shi. Abin da ya faru da ‘yan Canjin nan yana da darasi don dukan sararakin baya. Dabarar Shaitan don aiki sabanin Allah da maganarsa ba ta sake ba; har yanzu ba ya so a Littafi mai-bishewar rayuwa, kamar yadda bai so hakan ba a karni na sha shida. A zamaninmu, an rabu da koyaswoyin Littafin, kuma akwai bukatar komawa ga babban kaidan nan- Littafin da Littafin kadai, a matsayin kaidar imani da kaidar aiki kuma. Shaitan dai yana kan aiki ta kowace hanya don hallaka ‘yancin addini. Ikon antichrist da

masu Kin kaidodin paparuma suka ki yana kokari kwarai yanzu don mayar da fifikon sa da ya rasa. Mannewa da aka yi ga maganar Allah shi ne kadai begen Canjin a yau.

Alamun hatsari suka bayana ga masu aikin gyaran; an kuma ga alamu, cewa Allah Ya mika hannunsa domin Ya ceci amintattu. Wajen wannan lokacin ne "Melanchthon cikin gaggawa ya bi da abokin sa Simon Ggrynaeus ta titunan Spires zuwa kogin Rhine, ya matsa mashi ya ketare tekun. Abokin ya yi mamakin wannan gaggawar. 'Tsohon mutum natsatse, ni kuma ban san shi ba,'" in ji Melanchthon, 'ya bayana gare ni ya ce, Cikin minti daya Ferdinand zai aiki hafsoshin shari'a su zo su kama Grynaeus.'" Grynaeus, a karshe kuma ya yi masa fada wai don ya kare "wadansu kurakurai masu ban kyama." "Faber ya boye fushinsa, amma jima kadan bayan wannan ya je wurin sarkin, wanda ya rigaya ya ba shi oda sabanin shehun mallamin nan na Heideberg, mai-taurin kai. Melanchthon bai yi sahkka ba cewa Allah ne Ya ceci abokinsa ta wurin aiko wani malaika mai-tsarki ya gargade shi.

"Ya tsaya a gabar kogin Rhine, ba motsi har sai da ruwayen kogin suka ceci Grynaeus daga masu tsananta masa. Da ya gan shi a ketaren kogin, Melanchthon ya ce: 'A karshe dai an fizge shi daga mukamukan wadanda ke kishin jinin mara laifi.' Sa'anda ya koma gidansa aka fada ma Melanchthon cewa hafsoshi masu neman Grynaeus sun bincika gidan, sama da kasa." An kudurta habaka Canjin a gaban shugabannin duniya ma. Sarki Ferdinand ya rigaya ya ki sauraron yayan sarki masu bishara; amma za a ba su zarafi su gabatar da maganarsu a gaban babban sarkin tare da manyan kasa da na ekklesiya. Don kwantar da fadace fadacen da suka addabi kasar, Charles V, shekara ta biye, bayan kin yarda na Spires, ya kira taron majalisa a Augsburg, inda ya sanar da niyyarsa ta shugabantar taron da kansa. Can aka kira shugabannin kin yardar.

Manyan hadaruka sun yi ma Canjin barazana; amma magoya bayansa suka bar komi a hannun Allah, suka kuwa yi alkawalin yin aminci ga bisharar. Yan majalisar mai-zaben Saxony suka roke shi kada ya je Majalisar. Suka ce babban sarkin ya so yayan sarkin su je domin ya dana masu tarko ne. "Ko ba sa komi cikin kasada ne mutum ya je ya kulle kansa cikin ganuwar birni tare da magabci mai-iko ba?" Amma wadansu suka ce, "Bari 'ya'yan sarkin su kame kansu cikin karfin zuciya, aikin Allah kuwa ya kubuta ke nan. Allah Mai-aminci ne, ba zai rabu da mu ba," in ji Luther. Mai-zaben ya kama hanya, tare da masu rufe masa baya, zuwa Augsburg. Kowa ya san hatsarukan da ke fuskantarsa, da yawa kuma suka rika tafiya da duhun fuska da damuwar zuciya kuma. Amma Luther wanda ya bi su har Coburg, ya falkas da bangaskiyarsu ta wurin raira wakar da ya rubuta lokacin wannan tafiyar, wadda ke cewa, "Allahn mu Babban Hasumiya ne." Tsoro mai-yawa ya waste, zukata da yawa masu nauyi suka warware sa'anda suka ji wakan nan.

'Ya'yan sarki, 'yan canjin sun rigaya sun kudurta cewa za su shirya ra'ayoyinsu a jere a jere, tare da shaida daga Litafin, domin su gabatar ma Majalisar; aka kuma ba Luther aikin shirya ra'ayoyin, shi da Melanchthon, da abokansu. 'Yan Kin yardan suka karbi furcin nan a matsayin bayanin bangaskiyarsu, suka kuma taru domin rattaba sunayen su

kan takardar. Wannan mawuyacin lokaci ne. ‘Yan Canjin sun so kada a rikitar da maganarsu da zancen siyasa; sun so canjin ya yi tasirin da ya fito daga maganar Allah ne kawai. Sa’an da ‘ya’yan sarki Kirista din suka hallara don sa hannu kan Furcin nasu, Melanchthon ya ce: “Musamman tauhidi, da ya kamata ma’aikatan bishara ne su gabataar da ababan nan; mu kebe manyan kasa tukuna domin sauran al’amuran.” John na Saxony kuwa ya amsa cewa: “Allah Ya kiyaye ka hana ni. Na rigaya na kudurta yin abin da ke daidai, ba tare da damun kai na game da rawani na ba. Ina so in bayana Ubangiji. Hular sarauta ta, da matsayi, ba su da muhumminci gare ni kamr giciyen Yesu Kristi.” Bayan ya yi maganan nan sai ya rubuta sunansa. Wani dan sarkin kuma, sa’an da ya dauki alkalamin, ya ce: “Idan girman Ubangiji na Yesu Kristi yana bukataar wannan, ni ina shirye ... in bar dukiya ta da rai na a baya.” Ya ci gaba da cewa: “gwamma in sallamar da talakawa na da jihohi na, in bar kasar iyayena da sanda a hannu na, da in karbi wata koyaswa dabam da wannan takardar kuduri ta kunsa.” Irin bangaskiya da karfin mutanen Allahn nan kenan.

Lokacin bayanuwa gaban babban sarkin ya zo, Charles V kan kujerar sarautarsa, ga masu zabe da ‘ya’yan sarki sun kewaye shi, ya saurari yan Canji masu kin yarda da paparuman. Aka karanta Kudurinsu. A wannan babbar taron aka bayana gaskiyar bishara sarai sarai, aka kuma bayana kurakuran ekklesiyar paparuma. “Shi ya sa aka kira wannan ranar, rana mafi-girma ta Canjin, kuma daya daga ranaku mafi-daraja a tarihin Kiristanci da na yan Adam.”

Amma shekaru kalilan ne sun wuce, bayan Luther ya tsaya shi kadai a Worms a gaban majalisar kasa. Yanzu a madadin sa ga manyan yaran sarki na kasar, masu tarin iko. An hana Luther zuwa Augsburg, amma ya kasance a wurin, ta wurin maganar sa da addu’arsa. Ya rubuta cewa: “Ina cike da murna ganin cewa na rayu har wannan sa’a, inda aka daukaka Kristi a gaban jama’a ta bakin shahararru, masu shaida, kuma a gaban wannan taro mai daraja.” Ta haka aka cika abin da Littafin ya ce: “Ina kuwa furta shaidunka a gaban sarakuna.” Zabura 119:46.

A zamanin Bulus hakanan ne aka kawo bisharan nan da aka kulle shi sabo da ita a gaban ‘ya’yan sarakuna, da fadawan babban birnin kasar. Sabo da haka a wannan lokaci, wannan abin da babban sarki ya hana wa’azi daga bagadi, an yi shelarsa daga fadar sarkin; abin da mutane da yawa sun ce bai cancanta ko bayi masu ji ba, iyayen kasar suka ji shi. Sarakuna da manyan mutane ne masu sauraro, ‘ya’yan sarakuna masu rawani kuma suka zama masu wa’azin, kuma wa’azin shi ne gaskiya na Allah. “Tun zamanin manzani ba a taba yin wani aikin da ya fi wannan ban girma, ko kudurin bangaskiya da ya fi wannan ban sha’awa ba,” in ji wani marubucin.

Wani bishop, dan tsarin paparuma ya ce: “Duk abin da Luthawan suka fada gaskiya ce; ba za mu iya musunsu ba.” Wani kuma ya tambayi Dr. Eck, “Za ka iya karyata kudurin da mai-zabe da abokansa suka ambata?” Shi kuwa ya amsa: “Da rubuce rubucen manzani

da annabawa kam, babu!, amma da rubuce rubucen ubani da na majalisu kuwa, i !" Mai-tambayan ya ce: "Na gane. Lutherawa a ganin ka suna cikin Littafin, mu kuma muna waje."

Wadansu yayan sarakunan Jamus suka karbi sabuwar gaskiyar. Babban sarkin kan sa ya furta cewa ababan da masu kin paparuman suka rubuta gaskiya ne. Aka juya kudurin zuwa harsuna da yawa, aka kuma baza su ko ina a Turai, kuma miliyoyi cikin sararakin baya sun karbe shi a matsayin shaidan bangaskiyarsu.

Amintattun bayin Allah basu yi aikinsa ne kadai ba. Yayin da mulkoki da ikoki da masu ruhaniya na mugunta suka taru masu, Ubangiji bai kyale mutanensa ba. Da an bude idanunsu da sun ga shaidar kasancewar Allah da taimakonsa kamar yadda aka yi ma wani annabi na da. Sa'an da bawan Elisha ya nuna masa dakarun magabta da suka kewaye su, suka tare duk wata hanyar tsira, annabin ya yi addu'a cewa: "Ya Ubangiji, ina rokonka, ka Bude idanunsa domin shi gani." Sarakuna II, 6:17. Sai ga shi, dutsen ya cika da karusai da dawakin wuta, dakarun sama ke nan da aka aiko domin su tsare mutumin Allah. Hakanan ne malaikun Allah suka tsare masu aikin Canjin nan.

Wata kaidar da Luther ya rike ita ce cewa ba zai dogara ga ikon mutane don taimaka ma Canjin ba, kuma ba za a yi anfani da makamai don kare ta ba. Ya yi murna cewa 'ya'yan sarakunan kasar sun karbi bisharar; amma sa'an da suka shawarta hada kai domin tsaro, ya ce: "Koyaswar bishara, Allah ne kadai zai kare ta.... Allah zai fi sa hannu a madadin aikin idan mutane basu yi ma aikin karambani ba. Kowace shawara da ta hada da siyasa, a ganinsa sanadin tsoro ne ba dalili, da rashin dangana kuma."

Sa'an da manyan magabta ke hada kai don hambarar da sabuwar bangaskiyar, aka kuma fito da dubban makamai domin yin fada da ita, Luther ya rubuta cewa: "Shaitan yana sa fushinsa; shugabannin ekklesiya marasa tsoron Allah suna hada kai; mu kuma ana mana barazanar yaki. A karfafa mutane su yi hamayya sosai a gaban Ubangiji, ta wurin bangaskiya da addu'a, domin magabtanmu, sa'an da Ruhun Allah Ya yi nasara kansu, su nemi salama. Babban bukatar mu addu'a ce; bari mutanen su san cewa yanzu suna bakin kaifin takobi da fushin Shaitan, su kuma yi addu'a."

Kuma bayan lokacin nan, game da zancen hadin bakin nan da 'ya'yan sarakuna suka so a yi, Luther ya ce makamin kadai da za a yi anfani da shi a yakin nan shi ne "takobin Ruhu." Ya rubuta ma mai-zaben Saxony cewa: "Bisa lamirinmu, ba za mu iya amincewa da hadin kai da ake tunanin yi ba. Za mu gwammaci mutuwa sau goma da mu ga bisharar mu ta jawo zubar da digo daya na jini." Namu shi ne mu zama kamar 'ya'yan raguna da ake kaiwa mayanka. Dole a dauki giciyen Kristi. Mai-girma, ka kasance da rashin tsoro. Ta wurin addu'o'inmu za mu yi ababan da suka fi abin da dukan magabtanmu za su yi ta wurin faharyar su. Kada dai hannunka ya zub da jinin yan-uwanka. Idan babban sarkin yana so a kai mu gaban shari'arsa, muna shirye mu bayana. Kai ba za ka iya kare

bangaskiyarmu ba: ya kamata kowa ya ba da gaskiya amma ya san cewa kasada yake dauka."

Daga wurin addu'a a boye karfi ya zo wanda ya jijjiga duniya ta wurin babban Canji. Can fa bayin Allah a natse suka aza sawayensu bisa dutsen alkawuransa. Lokacin jayayyan nan a Augsburg, Luther "bai taba tsallaka rana guda ba, yana addu'a a kalla sa'a guda, kuma sa'o'in da suka fi dadin yin nazari kenan." Daga dakinsa akan ji shi yana bude ma Allah zuciyarsa cikin kalmomi "cike da daukaka, da tsoro da bege kamar yadda mutum yakan yi magana da aboki." Yakan ce: "Na san Kai ne Ubanmu, kuma za ka watsar da masu zaluntar 'ya'yan ka, gama kai kanka ma kana cikin hatsari tare da mu. Dukan al'amarin nan naka ne, kuma bisa ga umurninka ne kadai muka sa hannu a ciki. Don haka, ka tsare mu ya Uba."

Zuwa ga Melanchthon, wanda nauyin taraddadi da tsoro ya danne shi, ya rubuta cewa: "Alheri da salama cikin Kristi - na ce cikin Kristi, kuma ba cikin duniya ba. Amin. Na ki jinin matsanantan damuwa da ke cinye ka. Idan abin da muke yi ba nagari ba ne, ka bar shi; idan nagari ne, don me za mu karyata alkawuran Shi wanda Ya umurce mu mu yi barci ba tsoro?... Kristi ba zai rabu da aikin adalci da gaskiya ba. Yana raye, yana mulki; tsoron me kuwa za mu ji?"

Allah Ya saurari kukan bayinsa. Ya ba 'ya'yan sarakuna alheri da karfin zuciya don rike gaskiyar, sabanin shugabannin duhu na duniyan nan. Ubangiji Ya ce: "Ga shi, ina sanya dutse magabaci na kusurwa zababe, mai-daraja, a cikin Sihiyona: wanda ya ba da gaskiya gare shi kuma ba za ya kumyata ba." Bitrus I, 2:6. Yan Canji masu kin mulkin paparuma sun yi gini a kan Kristi, kuma kofofin lahira basu yi nasara kansu ba.

Babi na 12—Canjin Faransa

Shekarun fada da duhu ne suka biyo bayan Kin yardan nan na Spires da Kudurin nan na Augsburg da suka jawo nasarar Canjin a Jamus. Da shike tsatsaguwa tsakanin magoya bayanta ya raunana ta, magabata kuma suka rika cakunarta, Kin yardar ta fuskanci yiwuwar rushewa kwata kwata. dubbai suka hatimce shaidarsu da jininsu. Yakin basasa ya barke; daya daga cikin shugabannin Kin yardan ne kuwa ya bashe ta; mafiya martaba cikin ‘ya’yan sarakuna yan canji sun fada cikin hannun babban sarkin, aka rika jan su daga gari zuwa gari kamar kamammu. Amma lokacin da babban sarkin ya ga kamar ya yi nasara ne aka ka da shi. Yana gani aka kwace kamammunsa daga hannunsa, aka tilasta shi a karshe dai ya ba da yanci ga koyaswoyin da ya dade yana so ya rushe. Ya rigaya ya kashe kasarsa da rayuwarsa da dukiyarsa ma a kan rushewar ridda. Yanzu kuma ya ga mayakansa suna mutuwa a cikin yaki, dukiyarsa tana karewa, kasashensa da yawa suna fama da tawaye, yayin da ko ina bangaskiyan da ya kasa dannewa tana yaduwa ne. Charles V ya yi ta yaki da Mai-cikakken iko ne. Allah Ya ce: “Bari haske shi kasance,” amma babban sarkin ya so ya sa duhu ya dawama. Shirin shi ya rushe; cikin saurin tsufa kuwa, ga gajiyar yaki mai-tsawo, ya sauka daga sarautar, ya boye kansa cikin gidan masu zaman zuhudu.

A Switzerlaand, kamar Jamus, kwanakin duhu suka abko ma Canjin, yayin da jihohi da yawa suka karbi sabuwar bangaskiyar, wadansu suka manne ma koyaswar Rum. Zaluncin da suka yi ma masu so su karbi gaskiyar ya kawo yakin basasa a karshe. Zwingli da magoya bayansa cikin canji suka mutu a filin Cappel. Oecolampaedius, sa’an da masifun nan suka fi karfinsa, ya mutu nan da nan. Rum ta yi nasara, kuma a wurare da yawa ta kusa ta dawo da dukan ababan da ta yi hasarar su. Amma Shi wanda shawarin Sa tun fil azal ne, bai kyale aikinsa ko mutanensa ba. Hannun shi ya kawo masu kubuta. A wadansu kasashe Ya ta da ma’aikata da za su ci gaba da Canjin.

A Faransa, kafin a ji sunan Luther a matsayin dan Canji, gari ya fara wayewa. Daya daga cikin na farkon kama hasken shi ne tsohon nan Lefevre, mai tarin ilimi sosai, shehun mallami a Jami’ar Paris, amintacen da tsarin paparuma, mai-kwazo kuma. Cikin bincikensa na littattafai na da, hankalin sa ya kai ga Littafin, ya kuwa gabatar da nazarin sa ga dalibansa.

Lefevre mai-yawan sha’awar tsarkaka ne, ya kuma kudurta zai shirya tarihin tsarkaka da masu mutuwa sabo da addininsu, yadda yake cikin labaru na ekklesiya. Aikin nan ya kunshi fama mai-yawa; amma ya rigaya ya yi nisa da shi sosai, sa’an da, ganin cewa zai sami Karin taimako daga Littafi, ya shiga nazarin shi. Nan kuwa ya ga labarum tsarkaka, amma ba irin yadda ake nunawa cikin tsarin Rum ba. Ambaliyar hasken Allah ta kwararo ma tunaninsa. Cikin mamaki da kyama ya juya daga aikin da ya ba kan shi, ya dukufa ga maganar Allah. Nan da nan ya fara koyar da muhimman gaskiyan da ya gano a wurin.

A 1512, kafin Luther ko Zwingli su fara aikin canji, Lefevre ya rubuta cewa: “Allah ne yake ba mu ta wurin bangaskiya, adalcin nan da ke barataswa zuwa rai madawami.” Cikin bimbinin al’ajibin fansa, ya ce: “Dubi girman musayan nan, - an hukumta Mara-laifin, shi mai-laifin kuma an sallame shi; Mai-albarkan Ya dauki la’anar, mai-la’anar kuma ya sami albarka, Rai Ya mutu, matacen kuma ya rayu; Darajan ya nannadu cikin duhu, shi kuma wanda da bai san komi ba sai rudami an suturta shi da daraja.”

Kuma yayin da yake koyar da darajar ceto ta Allah ce Shi kadai, ya kuma ce aikin mutum biyayya ne. Ya ce: “Idan kai memban ekklesiyar Krisri ne, kai memban jikinsa ne; idan kai na jikinsa ne, to kana cike da yanayi na Allahntaka .... Da dai mutane za su gane zarafin nan, da za su yi rayuwar tsabta da tsarki, su kuma ga munin darajar duniyan nan idan aka gwada da darajan nan da ido ba zai iya gani ba.”

Akwai wadansu cikin daliban Lefevre da suka ji kalmominsa da marmari, wadanda kuma da dadewa bayan mutuwarsa suka ci gaba da shelar gaskiyar. William Farel yana daga cikinsu. Iyayensa masu ibada ne, an kuma koya ma shi ya yarda da koyaswoyin ekklesiya da bangaskiya, har ma kamar manzo Bulus, zai iya fadi game da shi kansa cewa: “Bisa ga tarika mafi kunci ta addininmu na yi zaman Ba-farisi.” Ayukan 16:5. Da shike tsayayyen dan ekklesiyar Rum ne, ya rika himmar hallaka dukan masu jayayya da ekklesiyar. “Ni kan rika cizon hakora kamar kerkeci idan na ji wani yana magana sabanin paparuma,” in ji shi. Ba ya gajiya da girmama tsarkaka, tare da Lefevre sukan bi majami’un Paris, suna sujada a haikalin, suna kuma barin kyautuka a bagadin. Amma ayukan nan basu ba shi salama ba. Laifin zunubin shi ya dame shi, kuma dukan ayukansa na neman gafara basu kau da alhakin laifin ba. Ya saurari kalmomin dan Canjin kamar murya daga sama, cewa: “Ceto daga alheri ne.” “An hukumta Mara-laifin, aka sallami mai-laifin.” “Giciyen Kristi ne kadai yake bude kofofin sama, yana kuma rufe kofofin lahira.”

Farel ya karbi gaskiyar da farinciki. Da irin tuban Bulus, ya juya daga bautar al’ada zuwa yancin yayan Allah. “Maimakon zuciyar kisa irin ta mugun kerkeci,” ya ce, na dawo “shuru kamar dan rago mai-tawali’u, mara cetaswa, da zuciya da aka bayas ga Yesu Kristi.”

Yayin da Lefevre ya ci gaba da watsa hasken a cikin dalibansa, Farel, da himma cikin aikin Kristi irin wanda ya nuna cikin aikin paparuma, ya ci gaba da bayana ma jama’a gaskiyar. Ba da jimawa ba, wani babban memban ekklesiyar Rum, bishop na Meaux, ya hada kai da su. Wadansu mallamia, shahararrun masana, suka hada hannu cikin shelar bisharan, ta kuwa sami magoya baya daga dukan bangarori, daga gidajen masu aikin hannu da fakirai, har fadar sarkin. Yar’uwar Francis I, wanda ke sarauta a lokacin, ta karbi sabuwar gaskiyar. Sarki kansa da uwarsa, sun nuna alamar goyon baya, da bege sosai kuma yan Canjin suka dinga begen ranan da Faransa za ta karbi bisharar.

Amma begensu bai cika ba. Kunci da zalunci sun abka ma almajiran nan na Kristi, amma cikin alheri aka boye wannan daga idanunsu. Lokacin salama ya shiga tsakani,

domin su sami karfi su fuskanci guguwar; canji kuma ya ci gaba sosai. Bishop na Meaux ya yi aikii tukuru a diocese dinsa don koya ma limamai da sauran mutane. Aka sauke jahilan priestoci da fasikan cikinsu, aka kuma sauya su da masu illimi da ibada. Bishop din ya so mutanensa su sami maganar Allah don kansu, hakan kuwa ya samu nan da nan. Lefevre ya shiga juya Sabon Alkawali zuwa Farasanci a Meaux. Bishop din bai yi kiwuya ba , ya kuma kashe kurdi don baza shi cikin kowane parish dinsa, jima kadan kuwa talakawan Meaux suka mallaki Littafin.

Kamar yadda matafiya da ke mutuwa da kishirwa sukan marabci mabulbular ruwa da murna, hakanan mutanen nan suka karbi sakon sama. Leburori da masu aikin hannu suka rika rage gajiyar aiki ta wurin tattaunawa game da gaskiyar Littafin. Da yamma, maimakon komawa wurin aiki, sukan taru a gidajen juna don karanta maganar Allah da kuma addu'a da yabo. Nan da nan aka ga babban canji cikin mutanen nan. Ko da shike talakawa ne su, marasa ilimi, masu zafin aiki , ikon alherin Allah mai-kawo canji da girmamawa ya bayana a rayuwarsu. Cikin tawali'u da kauna da tsarki, suka kasance shaidun abin da bishara za ta yi ma wadanda suka karbe ta da gaske.

Hasken da aka kunna a Meaux ya kai tsirkiyoyin sa da nisa. Kowace rana yawan masu tuba ya dinga karuwa. Sarkin ya dakatar da fushin ekklesiyar, ya rena rashin sassaucin masu zaman zuhudun; amma daga baya shugabannin yan paparuman suka yi nasara. Sai aka kafa wurin kisan. Bishop na Meaux da aka tilasata masa zabi tsakanin wuta da janyewa, sai ya zabi hanyar saukin; amma duk da faduwar shugaban, garkensa suka tsaya da karfi. Da yawa suka shaida gaskiyar a cikin wutan. Ta wurin karfin zuciyarsu da amincinsu, har mutuwa Kiristan nan suka yi ma dubbai magana, wadanda kuwa a lokacin salama basu taba jin shaidarsu ba.

Ba masu tawali'u da matalauta ne kadai suka shaida Kristi cikin wahala da reni ba. A dakunan taro na manyan gidaje da na fada, akwai masu sarauta da suka san anfanin gaskiya fiye da wadata ko matsayi ko rai kansa ma. Sulken sarauta ya boye ruhu mafi daraja fiye da yadda rigar priest da hularsa suka yi. Louis de Berquin haifaffen dan sarauta ne. Ba-fade ne mai-karfin zuciya da ya dukufa cikin nazari, mai halayyan kirki ne kuma mara kazanta ko halin fasikanci. Wani marubuci ya ce: "Shi babban mai-bin kundin tsarin dokokin paparuma ne, babban mai sauraron mass da wa'azu;... ya kuma kalmasa dukan halayyansa ta wurin kiyayya ta musamman da yake yi ma tsarin Luthanci." Amma kamar wadansu da yawa kuma, Allah Ya bishe shi zuwa Littafin, ya yi mamaki da ya ga a ciki, ba koyaswoyin Rum ba, amma koyaswoyin Luther." Daga nan sai ya mika kan sa da cikakkiyar dukufa ga aikin bishara.

Babban masani cikin fadawan Faransa, hikimarsa, da kaifin harshensa, karfin zuciyarsa da himar jaruntakansa, da kuma tasirinsa a fada — gama yana da farin jini a gaban sarkin — sun sa mutane da yawa suka dauka cewa shi ne zai zama dan Canjin kasarsa. Beza ya ce: "Da Berquin ya zama Luther na biyu, in da Francis I ya zama masa

mai-zabe na biyu.” Yan paparuma suka ce: “Ya fi Luther muni.” Masu bin Rum a Faransa sun fi jin tsoron sa kam. Suka jefa shi a kurkuku cewa shi mai ridda ne, amma sarkin ya fitar da shi. An yi shekaru ana ci gaba da jayayyar. Francis, da ya rika canjawa tsakanin Rum da Canjin, wani lokaci yakan kyale zazzafan ra’ayin masu zaman zuhudu, wani lokaci kuma ya hana. Sau uku mahukuntan ‘yan paparuma suka sa Berquin a kurkuku, sarkin kuma yana cire shi, kuma domin yana sha’awar hikimarsa, ya ki ya sadakar da shi ga kiyayyar ekklesiya.

An dinga yi ma Berquin kashedi akai akai game da hatsarin da ke kansa a Faransa, aka kuma shawarce shi ya bi sawun wadanda suka yi gudun hijira don kansu. Matsoracin nan Erasmus, wanda duk da yawan ilimin sa, ya kasa samun kyaun halin nan da kan daukaka gaskiya fiye da rai, da girma, ya rubuta ma Berquin cewa: “Ka roka a sa ka zama jakada a wata kasar waje; je ka yi tafiya a Jamus. Ka san Beda da irinsa, dodo ne shi mai kawuna dubu, yana fesa dafi kowane gefe. Sunan magabtan ka tuli. Ko aikin ka ya fi na Yesu Kristi, ba za su bari ka tafi ba, har sai sun hallaka ka a wulakance. Kada ka dogara sosai ga tsaron sarkin. Duk yadda aka yi, kada ka raunana ni da tunani na tauhidi.”

Amma sa’an da hatsaruka suka karu, himmar Berquin ta kara karfi ne. Maimakon yarda da shawarar Erasmus, ya shirya matakai mafi karfi ne. Ba kare gaskiya kadai zai yi ba, zai kuma tinkari kuskure. Zargin ridda da ‘yan Rum suka so su manna masa, shi ne zai juya a kansu. Abokan hamayyansa mafi kwazo da daci su ne likitocin nan da ‘yan zuhudu na sashen tauhidi a jami’ar Paris, daya daga shugabanni mafi girma na elkklesiya a birnin da kuma kasar. Daga rubuce rubucen likitocin nan Berquin ya samo ababa goma sha biyu da ya shaida a fili cewa sun “saba ma Littafin, kuma ridda ne;” ya kuma roki sari ya zama mai yanka hukmcin.

Sarkin da shike bai so ya nuna bamabncin karfin jarumawa biyu din ba, kuma yana murnar samun zarafin kaskantar da girman ran masu zaman zuhudun nan, ya bukaci Rum din su kare kansu ta wurin Littafin. Sun san sarai cewa wannan makamin ba zai haifar da komi ba; fursuna da zalunci da konewa ne makaman da suka iya anfani da su. Yanzu ga shi an juya kaidar, suka ga kansu gaf da faduwa cikin ramin da suka so su tura Berquin ciki. Cikin rudewa suka dinga neman mafita.

“Daidai wannan lokacin aka guguntule siffar Budurwa Maryamu a lungun wani titi.” Hankula suka tashi sosai a birnin. Jama’a suka yi ta tururuwa zuwa wurin, suna nuna bakin ciki da fushi. Sarkin ma ya damu sosai. Wannan al’amari ne da yan zuhudun za su iya mai da shi abin anfani, suka kuwa yi hakanan. Suka ce: “Sakamakon koyaswoyin kenan. Yanzu za a hambarar da komi — addini, dokoki, gadon sarauta kansa — ta wurin wanan hadin baki na Luthawa.”

Aka sake kama Berquin kuma. Sarkin ya janye daga Paris, aka kuwa bar masu zuhudun su yi abin da suka ga dama. Aka shar’anta dan Canjin, aka kuma hukunta cewa

za a kashe shi, kuma domin kada Francis ya shiga tsakani ya cece shi, aka aiwatar da hukumcin kisan ranan da aka sanar da shi. Da tsakar rana aka kai Berquin wurin mutuwarsa. Jama'a da yawa suka taru domin su kalli al'amarin, da yawa kuwa suka kalla cikin mamaki da tsoro, ganin cewa mutumin nan daga iyalai mafi nagarta, mafi karfin zuciya na Faransa, aka zabe shi. Mamaki da haushi da reni da kiyayya mai-daci suka cika fuskokin jama'an nan; amma fuska guda daya ba ta nuna damuwa ba. Tunanin Berquin ba ya wurin wannan hayaniyar; ya san da kasancewar Ubangijinsa ne kawai.

Bai damu da akwalar karusar da aka dauke shi ciki ba, ko fuskokin azalumansa, ko mumunan mutuwar da zai yi; shi wanda ke raye, kuma Ya mutu, kuma yana raye har abada, kuma yana da mabudai na mutuwa da na lahira, yana tare da shi. Fuskar Berquin ta haskaka da haske da salamar sama. Ya rigaya ya sa sutura masu kyau sosai. Zai shaida bangaskiyarsa a gaban Sarkin sarakuna da shaidu daga dukan halitta, kuma bai kamata wata alamar bakin ciki ta bata farin cikinsa ba.

Yayin da ake tafiya da shi ta titunan garin, mutane sun yi mamaki, ganin salama da murnan nasara da ke fuskarsa. Suka ce: "Ya yi kama da wanda ke zaune a haikali, yana tsakanci game da ababa masu tsarki."

A wurin kisan nasa, Berquuin ya yi kokarin yi ma mutane jawabi; amma masu zuhudun, sabo da tsoron sakamakon, suka fara ihu, sojoji kuma suna tafa makamansu, har surutunsu ya rufe muryar Berquin. Ta haka, a 1529, babban jigo, na ekklesiya da kuma littattafai na Paris, "ya kafa kwatanci ma mutanen 1793 na murkushe maganar wadanda ke bakin mutuwa a dakali."

An murde wuyan Berquin ne, sa'an nan aka kona gawarsa. Labarin mutuwarsa ya jawo bakin ciki ga abokan Canjin ko ina a Faransa. Amma kwatancinsa bai bata ba. Shaidun gaskiyan suka ce: "Mu ma muna shirye mu gamu da mutuwa cikin farin ciki, muna kafa idanunmu kan rai da ke zuwa."

Lokacin zaluncin Meaux, an hana mallaman sabuwar bangaskiyar lasin na yin wa'azi, suka kuwa koma wadansu wurare. Daga baya Lefever ya je Jamus. Farel ya koma kasarsa a gabashin Faransa don baza hasken a kasan da ya girma. Lokacin an rigaya an sami labarin abin da ke faruwa a Meaux, kuma gaskiyan da ya koyar da himma, ba tsoro, ta sami masu sauraro. Nan da nan shugabanni suka taso za su rufe masa baki, aka kore shi daga birnin. Ko da shike bai iya ci gaba da aikin a fili ba, ya shiga kauyuka yana koyarwa a gidajen mutane da filaye na gonaki, yana kwana kuma a dazuka ko kogunan duwatsu inda ya rika zuwa lokacin kuruciyarsa. Allah yan shirya shi don manyan jarabobi ne. Ya ce: "Giciye ad zalunci da kullekullen Shaitan da aka gargade ni akai sun faru; suna da zafi ma fiye da yadda ni kai na zan iya jimrewa; amma Allah Uba na ne; Ya tanada, kuma kullum zai rika tanada mani karfin da ni ke bukata."

Kamar zamanin manzanin, zalunci “ya kara ci gaban bishara ne.” Filibbiyawa 1:12. Da aka kore su daga Paris da Meaux, “Su fa da suka waste suka yi tafiya ko ina, suna wa’azin Kalmar.” Ayukan 8:4. Haka ne kuma hasken ya shiga laarduna da dama na Faransa.

Allah Yana kan shirya ma’aikata dai don fadada aikinsa. A wata makaranta a Paris, an yi wani saurayi mai basira da ladabi, wanda ke da alamar zama mai-zurfin tunani, ga kuma halin kirki da ilimi da ibada. Madaukakiyar iyawarsa da aikinsa sun ba shi farin jini a kolejin, aka kuma kau da shakka cewa John Calvin zai zama daya daga cikin mafi kwarewa da daukaka na masu kare ekklesiya. Amma tsirkiyar hasken Allah ta huda yawan ilimi da camfi da aka kange Calvin a ciki. Ya ji labarin sabuwar koyaswar da fargaba, ba tare da shakkar cewa wutar da aka ba masu riddar ta cancance su ba. Duk da haka, babu shiri aka kawo shi fuska da fuska da riddar, aka kuma tilasta shi ya gwada karfin tauhidin Rum don karawa da koyaswar masu Kin ikon paparuma.

Wani dan-uwan Calvin da ya zama dan Canjin, yana Paris. Shi da Calvin sukan rika tattauna al’amuran da ke damun addinin Kirista. Olivetan dan Canjin ya ce: “Akwai addinai biyu a duniya. Kashi na daya shi ne wadanda mutane suka kirkiro, kuma cikinsu duka, mutum ne yakan ceci kan sa ta wurin al’adu da kyawawan ayuka; na biyu din shi ne addinin nan daya da Littafi ya bayana, wanda ke koya ma mutum ya nemi ceto ta wurin alherin Allah kadai kyauta.”

Calvin ya amsa: “Ba na son sabobin koyaswoyin nan naka; kana tsammani duk rayuwa ta ina kuskure ne? Amma an ba shi tunani a zuciyarsa wanda bai iya watsarwa da sauki ba. A dakinsa, ya yi bimbini game da kalmomin dan-uwan nasa. Jin laifin zunubinsa ya rike shi sosai, ya ji kan shi, ba shi da matsakanci, a gaban Mai-shar’ia Mai-tsarki. Tsakanin tsarkaka da ayukan nagarta da al’adun ekklesiya duka ba su da ikon yin kafara don zunubi. Bai ga komi a gabansa ba sai duhun yakan kauna. A banza masanan ekklesiya suka yi kokarin magance damuwarsa. Furta zunubi da wahal da kai don samun gafara, duk basu biya bukata ba; basu sasanta mutum da Allah ba.”

Yayin da yake ci gaba da famar banzan nan, ya ziyarci wani dandali, sai ya tarar ana kone wani mai ridda. Ya cika da mamakin salamar day a gani a fuskar mutumin. Cikin azabar mumunan mutuwan nan, kuma kalkashin hukumcin eklesiya, mutumin ya nuna bangaskiya da karfin zuciya da dalibin nan Clavin ya bambanta da nashi fid da zuciya da kuma duhun nan, alhali yana rayuwar cikakkiyar biyayya ga ekklesiya. Ya san cewa masu riddan nan sun kafa bangaskiya kan Littafin ne. Ya kudurta zai yi nazarinsa don gano asirin farin cikinsu.

Cikin Littafi, ya sami Kristi. Ya ce: “Ya Uba, hadayarsa ta gamsar da fushin Ka; jininsa ya wanke dauda ta; Giciyensa ya dauki la’ana ta; mutuwarsa ta yi kafara domi na. Mun shirya ma kanmu wauta da yawa marasa anfani, amma kai ka sa maganar aka a gaba

na kamar fitilla, kai kuma ka taba zuciya ta, domin in yi kyamar kowane abu, sai dai cancantar Yesu."

Ilimin da Calvin ya samu na zama priest ne. Yana dan shekara goma sha biyu kadai aka sa ya zama mai lura da wata karamar ekklesiya, kuma bishop ya aske kansa bisa ga kaidar ekklesiya. Ba a shafe shi ba, kuma bai rigaya ya cika sharuddan priestanci ba, amma ya zama limami shi ma, ana kiransa da sunan aikinsa, yana kuma karban alawas don aikin.

Yanzu, da shike ya ga cewa ba zai taba zama priest ba, sai ya shiga makarantar aikin lauya, amma ya watsar kuma, ya kallafa ransa ga bishara. Amma kuma bai so ya zama mai koyar ma jama'a ba. Shi asalinsa mai kunya ne, ya kuma damu da nauyin aikin, ya so ya dukufa ga nazari. Rokon abokansa daga bisani dai ya sa shi ya yarda. Ya ce: "Abin mamaki ne a girmama dan talaka haka da irin wannan martabar."

Calvin ya shiga aikinsa shuru, kalmominsa kuma kamar raba ce mai fadowa don mayar ma kasa da karfinta. Ya bar Paris, sai ya koma wani gari a wani lardi da ke kalkashin gimbiya Margaret, wadda sabo da kaunar bishara ta fadada tsaron ta zuwa ga almajiran bisharar. Calvin dai matashi ne a lokacin, mai ladabi da gaskiya kuma. Ya fara aikin sa da mutanen a gidajensu ne. Sa'an da mutanen gidan suka kewaye shi, yakan karanta masu Littafi ya bude masu gaskiyar ceto. Wadanda suka ji sakon sukan kai ma wadansu kyakyawar labarin, ba da jimawaba kuwa mai koyaswar ya zarce birnin, ya kai kauyuka da garuruwan da ke kewaye. Ya shiga manyan gidaje da kanana, ya kuma ci gaba yana kafa harsashen ekklesiyoyi da za su haifar da shaidun gaskiyar.

Bayan watanni kadan, ya sake zuwa Paris. An rika samun damuwa tsakanin masana. Nazarin harsuna na dai ya kai mutane ga Littafin, kuma da yawa wadanda gaskiyar ta ba ta taba su ba, yanzu kuwa suka fara tattauna su, har ma suna mahawara da jarumawan tsarin Rum. Ko da shike Calvin kwararren mai mahawara ne a fagen tauhidi, yana da manufar da ta fi mallaman makarantan nan masu surutu. An rigaya an motsa zukatan mutane, yanzu kuma lokaci ya yi da za a bude masu gaskiyar. Yayin da manyan dakunan taruwar jami'o'in su ke cika da hayanniyar mahawarar tauhidi, Calvin yana zuwa gida gida yana koya ma mutane Littafin, yana kuma yi masu magana game da Kristi giciyayye.

Cikin alherin Allah, Paris ta sake samun bishara. An rigaya an ki sakon Lefevre da Farel, amma dukan sassan mutanen babban birnin sun sake jin sakon. Sarkin, sabo da dalilai na siyasa, bai rigaya ya goyi bayan Rum gaba daya sabanin Canjin ba. Margaret ta ci gaba da begen cewa Kin ikon paparuma zai sami ci gaba a Faransa. Ta kudurta cewa za a yi wa'azin sabuwar bangaskiyar a Paris. Lokacin da sarkin ba ya gari, ta umurci wani limami mai-kin ikon paparuma ya yi wa'azi a birnin. Da shike shugabannin 'yan paparuma sun hana yin hakan, gimbiyar ta bude fada domin yin wa'azin. Aka shirya wani gefe ya zama wurin karantarwar, aka kuma sanar da cewa kowace rana, daidai wani lokaaci, za a yi wa'azi, kuma an gayyaci dukan mutane su hallarta. Ba dakin karantarwar kadai ba, har

da sauran dakunan kewaye suka rika cika. Kowace rana dubbai sun rika taruwa: fadawa da manyan kasa, da lauyoyi da attajirai, da masu aikin hannu. Maimakon sarkin ya hana taruwar, sai ya umurta aka bude majami'u biyu na Paris. Birnin bai taba motsuwa da maganar Allah hakanan ba. Kamar ruhun rai daga sama ne aka hura ma mutanen. Kamewa, tsabta, oda da kokari ga aiki suka sauya shaye shaye da nishadi da fada da zaman banza.

Amma shugabannin ekklesiyar basu zauna kawai ba. Duk da haka sarkin ya ki hana wa'azin, sai suka koma ga jama'a. Sun yi iyakar kokarinsu don motsa tsoro da kiyayya da tsanancin ra'ayin jahilan nan masu camfi. Sa'an da ta yarda da mallamanta na karya, Paris, kamar Urushalima ta da, ba ta san lokacin ziyartarta ba, ko kuma al'amuran salamarta. Shekara biyu ana wa'azin maganar Allah a babban birnin; amma yayin da akwai da yawa da suka karbi bisharar, yawancin mutane suka ki ta. Francis ya nuna ba da yanci don cika burin kansa ne, 'yan paparuma kuma suka yi nasarar samun ci gaba. Aka sake rufe masujadu, aka kuma kafa wurin kashe masu laifi.

Calvin dai yana Paris, yana shirya kansa ta wurin nazari da bimbini da addu'a don aikin da ke gabansa, yana kuma ci gaba da baza hasken. Mahukumta suka kudurta kone shi. Yayin da ya dauka cewa inda ya boye kansa babu hatsari, sai ga abokansa a gurguje da labarin cewa hafsoshi suna hanyar zuwa su kama shi. Daidai lokacin aka ji an buga kofar waje da karfi sosai. Babu lokacin jinkiri. Wadansu abokansa suka tare hafsoshin a kofa yayin da wadansu suka taimake shi ya fita ta taga, nan da nan ya gudu zuwa bayan birnin. Daga masaukin da ya samu a gidan wani lebura abokin Canjin, ya canja kamaninsa da tufafin leburan, ya rataya garma a kafadarsa, ya kama hanya. Da ya nufi Kudu, sai ya sake samun mafaka a wata kasa da ke kalkashin ikon Magaret kuma.

A nan ya yi 'yan watanni kalkashin tsaron abokai masu iko, yana kuma ci gaba da nazari. Amma zuciyarsa tana wajen kai bishara Faransa dai, kuma dole ya fara aiki nan da nan. Da zaran guguwar ta huce, ya koma Poitiers da aikinsa, inda akwai jami'a, kuma inda aka rigaya aka karbi sabuwar koyaswar. Mutane daga kowane gefe suka saurari bishara da murna. Ba a yi wa'azin a fili ba, amma a gidan babban majistare, da masaukin shi Calvin, wani lokaci kuma a wurin hutawa na jama'a, Calvin yakan bude kalmomin rai madawami ga masu ji. Bayan wani lokaci, yayin da yawan masu sauraro ya karu, aka ga zai fi kyau a rika taruwa a bayan birnin. Sai aka zabi wani kogo a gefen wani kwazazzabo, inda itatuwa da duwatsu suka kara inganta mabuyar. Kananan kungiyoyin jama'a sukan bi ta hanyoyi dabam dabam zuwa wurin. A wannan wurin, a kan karanta Littafin ga jin mutane a kuma fassara shi. Nan ne masu Kin ikon paparuma a Faransa suka ci jibin su na farko. Daga wannan karamar majami'a aka aika da amintattun masu wa'azi zuwa wadansu wurare.

Calvin ya sake komawa Paris. Bai bar begensa cewa al'ummar Faransa baki daya za ta karbi Canjin ba har yanzu. Amma ya tarar da kowace kofar aiki a rufe. Koyar da bishara hakika kam hanya ne kai tsaye zuwa mutuwa. A karshe dai ya kudurta zai je Jamus. Yana

barin Faransa kuwa, guguwa ta abko ma masu Kin ikon paparuma, ta yadda, da yana wurin, da lallai ya hallaka.

‘Yan Canjin a Faransa, da kosawar ganin kasarsu tana tafiya daidai da Jamus da Switzerland, suka kudurta kai ma camfe camfen Rum babban bugu da zai falkas da dukan al’ummar. Don haka takardun sanarwa masu sokar mass suka bazu cikin dare daya, aka manna su ko ina a Faransa. Maimakon kawo ci gaban Canjin, wannan mataki na himma, amma bisa kuskure, ya jawo hasara ne kawai, ba kan masu aikata shi kadai ba, amma kan magoya bayan sabuwar koyaswar, ko ina a Faransa. Ya ba ‘yan Rum din abin da suka dade suna nema, watau dalilin bidar hallakawar masu ridda kwata kwata a matsayin masu tashin hankali, mumunan hatsari kuma ga gadon sarauta da zaman lafiyan al’ummar.

Wani wanda ba a san ko aboki ne ko makiyi ba, ya manna takardar sanarwan nan daya a kofar sarki. Sarkin kuwa ya fusata matuka. A wannan takardar aka yi ta sokar camfe camfen da aka kwashe sararraki da dama ana daukakawa. Kuma karfin halin kutsawa fadar sarki da kalaman nan ma ya ta da fushin sarkin. Cikin mamakinsa, sarkin ya tsaya shuru na dan lokaci, yana rawan jiki. Sa’an nan ya ce: “Bari a kama dukan wadanda ake zato ‘yan Luthanci ne. Zan hallaka su duka.” Sarki ya kudurta goyon bayan Rum gaba daya ke nan.

Nan da nan aka dauki matakan kama kowane mai ra’ayin Luther a Paris. Aka kama wani dan taliki mai aikin hannu, wanda ya saba kiran masu bangaskiya zuwa wuraren taronsu, aka tilasta shi nuna ma ‘yan sakon ‘yan paparuman gidan kowane mai Kin ikon paparuma a birnin. Jikin shi ya yi sanyi da wannan, amma daga baya tsoron mutuwa ta wurin wuta ya sha kansa, sai ya yarda ya zama mai bashewar ‘yan-uwansa. Morin, dansandan ciki na sarkin, tare da priestoci da masu rikon turaren hayaki, da masu zuhudu da sojoji, tare de mai bashewan, suka bi titunan birnin. An yi jerin nan don girmama mass mai-tsarkin nan ne, domin a nemi gafara sabo da wulakancin da aka yi ma mass din. Amma jerin gwanon nan tana da muguwar manufa a boye kuwa. Sa’an da aka kai gidan mai bin ra’ayin Luther, mai bashewan yakan yi wata alama, amma ba magana, sai a tsayar da jerin gwanon, a shiga gidan, a ja iyalin zuwa waje, a kuma daure su da sarka, sa’an nan sai a ci gaba da nema sauran su kuma. “Basu bar wani gida babba ko karami ba, ko kolejojin Jami’ar Paris.... Morin ya sa dukan birnin ya girgiza.... Aka shiga lokaci na ban razana kwarai.”

An kashe mutanen da azabar mugunta ne, aka umrta cewa a rage wutar domin a tsawaita azabarsu. Amma sun mutu masu nasara ne. Amincinsu bai raunana ba. Salamarsu kuma ba ta ragu ba. Masu tsananta masu da suka kasa raunana su suka ji kawai an ka da su. “An baza dakalin kisan ko ina a Paris, kuma aka rika kisa kowace rana, bi da bi, don tsawaita fallasa munin ridda. Amma a karshe dai, bishara ce ta yi riba. Abin da aka yi ya sa dukan Paris ta ga irin mutanen da sabobin koyaswoyin za su iya haifarwa. Babu bagadin da ya kai tudun gawayen da aka tara kasancewa dandalin wa’azi. Murna da salaman da suka haskaka fuskokin mutanen nan lokacin wucewarsu zuwa wurin mutuwarsu, da

jaruntakarsu yayin da suke tsaye a tsakiyar wutar, tawali'un gafararsu, sun canja fushin wadansu zuwa tausayi, kiyayya kuma zuwa kauna, wanda kuma da babban murya ya jawo hankula zuwa fifikon bishara."

Priestocin, don kara fusata mutane, suka yi ta baza zarge zarge mafi muni game da masu Kin ikon paparuma. Aka zarge su cewa sun shirya kashe dukan yan katolika, su hambarar da gwamnati, su kuma kashe sarki. Ko alamar shaidar zargin nan babu. Duk da haka, annabce annabcen muguntan nan sun cika, amma ta hanyoyi dabam. Zaluncin da 'yan Katolika suka yi ma masu Kin ikon paparuma sun tattaru don lokacin ramuwa, kuma daruruwan shekaru daga baya suka haifar da hallakan da suka ce an shirya ma sarki da gwamnatinsa da talakawansa kuma, amma kafirai ne suka kawo shi tare da 'yan paparuma kansu. Ba kafawar Kin ikon papruma ba, amma danne shi ne ya jawo ma Faransa masifun nan, shekaru dari uku daga baya.

Zato, rashin yarda, da tsoro mai yawa suka mamaye dukan mutane. Cikin wannan yanayi aka ga yawan tasirin da koyaswar Luther ta yi ga zukatan mutane shahararru ta fanin ilimi da masu martaba da halin kirki. Jima kadan sai aka iske ma'aikata masu rike manyan matsayi sun bar aiki. Masu aikin hannu, masu buga littattafai, 'yan makaranta, mawallafa, shehunan mallamai a jami'o'i, har da fadawa ma, suka salwanta. Daruruwa suka gudu daga Paris, suka zama yan gudun hijira daga kasarsu ta gado, ta haka kuma yawancinsu suka nuna goyon bayansu ga sabuwar bangaskiyar. 'Yan paparuman suka duba kewaye da su, da mamaki, suka gane mutane da yawa masu ridda da suka dade suna zama tare da su. Fushinsu ya huce kan jama'a da yawa marasa galihu masu ridda da ke kalkashin ikonsu har wannan lokacin. Gidajen kaso suka cika, iska kanata kuma ta duhunta da hayakin wutar da aka kunna kan masu goyon bayan bishara.

Da Francis I ya daukaka kansa don kasancewa shugaba cikin babban aikin falkas da ilimi a farkon karni na goma sha shida. Yakan ji dadin tara masana a fadarsa, daga kowace kasa. Son iliminsa da kyamar jahilci da camfin masu zaman zuhudun nan ne ya jawo irin zarafin da aka ba Canjin. Amma sabo da himmar batar da ridda, wannan shugaban ya yi dokar da ta hana buga littattafai ko takardu ko ina a Faransa! Francis I daya, daga misalai da yawa ne na cewa ilimi bai hana rashin sassauci da zalunci game da addini ba.

Faransa ta shirya za ta yi bukin shigar ta dungum cikin murkushe Kin ikon papapruma. Priestocin suka bidi cewa harin da aka kai ma Allah ta wurin sokar mass za a wanke shi da jini, kuma wai sarkin, a mdadin mutanensa, zai ba da goyon bayan sa ga aikin nan a gaban jama'a.

An zabi ran 21 ga watan Janairu, 1535 ne don bukin. An rigaya an motsa tsoron camfi da kiyayyar mutanen. Paris ta cika da jama'a da suka cika tituna daga kauyukan kewaye. An shirya fara ranar da babban jerin gwano ne mai ban sha'awa. "Gidajen gefen hanyan da za a bi suka cika da ado na ban mamaki, aka kuma kafa bagadi nan da can." A gaban

kowace kofa akwai tocilan da ke haskakawa don girmama mass din. Kafin wayewan gari, masu jerin gwanon sun taru a fadar sarki. “Da farko akwai tuta da giciye na kowane parish; bayansu sai ‘yan kasar, suna tafiya su biyu biyu, suna rike kuma da tocilan, kowane dayansu.” Kungiyoyi hudu na ma’aikatan ekklesiyar suka biyo, kowace daya da irin tufafinta. Sa’an nan babban tarin sifofi ya biyo baya. Biye da wadannan manyan shugabannin ekklesiya cikin tufafinsu masu launi iri iri da kayan ado, masu haskakawa, abin kallo.

“Bishop din Paris ne ya rike jibin a kalkashin wata babbar laima mai gwafa hudu da ‘ya’yan sarki su hudu suka rike.... bayan jibin, sarki ya biyo ... Ranan, Fancis I bai daura rawani ba, bai kuma sa kayan sarauta ba.” Da kai a bude, idanunsa suna kallon kasa, cikin hannunsa kuma ga kyendur da haskensa, sarkin Farnsa ya bayana “cikin yanayin mai tuba.” A kowane bagadi, yakan sunkuya don ban girma, ba don zunuban da sun kazanar da ransa ba, ko kuma jinin marasa laifi da ya zubar ba, amma wai don mumunan zunubin talakawan sa da suka soki mass. Bayansa sarauniya ta biyo da manyan jami’an kasa, suna tafiya biyu biyu su ma; kowa da tocilan da aka akunna.

Cikin hidimomin ranan, sarkin ya yi ma manyan ma’aikatan kasar jawabi a babban dakin taro na fadar bishop. Da bakinciki a fuskarsa ya bayana a gaban su, kuma da kalmomi na kaifin baki ya yi bakin cikin “laifi da sabo, da ranar bakin ciki da ban kunya” da ta abko ma al’ummar. Ya kuma kira ga kowne talaka mai-biyayya ya taimaka wajen murkushe annobar riddan nan da ke barazanar rushe Faransa. Ya ce: “Kamar yadda, da gaske ni ne sarkinku, idan na sa wata gaba ta ta harbu da wannan mumunar rubewar, zan ba ku ita ku yanke.... Biye da haka, in na g a daya daga yara na ya kazamtu da shi, ba zan bar shi ba, ... Ni da kai na zan mika shi, zan kuma mika shi hadaya ga Allah.” Hawaye sun bi maganarsa, dukan taron kuwa suka yi kuka, suna cewa da murya daya: “Za mu rayu mu mutu don addinin Katolika!”

Duhun al’ummar ya yi muni sosai, domin taka hasken gaskiya. Alherin da ke kawo ceto ya bayana, amma Faransa, bayan ta ga ikon sa da tsarkinsa, bayan kyaunsa na samaniya ya jawo dubbai, bayan birane da kauyuka sun haskaka da kyallinsa, ta juya ta zabi duhu maimakon haske. Sun kawar da kyautar sama din bayan an ba su ita. Suka kira nagarta mugunta, mugunta kuma nagarta, har sai da suka sami sakamakon rudin kansu da suka yi. Yanzu, ko da shike suna iya gani da gaske kamar suna yi ma Allah ne hidima ta wurin tsananta ma mutanensa, duk da haka, gaskiyan zatonsu bai mai da su marasa laifi ba. Hasken da da zai cece su daga yaudara, daga kazanta da laifn jini, sun ki shi da yardar ransu.

An dauki rantsuwar murkushe ridda a cikin majami’an nan ne da, kusan shekara dari uku daga baya, al’umman nan da ta ki Allah Mai-rai, ta daukaka Allahan Tunani a ciki. An sake yin jerin gwanon, wakilan Faransa kuma suka fito don fara aikin da suka rantse za su yi. “An kafa dakali na katako kusa kusa da juna, inda za a kone wadansu masu Kin ikon

paparuma da ransu, aka kuma shirya cewa za a sa wuta a kiraren, da zaran sarki ya iso, kuma cewa jerin gwanon jama'a za su tsaya su kalli kisar." Zaluncin da shaidun nan na Kristi suka sha ba shi da dadin fadi, sabo da yawan muninsa; amma wadanda aka kona din basu nuna rashin karfin hali ba. Da aka matsa ma wani ya janye, ya ce: "Na gaskata abin da annabawa da manzani suka yi wa'azinsa ne kawai da abin da dukan tsarkaka suka gaskata. Bangaskiya ta tana da dangana ga Allah, kuma za ta jimre dukan ikokin lahira."

Akai akai, jerin gwanon suka tsaya a wuraren zaluncin. Da suka kai inda aka fara tafiyar, a fadar sarki, jama'a ta waste, sarki da 'yan ekkledsiya kuma suka tafi, da gamsuwa game da yadda al'amura suka gudana a ranan, suka kuma gode ma kansu cewa aikin da suka fara yanzu zai ci gaba har sai an hallaka ridda gaba daya.

Bisharar salama da Faransa ta ki, hakika za a rushe ta, kuma sakamakon hakan mumuna ne. Ran 21 ga Janairu, 1793, shekara dari biyu da hamsin da takwas daga ranan da Faransa ta kudurta tsananta ma 'yan Canji, wani jerin gwano da wata manufa dabam ya bi titunan Paris kuma, "Sarkin ne kan gaba kuma; akwai kuma hayanniya da surutu; an kuma ji kukan mutane marasa laifi; akwai kuma dakali na katako, aka kuma rufa al'amuran wannan ranar da kashe kashe; Loius XVI ne, yana gardama da masu kulle shi a kurkuku da masu kisasa, suka kawo shi wurin akwatin, aka kuma danne shi a wurin aka rike har sai da gatarin ya fado, yankakken kan sa kuma ya gungura kan dakalin katakon." Kuma ba sarkin ne kadai ba, kusa da wurin ma mutum dubu biyu da dari takwas aka hallaka hakanan a zamanin Mulkin Ta'addanci.

Canjin ya mika ma duniya budadden Littafi, ya bayana kaidodin dokar Allah, ya kuma nuna muhimmancin ta ga lamirin mutane. Allah Ya bayana ma mutane dokoki da kaidodin sama. Allah fa Ya ce: "Ku kiyaye su fa ku aikata; gama hikimarku da azancinku kenan a idanun al'ummai wadanda za su ji dukan wadannan farillai, za su kwa che. Hakika wannan babbar al'umma mai-hikima che mai-azanchi." Kubawa 4:6. Sa'an da Faransa ta ki kyautar sama, ta shuka irin rudami da rushewa ne; dole kuwa sanadi da sakamako su haifar da Babban Tawaye da Mulkin Ta'addanci.

Da dadewa kafin zaluncin da takardun sanarwan da aka yi ta likawa a bango suka jawo, mai karfin zuciyan nan Farel mai-kwazo, ya gudu daga kasar sa ta haihuwa tilas. Sai ya je Switzerland. Ta wurin aikinsa da ya goyi bayan Zwingli, ya taimaka wajen goyon bayan Canjin. Nan ya karasa shekarunsa na karshe, duk da haka ya ci gaba da tasiri sosai ga Canjin a Faransa. Cikin shekarun farko na hijirarsa, kokarinsa na baza bishara a kasar sa ta gado ne. Ya ci lokaci mai yawa yana wa'azi ga yan kasarsa, kusa da kan iyaka, inda a natse, ya kalli jayayyar, ya kuma taimaka ta wurin kalmominsa na karfafawa da shawara kuma. Da taimakon wadansu 'yan gudun hijiran aka juya rubuce rubucen 'yan Canjin Jamus zuwa harshen Faransa. An rika ba masu sayarwa takardun, kan kurdi mara yawa, ta haka anfanin aikin ya taimaka masu suka ci gaba da aikin.

Farel ya shiga aikinsa a Switzerland da sunan cewa shi mallamin makaranta ne. Sa'anda ya koma wani parish na kauye, sai ya dukufa ga karantar da yara. Ban da ababan da aka saba koyarwa, ya rika koyar da gaskiya na Littafi da dabara, da begen cewa ta wurin yaran zai sami iyayen. Akwai wadanda suka gaskata, amma priestoci suka shigo domin su tsayar da aikin, aka kuwa zuga kauyawa masu camfi suka yi jayayya da aikin. Priestocin suka ce: "Wannan ai ba bisharar Kristi ba ce, ganin cewa w'azin ta ba ya kawo salama sai yaki." Kamar almajiran farko, sa'anda aka tsananta masa a wani birni, yakan gudu zuwa wani. Daga kauye zuwa kauye, daga birni zuwa birni, ya yi ta tafiya a kasa, yana jimre yunwa da sanyi da gajiya, kuma ko ina ya je dai, a bakin ransa. Ya yi wa'azi a kasuwanni da majami'u, wani lokaci ma a manyan majami'un. Wadansu lokuta, a majami'un ba ma wadanda za su ji wa'azin; wadansu lokuta a kan bata wa'azin da ihu da holo; kuma akan fizge shi da karfi daga bagadin. Fiye da sau daya yan iska suka tare shi suka yi masa duka har kusan mutuwa. Duk da haka dai ya ci gaba. Ko da shike an dinga koran sa akai akai, da naciya dai ya dinga komawa inda aka kore shi; daya bayan daya kuwa ya yi ta ganin birane da garuruwan da suka taba zama cibiyoyin 'yan paparuma suna karban bishara. Karamar parish inda ya fara aiki ta karbi sabuwar bangaskiyar. Biranen Morat da Neuchatel ma suka yi watsi da al'adun Rum, suka kuma cire gumaka daga majami'unsu.

Farel ya dade yana so ya kafa tutar Kin ikon paparuma a Geneva. Idan aka sami wannan birnin, zai zama cibiyar Canjin a Faransa, da Switzerland, da Italiya. Da wannan manufa a gabansa ya ci gaba da aikinsa har sai da, da yawa cikin garuruwa da kauyuka kewaye suka karbi sakon. Sa'an nan, tare da wani abokinsa, ya shiga Geneva. Amma wa'azi biyu kadai aka yarda mashi ya yi sa'an da prietocin suka kasa sa mahukuntan kasar su hukumta shi, suka kira shi gaban majalisar ekklesiya, inda suka je da makamai a boye cikin rigunansu, da niyyar dauke ransa. A waje, yan iska cike da fushi suka taru da takubba da kulake domin tabbatar da kutuwarsa, ko da ya tsere ma majalisar. Amma kasancewar majistarori da dakaru dauke da makamai ya cece shi. Washegari da sassafe, aka raka shi da abokinsa har ketaren korama zuwa inda babu hatsari. Karshen yunkurin sa na farko na kai bishara Geneva kenan.

Don gwaji na biye an zabi wani matashi ne wanda ganin tawali'un sa ma ya sa har masu cewa suna goyon bayan Canjin ma suka dinga rena shi. Amma me wannan zai iya yi inda aka ki Farel? Ta yaya mai kankantar karfin zuciya da kwarewa zai jimre guguwar da ta tilasta mafi karfi da karfin zuciya ya gudu? "Ba ta wurin karfi ba, ba kuwa ta wurin iko ba, amma ta wurin ruhuna, in ji Ubangiji mai-runduna." Zechariah 4:6. "Amma Allah Ya zabi kuma raunana na duniya, domin shi kunyatadda masu karfi." "Domin wautar Allah ta fi mutane hikima; rashi karfin Allah kuma ya fi mutane karfi." Korinthiyawa I, 1:27, 25.

Froment ya fara aikin sa kamar mallamin makaranta ne. Gaskiyan da ya koya ma yaran a makaranta sukan maimaita su a gidajensu. Ba da jimawa ba, iyaye suka fara zuwa sauraron fassarar Littafin, har ajin makarantar ya cika da masu sauraro. Akan rarraba Sabon

Alkawali da majallu kyauta, suka kuwa kai wurin mutane da yawa da basu isa su zo jin sabobin koyaswoyin a fili ba. Bayan wani lokaci, wannan ma'aikacin ma an tilasta shi ya gudu, amma gaskiyar da ya koyar ta rigaya ta mallaki zukatan mutane.

An dai shuka Canjin, ya kuma ci gaba yana kara karfi da fadi kuma. Masu wa'azin suka dawo, kuma ta wurin aikinsu, sujadar masu Kin ikon paparuma ta kafu a Geneva.

Birnin ya rigaya ya rungumi Canjin lokacin da Calvin, bayan kai da komowa dabam dabam da canje canje iri iri, ya shigo birnin. Da ya dawo daga ziyarar wurin da aka haife shi, yana kan hanyarsa zuwa Basel, sai ya lura cewa hanya mikakkiya ta cika da dakarun Charles V, wannan kuwa ya tilasta shi bin doguwar hanya mai kwane kwane zuwa Geneva.

A wannan ziyarar Favel ya gano hannun Allah. Ko da shike Geneva ta rigaya ta karbi sabuwar bangaskiyar, duk da haka akwai babban aiki da ya rage a yi a wurin. Ba kungiyoyi ake tubarwa zuwa wurin Allah ba, mutane daya daya ake tubarwa zuwa wurin Allah; dole a aiwatar da aikin Canjin a cikin zuciya da lamiri ta wurin ikon Ruhu Mai-tsarki, ba ta wurin dokokin majalisu ba. Yayin da mutanen Geneva suka rigaya suka yi watsi da ikon Rum, basu shirya ta hakanan su rabu da miyagun halayyan da suka yawaita a zamanin mulkinta ba. Tabbatar da kaidodin bishara a nan, a kuma shirya mutanen nan su cika matsayin da Allah ke bidarsu su dauka, ba kananan al'amura ba ne.

Farel ya tabbata cewa Calvin mutum ne wanda zai iya hada kai da shi cikin aikin nan. Cikin sunan Allah ya umurci saurayin ya yi aiki a nan. Calvin ya ja baya sabo da mamaki. Ga shi mai- yawan tsoro ne da son salama, ya yi dari dari da zancen saduwa da mutanen Geneva din nan masu karfin zuciya da 'yancin kai, har ma da son gwada karfi. Karancin lafiyarsa, hade da halayyan sa na yawan nazari, suka sa shi ya bidi yin ritaya. Da shike ya gaskata cewa da alkalaminsa zai fi yin aikin canjin, ya yi marmarin samun wurin da babu surutu domin yin nazarin, ta wurin wallafa littattafai da kasidu da dai sauran su kuma zai rika koyarwa ya kuma gina ekklesiyoyin. Amma umurnin Farel ya zo masa kamar kira ce daga sama, kuma bai isa ya ki ba. Ya ce ya ga kamar "hannun Allah ya mike sama, ya kama shi, ya kuma kafa shi babu kawuwa a wurin da ya kosa ya bari."

A wannan lokacin, manyan hadaruka sun kewaye aikin Kin ikon paparuman. Haramce haramcen paparuma sun rika taruwa kan Geneva, kuma manyan kasashe suka yi masa barazanar hallaka shi. Ta yaya wannan karamin birnin zai nuna tsayayya ga mulkin nan mai yawan iko da yakan tilasta sarakuna su yi biyayya? Ta yaya za ta yi tsayayya da dakarun manyan kasahen duniya?

Ko ina cikin Kirista, Kin yarda da ikon paparuma ya gamu da kiyayya daga manyan magabta. Bayan nasarorin farko na Canjin sun wuce, Rum ta tara sabobin dabaru da begen hallaka Canjin. A wannan lokacin aka kafa kungiyar Jesuits, kungiya mafi mugunta da zalunci da karfi daga cikin jarumawan paparuma. Da shike sun yanke daga danantaka na duniya da ababan burin na mutumtaka, sun mutu ga marmari irin na mutumtaka, an kuma

kashe tunani da lamiri kwata kwata, basu san wata kaida ko dangantaka ba, sai ta kungiyarsu, aikin su kadai kuma shi ne fadada ikon kungiyar. Bisharar Kristi ta sa masu bin ta suka iya jimre hadari da wahala, ba tare da damuwa game da sanyi ko yunwa ko aiki ko talauci ba, domin daga tutar gaskiya ko ana horo da kurkuku da kisa. Don yin fada da ‘yan Canjin nan, Jesuits suka motsa mabiyansu da matsanancin ra’ayin da ya sa suka iya jimre irin matsaloli dayan, su kuma yi jayayya da ikokin gaskiya, da kowane irin rudu. Babu laifin da ya fi karfin aikatawarsu, ba rudin da ba za su iya yi ba, ba sake kaman da ba za su iya yi ba kuma. Da shike sun ranatse suka rungumi talauci da kaskantarwa har abada, nufinsu ne su tara dukiya da iko don anfani wajen hambarar da Kin ikon paparuma, da sake kafawar daukakar paparuma din.

Sa’an da suka fita a matsayin su na ‘yan kungiyar, sukan yafa kamanin tsarki, suna ziyartar kurkuku da asibitoci, suna taimakon marasa lafiya da matalauta, suna cewa sun rabu da duniya, suna kuma amsa sunan Yesu, wanda Ya dinga aikata nagarta. Amma kalkashin kyaun nan na waje, akan boye manufofi mafi-muni. Wata muhimmiyar akidar kungiyar ita ce cewa, sakamako da ta yi kyau, ko ta halin kaka. Ta wurin wannan akidar, karya da sata da rantsuwar karya da kisan kai suka karbu, har ma aka daukaka su, sa’an da suka biya bukatun ekklesiya. Kalkashin bad da kamani iri iri, yan Jesuits sukan rika shiga ma’aikatun gwamanti, har suna zama yan majalisun sarakuna, suna tsara manufofin kasashe. Suka zama barori domin su zama masu leken asirin iyayen-gijinsu. Sukan kuma bude kolejoji don yaran fadawa da na yayan sarakuna, da makarantu don talakawa; yaran masu Kin ikon paparuma kuma aka jawo su cikin kiyaye al’adun yanpaparuma. Dukan holewa da adon sujada ta Rum an shirya su ne don rikitar da tunani, da burge zuciya, ta haka kuwa ‘yancin da ubani suka yi fama suka zub da jini a kai, yaransu suka yin banza da shi. ‘Yan Jesuit sun bazu ko ina a Turai da sauri, kuma duk inda suka je, an sami falkaswar tsarin paparuma.

Don kara masu iko, aka ba da wani umurni da ya sake kafa tsarin Binciken nan. Duk da kin shi da aka yi ko ina, har ma a kasashen marasa rinjaye, ‘yan paparuma sun sake kafa mumunan cibiyan nan, aka kuma maimaita munanan laifuka a kurkukunsa na boye. A kasashe da yawa, dubbai kan dubban shahararrun ‘yan kasa, mafiya tsabta da martaba, mafiya hikima da ilimi, masu ibada da amintattun pastoci, yan kasa masu kuzari da kishin kasa, masanan gaske, masu baiwar zane zane, kwararrun masu aikin hannu: aka karkashe su, ko kuma aka tilasta su gudu zuwa wadansu kasashe.

Irin hanyoyin da Rum ta yi anfani da su kenan don bice hasken canjin, a janye Littafi daga wurin mutane, a kuma dawo da jahilci da camfin sararakin zamanun. Amma a kalkashin albarkar Allah da aikin masu martaban nan da Ya shirya su gaji Luther, ba a hambarar da Kin ikon paparuma ba. Ba a wurin taimako ko makamai na yaran sarakuna ya sami karfin sa ba. Kasashe mafi kankanta, alummomi mafi rashin daraja da karfi, suka zama wuraren da Kin ikon paparuma ya fi karfi. Dan kankanin Geneva din nan ne a tsakiyar

manyan magabta masu shirin rushe shi; Holland ne a gabar tekun da ke Arewa da shi, yana fama da zaluncin Spain, wanda shi ne mulki mafi girma da wadata; Sweden din nan mara haske, sandararre, su ne suka samo ma Canjin nasarori.

Kusan shekara talatin Calvin ya yi ta aiki a Geneva da fari don kafa ekklesiya mai-bin halin kirki na Littafin, sa'annan kuma don ci gaban Canjin ko ina Turai. An sami la'ani game da hanyar shugabancinsa, kuma koyaswoyin shi sun kasance da kurakurai. Amma yana da hannu cikin koyar da gaskiya masu muhimmanci na musamman a zamaninsa, da karfafa kaidodin Kin ikon paparuma, sabanin hanzarin guguwar paparuma din, da kuma karyar da saukin kai da tsabtar rai a ekklesiyoyin da suka canja, maimakon girman kai da lalacewan da aka koyar kalkashin koyaswar Rum.

Daga Geneva, takardu da mallamai suka fita don shelar sabobin koyaswoyin. Ga wannan ne masu shan zalunci na dukan kasashe suka duba don koyaswa da shawara da karfafawa. Birnin Calvin ya zama mafakar yan Canjin dukan Yammacin Turai. Yayin da suke gudu daga guguwa da suka ci gaba har daruruwan shekaru, masu gudun suka zo kofofin Geneva. Ga yunwa ga raunuka ga rashin matsuguni, da rashin yan-uwa, aka marabce su da kyau, aka kuma lura da su sosai; da kuma suka sami gida a nan, suka albarkaci birnin ta wurin kwarewarsu, da iliminsu da ibadar su. Da yawa da suka nemi mafaka a nan suka koma kasashensu don yin jayayya da zaluncin Rum. Da John Knox da masu tsabar addini yan Ingila, da masu Kin ikon paparuma a Holland da Spain, da kuma Huguenots na Faransa da aka dauko daga Geneva, tocilan gaskiya don haskaka duhun kasashen su na gado.

Babi na 13—Netherlands da Scandinavia

A Netherlands, tun da wuri zaluncin paparuma ya jawo kin yarda. Shekaru dari bakwai kafin lokacin Luther, bishop biyu ba da tsoro ba, suka bayana kurakuran paparuma, domin sa'anda aka aike su jakadanci a Rum, sun gane ainihin halin tsarin paparuman: "Allah ya tanada ma amaryarsa ekklesiya kyakyawar guzuri don iyalinta, da gara mara shudewa ko lalacewa, ya kuma ba ta rawani da sandar sarauta na har abada … kana kuma anfani da dukan wadannan kamar taryen barawo. Ka aza kanka a haikalin Allah; maimakon makiyayi, ka zama kerkeci ga tumakin; … kana so mu gaskata cewa kai madaukakin bishop ne, amma kana yi kaman azalumi … maimako ka zama bawan bayi, yadda kake kiran kanka, kana kokarin zama Ubangijin iyayengiji. … kana jawo ma dokokin Allah raini …. Ruhu Mai-Tsarki ne mai gina dukan ekklesiyoyin duniya…. Birnin Allahnmu wanda dukan mu yan kasansa ne, yana kaiwa dukan yankunan sammai, ya kuma fi birnin da annabawa suka ba ta suna Babila, wadda ke da'awar cewa ita ta Allah ce, tana kai kanta sama, tana kuma yin alfaharin cewa hikimarta mara mutuwa ce; a karshe kuma, ko dashike ba dalili, tana da'awar cewa ba ta taba kuskure ba, kuma ba zata taba iya yin kurskure ba."

Wadansu sun taso daga karni zuwa karni suna maimaita wannan kin yardan kuma, da suka bi kasashe dabam dabam, aka kuma san su da sunaye iri iri, suna da irin halin masu bishara na Vaudois, suka kuma baza bishara ko ina, sun kuma shiga Netherlands. Koyaswoyinsu suka bazu da sauri. Suka juya Littafin Waldensiyawa zuwa harshen Dutch. "Suka ce wannan ya yi anfani sosai; ba ba'a, ba tatsuniyoyi, ba wasa, ba rudu, sai kalmomin gaskiya; cewa akwai dai wurare masu wuyan ganewa amma ainihin dadin abin da ke da kyau da tsarki kuma yana da saukin ganowa daga cikinsa" Abin da abokan bangaskiya ta da suka rubuta kenan a karni na goma sha biyu.

Sai zaluncin Rum ya fara; amma a tsakiyar wuta da azaba masu ba da gaskiya suna ci gaba da yawaita; suna furta cewa Littafi ne kadai iko mara kuskure a sha'anin addini, kuma "bai kamata a tilasta wani ya gaskata ba, sai dai a ganar da shi tawurin wa'azi."

Koyaswoyin Luther sun sami karbuwa a Netherlands, masu dukufa da aminci kuma suka shiga wa'azin bisharar. Daga wata lardin Holland, Meno Simons ya zo da iliminsa na Roman Katolika da shafewarsa priest duk da haka bai san Littafi ba, kuma bai yarda ya karanta shi ba don tsoron kada a yaudare shi ya yi ridda, sa'anda shakka game da koyaswar canja jibi zuwa ainihin jikin Yesu da jininsa ta dame shi, ya dauka jaraba ce daga Shaitan, kuma tawurin addu'a da furta zunubi ya yi kokarin kubutar da kansa daga jarabar; amma a banza. Tawurin zuwa cudanya a wuraren shakatwa ya yi kokarin danne muryar lamiri da ke zarginsa, amma a banza. Daga baya, ya shiga nazarin Sabon Alkawali, wannan kuwa tare da rubuce rubucen Luther, ya sa shi ya karbi sabuwar bangaskiyar. Bayan wannan, ya ga yadda a wani kauye kusa kusa aka yanke kan wani wai don an sake yi masa baptisma.

Wannan ya sa shi binciken Littafi game da baptismar yara. Bai ga dalilinsa daga Littafi ba, amma ya ga cewa ko ina tuba da bangaskiya ake bukata kafin a yi ma mutum baptisma.

Menno ya janye daga ekklesiyar Rum, ya kallafa ransa ga karya da gaskiyan da ya samu. A Jamus da Netherlands, wadansu masu matsanincin ra'ayi suka taso, suna koyaswoyi na wauta da hadasa hargitsi, suna bata oda da hankali, har ma suna jawo gwada karfi da bare. Meno ya ga munanan sakamakon da ayukan nan za su haifar, sai ya shiga hamayya da koyaswoyin kuskuren nan da munanan dabarun masu matsanancin ra'ayin. Amma sun rigaya sun rudi mutane da yawa, ko da shike mutanen sun watsar da munanan koyaswoyin; akwai kuma zuriyar Kirista na da da yawa, sakamakon koyaswar Waldensiyawan. Meno yayi aiki da nasara mai-yawa cikin wadannan kungiyoyin.

Ya yi shekara ashirin da biyar yana tafiye tafiye tare da matarsa da yaransu, suna jimre manyan wahaloli da talauci, kullum kuma ran shi na ciki musamman cikin marasa gata, amma yana tasiri ko ina. Yana da baiwar iya magana, ko dashike iliminsa ba yawa, shi kuwa mai cikakken aminci ne, mai tawali'u da halayyan kirki, da ainihin himmar ibada, yana ba da kwatancin koyaswarsa ta wurin rayuwarsa, ya kuma sami karbuwa ga mutane. Masu binsa a warwatse suke, kuma ana kuntata masu. Sun wahala kwarai daga gigicewar masu matsanancin ra'ayi. Duk da haka dai jama'a da yawa sun tuba sabo da aikinsa.

Ba inda aka karbi sabobin kowasoyin kamar Netherlands. A kasashe daya daya ne kawai aka fi tsananta ma masu kiyaye su. A Jamus, Charles V ya hana canjin, kuma son sa ne da ya hallaka dukan masu kiyaye sabobin koyaswoyin, amma 'ya'yan sarakuna suka yi tsayayya da zaluncinsa. A Netherlands ikonsa ya fi yawa, kuma dokokin zalunci suka rika bin juna akai akai. Karanta Littafi, ko ji ko wa'azin Littafi, ko ma yin Magana game da shi, yakan jawo horon kisa ne, yin addu'a ga Allah cikin sirri, kin sunkuya ma gunki, ko raira zabura, duk hukuncinsu kisa. Ko da ana ce an bari, har da rantsuwa ma, akan hukunta laifinsu, in maza ne, a kashe su da takobi; in mata ne, a bizne su da ransu. Dubbai sun hallaka a zamanin mulkin Charles V da na Philip II.

A wani likaci iyali guda aka kawo gaban masu binciken, aka zarge su da rashin zuwa mass da kuma yin sujada a gida. Sa'anda aka tambayi autan dan game da ayukansu cikin sirri sai ya amsa: "Mukan fadi a gwiwarmu ne, mu yi addu'a cewa Allah ya haskaka zukatanmu, ya kuma gafarta zunubanmu; mukan yi addu'a don sarkinmu; muna addu'a don majitarorinmu, cewa Allah ya kiyaye su?" Wadansu masu shari'an suka kadu, duk da haka an kashe uban da daya daga cikin 'ya'yansu.

Bangaskiyar wadanda aka yi wa zaluncin ta je daidai da fushin azaluman. Ba maza kadai ba, mata da 'yan mata ma sun nuna karfin zuciya mara kaduwa. "Mata sukan tsaya a gefen katakon da ake kashe mazasu, kuma yayinda yake jimre wutar, takan rada masa kalmomin ta'aziya, ko kuma ta raira zabura don karfafa shi." "Yan mata sukan kwanta cikin kabarinsu da ransu kamar suna cikin dakinsu da suke barci a ciki kowane dare; ko

kuma su je dakalin katakon nan da wutan, suna saye da tufafinsu mafi kyau, kamar za su bukin aurensu.”

Kamar lokacin da kafirci ya so ya hallaka bishara, jinin Kirista ya zama iri. Zalunci ya kara yawan shaidu na gaskiya. Shekara bayan shekara, sarkin da ya haukace da himmar mutane da ta ki mutuwa, ya ci gaba da muguntarsa; amma a banza. Kalkashin William bafaden Orange, canjin ya kawo ma Holland ‘yancin sujada ga Allah.

A duwatsun Piedmont, a filayen Faransa, da gaban tekun Holland, ci gaban bishara ya sami bayanuwa ta jinin almajiranta. Amma a kasashen Arewa ya shiga cikin salama. Dalibai a Wittenberg da suke dawowa gidajensu, suka kai sabuwar bangaskiyar har Scandinaviya. Wallafawar rubuce rubucen Luther ma ya baza hasken. Mutanen arewan nan masu saukin kai suka juya daga lalacewa da shagali, da kuma camfe camfen Rum, suka rungumi saukin kai da gaskiyar Littafi masu kawo rai.

Tausen, “mai-canjin Denmark,” dan talaka ne. Yaron ya nuna alamar yawan bisira; ya yi kishin samun ilimi, amma yanayin iyayensa ya hana shi samu, sai ya shiga zaman zuhudu. Nan fa tsabtar ransa da amincinsa sun burge mai gidansa. Da aka gwada shi sai aka ga cewa yana da baiwar da za ta zama da anfani ga ekklesiya nan gaba. Aka kudurta za a ba shi ilimi a wata jami’a a Jamus ko Netherlands. Sai aka ba dalibin nan damar zaben jami’ar da zai je, amma ban da Wittenberg. Ba a so a sa dalibin cikin hatsarin gubar ridda ba, in ji priestocin.

Tausen ya je Cologne, daya daga biranen da koyaswar Rum ta fi karfi. A nan, ba da jimawa ba, ya yi kyamar dabon masu makarantar. A lokaci dayan, ya sami rubuce rubucen Luther. Ya karanta su da marmari da mamaki kuma, ya kuma so da dan canjin da kansa ya koyar da shi. Amma kafin hakan ya faru, dole ya bata ma maigidansa zuciya har ma ya dena taimakonsa. Ba da jimawa ba, ya dauki kudurinsa, ba da jimawa ba kuwa aka yi rajistarsa a matsayin dalibi a Witternberg.

Sa’an da ya dawo Denmark, sai ya koma zaman zuhundu kuma. Ba wanda ya zata cewa yana Luthanci tukuna; bai bayana asirinsa ba, amma ya yi kokari, ba tare da ingiza kiyayar abokansa ba, don jawo su zuwa bangaskiya mafi tsabta da rayuwa mafi tsarki. Ya bude Littafi ya kuma bayyana ainihin ma’anarsa, daga bisani kuma ya yi wa’azin Kristi gare su a matsayin adalcin mai zunubi, da begensa na ceto. Mai gidansa a wurin zaman zuhudun nan ya fusata kwarai, domin ya yi bege mai yawa cewa Tansen zai zama gwarzon mai kare Rum. Nan da nan aka cire shi daga inda yake aka sake masa wuri inda aka tsare shi cikin dakinsa, ana duba shi ba sakewa.

Sabobin masu lura da shi sun razana sa’anda masu zaman zuhudu da yawa suka tuba suka zama masu Kin ikon paparuma. Daga dakin da aka tsare shi, Tausen ya rika shaida ma abokansa gaskiyar. Da a ce priestocin Denmark din nan sun kware a tsarin ekklesiya na magance ridda da ba a sake jin muryar Tansen ba kuma, amma maimakon tura shi wani

kurkuku na kalkashin kasa, sai suka kore shi daga gidan zaman zuhudun. Yanzu ba su da iko. Wata sabuwar doka ta ba da kariya ga masu koyar da sabuwar koyaswar. Tansen ya fara yin wa'azi. Aka bude masa majami'un, mutane kuma suka rika taruwa suna ji. Wadansu ma suka rika wa'azin maganar Allah, aka baza Sabon Alkawali na harshen Denmark ko ina. Kokarin 'yan paparuma don hambarar da aikin ya fadada shi ne, ba da jimawa ba kuma Denmark ta sanar da cewa ta karbi sabuwar bangaskiyar.

A Sweden ma, samari da suka rigaya suka sha daga rijiyar Witternberg sun kai ma yan kasarsu ruwan nan na rai. Biyu daga cikin shugabaninin canjin a Sweden, Olaf da Laurantius Petri, 'ya'yan wani makeri a Orebro sun yi makaranta kalkashin Luther da Melanchton, suka kuma koyas da gaskiyar da suka koya. Kamar Luther, Olaf ya motsa mutanen da himmarsa da kaifin bakinsa kuma, yayin da Laurentius kuma, kamar Melanchthon, mai sani ne mai zurfin tunani, natsetse kuma. Dukan su mutane ne masu zurfin ibada, kwararrun masanan tauhidi da karfin zuciya wajen fadada gaskiya. Sun gamu da jayayyar yan paparuma. Prestoci 'yan paparuma suka zuga jahilai da masu camfi. Yan iska sun rika kai ma Olaf Peteri farmaki, sau da yawa kuma da kyar ya tsira da ransa. Amma sarki ya goyi bayan 'yan canjin nan, ya kuma tsare su.

Kalkashin shugabancin ekklesiyar Rum mutanen sun nutse cikin talauci da danniya. Basu san Littafin ba; kuma da shike addininsu na alamu da bukuwa ne kawai, mara haskaka tunani, suka fara komawa zuwa bangaskiyar arnanci da ayukan kafirci na iyayensu. Kasar ta rabu ta yadda tashe tashen hankulansu suka kara ma kowa wahala. Sarkin ya kudurata yin canji a kasa da ekklesiya, ya kuma marabci kwararrun masu taimakon nan cikin yaki da Rum.

A gaban sarki da shugabanin Sweden, Olaf Pedri ya kare koyaswoyin sabuwar bangaskiyar, sabanin jarumawan Rum. Ya ce ya kamata a karbi kyaswoyin ekklesiya idan sun je daidai da Littafin ne kawai; cewa Littafin ya bayana muhimman koyaswoyin addini a fili da sauki kuma, domin dukan mutane su iya fahimtarsu. Kristi ya ce "Abin da ni ke koyarwa ba nawa ba ne, amma nasa ne wanda ya aiko ni." Yohanna 7:16; Bulus kuma ya ce: "idan har ya yi wa'azin wata bishara daban da wadda ya karba zai zama la'anne (Galatiyawa 1:8). Dan canjin ya ce; "Don me wadansu zasu kafa koyaswoyin da suka ga dama sa'annan su ce wajibi ne a kiyaye su don samun ceto?" Ya nuna cewa dokokin ekklesiya basu da iko idan suka saba ma dokokin Allah, ya kuma manne ma babban kaidan nan cewa "Littafin da Littafin kawai" shi ne ma'aunin bangaskiya da ayuka.

Wannan hamayyar tana nuna mana "irin mutanen mayakan canjin. Ba jahilai ba ne, ko yan darika, ko masu tada rudani, ko kusa; mutane ne da suka yi nazarin maganar Allah, suka kuma san yadda za su yi anfani da makaman da Littafi ya ba su. Game da sani, sun yi fice a zamaninsu. Idan muka mai da hankulan mu ga sunannun cibiyoyi kamar Witternberg da Zurich, da sannanun sunaye kamar Luther da Melanchthon, da Zwingli da Oecolampadius, nan da nan za a ce mana wadannan ne shugabannin aikin, kuma ya kamata

su nuna iko mai girma da nasarori masu yawa; amma ba haka na kasa da su ba. Bari dai mu koma lungun fagen faman nan na Sweden, wanda ba a saurin ganewa, da kuma sunayen nan Olaf da Laurentius Petri, da ba a san su sosai ba — daga iyayen gida zuwa almajiran kenan - me za mu gani? … Masana da kwarraru na tauhidi; wadanda suka kware a sanin dukan tsarin bishara ta gaskiya, kuma suna nasara kan masannan makarantun Rum da masu martabar ta.

Sakamakon wannan jayyayar, sarkin Sweden ya karbi bangaskiyar Kin ikon paparuma, jima kadan kuma majalisar kasar ta bayana cewa ta goyi baya ita ma. Olaf Petri ya rigaya ya juya Sabon Alkawali zuwa harshen Sweden, sarki kuma ya roke shi da dan'uwansa suka shiga juya dukan Littafin. Ta hakanan mutanen Sweden suka sami maganar Allah cikin harshensu. Majalisa ta umurta cewa ko ina a kasar, masu aikin bishara su bayana Littafin, a kuma koya ma yan makaranta karanta Littafi.

Sannu a hankali aka kori duhun jahilci da canfi ta wurin hasken bishara. Da shike an yantar da ita daga danniyar Rum, kasar ta sami karfi da girman da ba ta taba samu ba. Sweden ta zama babbar cibiyar Kin ikon paparuma. Shekaru dari daga bisani, a lokacin kunci sosai, wannan karamar kasa mara karfi wadda ita ce kadai a Turai ta taimaka — sai ga ta ta ceci Jamus a mumunan yakin shekaru Talatin din nan. Dukan Turai ta Arewa ta kusan sake nutsewa kalkashin zaluncin Rum kuma. Mayakan Sweden ne suka taimaki Jamus ta juya ci gaban Rum, ta samo yanci ma masu kin ikon Rum - Calvinawa da Luthawa - ta kuma dawo da yancin lamiri ga kasashen da suka karbi Canjin.

Babi na 14— 'Yan Canjin Ingila na Baya.

Yayin da Luther ke bude rufaffen Littafin ga mutanen Jamus, Ruhun Allah ya motsa Tyndale ya yi ma Ingila haka ma. An rigaya an juya Littafin Wycliffe daga na Latin, wanda ke da kurakurai da yawa. Ba a taba buga shi ba, kuma kurdin sayen rubutaciyar ya yi yawa ta yadda mawadata da fadawa ne kadai za su iya sayen shi, kuma da shi ke ekklesiya ta haramtadda shi, bai yadu sosai ba. A 1516, shekara daya kafin bayanuwar ra'ayoyin nan na Luther, Erasmus ya rigaya ya wallafa Sabon Alkawali da harshen Latin da na Helenanci. Yanzu, na farko kenan da aka buga maganar Allah cikin harshensa na asali. A wannan Littafin an gyara kurakurai da yawa daga juyin harsunan da aka fara bugawa, wanda ya fito da ainihin ma'anar. Wannan ya kai mutane da yawa ga sanin gaskiyar, ya kuma kara karkon Canjin. Amma yawancin talakawa basu sami maganar Allah kai tsaye ba tukuna. Tyndale ne ya kamala aikin Wycliffe na ba da Littafi ga yan kasarsa. Shi natsatsen dalibi ne mai kwazon neman gaskiya, ya kuma sami bisharar daga Sabon Alkawali na Hellennanci da Erasmus ya wallafa ne. Ya yi wa'azin ra'ayoyinsa ba tsoro, yana cewa a gwada dukan koyasuwoyi da Littafin. Game da kirarin yan paparuma cewa ekklesiya ce ta ba da Littafin, kuma ekklesiya ce kadai za ta iya fasarta shi, Tyndale ya amsa; "Kun san wanda ya koya ma gaggafa neman abincinsu? Haka kuwa Allah dayan ke koya ma mayunwata 'ya'yansa neman Ubansu cikin maganarsa. Maimakon ba mu Littafin, ku ne kuka boye mana shi, ku kuke kone wadanda ke koyar da shi, kuma da kun iya ma da za ku kone Littafin kansa."

Wa'azin Tyndale ya jawo marmari sosai, da yawa sun karbi gaskiyar. Amma Priestocin basu yi soke ba, kuma da zaran ya bar filin, suka yi kokarin rushe aikinsa ta wurin barazana da rudu. Sau da yawa sun yi nasara. Ya ce: "Me za a yi? Yayin da nike shuka a waje daya, magabcin yana tarwasa wurin da na bari yanzu. Ba zan iya kasancewa ko ina ba. Kash! Da Kirista suna da Littafin a harsunansu da sun iya yin jayayya da makaryatan nan da kansu, in babu Littafin ba zai yiwu a karfafa mutane cikin gaskiyar ba."

Wata manufa kuma ta shiga tunaninsa yanzu. Ya ce; "Da harshen Israila ne aka raira zabura a haikalin Yahweh; ashe bishara ba za ta yi yaren Ingila a cikinmu ba? … Ko ya kamata ekklesiya ta kasance da hasken tsakar rana da bai kai na wayewan gari ba? Dole Krista su karanta Sabon Alkawali ciki harshensu." Likitoci da mallaman ekklesiya suka sami sabanin ra'ayi tsakaninsu. Ta wurin Littafin ne kadai mutane za su san gaskiya. "Wannan ya yarda da wannan likitan, wani kuma ya yarda da wani likitan…. Yanzu fa likitocin nan suna sabanin ra'ayi da juna. Ta yaya kenan za mu iya bambanta mai fadin gaskiya da mai kuskure?.... Ta yaya? ….Hakika tawurin maganar Allah."

Ba da jimawa ba ne bayan wannan da wani masani, likitan Katolika, cikin mahawara da shi yace; "Gara mu kasance ba dokar Allah da mu kasance ba dokar paparuma." Tyndale ya amsa: "Na kangare ma paparuma da dukan dokokinsa, kuma idan Allah ya kiyaye raina, cikin shekaru kadan zan sa yaron da ke rike garma ya san Littafin fiye da kai."

Manufar da ya fara sha'awarta, ta ba mutane Sabon Alkawali cikin harshensu, yanzu ta tabbata, kuma nan da nan ya shiga aikin. Da zalunci ya kore shi daga gidansa, sai ya je London, can kuma ya ci gaba da aikinsa babu tashin hankali. Amma kuma nuna karfi na 'yan paparuma ya sake tilasta shi ya gudu. Sai ka ce dukan Ingila ta tasam masa, sai ya kudurta neman mafaka a Jamus. Nan ne ya fara buga Sabon Alkawali cikin harshen Ingilishi, sau biyu aka tsayar da aikin, amma sa'anda aka hana shi bugawa a wani birni, yakan tafi wani birnin. Kuma a karshe ya je Worms, inda, shekaru kalilan da suka gabata, Luther ya kare bishara a gaban majalisar. A wannan birnin akwai abokan Canjin da yawa, can kuma Tyndale ya yi aikinsa, ba abu mai hanawa. Nan da nan Sabon Alkali guda dubu uku suka kare, wani sabon bugun kuma ya biyo baya cikin shekarar.

Ya ci gaba da aikinsa da himma sosai, duk da cewa hukumomin Ingila sun tsare tashoshin jiragen ruwansu sosai, maganar Allah ta shigo London ta hanyoyi daban dabam daga nan kuma aka bazu ko ina a kasar. Yan paparuma sun yi kokarin danne gaskiyar, amma a banza. A wani lokaci bishop na Durham ya sayi kowane Littafin da ke shagon wani abokin Tyndale da niyyar kone su, yana zato cewa wannan zai ja aikin baya. Amma, sabanin haka, kurdin da ya biya ne aka buga wani sabon bugun Littafin da shi, ingantace kuma wanda ba don kurdinsa ba, da ba a iya buga sabon ba. Sa'anda daga baya aka mai da Tyndale fursuna, an yi masa tayin samun yancinsa bisa sharadin cewa zai bayana sunayen wadanda suka taimake shi biyan kurdin buga littafansa. Ya amsa cewa bishop na Durham ya fi kowa, domin tawurin biyan kurdi mai yawa don littatafan da ba a saya ba ya taimake shi ya ci gaba da karfin hali sosai.

An bashe Tyndale a hannuwan magabtansa, a wani lokaci kuma ya sha kurkuku na watanni da yawa. Daga baya ya shaida bangaskiyarsa tawurin mutuwan don bangaskiyar, amma makamai da ya shirya sun taimaki wadansu sojoji yin yaki cikin dukan sararaki har zuwa lokacin mu ma.

Latimer ya rika wa'azi daga bagadi cewa ya kamata a rika karanta Littafin da harshen mutane. Ya ce ai mawallafin Littafin, "Allah ne da kansa," kuma Littafin yana da girma da dawamar shi mai wallafa ta din. "Kowane sarki, da majistare, da mai mulki…. Wajibi ne su yi biyayya ga …. Maganarsa mai-tsarki." "Kada mu bi wata barauniyar hanya, amma bari maganar Allah ta bishe mu: kada mu yi tafiya kamar kakanin mu, ko mu bidi abin da suka bida, amma mu yi abin da ya kamata da sun yi."

Barnes da Frith, amintattun abokan Tyndale, sun tashi domin su kare gaskiyar. Su Ridley da Cranmer suka bi. Shugabannin nan na Canjin Ingila masane ne, an kuma kakame yawancinsu sabo da himma ko ibada a ekklesiyar Rum. Sabaninsu da tsarin paparuma sakamakon sanin su na tsarin ne. Sanin su na asiran Babila ya bada karin iko ga shaidarsu game da Babila din.

Latimer ya ce: “yanzu zan yi wata tambaya da ba a saba yi ba. Wane ne bishop mafi himma a dukan Ingila?... Na ga kana ji, kuma kana sauraro cewa in fadi sunansa…. Zan fada maku: Shaitan ne…. Ba ya taba barin diocese dinsa; a kira shi duk lokacin da aka ga dama, yana gida kullum: kowane lokaci yana wurin aikinsa… Ba za a taba samun shi yana zaman banza ba, ina tabbatar maku. Inda Iblis ke da zama, can fa ban da littafai, sai dai kyandir, banda littafi, sai dai cazbi, ban da hasken bishara, sai dai hasken kyandir, I, da tsakar rana ma; banda giciyen Kristi, sai dai yankan aljihu na purgatory;… ban da suturta marasa tufafi, da matalauta da mara lafiya, sai dai yi ma gumaka ado da shafa ma wuraren horon mutane kayan ado; daukaka al’adun mutum da dokokinsa, kasa da al’adun Allah da maganarsa mafi tsarki ….da dai priestocin mu za su zama da himmar shuka masarar koyaswa mai kyau, kamar yadda Shaitan ke himmar shuka ciyayi da zawan.”

Baban kaidan da ‘yan Canjin nan suka rike - wadda Wycliffe da John Huss da Luther da Waldensiyawa da Zwingli suka rike - ita ce iko mara kuskure na Littafin a matsayinsa na ka’idan bangaskiya da ayuka. Sun ki yancin paparuma da majalisu da ubani da sarakuna su mallaki lamirin mutane a sha’anin addini. Littafi ne ikonsu, kuma da koyaswarsa suka rika gwada kowace koyaswa. Bangaskiya ga Allah da maganarsa ne suka rike mutanen nan da suka ba da rayukansu aka kashe su. Latimer ya ce ma abokan famansa: “Ku kasance da kyakyawar ta’aziya, yau za mu kunna kyandir a Ingila wadda, da yardar Allah ba za a taba bicewa ba.”

A Scotland, ba a taba rushe gaskiyan da Columba da abokan aikinsa suka baza kwata kwata ba. Daruruwan shekaru bayan ekklesiyoyin Ingila suka yarda da Rum, na Scotland suka rike yancinsu. Amma a karni na sha biyu an kafa tsarin paparuma a nan, inda ya fi na kowace kasa tsananin iko kuwa. Ba inda duhun ya fi baki. Duk da haka tsirkiyoyin haske suka rika ratsa duhun suna ba da begen zuwan rana. Yan Lellard da suka zo daga Ingila da Littafi tare da koyaswoyin Wycliffe, sun yi aiki sosai don kiyaye sanin bishara, kuma kowane karni an sami shaidu da wadanda aka kashe don bangaskiyarsu.

Budewar Babban Canjin ta zo tare da rubuce rubucen Luther, sa’annan da Sabon Alkawali na Turanci na Tyndale. Ba da sanin yan ekklesiyar Rum ba, yan sakon nan suka rika ketare duwatsu da kauyuka suna kunna tocilar gaskiya da aka kusa kangewa a Scotland, suna kuma warware aikin danniyar Rum na karni hudu.

Sa’annan jinin masu bangaskiya ya kara ma aikin karfi. Da shugabannin yan paparuman suka gane hadarin da ke barazana ga aikinsu, sai suka rika kashe wadansu ‘ya’yan Scotland mafi martaba da daukaka. Amma wannan bagadi ne suka kafa daga inda aka ji kalmomin shaidun nan da ke mutuwa, ko ina a kasar, wanda ya motsa rayukan mutanen da niyyar tube sarkokin Rum.

Hamilton da Wishart, ‘ya’yan sarauta masu halin martaba tare da almajirai talakawa da yawa sun ba da rayukansu aka kashe su. Amma daga tarin itache wutan da aka kona

Wishart, wani ya taho wanda wutan ba za ta kashe shi ba, wanda a kalkashin Allah zai yi ma tsarin paparuma a Scotland bugun ajali.

John Knox ya juya daga al'adu da shirin ekklesiya, ya shiga ci daga gaskiyar maganar Allah, kuma koyaswoyin Wishart sun tabbatar da kudurinsa na barin ekklesiyar Rum. Ya kuma hada kansa da 'yan Canjin da ake wa zalunci. Sa'anda abokansa suka roke shi ya zama mai wa'azi, ya yi sanyin gwiwa saboda nauyin aikin, kuma sai bayan kwanaki na ware kansa cikin bimbini da kansa sa'anan ya yarda. Amma da zaran ya karbi matsayin, ya ci gaba da himman tare da karfin zuciya ainun duk tsawon rayuwarsa. Wannan tsayayyen dan Canjin bai ji tsaron mutum ba. Wutar mutuwa dan bangaskiya ta dinga kara ingiza himmarsa ne ma. Ga gatarin azalumi da aka daga ta kusa da shi don a kashe shi, amma ya ci gaba yana rushe bautar gumaka dama da hagu.

Sa'anda ya zo fuska da fuska da sarauniyar Scotland, wadda a gabanta himmar shugabannin Kin ikon paparuma da yawa ta rika karewa, John Knox ya shaida gaskiya ba tantama. Lallashi bai canja shi ba; bai raunana sabo da barazana ba. Sarauniyar ta zarge shi da ridda. Ya koya ma mutane su karbi adinin da kasa ta hana, ta ce, kuma wai ta hakanan ya ketare umurnin Allah cewa talakawa su yi biyayya ga yayan sarakunansu. Knox ya amsa: "Kamar yadda addinin na kwarai bai sami karfinsa daga 'ya'yan sarakunan duniya ba ne, amma daga madawamin Allah kadai, haka ne bai wajaba ma talakawa su sifanta addininsu bisa ga marmarin yayan sarakunansu ba. Gama sau da yawa 'ya'yan sarakuna ne suke fin kowa rashin sanin addinin gaskiya na Allah…. Da dukan zuriyar Ibrahim yan addinin Fir'auna ne, wadda sun dade suna masa bauta, ya uwargida, da wane addini ne ke duniya a lokacin? Ko kuma da dukan mutane a zamanin manzanin yan addinin sarakunan Rum ne, da wace addini ne ya kasance a fuskar duniya?... Sabo da haka, uwargida, za ki iya ganewa cewa ba wajibi ne ga talakawa su bi addinin yayan sarakunansu ba, ko da shike an umurce su su yi masu biyayya."

Mary kuma ta ce: "Kana fassara Littafin ta wata hanya, su kuma (mallaman Roman Katolika) suna fassara shi ta wata hanya, wa zan gaskata; kuma wa zai yi hukumci? Dan Canjin ya amsa: "Ki gaskata Allah, wanda ke maganarsa a bayane, kuma ba wani abin da ya fi wanda maganar ke koya maki, kada ki gaskata wannan ko wancan. Maganar Allah a bayane take da kanta; kuma idan akwai shakka a wani wuri, Ruhu Mai-Tsarki, wanda ba ya taba jayayya da kansa, yakan fassara wurin a bayane a wadansu wuraren, ta yadda ba za a iske wata shakka kuma ba sai ga wadanda suka nace ma jahilci."

Irin gaskiyan da dan Canjin nan mara tsoro ya furta a kunnen sarauniya, a bakin ransa. Da wannan karfin halin ne ya rike manufarsa yana addu'a, yana kuma yake yaken Ubangiji, har sai da aka 'yantar da Scotland daga tsarin paparuma.

A Ingila, kafawar Kin ikon paparuma a matsayin addinin kasa ya rage zalunci, amma bai kawar da shi kwata kwata ba. Yayin da aka yi watsi da koyaswowi da yawa na Rum,

an kuma rike kamaninsu da yawa. An ki daukakar paparuma, amma a madadinsa an daukaka sarki a matsayin kan ekklesiya. A cikin hidimar ekklesiya an iske bambanci mai yawa daga tsabta da saukin kan bishara. Ba a rigaya an fahimci babban kaidan nan na yancin addini ba lokacin. Ko da shike jefi jefi ne shugabannin ‘yan Kin ikon paparuma suka yi anfani da irin muguntan da Rum ta yi anfani da su kan masu ridda, duk da haka ‘yancin kowane mutum ya yi sujada ga Allah bisa ga lamirinsa bai karbu ba. An bukaci kowa ya karbi koyaswa ya kuma bi matakan sujada da ekklesiyar da aka sani ta tsara. Waddanda basu bi ba sun sha zalunci har tsawon daruruwan shekaru.

A karni na sha bakwai an sallami dubban pastoci daga matsayinsu. An hana mutane halartar duk wani taro na addini sai dai wand ekklesiya ta amince da shi, in bah aka ba kuwa a fuskanci tara ko fursuna ko kora daga kasar. Amittantun mutanen nan da ba su iya rabuwa da taron sujada ga Allah ba ya zama masu tilas suka rika saduwa da sakon tsakanin gidaje da benen gidaje, wadansu lokuta ma a kurmi da stakar dare. A kurmin haikalin da Allah ya gina da kansa, ‘ya’yan nan na Ubangiji da aka warwatsar aka kuma tsananta, sukan taru don yin addu’a da yabo. Amma duk kokarin buyansu, da yawa sun wahala sabo da bangaskiyarsu. Gidajen kaso suka cika. Aka rarraba iyalai. Da yawa aka kore su zuwa wadansu kasashe dabam. Duk da haka Allah yana tare da mutanensa, kuma zalunci bai tsayar da shaidar su ba. Aka kori wadansu zuwa ketare can Amerika inda suka kafa harsashen yancin addini da ya zama ginshiki da abin daukakar kasar nan Amerika.

Kuma, kamar zamanin manzani, zalunci ya kara ci gaban bishara ne. A wani kurkuku mai ban kyama, cike da masu manyan laifuka, John Bunyan ya shaki iskar yanayin sama, kuma nan ne ya rubuta littafin nan nasa da ya kamanta tafiyar Kirista daga kasar hallaka zuwa birni na sama. Har sama da shekara dari biyar wannan littafin daga kurkukun Bedford ya rika magana ga zukatan mutane da iko na ban mamaki. Littattafan Bunyan, “Pilgrims Progress” da “Grace Abounding to the Chief of Sinners,” sun bi da mutane da yawa zuwa hanyar rai.

Baxterm Florrel, Alleine da wadansu kuma masu baiwa da ilimi da kwakwaran dandanon Kristoci sun tashi tsaye don kare bangaskiyar da aka taba ba sarkaka, aikin da mutanen nan da suka yi, wanda masu mulkin duniyan nan suka haramta, ba zai taba lalacewa ba. Littattafan Florrel, “Fountain of Life” da “Method of Grace” sun koya ma dubbai yadda za su mika ma Kristi tsaron rayukansu. Littafin Baxter, “Reformed Pastor,” ya zama albarka ga masu marmarin falkaswar maganar Allah, wani littafin sa kuma, “Saint’s Everlasting Rest” ya jawo mutane zuwa “hutun” da ya rage don mutanen Allah.

Bayan shekaru dari, Whitefield da yaran Wesley suka fito a matsayin masu kai hasken Allah. A kalkashin shugabancin ekklesiyar kasar, mutanen Ingila sun rigaya sun shiga yanayin sanyin addini da ya zama da wuya a bambanta shi da kafirci. Addini na halitta ya zama abin da masu bishara suka fi so su yi nazarinsa, kuma ya kunshi yawancin tauhidinsu. Manyan mutane suka rena ibada suna alfaharin cewa sun fi karfin tsanancin talakawa,

kuma jahilci ya sha kansu, suka zama masu mugunta, ekklesiya kuma ta rasa karfin zuciyar da za ta goyi bayan aikin gaskiya.

Muhimmin koyaswar barata ta wurin bangaskiya da Luther ya koyar, an kusan mantawa da ita gaba daya, koyaswar Rum ta dogara ga kyawawan ayuka kuma ta dauki wurin. Whitefield da yaran Wesley, membobin ekklesiyar kasa ne, amma amintattun masu neman yardar Allah, kuma an koya masu cewa za su sami aminciwar Allah tawurin rayuwa na halin kirki ne da kiyaye hidimomin addini.

Sa'anda Charles Wesley ya kamu da rashin lafiya, ya kuma ga kamar mutuwa tana zuwa, an tambaye shi a kan me ya dangana begensa na rai madawami. Ya amsa da cewa: "Na yi iyakar kokari na in bauta ma Allah" Sa'anda abokin da ya yi tambayar ya nuna kamar bai gamsu da amsar ba, Wesley ya yi tunani cewa: "Kai! Watau kokari na bai isa ya ba ni bege ba kenan? Yana so ya kwace kokarin nawa ne? Ba ni da wani abu dabam da zan dogara a kai kuma". Yawan duhun da ya mallaki ekklesiya kenan, ya boye kafara, ya kwace ma Kristi daukakarsa, ya kuma juya zukatan mutane daga begensu kadai na ceto, watau jinin mai fansa giciyayye.

An nuna ma Wesley da abokansa cewa addinin gaskiya yana cikin zuciya ne, kuma cewa dokar Allah ta shafi tunani har da kalmomi da ayuka kuma. Da suka amince cewa tsabtar zuciya da kyawawan halayyan da ake gani wajibi ne, sai suka dukufa neman sabuwar rayuwa. Ta wurin kwazo da addu'a suka yi kokarin danne muguntar zuciya ta mutumtakar; sun yi rayuwa ta musun-kai, da kauna, da kaskantar da kai, suna himma sosai wajen bin kowane matakin da suka ga kaman zai taimake su samun babban abin marmarinsu, watau tagomashi daga Allah. Amma basu sami abin da suka nema ba. A banza suka yi kokarin yantar da kansu daga hukumcin zunubi ko kuma su karya ikonsa. Fama dayan da Luther ya sha kenan a dakinsa a Erfurt. Tambaya dayan kenan da ta dami zuciyarsa. "Amma kaka mutum za shi barata wurin Allah? " Ayuba 9:2.

Wutan gaskiyar Allah da ta kusan mutuwa ta sake kunnuwa daga tocilan nan na da, wanda aka mika ma Kiristan Bohemia. Bayan Canjin, Kin bin ikon paparuma ya fatattaka a hannun dakarun Rum. Aka tilasta dukan wadanda suka ki rabuwa da bangaskiyarsu, suka gudu. Wadansun su suka sami mafaka a Saxony inda suka ci gaba da bangaskiya ta da din. Daga muryar wadanan Kiristan ne haske ya zo ma Wesley da abokansa.

Bayan an shafi John da Charles Wesley cikin aikin bishara, aka aike su aikin mishan a Amerika. cikin jirgin akwai 'yan Moravia an fuskanci munanan guguwa cikin tafiyar, sai John Wesley, da ya zo fuska da fuska da mutuwa, ya ji kawai ba shi da tabbacin salama da Allah. Akasin haka, Jamusawan suka nuna kwanciyar hankali da danganan da shi bai sani ba.

Ya ce: "Da dadewa kafin nan na lura da irin halayyansu. Sun nuna saukin kai kowane lokaci, ta wurin yi ma sauran fasinja irin ayukan bauta da yan Ingilishi ba za su yarda su yi

ba, basu kuma ce a biya su ba, suna cewa abinda suke yi yana da kyau don zukatansu na fahariya, kuma Mai-cetonsu mai kauna, ya yi masu abinda ya fi haka. Kowace rana kuma ta ba su damar nuna tawali'un da babu laifin da ke rage shi. Ko da an tura su, ko an buge su ko an jefar da su, sukan tashi ne su tafi abinsu, ba a ji kara daga bakinsu ba. Sai kuma zarafi ya zo don gwada ko an kubutar da su daga ruhun tsoro, da na girman rai ko fushi ko ramuwa. A tsakiyar wakar budewar sujadarsu sai teku ya rikice, ya tarwasa babban abin da ke sa iska ya sa jirgin ruwan ya ci gaba da tafiya, ya rufe jirgin, sa'anan ruwa ya fara zubowa cikin jirgin, sai ka ce tekun ya rigaya ya hadiye mu ne. Yan Ingila suka fara ihu mai yawa. Jamusawan nan suka ci gaba da wakarsu. Daga baya na tambayi dayansu, Ba ka ji tsoro ba? Ya amsa cewa, "Godiya ga Allah, babu! Na tambaye shi, "Amma matanku da 'ya'yanku basu ji tsoro ba?" Ya amsa a hankali cewa, 'Babu; matanmu da 'ya'yanmu ba sa tsoron mutuwa.'"

Sa'anda suka iso Savannah, Wesley ya zauna da yan Maravian nan na guntun lokaci, ya kuma yi sha'awar halayyansu na Kristanci sosai. Game da wata hidimarsu ta addini da ta bambanta da ta Ekklesiyar Ingila, ya rubuta; "Yawan saukin kai da kuma yin dukan hidimar ya kusa sa ni in manta shekaru dubu da dari bakwai da ke tsakani, na ga kaina kamar ina cikin taron nan da Bulus mai yin tent da Bitrus masunci suka shugabanta: ga Ruhu ga kuma iko."

Da ya koma Ingila, Wesley, tawurin koyaswar wani mai wa'azi dan Moravia, ya kara fahimtar bangaskiya ta Littafi. Ya gane cewa dole ne ya dena dogara ga ayukan kansa don ceto, ya kuma dogara ga "Dan rago na Allah mai dauke da zunubin duniya" kadai. A wani taron kungiyar yan Moravia a London, an karanta wata maganar Luther inda yake bayana Canjin da Ruhun Allah ke haifarwa cikin zuciyar mai bi. Yayin da Wesley ke sauraro, bangaskiya ta zo cikinsa, ya ce, "Na ji zuciya ta ta dimu sosai, na ji kawai na amince da Kristi, Kristi kadai, don ceto na: na kuma sami tabbaci cewa Kristi ya dauke zunubai na, ya kuma cece ni daga dokar zunubi da mutuwa."

Wesley da farko ya kwashe shekaru yana fama da musun kai da shan zargi da cin mutunci cikin kokarinsa na neman Allah. Yanzu ya same shi, ya gane kuma cewa alherin da ya yi ta faman nema ta wurin addu'a da azumi da ba da sadaka da musun kai, ashe kyauta ce, ba da kurdi ba, kuma ba da farashi ba.

Da ya kafu cikin bangaskiyar Kristi, ruhun sa ya motsu da marmarin baza sanin bisharar alherin Allah. Ya ce: "Ina ganin dukan duniya kamar coci na ne, duk inda nike, ina gani ya dace, kuma daidai ne, aiki na ne in shaida ma dukan wadanda suke so su ji labari mai dadi na ceto." Ya ci gaba da rayuwarsa ta musun kai, a matsayin sakamakon bangaskiya; ba tushen tsarkakewa ba, amma sakamakonsa. Alherin Allah cikin Kristi shi ne tushen begen Kirista, kuma za a nuna wannan alherin tawurin biyayya ne. Wesley ya ba da ransa ga wa'azin muhimman gaskiya da ya karba ne barata tawurin bangaskiya cikin

jinin kafara na Kristi, da kuma ikon sabontawa na Ruhu Mai-tsarki kan zuciya wanda ke haifar da ‘ya’ya ga rayuwar da ta yi daidai da kwatancin Kristi.

An shirya Whitefield da su Wesley domin aikinsu, tawurin ganewarsu da dadewa cewa su kan su batattu ne, kuma cewa za su iya jimre wahala kamar sojojin Kristi, sun rigaya sun sha ba’a da raini da zalunci, a jami’a da kuma sa’anda suke shiga aikin bishara. Su da wadansu kalilan da suka tausaya masu, yan’uwansu dalibai, marasa sanin Allah, suka rada masu sunar ba’a wai Methodist, sunan da a zamanin nan ake gani da daraje ga daya daga dariku mafi girma a Ingila da Amerika.

A matsayinsu na yan Ekklesiyar Ingila, sun manne ma tsare tsoranta na sujada sosai, amma Ubangiji ya nuna masu hanya mafi inganci cikin maganarsa. Ruhu Mai-Tsarki Ya umurce su su yi wa’azin Kristi giciyayye. Ikon Madaukaki ya bi aikinsu. Dubbai suka amince suka kuma tuba. Ya zama wajibi a tsare tumakin nan daga kerketai. Wesley bai yi tunanin kafa sabuwar darika ba, amma ya shirya su kalkashin abin da ya kira “Methodist Connection.”

Hamayyar da masu wa’azin nan suka fuskanta daga hannun ekklesiyar kasa babba ce mai ban mamaki kuma, duk da haka Allah cikin hikimarsa Ya canja alamura Ya sa canji ya fara daga cikin ekklesiyar kanta. Da daga waje kadai canjin ya zo, da bai shiga inda aka bukace shi sosai ba. Amma da shike masu wa’azin falkaswan yan ekklesiyar ne, kuma sun yi aiki cikin ekklesiyan ne duk inda suka sami zarafi, gaskiya ta sami shiga ta inda da kofofin sun kasance a kulle. Wadansu masu aikin bishara an falkas da su daga barcin ruhaniya suka zama masu wa’azi a ekklesiyoyin da suke mulki. Ekklesiyoyin da suka kangare cikin rashin ruhaniya suka falka.

A zamanin Wesley, kamar dukan sararakin tarihin ekklesiya mutane masu baye baye dabam dabam suka yi aikin da aka basu. Basu sami ra’ayi daya game da kowace koyaswa ba, amma Ruhun Allah Ya motsa kowa, suna kuma hada kai wajen ribato rayuka domin Kristi. Bambance bambance tsakanin Whitefield da yaran Wesley sun so su jawo rabuwa a wani lokaci, amma yanzu da suka koyi tawali’u a makarantar Kristi, hakuri da juna da kauna sun sasanta su. Ba su da lokacin jayayya yayinda kuskure da zunubi ke habaka ko ina, masu zunubi kuma suna nutsewa cikin hallaka.

Bayin Allah sun yi tafiya a mawuacin hanya ne. Masana da masu martaba suka yi anfani da ikonsu don sabani da su. Daga baya wadansu ma’aikatan bishara suka nuna magabtaka kwarai, aka kuma rufe kofofin ekklesiyoyi daga bangaskiya mara aibi da masu shelarta. Zarginsu daga bagadi da ma’aikatan bishara suka rika yi ya falkas da duhu da jahilci da zunubi. Akai akai John Wesley ya rika tsere ma mutuwa tawurin al’ajibin alherin Allah. Sa’anda aka ta da fushin yan iska a kansa, kuma ba alamar hanyar tsira, malaika cikin kamanin mutum yakan zo kusa da shi, yan iskan kuma sukan ja da baya, sai bawan Allah ya wuce lafiya daga wurin hatsarin.

Game da kubutarwarsa daga yan iska a wani lokacin, Wesley ya ce, “Da yawa sun yi kokarin tura ni a kasa yayin da muke gangarawa wata hanya mai-tsantsi zuwa garin, da sanin cewa idan har na kai kasa, ba zan tashi kuma ba. Amma ko tuntube ban yi ba, ko tsantsi ma bai ja ni ba, har na tsere gaba daya daga hannunsu … ko dashike da yawa sun so su kama kwala ta ko riga na, su ja ni kasa, basu iya rikewa ba sam: mutum daya ne kadai ya iya rike shafin kwat di na, na kuma bar mashi a hannunsa; daya shafin, inda akwai takardar kurdi, ya yage rabi ne kawai, wani mutum daga baya na ya yi ta duka na da katon sanda, wadda in da ya buga ni sau daya a keyata, da bai sha wani wahala kuma ba. Amma kowane lokaci, akan kawar da bugun, ban san ta yaya ba, don ban iya kaucewa dama ko hagu ba. Wani kuma ya zo a guje, ya kutsa ta cikin jama’ar, ya kuma daga hannu zai kai duka, amma kuma ya saukar nan da nan, sai dai ya shafa kai na ne kawai, yana cewa: “Ji laushin sumansa!” … Wadanda zukatansu suka fara tuba jarumawan garin ne, shugabannin yan iskan, dayansu kuwa shahararren mai fada ne a mashaya.…

“A hankali Allah ke shirya mu don nufinsa! Shekara biyu da suka wuce, wani gutsuren tubali ya kuje mani kafada, shekara daya bayansa, dutse ya buge ni a sakanin idanu na. Watan da ya wuce an naushe ni sau daya, da yamman nan ma na sami saushi biyu, daya kafin mu shigo gari, daya kuma bayan mun fita; amma dukansu biyu kamar ba komai ba ne: gama ko dashike wani mutum ya buge ni a kirji da dukan karfinsa, dayan kuma a baki da karfin da ya sa jini ya bulbulo nan da nan, ban ji zafin kowane bugun ba, kamar ma da tsinke suka taba ni.”

Yan Methodist na kwanakin farko, pastoci da membobi, sun sha wulakanci da zalunci a hannun membobin ekklesiya da marasa addini wadanda karyar membobin ta fusata. An gurbabar da su a gaban kotunan kasa, inda ba a cika samun adalci ba a wancan zamanin. Sau da yawa sun sha duka a hannun masu tsananta masu. ‘Yan iska sun dinga bi gida gida suna lalata kayan daki, da dukiya, suna kwasar ganiman duk abinda suka ga dama, suna kuma cin zarafin maza da mata da yara. A wadansu lokuta an rika manna sanarwa ga jama’a, ana kira ga masu so su taimaka wajen fasa tagogi da yin fashi a gidajen yan Methodist, su taru a wani wuri daidai wani lokaci. Ketarenwar dokokin mutum da na Allah hakanan sun rika faruwa ba tare da ko tsautawa ba. Aka rika cin zalin mutanen da laifinsu kadai shi ne kokarin da suka yi na kau da masu zunubi daga hanyar hallaka zuwa hanya mai-tsarki.

Game da zarge zargen da aka yi ma John Wesley da abokansa, ya ce: “Wadansu suna cewa koyaswoyin mutanen nan karya ne, kuskure ne, kuma sha’awa ce kawai; wai sabobi ne da ba a ta ba ji b a sai kwanan nan, cewa kowane bangaren koyaswan nan ainihin koyaswar littafi ne da ekklesiyarmu ta fasarta. Sabo da haka ba za ta zama karya ko kuskure ba, muddan dai Littafi gaskiya ce. “Wadansu suna cewa: ‘koyaswarsu ta cika tsanani; suna sa hanyar sama ta zama matsatsiya da yawa. ‘Da gaske kuma wannan ne ainihin zargin, kuma shi ne ginshikin zarge zarge dubu da ke daukan kamani dabam dabam. Amma tana

kara matsuwar hanyar sama fiye da yadda Ubangijinmu da manzaninsa suka tsara ta? Ko tasu koyaswa ta fi Littafin tsanani? A dubi nassosi kalilan kawai: ‘Ka yi kamnar Ubangiji Allahnka da dukan zuchiyarka, da dukan ranka, da dukan azanchinka; ‘kowace maganar banza da mutane ke fadi, a chikin ranar shari’a za su ba da lissafinta.’ ‘Ko kuna chi fa, ko kuna sha, ko kwa iyakar abinda ku ke yi, a yi duka domin a girmama Allah.’

“Idan koyaswarsu tafi wannan tsanani, laifinsu ne; amma kun sani cikin lamirinku cewa ba ta fi ba. Kuma wa zai yi karancin tsananin, komi kankanta, ba tare da lalata maganar Allah ba? Ko za a iske wani wakilin Allah da aminci idan ya canja wani fanni na ajiyan nan mai-tsarki? Babu. Ba zai iya rage komai ba, ba zai iya sassauta komai ba, ana bukatar shi ya sanar ma dukan mutane cewa, “Ba zan iya saukar da Littafin zuwa inda kuke so ba. Dole ku hau zuwa wurinsa, ko kuma ku hallaka har abada. Wannan ne ainihin dalilin abin da ake ta fadi game da rashin kauna da mutanen nan suke da shi. Rashin kauna, haka suke? Ta wace hanya? Ba sa ciyar da mayunwata, ba sa kuma suturta marasa tufafi? “Babu, ba maganan kenan ba: suna dukan wadannan: amma suna da rashin kauna wajen shar’anta mutane! Suna gani kamar ba wanda zai iya samun ceto sai ‘yan kungiyarsu.”

Lalacewar ruhaniya da ta mamaye Ingila gaf da lokacin Wesley sakamako ne na koyaswar cewa ta wurin bangaskiya kadai ake samun ceto, kuma wai ayukan kiyaye doka ba su da wani anfani ma game da ceto. Da yawa sun koyar da cewa Kristi ya warware dokoki goman anan, sa’an nan wai ba wajibi ne ga Kirista su kiyaye doka ba, cewa wai an yantar da mai ba da gaskiya daga “bautar nagargarun ayuka.” Wadansu da suka amince da dawamar dokar, suka koyar da cewa wai ba lallai ne ma’aikatan bishara su bukaci mutane su yi biyayya ga kaidodinta ba, da shike wadanda Allah ya zabe su sami ceto, tawurin alherin Allah wanda, ba za su iya ki ba, za a bishe su zuwa ayukan ibada da halayyan kirki, yayin da wadanda aka kadara zuwa ga hallaka ta har abada kuwa ba su da ikon yin biyayya ga dokar Allah.”

Wadansu da suka gaska ta cewa “zabbabu ba za su iya faduwa daga alherin Allah ko kuma su rasa tagomashin Allah ba,” sun kuma koyar da cewa “miyagun ayukan da su ke aikatawa ba zunubi ne ainihi ba, ko kuma abin da za a ce da su ketarewar dokar Allah, kuma cewa, saboda haka, ba su da dalilin furta zunubansu ko kuma su rabu da su ta wurin tuba.” Saboda haka suka sanar cewa ko daya daga zunubai mafi muni “wanda ko ina ana gani babban ketarewar dokar Allah ne, ba zunubi ne ba a ganin Allah,” idan daya daga cikin zabbabu ne ya aikata, “domin, daya daga cikin muhimman halayyan zababbu kenan da ya bambanta su, cewa ba za su iya yin wani abin da Allah ba ya so ko kuma doka ta hana ba.”

Wadannan munanan koyaswoyin daidai suke da koyaswar sananun mallamai da masanan hauhidi - cewa ba wata dokar Allah mara canjawa a matsayin ma’aunin cancanta, amma cewa jama’a ne kansu suke tsara ma’aunin cancanta, kuma a kullum ana canja shi.

Dukan wadannan ra'ayoyi ruhu dayan ne ke ba da su - shi wanda ko cikin mazamnan sama marasa zunubi, ya fara aikinsa na neman rushe kaidodi masu tsarki na dokar Allah.

Koyaswar cewa umurnin Allah yana kafa halayen mutane yadda ba za'a iya canjawa ba, ta kai mutane inda kusan sun ki dokar Allah ma. Wesley ya yi jayyaya da kurakuran masu koyar da zancen ceto tawurin alheri kawai, kuma doka ba ta da anfani, yak uma nuna cewa koyaswar ta saba ma Littafin. "Alherin Allah ya bayana, mai-kawo ceto ga dukan mutane" "Wannan mai-kyau ne abin karba kwa ga Allah mai chetonmu; shi wanda yake nufi dukan mutane su tsira, kuma su kawo ga sanin gaskiya. Gama akwai Allah daya, matsakanchi daya kuma tsakanin Allah da mutane, shi kwa mutum ne, Kristi Yesu wanda ya ba da kansa pansar dukan mutane." Titus 2:11; 1 Timothawus 2:3-6. Ana ba da Ruhun Allah kyauta domin kowane mutum shi iya kama hanyar ceto. Don haka, Kristi, hasken gaskiyan, "yana haskaka kowane mutum, yana zuwa chikin duniya." Yohanna 1:9. Mutane suna rasa cetonsu tawurin kin kyautar rai da su kansu suke yi ne.

Don amsa koyaswan nan cewa wai daga mutuwar Kristi an kawas da dokoki goman tare da dokokin bukukuwa, Wesley ya ce; "Dokoki goma din nan, wanda annbawa suka kiyaye, Allah bai kawar ba. Bai zo don warware su ba ne. Wannan kundin doka ne da ba za a iya karya shi ba, wanda ya tsaya sosai a matsayin amintacen shaida a sama… Wannan tun kafuwar duniya, aka rubuta shi, ba kan allon dutse ba, amma a zukutan dukan 'ya'yan mutane, sa'anda suka fito daga hannuwan mahalicin. Kuma komi yawan sharewa da zunubi ke yi ma bakaken da Allah ya rubuta da yatsansa, duk da haka ba za a iya share su gaba daya ba, muddan muna da sanin nagarta da mugunta. Dole kowane sashin dokan nan ya kasance da iko kan mutane duka, a dukan sararaki, cewa basu dangana ga lokaci ko wuri ba, ko kuma wani yanayi da kan iya canjawa ba, amma kan yanayin Allah, da yanayin mutum, da dangantakarsu da juna, mara sakewa.

"Ban zo domin in warware ba, amma domin in chichika." … Ba shakka, nufinsa a nan shine, Na zo domin in tabbatar da ita ne duk cikar ta, duk dai da dukan kyaliyar da mutane ke yi: na zo ne in bayyana a fili duk wani abinda ke da wuyan ganewa a ciki; na zo ne in bayyana ma'anar kowane bangarenta, in nuna tsawo da fadin kowane doka cikin kundin, da kuma bisa da zurfinta, tsarki da ruhaniyarta cikin kowane fanninta."

Wesley ya sanar da rashin sabanin doka da bishara. "Sabo da haka awai dangantaka mafi karfi tsakanin doka da bishara. A bangare guda dokar tana ba bishara fifiko, tana kuma nunawa zuwa ga bishewar, a daya bangaren kuma, bishara tana bishemu kullum zuwa ainihin cikawar dokar. Misali, dokar tana kai mu ga kaunar Allah ne, mu kaunaci makwabcin mu, mu zama masu tawali'u da saukin kai, ko tsarki. Muna gani kamar ba za mu iya yin wadannan ba, hakika kam, ga mutum, ba mai yiwuwa ba ne mamma Allah Ya yi alkawain ba mu kaunan nan, zai kuma mai da mu masu saukin kai da tawali'su da tsarki; sai mu kama bisharan nan, labarin nan mai dadi; akan yi mana bisa ga bangaskiyarmu ne; kuma adalcin dokar yana cika cikin mu tawurin bangaskiya da ke cikin Kristi Yesu ne.

Wesley yace: “Cikin mafi magabtaka da bisharar Kristi, akwai wadanda a fili suke shar’anta dokar kanta, suna neman zargin dokar; suna koya ma mutane su ketare dokokin gaba daya…. Mafi ban mamaki aikin Yahuda ya yi ne lokacin da ya ce, ‘A gaishe ka, Rabbi’, ya yi ta yi masa sumba, kuma Yesu zai iya ce ma kowane dayansu, ‘Da sumba ka ke chin amanar Dan mutum?’ Cin amanarsa da sumba ne idan an yi zancen jininsa, amma aka dauke rawaninsa, a rage karfin wani bangaren dokarsa, da sunan taimakon bishara. Kuma ba wanda zai kauce ma zargi nan idan yana wa’azin bangaskiya ta hanyar da ke soke zancen biyayya, idan yana wa’azin Kristi ta yadda yana soke mafi kankantar dokar Allah, ko rage karfinta.

Ga masu wa’azin cewa “wa’azin bishara yana amsa kowace doka,” Wesley ya amsa: “Ba mu yarda da wannan ba, sam. Bai amso manufar farko na dokar ma, watau, nuna ma mutane zunubin su, falkas da wadanda ke cikin barci gaf da lahira. “Manzo Bulus ya bayana cewa ta wurin doka ake sanin zunubi, kuma sai mutrun ya gane zunubinsa zai ji bukatarsa t jinin kafara na Kristi…. Ubangijinmu kansa ya ce: “Masu lafiya ba su da bukatar mai-magani ba; sai dai masu chiwuta.” Saboda haka ba daidai ba ne a mika ma masu lafiya mai-magani. Za ka fara tabbatar masu ne cewa suna da ciwo, in ba haka ba, ba za su gode maka da wahalar ka ba.

“Haka kuma kuskure ne a mika ma masu tsabtar rai Kristi, su kuwa basu ta ba ba,” sabo da haka yayin da yake wa’azin alherin Allah, Wesley, kamar mai-gadonsa, ya so ya dadada dokar ne ya girmama ta. Da aminci ya aiwatar da aikin da Allah ya ba shi, kuma sakamako masu daraja aka ba shi zarafin gani. A karshen rayuwarsa mai tsawon shekara tamanin - wanda yafi rabin karni yana aikin bishara - wadanda suka bayana goyon bayansu sun zarce mutum rabin miliyan.

Amma jama’a da tawrin aikinsa aka fitarda su daga hallakar zunubi zuwa rayuwa mafi inganci da tsarki, da wadanda tawurin koyaswarsa suka sami dandano mafi anfani da inganci, ba za a taba iya sanin yawansu ba, sai an tara dukan iyalin fansassu a mulkin Allah. Rayuwarsa darasi ne mai tamani mara iyaka ga kowane Kirista. Da dai ya iske irin bangaskiya da saukin kai, da himma da sadakar da kai da daukufar wannan bawan Allah cikin ekklesiyoyi na yau!

Babi na 15—Littafi da Juyin-Danwaken Faransa

Cikin karni na sha shidda, Canjin da ta gabagtar da budediyar Littafi ga duniya, ya so ya shiga dukan kasashen Turai, wadansu kasashe suka karbe shi da murna, kamar dan sakon sama. A wadansu kasashe, tsarin paparuma ta hana Canjin shiga sosai, hasken sanin Littafi kuma da tasirinsa, kadan kawai aka samu. A wata kasar, ko dashike hasken ya shiga, duhu bai fahimce shi ba. Gaskiya da kuskure sun dinga fadan neman fifiko. A karshe mugunta ta yi nasara, aka kuma jefar da gaskiya waje. “Shari’a fa kenan, haske ya zo chikin duniya, amma mutane suka fi son dufu da haske.”

Yakin da aka yi tsakanin Littafin a Faransa har tsawon daruruwan shekaru, ya kai ga Babban Tawayen nan. Mumunan al’amarin nan sakamoko ne kai tsaye na danne Littafin da Rum ta yi. Ya nuna a fili sakamakon manufar tsarin paparuma-kwatancin sakamakon da koyaswar ekklesiyar Rum ke shirgawa har tsawon shekaru dubu.

Annabawa sun yi annabcin dannewar Littafin a lokacin daukakar paparuma; mai ruya kuma ya nuna sakamakon da danniyar “mutumin zunubi” za ta jawo musanman ga Faransa.

Malaikan Ubangiji ya ce: “Gama an bayas ga al’ummai: za su tattake birni mai-tsarki kalkashin sawaye wata arba’in da biyu. Kuma zan ba shaiduna biyu iko, su yi annabci kuma kwana dubu da metin da sattin, a yafe chikin gwado…. Sa’anda suka gama shaidarsu kuma, bisan da ke fitowa daga chikin rami mara matuka za ya yi gaba da su, za ya rinjaye su, ya kashe su kuma. Gawansu kuma suna nan kwanche chikin karabkar babban birni, wand ake che da shi a ruahaniya Saduma da Masar, inda aka gichiye Ubangininsu kuma…. Kuma wadanda su ke zamane a duniya suna murna a kan su, suna ta nishatsi: za su aike da kyautai kuma zuwa ga junansu; domin wadannan annabawa biyu suka azabadda mazamnan duniya. Bayan kwana uku din da rabi, lumfashin rai daga wurin Allah ya shiga chikinsu, suka tsaya bisa kafafunsu; babban tsoro fa ya fada ma wadanda suka gan su.” Ruya 11:2; 11

Lokaci da aka ambata a nan - “wata arba’in da biyu” da “kwana dubu da metin da sattin” - daya ne, suna kuma matsayin likacin da ekklesiyar Kristi za ta sha danniya daga Rum. Shekaru 1260 na mulkin paparuma sun fara a AD 538 ne suka kuma kare a 1798. A wannan lokacin (1798) dakarun Faransa suka shiga Rum suka kuma mai da paparuma fursuna, ya kuma mutu cikin hijira, ko da shike an zabi sabon paparuma nan da nan, mulkin paparuma bai sake samun irin ikon da yake da shi da ba.

Tsananta ma ekklesiya bata ci gaba cikin dukan shekaru 1260 din ba. Allah cikin jinkansa ya takaita lokacin wahalar mutanensa. Sa’anda yake annabcin “kunchi mai girma” da zai abko ma ekklesiya, Mai- ceton ya ce: “kuma da ba domin mun gajartadda wadanan kwanaki ba, da ba mai-rai da za ya tsira ba: amma sabili da zababbu, za a gajertadda su.” Matta 24:22. Tawurin tasirin Canjin, tsanantawar ta kare kafin 1798.

Game da shaidu biyu din, annabin ya ce: “Wadannan su ne itatuwa noui na zaitun, da fitilla biyu suna tsaye a gaban Ubangijin duniya. “Maganarka fitilla che ga sawayena, haske ne kuma a tafarkina. Ruya 11:4; Zabura 119:105. Shaidu biyu din suna matsayin Tsohon Alkawali da Sabon Alkawali ne. Dukansu muhimman shaidu ne na tushen dokar Allah da dawamar ta kawai. Dukansu kuma shaidu ne na shirin ceto. Alamu da hadayu, da annabce annabcen Tsohon Alkawali suna nunawa zuwa ga Mai-ceto da za ya zo. Linjila da Wasikun Sabon Alkawali suna maganar Mai-ceto da ya zo daidai yadda alamu da annabci suka fada ne.

Za “su yi annabchi kuma kwana dubu da metin da sattin a yafe chikin gwado.” Yawancin wannan lokacin shaidun Allah sun kasance yanayin duhu-duhu. Mulkin paparuma ya so ya boye ma mutane maganar gaskiya, ya kuma ajiye shaidun karya a gabansu don karyata shaidar maganar gaskiyar. Sa’anda masu iko na addini da na kasa suka hana bazawar Littafin, sa’anda aka tankware shaidarsa, mutane da aljannu kuma suka yi iyakar kokari don juya zukatan mutane daga wurinta; sa’anda wadanda aka rika farautarta, masu shelarsa, ana cin amanarsu, ana azabar da su, ana kuma bizne su a kurkuku da ramuka ko kogon kasa, ana kashe su saboda bangaskiyarsu, ko kuma a tilasta su gudu zuwa sansani na duwatsu, a lokacin ne amintattun shaidun suka yi annabci yafe da gwado. Duk da haka suka ci gaba da shaidarsu duk tsawon shakaru 1260 din. A zamanu mafi duhu akwai amintattun mutane da suka kaunaci maganar Allah, suka kuma yi kishin daukakarsa. Ga wadannan amintattun bayin aka ba da hikima, da iko da karfi don sanar da gaskiyarsa cikin dukan wannan lokacin.

“Idan kwa kowane mutum yana so ya chiwuche su, wuta na fitowa daga bakinsu tana chinye makiyansu: idan kuma kowane mutum yana so ya chiwuce su, dole hakanan za a kashe shi.” Ruya 11:5. Mutane ba za su iya taka maganar Allah hakanan kawai ba sakamo ba. Surar karshe ta littafin Ruya ta bayana ma’anar wannan la’anar inda ta kai. “Ina shaida ma kowane mutum wanda yake jin zantattukan annabchi na wannan littafi, idan kowane mutum ya kara bisa garesu, Allah za ya kara masa alobai wadanda aka rubuta chikin wannan litaffi kuma idan kowanne mutum ya dauki wadansu daga chikin zantatukan litafin wannan annabchi, Allah za ya kawas da rabonsa daga chikin itache na rai, daga chikin birni mai-tsaarki kuma, watau daga chikin abin da aka rubuta chikin wannan litafi?” Ruya 22:18,19.

Irin kashedin da Allah ya ba mutane kenan don tsaronsu daga canja abin da Shi ya bayana ko kuma ya urmurta. Wannan la’anar sun shafi dukan wadanda tawurin tasirinsu suke sa wadansu su yi wasa da dokar Allah. Ya kamata kashedin nan su ba da tsoro ga masu cewa wai kiyayya ko rashin biyayya ga dokar Allah wani muhimmin abu ba ne. Dukan masu daukaka ra’ayinsu bisa abinda Allah ya bayana, dukan masu canja ma’anar maganar Allah don cim ma burin kansu, ko kuma domin daidaituwa da duniya suna jawo

ma kansu sakamako mai ban tsoro ne. Rubuttaciyar Kalmar dokar Allah, za ta gwada halin kowane mutum ta kuma hukumta wadanda ta iske da laifi.

“Sa’anda suka gama [suke karasa] shaidarsu.” Lokacin da shaidu biyu din za su yi annabci yafe da gwado ya kare a 1798 ne. Yayinda suka kusa karshen aikinsu cikin yanayin duhu-duhu, ikon da aka kamanta da “bisan da ke fitowa daga rami mara matuka,” zai yake su. A kasashen Turai da yawa, ikokin da suka yi mulkin ekklesiya da na kasa Shaitan ya yi daruruwan shekaru yana mulki kansu ta wurin tsarin paparuma. Amma a nan ana maganar bayanuwar wani iko ne na Shaitan.

Da manufar Rum ne ta kulle Littafin cikin wani harshe da ba a sani ba, a kuma boye shi daga mutane. Kalkashin mulkin ta shaidun sun yi annabci “yafe da gwado,” Amma wani ikon kuma — bisan nan daga rami mara matuka — zai taso, yay i yaki a fili kai tsaye ka maganar Allah. “Babban birnin,” “wadda a karabkar ta aka kashe shaidun, kuma inda gawansu suna kwance, a ruhaniya” shi ne Masar. A dukan al’ummai na tarihin Littafin, Masar ce ta fi musun kasancewar Allah Mai rai ta kuma yi tsayayya da umurninsa ba tsoro. Ba sarkin da ya taba gwada tawaye a fili da girman rai kuma sabanin ikon Allah kamar yadda sarkin Masar ya yi. Sa’anda Musa ya kawo masa sakon, a cikin sunan Ubangiji, Firauna ya amsa da alfarma cewa; “Wane ne Ubangiji, har da an ji muryatasa in saki Israila kuma? Ni ban san Ubangiji ba, ba kwa zan saki Israila ba.” Fitowa 5:2. Wannan kafirci ne, kuma al’ummar da aka misalta da Masar za ta furta irin bijirewan nan ma. Allah Mai-rai, ta kuma nuna wannan irin ruhun, na kafirci da tumbe. An kuma kamanta babban birnin na ruhaniyan da Saduma [Sodom]. Lalacewar Saduma wajen ketare dokar Allah ya fi bayanuwa musamman ta wajen fasikanci ne. Kuma wannan zunubin zai zama babba cikin halayyan al’ummar da za ta cika wannan nassin.

Bisa ga maganar annabin, sa’an nan, gaf da shekara ta 1798 wani mulki mai asali daga Shaitan da kuma irin halinsa, zai taso ya yi yaki da Littafin. Kuma a kasar da za a bice maganar Allah hakanan, za a ga kafircin Fir’auna da fasikancin Saduma.

Wannan anabcin ya cika daidai a tarihin Faransa. Lokacin Juyin danwaken, cikin 1793, “sau na fari duniya ta ji taron mutane, wadanda aka haife su aka kuma ilimantar da su cikin wayewan kai, masu cewa kuma wai suna da ‘yancin yin mulkin daya daga al’ummai mafi kyau a Turai, suka ta da muryarsu, suka ki gaskiya mafi girma da mutum ke karba ba hamayya, suka kuma ki bangaskiya da sujada ga Allah.” Faransa ce kadai al’ummar duniyan nan da maganar ta dace da ita, cewa kamar al’umma, ta daga hannun ta, ta yi tawaye a fili sabanin mahalicin dukan halitta. Akwai masu sabo da yawa, da kafirai da yawa, da kuma har yanzu akwai su a Ingila da Jamus, da Spain, da sauran wurare, amma Faransa ta yi suna a tarihin duniya a matsayin kasa daya tilo da, tawurin dokar Majalisar Dokokinta, ta furta cewa wai babu Allah, wadda kuma dukan mutanen da ke babban birnin kasar, tare da yawancin sauran mutanen, mata da maza, suka yi rawa suna waka da murna wajen amincewa da sanarwar.”

Faransa ta kuma nuna irin halayyan da suka bambanta Saduma. Lokacin juyin danwaken, an nuna yanayin fasikanci da lalacewar hali irin wadanda suka kawo hallaka ga biranen Saduma da Gomorrah. Mai-tarihin yana bayana kafirci da fasikancin Faransa yadda aka bayana a annabcin cewa; “Itace da dokokin nan game da addini, akwai dokar da ta rage dawamar aure-dangangaka mafi tsarki da yan Adam za su iya samu, wadda dawamar ta ke jawo karfafawar zaman tare, an rage ta, ta zama yarjejjeniya kawai mara dadewa, wadda mutum biyu za su iya sa hannum su kuma warware shi yadda suka ga dama. Ko da aljannu ne suka hada kai don gano hanya mafi tabbaaci don hallaka duk wani abu mai-tsarki, mai ban sha’awa ko mai dawama a rayuwar iyali, su kuma sami tabbaci cewa illar da suke so ta samu za ta dawama daga sara zuwa sara, aljannun nan da basu iya kirkiro wani shiri kamar rage darajar aure ba… Sophie Arnnoult, mai wasan kwaikwayo da ta yi suna tawurin ababan nuna hikima da takan rika fadi, da bayana irin auren nan “bukin zina mai-tsarki.”

“Inda aka giciye Ubangijinmu kuma” Faransa ta kuma cika wannan fannin annabcin. Ba kasar da aka fi nuna ruhun magabtaka da Kristi a fili. Ba kasar da gaskiya ta fuskanci jayayya mafi daci da mugunta. Cikin zaluncin da Faransa ta yi ma masu goyon bayan bishara, ta giciye Kristi tawurin giciye almajiransa.

Karni bayan karni aka rika zub da jinin tsarkaka. Sa’anda Waldensiyawa suka ba da rayukansu a kan duwatsun Piedment “domin maganar Allah da shairdar Yesu Kristi, yanuwansu Albigensiyawan Faransa ma sun ba da irin wannan shaidar na gaskiya. A zamanin Canjin an yi ta kashe almajiransu da azaba mai-tsanani. Sarakuna da fadawa, manyan mata da kananan ‘yan mata, abin alfarma da mutuncin kasar, sun kalli azabar wadanda aka kashe don Yesu. Hugeunots masu karfin zuciyan nan da suka sha fama don ‘yancin dan Adam mafi muhimanci, sun zub da jininsu a fagen fama da yawa. Aka mai da masu Kin ikon paparuma marasa bin doka, aka sa farashi a kansu, aka kuma yi farautarsu kamar namomin jeji.

“Ekklesiyar cikin Hamada,” watau tsirarun zuriyar Kiristan da suka rage a Faransa a karni na sha takwas, da suka buya a duwatsun kudu, sun rike sha’awarsu ta bangaskiyar Ubaninsu. Idan suka gwada saduwa da dare a gefen dutse ko cikin ciyawa, muggan dabbobi sukan kore su, ko kuma a ja su a kai wurin bauta har tsawon rayuwarsu. Yan Faransa mafi tsarki, mafi wayewa, mafi hikima kuma aka rika daure su da sarka cikin azaba mai-tsanani, a tsakanin mafasa da masu kisan kai. Wadanda aka tausaya masu aka rika harbinsu da bindiga har lahira yayinda suna durkushe suna addu’a, ba komai a hannunsu. Daruruwan tsofofi da mata da yara aka rika kashewa a wurin saduwarsu. Yayinda suke ketare wurin saduwansu, ba abin mamaki ba ne a iske “kasarsu da aka kankare da takobi da gatari da wutan yayi aka mai da shi wani babban daji mai fadi mara haske.” An tabka muguntan nan fa ba a zamanin jahalliya ba ne, amma a zamanin haske na Louis XIV. A lokacin, kimiyya

ta yadu, ilimi ya habaka, shugabannin kotu da na kasa masana ne masu kaifin baki, kuma suna yawan nuna cewa su masu tawaliu da kauna ne."

Amma mafi muni cikin laifuka da ayukan munanan sararakin shi ne kisan kiyashi na St. Batholomew. Har yanzu duniya tana tuna wannan mumunar mugunta mai ban kyama kuwa. Sarkin Faransa, da zugin Priestocin Rum, ya ba da yardarsa aka aikata wannan danyen aikin. Kararrawa aka rika bugawa da tsakar dare, alamar fara kashe kashen. An rika jan dubban masu Kin ikon paparuma daga barcinsu a gidajensu, ba zato ba tsamnni, aka dinga kashe su cikin ruwan sanyi.

Kamar yadda Kristi ya shugabanci mutanensa daga bautar Masar, haka kuma Shaitan ya shugabanci mutanensa cikin wannan mumunan aiki na kisan masu bangaskiya. Kwana bakwai ana kisan kiyashin nan a Paris, kuma ba a birnin kadai aka yi shi ba, amma bisa ga umurnin sarki musamman, an yi shi a larduna da garuruwan da aka iske 'yan Kin ikon paparuma ma. Ba a damu da shekaru ko jinsi ba. Ba a bar jinjiri ko tsoho ba. Atajiri da talaka, tsofafi da matasa, uwa da 'ya'ya, aka karkashe su duka. An ci gaba da kashe kashen nan ko ina a Faransa har tsawon wata biyu. Mutum dubu saba'in aka hallaka.

"Sa'anda labarin kisan ya kai Rum, ma'aikatan ekklesiya suka yi murna ba iyaka. Dan majalisar paparuma daga Lorraine ya ba dan sakon da ya kawo labarin ladar rawani dubu; shugaban St. Angelo ya yi ihun gaisuwar bangirma; aka buga kowace kararrawar coci, hasken wuta da aka rika kunnawa na tayoyi da sauransu ya mai da dare rana, kuma Gregory X111, tare da 'yan majalisa da wadansu shugabannin ekklesiya, suka yi jerin gwano zuwa majami'ar St. Louis, inda dan majalisar Lorraine ya raira yabon Allah…. aka manna lambar yabo don tuna kisan kiyashin, kuma a Vatican ana iya ganin zanen Vasari guda uku da ke bayyana harin a kan shugaban jiragen teku, da na sarkin a cikin majalisa yana shirya kisan, da kisan kan ta. Gregory ya aika ma Charles Furen Zinariya; wata hudu bayan kisan kuma, … ya saurari wa'azin wani priest dan Faransa inda ya yi magana game da ranan nan cike da murna da farinciki da uba mafi tsarki ya sami labarin, ya kuma shiga yanayin saduda don yin godiya ga Allah da St. Louis."

Ruhun da ya zuga kashe kashen St. Louis shi ne ya ruhu dayan da ya zuga ababan da aka yi lokacin juyin danwaken. Aka ce Yesu Kristi sojan gona ne, kuma taken kafiran Faransa a lokacin shi ne, "A murkushe Dan Banzan," watau Kristi kenan. Sabo na raini ga Allah, da mugunta na ban kyama, aka dinga yi tare, kuma aka girmama 'yan iska da 'yan banza da miyagu sosai. Cikin dukan wannan, Shaitan ne aka daukaka shi, amma Kristi cikin halayyansa na gaskiya da tsarki da kuma mara son kai, aka giciye Shi.

"Bisan da ke fitowa daga chikin rami mara matuka za ya yi gaba da su, za ya rinjaye su, ya kasha su kuma." Ikon kafirci da ya yi mulki a Faransa lokacin Juyin danwaken da mulkin razana, ya yi yaki da Allah da maganarsa da ba a taba ganin irinsa ba. Aka haramta sujada ga Allah. An kawas da ranar hutu ta mako makon a maimakon ta kuma aka kebe

kowace rana ta goma don shaye shaye da sabo. Aka haramta baptisma da cin jibi. Sanarwa da aka manna a wuraren biso suka rika nuna cewa mutuwa barci ne na har abada.

Sun ce tsoron Allah mafarin wauta ne ba mafarin ilimi ba. Aka haramta yin sujada na addini sai dai sujada ga 'yanci da kuma kasar. "Bishop na Paris bisa ga dokan kasa ne aka gabatar domin ya shugabanci wannan raini da abin kunya mafi muni da wata kasa ta taba aikatawa.… An kawo shi gaba da dukan girmamawa domin shi sanar ma taron cewa addinin da ya yi shekaru da yawa yana koyarwa rudu ne na priestanci wanda ba shi da tushe ko a tarihi ko a gaskiya mai tsarki. Ya musunci kasancewar Allahn da aka shafe shi ya yi masa sujada, ya kuma kebe kansa don sujada ga 'yanci da daidaito da nagarta da halin kirki. Sa'an nan ya aza lambobinsa na aikin ekklesiya a kan tebur, ya karbi rungumar yan-uwantaka daga shugaban Taron. Priestoci da yawa masu ridda suka bi kwatancinsa."

"Kuma wadanda suke zamne a duniya suna murna a kansu, suna ta nishatsi: za su aike da kyautai kuma zuwa ga junansu; domin wadannan annabawa biyu suka azabadda mazamanan duniya." Faransce shiru a titunan kasar, wadanda kuma suka ki jinin takura da bukatun dokar Allah suka ji dadi. Mutane suka rika kangare ma sanin sama a gaban jama'a. Kamar masu zunubi na da, suka ce; "kaka Allah ya sani? Da wani sani kuma a wurin madaukakin?" Zabura 73:11.

Da karfin zuciya irin na sabo, mai ban mamaki, daya daga cikin priestocin sabuwar kungiyar ya ce: "Allah, idan kana nan, ka rama ma sunanka da aka bata. Na kangare maka! Kana shiru; ba ka isa ka ture tsawanka ba. Bayan wannan wa zai gaskanta cewa kana nan?" Wannan daidai yake da maganar Fir'auna cewa: "Wane ne Ubangiji har da zan ji muryatasa?" "Ni ban san Ubangiji ba:"

"Wawa ya fadi chikin zuchiyatasa, Babu Allah." Zabura 14:1. Ubangiji kuma yana cewa game da masu kangare ma gaskiya: "Gama wautassu za ta bayana a sarari ga dukan mutane." II Timotawus 3:9. Bayan Faransa ta rabu da sujada ga Allah Mai-rai, madaukaki, madawami kuma, ba da jimawa ba kuwa ta shiga bautar gumaka, tawurin sujada ga allahr Basira, wata fasika kawai. Wannan kuma a majalisar wakilai na kasar, kuma mahukumta mafi girma na kasa da na dokoki suka yi! Mai tarihi ya ce: "daya daga bukukuwan wannan mahaukacin lokacin ba shi da makamanci wajen wauta hade da rashin ibada. Aka shigo da kungiyar wake wake da raye raye wajen Taron, bayan yan majalisan suka shigo ta jerin gwano suna raira wakar yabon 'yanci, suna kuma rakiyar abin sujadarsu nan gaba, watau wata mace cikin lullubi, wadda suka ba ta suna Allar Basira. Sa'anda aka kawo ta cikin wurin shaye shayen, aka bude ta, budewa na musamman, aka kuma ajiye ta a hannun daman shugaba, sai aka gane ta, cewa wata yarinya ce mai-rawa a wasannin kwaikwayo, macen nan da suka ce ta fi dacewa a matsayin wakiliyar basiran nan ce suke yi mata sujada, majalisar kasa ta Faransa ta yi mata mubaya'a.

“Wannan buki mara ibada ne, wanda isa a yi masa ba’a kuma, ya kasance da wani kamani, aka kuma sabonta nadawar Allar Basiran, ana kwaikwayon nadin, ko ina a kasar, a wuraren da mutanen suka so nuna cewa sun cika yan Juyin danwake ta kowace fuska.”

Mai shelan da ya gabatar da sujada ga Basira ya ce: “Masu yin dokoki! tsanancin ra’ayi ya kauce ya ba basira wuri. Idanunsu basu iya jimre walkiyar hasken ba. Yau jama’a da yawa sun taru a kalkashin rufin daki, suka nanata gaskiyar,” abin da ba a taba yi ba. A can Faransa mun yi bukin sujada ta gaskiyar - sujada ta yanci, sujada ta hikima. Can muka tsara fatar ci gaban Jamhurriyar. Can muka rabu da gumaka marasa rai, muka rungumi Hikima, gunkin nan da aka rayar; halitta mafi-kayu.”

Sa’anda aka kawo allar cikin Taron, mai-shelar ya rike ta a hannu, ya kuma juya ga jama’ar, ya ce: “Ya masu mutuwa, ku dena rawan jiki a gaban tsawan Allah mara iko da tsroron ku ya halita. Daga yanzu, kada ku yarda da wani Allah sai Basira. Ina mika maku gunkinsa mafi tsarki da martaba; in ya kama dole ku yi gumaka, ku yi hadayar ku ga irin wannan gunkin ne kadai.… ku fadi a gaban majalisar ‘yancin kai! Mayafin Basira!”

“Bayan shugaban ya rungumi allar, sai aka aza ta a kan wata mota mai-ban sha’awa, aka kewaye da ita cikin babban taron jama’a, zuwa babban majami’ar Notre Dame, domin ta dauki wurin Allah. Can aka aza ta kan babban bagadi, ta kuma karbi yabon dukan wadanda ke wurin.”

Jima kadan bayan wannan, aka bi da konawar Littafin. A wani lokacin, “Shahararriyar Kungiyar Ma’adanar Kayayyakin Tarihi” ta shiga babban dakin taron garin, tana cewa, “Lale Basira!” suna kuma dauke da guntayen burbushin littattafai da yawa da aka kona, ciki har da littattafan addu’a da na wakoki, da Tsohon Alkawali, da Sabon Alkawali “da cikin wuta suka yi kafara dukan wautan da suka sa ‘yan Adam suka aikata,” in ji shugaban.

Tsarin papaaruma ne ya fara aikin da kafirci ke karasawa. Manufafin Rum ne suke tanada yanayin jama’a da na siyasa da na addini da suka hanzarta rushewar Faransa. Yayin da marubuta ke rubutawa game da ababan ban kyama na Juyin Danwanken, sukan ce sarauta da ekklesiya ne ke da alhakin jawo laifukan nan. Ainihin gaskiya ma, alhakin yana wuyar ekklesiya ne. Tsarin paparuma ya rigaya ya bata tunanin sarakukan game da Canjin, cewa magabcin sarutasa ne, abin da kuwa ya jawo rashin jituwa da ya kashe salamar kasar da jituwarta. Rum ce ta haifar da mugunta mafi muni da duniya mafi daci da sarakuna suka rika aikatawa.

Ruhun ‘yanci ya tafi tare da Littafi. Duk inda aka karbi bishara, an falkas da tunanin mutanen. Suka fara watsar da sakokin da sun dade suna danne su cikin bautar jahilci da mugunta da camfi. Suka fara tunani da ayuka kamar mutane. Sarakunan sun ga wannan, suka fara rawan jiki saboda danniyarsu.

Rum ba ta yi jinkirin zuga tsoronsu mai-kishi ba. Paparuma ya ce ma mukaddashin sarkin Faransa a 1525, “Wannan haukan (watau Kin ikon paparuma) ba kawai zai rikitar da addini ya kusa rushe shi ba ne, amma har da dukan ikoki da masu sarauta, da dokoki da kungiyoyi, da mukamai ma.” Shekaru kalilan bayan haka, wani jami’in ‘yan paparuma ya gargadi sarkin cewa: “Mai-gida, kada a rude ka. ‘Yan Kin ikon paparuman nan za su wargaje dukan kaida ta kasa da ta addini,… Sarauta tana fuskantar hatsarin da ekklesiya ke fuskanta ne.… Dole kirkirowar sabon addini ya haifar da sabon gwamnati.” Masanan tauhidi kuma suka zuga kiyayyar mutanen ta wurin koyar da cewa wai koyaswar Kin ikon papruma tana “jan hankalin mutane zuwa sabobin ababa da wauta, tana kuma lalata ekklesiya da kasa ma.” Ta haka Rum ta yi nasarar hada gaba tsakanin Faransa da Canjin.” Don girmama sarauta da kiyaye fadawa da karfafa dokoki ne aka zare takobin zalunci a Faransa.

Shugabannin kasar basu hangi sakamakon wannan matakin ba. Da koyar da Littafin ya shuka kaidodin nan na adalci da kamewa da gaskiya da nagarta da soyayya wadanda kuwa su ne ginshikin ci gaban kasar “Adilchi yakan daukaka al’umma,” Gama kursiyi bisa adilchi yake kafuwa.” Misalai 14:34; 16:12. “Aikin adilchi kuma salama ne.” Sakamakon kuma, “kwanciyar rai da sakankanchewa har abada,” Ishaya 32:17. Wanda ya yi biyayya ga dokar Allah zai girmama ya kuma yi biyayya ga dokokin kasar sa. Wanda ke tsoron Allah zai girmama sarki cikin anfani da ikonsa yadda ya kamata. Amma Faransa ta haramta littafi, ta hana almajiransa anfani da shi. Karni bayan karni, mutane masu kaida da aminci, masu kaifin hikima da halin kirki, wadanda ke da kwarin gwiwan bayana ra’ayinsu, su kuma sha wahala saboda gaskiya, sun rika aikin bauta suka yi ta mutuwa ko kuma rubewa a cikin kurkuku ma. Dubban dubbai suka rika gudun hijira; hakan ya ci gaba fa har shekaru dari biyu da hamsin bayan farawar Canjin.

“Da wuya a sami wata sarar ‘yan Faransa da ba ta ga almajiran bishara suna gudu daga haukar fushin azalumin suna kuma tafiya tare da hikima da fasaha da kwazo da ado da suka kware a kai ba, don arzunta kasashen da suka ba su mafaka. Kuma daidai yadda suka inganta wadansu kasashe da baye baye masu kyau, daidai haka kuma suka raba kasarsu da baye bayen. In da dukan abin da aka kora daga Faransa sun kasance a kasar, da cikin shekaru dari uku din an yi anfani da kwarewar korarun game da masana’antu don aikin noma; kuma in da kwarewarsu ta fasaha ta ci gaba da inganta masan’antun kasar, in da cikin shekaru dari uku din nan, basirar su ta kirkirowar ababa ta ci gaba da habaka littattafai da inganta kimiyar, da hikimarsu ta ci gaba da ba da bishewa ga majalisun kasar, da karfin zuciyarsu kuma wajen yakokin kasar, da adalcin su wajen tsara dokokinta, addinin Littafin kuma yana karfafa kangado yana kuma mallakar lamirin mutanenta, ina yawan daukakan da da ya mamaye Faransa yau! Ina girma da yawan ci gaba da farincikin da ya kamata da kasar ta samu, kwatanci ga sauran al’ummai?

“Amma makauniyar rashin sassauci ta kori kowane mai koyar da nagarta, kowane jarumin oda, kowane amintacen mai-kare gadon saruta; ta ce ma mutane da da sun mai da kasarsu sananniya maidaukakiya a duniya, zabi wanda za ka samu: mutuwa ko gudun hijira. A karshe, rushewar kasar ta cika; ba sauran addinin da za a kai wurin kisa kuma, ba sauran kishin kasa da za a bi zuwa kora daga kasar. Kuma Juyin Danwaken da dukan muguntansa, shine ya zama sakamako.

u“Sa’anda Huguenots saka gud, Faransa ta rika lalacewa sosai. Birane masu ci gaba wajen masana’antu suka fara lalacewa, larduna masu yawan anfanin gona suka koma dazuzuka; rashin bisira da lalacewar halayen kirki suka dauki wurin ci gaba. Paris ya zama wani gidan bara mai fadi, an kuma kiyasta cewa sa’anda Juyin Danwaken ya fara, miskinai dubu dari biyu sun rika rayuwa ta wurin sadaka daga hannun sarkin. Yan Jesuits ne kadai suka sami ci gaba a kasar, yayinda ta ke rubewa, suka kuma yi mulki da zalunci na ban tsoro bisa ekklesiyoyi da makarantu da kurkuku.

Ya kamata da bishara ta kawo ma Faransa maganin matsalolin nan na siyasa da zamantakewa da suka razana kwarewar ma’aikatanta na addini da sarkinta, da masu yin dokokinta, a karshe suka kuma jefa kasar cikin rudani da hallaka. Amma kalkashin bishewar Rum, mutanen sun rasa darussan sadakar da kai da kauna mara son kai. An rigaya an janye su daga ayukan musun kai don anfanin wadansu. Mawadata basu sami tsautawa game da danniyar da suka yi ma matalauta ba, matalauta kuma basu sami taimako game da bautarsu da wulakancinsu ba. Son kan mawadata masu iko ya yi ta ci gaba akai akai a bayane. An yi daruruwan shekaru handama da almubazzarancin mawadata ya kai ga mumunar tsotsewar talaka. Masu arziki sun yi ma matalauta laifi, matalauta kuma suka ki jinin masu arziki.

A yawancin larduna, masu sarauta ne suka mallaki gidaje, talakawa kuma ‘yan haya ne kawai, sai abin da masu gidajensu suka ce masu, kuma dole su amince da abin da masu gidajen suka bukata daga wurinsu. Nawayar tokarar ekklesiya da kasa ta rataya a kafadar ma’aikata ne da talakawa da mahukuntan kasa da na ekklesiya suka aza masu haraji mai yawa sosai. “Gamsuwar masu sarauta ce aka mai da ita doka mafi daukaka; ko da manoma da talakawa sun fama da yawa, ba damuwar masu yi masu danniya ba ne…. Dole kowane lokaci mutanen su nemi sanin abin da mai gidan ke so. Rayuwar manoman ta kasance rayuwar aiki ne kullum cikin talauci kawai; idan har suka nuna damuwa ma, akan amsa masu da zagi ne da raini kuma. A kullum kotuna sukan saurari mai sarauta ne sabanin talaka; masu shari’a suka yi kaurin suna wajen karban cin hanci; kuma duk abin da mai sarauta ke so yakan sami goyon bayan doka a wannan tsarin. Daga harajin da jami’an kasa da na ekklesiya suka rika karba, ko rabi bai rika shiga baitulmalin kasa ko na ekklesiya ba ma. Sauran akan kashe wajen almubazzaranci ne da holewa kawai. Wadanda kuwa suka tsotse yan’uwansu hakanan an ware su daga biyan haraji, kuma doka da al’ada sun ba su

‘yancin samun kowane aiki a kasar. Masu gatan sun kai mutum dubu dari da hamsin kuma don gamsar da su miliyoyi suka kasance masu rayuwar kaskanci da rashin bege.”

Fada ta cika da holewa da almubazzaranci, tsakanin mutane da shugabbi babu yarda. Kowane matakin gwamnati akan dauka cewa dabara ce ta son kai kawai. Har sama da shekara hamsin kafin Juyin Danwaken, Louis XV ne ke kan gadon sarauta, wanda kuma ko a wadancan zamanu na mugunta an san shi sarki ne mai kiwuya da shashanci da fasikanci. Inda akwai lalatattun masu sarauta azalumai, da kuma matalautan talakawa jahilai, ga kasa cikin rashin kurdi, mutanen kuma kullum suna fushi, ba sai da idon annabci ba, za a hangi barkewar mumunar damuwa ba da dadewa ba. Game da gargadin mashawaransa sarkin yakan amsa: “A yi kokari a sa al’amura su ci gaba duk tsawon rayuwata; bayan mutuwata abinda zai faru ya faru.” A banza aka rika nuna cewa akwai bukatar canji. Ya ga matsalolin amma ba shi da karfin hali ko ikon fuskantarsu. Amsarsa cewa “Bayana, ambaliyar!” ta bayyana ainihin matsalar da ke jiran Faransa.

Tawurin anfani da kishin sarakuna da masu shugabanci, Rum ta sa su suka rike mutane cikin bautan, da sanin cewa wannan zai nakasa kasar, ita Rum kuma za ta daure shugabannin da mutanen cikin bautarta. Ta hangi cewa idan har za a rike mutane cikin bauta sosai, dole ne a takura ma tunaninsu; cewa hanya mafi tabbaci ta hana su tsere ma bautarsu ita ce a hana su iya samun ‘yanci. Munin lalacewar halin kirkinsu ya fi wahalarsu ta jiki muni sau dubu. Dashike an hana su Littafi an kuma bar su da koyaswar rashin sassauci da son kai, mutanen sun kasance cikin jahillci da camfi, suka kuma nutse cikin mugunta ta yadda ba su cancanci mulkin kansu ba.

Amma abida wannan ya haifar ya bambanta gaba daya daga abinda Rum ta nufa. Maimakon rike talakawa cikin amincewa da koyaswarta a makance, aikin ta ya mai da su kafirai ne ‘yan juyin danwake. Suka yi kyamar Romanci cewa tsarin priestoci ne kawai, sun ga masu aikin bishara suna da hannu cikin danniya da ake masu. Basu san wani Allah ba sai allan Rum, koyaswarta ne kadai addininsu. Sun dauka cewa handamarta da zaluncinta sakamakon Littafin ne, kuma ya ishe su. Rum ta yi karya game da halin Allah, ta kuma wofinta dokokinsa, yanzu kuma mutane suka ki Littafin da Mai-wallafa shi ma. Ta bukaci biyayya ga koyaswarta ko ta halin kaka, cewa haka Littafin ya ce. Saboda haka Voltaire da abokansa suka yi watsi da maganar Allah gaba daya, suka kuma baza dafin kafirci ko ina. Rum ta murkushe mutane kalkashin duddugenta na karfe; yanzu kuma mutane wulakanttattu, rusassu suka watsar da ka’ida. Sun fusata game da macucin da suka dade suna masa mubaya’a, suka kuma ki gaskiya da karya baki daya; bayin mugunta suka yi murna game da abin da suka ga kamar ‘yanci ne.

Da farkon Juyin Danwaken, da yardar sarki aka ba mutanen wakilci da ya fi na masu sarauta da ma’aikatan bishara gaba daya. Ta haka iko ya koma hannunsu, amma basu shirya anfani da shi da hikima da sassauci ba. Da marmarin magance laifukan da suka yi masu, suka kudurta sake tsarin zamantakewar jama’a. Jama’a cike da fushi, wadanda tutaninsu

ke cike da muguntan da aka masu, suka kudurta cewa za su juya yanayin wahala da ta kai makura, su kuma yi ramuwa a kan wadanda suka dauka cewa su ne sanadin wahalarsu. Wulakanttatun sun yi anfani da darasin da suka koya lokacin zalunci sai suka zama masu danniya ga wadanda suka yi masu danniya.

Faransa ta girbe jinin da ta shuka. Sakamakon amincewarta da mulkin Rum ya yi muni sosai. Wurin da Faransa a farkon Canjin nan, kalkashin tasirin Rum, ta kafa wurin kisa nan ne Juyin Danwaken ya kafa injin yanke kawunan mutane. Daidai inda aka kone masu Kin ikon paparuma na farko, a karni na sha shidda, nan aka fara yanke kawunan mutane da inji a karni na sha takwas. Ta wurin kin bishara, wadda da ta kawo warakar ta, Faransa ta bude kofar kafirci da hallaka. Sa'anda aka kawar da sassaucin dokar Allah, dokokin mutum suka kasa sassauta fushin 'yan Adam, kasar kuma ta ci gaba zuwa tawaye da hargitsi. Yaki da Littafin ya shigo da zamanin da a tarihin duniya aka ce da shi Mulkin Razana. Aka kori farinciki da salama daga zukatan mutane. Babu wanda ke da tsaro. Wanda ya yi nasara yau, gobe akan zarge shi, a hukumta shi, gwada karfi da sha'awa suka mamaye kasar.

An tilasta sarakuna da masu bishara da fadawa suka amince da muguntar mutanen da suka haukace. Kashe sarki da aka yi ya ta da marmarin su na ramuwa ne kawai; wadanda kuma suka umurta aka kashe shi, su ma an kashe su ba da jimawa ba. Aka kudurta kisar dukan wandanda aka zata ba sa goyon bayan Juyin Danwaken. Kurkuku suka cika, a wani lokacin ma akwai kamamu fiye da dubu dari biyu a cikinsu. Biranen kasar suka cika da al'amura masu ban kyama. Wata kungiyar 'yan Juyin Danwaken sukan yi sabani da wata kuma, kuma Faransa ta zama babbar fagen talakawa masu jayayya da juna, cike da fushi kuwa. "A Paris, wata rigima takan bi bayan wata, 'yan kasan kuma suka rarrabu cikin bangarori da yawa da burinsu kadai shi ne su murkushe juna." Domin kara masu damuwar kuma, kasar ta shiga mumunan yaki mai tsawo da manyan kasashen Turai. "Kasar ta kusa tsiyacewa, mayakan suka rika kukan cewa a biya su albashin baya da ba a biya su ba, 'yan Paris suna fama da yunwa, mafasa suka mai da larduna kango, wayewa kuma saura kadan kawai ta kare cikin rashin zaman lafiya."

Mutanen sun rigaya sun koyi darusan mugunta da zaluncin da Rum ta koyar. Ranar sakamako ta zo. Yanzu kuma ba almajiran Yesu aka jefa cikin kurkukum aka kuma kai su wurin kisa ba, wadannan sun hallaka ko an kore us daga kasar da dadewa. Yanzu Rum ta ji ikon kisa na wadanda ta koya masu su ji dadin zub da jini. "Kwatancin zaluncin da masu aikin ekklesiya a Faransa suka nuna na tsawon sararaki da yawa, shi ne yanzu kuma aka mayar masu babu sassauci. Katakai na kisa suka zama jajaye da jinin priestoci. Kurkuku da can baya suka cika da Huguenots yanzu suka cika da azalumansu. Ma'aikatan Roman Katolika suka dandana dukan azaban da ekklesiyarsu ta gana ma masu ridda."

"Sai kuma ga kwanakin suka zo da wata hukuma mafi jahilci ta aiwatar da kaidodi mafi muni, sa'anda ba wanda ya iya gaisuwa da makwabtansa ko kuma yin addu'a….ba tare da yiwuwar aikata laifin da horonsa kisa ne ba. Sa'anda yan lekan asiri suka buya a

kowane lungu; sa'anda injin yanke kawuna ya rika aiki kowace safiya, sa'anda kowane kurkuku ya cika makil kamar jirgin daukan bayi; sa'anda lambatu suka cika da kumfar jini da suka rika kwararowa zuwa cikin kogin Seine…. Yayin da aka rika wucewa da tarago bayan tarago cike da wadanda za a kashe, ana bi ta titunan Paris, jami'an da babban komiti ya aika zuwa bangarorin, suka rika tabka zaluncin da ko a babban birnin ma ba a taba ganin irinsa ba. Wukar injin yankan yi ta yi masu jinkirin yanka da yawa. Aka dinga yanke kamammu da yawa. Sai aka huda ramuka a gindin kowane kwalekwale cike da mutane. Aka mai da birnin Lyons Hamada. A birnin Arras kuma ko jinkai na mutuwa da wuri ba a ba fursunonin ba. Duk tsawon kogin Loire, daga Saumur zuwa teku, garkunan tsuntsaye suka rika buki akan gawaye a tattare. Ba a damu da jinsi ko shekaru ba. Yawan samari da 'yan mata 'yan wajen shekara sha bakwai da gwamnati ta karkashe ya kai daruruwa. Jarirai da aka fizge su daga nonon uwaye, akan dinga wurga su ana yayanke su da takobi akan ciyawa." Cikin shekara goma kadai jama'a da yawa suka hallaka.

Duk wannan yadda Shaitan ya so ke nan. Abin da ya yi sararraki yana so ya tabbatar an yi kenan. Hanyarsa rudu ne daga farko har karshe, kuma nufinsa ne kullum ya kawo ma mutane kaito da talauci, ya lalata ya kuma kazantar da aikin Allah, ya bata manufan Allah na kauna da halin kirki, ta haka kuma ya jawo bakinciki a sama. Sa'an nan tawurin karyarsa, yana makantar da tunanin mutane, ya sa su jefa laifin aikinsa a kan Allah, sai ka ce dukan wahalolin nan shirin Allah ne. Hakanan kuma, sa'anda wadanda aka wulakanta su aka kuma zalunce su ta wurin ikon sa suka sami 'yanci, yakan zuga su zuwa wuce gona da iri da kuma aikata laifuka. Sa'annan azalumai sukan nuna kamar hoton nan na rashin sassauci shaida ce ta sakamakon 'yanci.

Sa'anda aka gane wani salon kuskure, Shaitan yakan sake masa kama ne, jama'a kuma sukan karbe shi da marmari kamar karon farkon. Sa'anda mutanen suka gane cewa Rumanci rudu ne, ya ga kuma ba zai iya kai su ga ketare dokar Allah tawurin wannan hanyar ba, sai ya zuga su suka mai da kowane addini wai zamba ne, littafi, tatsuniya kuma; kuma sa'anda suka watsar da dokokin Allah, suka ba da kansu ga zunubi ba sassauci.

Babban kuskuren da ya jawo ma mazaman Faransa kaiton nan shi ne kyale gaskiya dayan nan da aka yi: cewa ainihin 'yanci yana cikin kaidodin dokar Allah ne. "Da ma ka yi sauraro ga dokoki na! da hakanan ne da salamakka ta yi kamar kogi, adilchinka kuma kamar rakuman teku." "Babu lafiya, in ji Ubangiji, ga masu mugunta." "Amma dukan wanda ya saurara gare ni za ya zamna da rai a kwanche, ba tsoron masifa ba." Ishaya 48:18, 22; Misalai 1:32.

Kafirai da masu ridda suna jayayya da dokar Allah; amma sakamakon tasirinsu yana nuna cewa zaman lafiyan mutum ya danganta ga biyayyarsa ga dokokin Allah ne. Wadanda ba za su karanta darasin daga maganar Allah ba, ana shawarta su su karanta shi cikin tarihin al'umma.

Sa’anda Shaitan ya yikokari tawurin ekklesiyar Rum ya kawar da mutane daga biyayya, ya boye wakilinsa, aikin sa kuma ya badda kama ta yadda ba a ga rage daraje da bakinciki da ya haifar kamar sakamakon ketare doka ne ba. Aikin Ruhun Allah kuma ya yi gaba da shi ta yadda aka hana manufofinsa haifar da dukan sakamakon da sanadinsa don gane tushen bakincikinsu ba. Amma a Juyin Danwaken, majalisar kasa ta kawar da dokar Allah kai tsaye a fili. Kuma cikin mulkin Razana da ya biyo baya, kowa ya ga yarda, sanadi ya jawo sakamako.

Sa’anda Faransa ta ki Allah a fili ta kuma kawas da Littafin, miyagun mutane da ruhohin duhu sun yi murnar samun mulkin da suka dade suna so - mulkin da babu hane hanen dokar Allah. Domin ba a aiwatar da hukumci nan da nan ba, “saboda haka zukatan yayan mutane suka ji karfin aika mugunta.” Mai-wa’azi 8:11. Amma ketare doka mai-adalci dole yakan kai ga bakinciki da hallaka. Ko da shike ba a hukunta muguntar mutane nan da nan ba, muguntar ta ci gaba da shirya hallakarsu. Daruruwan shekarun ridda da laifuka sun yi ta tattara fushi don ranar ramako; kuma sa’anda zunibinsa ya cika, masu raina Allah suka gane a makare cewa kure hakurin Allah da suka yi abin tsoro ne, Ruhun Allah wanda ke takura ma ikon muguntar Shaitan an cire shi, kuma shi wanda abin sonsa kadai shi ne bakincikin mutane ya sami damar aikata nufinsa. Wadanda suka zabi tawaye aka bar su su girbe ‘ya’yansa har sai an cika kasar da laifuka da ke da munin da ya fi karfin rubutawa. Daga rusassun larduna da birane aka ji mumunan kuka mai-daci, mai-zafi kuma. Faransa ta girgiza sai ka ce an yi rawan duniya. Addini, doka, oda, iyali, kasa, da ekklesiya, dukansu hannun nan na kafirci da aka daga don sabani da dokar Allah ya rusar da su. Mai-hikima ya ce: “Mugu za ya fadi tawurin muguntar kansa.” “Mai-zunubi ya yi mugunta so dari, har ma ya dade a duniya, duk da haka na sani lallai, wadanda ke tsoron Allah za su zama lafiya, masu ibada ke nan: amma babu lafiya ga miyagu.” Misalai 11:5. Mai-wa’azi 8:12,13. “Gama suka ki ilimi, basu zabi tsoron Ubangiji ba:” “Zasu fa chi alhakin hanyassa, su koshi da nasu dabarbaru.” Misalai 1:29, 31

Amittantun shaidun Allah da iko mai-sabon nan da ke tasowa daga rami mara matuka, ba za su dade suna shuru ba. “Bayan kwana uku din da rabi, lumfashin rai daga wurin Allah ya shiga chikinsu. Suka tsaya bisa kafafunsu; babban tsoro fa ya fada ma wadanda suka gansu” Ruya 11:11. Cikin 1793 ne dokokin da suka haramta addinin Kirista suka kuma kawar da Littafin, suka sami wucewa a Majalisar Faransa. Shekaru uku da rabi daga baya wani kudurin majalisa dayan ya warware wadancan dokokin, don haka aka ba Littafin dama. Duniya ta yi mamakin yawan girman laifin da ya taso daga kin Magana mai-tsarki, mutane kuma suka gane muhimmancin bangaskiya ga Allah da maganarsa a matsayin harsashen nagarta da halin kirki. In ji Ubangiji, “Wane ne ke nan ka yi masa zargi, ka sabe shi kuma? A kan wane ne kuma ka daukaka muryarka ka ta da idanunka sama kuma? Mai-tsarki ne na Israila.” Ishaya37:23. “Shi ya sa fa, yanzu so dayan nan zan sanashe su hannu na da iko na; za su kwa sani sunana Yahweh ne.” Irmiya 16:21.

Game da shaidu biyu din, annabin ya kuma ce: “Suka ji babban murya daga sama ta che masu, ku hau daga nan. Suka hau kuma zuwa chikin sama chikin girgijen: makiyansu kuma suna duban su.” Ruya 11:12. Tun da Faransa ta yi yaki da shidun Allah biyu din nan, an daukaka su fiye da duk yadda aka taba yi. A 1804 aka kafa kungiyar Littafin na Birtaniya da kasashen waje (British and Foreign Bible Society). Aka bi da kungiyoyi irin sa da ressa da yawa, a nahiyar Turai. A 1816 aka kafa “American Bible Society.” Sai aka buga aka kuma baza Littafin cikin harsuna hamsin. Yanzu ma an rigaya an juya shi zuwa daruruwan harsuna.

Cikin shekaru hamsin kafin 1792 ba a mai da hankali sosai ga aikin mishan na kasashen waje ba. Ba a kafa sabbin kungiyoyi ba, kuma ekklesiyoyi kalilan ne suka yi kokarin baza Kiristanci a kasashen kafirai. Amma kusa da karshen karni na sha takwas an sami babban canji. Mutane suka gane muhimmancin wahayin Allah da addini na tabbatar da abin da aka ji.

Daga wannan, lokacin aikin mishan na kasashen waje ya ci gaba sosai. Karin ingancin harkar buga littattafai ya kara ma aikin baza Littafin kwarin gwiwa. Karin hanyoyin sadarwa tsakanin kasashe dabam dabam, da rushewar shingayen wariya, da rashin ikon kasa da paparuma ya yi, sun bude hanya don shigowar maganar Allah. Shekaru da dama ana sayar da Littafin a titunan Rum ba takura, kuma yanzu an kai shi ko ina a duniya.

Kafirin nan Voltaire ya taba buga kirji ya ce: “Na gaji da jin mutane suna cewa wai mutum sha biyu ne suka kafa addinin Kirista. Ni zan nuna cewa mutum daya ya isa ya hambarar da shi.” Sararraki sun wuce bayan mutuwarsa. Miliyoyi sun sa hannu cikin yaki da Littafin. Amma maimakon hallaka shi, in da akwai Litattafai guda dari a zamanin Voltaire, yanzu akwai dubu goma, I, Littafin Allah guda dubu dari ma. Ta bakin wani dan Canji, game da ekklesiyar Kirista: “Littafin make ra ce da ta shude guduma da yawa.” In ji Ubangiji: “Babu alatun da aka halitta domin chiwutanki da za ya yi albarka; iyakar harshe kuma da za shi tashi gaba da ke, a shari’a za ki koyas da shi.” Ishaya 54:17. “Maganar Ubangiji za ta tsaya har abada.” “Dukan dokokinsa masu-aminchi ne. Sun kafu har abada abadin an gudana su chikin gaskiya da adalchi.” Ishaya 40:8; Zabura 111:7,8. Duk abin da aka gina bisa ikon mutum za a hambarar, amma abinda aka kafa bisa Dutsen maganar Allah zai tsaya ha abada.

Babi na 16—Ubani Matafiya

Yan Canjin Ingila, yayin da suka watsar da koyaswoyin Rum, sun rike siffofinta da yawa. Sabo da haka, ko da shike an ki ikon Rum da koyaswarta, an shigar da al'adunta da bukukuwanta cikin sujadar Ekklesiyar Ingila. An rika cewa wai wadannan ababa ba batutuwan lamiri ba ne, cewa ko da shike Littafin bai umurta a yi su ba, saboda haka kuma wauta ne su, duk da haka ba a hana su ba, don haka kuma su kansu ba mugunta ba ne. Kiyaye su ya rage banbancin da ya raba ekklesiyoyin da suka canja daga Rum, aka kuma ce wai za su taimaka wajen sa Rum ta karbi bangaskiyar masu Kin ikon paparuma.

Ga masu ra'ayin mazan jiya da masu son daidaitawa, wadannan ra'ayoyin sun nuna kamanin gaskiya. Amma akwai wata kungiya da bata yarda hakan ba. Zancen cewa al'adun nan "suna iya cire bambancin da ke tsakanin Rum da canjin" dalili ne da ya sa bai kamata a ci gaba da al'adun ba. Sun ga al'adun kamar alamun bautan da suka fito daga ciki wanda kuma basa sha'awar komawa ciki. Sun yi tunanin cewa Allah ya tanada kaidodin sujadarsa cikin maganarsa, kuma mutane ba su da yanci su kara a kansu ko su rage daga cikin su. Farkon babban riddar ita ce neman tokarar ikon Allah da ta ekklesiya. Rum ta fara da hana abin da Allah bai hana ba, ta kuma karasa da hana abinda Ya umurta a sarari.

Da yawa sun yi sha'awar komawa tsarki da saukin kan ekklesiyar farkon, sun mai da yawancin kafaffun al'adun Ekklesiyar Ingila tamkar al'adun bautar gumaka, kuma ba za su iya hada kai da su cikin sujada ba. Amma ekklesiyar, da goyon bayan hukumomin kasa, ba ta yarda da bambancin ra'ayi game da al'adunta ba. Akwai dokar da ta tilasta halartar sujada, ta kuma haramta duk-wani taron sujada ba tare da iznini ba, wanda ya yi kuma a jefa shi a kurkuku, ko a kore shi a kasar, ko a kashe shi.

A farkon karni na sha bakwai sarkin da ya fito hawa gadon sarautar Ingila ya sanar da niyyarsa ta sa masu ra'ayin tsabtata adini su "yi sauron ekklesiya ko a kore su daga kasar, ko ma abinda ya fi haka muni," Sa'an da aka rika farautarsu, ana zaluntarsu, anakuma tura su kurkuku, basu ga alamar gyara nan gaba ba, da yawa kuma suka yarda cewa ga dukan wadanda ke son bauta ma Allah bisa ga lamirinsu, Ingila ba wurin zama ba ne. Wadansu karshen ta suka bidi mafaka a Holland. An fuskanci wahaloli da hasara da kurkuku kuwa. Aka rushe manufofinsu, aka kuma bashe su a hannun magabtansu. Amma naciya ta yi nasara a karshe, suka kuma sami mafaka a jamhuriyar Holland.

Garin gudunsu, sun bar gidajen su da dukiya, da hanyar rayuwarsu. Suka zama baki a kasar bakunci, cikin mutane masu harshe dabam da al'adu dabam. Dole suka shiga sabobin hanyoyin neman abin zaman gari da ba su taba gwadawa ba. Mutane da duk rayuwarsu manema ne, yanzu suka fara koyon kanikanci. Amma da farinciki suka amince da sabon yanayinsu, maimakon zaman banza da gunaguni. Ko da shike talauci ya dinga damun su, sun gode ma Allah da albarkun da ya masu, suka yi farinciki da yancin sujadarsu, ba fitina.

“Sun san su baki ne, basu damu da komai ba sosai, amma suka dubi sama kamnataciyar kasarsu, suka kwantar da hankulansu.”

Cikin hijira da wahala kaunarsu da bangaskiyarsu sun kara karfi. Suka gaskata alkawuran Ubangiji, shi kuwa bai yashe su a lokacin bukatar su ba. Alaikunsa sun kasance tare da su don karfafa su da taimaka masu, suka tokare su kuma. Sa’anda kuma hannun Allah ya nuna masu ketaren teku, kasa inda za su kafa kasar kansu, su kuma bar ma ‘ya’yansu gadon ‘yancin ibada, suka ci gaba, ba da shakka ba, inda Allah Ya bi da su.

Allah Ya bar jarabobi suka abko ma mutanensa domin a shirya su cika nufinsa domin su. An kaskantar da ekklesiya domin a daukaka ta. Allah yana gaf da nuna ikonsa a madadin su, ya ba duniya wata shaida kuma cewa ba zai bar wadanda suka amince da Shi ba. Ya shirya al’amura ta yadda fushin Shaitan da dabarun miyagun mutane za su kawo ci gaban daukakarsa su kuma kawo mutanen Sa wurin tsaro. Zalunci da hijira sun bude hanyar yanci.

Sa’anda ya zama masu dole su rabu da Ekklesiyar Ingila, masu son tsarkin ekklesiyar suka dauki alkawali, kamar yantattun mutanen Ubangiji, za su “yi tafiya tare cikin dukan hanyoyinsa da aka sanar masu ko kuma za sanar masu.” Ainihin ruhun kaidar Kin ikon paparuma kenan. Da wannan manufan ne matafiyan nan suka bar Holland zuwa sabuwar duniya. Pastonsu John Robinson, wanda Allah ya hana shi tafiya tare da su, cikin jawabinsa na ban kwana dasu ya ce ma yan hijiran:

“Yan’uwa, yanzu za mu rabu, kuma Ubangiji ne Ya san ko zan sake ganin fuskokinku kuma. Amma ko Ubangiji Ya shirya haka ko babu, na gardade ku a gaban Allah da malaikunsa masu tsarki, ku bi ni daidai iyakar inda na bi Kristi kadai. Idan Allah Ya bayyana kansa gareku ta wurin wani kayan aikinsa kuma, ku kasance a shirye ku karbe shi kamar yadda kuka kasance a shirye ku karbi kowace gaskiya daga hidimata, gama na tabbata cewa Ubangiji yana da karin gaskiya da hasken da zai bayyana daga maganarsa mai-tsarki.”

“Ni kuma, na damu sosai game da yanayin ekklesiyoyin canjin, yadda suka kai wani zamani na addini, suka kuma kasa ci gaba fiye da lokacin canjinsu. Luthawa basu iya wuce abinda Luther ya gani ba, Calvinawa kuma, kun ga sun tsaya cik, inda shahararren mutumin Allahn nan da bai ga dukan ababa ba ya bar su. Wannan abin bakin ciki ne sosai, domin ko da shike su haske ne da ya haskaka a zamaninsu, duk da haka basu shiga cikin dukan hikimar Allah ba, amma da suna da rai yanzu da sun kasance a shirye su rungumi karin haske kamar yadda suka karbi na farkon.

“Ku tuna alkawalin ekklesiyarku, inda kuka yarda za ku yi tafiya cikin dukan hanyoyin Ubangiji da aka sanar da ku ko kuma za a sanar da ku. Ku tuna yarjejjeniyarku da Allah da juna kuma, cewa za ku karbi kowane haske da gaskiya da za a nuna maku daga rubutaciyar maganarsa, amma ku yi hankali, ina rokon ku, game da abinda za ku karba kamar gaskiya, ku gwada shi ku kuma auna shi da sauran nassosin gaskiya kafin ku karbe

shi, gama ba shi yiwuwa duniyar Krista ta fito ta fito kwanan nan daga irin bakin duhun nan na kin Kristi, a ce kuma an sami cikakken haske a lokaci daya."

Marmarin yancin lamiri, ne ya motsa matafiyan suka dauki kasadar doguwar tafiyan nan na ketarewar teku, suka jimre wahalolin jeji, kuma da albarkar Allah, suka shuka harsashen al'umma mai-girma a Amerika. Amma duk da amincinsu da tsaron Allah da suke da shi matafiyan basu rigaya suka fahimci babban kaidar 'yancin addini ba. Su basu kasance a shirye su ba wadansu 'yancin nan da suka sha wahalar samo ma kan su ba. Kalilan ne ke daga shahararun masana da masu halin kirki na karni na sha bakwai suka ainihin gane muhimmiyar kaidan nan, wadda ta fito daga Sabon Alakawali, wadda ta yarda da cewa Allah ne kadai mai shar'anta bangaskiyar "yan adam." Koyaswar cewa Allah Ya ba ekklesiya damar mallakar lamiri, ta kuma sansance ridda har ta hore shi, daya daga cikin kurakurai masu zurfi na tsarin paparuma ne. Yayin da 'yan canjin suka ki koyaswar Rum, ba su rabu da ruhun rashin hakuri ba. Bakin duhun da tsarin paparuma ya kunsa Kiristanci ciki a lokacin mulkin nan nasa mai-tsawo, bai gama shudewa ba a lokacin. In ji wani jagaban Pastocin Massacusetts, ya ce: "Hakuri da juna ne ya mai da duniya masu sabani da Kristi, kuma ekklesiya bata taba samun damuwa game da horon masu ridda ba." Makauratan suka yi wata doka cewa membobin Ekklesiya ne kadai za su iya yin magana a gwamnatin kasar. Aka kafa ekklesiya ta kasa, aka kuma bukaci dukan mutane su hada hannu don biyan bukatun masu aikin bishara, majistarori kuma aka ba su ikon ladabtar da masu ridda. Ta hakanan ikon kasa ya kasance a hannun ekklesiya. Ba da jimawa ba wadannan matakai suka haifar da sakamakonsu, watau zalunci.

Shekaru sha daya bayan an kafa kasar makaurata ta farko, Roger Williams ya zo Sabuwar Duniyar. Kamar matafiyan farkon, ya zo ne don ya mori 'yancin addini, amma ba kamar su ba, shi ya ga abinda kalilan ne daga cikinsu suka gani a zamaninsa, cewa 'yancin nan na kowa ne kuma ba za a iya kwace shi ba. Shi mai neman gaskiya ne da himma, kuma kamar Robinson, ya gaskata cewa ba shi yiwuwa a ce an rigaya an sami dukan haske daga maganar Allah. Williams ne "mutum na farko a Kristancin zamani da ya kafa gwamnatin kasa kan koyaswar 'yancin lamiri da daidaiton ra'ayi a doka." 'Ya ce aikin majistare ne ya hana aikata laifi, amma ba ya mallaki lamiri ba. Ya ce: "Majistarorin za su iya yanke hukunci game da haki tsakanin mutum da mutum, amma sa'anda suka yi kokarin umurta alhakin da ke wuyar mutum ga Allah, sun yi kuskure, kuma akwai hadari; gama a bayane yake cewa idan majistare yana da ikon nan, zai iya umurta wadansu ra'ayoyi ko koyaswoyi yau, gobe kuma ya canza su, kamar yadda sarakuna daban dabam da paparuma da majalisa daban dabam na ekklesiyar Rum suka yi a Ingila, ta yadda imani zai zama tarin rudani kawai."

Halartar sujadar ekklesiya ya zama dole a lokacin, in ba haka ba akwai biyan tara ko zuwa kurkuku. "Williams yaki dokar cewa ba ta da ma'ana, doka mafi muni a Ingila ita ce wadda ta umurta halartar sujada a majamiu. Ya ce tilasta mutane saduwa da wadanda

koyaswar su ba daya ba ta kawar da hakokinsu ne a sarari, tilasta kafirai da wadanda zuwa sujada tare da jama'a daidai yake da bidar riya daga gare su.… Ya kara da cewa, 'kada a tilasta ko wani yin sujada ko ci gaba da sujada ba da yardarsa ba.' Masu hamayya da shi cikin mamakin koyaswoyinsa suka ce: 'Kai! Ashe ma'aikaci bai isa ajiyarsa ba?' Ya amsa: "I, daga wadanda suka ba shi aikin.?"

An martaba Roger Williams aka kuma kaunace shi a matsayin amintacen ma'aikacin bishara, mai baye baye na musamman, mai aminci da kauna ta gaskiya; duk da haka ba a iya jimre yadda ya ki zancen ikon majistarori kan ekklesiya, ya kuma bidi 'yancin addini ba. Aka ce anfani da wannan sabuwar koyaswar zai "gurguntar da asalin kasar da gwamnatinta." Aka masa hukumcin kora daga kasar, a karshe kuma don kada a kama shi, dole ya gudu cikin sanyin guguwan lokacin dari, zuwa kurmin daji,

Ya ce: "Har mako sha hudu na sha fama cikin mawuyacin yanayi, ban san abinci ko wurin kwanciya ba." Amma "hankaku sun rika ciyar da ni a dajin," kuma ya rika samun mafaka a ramin wani itace. Ta haka ya ci gaba da gudu cikin kankara da jeji inda ba hanya, har sai da ya sami mafaka wajen wata kabilar Indiyawa da ya sami yarda da amincewarsu yayin da yake kokarin koya masu gaskiyar bishara.

Bayan wadansu watani, ya kai gabar tekun Narragansett inda ya kafa harsashen kasar farko a zamanin nan da ta fara amincewa da 'yancin addini. Babbar kaidar kasar Roger Williams ita ce "cewa kowane mutum shi sami 'yancin yin sujada ga Allah bisa ga hasken lamirinsa." 'Yar karamar kasarsa Tsibirin Rhode (Rhode Island), ta zama mafakar wulakantattu, ta kuma karu, ta ci gaba har sai da kaidodin tushenta, watau 'yancin kasa da na addini, suka zama ginshikin Jamhuriyar Amerika.

Cikin wannan babbar tsohuwar takarda da kakaninmu suka zana a matsayin kaidar 'yanci, watau Sanarwar 'Yancin Kai, suka sanar cewa: "Mun amince cewa gaskiyan nan a bayane suke, cewa an halici dukan mutane daidai ne; cewa mahalicinsu ya ba su wadansu 'yanci da ba za a iya karabewa ba; cewa cikinsu akwai rai, 'yanci, da neman farinciki." Kundin Tsarin Dokokin kuma a sarari ya lamunci cewa ba za a keta lamirin mutum ba. Ya ce: "Ba za a taba bidar gwadawa ta addini a matsayin sharadin samun wani mukami na kusa a haddadun Jihohin Amerika ba." "Majalisa ba za ta yi wata doka game da kafawar addini, ko hana 'yancin bin addinin ba."

"Masu tsara Kundin Tsarin Dokokin sun gane madawmiyar kaidan nan cewa dangantakar mutum da Allah ya fi karfin dokokin mutane, kuma hakkokin sa na addini ba za a iya karbewa ba. Ba sai an yi tunani kafin a tabbataar da wannan ba, yana hammatar mu, mun kuma san shi. Wannan sani, wanda baya kula dokokin mutane, shi ne dinga karfafa mutane da ake kashewa don ibadarsu, yayin da ake zaluntarsu, ana kuma kashe su. Suka ji cewa alhakinsu ga Allah ya fi karfin dokokin mutane, kuma mutum bai isa ya yi

iko bisa lamirin su ba. Kaida ce da ake haifar dan Adam da shi, wadda ba abin da zai kankare shi."

Sa'anda labari ya bazu cikin kasashen Turai, na wata kasa inda kowane mutum zai iya cin moriyar aikinsa ya kuma bi abin da lamirinsa ke fada masa, dubban mutane suka yi turruwa zuwa Sabuwar Duniyar. "Massacusetts, tawurin doka ta musamman, ta yi tayin kyautar maraba da taimako daga gwamnati ga Kiristan kowace kasa da za su ketare tekun Atlantic "don tsere ma yake yake ko yunwa, ko kuma danniyar azalumansu." Ta haka masu gudun da marasa gata suka zama bakin kasar, bisa ga doka." Shekaru ashirin daga ranan da aka fara zuwa suka sauka a Plymouth, wajen mutum dubu ashirin suka sauka a England (Sabuwar Ingila).

Domin cimma manufarsu, "suka gamsu da dan abin da ya isa ya rike su, tawurin rayuwar tsimi, da yin aiki. Basu bidi komi daga kasar ba sai dai sakamakon aikinsu. Ba abin da ya rude su….Suka gamsu da ci gaban kasarsu a hankali amma ba tsayawa. Da hakuri suka jimre wahalolin jejin, suna ban-ruwa ga itacen 'yanci da hawayensu, da kuma zufan fuskansu, har sai da tsaiwarsa ta yi zurfi cikin kasar."

Littafi ne ya zama harsashen bangaskiya, tushen hikima, da takardar sharuddan 'yanci. An rika koyar da kaidodinsa da himma a gidaje da makarantu da majmi'u, sukamakonsa kuma ya nuna halin tanadi da na basira da tsarki da kamewa. Mutum zai iya yin shekaru a garin masu son tsabtar addinin nan, "kuma ba zai ga mashayi, ko ya ji rantsuwa, ko ya sadu da mai-bara ba." Sun nuna cewa kaidodin Littafin ne suka fi tabbatar da girman al'umma. Kananan kasashen nan a rarrabe da juna, suka girma suka zama tarayyar jihohi masu karfi, duniya kuma cikin mamaki ta ga salama da ci gaban "ekklesiya mara paparum da kasa mara sarki."

Amma Karin mutane suka rika zuwa kasar Amerika, sabo da dalilai da suka bambanta da na matafiyan farkon. Ko dashike ainihin bangaskiya da tsabta sun nuna ikon sifantawa mai yawa, duk da haka tasirin ta ya rika raguwa akai akai sa'anda yawan masu zuwa sabo da dalilan abin duniya kadai ya dinga karuwa.

Ka'idan da masu zuwan farkon suka kafa, cewa membobin ekklesiya ne kadai za su iya jefa kuri'a ko su rike matasyi a gwamnatin kasar ta haifar da munanan sakamako sosai. Da an dauki matakin nan a matsayin hanyar kiyaye tsabtar kasar ne, amma sai ya jawo lalacewa ga ekklesiya. Da shike addini ne sharadin yin zabe da samun matsayi da yawa, domin son samun abin duniya kawai, suka hada kai da ekklesiya ba tare da sakewar zukatansu ba. Ta hakanan, ekklesiyoyin suka cika da mutanen da basu tuba ba; kuma ko cikin ma'aikatan ekklesiya ma an iske wadanda ban da ma kurkuran koyaswa da suke da shi, basu ma san ikon sabuntawa na Ruhu Mai-tsarki ba. Wannan kuma ya sake nuna miyagun sakamakon kokarin gina ekklesiya tawurin anfani da gwamnatin kasa, da kokarin anfani da ikon duniya don taimaka ma bisharar wanda ya ce: "Mulki na ba daga nan yake

ba.” Yohanna 18:36. Tun zamanin Constantine, har zuwa yau, ana wannan kuskuren kuwa. Hadin kan ekklesiya da kasa, komi kankantarsa, yayin da ake gani kamar yana kawo duniya kusa da ekkleisya, yana ainihin jawo ekklesiya kusa da duniya ne.

Muhimman kaidodin da Robinson da Roger Williams suka koyar, cewa gaskiya tana ci gaba ne, cewa Kirista ya kamata su kasance a shirye su karbi dukan hasken da zai haskaka daga magana mai-tsarki na Allah, zuriyarsu da suka biyo baya sun manta gaba daya. Ekklesiyoyin Amerika masu Kin ikon paparuma da na Turai ma, ga su dai sun sami tagomashi da suka karbi albarkun Canjin, amma suka kasa ci gaba da bin hanyar canji. Ko da shike amintattun mutane kalilan sun taso loto loto, suka yi shelar sabuwar gaskiyar, suka kuma bayana kuskuren da aka dade ana yi, yawanci, kamar Yahudawan zamanin Kristi, ko yan paparuman zamanin Luther, sun gamsu da irin bangaskiyar iyayensu, da kuma irin rayuwar iyayen na su. Don haka, addini ya sake lalacewa, ya zama al’ada, kurakurai kuma da camfe camfe da ya kamata da su kawas da su inda ekklesiya ta ci gaba da tafiya cikin hasken maganar Allah, aka rike su aka kuma so su. Ta hakanan ruhun da canjin ya kawo ya mutu a hankali, har sai da ka kai ga bukatar canji cikin ekklesiyoyin masu Kin ikon paparuma, kusan yadda aka bukata a ekklesiyar Rum a zamanin Luther. Aka iske son abin duniya, da sanya koyaswoyin maganar Allah da ra’ayoyin ‘yan Adam, irin na wancan zamanin.

Bazawar Littafin sosai a farkon karni na sha tara, da yawan hasken da wannan ya haskaka duniya da shi, ba a bi shi da ci gaban sanin gaskiya ko addini na aikatawa daidai da hasken da aka samu ba. Shaitan bai iya hana mutane maganar Allah kamar zamanin da ba; an rigaya an kai ta inda kowa zai iya samu, amma domin dai cim ma burinsa, ya sa mutane da yawa basu ba shi muhimmanci sosai ba. Mutane suka dena binciken Littafin, sabo da haka kuwa suka ci gaba suna yarda da fasarar karya, suna anfani da koyaswoyi marasa tushe daga Littafin.

Da ya gaza murkushe gaskiya tawurin zalunci, Shaitan ya koma ga sassauci da ya kai ga ridda da kafawar Ekklesiyan Rum. Ya sa Kirista suka hada kai da wadanda son abin duniya ya mai da su kamar masu bautar gumaka. Sakalamakon wannan hadin kai bai bambanta da na zamanin da ba; girman kai da almubazzaranci suka karu a sunan addini, ekklesiyoyi suka lalace. Shaitan ya ci gaba bata koyaswoyin Littafin, al’adu kuma suka habaka. Ekklesiya ta karfafa al’adun maimakon goyon bayan imani, wanda aka bayar ga tsarkaka so daya dungum. “Ta haka aka rage darajar kaidodin da yan Canjin suka wahala sosai a kai.

Babi na 17—Alkawuran Dawowan Kristi

Daya daga cikin gaskiya mafi saduda da daraja da aka bayana a Littafin shi ne na zuwan Kristi na biyu don karasa babban aikin nan na fansa. Ga mutanen Allah da suka dade cikin bakunci “ainihin wurin mutuwa da inuwatta,” aka ba da bege mai kawo murna cikin alkawalin bayyanuwarsa, wanda Shi ne tashin matattu, Shi ne rai, domin ya dawo da horraru gida. Koyaswar zuwan Yesu na biyu ita ce cibiya cikin Littafin. Daga ranan da Adamu da Hawa’u suka fita daga Adnin, masu bangaskiya suna sauraron zuwan Yesu domin ya karya ikon mai-hallakasuwan, ya kuma sake dawo da su paradise da suka rasa. Mutanen da masu tsarki sun yi sauraron zuwan Masiya cikin daukaka, domin cikar begensu. Enoch (Ahnuhu) na bakwai cikin zuriyar Adamu da Hawa’u, shi wanda ya yi tafiya da Allah har shekaru dari uku, aka ba shi damar hangen zuwan Mai-kubutarwan. Ya ce: “Ku duba ga Ubangiji ya zo da rundunan tsarkakansa, garin ya hukumta shari’a bisa dukan mutane.” Yahuda 14:15. Ayuba kuma a daren azabarsa, da cikakkiyar bangaskiya ya ce: “Gama na sami mai-pansana yana da rai, a karshe kuma za ya tsaya a bisa duniya.… Zan kwa gan shi, ni kai na, yana goya bayana, idanuna za su gan shi, ba kwa kamar bako ba.” Ayuba 19:25-27.

Zuwan Kristi domin shigo da mulkin adalci ya motsa rubutu da yawa mafi ban sha’awa da aka yi a cikin Littafin. Annabawan suka rika magana game da shi cikin kalmomi masu walkiya da wutar samaniya. Mai-zabinta ya raira game da iko da martabar Sarkin Israila: “Allah ya bullo da haske daga chikin Sihiyona, na kamilin jamali. Allahnmu yana zuwa, ba kwa za ya yi shuru ba…. Za ya kira sammai daga bisa, za ya kira duniya kuma, domin ya yi ma mutanensa shari’a” Zabura 50:2-4. “Bari sammai su yi murna, duniya kwa ta yi farin zuchiya:… A gaban Ubangiji, gama yana zuwa: yana zuwa domin ya shara’anta duniya da adilchi, al’umai kuma da aminchinsa.” Zabura 96:11-13.

In ji annabi Ishaya: “Ku falka ku raira waka, ku da ke zamne chikin turbaya: gama rabarka rabar haske che, kasa kwa za ta fitasda matattu.” “Ya hadiye mutuwa har abada: Ubangiji Yahweh zaya shafe hawaye daga dukan fuskoki.” Za ya kuma kawasda zargin mutanensa daga dukan duniya: gama Ubangiji ya fadi. A ranan nan fa za ya che, Ga shi wannan Allahnmu ne; mun jirashe shi, za mu yi murna, mu yi farinchiki chikin chetonsa.” Ishaya 26:19; 25:8,9.

Habakuk kuma, cikin wahayi mai-tsarki, ya hangi bayanuwarsa. “Allah ya zo daga Teman, mai-tsarki kuma daga dutsen Paran. Darajatasa ta rufe sammai, duniya kwa ta chika da yabonsa. Shekinsa yana kama da haske.” “Ya staya ya auna duniya; ya duba, ya kori al’umamai ya warwatsa su; madawaman duwatsu kuma suka warwatsu, tuddai na fil’azal suka sunkuya; tafarkunsa na tun zamanu ne.” “Har da ka hau dawakanka, bisa karusanka na cheto.” “Duwatsu suka gan ka, suka ji tsoro;…zurfafa suka furta murya, suka tada hannuwansu sama. Rana da wata suka tsaya kurum a mazamninsu; da ganin hasken

kibawanka yayinda, suke tafiya, da shekin mashinka mai-walkiya." "Ka fita domin cheton mutanenka, domin cheton shafaffenka." Habakuk 3:3,4,6,8,10,11,13.

Sa'anda an kusa raba Mai-ceto da almajiransa, ya ta'azantar da su cikin bakinchikinsu da tabbacin cewa za ya zo: "Kada zuchiyarku ta bachi;… A chikin gidan Ubana akwai wurin zama da yawa… zan tafi garin in shirya maku wuri, kadan na tafi na shirya maku wuri kuma, sai in sake dawowa, in karbe ku wurin kaina," Yohanna 14:1-3. "Dan mutum za ya zo chikin darajassa, da dukan malaiku tare da shi." "Sa'an nan za ya zamna bisa kursiyin darajassa: a gabansa kuma za a tattara dukan al'ummai." Matta 25:31,32.

Malaikun da suka kasance a kan Dutsen Zaitun bayan tafiyar Kristi zuwa sama, sun maimaita ma almajiran alkawalin dawowansa: "Wannan Yesu wanda aka dauke shi daga wurinku aka karbe shi sama, kamar yadda kuka ga tafiyatasa zuwa chikin sama, hakanan za shi dawo." Ayukan 1:11. Manzo Bulus kuma ya shaida cewa; "Gama Ubangiji da kansa za ya sabko daga sama, da kira mai-karfi, da muryar sarkin malaiku, da kafon Allah kuma." Tassalunikawa 1 4:16. Annabin Patmos ya ce: "Ga shi yana zuwa tare da gajimarai; kowane ido kuma za ya gan shi." Ruya 1:7.

Zuwansa ne zai kawo "mayasda kowane abu, abin da Allah ya ambata ta bakin annabawansa masu tsarki wadanda ke tun farkon duniya." Ayukan 3:21. Sa'anan za a karye mulkin mugunta, "mulkin duniya ya zama na Ubangijinmu da na Kristinsa: za ya yi mulki kuma har zuwa zamanun zamani." Ruya 11:15. "Daukakar Ubangiji kuma za ta bayana, masu rai duka kuma za su ganta baki daya." "Ubangiji Yahweh za ya sa adilchi da yabo su tsiro a gaban dukan-al'ummai za ya zama "kambi na daraja, da rawani na jamali ga ringin mutanensa." Ishaya 40:5; 61:11; 28:5.

Lokachin ne za a kafa mulkin Masiya mai-ban sha'awa da salama da aka dade ana begensa. "Ubangiji za ya ta'azantadda Sihiyona: ya ta'azantadda dukan kufaifanta, ya maida jejinta kamar Eden, hamadatta kuma kamar gonar Ubangiji." "Daukaka ta Lebanon za a bayas a gareta, mafificiyar daraja ta Karmel da Sharon." "Ba za a kara che da ke yasashiya ba: ba kwa za a kara fadin kasarki Risbewa ba, amma za a che da ke Daulata, kasarki kuma amrarriya." "Kamar yadda ango yakan yi farinchiki da amarya, hakanan Allahnki za ya yi farinchiki da ke." Ishaya 51:3; 35:2; 62:4,5.

A dukan sararraki zuwan Ubangiji ne begen ainihin masu binsa. Alkawalin ban kwana na Mai-ceton a Dutsen zaitun, cewa zai sake zuwa, ya haskaka ma almajiransa gaba, ya cika zukatansu da murna da begen da bakinciki bai iya bicewa ba, wahaloli kuma basu iya duhuntawa ba. Cikin wahala da zalunci, "bayanuwar darajar Allahnmu mai-girma mai-cetonmu kuma Yesu Kristi" ne ta kasance "begen nan mai-albarka." Sa'anda kristan Tassalunika suka cika da bakinciki, yayin da suke bizne kaunattatunsu da suka yi begen kasancewa a raye su ga zuwan Ubangiji, Bulus ya ja hankalinsu ga tashin matattu, da zai faru lokacin zuwan Mai-ceto. Sa'an nan matattu cikin Kristi za su tashi, a kuma wanzar da

su tare da masu rai su sadu da Ubangiji a sararin sama. Ya ce: “Hakanan za mu zauna har abada tare da Ubangiji. Domin wannan fa ku yi ma junanku ta’aziya da wadannan Magana.” Tassalunikawa I, 4:16-18.

A Patmos kaunatacen almajirin ya ji alkawalin, “ina zuwa da samri,” amsarsa kuma ta bayana addu’ar ekklesiya cikin dukan tafiyarta, “Amin: ka zo ya Ubangiji, Yesu.” Ruya 22:20. Daga kurkuku da wuraren kisa inda tsarkaka da wadanda aka kashe don bangaskiyarsu suka shaida gaskiya, ana samun furcin bangaskiya da begensu. Wani Kirista ya ce: “Da shike suna da tabbacin tashinsa, da kuma tashinsu lokacin zuwansa, saboda haka, suna raina mutuwa, suka kuma fi karfinta.” Sun yarda su je kabari domin su tashi ‘yantattu. Sun yi begen zuwan Ubangiji daga sama da darajar Ubansa, da zai kawo ma tsarkaka mulkinsa, Waldensiyawa ma sun yi marmarin wannan. Wycliffe ya yi begen bayanuwar Mai-fansa, begen ekklesiya.

Luther ya ce: “Na tabbata cewa ranar hukumci za ta iso kafin cikar shekaru dari uku. Allah ba zai iya barin muguwar duniyan nan ta fi haka dadewa ba.” “Babbar ranar tana kusatowa da za a hambarar da mulkin haram.”

In ji Melanchthon, “Tsohuwar duniyan nan ba ta yi nisa da karshen ta ba.” Calvin ya bukaci Krista kada su “yi jinkiri, suna marmarin ranar zuwan Kristi, rana mafi muhimmanci,” Ya kuma ce: “dukan iyalin amintattu zai yi jira don wannan ranar.” “Dole mu yi marmarin Kristi, dole mu nema, mu yi bimbini, har wannan babban ranar, sa’anda Ubangijinmu za ya bayana dukan darajar mulkinsa.”

Knox ya ce: “Ba Ubangiji Yesu ya dauki nman mu zuwa sama ba? Kuma ba zai dawo ba? Mun san cewa za ya dawo, da sauri kuma.” Ridley da Latimer da suka ba da rayukansu saboda gaskiya sun yi begen zuwan Ubangiji, cikin bangaskiya. Ridley ya rubuta: “Babu shakka duniya, na gaskata, don haka ni ke fadi, ta kusa karshenta. Tare da Yohanna bawan Allah bari mu yi kuka cikin zukatanmu ga mai-cetonmu Kristi, Ka zo, Ubangiji Yesu, ka zo.” Baxter ya ce: “Tunanin zuwan Ubangiji yana da dadi da farinciki gareni.” Aikin bangaskiya da halin tsarkakansa ne su yi kaunar bayanuwarsa, su kuma nemi bege mai albarkan nan.” Idan mutuwa ce magabci na karshe da za a hallaka lokacin tashin matattu, za mu ga yadda ya kamata masu ba da gaskia su yi marmari su kuma yi addu’a sosai domin zuwan Kristi na biyu, sa’anda za a yi wannan cikakkiyar nasara ta karshe.”

Ban da bayana yadda Kristi za ya dawo da dalilin zuwansa, annabci ya ba da alamun da za su nuna cewa ya kusa. Yesu ya ce: “A chikin rana da wata da tamrari za a ga alamu.” Luka 21:25. “Rana za ta yi dufu, wata ba za ya ba da haskensa ba, tamrari suna ta fadowa daga sama, ikokin da ke chikin sammai za su raurawa. Sa’an nan za su ga Dan mutum yana zuwa chikin gizagizai tare da iko mai-girma da daukaka.” Markus 13:24-26. Mai-ruya ya bayana alamar farko ta zuwan Yesu na biyu din: “Sai ga babban rawan duniya; rana kuma ta koma baka kamar gwado na gashi, wata kuma gudansa ya zama kamar jini.” Ruya 6:12.

An ga alamun nan kafin farkon karni na sha tara. Don cika annabcin nan na 1755 an yi rawan duniya mafi muni da aka taba sani. Ko da shike an cika kiran shi rawan duniyan Lisbon, ya kai yawancin Turai da Afirka da Amerika. An ji shi a Greenland da West Indies da tsibirin Madeira, a Norway da Sweden da Birtaniya da Ireland kuma. Ya rufe a kalla mil miliyan hudu murabbai. A Afirka girgizan ya yi tsanani yadda ya yi a Turai. Ya hallaka wuri mai yawa a Algiers; kuma kusa da Morocco, ya hadiye wani kauye mai mutum dubu takwas zuwa dubu goma. Wani babban rakumin ruwa ya share gabar Spain da Afirka, ya jawo hallaka mai yawa a birane.

A Spain da Portugal ne girgizar ta fi karfi. A Cardiz, rakumin ruwan aka ce bisan sa ya kai kafa sittin. Duwatsu, “wadansu mafi girma a Portugal, suka raunana kwarai kamar ma daga tushensu, wadansun su kuma suka bude a samansu, suka rarrabu suka yayage, abin al’ajibi, manyan bangarorinsu kuma suka gangara zuwa kwarin da ke kewaye. An ce harsunan wuta sun rika fitowa daga duwatsun nan.”

A Lisbon, “an ji karar tsawa a kalkashin kasa, jima kadan kuma wata girgiza mai-karfi ta rusar da yawancin birnin cikin misalin minti shida, mutum dubu sittin suka hallaka. Da farko teku ya ja da baya, ya bar yashin gabar, sa’annan ya dawo, ya hau kafa hamsin ko fiye da ainihin yadda ya saba kaiwa.” Cikin sauran ababan ban mamaki da aka ce sun faru a Lisbon, lokacin bala’in, akwai nutsewar wani masaukin jiragen ruwa da aka gina da kurdi mai yawa. Mutane da yawa sun taru a wurin don fakewa daga baraguzan rushe rushe; amma faraf daya wurin ya nutse da dukan mutanen, kuma ko gawa daya bai taba fitowa kan ruwan ba.”

“Motsin rawan duniyar ke da wuya, nan da nan kowace ekklesiya da gidan masu zaman zuhudu, da kusan kowane babban ginin gwamnati da fiye da daya daga cikin hudu na gidaje suka rushe. Kamar sa’oi biyu bayan matsannacin motsin, wuta ta kama wurare daban dabam ta rika ci kuma da karfi sosai har kusan kwana uku, har birnin ya zama kango gaba daya. Rawan duniyan ya faru a rana ce mai tsarki, yayin da majami’u da gidajen ma’aikatan ekklesiya sun cika da mutane, kalilan daga cikinsu ne kuwa suka tsira. “Razanar mutanen ta wuce misali. Ba wanda ya yi kuka; ya fi karfin hawaye, sun rika gudu nan da can, a rikice da tsoro da mamaki, suna kuka cewa duniya ta kare. Uwaye suka manta ‘ya’yansu, suka rika gudu cike da gumaka masu alamar giciye. Cikin rashin sa’a mutane da yawa sun gudu zuwa majami’u don neman tsaro; amma a banza aka bude farantin jibi; a banza aka rika rungumar bagadi; gumaka da pristoci da mutane suka kone tare a lokaci daya.” An kiyasta cewa mutum dubu tasa’in ne suka mutu a wannan ranar.

Bayan shekara ashirin da biyar, alama ta biye da annabci ya ambata ta bayyana-duhuntawar rana da wata. Abin da ya sa wannan ya fi daukan hankali shi ne cewa an ambaci ainihin lokacin cikawarta. Cikin hirar Mai-ceton da alamjiransa a Dutsen Zaitun, bayan Ya bayana lokacin jaraba ga ekklesiya mai-tsawon nan, shekaru 1260 na zaluncin paparuma, inda ya ce za a takaita kuncin - Ya ambaci wadansu al’ammura da za su rigayi zuwansa,

Ya kuma fadi lokacin da na farkon zai faru: “Amma a chikin wadannan kwanaki, bayan wannan kunchi, rana za ta yi dufu, wata ba za ya ba da haskensa ba.” Markus 13:24. Kwana ko shakaru 1260 din sun kare a 1798 ne. Shekara ashirin da biyar kafin nan, zalunci ya kusa tsayawa gaba daya. Bayan wannan zaluncin, bisa ga maganar Kristi, rana za ta duhunta. Ran 19 ga Mayu, 1780, an cika wannan annabcin.

“Kusan gaba daya ba abinda ya fi ranan duhun nan na 19 ga Mayu, 1780, inda ba dalili kawai sama da sarari ko ina a New England ya yi duhu.”

Wani mazamnin Massachusets da aka yi abin a idonsa ya bayana al’amarin kamar haka: “Da safe rana ta fito da haske, amma nan da nan ta rufu. Gizagizai suka duhunta, daga cikinsu kuma, da suka kara duhu da ban tsoro, walkiya ta haskaka, tsawa ta buga, ‘yar ruwan sama kadan kuma ta fado. Kusan karfe tara, gizagizan suka rage duhu, suka zama kamar kalan jan karfe, kuma hasken da ba a saba gani ba ya canja kasa da duwatsu da itatuwa da gine gine da ruwa da mutane. Mintoci kadan bayan wannan, wani babban bakin girgije ya rufe dukan sararin sama, sai dai karamar layi a gefe, wuri kuma ya yi duhu kamar yadda yakan kasance karfe tara na dare da damina …. “Tsoro, damuwa da fargaba suka cika zukatan mutane a hankali. Mata suka tsaya a kofa, suna kallon duhun; maza suka dawo daga gonakinsu, kafinta ya bar kayan aikinsa, makeri ya bar makera, mai-shago ya bar kantarsa. Matafiya suka sauka a gidan gona da ya fi kusa. Aka rufe makarantu, ‘yan makaranta kuma da rawan jiki suka ruga zuwa gida. Kowa ya dinga tambaya, “Me ke faruwa ne?” Kamar dai mahaukaciyar guguwa ce za ta abko ma kasar, ko kuma kamar ranar karshen komi kenan.

“An yi anfani da kyandir ko ina, wurtar muruhu ta haskaka Kaman ana duhun dare inda ba wata da bazara.… Kaji suka koma wurin kwanansu, suka yi barci, shanu suka tattaru a wurin kwanansu, kwadi suka rika kara, tsuntsaye suka raira wakokin su na yamma, jemage suka rika firiya ko ina. Amma dan Adam ya san cewa dare bai yi ba.

“Dr. Nathanael Whittaker, paston ekklesiyar Tabernacle a Salem, ya rika yin sujada a majami’ar, ya kuma yi wa’azi inda ya nace cewa duhun nan ya wuce ikon dan Adam. A wadansu wurare da yawa ma an taru. Nassosin da aka karanta a wurin kowane taro duka masu nunawa ne cewa duhun nan cikan annabci ne... Duhun ya fi yawa jima kadan bayan karfe sha daya ne.” A yawancin sassan kasar, ya yi yawa da rana, ta yadda mutane basu iya fadin lokaci tawurin duba agogo ba, ko cin abinci, ko yin ayukan su na gida ma basu yiwu ba, sai da hasken kyandir…..

“Yawan wuraren da duhun nan ya kai ba na kullum ba ne. An gan shi har can Famentta. Ta yamma ya kai har kurewar Connecticut, har Albany ma. Ta kudu, an gan shi a gabar teku, ta arewa kuma har duk inda kasar Amerika ta kai.”

Sa’a daya zuwa biyu kafin yamma, haske ya bayana kadan bayan bakin duhun nan na ranan, rana kuma ta fito, ko da shike bakar raba mai-nauyi ta rage hasken ranan. “Bayan

faduwar rana, gizagizan suka sake dawowa, nan da nan kuma wuri ya yi duhu.” “Kuma duhun daren bai kasa na rana ban mamaki da ban tsoro ba; ko da shike akwai kusan cikakken wata, ba a iya ganin komi ba sai da haske wanda mutum ne ya harhada, wanda idan aka gani daga gidaje makwabta da wadansu wurare daga nesa, suka nuna kamar ta duhun Masar wadda ta kusa ta gagari haske wucewa.” Wani wanda aka yi abin a idonsa ya ce: “Dole a lokacin na yi tunani cewa da an nade kowane abu mai ba da haske cikin dukan duniya da wani abinda haske ba zai wuce ta cikin sa ba, ko kuma a batar da duk ababa masu ba da hasken ma, da duhun ba zai fi wanda aka yi ba.” Ko da shike da karfe tara na daren, wata ta kai cikarta, “ba ta yi wani anfani wajen korar duhun ba.” Bayan tsakar dare duhun ya watse, wata kuma sa’anda ya fara ganuwa, ya zama kamar jini.

A tarihi ana ce da 19 ga Mayu, 1780 “Ranar Duhu” ce. Tun lokacin Musa ba wani lokacin duhu da ya kai wannan zurfi da fadi da dadewa. Yadda wadanda aka yi a idonsu suka bayana shi, al’amarin daidai ne da kalmomin Ubangijimu ta bakin annabi Joel, shekara dubu biyu da dari biyar kafin cikawar su. Ya ce: “Rana za ta juya ta zama dufu wata kuma za ya zama jini, kamin babbar rana mai-ban razana ta Ubangiji ta zo. Joel 2:31

Kristi ya ce ma mutanensa su lura da almun zuwansa, su kuma yi farinciki yayinda za su ga alamun Sarkinsu da ke zuwa. Ya ce: “Amma sa’anda wadannan al’amura sun soma faruwa, ku duba bisa, ku ta da kanku; gama pasarku ta kusa.” Ya nuna ma masu binsa itatuwa masu fitarda furanni da bazara, Ya ce: “Sa’anda suna tofuwa, kukan gani, kun sani kuma chikin rayukanku bazara ta kusa. Hakanan kuma, lokochin da kun ga wadannan al’amura suna faruwa, ku sani mulkin Allah ya kusa.” Luka 21:28, 30, 31.

Amma sa’anda ruhun tawali’u da dukufa ya zama ruhun girman kai da al’adu, kaunar Kristi ta yi sanyi. Da mutanen Allah suka tsunduma cikin son duniya da holewa sai suka manta umurnin Mai-ceton game da alamun bayanuwarsa. Aka manta batun zuwan sa na biyu din. Aka dinga karkata fasarar nassosin da suka shafi zuwan na sa har ya kai inda aka manta da shi ma, musamman a ekkleisiyoyin Amerika. ‘Yanci da holewa da jama’a suka samu, burin samun wadata da busar iska, dukufa ga neman kurdi, gaggawar neman suna da iko, sun sa mutane suka mai da hankullansu da begensu ga kayan rayuwa na yanzu, suka kuma nisantar da zancen ranan nan da al’amuran rayuwan nan za su shude.

Sa’anda Mai-ceton Ya bayana ma masu bi ga alaman zuwansa, Ya yi annabcin koma baya da za a samu gaf da komowansa. Kamar kwanakin Nuhu, za a shagala cikin ayukan duniya da son jin dadi - saye da sayarwa, shuka, gine-gine, aure da auraswa- an manta Allah da rai da ke zuwa. Ga masu rai a wannan lokaci, gargadin Kristi shi ne: “Amma ku yi hankali da kanku, kada ya zama zukatanku su yi nauyi da zarin ci da maye da shagulgula na wannan rai, har ranan nan ta hume ku ba labari kamar tarko.” “Amma a kowane loto sai ku yi tsaro, kuna yin roko ku sami ikon da za ku tsere ma dukan wadannan al’amuran da za su faru, ku tsaya kuma a gaban Dan mutum.” Luka 21:34, 36.

Maganar Mai-ceton, cikin littafin Ruya ta yi annabcin yanayin ekklesiya a wannan lokacin: “Kana da suna mai-rai ne, amma matache ne.” Ga wadanda suka ki tashi daga gamsuwa da rashin kulawansu an ba da gargadi cewa: “Idan fa baka yi tsaro ba, ina zuwa da kamar barawo, ba kwa za ka san sa’an da zan afko maka ba.” Ruya 3:1,3.

An bukaci falkas da mutane daga hatsarinsu, domin su shirya ma al’amuran da suka danganci rufewar gafara. Anabcin Allah ya ace: “Gama ranar Ubangiji mai-girma che, mai-ban razana kwa; wa ke da iko ya jimre da ita?” Wa zai tsaya sa’anda ya bayana, Shi “wanda tsarkin idon sa ya fi gaban duban mugunta,” Ga wandanda ke kuka cewa, “Ya Allah na, mun sanka,” amma suka ketare alkawalinsa, suka kuma bi wani allah, suna boye zunubi a zukatansu, suna nuna kaunar tafarkun rashin adalci, a gare su rana ta Ubangiji za ta zama “dufu kwarai ma, babu haske a chiki ko kadan.” Hosea 8:2, 1; Zabura 16:4; Amos 5:20. Ubangiji ya ce: “Za ya zama kwa a loton nan, zan yi binchiken Urushalima da fitillu, in hukumta mutanen da ke zamne lubus, masu-chewa chikin zuchiyassu, Ubangiji ba za ya aika nagarta ba, ba kwa za ya aika mugunta ba.” Zaphaniah 1:12. “Zan fori duniya kuma domin muguntassu, da miyagu kuma saba da laifofinsu: zan sa alfarmar masu griman kai ta dena, in kaskantar da alfarmar mutane masu ban tsoro kuma.” Ishaya 13:11. “Ko azurfassu ko zinariyassu ba za su iya chetonsu ba,” “Wadatassu za ta zama ganima, gidajensu kuma risbewa.” Zaphaniah1:18, 13.

Sa’anda annabi Irmiya ya hangi wannan lokaci mai-ban tsoro, ya ce: “Chiwo ni ke ji har chikin zuchiyata:…ban iya zama shuru ba, domin ka ji karar kafo, hargitsin yaki, ya raina. Ana hiran hallaka a kan hallaka.” Irmiya 4:19,20.

“Wannan rana ranar hasala che, ranar wahala da kumchi, ranar kadaichi da risbewa, ranar dufu da gama gira, ranar hadura masu-zurfi da dufu baki kirin, ranar kafo da ihu.” Zaphaniah 1:15,16. “Duba ga ranar Ubangiji tana zuwa;… garin a mai da kasa kango, a kuma hallaka masu-zunubin da ke chiki, su kare” Ishaya 13:9.

Sabo da babbar ranan nan maganar Allah da babban murya tana kiran mutanensa su falka daga barcinsu na ruhaniya su bidi fuskarsa da tuba da kaskantar da kai: “Ku busa kafo chikin Sihiyona, ku buga ihu chikin dutse na mai-tsarki; bari dukan mazamnan kasa su yi rawan jiki; gama ranar Ubangiji tana zuwa, har ma ta yi kusa.” “A tsarkake jama’a, a tattara dattibai, a tattara yara:… bari ango shi fita dakinsa, amarya kuma daga chikin lolokinta. Bari priest masu- hidimar Ubangiji, su yi kuka tsakanin haraba da bagadi,” “Ku juyo mani da dukan zuchiyarku, tare da azumi da kuka da bakinchiki: ku tsaga zukatanku ba tufafin ku ba, ku juyo wurin Ubangiji Allahnku: gama shi mai-alheri ne chike da juyayi, mai-jinkirin fushi, mai-yalwar jinkai.” Joel 2:1; 15-17, 12, 13.

Domin shirya jama’a su tsaya a rana ta Allah, an yi babban aikin canji. Allah Ya ga cewa da yawa cikin masu-cewa su nasa ne ba sa shiri don rai na har abada, kuma cikin

jinkansa Ya shirya aiko da sakon da zai falkas da su daga barci ya sa su shirya domin zuwan Ubangiji.

Ruya 14 ya ambaci wannan gargadin. Nan ga sako mai-sassa uku da aka ce malaiku ne suka sanar wanda kuma zuwan Dan mutum ya bi nan da nan domin girbe duniya. Gargadi na farkon yana ba da sanarwar hukumci da ke zuwa. “Annabin ya hangi malaika yana firiya a tsakiyar sararin sama, yana da bishara ta har abada wadda za a yi shellatta ga mazamnan duniya, ga kowanne iri da kabila da harshe da al’umma; da babbar murya kwa ya che, ku ji tsoron Allah, ku ba shi daraja; gama sa’ar hukmchinsa ta zo; ku yi sujada ga wanda ya yi sama da duniya da teku da mabulbulan ruwaye.” Ruya 14:6,7.

Sakon nan aka ce wani bagangare ne na “bishara ta har abada.” Ba malaiku aka ba su aikin shelar bisharar ba, mutane ne aka ba su. An bukaci malaiku su bi da wannan aikin. Su ke lura da aikace aikace na ceton mutane, amma bayin Kristi a duniya ne suke anihin shelar bisharar.

Amintattun mutane da suka yi biyayya ga ruhun Allah da koyaswoyoyin maganarsa ne masu-shelar kashedin nan ga duniya. Su ne wadanda suka ji “maganar annabchi wadda aka fi tabbatasda ita,” a fitilla mai-haskakawa chikin wuri mai-dufu, har gari yawaye, tamraro na assubahi kuma ya fito.” II Bitrus 1:19. Sun rika neman sanin Allah fiye da boyayyun dukiya, suka dauka cewa “ya fi chinikin azurfa kyau, ribatta kuma tafi suhihiyar zinariya.” Misalai 3:14. Ubangiji kuma ya bayana masu muhimman al’amura na mulkin. “Asirin Ubangiji ga masu tsoron sa yake; za shi kwa nuna masu wa’adinsa.” Zabura 25:14.

Ba masanan tauhidi ne suka fahimci gaskiyan nan, suka kuma yi shelarta ba. Da sun yi aminci, suka dukufa cikin addu’a da nazarin Littafin, da sun san likacin daren, da annabce anabcen sun bayana masu al’amuran da za su faru. Amma basu dauki matsayin nan ba, aka kuma ba ma su tawali’u sakon. In ji Yesu: “Ku yi tafiya tun kuna da haske, domin kada dufu ya chim maku.” Yohanna 12:35. Wadanda ke juyawa daga hasken da Allah a bayar ko kuma suka ki neman Shi lokacin da za su iya samun Shi, za a bar su cikin duhu. Amma Mai-ceton ya ce: “Wanda yana biyo na ba za shi yi tafiya cikin dufu ba, amma za ya sami hasken rai.” Yohanna 8:12. Duk wanda da, zuciya daya ke kokarin yin nufin Allah, yana kuma bin hasken da an rigaya an bayar, za ya sami Karin haske, a gare shi za a aiko da wani tauraro mai-walkiyar sama domin bishe shi zuwa dukan gaskiya.

Lokacin zuwan Kristi na farko, priestoci da marubuta na Birni Mai-tsarkin, wadanda aka ba su amanar maganar Allah, ya kamata da sun gane alamun zuwan Yesu. Anabcin Mikah ya ambaci wurin da za a haife shi; Daniel ya fadi lokacin zuwansa, Mikah 5:2; Daniel 9:25. Allah Ya ba shugabanin Yahudawa annabce annabcen nan; ba su da hujjar rashin bayana ma mutane cewa zuwan mai-ceton ya kusa. Jahilcinsu sakamakon kyaliya ne. Yahudawa sun rika gina ababan tunawa da annabawan Allah da aka kashe amma kuma

tawurin girmama manyan mutane na duniya sun rika daukaka Shaitan ne. Yayin da neman matsayi da iko ya dauke hankalinsu, suka manta darajan da sarkin sama ke mika masu.

Yakamata da dattiban Israila cikin marmari suka rika nazarin wuri da lokaci da yanayin abin nan mafi girma a tarihin duniya, watau zuwan Dan Allah domin fansar mutum. Ya kamata da dukan mutane sun yi tsaro suna jira domin su zama na farko da za su marabci Mai-fansar duniya. Amma, ga shi, a Baitalahmi, gajiyayyun matafiya daga Nazareth su biyu suka bi duk tsawon titin garin har kurewar gabas, a banza, suna neman mafaka da wurin kwana. Ba inda aka karbe su. A wani dakin shanu suka sami mafaka, kuma nan ne aka haifi Mai-ceton duniya.

Malaikun sama sun ga darajan da Dan Allah yake da shi tare da Uban, kafin halittar duniya, kuma da marmari sosai suka rika begen bayanuwarsa a duniya a matsayin al'amarin da ke cike da mafificin farinciki ga dukan mutane. Aka sa malaiku suka kai labari mai dadin nan ga wadanda ke shirye su karbe shi su kuma sanar da shi da farinciki ga mazamnan duniya. Kristi Ya sunkuya domin shi dauka ma kansa yanayin mutuntaka; za ya dauki nauyi mai-ban tausayi yayinda zai mai da ransa hadaya don zunubi; duk da haka malaiku sun so da ko cikin kaskantarwarsa ma Dan Allah shi bayana a gaban mutane da martaba da darajan da suka cancanci halinsa. Ko manyan mutane za su taru a babban birnin Israila don marabtarsa? Ko tulin malaiku za su gabatar da shi ga masu begen zuwan nasa?

Malaika ya ziyarci duniya domin ya ga wadanda ke shirye su tarbi Yesu. Amma bai ga alamun jira ba. Bai ji muryar yabo da nasara cewa lokacin zuwan Masiyan ya yi kusa ba. Malaikan ya yi shawagi kewaye da birni mai-tsarkin da haikalin, inda kasancewar Allah ta dinga ganuwa har zamanu, amma ko a nan ma rashin kulawan ne ya tarar. Priestoci cikin alfarmarsu da holewarsu suna mika kazamattun hadaya a haikalin. Farisawa da manyan muryoyi suna ma mutane jawabi ko kuma addu'o'i na girman kai a gefen tituna. A gidajen sarakuna da wuraren taron masana da makarantun mallaman Yahudawa, duka basu damu da al'amarin nan da ya cika sama da murna da yabo ba - cewa Mai-fansar mutane ya kusa bayanuwa a duniya.

Ba alama cewa ana sa rai Kristi zai zo, kuma ba shiri domin sarkin rai. Cikin mamaki dan sakon saman zai koma sama kenan da labari mai-ban kuyan, sai ya ga wadansu makiyaya suna tsaron tumakinsu da dare, kuma yayin da suke kallon sammai cike da taurari, suna bimbinin annabcin Masiyan da ke zuwa duniya, suna kuma begen zuwan Mai-fansar duniya. Wannan kam suna shirye su karbi sakon daga sama. Nan da nan kuwa malaikan ya bayana, yana shelar labari mai-kyau na babban murna. Darajar sama ta cika dukan wurin, wata kungiyar malaiku da ba a iya kirgawa ba ta bayana, kuma kamar murnar ta fi karfin mutum daya ya kawo daga sama, tulin muryoyi suka shiga raira wakar da dukan al'ummai na cetattu za su raira wata rana: "Alhamdu ga Allah a chikin mafi daukaka, a duniya kuma salama wurin mutane." Luka 2:14.

Labarin nan na Baitalahmi darasi ne babba. Yana tsauta ma rashin bangaskiyarmu da faharyarmu da isarmu. Yana mana kashedi mu yi hankali, kada saboda kyaliyarmu mu ma mu kasa gane almun zamanai, har mu kasa sanin ranar ziyartarmu.

Ba a duwatsun Yahudiya, ko kuma cikin makiyaya ne kadai malaikun suka iske masu begen zuwan Masiyan ba. A kasar kafirai ma an iske masu nemansa; masu hikima ne, mawadata masu martaba, shehunan gabas. Cikin nazarin halitta, shehunan nan sun iske Allah cikin aikin hannuwansa. Daga Littafi na Yahudawa sun ga cewa wani Tauraro zai taso daga Yakub kuma da marmari mai-yawa suka jira zuwansa, shi wanda zai zama "Ta'aziya ta Israila" da kuma "Haske domin bayananuwa ga Al'ummai," da kuma "kawo cheto har iyakachin duniya." Luka 2:25,32; Ayukan 13:47. Masu neman haske ne su, kuma haske daga kursiyin Allah ya haskaka sawayen su. Yayin da priestoci da mallami na Urushalima, wadanda aka zaba su zama wakilan gaskiyar da masu koyar da ita ke fama cikin duhu, taruraron da Allah ya aika ya bi da alumman nan zuwa inda aka haifi Sarkin.

Ga "wadanda suke sauraronsa" ne Kristi "za ya sake bayanuwa ban da zunubi… zuwa cheto." Ibraniyawa 9:28. Kamar labarin haihuwar Mai-ceton, ba a ba shugabannin addini amanar sakon zuwansa na biyu ba. Sun kasa rike dangantakarsu da Allah, suka kuma ki haske daga sama; sabo da haka ba sa cikin wadanda manzo Bulus ya ce masu, "Amma ku, yan'uwa ba chikin dufu kuke ba, da ranan nan za ta tarshe ku kamar barawo: gama ku duka yayan haske ne, yayan rana kwa; mu ba na dare ba ne, ba kwa na dufu ba." Tasssalunikawa I, 5:4,5. Masu tsaro a kan ganuwar Sihiyona ne ya kamata su fara samun labarin zuwan mai-ceton, na farko da zasu ta da murya su bayana cewa Ya kusa, na farko da za su gargadi mutane su shirya domin zuwansa. Amma sun yi sake, suna mafalkin salama da zaman lafiya, yayinda mutanen ke barci cikin zunubansu. Yesu ya ga ekklesiyarsa, kamar itacen bauren nan mara 'ya'ya, yafe da ganyaye na rudu kawai, amma ba 'ya'ya. Sun rika kiyaye al'adun addini, amma ba ruhun ainihin tawali'u da tuba da bangaskiya wanda shi ne kadai zai iya sa ibadarsu ta karbu ga Allah. Maimakon halayya na Ruhu, an rika nuna girman kai, da burga da son kai, da danniya. Ekklesiya mai koma baya ta rufe idanunta ga alamun zawanun. Allah bai rabu da su, ko kuma ya bar amincinsa ya kare ba, amma su sun rabu da shi, suka kuma raba kansu da kaunarsa. Da shike sun ki cika sharuddan, ba a cika alkawaran a garesu ba.

Haka sakamakon rashin fahimta a kuma yi anfani da haske da tasirin da Allah ya bayar. Idan ekklesiya ba ta bi umurninsa, ta karbi kowace tsirkiyar haske, ta yi dukan aikin da aka bayyana ba, addini zai tabarbare, ya zama kiyayewar al'adu kadai, ruhun ainihin ibada kuma shi bata. Tarihin ekklesiya ya rika bayana gaskiyan nan akai akai. Allah yana bidar ayukan bangaskiya da biyayya da suka je daidai da albarku da zarafin da Ya bayar. Biyayya tana bukatar sadakarwa ta kuma kunshi giciye; kuma dalili kenan masu bin Kristi da yawa suka ki karban hasken daga sama, kuma kamar Yahudawa na da, basu san lokacin ziyartar su ba. Luka 19:44. Sabo da girman kansu da rashin bangaskiyarsu, Ubangiji Ya

tsallaka su ya kuma bayana gaskiyarsa ga wadanda kamar makiyayan Baitalmi da Shehunan Gabas, suka yi amfani da dukan hasken da suka samu.

Babi na 18—Dan Canji America

Wani amintacen manomi da aka sa shi yayi shakkar cewa Littafin maganar Allah ne, amma kuma ya kasance da burin sanin ainihin gaskiyar, shi ne mutumin da Allah ya zaba ya zama shugaba wajen shelar zuwan Kristi ba Biyu. Kamar sauran 'ya Canjin, William Miller a farko rayuwansa ya fama da talauchi, ta haka kuma ya koyi darussan kwazo da musun kai. 'Yan iyalin da ya fito sun saba da dogaro da kai da son 'yanci, da dauriya da kishin kasa, hallayan nan kuwa sun nuna a halinsa. Baban shi kaftin ne na mayakan Juyin Danwaken, kuma sadakarwan da ya yi cikin gwagwarmaya da wahalolin mawuyacin zamanin can ne suka haifar da irin yanayin rayuwar Miller a kurichiyarsa.

Lafiyayye ne shi, kuma ko a kuruciya ya ba da alamar bisira ta musamman. Yayin da yake girma, wannan ya kara bayanuwa. Yana da zurfin tunani kwarai, da marmarin samun sani. Ko da shike bai sami gatan zuwa jami'a ba, son nazari da zurfin tunani da halin sakewansa sun sa ya zama mutum mai-basira da ra'ayoyi masu tarin anfani. Ya kasance mai halin kirki mara abin raini, da suna mai ban sha'awa sabo da halin sa na aminci da tsimi da son mutane. Sabo da kwazo da hikimarsa, tun a kurchiya ya sami kwarewa, amma bai rabu da halin sa na son nazari ba. Ya rike matsayi dabam dabam na gwamnati da na soja da kyau, kuma kofofin samun wadata da suna sun bude masa sosai.

Uwarsa mace ce mai ibada kwarai, kuma a kurchiyarsa an koya masa addini sosai. Amma a samartakarsa ya kasance cikin jama'a da suka ba da gaskiya wai Allah bai damu da abinda ke faruwa da yan Adam ba, abin da ya burge su kadai shi ne cewa su masu halin kirki ne, da halayya masu-ban mamaki. Da shike suna tare da cibiyoyin Kirista, Kiristancin ne ya sifanta halayensu. Littafin ne ya sa suka mallaki halayyan da suka ba su martaba, amma aka lalata kyawawan baye bayen nan ta yadda suka saba ma maganar Allah kuma. Ta wurin chudanya da mutanen nan, Luther ya yarda da ra'ayoyinsu. Irin fasaran da aka rika yi ma Littafin a lokacin ya jawo matsalolin da kusan ba a iya magancewa ba; duk da haka, yayin da sabuwar bangaskiyarsa ta yi watsi da Liffafin, ba ta ba da wani abu a madadinsa ba, bai kuma sami gamsuwa ba. Amma ya ci gaba da ra'ayoyin nan har wajen shekara goma sha biyu. Amma da ya kai shekara talatin da hudu, Ruhu Mai-tsarki ya cika zuciyarsa da ganewar cewa shi mai zunubi ne. Bai sami tabbacin farin ciki bayan mutuwa ba daga bangaskiyarsa ta da. Gaba sai bakin ciki da duhu kadai. Game da yadda yaji a lokacin, daga baya ya ce:

"Hallaka ta zama abin tsoro, zancen ba da lissafi kuma ya nuna kowa zai hallaka kenan. Sammai suka kasance mini kamar inda ba shiga, duniya kuma kamar karfe ne ga sawaye na. Mene ne har abada? Mene ne dalilin mutuwa? Duk tunanin na ya kara nisantar da ni daga samun ganewa. Ina kara tunani, ina kara rudewa. Na yi kokarin dena tunani amma tunanin ya ki bari na. Na zama abin tausayi kwarai, amma ban san dalilin ba. Na yi

ta gunaguni amma ban san ko da wa nike ba. Na san akwai kuskure da aka yi, amma ban san yadda, ko kuma inda zan sami na daidai din ba. Na yi bakin ciki amma ba bege."

Ya kasance cikin wannan yanayi har sawon watanni, ya ce, "Nan da nan aka bayana mini halin Mai-ceto a sarari ga zuchiyata. Naga kamar akwai wani nagari mai-tausayi da har ya yi kafara da kansa, domin laifofinmu, ta haka kuma ya cece mu daga horo ta zunubi. Na ji kawai mutumin nan abin kauna ne matuka, na ji kawai da ma a ce na ga kaina a hannayensa, in dogara ga alherinsa. Amma tambaya ta taso, Ta yaya za a tabbatar cewa akwai wani haka? Ban da Littafin, na gane cewa ba inda zan sami shaidar cewa akwai wani Mai-ceto hakanan, ko ma wata kasancewa nan gaba….

"Na gane Littafin ya bayana daidai irin Mai-ceton da nike bukata. Na kuma kasa gane yadda za a ce Littafin da ba horarre ba ne zai haifar da kaidodi da suka dache daidai da bukatun duniya ta zunubi hakanan. Dole na yarda cewa Littafin ruya ce daga Allah. Nassosin suka zama abin marmari na. Yesu kuma ya zama mani aboki. Mai-ceto ya zama gareni mafi-girma duka; Nassosin da a baya suka kasance duhu-duhu yanzu suka zama fitilla ga sawayena, haske kuma ga tafarkina, zuchiyata ta kwanta ta kuma gamsu. Na iske cewa Ubangiji Allah dutse ne cikin tekun rayuwa. Yanzu kuma Littafin ya zama babban abin nazari na, kuma zan iya fadi da gaske cewa na bincika shi da marmari sosai. Na tarar cewa ko rabi ma ba a fada mini ba. Na yi mamakin yadda kafin nan ban ga kyaunsa da darajarsa ba. Na yi mamaki cewa har ma na taba kinsa. Na sami bayanin duk wani abin da zuchiyata ta taba bukata, da maganin kowane ciwo na rayuwa. Ban sake marmarin karanta wani abu dabam kuma ba, na kallafa zuciyata ga neman hikika daga Allah"

A gaban jama'a Miller ya bayana bangaskiyarsa ga addinin da ya rena a da. Amma kafin nan abokansa suka kawo masa dukan dalilan da shi kansa ya dinga bayarwa don nuna cewa Littafin ba daga Allah ba ne. Alokachin bai shirya amsa masu ba; amma ya yi tunani cewa idan Littafin daga Allah ne lallai ba za ya yi sabani da kansa ba; kuma cewa dashike an ba da shi don koya ma mutane ne, dole zai kasance abin da mutum zai iya ganewa, ya kudurta yin nazarin Littafin don kansa, domin shi kuma gane ko za'a iya daidaita kowane kamanin sabani.

Da kokarin rabuwa da dukan ra'ayoyin sa na da, da kuma kyale kowane sharhi, ya dinga gwada nassi da nassi, ya yi nazarin sa da fasali; tun daga Farawa, yana karanta aya bayan aya, bai wuce nassi ba har sai ya gane ma'anarsa sarai, sarai. Idan wani abu ya shiga masa duhu yakan gwada shi da kowane nassin da ya shafi abin da ake magana akai a wannan nassin. Yakan bar kowace kalma ta nuna anfaninta ga batun da ake yi a nassin, kuma idan tunaninsa game da shi ya daidaita da kowace nassi, matsalar takan warware. Ta haka duk sa'anda ya ga wata Magana mai wuyan ganewa, yakan sami fasara a wani fanni na Littafin. Yayin da ya rika nazari yana addu'a don samun haske daga Allah, abin da bai gane ba yakan zama a bayane. Ya dandana gaskiyar maganar mai-zabura cewa, "Bude zanttatukan ka yana ba da haske; yana ba da fahimi ga sahihai" Zabura 199:130.

Da marmari mai-yawa ya yi nazarin littafin Daniel da Ruya, yana anfani da ka'idodin fassara da ya yi anfani da su game da sauran nassosi, ya kuma yi murna sosai ganin cewa ana iya gane alamun annabce annabcen. Ya ga cewa annabce annabcen da aka cika zahiri ne, cewa an fassara dukan siffofin da kamancewa da misalai, da dai sauran su, daidai inda aka ambace su ne, ko kuma an bayana ma'amarsu a wani nassi dabam, kuma akan gane su a zahiri ne, wani lokaci ya ce, "Ta hakanan na gamsu cewa Littafin tsari ne na gaskiya da aka bayana su, aka ba da su a sarari kuma a saukake, ta yadda kowane mutum, ko wawa ne ma, ba zai yi kuskure ba." Ya rika gano jerin gaskiya nan da can, yayin da ya rika bin muhimman matakan annabci daki-daki.. Malaikun sama sun rika bi da tunaninsa, suna bude nassosi ga ganewarsa.

Da shike ya dauka cewa yadda aka cika annabce annabcen a baya mizani ne na auna cikawar annabce annabce na nan gaba, sai ya gane cewa ra'ayin nan da ya cika wurin, cewa Kristi zai yi mulki cikin Ruhu a wannan duniya har Shekara Dubu kafin karshen duniya, ba shi da tushe daga maganar Allah. Wannan Koyaswa game da wadansu shekaru dubu na adalci da salama kafin zuwan Yesu kansa, ta jinkirta ababan ban razana na rana ta Ubangiji. Amma komi dadin koyaswar, ta yi sabani da koyaswoyin Kirsti da manzaninsa, wadanda suka ce dole a bar alkama da zawan su girma tare har sai lokacin girbi, watau karshen duniya; cewa " miyagun mutane da masu-hila zasu dada mugunta gaba gaba" cewa "chikin kwanaki na karshe miyagun zamanu zasu zo;" kuma cewa mulkin duhu zai ci gaba har zuwan Ubangiji, kuma ruhun bakinsa zaya cinye mulkin duhu ya hallaka shi da walkiyar zuwansa. Matta 13:30, 38-41, Timothawus II, 3:13; Tassalanikawa II, 2:8.

Ekkelisiyar Manzanin ba ta koyar da cewa duniya zata tuba, Yesu kuma zai yi mulki cikin ruhu ba, Kirista basu yarda da wannan ba har sai kusan farkon karni na sha takwas, kamar kowane kuskure, sakamakon koyaswar sun yi muni. Ta koya ma mutane suka dauka cewa zuwan Ubangiji yana da nisa sosai, ta kuma hana su kulawa da alamun zuwanasa. Ta jawo gamsuwa mara tushe, ta kuma sa mutane da yawa suka dena shiri don saduwa da Ubangijinsu.

Miller ya ga cewa Littafin yana koyar da cewa Kristi zai zo zahiri ne da kansa. Bulus ya ce; "Gama Ubangiji da kansa zaya sabko daga sama, da kira mai-karfi, da muryar sarkin malaiku, da kafon Allah kuma" Tassalunikawa I, 4:14. Mai-ceton kuma ya ce "za su kwa ga Dan mutum yana zuwa a bisa gizagizai na sama tare da iko da daukaka mai-girma." Gama kamar yadda walkiya takan fito daga gabas, ana kwa ganinta har yamma; hakanan bayanuwar Dan Mutum za ta zama" Matta 24:30,27. Dukan rundunan sama za su zo tare da shi, "Dan mutum zai zo chikin darajassa, da dukan malaiku tare da shi" Matta25:31. Kuma za ya aike malaikunsa da babbar karar to kafo, su kuma zasu tattara zabbaunsa" Matta 24:31.

Sa'anda ya zo za a tada mattatu masu adalci, a kuma wanzar da masu adalci da ke raye. Bulus ya ce "Ba dukanmu za mu yi barci ba, amma za a sake mu duka farap daya, da

kyaptar ido, da karar kafo na karshe; gama kafo za shi yi kara, mattatu kuma za su tashi marasa rubuwa, mu kuma za mu sake. Gama dole mai wannan mai-rubuwa za shi yafa rashin ruba wannan mai-mutuwa kwa shi yafa rashin mutuwa." Korantiyawa I, 15:51-53. Kuma cikin wasikar sa ga Tassalunikawa, bayan ya bayana zuwan Ubangiji ya ce, Mattatun da ke cikin Kristi za su fara tashi: sa'an nan mu da ke da rai, mun wanzu, tare da su, za a fyauce mu zuwa chikin gizagizai, mu tarbi Ubangiji a sararin sama; hakanan za mu zauna har abada tare da Ubangiji." Tassalunikawa I, 4:16,17.

Sai Kristi da kansa ya zo kafin mutanensa su karbi mulkin. Mai-ceto ya ce "Amma sa'anda dan mutum za ya zo chikin darajassa, da dukan malai ku tare da shi, sa'an nan zaya zauna bisa kursiyin darajassa. A gabansa kuma za a tattara dukan alumai; shi kwa za ya rarraba su da juna, kamar yadda makiyayi yakan rarraba tumaki da awakai; kuma za ya sanya tumaki ga hanuin daman sa, amma awakai ga hagu sa'an nan shi sarkin za y ache ma wadanda ke hanun damansa, ku zo ku masu albarka na Ubana, ku gaji mulki da na shirya domin ku tun kafuwar duniya" Matta25:31-34. Daga nasosin nan mun ga cewa sa'anda Dan mutum ya zo za a tada mattatu ban da ruba a kuma wanzar da wadan da ke raye. Tawurin wan nan wanzuwar za a shirya su domin karban mulkin, domin Bulus ya ce: " Nama da jini ba su da iko su gaji mulkin Allah ba; mai-rubewa kuma ba shi da gadon rashin ruba" 1Korantiyawa 15:50. Yanayin mutun yanzu mai-mutuwa ne, mai-ruba; amma mulkin Allah ba ruba, kuma na har abada ne. Sabo da haka a wannan yanayi na mutum ba zai iya shiga mulkin Allah ba. Amma sa'anda Yesu zai ba mutanensa rashin mutuwa, sa'annan zai kira su, su gaji mulkin nan da tun da ma abin gadon su ne.

Wadannan da wadansu nassosin kuma sun tabbatar ma Miller cewa al'amuran da ake ta cewa wai zasu faru kafin zuwan Kristi, kamar mulkin salama ga dukan duniya, da kafawar mulkin Allah a duniya, ashe bayan zuwan Kristi din ne kuma, dukan alamun zamanun da yanayin duniyan sun je dai dai da yadda anabci ya bayana kwanakin karshe. Dole ya gane daga binciken Littafin kawai cewa kwanakin duniyan nan a yanayinta yanzu sun kusa karewa. Ya ce; "Wata irin shaida kuma da ta taba zuciyata ita ce, yadda nassosin suka jeru bi da bi… Na gane cewa al'amuran annabci da suka riga suka cika sun auku ne a wani lokachi na musamman. Shekaru dari da ashirin din nan kafin ruwan tufana (Farawa 6:3); kwana bakwai din nan kafin ita ambaliyar, da kwana arba'in na ruwan sama da aka ce za a yi (Farawa 7:4); shekara dari hudu na bakunchin zuriyar Ibrahim (Farawa 15:13); kwana uku na mafalkan mai shayaswan Fir'auna da mai-tuyansa (Farawa 40:12-20); shekara bakwai na mafalkin Fir'auna (Litafin Lisafi) 14:34); Shekara uku da rabi na yunwa (Sarakuna I, 17:1) (Dubi Luka 4:25); shekara saba'in na kasancewa kamammu (Irmiya 25:11); wokatai guda bakwai na Nebuchadnezzar (Daniel 4:13-16); da kuma bakwai, bakwai, satin da biyu, da kuma bakwai guda, wadanda jimlar su ta kai bakwai saba'in, da aka kadara ma Yahudawa (Daniel 9: 24-27); al'amuran wokatan nan a baya da annabci ne kawai sun kuma cika daidai bisa ga annabchi."

Sabo da haka sa'anda cikin binciken Littafin ya ga lokuta a jere a jere da bisa ganewarsa suka kai har zuwan Kristi na biyu, sai ya dauka cewa lokacin da aka ayyana kenan, wanda Allah ya bayana wa bayinsa. Musa ya ce; "Al'amura na asirin ga Ubangiji Allahnmu suke; amma wadanda am bayyana, a gare mu suke duk da yayan mu har abada;" kuma Ubangiji tawurin annabi Amos, ya ce, "Ba za ya yi komai ba, sai shi baiyana asirinsa ga bayinsa annabawa." Kubawar Shari'a (29:29); Amos 3:7. Sabo da haka masu binciken maganar Allah za su yi begen samun bayani a sarari cikin Littafin, na abu mafi girma da zai faru cikin tarihin dan Adam. Miller ya ce, "Da shike na gamsu cewa kowane nassi horarre daga wurin Allah mai amfani ne (Timthawus II, 3:21), kuma cewa ba a taba kawo wani annabci bisa ga nufin mutum ba, amma an rubuta su yayin da Ruhu Mai-tsarki yana motsa su ne (Bitrus II, 1:21), an kuma rubuta su domin koyaswarmu, domin tawurin hakuri da ta'aziyar litattafai mu zama da bege" (Romawa 15:4), Sai na ga sassan Littafin da suka kunshi jeri jerin al'amura sun zama wajibi gare mu mu yi nazarinsu kamar kowane sashi na Littafin. Sai na ga cewa cikin kokarin fahimtar abin da Allah cikin jinkansa ya ga ya dace ya bayana mana, bani da yanci in tsallaka lokutan annabci.

Annabcin da yafi bayana lokacin zuwan Yesu na biyun shi ne Daniel 8:14: "Har yamma da safiya guda alfin da dari Uku; kana za a tsarkake wuri mai-tsarki." Bisa ga kaidarsa ta barin Littafin ya fassara kansa, Miller ya ga cewa rana daya a annabci yana matsayin shekara daya ne (Lissafi 14:34; Ezekiel 4:6), ya ga cewa kwana 2,300 din nan na annabci, ko kuma shekaru a zahiri, zai wuce zamanin Yahudawa sosai ma, don haka hakika annabcin bai shafi haikalin wancan zamanin ba. Miller ya yarda da ra'ayin da aka fi yarda da shi cewa a zamanin Kirista, duniya ita ce haikalin, sabo da haka ya dauka cewa tsarkakewar haikalin da Daniel 8:14 ya ambata yana nufin tsarkakewar duniya ne da wuta lokacin zuwan Kristi na biyu. Idan kuwa za a iya sansance farkon kwana 2,300 din, a ganinsa za a iya gane lokacin zuwansa na biyu din. Watau ta haka ne za a bayana lokacin nan da yanayi na yanzu, da "dukan iko da shagulgulan sa da fahariyarsa da danniyarsa zai kai karshen;" lokacin da za a "cire la'anan nan daga duniya, a murkushe mutuwa, a ba bayin Allah lada, annabawa da tsarkaka da masu-tsoron sunansa, a kuma hallaka masu-hallaka duniya."

Da karin himma, Miller ya ci gaba da binciken annabce annabcen dare da rana, yana binciken wannan al'amari mai-tarin muhimmanci. Bai sami haske daga Daniel 8, game da inda kwana 2,300 din ya fara ba. Ko da shike an umurci malaika Jibrailu ya ba Daniel fahimin wahayin, bai ba shi fasarar duka ba. Sa'anda aka bayana ma annabin muhiman tsananin da zai abka ma ekklisiya; karfin sa ya kare. Bai iya jimrewa ba kuma, sai malaikan ya bar shi tukuna. Daniel ya suma, ya yi chiwo kuma 'yan kwanaki. Ya ce, " Na yi mamaki da ruyan, amma babu wanda ya gane ta."

Amma kuma Allah Ya rigaya Ya ce ma maliakan, "Ka sanas da mutanen nan da ruyan." Dole a cika umurnin nan. Daga baya, malaikan ya dawo wurin Daniel ya ce,

“Yanzu na fito domin in ba ka hikimar ganewa.” “Ka sani fa ka fahimta kuma.” Daniel 8:27,16; 9:22,23,25-27. Akwai abu daya muhimmin cikin ruyar sura 8 da ba a fassara ba, watau abin da ya shafi lokaci-kwana 2,300 din nan; don haka malaikan ya fi mai da hankali ga batun lokaci yanzu.

“An kadara bakwai, bakwai sau sabain domin mutanen ka da birninka mai-tsarki…. Ka sani fa, ka fahimta kuma, tun daga loton fitowar doka a mai da Urushalima, a ginata kuma, har zuwa loton Masiya sarki, za a yi bakwai bakwai; chikin bakwai sattin da biyu kuma za a sake gininta da karabku da ramin ganuwa, cikin kwanakin masifa ke nan. Bayan bakwai din nan sattin da biyu kuma, za a datse Masiyan, ba kwa za ya bar kowane nasa ba…. Za ya yi wa’adi mai-kwari kuma da masu-yawa domin bakwai daya; a tsakiyar bakwai din kuma za ya sa sacrifice da hadaya ta gari su fasa.”

An aiki malaikan wurin Daniel domin shi bayana masa abin nan da bai gane ba cikin wahayin sura ta takwas din na zancen lokacin nan; “Har yamma da safiya guda alfin da dari uku; kana za a tsarkake wuri mai-tsarki.” Bayan ya ce ma Daniel “Ka sani fa, ka fahimta kuma,” sai ya ce, “An kadara bakwai bakwai har saba’in domin mutanen ka da birninka mai-tsarki.” Ma’anar kalman nan “Kadara,” a nan “an yanke” ke nan. Malaikan ya ce an yanke bakwai saba’in, watau shekara 490, musamman domin Yahudawa. Amma daga ina aka yanke? Da shike kwana 2,300 din nan ne kadai aka ambata cikin sura 8, hakika daga cikin su ne aka yanke bakwai saba’in din; sabo da haka bakwai saba’in din zai fara daidai da kwana 2300 din ne. Malaikan ya ce bakwai saba’in din za su fara “daga fitowar doka a mai da Urushalima” ne. Idan aka gano ranan da aka ba da dokan nan, an gano inda kwana 2300 din sun fara ke nan.

Cikin Ezra 7, akwai wannan dokar. Dubi aya 12-26. Artaxexes, sarkin Persia ne ya ba da cikakkiyar dokar a 457 B.C. Amma cikin Ezra 6:14 an ce an gina gidan Ubangiji a Urushalima “bisa ga umurnin Cyrus kuma, da Darius da Artaxerxes sarkin Percia” ne. Sarakuna ukun nan ne, ta wurin farawa da kara tabbatarwa da karasa yin dokar suka kai ta cikar da annabcin ya bukata domin shi zama farkon shekara 2300 din. Idan aka dauki 457 B.C; shekaran da aka kamala yin dokar, a matsayin shekarar da aka yi dokar, za a tarar cewa kowane abin da annabcin ya ambata game da bakwai saba’in din ya cika.

“Tun daga fitowar doka a maida Urshalima, a ginata kuma, har zuwa loton Masiya sarki; za a yi bakwai bakwai: cikin bakwai sattin da biyu kuma,” watau bakwai sittin da tara, ko kuma shekara 483. Dokar Artaxerxes, sarkin Persia, ta fara aiki cikin kaka ne na 457 BC. Daga nan shekara 483 sun kai har kaka na A.D 27. Lokacin kuwa an cika wannan annabcin. Ma’anar “Masiya” it ce “Shafaffe”. A kakan A.D 27, Yohanna ya yi ma Kristi baptisma, ya kuma sami shafewa na Ruhu. Manzo Bitrus ya shaida cewa Allah ya zuba ma Yesu Ba-nazarat Ruhu Mai-tsarki da iko. Ayukan 10:38. Mai-ceton kansa kuma Ya bayana cewa: “Ruhun Ubangiji yana bisa gareni, gama ya shafeni da zan yi shelar bishara ga

talakawa.” Luka 4:18. Bayan baptismarsa ya je Galili, “yana wa’azin bishara ta Allah, ya ce, Zamani ya chika” Markus 1:14,15.

“Zaya yi wa’adi mai-kwari kuma da masu yawa domin bakwai daya” (ko kuma har bakwai daya). Bakwi daya din nan shi ne na karshe cikin bakwai saba’in din nan; shi ne shekara bakwai na lokocin nan daga A.D 27 zuwa A.D 34, Kristi, da farko dai da kansa, daga baya kuma tawurin almajiransa, Ya mika ma Yahudawa gaiyatar bishara musamman. Yayin da manzanin suka tafi da albishiri din mulkin, umurnin mai-ceton shi ne: “Kada ku bita hanyar Alummai, Kada ku shiga kowane birni kuma na samariyawa; sai dai ku tafi wurin battatun tumaki na gidan Israila” Matta 10:5,6

“A tsakiyar bakwai din kuma za ya sa sacrifice da hadaya to gari su fasa.” A.D 31, shekara uku da rabi bayan baptimarsa, aka gichiye Ubangijin mu. Da babban hadayan nan da aka yi a Kalfari, tsarin nan na hadaya da har shekara dubu hudu ya rika misalta Dan-rago na Allah ya kai karshensa. Kamani ya sadu da abin da ya kamanta, aka kuma dena dukan hadayu na tsarin bukukuwan nan.

Kamar yadda mun rigaya mun gani, bakwai saba’in ko shekara 490 din sun kare a A.D 34 ne. A lokacin, tawurin kashe Istifanus da tsananta ma masu-bin Kristi. Sa’an nan aka ba duniya sakon ceton. Almajiran da zalunci ya tilasta su barin Urshalima, “suka tafi ko ina suna wa’azin Kalmar.” Filibus ya tafi birinin Samariya, ya yi masu wa’azin Kristi.” Bitrus, bisa ga bishewar Allah, ya bude bishara ga jarumin nan na Kaisariya, watau Karniliyus Mai-tsoron Allah, Bulus mai-kwazo kuma, aka aike shi ya kai albishirin “Chan nesa wurin al’ummai” Ayukan 8:4,5; 22:21.

Har wannan lokacin dai an cika kowane abin da annabci ya ambata, kuma an tabbatar da farkon bakwai saba’in din cewa 457B.C ne, kuma sun kare a A.D 34 ne. Daga wadannan, sansancewar karshen shekara 2,300 din ba abu mai-wuya ba ne. Bakwai saba’in din kwana 490 da aka yanke daga 2,300 din sun saurar kwana 490 da aka yanke daga 2300 din sun bar sauran kwana 1810. Bayan karshen kwana 490, za a dai cika kwana 1810 din. Daga A.D 34, shekara 1810 sun kai shekara ta 1844. Sabo da haka kwana 2,300 na Daiel 8:14 din nan sun kare a 1844 ne. A karshen wannan lokaci na annabcin, bisa ga shaidar malaikan Allah, “za a tsarkake haikalin” Ta haka kuwa an sansance lokacin tsarkakewar haikalin wanda ko ina an dauka cewa zai faru lokachin zuwan Kristi na biyu ne.

Da farko Miller da abokansa sun dauka cewa kwana 2300 din nan za su kare cikin bazarar 1844 ne, alhali annabcin yana maganar kaka ne. Wannan kuskuren ya jawo damuwa ga wadanda suka dauka cewa da bazaar ne Yesu zai dawo. Amma wannnan bai shafi koyaswar da ta nuna cewa 1844 ne karshen kwana 2300 din, kuma za a tsarkake haikali a lokachin ba.

Sa’ada Miller ya shiga nazarin Littafin don hakikance cewa wahayin ne daga Allah, da farko Miller bai za ta zai sami ganewa da ya samu yanzu ba. Shi kansa bai tabbatar da

sakamakon bincikensa sosai ba. Amma shaidar Liffatin ta bayana a sarari ta yadda ba a iya kawas da ita ba.

Ya kebe shekara biyu don nazarin Littafin, a 1818 kuwa sai ya gane cewa shekara ashirin da biyar nan gaba Kristi za ya dawo don fansar mutanensa. Miller ya ce, " Ba sai na fadi murnan da ta cika zuciyata sabo da abin faranta zuchiyan nan ba, ko kuma sabo da begena don kasancewa cikin farincikin fansassu. Littafin ya zama mani sabuwar littafi na. Hasken sa ya kawar da duk wani duhu da rashin fahimta daga kowace koyaswarsa; gaskiyar kuwa ta haskaka da daraja ainun! Kowane sabani da na gani a cikin maganar a da ya bata, kuma ko dashike ban gamsu da ganewata ta wadansu sassan ba, duk da haka haskensa ya wayar da duhun kai na har na sami marmarin binciken Littafin da ban sani za a taba samu daga koyaswoyinsa ba."

"Da ganewar cewa Littafin ya yi annabcin aukuwar muhimman al'amuran nan cikin kankanin lokaci hakanan tambaya ta zo mani da karfin gaske game da alhakin da ke wuyana zuwa ga duniya, bisa ga shaidar da ta canja nawa tunanin." Ya ji cewa wajibi ne gare shi ya mika ma wadansu hasken da shi ma ya samu. Ya san zai sami sabani daga marasa tsoron Allah, amma ya tabbata dukan Krista za su yi farincikin saduwa da Mai-ceton da suka ce suna kaunarsa. Tsoronsa kadai shi ne cewa cikin yawan murnarsa game da kusantowar kubutarwarsu, da yawa za su karbi koyaswar ba tare da bincika Littafin don gane gaskiyarsa ba. Sabo da haka ya jinkirta gabatar da shi, kada ya yi kuskure ya zama dalilin batar da wadansu. Wannan ya sa shi ya sake binciken ababan da suka goyi bayan ra'ayoyin da ya samu, ya kuma yi bimbini a hankali game da kowane abin da ya shiga masa duhu. Ya ga cewa hasken maganar Allah ya kawar da kowane jayayya. Cikin shekara biyar ya sami gamsuwa da masayin da ya dauka.

Yanzu kuma Alhakin sanar ma wadansu da abin da ya gaskanta ya sake dawo masa da karin karfi. "yayin da ni ke harka na, na rika ji a kunne na, 'Je ka fada ma duniya hatsarinsu.' Nassin nan ya dinga zuwa mani: 'Kadan na che ma mungun mutum, Ya kai mungun mutum, lallai za ka mutu, kai kwa ba ka yi managa domin ka fadakadda mugun shi bar hanyassa; wannan mugun mutum za ya mutu domin laifinsa, amma zan bidi jininsa gare ka. Amma idan ka fadakadda mugun mutum domin shi juyo ga barin hanyanssa, shi kwa baya juya ga barin hanyassa ba; za ya mutu sabada laifinsa, amma ka cheche ranka." Ezekiel 33:8,9. Na gane cewa idan aka fadakar da miyagun da kyau, da yawansu za su tuba; idan kuwa ba'a fadakar da su ba, za a bidi jininsu daga gareni."

Ya fara bayana ra'ayoyinsa, ba cikin jama'a ba, duk sa'anda ya sami zarafi, yana addu'a cewa wani mai-bishara zai ga muhimmancinsu ya dukufa ga shelarsu. Amma bai iya rabuwa da sanin cewa shi kanshi yana da alhakin fadakarwar ba. Kalmomin nan sun dinga dawowa zuchiyarsa; "Je ka shaida ma duniya; zan bidi jininsu gareka" shekara tara yana jira, abin yana damunsa, har sai 1831 sa'an nan ya bayana dalilin bangaskiyarsa a gaban jama'a.

Kamar yadda aka kira Elisha daga bin shanun nomansa a jeji, ya karbi alkyabar tsarkakewa don zama annabi, haka aka kira William Miller ya bar garmarsa domin shi bude ma mutane asiran mulkin Allah. Da rawan jiki ya shiga aikinsa, yana bi da masu sauraronsa a hankali ta lokutan annabci har zuwan Yesu ba biyu. Kowane yunkurin ya kara masa karfi da jarumtaka yayin da ya ga marmarin da kalmominsa suka jawo.

Daga kalmomin ‘yan-uwan shi ne, inda ya ji kiran Allah, Miller ya yarda ya bayana ra’ayoyinsa ga jama’a. Yanzu shekarun haifuwarsa hamsin, bai saba da magana a gaban jama’a ba, kuma ya damu da cewa shi bai cancanci yin wannan aikin ba. Amma tun daga fari an albarkaci aikinsa sosai da ceton rayuka. Falkaswar addini ta biyo bayan laccar sa ta farko, har iyalai sha-uku suka tuba dukansu, banda mutum biyu kawai. Nan da nan aka roke shi ya yi magana a wadansu wurare kuma, a kowane wuri kuma, aikin sa ya kai ga falkaswar aikin Allah. Masu-zunubi suka tuba, Kirista suka kara dukufa da addinin Kirista. Shaidar wadanda ya yi aikin su ta ce; “Yana taba zukatan irin mutanen da sauran mutane basu iya masu komi ba.” Wa’azin sa yakan falkas da zukatan jama’a game da muhimman al’amura na addini, kuma yakan kawo ragewar sha’awar duniya na zamanin.

A kusan kowane gari mutane da yawa, daruruwa ma a wadansu garuruwa, suka tuba sakamakon wa’azinsa. A wurare da yawa aka bude masa ekklesiyoyi masu Kin ikon Paparuma, kuma pastocin ekklesiyoyin ne sukan gayyace shi wa’azin. Ya kudurta cewa ba zai yi aiki a wurin da ba’a gaiyace shi ba, duk da haka ya iske cewa baai iya zuwa rabin wurarren da aka gayyace shi ba. Da yawa da basu karbi ra’ayoyinsa game da ainihin lokacin zuwan Yesu na biyu ba sun yarda cewa hakika Yesu zai dawo, ba da jimawa ba, kuma ya kamata su shirya. A wadansu manyan birane, aikin shi ya yi tasiri sosai. Masu shagunan giya suka watsar da jarinsu, suka mai da shagunan nasu wuraren taruwa; aka tarwasa wuraren chacha; kafirai da masu cewa ba ruwan Allah da abinda mutane ke yi, har ma da gagararrun ‘yan iska, suka sake, wadansun su kuwa sun yi shekaru basu shiga gidan sujada ba ma. Dariku dabam dabam suka fara addu’oi a wurare dabam dabam, kusan kowace sa’a kuma masu jari sukan hadu da tsakar rana domin addu’a da yabo. Babu yawan ta da hankali, sai saduda ko ina cikin zukatan mutane. Aikinsa, kaman na yan canji na farko, ya shafi ganar da mutane ne da taba lamirinsu, maimakon ta da hankulansu.

A 1833, Miller ya sami lasin na yin wa’azi, daga ekklesiyar su ta Baptist. Pastocin darikarsa da yawa suka amince da aikinsa, kuma da yardar su ne ya ci gaba da aikin. Ya rika tafiya yana wa’azin ba fasawa, ko da shike ya fi kasancewa a New England ne da jihohin tsakiya. Shekaru da dama yana biyan bukatunsa daga aljihunsa, bai kuma taba samun isashen kurdi ma don tafiya wuraren da aka gayyace shi ba. Sabo da haka, aikinsa ga jama’a, maimakon kawo masa kurdi ma, ya janye ne daga dukiyar sa da ta dinga raguwa don haka, a wannan lokachin na rayuwarsa. Ya zama uba na babban iyali, amma da shike sun kasance masu tsimi da kuma kwazo, gonarsa ta isa biyan bukatunsu da na shi kansa.

Cikin 1833, shekara biyu bayan Miller ya fara bayana ma jama'a shaidu cewa Kristi Ya kusan zuwa, alama ta karshe daga alamun da Mai-ceton ya bayar na zuwan sa ta bayana. Yesu ya ce: "Tamrari za su fado." Matta 24:29. Yohanna kuma, game da alamun rana ta Allah ya ce; "Tamrarin sama kuma suka fado a duniya, kamar itachen baure yakan kakabe yayansa da basu nuna ba, sa'anda babban iska ya raurawadda shi." Ruya 6:13. Wannan annabcin ya cika sa'an da aka yi babban yayyafin taurari ran 13 ga Nuwamba, 1833. "Fadowar tamrari mafi yawa da ban mamaki da aka taba yi kenan;" "dukan sararin samaniya ko ina a Amerika, ya rude da haske kamar wuta! Babu wani abu da ya taba faruwa a sararin sama a kasan nan da aka kalle shi da sha'awa mai-yawa da kuma tsoro kamar wannan." "Har yanzu kyaunsa yana zukatan mutane da yawa,… Ruwan sama bai taba zuba da kauri kamar yadda taurarin nan suka zubo a duniya ba, gabas da yamma, arewa da kudu, duk daya. A takaice, dukan sammai sai ka ce suna motsi ne,… kamar yadda Majallar Shehun Mallami Silliman ya ruwaito, an ga wannan al'amari ko ina a Amerika ta Arewa,… Daga karfe biyu har wayewan gari, sararin sama yana kwance shuru, kuma ba gizagizai, sai aka ajiye tarurari masu hasken gaske a dukan sararin sama."

"Babu harshen da zai iya bayana kyaun wannan al'amarin,… wanda bai gani da idon shi ba, ba zai iya gane daukakar abin ba. Ya yi kamar dukan taurarin sama sun taru a wani wuri daya ne a sama kusa da tushen, suna kuma harbowa da sauri daidai da gudun haske, zuwa kowane bangon duniya, duk da haka kuma basu kare ba, dubbai suka bi bayan dubbai, sai ka ce an halice su don wannan al'amarin ne." "Ba shi yiwuwa a sami wani kamanin itacen baure da ke kakkabe yayansa da basu nuna ba sa'anda babban iska ya raurawadda shi" kamar wannan.

A majallar kasuwanci ta New York ta ran 14 ga Nuwamba, 1833, an rubuta wani dogon sharhi game da wannan abu inda aka ce: "Babu mai-bin ussan ilimi ko kuma masanin da ya taba rubuta labari ko rahotun al'amari irin na safiyar jiya ba. Shekara dubu da dari takwas da suka wuce wani annabi ya yi annabcin wannan abin daidai,… idan za mu yarda cewa faduwar taurarin nan taurari ne suka fadi zahiri."

Ta haka aka bayana alaman nan ta karshe ta zuwansa, game da shi kuwa Yesu ya ce ma almajiransa: "Lokacin da kun ga wadannan al'amura duka, ku sani ya yi kusa, har bakin kofa." Matta 24:33. Bayan alamun nan, Yohanna ya ga babban al'amarin da ke biye, watau sararin sama ya shude kamar takarda yayin da duniya ta raunana, duwatsu da tsibirai kuma suka gusa daga wurarensu, miyagu kuma cikin tsoro suka so su gudu daga fuskar Dan mutum. Ruya 6:12-17.

Da yawa da suka ga fadowar taurarin sun gan shi kamar alamar hukumcin da ke zuwa ne, "mai-ban tsoro, alama tabbataciya ta jinkai, ta wancan babar rana mai-ban tsoro." Ta haka aka jawo hankulan mutane zuwa cikar annabci, aka kuwa kai mutane da yawa ga jin kashedin zuwan Yesu na biyu din.

A shekara ta 1840, wata cikar annabcin kuma ta ja hankulan mutane sosai. Shekara biyu kafin nan, Josiah Litch, da ya daga manyan masu wa'azin zuwan Yesu na biyu, ya wallafa fasarar Ruya 9 da ya yi annabcin Mulkin Ottoman. Bisa ga lissafinsa, za a hambarar da mulkin nan "a AD 1840 ne, cikin watan Agusta," kuma kwanaki kadan kafin hambararwar, ya rubuta cewa; "Idan sashen farkon, shekara 150, ya cika daidai kafin Deacozes ya hau gadon sarauta da izinin Turkawa, kuma shekara 391 da kwana goma sha biyar, sun fara a karshen sashe na farkon, za ya kare ran 11 ga Agusta, 1840 ne, sa'anda mulkin Ottoman a Constatinaple zai wargaje. Kuma na gaskata haka din ne zai faru."

A daidai lokacin da aka ambata, Turkiya, tawurin jakadunta, ta amince da tsaron kungiyar kasashen Turai, ta haka kuma ta sa kanta kalkashin mallakar kasashen Kirista. Al'amarin ya cika annabcin daidai. Sa'anda aka sani, mutane da yawa suka yarda da sahihancin kaidodin fassara annabci da Miller tare da abokansa suka yi anfani da su, zancen dawowan Kristi din nan kuma ya kara ci gaba. Masana da masu matsayi suka hada kai da Miller wajen yin wa'azi da wallafa ra'ayoyinsa, kuma daga 1840, zuwa 1844 aikin ya ci gaba akai akai.

William Miller ya mallaki basira kwarai, ya kuma hada da horuwa da nazari; ya kuma kara da hikimar sama ta wurin hada kansa da tushen hikima. Mutum ne mai daraja, wanda dole ne a girmama shi a kuma daukaka shi, duk inda ake zancen aminci da halin kirki. Da shike ya hada halin kirki da tawali'un Kirista, da kuma kamewa, ya zama mai-sauraron kowa, yana sauraron ra'ayin sauran mutane tare da auna abin da suke fadi. Ba tare da fushi ko garaje ba, yakan gwada kowace koyaswa da maganar Allah, kuma bisirarsa da kyakyawar sanin sa na Littafin sun sa shi ya iya karyata kuskure ya kuma fallasa karya.

Duk da haka bai yi aikinsa ba tare da jayayya ba. Kamar 'yan canji na farko mallaman addini basu karbi gaskiyan da ya koyar da soyayya ba. Da shike su basu iya kare ra'ayinsu ta wurin Littafin ba, sai suka shiga anfani da kalamai da koyaswoyin mutane, da al'adun ubani. Amma masu wa'azin gaskiyar sun yarda da maganar Allah ne kadai. "Littafin da Littafin kadai," taken su ke nan. Rashin goyon bayan Littafin ya sa masu sabani da su suka shiga yi masu ba'a. aka yi anfani da lokaci da arziki da baiwa don wulakanta wadanda laifinsu kadai shi ne cewa sun yi begen dawowar Ubangijinsu da farinciki, suna kuma kokarin rayuwa mai-tsarki suna karfafa wadansu su ma su shirya domin bayyanuwarsa.

An yi kokari sosai don janye tunanin mutane daga zancen dawowan Yesu. Aka mai da shi kamar zunubi, abin duniya, a ce mutum yana binciken annabce annabcen da suka shafi zuwan Kristi da karshen duniya. Ta haka hidimar da aka fi sabuwa da ita ta raunana bangaskiya ga maganar Allah. Koyaswarsu ta mai da mutane kafirai, da yawa kuma suka shiga bin sha'awar zukatansu kawai. Sai kuma wadanda suka jawo matsalar suka masu begen zuwan Kristi laifin jawo matsalar.

Yayin da yake jan taron jama'a a gidaje suna jinsa, ba a cika ambaton sunan Miller ba, sai daita hanyar ba'a ko soka. Yan iska da kafirai, da karfafawa da suka samu daga ra'ayoyin mallaman addini, suka shiga zage zage, da maganganu na sabo cikin kokarin su na jibga zage zage da reni akansa da aikinsa. Mai furfuran nan da ya bar gidansa yana tafiya da kurdin aljihunsa daga birni zuwa birni, gari zuwa gari, yana aiki ba fasawa don kai ma duniya kashedi game da kusantowar hukunci, sai kuma aka soke shi cewa mai-tsananin ra'ayi ne, makaryaci, mai-rudu.

Ba'a da karya da zagi da aka jibga masa sun jawo masa fushin 'yan jarida na duniya ma. Suka ce, "Mai da batu mai-girma da martaba mai-ban tsoro kamar wannan" abin wasa "ba wasa kawai ake yi da hankulan mutane ba" amma "ba'a ma ake yi da ranar hukumci, ana ba'a da Allah kansa, ana kuma rena ban razanar wurin hukumcinsa."

Mai-zuga dukan mugunta ba ya so ne kawai ya karyata sakamakon sakon zuwan Yesu ba, amma ya hallaka dan sakon ma. Miller ya yi anfani da gaskiyar Littafin ga zukatan masu jinsa, yana tsauta ma zunubansu, yana kuma raunana gamsuwa da kansu da suke yi, kuma kalmominsa kai a waye sun jawo magabtaka gare shi. Jayayyan da 'yan ekklesiya suka nuna ma sakonsa ta karfafa 'yan iska kara sabani, magabta suka shirya kashe shi yayin da ya bar wurin taron. Amma malaiku masu-tsarki suna cikin taron, dayansu kuma, cikin kamanin mutum ya rike hannun bawan Allahn nan ya kai shi inda yan iskan basu gan shi ba. Bai rigaya ya gama aikinsa ba, shirin Shaitan da 'yan sakon sa kuma bai yi nasara ba.

Duk da yawan sabani, sha'awar sakon zuwan Yesu ya ci gaba da karuwa. Daga ashirin ashirin da dari dari, jama'a suka karu har zuwa dubbai. An rika tuba ana shiga ekklesiyoyi, amma daga baya ruhun jayayya ya shiga, sabanin tubabbun nan, ekklesiyoyin kuma suka fara daukan matakan horon wadanda suka karbi koyaswar Miller. Wannan ya sa shi ya rubuta ma Kirista na dukan dariku jawabi inda ya ce idan koyaswoyinsa karye ne, a nuna masa kuskurensa daga Littafin.

Ya ce: "Mene ne muka gaskata da maganar Allah ba ta ce mu gaskata ba, kuma ku kanku kun ce Littafin ne kadai ka'idar bangaskiyarmu da ayukanmu? Menene, mun yi da ya jawo munanan soke soken da ake mana daga bagadi da kuma alkalami, ya kuma ba ku dalilin cire mu (Adventist) daga ekklesiyoyinku?" Idan mun yi kuskure, ku nuna mana inda muka yi kuskuren, ku nuna mana daga maganar Allah cewa mun yi kuskure; wulakancin ya ishe mu; wannan ba zai gamsar da mu cewa mun yi kuskure ba, maganar Allah ce kadai za ta sa mu canja ra'ayinmu. Ta wurin addu'a muka cimma matsayarmu, bisa ga shaida da muka gani a Littafin.

Daga sara zuwa sara gardadin da Allah ya aiko ma duniya ta wurin bayinsa an karbe su da shakka da rashin bangaskiya ma. Sa'an da zunubin mutanen zamanin Nuhu ya motsa Allah Ya kawo ambaliyar ruwa ga duniya, ya fara sanar masu da nufinsa domin su sami zarafin juyawa daga muggan halayyansu. Shekaru dari da ashirin ana jan kunnen su su

tuba, kada Allah Ya bayana fushinsa ta wurin hallaka su. Amma sun ga sakon kamar tatsuniya ce, basu kuma gaskata shi ba. Cikin muguntarsu, sun yi ma dan sakon Allah ba'a, suka wofinta rokonsa, har ma suka zarge shi da tsageranci. Wane mutum daya ne ya tsaya yayi jayayya da dukan manyan mutanen duniya? Idan sakon Nuhu gaskiya ne, don me dukan duniya ba ta gan shi ta gaskata shi ba? Ra'ayin mutum daya sabanin hikimar dubbai! Ba za su ji gargadin ba, kuma ba za su fake a jirgin ba.

Masu ba'a suka nuna ababa na halitta, rani da damina ba sa fasawa, sararin sama bai taba zubo da ruwa ba, kullum raba ce tana kawo yabanya - suka ce: "Ba misalai ya ke yi ba kuwa? Da reni suka ce mai-wa'azin nan yana da yawan sha'awa ne kawai, suka kuma ci gaba da holewa, da muguntarsu fiye da da. Amma rashin bangaskiyarsu bai hana cikar annabcin ba. Allah Ya dade yana hakuri da muguntarsu, yana ba su damar tuba, amma daidai lokaci, hukumcinsa ya sauko kan masu kin jin kan sa.

Kristi ya ce za a yi irin rashin bangaskiyan nan game da zuwan sa na biyu. Kamar yadda a zamanin Nuhu "basu sani ba har rigyawa ta zo ta kwashe su duka, hakanan kuma bayanuwar Dan Mutum za ta zama," in ji Mai-ceton. Matta 24:39. Sa'anda mutanen Allah ke hada kai da duniya, suna rayuwarsu, suna yin haramtattun ababa, sa'anda ekklesiya tana jin dadi irin na duniya yayin da ake aure-aure, kowa kuma yana begen shekaru da yawa na ci gaba irin na duniya, sa'an nan, faraf daya kamar walkiya, karshen burinsu da begen su zai zo.

Yadda Allah ya aiko bawan sa ya gardadi duniya game da rigyawa da ke zuwa, haka ya aiko zababbun yan sako su sanar da kusantuwar hukumci na karshe. Kuma kamar yadda mutanen zamanin Nuhu suka yi dariyan annabcin Nuhu, haka a zamanin Miller aka yi dariyan gargadinsa.

Don me ekklesiyoyin basu so wa'azin zuwan Yesu na biyu ba? Yayin da zuwan Ubangiji zai kawo ma miyagu wahala da hallaka, ga masu adalci yana cike da murna da bege ne. Wannan gaskiyar ce begen amintattu na Allah a dukan sararraki, don me ya zama "Dutsen tuntube" ga mutanensa? Ubangiji da kansa ne Ya yi ma alamajiran sa alkawali cewa: "Kadan na tafi na shirya maku wuri kuma, sai in sake dawowa, in karbe ku wurin kaina." Yohanna 14:3. Mai ceton ne ma da ya hangi kadaici da bakincikin masu binsa, ya aiko malaiku su ta'azantar da su da alkawalin cewa zai sake dawowa da kansa, kamar yadda Ya hau sama, yayin da almajiran ke tsaye suna kallon haurawar kaunatacensu sama, hankalinsu ya koma ga kalmomin nan; "Ku mazajen Galili, don mi ku ke tsaye kuna duba zuwa sama? Wannan Yesu wanda aka dauke shi daga wurinku, aka karbe shi sama, kamar yadda kuka ga tafiyatasa zuwa chikin sama hakanan za shi dawo." Ayukan 1:11. Sakon malaikun ya sake kawo bege. Almajiran "suka koma Urushalima da farinciki mai-girma: suna chikin haikali kullayaumi, suna albarkachi Allah." Luka 24:52,53. Ba su yi farinciki don an raba su da Yesu aka bar su su yi ta fama da wahaloli da jarabobin duniya ba ne, amma domin tabbacin mai-ceton cewa zai sake zuwa ne.

Ya kamata shelar zuwan Kristi ta zama bishara ta farinciki mai-girma kamar wadda malaiku suka ba makiyayyan Baitalahmi. Masu kaunar Kristi da gaske dole za su marabci sanarwan nan mai-tushe daga maganar Allah cewa za Ya sake dawowa, ba domin a zage Shi, a rena Shi, a ki Shi, kamar zuwansa na farko ba, amma cikin iko da daukaka domin Ya fanshi mutanensa. Wadanda ba sa kaunar Mai-ceton ne suke so Ya kasance can; kuma ba abinda ya fi tabbatar da cewa ekklesiyoyin sun rabu da Allah kamar haushi da kiyayyar da sakon nan daga sama ke jawowa.

Wadanda suka karbi sakon zuwan Kristi sun ga anfanin tuba da kaskantar da kai a gaban Allah. Da yawa sun dade suna jinkiri tsakanin Kristi da duniya; yanzu sun ga cewa lokaci ya yi da za su dauki matsayi, “Ababa na har abada suka zama zahiri a gare su. An kawo sama kusa, suka kuma ga kansu masu-laifi ne a gaban Allah.” Aka motsa Kirista zuwa sabuwar rayuwa ta ruhaniya. Suka ga cewa lokaci ya kasa, cewa abinda ya kamata su yi ma mutane dole su yi shi da sauri. Suka hangi har abada a gabansu, duk wani abin duniya kuma ya dena burge su. Ruhun Allah Ya sauko masu, Ya kuma ba da iko ga rokerokensu ga yan’uwansu da masu zunubi, cewa su shirya domin rana ta Allah. Shaidar rayuwarsu ta yau da kullum ta rika tsauta ma ‘yan ekklesiya da basu tuba ba. Wadannan basu so a dame su cikin neman holewarsu, da son kurdinsu, da kuma neman sunan su ba. Shi ya jawo kiyayya da sabani da aka yi ma bangaskiya ga zuwan Kristi da masu shelarta.

Sa’anda aka iske cewa ba za a iya karyata koyaswoyin nan na wokatai na annabci ba, musu hamayya suka yi kokarin hana binciken tawurin koyar da cewa an hatimce annabce annabacen. Ta hakanan ‘yan Kin ikon paparuma suka bi sawun yan Rum. Yayin da ekklesiyar paparuma ke hana ma mutane Littafin, ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma sun ce wai wani muhimmin sashen maganar Allahn ma da ke koyar da gaskiyar da ta shafi lokacin mu, wai ba za a iya gane shi ba.

Masu aikin bishara da sauran mutane suka ce wai littafin Daniel da na Ruya asirai ne da ba za a iya ganewa ba. Amma Kristi Ya ja hankulan almajiransa zuwa maganar annabi Daniel game da al’amuran da za su auku a zamaninsu, Ya ce: “Bari mai-karantawa shi fahimta,” Matta 24:15. Kuma zacen cewa wai littaffin Ruya asiri ne da ba za a iya fahimta ba ya bambanta da sunan littafin kansa, watau, “Ruya ta Yesu Kristi wadda Allah ya ba shi domin shi bayana ma bayinsa, al’amura ke nan da za su faru ba da jinkiri ba,… mai-albarka ne shi wanda ke karantawa, da su kuma wadanda ke jin zantattukan annabcin, suna kwa kiyayae abin da an rubuta a chiki, gama sa’a ta kusa.” Ruya 1:1-3.

Annabin ya ce “Mai-albarka ne shi wanda ke karanatawa”- akwai wadanda ba za su karanta ba; albarkar ba tasu ba ce. “Suna kwa kiyaye abin da an rubuta a ciki.” Da yawa suna kinjin gargadi da umurni da ke cikin littafin Ruya; ba wanda a cikin su zai iya samun alabarkan da aka yi alkawalinsa. Dukan masu yi ma annabcin da alamun da aka bayar a nan ba’a, dukan wadanda suka ki canza rayuwarsu, su kuma shirya domin zuwan Dan mutum, ba za a masu albarka ba.

Bisa ga shaida daga Littafin, don me mutane ke koyar da cewa Ruyan asiri ne da ya fi karfin ganewar mutum? Asiri ne da aka bayana, littafin da aka bude. Nazarin Ruyan yana kai hankali mutum zuwa annabce annabcen Daniel, kuma dukansu suna ba da gargadi mafi muhimmanci daga Allah zuwa ga mutane game da al'amura da za su auku a karshen tarihin duniya.

Ga Yohanna aka bayana al'amura masu ban sha'awa cikin rayuwar ekklesiya. Ya ga matsayi da hatsarori da sabani, da kuma kubutawar karshe ta mutanen Allah. Ya rubuta sakonin karshe da za su nunar da girbin duniya, ko a matsayin dammuna don rumbun sama ko kuma yayi domin wutar halaka. An bayyan masa batutuwa masu tarin muhimmanci, musamman ga ekklesiya ta karshe, domin wadanda za su juyo daga kuskure zuwa gaskiya su sami gargadi game da hatsaruka da sabanin da ke gaban su. Bai kamata wani ya kasance cikin jahilci game da abin da ke zuwa duniyan nan ba.

Amma don me jahilci ya yi yawa game da muhimmin fannin Littafin hakanan? Don me ake kiwuyan binciken koyaswoyinsa? Sakamako ne na kokarin Shaitan don boye ma mutane abin nan da ke fallasa rudunsa. Don haka Kristi mai Ruyan, da shike ya hangi yakin da za a yi da nazarin ruyar, ya furta albarka kan dukan wadanda za su karanta, su ji su kuma aikata kalmomin annabcin.

Babi na 19—Haske Ta wurin Duhu

Aikin Allah a duniya yana nuna kamani mai-yawa tsakanin manyan canje canje daga sara zuwa sara. Kaidodin dangantakar Allah da mutane ba sa sakewa. Muhimman al'amura na yanzu suna da makamantansu a tarihi, kuma abinda ya faru da ekklesiya a zamanun baya yana da darussa masu tarin anfani ga lokacinmu.

Babu gaskiyan da Littafin ya fi koyarwa a sarari kamar cewa Allah ta wurin Ruhunsa Mai-tsarki musamman yana bi da bayinsa a duniya cikin manyan canje canje da kan kawo ci gaban aikin ceto. Mutane kayan aiki ne a hannun Allah da yake anfani da su don cim ma manufofinsa na alheri da jin kai. Kowa yana da abin da zai yi, an ba kowa haske daidai da bukatun lokacinsa, isashe kuma don yin aikin da Allah Ya ba shi. Amma ba mutumin da komi darajan da Allah Ya ba shi, ya taba samun cikakkiyar ganewar babban shirin nan na ceto, ko ma cikakkiyar fahimtar manufar Allah game da aikin don zamaninsa. Mutane ba sa samun cikakken ganewar abin da Allah zai yi tawurin aikin da yake ba su, ba sa fahimtar dukan fannonin sakon da suke furtawa cikin sunansa.

"Ka iya binchike har ka tone al'amura na Allah? Ka iya binchiken mai-iko duka sosai?" "Gama tunanina ba tunaninku ba ne, al'amuranku kuma ba al'amurana ba ne." "Ni ne Allah kuma babu wani mai-kama da ni, mai-bayyana karshe tun daga mafarin, tun zamanin da kuma, al'amuran da ba a rigaya an aika ba tukuna." Ayuba 11:7; Ishaya 55:8-9; 46:9-10.

Ko annabawan da ana basu hasken Ruhu na musamman ma basu sami cikakkiyar fahimtar ma'anar ruyan da aka ba su ba. Akan dinga bayana ma'anan daga sara zuwa sara ne daidai da yadda mutanen Allah ke bukatar sakon da ke ciki.

Game da ceton da aka bayana tawurin bishara, Bitrus ya rubuta cewa; "annabawan da suka yi annabcin alheri wanda ke zuwa a gareku suka yi bidassa, suka bincike kuma da himma; suna nema su sani ko wane loto ne ko kwa irin loto Ruhun Kristi da ke chikinsu yana nuna, sa'anda ya shaida a gaba ra'adai na Kristi, da daraja da za ta bi bayan su. Su kwa aka bayana masu, ba kansu ba ne, amma ku ne suka hidimta maku wadannan abu." 1Bitrus 1:10-12.

Amma ko dashike ba a ba annabawa cikakkiyar ganewar ababan da aka bayana masu ba, sun yi kokarin samun dukan hasken da Allah ya ga daman bayyanawa. Sun tambaya, suka bincika da himma, suna neman sanin lokaci da irin lokacin da Ruhun Kristi da ke cikinsu ya bayyana. Wannan darasi ne ga mutanen Allah a zamanin Kiristanci wadanda don anfaninsu aka ba bayinsa annabce annabcen nan. Ba ga wadanda aka bayana masu suka yi anfani ba, amma gare mu suka yi anfanin. Lura da tsarkakan nan na Allah yayin da suka yi bincike suka nema da himma game da ruyai da aka ba su daga sararakin da ba a rigaya an haifa ba. Gwada himmarsu da halin kyaliya da kamnatattu na sararakin baya suka

rike kyautar Allah da shi. Wannan tsautawa ce ga kiwuya da kyaliyan da ake yi, ana wani cewa ba za a iya fahimtar annabce annabcen ba!

Ko da shike tunanin mutane basu isa su san tunanin Allah ko su gane yadda manufofinsa ke aiki ba, duk da haka sau da yawa sabo da wani kuskure ko kyaliyarsu ne ba sa fahimtar sakonin Allah. Sau da yawa ra'ayoyin mutane da al'adu da koyaswoyin karya na yan Adam sukan makantar da tunanin mutane ta yadda da kadan kawai suke fahimtar muhimman ababan da Ya bayana cikin maganarsa. Haka ya kasance game da almajiran Kristi, har lokacin da mai-ceton ke tare da su ta jiki ma. Zukatansu sun shaku da zancen da mutane ko ina suka dauka cewa Masiyan dan sarki ne na duniya wanda zai daukaka Israila zuwa gadon sarautar mulkin dukan duniya, basu iya gane ma'anar maganarsa da ya yi annabcin wahalolinsa da mutuwarsa ba.

Kristi kansa ya rigaya ya aika da sako, "Zamanin Allah ya chika, mulkin Allah kwa yana nan: ku tuba ku ba da gaskiya ga bisharan." Markus 1:15. Sakon nan daga annabcin Daniel 9 ne. Malaikan ya ce bakwai sattin da tara din za su kai har zuwa loton "Masiya sarki," kuma da bege mai yawa almajiran suka yi jiran kafawar mulkin Masiyan a Urushalima domin shi yi mulkin dukan duniya. Sun yi wa'azin sakon da Kristi ya dauka masu, ko da shike su kansu basu fahimci ma'anar sa daidai ba. Yayin da ginshikin sanarwar su Daniel 9 ne, basu ga cewa aya ta biye ta nuna cewa za a datse Masiyan ba. Tun haifuwarsu tunanin su yana kan wata daukaka ta mulki na duniya, wannan kuwa ya rufe tunaninsu daga kalmomin annabcin da kalmomin Kristi ma.

Sun cika aikinsu na mika ma al'ummar Yahudawa gaiyatar jinkai, sa'an nan, daidai lokacin da suka zata za su ga Ubangijinsu Ya hau gadon sarautar Dauda, suka ga an cafke Shi kamar mai-laifi, aka masa bulala, aka wulakanta Shi, aka hukumta Shi, aka kuma daga Shi a akan giciyen kalfari. Sanyin gwiwa da bakinciki kwarai suka cika zukatan almajiran duk sa'anda Ubangijinsu ke kwance cikin kabarin!

Kristi ya zo daidai lokaci, kuma daidai yadda annabci ya ce. Kowane fannin aikinsa ya cika shaidar Littafin. Ya yi shelar sakon ceto, kuma Kalmarsa cike da iko ne. Zukatan masu jinsa sun shaida cewa sakonsa daga sama ne. Kalmar da Ruhun Allah sun shaida cewa sakon Dan daga Allah ne.

Almajiran sun ci gaba da kaunarsu ga maigidansu. Amma duk da haka tunaninsu ya cika da rashin tabbaci. Cikin bakincikinsu basu tuna maganar Yesu da ta nuna cewa zai wahala Ya kuma mutu ba. Da Yesu Ba-nazarat ne ainihin Masiyan, da an sa su cikin bakinciki da cizon yatsa, tamboyoyin da suka dinga damunsu ke nan yayin da Mai-ceton ke kwance cikin kabarinsa, ran Assabat din nan tsakanin mutuwarsa da tashinsa.

Ko da shike daren bakinciki ya cika masu bin Yesu din nan, duk da haka ba a rabu da su ba. In ji annabin: "Sa'anda na zamna a chikin dufum Ubangiji za ya zama haske a gareni… za ya fito da ni wajen haske, zan kwa duba adilchinsa." "Ko dufu ma ba dufu ne

gareka ba, amma dare yana haskakawa kamar rana; da dufu da haske gare ka duk daya ne." Allah Ya ce: "Haske yana fitowa chikin dufu akan masu gaskiya." "Zan kuma jawo makafi ta hanyar da basu sani ba, tafarkun da basu sani ba in bishe su; in mai da dufu haske a gabansu; karkatattun wurare kuma su zama sosai. Wadannnan abu zan yi, ba ni kwa bari ba." Mikah 7:8,9; Zabuara 139:12; 112:4; Ishaya 42:4.

Sanarwa da almajiran suka yi cikin sunan Ubangiji daidai ne ta kowace fuska, kuma al'amuran da ta nuna suna faruwa a lokacin ma. "Lokaci ya yi kuma mulkin Allah ya yi kusa," shine sakon su. Da cikar bakwai sittin da tara na Daniel 9 din nan, da suka kai har ga Masiyan "Shafaffen, Kristi ke nan, Ya karbi shafewar Ruhu Mai-tsarki bayan baptismar da Yohanna ya yi masa a Urdun. Kuma "mulkin Allah" da suka ce ya kusa ya kafu ta wurin mutuwar Kristi. Mulkin nan ba na duniya ba ne yadda aka koya masu. Kuma ba mulkin nan mai-zuwa na har abada da za a kafa sa'anda "za a ba da sarauta da mulkin, da girman mulkokin da ke kalkashin sama, duka ga mutanen tsarkakan madaukaki" ba, ma mulkin nan na har abada inda "dukan mulkoki kuma za su bauta masa su yi biyayya da shi." Daniel 7:27. Bisa ga Littafin, "mulkin Allah shi ne mulkin alheri da mulkin daukaka kuma. Bulus ya yi zancen mulkin alheri cikin wasika ga Ibraniyawa, bayan ya bayana Kristi, Matsakanci nan mai-tausayi da ke "tabuwa da tarayyar kumamancin mu." Manzon ya ce: "Bari mu gusa fa gaba gadi zuwa kursiyi na alheri, domin mu karbi jin kai mu sami alheri." Ibraniyawa 4:15,16. Kursiyin alheri yana nufin mulkin alheri ne, da shike kasancewar kursiyi yana nuna kasancewar mulki ne. Cikin misalansa da yawa Kristi Ya yi anfani da kalamin nan "mulkin sama" don bayana aikin alherin Allah kan zukatan mutane.

Saboda haka kursiyin daraja shi ne mulkin daukaka, kuma mai ceto ya ambaci mulkin nan, cewa: "Amma saboda Dan mutum za ya zo chikin darajassa, da dukan malaiku tare da shi, sa'anan za ya zamna bisa kursiyin darajassa; a gabansa kuma za a tattara dukan al'ummai." Matta 25:31,32. Mulkin nan na nan gaba ne. Ba za a kafa shi ba sai zuwan Yesu na biyu.

An kafa mulkin alheri nan da nan bayan faduwar mutum. Lokacin da aka tsara shirin fansar 'yan Adam. Ya kasance cikin shirin Allah tawurin alkawalinsa kuma, tawurin bangaskiya kuwa za a iya zama talakawansa. Amma ba a ainihin kafa shi ba sai da Yesu Ya mutu. Ko bayan shigarsa hidimarsa ta duniya Mai-ceton, saboda Ya gaji da taurin kai da rashin godiyan mutane, da Ya ga dama da Ya fasa hadayarsa ta Kalfarin. A Gethsemani, kokon wahalar ta raunana a hannunsa. A lokacin da Ya share zufan goshinsa, ya bar masu zunubi su hallaka cikin zunubinsu. Da Ya yi haka, da babu ceto domin fadaddun mutane. Amma sa'anda Mai-ceton ya bada ransa, ya kuma ce, "an gama," lokacin ne aka tabbatar da cikar shirin fansa. An hakikance alkawalin ceto da aka yi ma Adamu da Hauwa'u masu zunubi a Adnin ke nan. Mulkin alheri, wanda ya kasance tawurin alkawalin Allah ne, ya kafu a lokacin.

Ta hakanan mutawar Kristi, wadda almajiran suka dauka cewa ta murkushe begensu, ita ce ta tabbatar da bege har abada, ko da shike ta jawo masu sanyin gwiwa, ita ce makurar tabbacin cewa bangaskiyarsu daidai ne. Al'amarin da ya cika su da makoki da cizon yatsa, shi ne ya bude kofar bege ga kowane dan Adam, cibiyar rayuwa nan gaba da farinciki mara matuka na dukan amintattun Allah na dukan sararraki.

Manufofin jin kai mara matuka sun rika cika, ko tawurin yankan burin almajaran ma, ko da shike alherin Allah da karfin koyaswar Kristi sun ribato zukatansu, duk da haka, garwaye da kaunarsu ga Yesu akwai girman kai da buri na son kai. Ko a zauren paskan, sa'an nan da mai-gidansu ya rigaya ya fara sunsuna giciyewarsa "makagara kuma ta tashi a tsakaninsu, ko wane ne ake maishe shi babba a chikin su." Luka 22:24. Zukatansu suna cika da zancen rawani da kursiyi da daraja, alhali a gabansu ga kunya da azabar lambun Gethsamani, da dakin shari'a da giciyen kalfari. Girman kansu, da burin daraja ta duniya ne suka sa su manne ma koyaswar karya ta zamaninsu, suka kasa kula maganar Mai-cetonsu da ta nuna ainihin yanayin mulkinsa, da kuma radadinsa da mutuwarsa. Kurakuran nan kuma suka haifar da gwajin da aka bari ya faru domin yi masu gyara. Ko da shike almajiran sun yi kuskuren ma'anar sakonsu, suka kuma kasa cika begensu, duk da haka sun yi shelar gargadin da Allah ya ba su, Ubangiji kuma zai ba su ladar bangaskiyarsu ga dukan al'ummai. Domin shirya su don wannan aikin ne aka bari suka sha bakincikin nan.

Bayan tashinsa, Yesu ya bayyana ga almajiransa a hanyar Imwasu, kuma "tun daga Musa da dukan annabawa, chikin dukan littattafai yana fasalta masu al'ammura na bisa kan sa." Luka 24:27. Zukatan almajiran suka motsu. Bangaskiya ta taso. Suna sake samun bege mai rai, tun ma kafin Yesu Ya bayana kansa garesu. Nufinsa ne Ya ba su ganewa, Ya kuma kafa bangaskiyarsu ga tabbataciyar Kalmar annabci. Ya so gaskiya ta kafu da karfi cikin zukatansu, ba kawai don shaidarsa da kansa ba, amma domin tabbataciyar shaidar da dokar alamu da kamani da kuma annabce annabce na Tsohon Alkawali suka bayyana ne. Ya zama wajibi masu bin Kristi su sami bangaskiya mai basira ba domin kansu kadai ba, amma domin su kai ma duniya sanin Kristi. Kuma matakin farko don ba su wannan sanin shi ne cewa Yesu ya kai hankulan almajiran zuwa ga "Musa da dukan annabawa." Shaidan da Mai-ceton ya bayar ke nan game da muhimmancin Tsohon Alkawali, bayan tashinsa daga matattu.

An kawo sakewa sosai ga zukatan almajiran, sa'anda suka sake kallon fuskar Mai-gidansu! Luka 24:32. Ta hanya mafi inganci, sun same shi, wanda Musa cikin shari'ar da kama annabawa suka rubuta. Rashin tabbaci, da bacin rai, da cizon yatsa, sun kauce, tabbaci da bangaskiya suka shigo. Shi ya sa bayan komawarsa sama suka kasance cikin haikali kullum suna yabon Allah. Mutane, da shike mutuwarsa kadai suka sani, sun zata za su ga bakinciki da rudani a fuskokinsu, amma murna da nasara suka gani. Almajiran nan sun sami shiri sosai don aikin da ke gabsu. Sun rigaya sun wuce gwaji mafi tsanani, suka kuma ga yadda, sa'anda bisa ga ganin mutum, sun rasa komi, maganar Allah ta cika daidai.

Daga nan, mene ne kuma zai rage bangaskiyarsu, ko kuma ya sa kaunarsu ta yi sanyi? Cikin tsananin bakin ciki, sun sami karfafawa sosai, “anchor na rai, tabbatachen bege mai-tsayawa.” Ibraniyawa 6:18,19. Sun rigaya sun shaida hikimar Allah da ikonsa, suka kuma “kawas da shakka ba mutuwa, ba rai, ba malaiku, ba sarautai, ba al’amuran yanzu, ba al’amura na zuwa, ba ikoki, ba tsawo, ba zurfi, ba kwa wani halitaccen abu, da za ya iya raba mu da kamnar Allah, wanda ke chikin Kristi Yesu Ubangijin mu.” Suka ce: “Cikin dukan wadannan al’amuran, mun fi gaban masu-nasara tawurin wanda ya kamnache mu.” Romawa 8:38,39, 37. “Amma maganar Ubangiji ta tabbata har abada.” 1 Bitrus 1:25. Kuma “wa za ya koyas? Kristi Yesu ne ya mutu, I kwa, har yatashi daga matattu, yana hannun dama na Allah, yana yin roko kuma sabili da mu.” Romawa 8:34.

In ji Ubangiji, “Mutane na kuma ba za su kumyata ba dadai.” Joel 2:26. “Kuka ta na sabka da dare amma murna ta kan zo da safe.” Zabura 30:5. Sa’anda almajiran nan suka sadu da Mai-ceton a ranar tashinsa, zukatansu kuma suka kuna daga cikin su yayinda suke jin maganarsa, sa’anda suka kalli kai da hannaye da sawayen da aka kuje domin su; sa’anda, kafin hawan sa sama Yesu Ya kai su har Baitanya, Ya kuma daga hannuwansa sama Ya yi masu albarka, Ya ce masu “Ku tafi chikin duniya duka, ku yi wa’azin bishara,” Ya kuma kara da cewa: “Ga shi kwa ina tare da ku kulluyomi” (Markus 16:15; Matta 28:20), sa’anda a ranar Pentecost mai-taimakon da aka yi alkawalin sa Ya sauka aka kuma ba da iko daga sama, rayukan masu bada gaskiya kuma suka yi murna da sanin kasancewar Ubangijinsu da ya koma sama, sa’an nan ne su, ko da shike hanyarsu ta bi ta hanyar hadaya da mutuwa ma, sa’an nan ne da sun sauya hidimar bishara ta alherinsa da “rawanin adalci” da za a karba lokacin zuwansa, da daukakar kursiyi na duniya, wadda ita ce da begen almajirancinsu, Shi “wanda yake da iko shi aikata kwarai da gaske gaba da dukan abin da muke roko ko tsammani,” Ya rigaya Ya ba su murnar kawo ‘ya’ya da yawa wurin daraja, da murna mai-yawa da “nauyin daraja” wanda Bulus Ya ce “kunchinmu mai-sauki, wanda ke na lokaci kadan,” bai isa a gwada da shi ba.

Dandanon almajiran da suka yi wa’azin “bishara ta mulkin” a zuwan Kristi na fari, ya sami na biyu dinsa a dandanon wadanda suka yi shelar zuwan sa na biyu. Kamar yadda almajiran suka yi wa’azi cewa: “zamani ya chika, mulkin Allah kwa yana nan,” haka ne Miller da abokansa suka yi shela cewa lokacin annabci mafi tasawo, kuma na karshe, da Littafin ya ambata ya kusan karewa, cewa hukumcin ya kusa, kuma za a shigo da mulki na har abada-din. Wa’azin almajiran game da lokaci ya danganci bakwai sab’in din nan na Daniel 9 ne. Sakon da Miller da abokansa suka bayar ya sanar da karewar shekara 2,300 na Daniel8:14 ne, wanda suka kunshi bakwai saba’in din. Kowane wa’azin ya shafi wani fanni dabam ne na annabci dayan.

Kamar almajirai na farkon, William Miller da abokansa basu fahimci cikakkiyar ma’anar sakon da suka kai ba. Kurakurai da suka dade cikin ekklesiya sun hana su kaiwa ga kyakyawar fasarar wani muhimmin fannin annabcin. Saboda haka, ko dashike sun yi

shelar sakon da Ubangiji Ya ba su su kai ma duniya, duk da haka tawurin rashin fahimtar ma'anarsa, suka sha yankan buri.

Domin fassara Daniel 8:14, "Har yamma da safiya guda alfin da dari uku; kana za a tsarkake wuri mai-tsarki" Miller ya yi anfani da ra'ayin nan da ya fi karbuwa ne a zamanin, cewa duniya ce haikalin, ya kuma dauka cewa tsarkakewar hailakin shi ne tsarkakewar duniya da wuta lokacin zuwan Ubangiji. Saboda haka da ya gane karshen kwana 2,300 din sai ya dauka cewa lokacin zuwan Yesu na biyu ke nan. Kuskuren shi karban ra'ayin nan ne cewa duniya ce haikalin.

Cikin tsarin kamani, wanda inuwar hadayar Yesu da priesthood na sa, tsarkakewar haikalin ne hidima ta karshe da babban priest yakan yi a hidimominsa na shekara. Shi ne aikin karshe na kafarar, watau cirewar zunubi daga Israila. Inuwa ce ta aikin karshe na hidimar Babban priest namu a sama, wajen sharewa ko cirewar zunuban mutanensa da aka rubuta a littattafai na sama. Wannan hidimar ta kunshi aikin bincike, aikin hukumci; kuma zai rigayi zuwan Kristi cikin gizagizai na sama da iko da kuma daraja mai yawa; gama zai zo bayan an rigaya an gama hukumcin ne. In ji Yesu: "Haki na yana tare da ni kuma, da zan saka ma kowane mutum gwalgwadon aikinsa." Ruya 22:12. Wannan aikin hukumcin ne, gaf da zuwansa na biyu din. Sakon malaika na fari na Ruya 14:7 yana shelar cewa: "Kuji tsoron Allah, ku ba shi daraje, gama sa'ar hukumcinsa ta zo."

Wadanda suka yi shelar sakon nan sun ba da sakon da ya kamata a lokacin da ya kamata. Amma kamar yadda lamajiran farko suka fada, "lokacin ya cika, kuma mulkin Allah yana nan," bisa ga annabcin Daniel 9, ba tare da fahimtar cewa an yi annabcin mutuwar Masiyan a nassi dayan ba, don haka Miller da abokansa sun ji wa'azin sakon bisa ga Daniel 8:14 da Ruya 14:7 ne, suka kuma kasa gane cewa akwai wadansu sakoni kuma cikin Ruya 14 din, da su ma za a ba da su kafin zuwan Ubangiji. Yadda almajiran suka yi kuskure game da mulkin da za a kafa a karshen bakwai saba'in din, haka Adventist suka yi kuskure game da al'amarin da zai auku a karshen kwana 2,300 din. A duk lokutan biyu, an rike kurakurai da yawancin mutane suka amince da su, kurakuran kuma suka boye gaskiyar daga tunaninsu. Dukansu sun cika nufin Allah wajen kai sakon da ya so su kai, kuma dukansu, ta wurin kuskuren fasarar sakonsu, suka sha yakan buri.

Duk da haka, Allah Ya cimma manufarsa tawurin bari da Ya y i aka ba da gargadin yadda yake. Babbar ranar ta kusa, kuma cikin ikonsa, aka kawo mutanen wajen gwaji game da ainihin lokaci, domin a bayana masu abin da ke zukatansu. An shirya sakon domin gwadawa da tsarkakewar ekklesiyan ne. An kai su inda za su gane ko zukatan su na wurin wannan duniyan ne ko kuma wurin Kristi da sama. Sun ce suna kaunar Mai-cetonsu, yanzu kuma ya kamata su hakikance kaunar ta su, ko suna shirye su sadakar da begen su da burinsu na duniya, su kuma marabci zuwan Ubangijinsu da farin ciki? An shirya sakon domin su iya sansance ainihin yanayin ruhaniyarsu ne; an aiko da shi cikin jin kai ne domin a falkas da su, su nemi Ubangiji cikin tuba da tawali'u.

Kuma, ko da shike yankan burin sakamakon rashin fahimtarsu ta sakon da suka bayar ne, an yi anfani da yankan burin ya zama alheri. Ya gwada zukatan wadanda suka ce sun karbi gargadin. Ko saboda yankin burinsu za su watsar da abin da suka sani, su yi watsi da amincewar su ga maganar Allah? Ko kumacikin addu'a da tawali'u, za su nemi gano inda suka yi kuskuren fahimtar muhimmancin annabcin ne? Nawa ne suka motsu sabo da tsoro, ko buri? Nawa ne masu zuciya biyu biyu da kuma rashin bangaskiya? Da yawa sun ce suna kaunar bayanuwar Ubangiji. Sa'anda aka bukace su su jimre ba'a da renin duniya, da gwaji da jinkiri da kuma yankan burin, ko za su musunci bangaskiyarsu? Da shike basu gane yadda Allah ke bi da su ba, ko za su kawas da gaskiyan shaidar maganarsa?

Wannan gwajin zai bayyana karfin wadanda, da ainihin bagaskiya suka yi biyayya ga abinda suka gaskata cewa shi ne koyaswan Maganar Allah da Ruhunsa. Zai koya masu hatsarin karban ra'ayoyin mutane da fassararsu, maimakon barin Littafin ya fassara kansa. Ga masu bangaskiya rikicewa da bakin ciki da kuskurensu ya jawo zai kai ga gyaran da ake bukata. Za su kai ga Karin nazarin annabcin. Zai sa a koya masu su kara binciken harsashen bangaskiyarsu, kuma su ki duk wani abu, komi yawan Kiristan da suka yarda da shi, wanda ba shi da tushe a ainihin maganar Allah.

Ga wadannan masu bangaskiyar, kamar almajirai na farkon, abin da a lokacin gwaji ya yi duhu, ga ganewarsu daga baya za a bayana shi a sarari. Sa'anda suka ga karshen komi, za su san cewa, duk da gwajinsu da kurakuransu suka haifar, manufofinsa dominsu suna cika a hankali. Za su gane tawurin dandano mai-albarka cewa Shi mai-tausayi na kwarai, Mai-jinkai kuma, cewa dukan tafarkunsa "rahama ne da gaskiya ga irin wadanda su ke masu kiyaye alkawalinsa da shaidunsa."

Babi na 20—Babban Falkaswa na Ibada

Cikin annabcin sakon malaika na fari na Ruya 14, an yi annabcin babban falkaswar addini kalkashin shelar kusantowar zuwan Kristi na biyu. An ga malaika yana firiya “a tsakiyar sararin sama, yana da bishara ta har abada wadda za ya yi shelatta ga mazamman duniya, ga kowane iri da kabila da harshe da al’umma.” “Da babban murya kwa” ya yi shelar sakon, cewa: “Ku ji tsoron Allah, ku ba shi daraja; gama sa’ar hukunchinsa ta zo: ku yi sujada ga wanda ya yi sama da duniya da teku da mabulbulan ruwaye.” Ruya 14:6,7.

Akwai muhimmanci game da cewa malaika ne mai-shelar gargadin nan. Ya gamshi Allah, ta wurin tsarki da daraja da karfin mai shelar sakon, ya bayana girman yanayin aikin da sakon zai aiwatar, da kuma iko da darajar da aikin zai kunsa. Kuma firiyar malaikan, “a tsakiyar sararin sama,” da babbar murya” da ake shelar gargadin da ita, da kuma shelar ta “ga mazamnan duniya”- “ga kowane iri da kabila, da harshe da al’umma - suna nuna sauri da kuma mamayewar duniya da aikin zai kunsa.

Sakon kansa yana ba da haske game da lokacin da wannan aikin zai gudana. An ce shi wani sashi ne na “bishara ta har abada,” yana kuma shelar farawar hukumcin. An yi wa’azin sakon ceto a dukan sararaki; amma sakon nan wani sashi ne na bishara, wanda a kwanakin karshe ne kadai za a yi shelar sa, domin a lokacin ne kadai za a iya cewa sa’ar hukumcin ta zo. Annabce annabcen suna byayana al’amuran da za su kai ga farawar hukumcin, musamman ma littafin Daniel. Amma an bukaci Daniel ya kulle fannin nan na annabcinsa da ya shafi kwanakin karshe, ya kuma rufe shi da hatimi “har kwanakin karshe.” A wannan lokacin ne kadai za a iya shelar sako bisa ga cikawar annabce annabcen nan. Amma annabin ya ce, a lokacin karshen “mutane da yawa za su kai da kawo a guje, ilimi kuma za ya karu.” Daniel 12:4.

Manzo Bulus ya gargadi ekklesiya kada ta yi zaton zuwan Kristi a zamaninsa. Ya ce: “Gama wannan sai riddan ta fara zuwa, mutumin zunubi kuma ya bayanu, dan hallaka,” kafin ranar ta zo. 11 Tassalunikawa 2:3. Sai bayan babban riddar, da lokacin nan mai-tsawo na mulkin “mutumin zunubi,” kafin mu fara neman zuwan Ubangijinmu. “Mutumen zunubin” wanda ake kuma ce da shi “kyamar lalata,” “dan hallaka,” mai-mugunta kuma, shi ne tsarin paparuma, wanda bisa ga annabci, zai yi mulkinsa har shekaru 1260. Wannan lokacin ya kare a 1798 ne. zuwan Kristi bai faru kafin lokacin ba. Gargadin Bulus ya kunshi har zuwa 1798. Bayan nan ne za a yi shelar sakon zuwan Kristi na biyu.

Ba a taba ba da irin sakon nan a sararakin baya ba. Bulus bai yi wa’azinsa ba; ya kai hankulan yan’uwasa can gaba game da zuwan Ubangiji. Yan canji basu yi shelarsa ba. Martin Luther ya kai hukumcin har wajen shekara dari uku daga zamaninsa. Amma tun 1798 an bude littafin Daniel, sanin annabci ya karu, kuma da yawa sun yi shelar sakon nan na kusantowar hukuncin.

Kamar abban Canjin nan na karni na sha shidda, wa'azin zuwan Kristi ya gudana a kasashen Kirista dabam dabam ne a lokaci daya. A Turai da Amerika, masu bangaskiya da addu'a sun yi nazarin annabcin, suka kuma sami shaida kwakwara cewa karshen kowane abu ya kusa.

A 1821, shekara uku bayan Miller ya fassara annabcin da ya bayana lokacin hukuncin, Dr. Joseph Wolf ya fara shelar gagabtowar zuwan Ubangiji. An haifi Wolf a Jamus ne, Ba-yahudi ne, babansa kuma rabbi ne na Yahudawa. Yana dan saurayi ne ya karbi gaskiyar addinin Kirista. Yakan saurari hiran da akan yi a gidan babansa yayin da manyan Yahudawa ke magana game da bege da burin mutanensu, da darajar Masiya da ke zuwa da kuma mayaswar Israila. Wata rana da yaron ya ji an ambaci Yesu Ba-nazarat, sai ya tambaya ko wane ne shi. Aka amsa masa cewa "Wani Ba-yahudi ne mai-matukar baiwa, amma da shike ya yi da'awar cewa wai shi ne Masiyan sai hukumar Yahudawa ta masa hukumcin kisa." Sai yaron ya tambaya, "Don me aka hallaka Urushalima, kuma don me muka zama kamammu?" Sai babansa ya amsa: "Domin Yahudawa sun kashe annabawa ne." Nan da nan ya yi tunanin, "ko Yesun ma annabi ne, kuma Yahudawan suka kashe shi bai yi laifin komai ba?" Wannan tunanin ya yi karfi ta yadda ko da shike an hana shi shiga majami'ar Kirista, yakan rabe a waje, ya saurari wa'azin.

Yana dan shekara bakwai kadai ya yi ma wani Kirista tsoho makwabcinsa fariyar nasarar Israila sa'anda Masiya zai zo, sai tsohon, a natse ya ce masa: "Ya kai yaro, zan fada maka ko wane ne ainihin Masiyan: shi ne Yesu Ba-nazarat, … wanda kakanin ka suka giciye, yadda suka yi da annabawa na da. Je gida ka karanta Ishaya 53, za ka kuwa gamsu cewa Yesu Kristi ne Dan Allah." Ya kuwa je gida, ya karanta nassin, yana mamakin yadda ya acika dai dai kan Yesu Ba-nazarat. Ko maganar Kiristan nan gaskiya ce kam? Yaron ya tambayi babansa fasarar annabcin, amma irin shurun da aka masa ya sa bai sake magana a kan batun ba. Amma kuma wannan ya kara masa marmarin karin sani ne game da addinin Kirista.

A gidan su na Yahudawa an hana shi sanin da ya bida, amma sa'anda yana dan shekara sha daya kacal ya bar gidan ubansa, ya shiga cikin duniya neman ilimi ma kansa, ya kuma zabi addininsa da aikin neman abin daman gari. Da farko ya zauna a gidan ya'uwa, amma nan da nan suka kore shi cewa mai-ridda ne, cikin talauci da kadaici kuwa dole ya yi rayuwarsa tare da baki. Ya rika zuwa wurare dabam dabam yana nazari, yana kuma koyar da Ibrananci don samun abin biyan bukata. Ta wurin wani mallaminsa dan Katolika, ya karbi addinin Romawa. Ya kuma dauki kudurin zama mai-wa'azi ga mutanensa, da wannan manufar, bayan yan shekaru, ya shiga neman iliminsa a "College of the Propaganda," a Rum. A nan, halinsa na mai-fadin ra'ayinsa kai tsaye ya sa aka mai da shi mai bidi'a. A fili ya rika sokar kurakuran ekklesiya, yana kira cewa a yi gyara. Ko da shike da farko manyan 'yan paparuma sun nuna masa soyayya ta musamman, daga baya an cire shi daga Rum,

kalkashin kulawar ekklesiya ya rika zuwa wurare dabam dabam, har sai da ya bayana a fili cewa ba za su iya sa shi ya yarda da bautar tsarin Rum ba.

Sai aka bayana cewa shi mara-gyaruwa ne, aka kuma ba shi dama ya je duk inda ya ga dama. Sai ya koma Ingila, ya rungumi Kin ikon paparuma, sa'an nan ya zama dan Ekklesiyar Ingila. Bayan makaranta na shekara biyu, ya fita a 1821, ya kama aikinsa.

Yayin da Wolf ya karbi gaskiyar zuwan Kristi na farko a matsayin wanda "mai-bakinciki ne, ya saba da chiwuta," ya ga cewa annabci ya bayana zuwansa na biyu da iko da daraja kuwa. Kuma yayin da ya yi kokarin jawo mutanensa wurin Yesu Ba-bazarat, cewa Shi ne wanda aka yi alkawali, da kuma nuna masu zuwansa na farko cikin kaskanci a matsayin hadaya don zunuban mutane, ya kuma koya masu game da zuwansa na biyu a matsayin sarki mai-kubutarwa.

Ya ce: "Yesu Ba-nazarat, wanda aka soki hannuwansa da sawayensa, wanda aka kawo kamar dan rago zuwa mayanka, wanda Mai-bakinciki ne; ya saba da chiwuta, wanda bayan da an karbe sandar sarauta daga Yahuda, ikon doka kuma daga tsakanin sawayensa, ya zo da fari; zai zo na biyu a gizagizai na sama, da kafon malaiku kuma, zai kuma tsaya kan Dutsen Zaitun, kuma mulkin nan da aka ba Adamu bisa sauran halitta, ya kuma sallamar (Farawa 1:26; 3:17), za a ba Yesu. Za ya zama sarki bisa dukan duniya. Nishin halitta da makokinta za su dena, amma za a ji wakokin yabo da godiya,… Sa'an da Yesu zai zo cikin darajar Ubansa, da malaiku masu-tsarki, matattun da suka ba da gaskiya za su fara tashi. Tassalunikawa I, 4:16; Korrinthiyawa I, 15:32. Abinda Kirista ke kira tashin mattattu na farko ke nan. Sa'an nan al'ummar dabbobi za ta canja yanayinta (Ishaya 11:6-9), ta kuma koma kalkashin Yesu. Zabura 8. Salama za ta mamaye dukan halitta." "Ubangiji, kuma zai sake duban duniya, Ya ce "Ga shi kwa, yana da kyau kwarai."

Wolf ya gaskata cewa zuwan Ubangjiji ya kusa, kuma bisa ga fasararsa ta annabcin wokatai, ya nuna cewa bambancin lokacin da shi ya zata Yesun zai dawo, da lokacin da Miller ya zata 'yan shekaru kalilan ne kawai. Ga wadanda, bisa ga fadin Littafin cewa "Amma zanchen ranan nan da sa'an nan ba wanda ya sani ba," suna cewa bai kamata mutane su san komi game da kusantawar zuwan ba, Wolf ya amsa cewa: "Ubangijinmu Ya ce ba za a taba sanin rana ko sa'an ba ne? Ko bai ba mu alamun lokacin domin a kalla mu san kusantowar zuwansa, yadda akan san kusantowar bazara ta wurin zubawar ganyayen itacen baure ba? Matta 24:32. Ashe bai kamata mu taba sanin lokacin ba, alhali Shi kansa ya shawarce mu cewa mu karanta annabcin Daniel mu kuma gane shi? Kuma cikin Daniel din inda aka ce an kulle kalmomin har sai lokacin karshe, kuma da yawa za su kai da kawo (watau za su lura su kuma yi tunani game da lokacin), 'ilimi kuma za ya karu' (game da lokacin). Daniel 12:4. A nan, Ubangijinmu ba Ya nufin cewa ba za a san kusatowan lokacin ba, amma cewa daidai ranan da sa'ar ba wanda ya sani. Yana cewa ta wurin alamun wokatai za a sami isashen sanin da zai motsa mu mu shirya domin zuwansa, yadda Nuhu ya shirya jirgin.

Game da yadda aka saba fassara annabci, Wolf ya rubuta cewa: “Yawancin ekklesiyar Kirista sun kauce daga bayananniyar ma’anar Littafin, suka koma tsari irin na ‘yan addinin Budhism, suka gaskata cewa farincikin ‘yan Adam nan gaba zai kunshi yawo ne a iska, suna kuma zato cewa duk inda aka ambaci Yahudawa ana nufin al’ummai ne, inda suka ga Urushalima kuma ekklesiya ke nan; idan kuma aka ambaci duniya, sama ke nan, sa’an nan zuwan Ubangiji ci gaban kungiyoyin masu-wa’azi ke nan; kuma hawa Dutsen gidan Ubangiji shi ne babban taro na Methodist.”

Cikin shekaru ashirin da hudun nan daga 1821 zuwa 1845, Wolf ya yi tafiya sosai: a Afirka, ya ziyarci Masar da Habasha; a Asia, ya je Falesdinu da Syria da Persia da Bokhara, da Indiya. Ya kuma ziyarci Amerika, inda ya yi wa’azi a tsibirin Saint Helena. Ya isa New York cikin Agusta na 1837, kuma bayan ya yi magana a birnin, ya yi wa’azi a Filadelfiya da Baltimore, a karshe kuma ya ci gaba zuwa Washington. A nan, ya ce, “game da wata takardar roko da shugaba John Quicy Adams mai-barin gado ya kawo, a daya daga cikin Majalisun, Majalisar ta ka da kuriya gaba gadi ta ba ni izinin anfani da Zauren Majalisar don yin lacca ta, wadda kuwa na yi wata ranar Asabar, dukan ‘yan majalisar kuma suka girmama ni tawurin halartar laccar, da kuma bishop na Virginiya, da masu aikin bishara da mutanen Washington kuma. Membobin gwamnatin New Jersey, da Pennsylvania ma sun girmama ni hakanan, na ba da laccoci game da bincike na a Asia da kuma game da mulkin Yesu Kristi da kan sa.”

Dr.Wolf ya rika tafiya a kasashe mafi-kauyanci da mugunta ba tare da tsaro daga hukumomin Turai ba. Ya jimre wahaloli ga hatsaruka kewaye da shi. An yi masa duka da sanduna, ga yunwa, aka sayar da shi kamar bawa, sau uku kuma aka masa hukuncin kisa, ya gamu da mafasa, wadansu lokuta kuma ya kusa mutuwa da kishirwa. An taba kwace duk abin da yake da shi, ya yi tafiyar daruruwan mil a kafa, yana ketare duwatsu, daskararriyar iska tana karo da fuskarsa, sawayensa kuma suka kangare saboda sanyi.

Sa’an da aka gargade shi kada ya yi tafiya ba tsaro a cikin kabilu marasa mutunci, magabta kuma, “ya ce shi yana da makamai”, “watau addu’a, himma don Kristi, da amincewa da taimakonsa.” Ya ce: “An kuma tanada mani kaunar Allah da makwabci na a zuciyata, Littafi kuma yana hannuna.” Ya rika tafiya da Littafin, na harshen Ibrananci da na harshen Hellenanci ko ina ya je. Game da wata tafiyar sa ya ce: “Na rike budediyar Littafin a hannuna. Na ji a jiki na cewa karfi na yana cikin Litafin ne, kuma girmansa zai taimake ni.”

Hakanan ne ya nace cikin aikinsa har sai da aka kai sakon hukumcin ga mutane da yawa a duniyan nan. Ya raba cikin harsunan Yahudawa da Turkawa da Parsiyawa, da Hindawa da kuma kabilu da jinsuna da yawa, kuma ko ina ya dinga shelar kusantawar mulkin Masiya.

Cikin tafiye tafiyensa, a Bokhara ya tarar da wadansu makadiata masu nisa da suke koyar da sakon kusantowar zuwan Ubangiji. Larabawan Yamal, in ji shi, “suna da wani Littafi mai-suna Seera, wanda ke sanar da zuwan Kristi da mulkinsa cikin daraja, kuma suna begen cewa manyan al’amura za su faru a shekara ta 1840.” Ya ce: “A Yamal …. na yi kwana shidda da yayan Rechab. Ba sa shan barasa, ba sa shuka inabi, ba sa shuka iri, kuma suna zama a tents ne, suna kuma tuna nagarin tsohon nan Janadab, dan Rechab, na kuma tarar da ‘ya’yan Israila a cikinsu, yan kabilar Dan,… wadanda, tare da ‘ya’yan Rechab din, su ke begen zuwan Masiya cikin gizagizai na sama, da sauri.”

Wani dan mishan ma ya tarar da irin wannan koyaswar a Tatary. Wani priest na Tatar ya tambayi dan mishan din ko yaushe ne Yesu zai sake zuwa. Sa’an da dan mishan din ya ce bai san komi game da wannan ba, priest din ya yi mamaki sosai game da wannan rashin sani daga mutumin da ke kiran kansa mai koyar da Littafin, sai ya bayana nasa bangaskiyar, bisa ga annabci, cewa Kristi zai zo wajien 1844 ne.

Daga 1826, an fara wa’azin zuwan Kristi a Ingila. Aikin a can bai bi wani takamamen tsari kaman na Amerika ba, ba a koyar da ainihin lokacin zuwan ba, amma babban gaskiya na kusantowar zuwan Kristi da iko da daraja dai an koyar da shi sosai, kuma ba cikin masu musu da masu-ta da kayar baya kadai ba. Mourant Brock, wani mawallafi dan Ingila, ya ce wajen masu aikin bishara na Ekklesiyar Ingila sun rika wa’azin “wanan bishara ta mulkin.” A Birtaniya ma, an ba da sakon da ya nuna cewa 1844 ne lokacin zuwan Ubangiji. An dinga raba wallafafun rubuce rubuce daga Amerika game da zuwan Kristi din. Aka sake wallafa littafai da majallu a Ingila. A 1842 kuma, Robert Winter, haifaffen dan Ingila, wanda ya karbi bangaskiyar zuwan Kristi din a Amerika, ya dawo kasarsa ta gado don yin shelar zuwan Ubangiji. Da yawa suka hada hannu da shi cikin aikin, aka kuwa yi shelar sakon hukumcin a sassa da yawa na Ingila.

A Amerika ta kudu, a tsakiyar kauyanci da tsafi, Lacunza, dan Spain, kuma dan kungiyar Jesuit, ya sami hanyar karanta Littafin, ta haka kuma ya sami gaskiyar dawowar Kristi da sauri. Da marmarin ba da gargadin, ga shi kuma yana so ya kauce ma horon daga Rum, sai ya wallafa ra’ayoyinsa da wata suna dabam da ya ba kansa wai “Rabbi Ben-Ezra,” yana nuna kansa wai tubabben Ba-Yahudi ne. Lacunza ya yi rayuwarsa a karni na sha takwas ne, amma wajen 1825 ne aka juya littafinsa da ta shigo London zuwa turanci. Wallafawar ta kara zurfafa sha’awa a Ingila game da batun zuwan Kristi na biyu din.

A Jamus an rigaya an koyar da koyaswar a karni na sha takwas ta bakin Bengel, wani ma’aikacin bishara a ekklesiyar Lutheran, shahararren masani mai-ba yin sharhi game da aikin wadansu. Sa’anda ya gama makarantarsa, Bengel ya dukufa ga nazarin ilimin tauhidi, wanda ya je daidai da zuciyarsa ta son addini da kuma irin horon da ya samu tun kuruciyarsa. Kamar sauran samari masu-tunani, ya dinga fama da shakku da rashin fahimta na addini, ya kuma ambaci matsaloli da yawa da suka rika addabar zuciyarsu suka kuma sa samartakar sa ta zama masa da wahala. “ Da ya zama dan majalisar Warttemberg, ya ba

da shawara cewa a ba kowa ‘yancin addini”. “Yayin da ya girmama ‘yancin ekklesiya, ya dinga shawarta cewa a ba duk mai son janyewa daga cikinta sabo da lamirinsa ‘yancin ficewa. “Har yau ana cin moriyar wannan ra’ayin a kasarsa ta gado.”

Yayinda yake shirya wa’azi daga Ruya 21 ne hasken zuwan Yesu na biyu ya shigo zuciyar Bengel. Ya fahimci annabce annabcen littafin Ruya fiye da yadda ya taba fahimta. Sabo da yawan muhimmanci da darajar ababan da annabin ya gabatar, dole ya dakatar da binciken batun tukuna. A bagadi, batun ya sake zuwa masa a sarari da karfi kuma. Daga wannan lokacin ya dukufa wajen yin nazarin annabce annabcen, musamman game da karshen duniya, nan da nan kuma ya gane cewa sun nuna cewa zuwan Kristi ya kusa. Ranan da ya aza cewa ita ce ranar zuwan Kristi din ba ta yi nisa da shekaran da Miller daga baya ya aza cewa Kristi ba zai dawo ba.

An baza rubuce rubucen Bengel ko ina cikin Kirista. Da yawa a jiharsa ta Wuttenberg sun amince da ra’ayoyinsa game da annabci, haka kuma, a wadansu sassan Jamus ma. Aikin ya cigaba bayan mutuwarsa, aka kuma ji sakon zuwan Kristi a Jamus daidai lokacin da yana jan hankula a wadansu kasashe. Ba da jimawa ba wadansu masu ba da gaskiya suka je Rasha, can kuma suka kafa kungiyoyi, kuma har yanzu ekklesiyoyin Jamus suna rike da bangaskiya game da kusatowar zuwan Kristi.

Hasken ya kuma haskaka a Faransa da Switzerland. A Geneva inda Farel da Calvin suka baza gaskiyar Canjin, Gausen ya yi wa’azin zuwa na biyu din. Yayin da yake dalibi a makaranta, Gausen ya sadu da ruhun nan na dogara ga tunani maimakon bangaskiya ko wahayi, wanda ya mamaye Turai a karshen karni na sha takwas zuwa farkon karni na sha tara; kuma sa’an da ya shiga aikin bishara, bai san ainihin bangaskiya ba, har ma ya fi zama mai yawan shakka. A samartakarsa, ya yi sha’awar nazarin annabci. Bayan ya karanta littafin Rollin, mai-suna “Tarihin Zamanin Da,” hankalin sa ya koma littafin Daniel, ya kuma yi mamakin yadda annabcin ya cika daidai, bisa ga tarihi. Wannan ya zama shaida gareshi cewa Littafin hurare ne daga Allah, abin da kuma ya zama masa madogara cikin matsalolin rayuwa. Bai gamsu da koyaswoyin ra’ayin nan cewa tunani ya fi wahayi ko bangaskiya ba, kuma yayin da yake nazarin Littafin, ya sami bangaskiya mafi haske.

Yayin da ya ci gaba da binciken annabci, ya kai inda ya gaskata cewa zuwan Ubangiji Ya kusa. Sabo da muhimancin gaskiyan nan, ya yi sha’awar kawo shi gaban mutane, amma ra’ayin nan cewa annabce annabcen Daniel asirai ne da ba za a iya fahimta ba ya kawo masa cikas. A karshe dai ya kudurta kai bisharar a Geneva, zai kuma fara da yara, tawurinsu kuma zai jawo hankulan iyayen.

Daga baya ya ce: “Ina so a gane, ba don kankantan muhimmancinsa ba ne, amma sabo da yawan anfaninsa ne na so in bayana shi hakanan, na kuma sanar da shi ga yara. Na so a saurare ni, na kuma ji tsoron cewa ba za a saurare ni ba idan na fara da manya tukuna.” “Sabo da haka na kudurta farawa da kananan. Ni kan tara yara; idan yawansu ya karu, idan

an ga suna sauraro, sun ji dadi, suna sha'awa, suna ganewa har ma su fassara batun, na tabbata ba da jimawa ba zan sami kungiya ta biyu, su manya kuma za su ga cewa ya kamata su zauna su yi nazari. Idan aka yi haka, an yi nasara."

Kokarin ya yi nasara. Yayin da yake ma yaran jawabi, manya sukan zo su ji. Kowane dakin taro na majami'arsa yakan cika da masu-sauraro. Cikinsu akwai masana da masu-matsayi, da baki da ke ziyartar Geneva; ta hakanan aka kai sakon wadansu sassan.

Wannan nasarar ta karfafa Geneva, sai ya wallafa darussan sa, da niyyar karfafa nazarin litattafan annabci a ekklesiyoyi masu karshen Faransa. Ya ce: "Wallafa koyaswa da aka yi ma yara yana ce ma manya ne da ke kin kula littattafan a kan cewa wai ba za a iya gane su ba, 'Yaya ba za a iya fahimtarsu ba, tun da yaranku suna fahimtarsu?' " Ya kara da cewa: "Na yi sha'awa kwarai in sa sanin annabce annbcen ya zama abin sha'awa ga mutanenmu, idan zai yiwu." "A gani na ba nazarin da ya fi biyan bukatun zamanin." "Ta wurin wannan ne za mu shirya domin kuncin da ke zuwa ba da jimawa ba, mu kuma yi tsaro, mu jira Yesu Kristi."

Ko da shike Gausen yana daya daga cikin shahararrun masu-wa'azi da harshen Faransa, bayan wani lokaci an dakatar da shi daga aikin bishara a kan cewa ya yi anfani da Littafin don koyar da matasa, maimakon wata takardar koyarwa mara takamemmen matsayi game da bangaskiya, wadda ekklesiya ke anfani da ita. Daga bisani ya zama mai koyarwa a makarantar ilimin tauhidi, ran Lahadi kuma yakan ci gaba da aikinsa na koyar ma matasa Littafin. Rubuce rubucensa game da annabci ma sun ja hankula sosai. Daga aikin sa na shehun mallami zuwa mawallafi da mai-koyar da yara, ya yi shekaru da yawa yana tasiri kwarai, ya kuma yi aiki sosai wajen jawo hankulan mutane da yawa ga nazarin annabce annabcen da suka nuna cewa zuwan Ubangiji ya kusa.

A Scandinavia ma an yi shelar sakon zuwan Kristi, aka kuma ta da sha'awar mutane da yawa. Da yawa suka falka daga kyaliyarsu, suka furta suka kuma rabu da zunubansu, suka kuma bidi gafara a cikin sunan Kristi. Amma masu aikin bishara na ekklesiyar kasar sun yi jayayya da aikin, kuma tawurin su aka jefa wadansu masu wa'azin sakon cikin kurkuku. A wurare da yawa inda aka hana masu-shelar zuwan Ubangiji hakanan, Allah Ya aika da sakon ta hanyar al'ajibi, tawurin yara kanana. Da shike yara ne, dokar kasa ba ta iya hana su ba, aka kuma yarda masu suka yi magana babu tsangwama.

Yawancin aikin, talakawa ne suka yi, kuma a gidajen masu aikin ne mutane suka rika taruwa don jin gargadin. Yara masu wa'azin ma kauyawa ne. Wadansu basu fi shekara shida ko takwas ba, kuma yayin da rayuwarsu ta shaida cewa suna kaunar Mai-ceton, kuma suna kokarin rayuwar biyayya ga umurnin Allah, sun nuna irin basira da kwarewa da ake samu daga saransu ne kawai. Amma sa'anda suke tsaye a gaban mutane, yakan bayana a fili cewa wani iko fiye da kwarewarsu ta mutuntaka ne ke aiki a cikinsu. Muryarsu da hallayyansu sukan sake, da iko mai-saduda kuma su kan ba da gargadi game da hukumcin,

suna anfani da kalman nassin cewa, “Ku ji tsoron Allah, ku ba Shi daraja; gama sa’ar hukumshinsa ta zo.” Sun tsauta ma zunuban mutanen, ba fasikanci da mugunta kadai ba, amma suka tsauta ma son abin duniya da koma-bayan ruhaniya, suka kuma gargadi masu jinsu su yi sauri su guji fushi da ke zuwa.

Mutanen sun rika sauraro da rawan jiki. Ruhun Allah ya yi magana da zukatansu. Da yawa suka fara binciken Littafin da sabon marmari mai-zurfi, marasa kamewa da fasikai suka canja, wadansu suka rabu da rashin gaskiyansu, kuma aka yi aikin da ya yi anfani ta yadda ko ma’aikatan ekklesiyar kasar dole suka yarda cewa hannun Allah na cikin aikin.

Nufin Allah ne cewa a ba da sakon zuwan Mai-ceton a kasashen Skandivavia, kuma sa’an da aka rufe muryoyin bayinsa, Ya sa Ruhunsa cikin yara domin a gama aikin. Sa’anda Yesu Ya kai kusa da Urushalima tare da jama’a da ke farinciki, suna rairawa ta nasara da ganyayen dabino kuma a hannayen su, suna shelar cewa Shi ne Dan Dawuda, Farisawa masu kishin nan suka ce mashi Ya sa su yi shuru; amma Yesu ya amsa cewa dukan wannan cikar nabbabci ne, kuma idan wadannan suka yi shuru duwatsu za su ta da murya. Mutanen, sabo tsoron priestoci da shugabannin, suka dena shelar ta su yayin da suka shiga Urushalima, amma bayan haka yara a harabar haikalin suka daga wakar, suna kada ganyayen dabino, kuma suka rika cewa: “Hossana ga Dan Dawuda!” Matta 21:8-16. Sa’anda Farisawa cikin fushi suka ce masa: “Kana jin abin da wadannan su ke fadi?” Yesu Ya amsa: “I, ba ku taba karantawa ba, daga chikin bakin jarirai da masu shan mama ka chika yabo?” Kamar yadda Allah Ya yi ta wurin yara a lokacin zuwan Krisiti na farkon, haka kuma Ya yi ta wurinsu game da ba da sakon zuwansa na biyu. Dole maganar Allah ta cika, cewa za’a yi shelar zuwan Mai-ceton ga dukan mutane, da harsuna, da al’ummai.

William Miller da abokan aikinsa ne aka ba su wa’azin gargadin Amerika. Wannan kasar ta zama cibiyar babban aikin shelar zuwan Yesu. A nan ne annabcin sakon malaika na fari ya fi cika kai tsaye. Rubuce rubucen Miller da abokansa sun kai kasashe masu nisa. Duk inda ‘yan mishan suka shiga a duniya, an aika da labarin zuwan Kristi da sauri. Ko ina sakon bishara ta har abada ya bazu cewa; “Ku ji tsoron Allah, ku ba Shi daraja, gama sa’ar hukumcinsa ta zo.”

Shaidar annabcin da ya nuna kamar Kristi zai zo a bazarar 1844 ne ya shiga tunanin mutanen sosai. Yayin da sakon ya je daga jiha zuwa jiha, ko ina aka ta da sha’awar mutane. Da yawa sun yarda cewa fasarar annabcin game da lokaci daidai ne, kuma suka sallamar da ra’ayin su suka karbi gaskiyar. Wadansu ma’aikatan bishara suka bar ra’ayoyin darikunsu, suka bar albashinsu, da ekklesiyoyinsu, suka hada kai wajen shelar zuwan Yesu. Amma masu aikin bishara kalilan ne fa suka karbi sakon nan, sabo da haka an bar ma masu sa kai ne yawancin aikin. Manoma suka bar gonakinsu, makanikai suka bar kayan aikinsu, yan tireda suka bar kayan jarinsu, masu-aikin gwamnati suka bar matsayinsu; amma duk da haka yawan mutanen ya kasa idan aka gwada da aikin da za a yi. Yanayin ekklesiya mara bin Allah da duniya da ke kwance cikin mugunta ya dami masu tsaron, suka kuma

yarda suka jimre aiki da rashi da wahala, domin su kirawo mutane zuwa tuba da ceto. Ko da shike Shaitan ya yi jayayya da su, aikin ya ci gaba, dubbai kuma suka karbi gaskiyar zuwan Kristi din.

Ko'ina an ji shaidar, ana gargadi ga masu zunubi, 'yan duniya da 'yan ekklesiya, cewa su gudu daga fushin da ke zuwa. Kamar Yohanna mai-baftisma, wanda ya share ma Kristi hanya, masu wa'azin sun sa gatari a gindin itatuwa suka bukaci mutane su fito da 'ya'ya fa masu-isa tuba. Gargadinsu ya banbanta da tabbacin salama da zsaman lafiya da aka dinga ji daga majami'u da yawa; kuma duk inda aka ba da sakon, ya motsa mutanen. Shaidar Littafin kai tsaye da Ruhu mai-tsarki ya bayana, ya jawo ganewa kwarai. Masu addini suka falka daga gamsuwarsu ta karya, suka ga koma-bayansu, da son duniya da rashin bangaskiyansu, da fadin ransu da kuma son kansu. Da yawa suka bidi Ubangiji da tuba da tawali'u. Kaunar duniya ta koma kaunar sama. Ruhun Allah Ya sauko kansu, kuma da zukata da aka tausasa aka kuma rinjaya, suka sa hannu cikin shelar cewa; "Ku ji tsoron Allah, ku ba shi daraja, gama sa'ar hukumcinsa ta zo."

Masu zunubi cikin kuka suka ce: "Mene ne zan yi domin in sami ceto?" Masu rashin gaskiya suka nemi mayas da abinda suka karba tawurin rashin gaskiyan. Dukan wadanda suka sami salama cikin Kristi suka yi sha'awar ganin wadansu ma sun sami albarkar. Zukatan iyaye suka koma ga yayansu, zukatan 'ya'ya kuma ga iyayensu. Aka kawar da shingen girman kai. An furta laifuka da gaske 'yan gida kuma suka yi aiki don ceton kaunatattu na kusa da su. Sau da yawa akan ji addu'a da gaske da ake ma wani. Ko ina rayuka cikin bakinciki suka dinga rokon Allah. Da yawa sun dinga addu'a duk dare don samun tabbacin cewa an gafarta zunubansu, ko kuma don tubar yan-uwa ko makwabta.

Mutane kowane iri sun dinga halartar kowane taron wa'azin, mawadata da matalauta, manya da kanana, sabo da dalilai dabam dabam, da taraddadi, suka so su ji ma kansu koyaswar zuwan Kristi na biyu din. Ubangiji ya hana ruhun jayayya yayin da bayinsa suka bayana dalilin bangaskiyar su. Wani lokaci mai-wa'azin yana da kumamanci, amma Ruhun Allah Ya ba da iko ga gaskiyarsa. An ji kasancewar malaiku masu tsarki a wuraren taron nan, kuma aka kara masu bangaskiya da yawa. Yayin da aka maimaita shaidun kusantowar zuwan Kristi, jama'a da yawa suka rika sauraro shuru. Sai kace sama da duniya suna saduwa da juna. An ji ikon Allah a kan tsofoffi da yara da matasa. Mutane suka bidi gidajensu da yabo a lebunan su, sautin farincikin kuma ya cika ko ina cikin daren. Duk wadanda suka halarci taron ba za su taba manta abinda ya gudana ba.

Shelar takamammen lokacin zuwan Kristi ya jawo jayayya sosai daga mutane da yawa, daga kowane sashi, daga masu wa'azi zuwa yan banza marasa tsoron Allah ma. Kalmomin annabci sun cika cewa: "Cikin kwanaki na karshe masu-ba'a, suna bin nasu sha'awoyi, suna chewa, ina alkawalin tafowassa? Gama tunda randa ubanni suka kwanta barci, dukan al'amura suna nan kamar yadda suke tun farkon halitta. Bitrus II 3:3,4. Da jayayya game da koyaswar zuwansa na biyu din; su dai basu yarda da takamammen lokacin

ba ne. Amma idon Allah ya karanta zukatansu. Basu so su ji maganar zuwan Kristi don shar'anta duniya cikin adalci ba ne. Su bayi marasa aminci ne, ayukansu ba za su jimre binciken Allah ba, suka kuwa ji tsoron saduwa da Ubangijinsu. Kamar Yahudawa lokacin zuwan Kristi na farkon, su ma ba sa shirye su tarbi Yesu din. Ban da kin sauraron bayanai daga Littafin ma, suka kuma yi ma masu-bidar Ubangiji ba'a. Shaitan da malaikunsa suka ji dadi, suka wurga ma Kristi ba'ar a fuskarsa da fuskar malaikunsa masu tsarki cewa mutanen nasa ma ba sa kamanarsa, har ma ba sa son bayyanuwarsa.

Masu kin batun zuwan Yesu sukan dogara ga furcin nan ne. "Ba wanda ya san rana ko sa'a. Nassin ya ce: "Amma zanchen ranan nan da sa'an nan ba wanda ya sani ba, ko malaiku na sama, ko Da, sai Uban kadai." Matta 24:36. Wadanda ke neman Ubangiji suka fassara nassin daidai a bayane, amma masu jayayya da su suka yi anfani da nassin ta yadda bai kamata ba. Yesu ya fadi kalmomin nan a cinin hirarsa da almajiran ne a kan Dutsen Zaitun bayan ya bar haikalin, bari na karshe. Almajiran sun tambaya: "Mi ne kuma alamar zuwanka da cikar zamani?" Yesu Ya ba su alamu, ya kuma ce. "Lokacinda kun ga wadannan al'amura duka, ku sani ya yi kusa, har bakin kofa." Aya 3, 33.

Ba yadda za a sa wani furcin Yesu ya rushe wani furcin nasa kuma. Ko da shike ba wanda ya san rana ko sa'ar zuwansa, an umurce mu mu san lokacin da zuwan ya kusa. An kuma koya mana cewa rashin kulawa game da sanin kusantowar zuwan sa zai zama da hatsari garemu kamar yadda ya zama ma mutanen lokacin Nuhu da basu san ambaliyar ta zo ba. Kuma misalin da ke cikin suran nan din, wanda ya bambanta amintacen bawa da bawa mara aminci, ya kuma bayana kaiton wanda ya ce a zuciyarsa; "Ubangiji na yana jinkiri," ya nuna ta yadda Kristi zai mai da wadanda zai tarar da su suna tsaro, suna kuma koyar da batun zuwansa da kuma wadanda ke kinsa. Ya ce: "Ku yi tsaro fa, wannan mai-albarka ne wanda Ubangijinsa sa'anda ya zo za ya iske shi yana yin haka." Aya 42, 46 "Idan fa ba ka yi tsaro ba, ina zuwa da kamar barawo ba kwa za ka san sa'an da zan afko maka ba." Ruya 3:3.

Bulus ya yi magana game da wadanda bayanuwar Ubangiji tana zuwa misalin barawo da dare. "Suna chikin fadin, kwanchiyar rai da lafiya, sai ga hallaka farap daya ta abko masu,… ba kwa za su tsira ba ko kadan." Amma ya kara, ga wadanda suka saurari gargadin Mai-ceton: "Amma ku yan-uwa ba chikin dufu kuke ba da ranan nan za ta tarshe ku kamar barawo; gama ku duka yayan haske ne, yayan rana kwa: mu ba na dare ba ne, ba kwa na dufu ba." Tassalunikawa I, 5:2-5.

Ta hakanan aka nuna cewa Littafin bai ba mutane damar kasancewa cikin jahilci game da kusantowar zuwan Kristi ba. Amma wadanda suka so hujjar kin gaskiya suka rufe kunnuwasu, kuma masu ba'a, har ma da masu kiran kansu ma'aikatan bishara suka ci gaba da maimaita kalmomin nan "Ba wanda ya san rana ko sa'a." Sa'anda mutane suka falka, suka fara neman hanyar ceto, shugabannin addini suka shiga tsakaninsu da gaskiyar, suna nema su kwantar da hankulansu ta wurin fassara maganar Allah a karkace. Marasa aminci

suka hada kai cikin aikin mai-rudun nan, suna cewa, salama, salama, alhali Allah bai ba da salama ba. Kamar Farisawa a zamanin Kristi, da yawa sun ki shiga mulkin sama da kansu, suka kuma hana masu shiga. Za a bidi jinin mutanen nan daga hannunsu.

Mutane mafi tawali'u da dukufa cikin ekklesiyoyin ne suka fara karban sakon. Wadanda suka yi nazarin Littafin ma kansu dole suka ga kuskuren ra'ayoyi da mutane suka fi karba game da annabci, kuma duk inda tasirin masu aikin bishara bai shafi mutanen ba, sukan gwada koyaswar zuwan Kristi da Littafin ne kawai su ga cewa Allah ne tushen koyaswar.

Da yawa yan'uwansu marasa ba da gaskiya ne suka tsananta masu. Domin su rike matsayinsu a cikin ekklesiya, wadansu suka yarda su yi shuru game da begensu; amma wadansu sun ga cewa aminci ga Allah ya hana su boye gaskiyan da shi yaba su amanarta. An cire wadansu daga zumuncin ekklesiya don kawai sun bayyana bangaskiyar su game da zuwan Kristi. Gare su, kalmomin annabin sun zama da anfani sosai, cewa, "Yan'uwanku wandanda sun ki ku, su wadanda suka yasda ku sabili da sunana, sun che, Bari Ubangiji shi daukaka, domin mu ga farincikiku; amma su za su kumyata." Ishaya 66:5.

Malaikun Allah sun yi ta kallon sakamakon gargadin. Sa'anda yawancin ekklesiyoyi suka ki sakon, malaiku suka juya cikin bakinciki. Amma akwai da yawa da ba a rigaya an gwada su ba game da gaskiyar zuwan Kristi din. Da yawa mazasu da ko matansu, ko iyayensu, ko yaransu ne suka rude su, suka kuma sa suka gaskata cewa sauraron koyaswoyin Adventist na zuwan Kristi din ma zunubi ne. Aka sa malaiku tsaron mutanen nan da aminci domin wani hasken kuma zai haskaka su daga kursiyin Allah.

Da marmari kwarai wadanda suka karbi sakon suka saurari zuwan mai-cetonsu. Lokacin da suka zata zai zo ya yi. Sun kai wannan sa'ar da saduda cikin natsuwa suka huta cikin sadarwa mai-dadi tare da Allah, kwatancin salamar da za su samu nan gaba. Duk wanda ya dandana begen nan da amincewan nan ba zai iya manta sa'o'in jiran nan ba. Makonni kafin lokacin, an dakatar da yawancin harkokin duniya. Ainihin masu-bada gaskiyan suka bincika kowane tunanin zuciyarsu da kyau kamar lokacin mutuwarsu ta iso sauran sa'o'i kadan kawai. Kowa ya ga bukatar tabbacin cewa yana shirye don saduwa da Mai-ceton; fararen tufafinsu, tsabtar rai ne -halayen da aka tsrakake daga zunubi ta wurin jinin kafara na Kristi. Ina ma ace da har yanzu cikin mutanen Allah akwai wannan ruhun binciken zukatan, irin himman bangaskiyan nan. Da sun ci gaba suna kaskantar da kansu hakanan a gaban Ubangiji, suka kuma kai roke rokensu a kujerar jin kai, da suna da dandano mai-yalwar anfani fiye da wanda suke da shi yanzu. Akwai karancin addu'a, karancin amincewa, cewa an yi zunubi, kuma rashin bangaskiya na kwarai yana hana mutane da yawa alherin da mai-fansarmu ya tana da mana.

Allah Ya shirya gwada mutanensa. Hannunsa Ya rufe wani kuskuren fasarar wokatan annabcin. Adventist basu gane kuskuren ba. Kuma masanan abokan hamayyansu ma basu

gane ba. Yan hamayyan suka ce: “Lissafin ku na wokatan annabcin daidai ne. Wani babban al’amari yana gaf da faruwa, amma ba abin da Miller ke fadi ba ne, tubar duniya ne, amma ba zuwan Kristi na biyu ba ne.”

Lokacin da aka zata zai zo din ya wuce, Kristi kuma bai bayana don kubutar da mutanensa ba. Wadanda da ainihin bangaskiya da kauna suka nemi Mai-cetonsu, sun yi cizon yatsa mai daci sosai. Duk da haka an rika cika manufofin Allah. Ya gwada zukatan masu cewa suna sauraron bayanuwarsa ne. Cikinsu akwai da yawa da tsoro ne kawai ya motsa su. Furcin bangaskiyarsu bai shafi rayuwarsu ko zukatansu ba. Sa’anda al’amarin da aka yi tsammaninsa bai faru ba, mutanen nan suka ce basu sami yankan buri ba, basu taba gaskatawa ma cewa Yesu zai zo ba. Suna cikin wadanda suka fara yi ma bakincikin masu-bada gaskiyan ba’a.

Amma Yesu da dukan rundunan sama sun dubi amintattun da aka gwada su, ko da shike sun sami yankan buri. Da an bude labulen da ke raba tsakanin duniyan da ake gani da wanda ba a gani, da an ga malaiku suna kusatowa wurin amintattun nan suna kuma ba su kariya daga hare-haren Shaitan.

Babi na 21—Gargadin da Aka Ki

Cikin wa'azin koyaswar zuwan Yesu na biyu. William Miller da abokansa sun yi aikin da niyyar falkar da mutane ne su shirya domin hukumcin. Sun so su falkar da masu addini ne ga ainihin begen ekklesiya da kuma bukatarsu ta kara zurfin Kiristancinsu; sun kuma yi aikin domin falkar da wadanda basu tuba ba don bukatarsu ta tuba ga Allah nan da nan. "Basu yi kokarin tubar da mutane zuwa wata darika ko kungiyar addini ba. Dan haka sun yi aiki cikin dukan dariku da kungiyoyi, ba tare da tsoma baki cikin tsarin su ba."

Miller ya ce: "Cikin dukan aikina, ban taba sha'awa ko tunanin kafa wata kungiya dabam da darikun da suke nan ba, ko kuma in ba wani fifiko bisa wani ba. Na so duka su anfana ne. Da shike na zata cewa dukan Kirista za su yi murna game da zuwan Yesu, kuma cewa wadanda ba sa gani kamar yadda ni ke gani ba za su ki jinin wadanda za su rungumi koyaswar ba, ban zata za a taba bukatar tattaruwa dabam dabam ba. Nufi na kawai in tubar da mutane zuwa wurin Allah ne, in sanar da duniya cewa hukunci yana zuwa, in kuma motsa mutane su shirya zukatansu ta yadda za su iya saduwa da Allahnsu cikin salama. Yawancin wadanda suka tuba sakamakon aiki na, sun shiga ekklesiyoyin da ke akwai ne."

Sa'an da aikinsa ya fara inganta ekklesiyoyi, an goyi baya sa. Amma sa'anda ma'aikatan bishara da shugabannin addini suka dauki mataki sabanin koyaswar zuwan Kristi din, suka kuma so su danne kowane kokari na ta da batun, ba daga bagadi kadai suka yi hamayya da shi ba, amma suka kuma hana membobinsu damar halartar wa'azi game da zuwan Yesu na biyu, ko ma yin magana game da begensu a cikin ekklesiya. Ta hakanan masu bada gaskiya suka iske kansu cikin mumunan gwaji da rudewa. Sun kaunaci ekklesiyoyinsu, ba sa kuma so su rabu da su; amma yayin da suka ga an danne shaidar maganar Allah aka kuma hana su 'yancin su na bincike annabci, suka ga cewa biyayya ga Allah ya hana su amincewa. Suka ga cewa ba za su iya gani wadanda suka so su kulle shaidar magana kamar ekklesiyar Kristi, "madogara da dalilin dukan gaskiya ba."

Sabo da haka suka ji kawai ya kamata su rabu da kungiyoyinsu na da. Cikin bazarar 1844, wajen mutum dubu hamsin suka fice daga ekklesiyoyin. Wajen wannan lokacin an sami canji mai-yawa cikin yawancin ekklesiyoyi ko ina a Amerika. An yi shekaru da dama ana samun karin daidaituwa da ayukan duniya da alladunta, da kuma lalacewar ainihin rayuwa ta ruhaniya; amma a waccan shekarar an sami shaidar raguwa mai yawa na membobi cikin kusan dukan ekklesiyoyin kasar. Ko da shike ba wanda ya gane dalilin, ko ina an gane cewa hakan ya faru, aka kuma dinga sharhi a kan lamarin a masujadu da haridu.

A wani taron ekklesiya a Filadalfia, Mr. Barnes, wanda ya wallafa wani kundin sharhi da ko ina aka yi anfani da shi, kuma paston daya daga cikin manyan ekklesiyoyin birnin, "ya furta cewa yana aikin bishara har shekara ashirin, kuma ban da jibin da ya wuce, bai taba ba da jibi, a ce ba a sami karuwa ko raguwa a cikin ekklesiyar ba. Amma yanzu ba falkaswa, ba tuba, ba alamar ingantuwar alheri cikin masu bi, kuma ba wanda ke zuwa

wurinsa domin hira game da ceton rayukansu. Idan jari da kasuwanci da masana'antu suka karu, son abin duniya yakan karu.

A watan Fabrairu na shekara dayan, shehun mallami Finney na Oberlin College ya ce: "Muna da tunanin nan a zukatan mu cewa ekklesiyoyin kasarmu masu Kin ikon paparuma, ko basu kula ba, ko kuma sun yi gaba da kusan dukan halayyan kirki na zamanin. Ban da wadansu dai, amma yawanci haka din ne. Muna kuma da wani tabbatacen dalili, watau rashin tasirin farkaswa cikin ekklesiyoyin, ko ina. Sanyin ruhaniya kusan ko ina ne, kuma ya yi zurfi da yawa; haka masu watsa labarum dukan kasar ke fadi." Membobin ekklesiya da yawa suna zama masu bautar ado, suna hada hannu da marasa tsoron Allah suna shagulgulan jin dadi, da rawa da bukukuwa, da dai sauran su,… Amma bai kamata mu fadada wannan batu mai kawo bacin rai ba. Akwai shaida dai da ke karuwa cewa ekklesiyoyi suna kara lalacewa ne, abin bakinciki. Sun yi nisa da Ubangiji, shi kuma Ya janye kan sa daga gare su."

Kamar yadda mawallafin majalla mai-suna Religious Telescope ya rubuta, "Ba mu taba ganin lalacewar addini irin na yanzu ba. Hakika, ya kamata ekklesiya ta falka, ta bincika dalilin wannan bala'in; gama dole kowane mai-kaunar Sihiyona ya gan shi kamar bala'i. Idan muka yi la'akari da yadda mutane kalilan ne suke tuba jefi jefi, da kuma rashin tuba da taurin kan masu zunubi, irin da ba a taba gani ba, za mu kusan ihu mu ce: "Ko Allah ya manta yin alheri ne? ko kuma, Ko an rufe kofar jinkai ne?

Irin wannan yanyin ba ya aukuwa sai in da dalili cikin ekklesiya kanta. Duhun ruhaniya da kan fado ma kasashe da ekklesiyoyi da mutane ba don janyewar alherin Allah ba ne yakan faru, amma don kyalewa ko kuma kin hasken Allah ne da mutane sukan yi. Akwai misalin wannan cikin tarihin Yahudawa a zamanin Kristi. Ta wurin mannewarsu ma duniya da mantawa da Allah da maganarsa, gamsuwarsu ta duhunta, zukatansu suka zama na duniya da son sha'awa. Ta hakanan suka jahilci zuwan Masiyan, kuma cikin fadin ransu da rashin bangaskiyarsu, suka ki Mai-fansar. Ko a wancan lokacin ma Allah bai datse al'ummar Yadudawan daga sani ko sa shiga cikin albarkun ceto ba. Amma wadanda suka ki gaskiyar sun rasa sha'awar kyautar Allah. Sun mai da duhu haske, haske kuma duhu, har sai da hasken da ke cikinsu ya zama duhu; duhu mai yawa kuwa!

Shaitan yana so mutane su rike alamun addini muddan dai ba su da ruhun ibada na kwarai. Bayan sun ki bisharar, Yahudawan suka ci gaba da rike al'adun su na da, suka kiyaye rashin cudanyansu da sauran mutane, alhali dukansu sun amince cewa kasancewan Allah ba ya tare da su kuma. Annabcin Daniel ba kuskure ya bayyana lokacin zuwan Masiyan, ya kuma yi annabcin mutuwarsa kai tsaye, ta yadda su kuma suka hana yin nazarinsa, a karshe kuma mallamansu suka furta la'ana kan dukan wanda ya yi kokarin sansance lokacin. Cikin makanta da rashin tuba mutanen Israila cikin sararaki na biye sun nuna halin kin kulawa da tayin ceto da ake masu, basu damu da albarkun bishara ba, ga kashedi mai ban tsoro kuma game da hatsarin kin haske daga sama.

Duk inda dalili yake, sakamako dayan ake samu. Duk wanda da gangan ya bice lamirin sa game da abinda ya kamata yayi, don kawai bi je daidai da muradin zuciyar sa ba, a karshe zai kasa bambantawa stakanin gaskiya da kuskure. Ganewarsa za ta duhunta, lamiri ya kangare, zuciyata taurara, har mutumin ya rabu da Allah. Idan aka yi banza da sakon Allah, ekklesiya takan nannadu cikin duhu, bangaskiya da kauna sukan yi sanyi, tsatsaguwa kuma takan shigo. 'Yan ekklesiya sukan kallafa ransu ga kayan duniya, masu zunubi kuma su taurara cikin rashin tuba.

Sakon malaika na fari na Ruya 14 da ke shelar sa'ar hukumcin Allah, yana kuma kiran mutane su ji tsoron Allah, su yi masa sujada, an shirya shi ne ya raba mutanen Allah, su yi masa sujada. An shirya shi ne ya raba mutanen Allah daga tasirin lalacewa na duniya, ya kuma falkas da su su ga ainihin yanayinsu na zunubi da sanyin ruhaniya. A wannan sakon, Allah Ya aika ma ekklesiya gargadi wanda da an karba, da ya gyarta muguntan da yake raba su da shi. Da sun karbi sakon nan daga sama, suka kaskantar da kansu a gaban Ubangiji, suna kuma bidar shiri domin tsayawa a gabansa, da Ruhun Allah da ikonsa sun bayana a cikinsu. Da ekklesiya kuma ta sake samun hadin kai da bangaskiya da kaunan nan da ta kasance da su a zamanin manzanin, lokacin da masu bi suka kasance "zuchiyarsu da ransu kuma daya," kuma "suka fadi maganar Allah da karfin zuchiya," sa'an da Ubangiji kuma "yana tattarawa yau da gobe wadanda ake chetonsu," Ayukan 4:32, 31; 2:47.

Idan mutanen Allah za su karbi hasken da ke haskaka su daga maganarsa, za su kai ga dayantakan nan da Kristi ya yi addu'a su samu, wadda manzon ya bayyana kamar "danyantuwar Ruhu chikin damrin salama." Ya ce: "Akwai jiki daya, da Ruhu daya, kamar yadda aka kiraye ku kuma chikin begen nan daya na kiranku, Ubangiji daya, imani daya, baptisma daya." Afisawa 4:3-5.

Irin sakamakon da wadanda suka karbi sakon zuwan Kristi suka samu ke nan. Sun fito dariku dabam dabam, aka kuma watsar da bambancin darika a kasa, aka kacancana bambancin koyaswa suka zama burbushi, aka yi watsi da begen nan na wadansu shekaru dubu a duniyan nan, aka grarta ra'ayoyin karya game da zuwan Kristi na biyu, aka share girman kai da sajewa da duniya, aka gyara kurakurai; zukata suka hadu cikin zumunci mafi dadi, kauna da murna kuma suka yawaita. Da shike koyaswan nan ta yi dukan wadannan ga kalilan da suka karbe ta, da kowa ya karbe ta ma da ta yi ma kowa hakanan ma.

Amma yawancin ekklesiyoyin basu karbi gargadin ba. Ya kamata da shugabanninsu ne suka fara gano alamun zuwan Yesu, amma suka kasa gane gaskiyar, ko daga annabci ko kuma daga alamun zamanai. Sa'anda buri da begen abin duniya suka cika zuciya, kaunar Allah da bangaskiya ga maganarsa sun yi sanyi, kuma sa'anda aka yi shelar koyaswar zuwan Yesu, ya ta da kiyayarsu da rashin bangaskiyarsu ne kawai. Da shike galibi masu sa kai ne suka yi wa'azin sakon, aka ce wannan ya nuna gazawar sakon. Kamar da, aka tare bayyananiyar shaidar maganar Allah da tambaya cewa: "A chikin hakimai, ko chikin Farisawa, akwai wadanda sun ba da gaskiya gare shi?" Kuma da shike an kasa karyata

koyaswoyin da aka samo daga annabcin zamanun da yawa suka yi kokarin hana nazarin annabcin, suka koyar da cewa an kulle littattafan annabci, kuma ba za su fahimce su ba. Jama'a da yawa da suka amince da pastocinsu, suka ki jin gargadin annabcin, wadansu kuma, ko da shike sun gamsu da gaskiyar, basu iya furta ta ba, domin kada a fitar da su daga ekklesiya. Sakon da Allah ya aika domin gwadawa da tsarkakewar ekklesiya ya bayana, ba shakka, yawan jama'ar da suka ba da zukatansu ga duniyan nan maimamakon Kristi. Suka so su saurari muryar hikimar duniya suka juya daga sakon gaskiya.

Ta wurin kin gardadin malaika na farin, sun ki hanyar da Allah ya tanada don mayaswarsu. Sun ki dan sakon da ya kamata ya gyarta muguntar da ta raba su da Allah, suka kuma juya suka nemi abotar duniya. Dalilin son duniya da sanyin ruhaniya da mutuwa ta ruhaniya da suka kasance cikin ekklesiyoyi a 1844 ke nan.

Cikin Ruya 14, malaika na biyu ya bi na farkon yana shela cewa: "Ta fadi, Babila babba ta fadi, ita wadda ta sa dukan al'ummai sun sha ruwan anab na hasalar faskancin ta." Ruya 14:8. Kalman nan "Babila" daga "Babel" ne, ma'anarsa kuma, birkicewa. Ana anfani da shi a Littafin don bayana yanayin dabam dabam na addinin karya ne. Cikin Ruya 17, an bayana Babibla kamar mace, Littafin kuma yana anfani da kalman nan "mace" kamar alamar ekklesiya, mace mai halin kirki ekklesiya mai-tsarki ke nan, mace mai halin banza kuwa ekklesiya mai-ridda.

Cikin Littafin, yanayi mai-tsarki mai jurewa kuma na dangataka da ke tsakanin Kristi da ekklesiyarsa ana kamanta shi da aure ne. Ubangiji ya hada mutanensa da shi kansa ta wurin alkawali mai-nauyi inda yake alakwalin zama Allahnsu, su kuma suna alkawalin zama nasa Shi kadai. Ya ce: "Zan damra alkawalin aure da ke har abada; I, chikin adilchi, da chikin shari'a, da rahama, dajin kai." Hosea 2:19. Ya kuma ce; "Ni miji ne a gareku." Irmiya 3:14. Bulus kuma ya yi anfani da wannan alamar a Sabon Alkawali inda ya ce: "Na damre amrenku ga miji daya domin in mika ku budurwa mai-tsabta ga Kristi." Korinthiyawa II, 11:2.

Rashin amincin ekklesiya ga Kristi tawurin kawar da kaunar ta da amincin ta daga gare shi, da barin son kayan duniya ya mallaki rayuwar, ana kamanta shi da ketarewar alkawalin aure ne. Ana bayana zunubin Israila na rabuwa da Ubangiji da wannan alaman ne, ana kuma bayana kaunar Allah da suka rena hakanan: "Na rantse maki, na kwa yi alkawali da ke, in ji Ubangiji Yahweh, kin zama tawa." "Kin zama kyakyawa kwarai da gaske kin yi arziki har kin kai matsayin sarauta. Sunanki ya tafi ko ina wurin al'ummai domin jamalinki; gama ya chika, tawurin daukaka ta da na sa maki." Amma kin dogara ga jamalin ki, kin yi karuwanchi domin girman sunanki," "kamar yadda mace maciyar amana ta kan bar mijin ta, hakanan kun chi amana da ni, ya gidan Israila, in ji Ubangiji." "Matar aure mazinaciya, mai daukan baki maimakon mijinta." Ezekiel 16:8, 13-15, 32; Irmiya 3:20.

Ana anfani da irin wannan magana cikin Sabon Alkawali game da Kirista masu neman abotan duniya fiye da alherin Allah. Manzo Yakub yace: “Ku mazinata, ba ku sani ba abutar duniya magabtaka che da Allah? Dukan wanda yake so ya zama abokin duniya fa yana mai da kansa magabcin Allah.”

Macen (Babila) na Ruya 17 an bayana cewa “tana yafe da shunaiya da mulufi, tana ado da zinariya da duwatsu masu tamani da lu’ulu’ai chikin hannunta tana da koko na zinariya chike da kazamche-kazamche, watau abubuwa masu - dauda, … bisa goshinta kuma da suna a rubuce, “ASIRI, BABILA BABBA, UWAR KARUWAI”. Annabin ya ce: “Na ga machen kuma tana maye da jinin tsarkaka, da jinin shaidu na Yesu.” An kuma bayana cewa Babila “babban birnin ne wanda ke mulki bisa sarakunan duniya.” Ruya 17:4-6,18. Mulkin da ya yi daruruwan shekaru yana yi ma sarakunan kasashen Kirista mulkin daniya shi ne Rum. Launin shunaiya da mulufi, da zinariya da duwatsu masu tamani suna bayana kyau da alfarman da Rum ta mallaka ne. Kuma ba wani mulkin da za a ce ya yi “maye da jinin tsarkaka” kamar mulkin nan da ya zalunci masu bin Kristi. Ana kuma zargin Babila da zunubin dangantaka ba bisa doka ba da “sarakunan duniya.” Ta wurin rabuwa da Ubangiji, da abuta da kafirai ne ekklesiyar Yahudawa ta zama karuwa; Rum kuma da shike ta lalata kanta hakanan tawurin neman hadin kan mulkokin duniya, ta sami hukumci dayan.

An ce Babila ce “uwar karuwai.” Ya nuna cewa ‘ya’yanta su ma dole ana misalta su da ekklesiyoyin da su ke rike da koyaswoyinta da al’adunta ke nan, suna kuma bin kwatancinta na sadakar da gaskiya da nufin Allah domin hada abuta ba bisa doka ba da duniya. Dole sakon Ruya 14 dake shelar faduwar Babila, yana magana kan kungiyoyin addini ne da suka taba kasancewa tsarkaka amma suka lalace. Da shike sakon nan yana bin gargadin hukukumcin ne, dole a kwanakin karshe ne za a ba da shi, sabo da haka ba ekklesiyar Rum kadai yake magana a kai ba, da shike wannan ekklesiyar ta kasance fadaddiya na daruruwan shekaru. Biye da haka, a Ruya 18 ana kira ga mutanen Allah su fito daga cikin Babila.

Bisa ga nassin nan akwai mutanen Allah har yanzu a cikin Babila ke nan. Kuma a wadanne kungiyoyin addini ne yawancin masu bin Kristi suke yau? Ba shakka, a cikin ekklesiyoyi masu kin ikon paparuma ne. Lokacin da suke tasowa, ekklesiyoyin nan sun dauki matsayi mai kyau don Allah da gaskiya, kuma albarkansa ya kasance tare da su. Ko marasa bi ma sun yarda cewa sakamakon amincewa da kaidodin bishara ya haifar da sakamako masu anfani. Ta bakin annabi zuwa ga Israila: “Sunanki ya tafi ko ina wurin al’ummai domin jamalin ki, gama ya chika ta wurin daukaka ta da na sa maki, in ji Ubangiji Yahweh.” Amma sun fadi tawurin sha’awa dayan wanda ya zama la’ana da rushewar Israila - sha’awar kwaikwayon halayya da neman abutan marasa bin Allah. Kin dogara ga jamalin ki, kin yi karuwanci domin girman sunan ki.” Ezekiel 16:14, 16.

Yawancin ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma suna bin kwatancin Rum na dangantakar zunubi da “sarakunan duniya ne” - ekklesiyoyin kasa tawurin dangantakarsu

da gwamnatocin duniya, sauran dariku kuma ta wurin neman goyon bayan duniya. Kuma za a iya kiran ekklesiyoyin nan “Babila,” watau birkicewa, ko da shike dukansu suna cewa suna samun koyasuyoyinsu daga Littafin ne, amma sun rarrabu zuwa dariku da ba a iya lisaftawa ba, da koyaswoyi daban dabam da ke saba ma juna.

Ban da abutan zunubi da duniya, ekklesiyoyin da suka rabu da Rum suna kuma nuna wadansu halayyan ta.

Wani littafin Katolika ya ce: “Idan ekkelsiyar Rum ta taba laifi game da tsarkaka, diyar ta, Ekklesiyar Ingila, ma ta yi laifi dayan domin tana da ekklesiyoyi goma da suka kallafa kansu ga Maryamu duk inda take da guda daya da ta kallafa kan ta ga Kristi.”

Dr. Hopkins kuma ya ce: “Ba dalilin da za a ce Ekklesiyar Rum ce kadai mai ruhu da ayukan sabani da Kristi. Ekklesiyoyin masu Kin ikon paparuma suna da sabani da Kristi a cikin su, kuma suna da nisa daga Canji daga… lalacewa da mugunta.”

Game da rabuwar Ekklesiyar Presbyterian daga Rum, Dr. Guthrie ya rubuta cewa: “Shekaru dari uku da suka gabata, ekklesiyarmu, da budadden littafi a tutarta, da kuma taken nan, “Binciken Littafin,” a kambinta, ta fice daga kofofin Rum.” Sa’an nan ya yi tambaya mai ma’ana: “ko sun fito sarai daga Babila?”

Spurgeon ya ce: “Ekklesiyar Ingila, kamar tsare-tsaren ibada sun cinye ta, amma rashin bin abin da aka saba, shi ma kaman yana fama da rashin aminci. Wadanda muka yi tsanamanin ababa mafi-kyau, suna juyawa daya daya daga asalin bangaskiyar. Na ba da gaskiya ainihin cibiyar Ingila ta cika da rashin aminchi wanda ke kiran kansa Kiristanci.

Menene tushen babban riddar? Yaya aka yi ekklesiya ta fara rabuwa da saukin kan bishara? Tawurin bin ayukan kafirci, domin Kiristanci ya sami karbuwar kafirai. Manzo Bulus ya ce, ko a zamaninsa ma “asiri na taka sharia yana ta aikawa ko yanzu.” Tassalunikawa II, 2:7. Lokacin rayuwar manzain, ekkesiya ta kasance da tsarki. “Amma zuwa karshen karni na biyu yawancin ekklesiyoyi sun dauki sabon kamani, saukin kai ya watse, kuma yayin da tsofofin almajiran suka mutu, yaransu, tare da sabobin tuba suka shigo suka sake salon aikin.” Domin a sami masu tuba sai aka rage ingancin imanin Kirista, sakamakon haka kuwa “ambaliyar kafirci ta shigo cikin ekklesiya tare da al’adun ta da gumakanta.” Sa’anda addinin Kirista ya sami goyon bayan shugabannin kasa, jama’a da yawa sun karbi addinin sama - sama; amma yayin da a ganin ido Kirista ne su, yawancinsu sun “kasanche ainihin kafirai, musamman ma suna bautar gumakansu cikin sirri.”

Ba a maimaita matakai dayan a kusan kowace ekklesiya mai Kin ikon paparuma ba? Sa’anda masu kafa ekklesiyar sun mutu zuriyarsu sukan guso su sabunta salon aikin. Yayin da suke manne ma koyaswar ubaninsu a duhunce, suna kuma kin karban karin gaskiyar, yaran masu-canjin sukan kauce daga kwatancin tawali’un iyayen, da musun kansu, da kin

duniyansu. Ta hakanan saukin kan farko yakan bata. Ambaliyar duniya takan shigo cikin ekklesiya, “tare da al’adu, da ayuka, da gumakanta.

Abin tsoro ne kuwa abutan nan da duniya wadda gaba ce da Allah, wanda masu bin Kristi suke yi yanzu. Dubi yawan kaucewa da sanannun ekklesiyoyi suka yi daga koyaswar Littafin game da tawali’u da musun-kai, da saukin kai, da tsoron Allah! Game da anfani da kurdi yadda ya kamata, John Wesley ya ce: “Kada a yi barnar muhimmin talent din nan mai-daraja wajen biyan bukatar sha’awar ido, ko tufafi, masu tsada ko masu yawa, ko kuma kayan ado da ba a bukata. Kada a lalata shi wajen yawan kayan gida ko kuma tsadarsu, ko hotuna… kada a yi ajiya don biyan muradin alfarmar rai, ko neman sha’awar mutane ko kuma yabonsu. ‘Muddan kana aikata nagarta, mutane za su yaba maka.’ Muddan kana ‘sa sutura masu tsada’ kana kuma holewa mutane da yawa za su yabi adonka da yawan kyautanka da liyafarka. Amma kada ka sayi yabonsu da tsada hakanan. Maimaikon haka, ka gamsu da daukakan da ke zuwa daga Allah.” Amma ekklesiyoyi da yawa a zamaninmu, ba a kula irin koyaswan nan.

Da’awar cewa ana addini ya mamaye duniya. Shugabanni, ‘yan siyasa, lauyoyi, likitoci, ‘yan kasuwa, suna shiga ekklesiya don samun ban girma da amincewar jama’a, da kuma ci gaban kansu a duniya. Ta hakanan sukan so su rufe dukan laifofinsu da sunan Kiristanci. Kungiyoyin addini, da goyon bayan arziki da tasirin ‘yan duniyan nan da aka masu baptisma, sukan kara neman suna da samun sabobin membobi. Ana gina manyan majami’u da ake yi masu ado a yalwace, a manyan tituna. Masu sujada sukan yi ado mai tsada wanda ake yayi. Akan biya albashi mai-yawa ma wani mai-bishara wawnda ke da baiwa domin ya ba mutane nishadi ya kuma jawo hankulan mutanen. Wa’azinsa ba zai shafi zunuban da an cika aikatawa ba, amma wa’azin yakan zama mai sumul, mai gamsar da ‘yan zamani kuma. Ta hakanan akan sami ‘yan zamani su zama ‘yan ekklesiya, zunubansu na zamani kuma akan rufe su da imani na karya.

Game da halayyan Kirista yanzu, game da duniya, wata shahararriyar majalla, ba ta addini ba, ta ce: “Ba tunani, ekklesiya ta amince da ruhun zamanin, ta canja yanayin sujadar ta zuwa abinda zamani ke so.” “Hakika ekklesiya tana anfani da duk ababan da ke sa addini ya zama abin sha’awa.” Wani mawallafi a jaridar “New York Independent” kuma ya yi magana game da ekklesiyar Methodist, cewa: “Bambanci tsakanin masu addini, da marasa addini ya shude, masu himma a kowane gefen kuma suna kokari su share banbancin da ke tsakinin irin halayyansu da jin dadi.” Farin jinin addini yakan kara yawan masu son anfaninsa ba tare da cika bukatunsa ba.”

In ji Howard Crosby: “Abin damuwa ne kwarai cewa ekklesiyar Kristi ba ta cika nufin Ubangijita. Kamar yadda Yahudawa ne da suka bar sabawa da yin ma’amala da al’ummai masu bautar gumaka ya sace zukatansu daga Ubangijin…. Haka ekklesiyarmu yanzu, ta wurin hadin kansu da duniya mara ba da gaskiya, da barin hanyoyin Allah da kuma hada kanta da halayyan jama’a na rashin ibada, ko da shike suna da ban sha’awa, tana anfani da

ra'ayoyin nan tana kuma samun sakamakon da sun bambanta da wahayin Allah, tana gaba kai tsaye kuma da batun girma cikin alheri."

Cikin wannan malalar sha'awar duniya da neman jin dadi, musun kai da sadakarwa don Kristi sun kusa shudewa gaba daya. "Wadansu maza da mata masu kwazo a ekklesiyoyinmu yau an ilimantar da su tun suna yara su yi sadakarwa domin su iya bayaswa ko yin wani abu don Kristi." Amma "idan ana bukatar kurdade yanzu,… bai kamata sai an ce ma wani ya bayas ba. Da ma a ce za a yi wata wasar kwaikwayo, ko liyafa, ko cin abinci, wani abu dai da zai ba mutane dariya.

Gwamna Washburn na Wisconsin, cikin sakonsa a shekara - shekara, ran 9 ga Janairu, 1873 ya ce: "Ya kamata a yi wata doka don wargaza makarantu inda ake haifar da yan caca. Suna ko ina, ko ekklesiya ma (ba da sanin ta ba dai) akan iske tana aikin iblis wani lokaci jari ko rehul na kyautattuka, wasu lokuta don taimakon addini ko aikin agaji, amma sau da yawa sabo da ababa da basu kai wadannan ba, ababan nan hanyoyi ne na samun kurdin banza. Ba abinda ya fi kashe jiki ko bugarwa, musamman ga matasa, kamar samun kurdi, ba tare da yin aiki ba. Mutane da ake ba su girma ma suna shiga irin ayukan nan, su kuma ba kansu hujja cewa abu mai kyau ne za a yi da kurdin. Ba abin mamaki ba ne kuwa a iske matasa suna shiga halayyan.

Ruhun daidaituwa da duniya yana shigowa ekklesiyoyi ko ina. Robert Atkins cikin wa'azinsa a London ya nuna munin lalacewar ruhaniya da ta mamaye Ingila, ya ce: "Masu ainihin dalci suna raguwa a duniya, kuma ba wanda ya kula, masu addini a zamanin nan, a kowace ekklesiya, masu kamnar duniya ne, masu daidaituwa da duniya, masu kaunar holewa da masu neman bangirma. An kiraye su su sha wahala don Kristi, amma suna gudun reni ma, … Ridda, ridda, ridda, aka zana a gaban kowace ekklesiya; kuma da sun sani, da akwai bege, amma ina! Suna cewa, "Na wadata, na sami dukiya, ban bukachi komi ba."

Babban zunubin da aka zargi Babila da ita shi ne cewa "ta sa dukan al'ummai su sha ruwan annab na hasalar fasikancinta." Kokon mayen nan da take mika ma duniya shi ne koyaswar karya da ta karba, sakamakon hada kanta da shugabanin duniya. Abota da duniya yana lalata imaninta, ita kuma tana mumunan tasiri ga duniya tawurin koyar da koyaswoyin da ke sabani da maganar Littafin.

Rum ta hana ma mutane Littafin, ta kuma bukaci kowa ya yarda da koyaswoyinta a maimako. Aikin canjin ne shi mayar da maganar Allah ma mutane, amma ko ba gaskiya ba ne, cewa a ekklesiyoyin zamaninmu ana koya ma mutane su dangana bangaskiyarsu kan koyaswoyin ekklesiyarsu maimakon Littafin ba? Game da ekklesiyoyin masu Kin ikon paparuma, Charles Beecher ya ce: "Suna tsoron fadin wata kalmar zargi game da koyaswa, daidai da yadda su Fada suke tsoron fadin wata kalmar zargi sabanin sujada ga tsarkaka da wadanda aka kashe don imaninsu,… Darikun masu Kin ikon paparuma sun daure hannuwansu da na juna ta yadda tsakaninsu duka, mutum ba zai zama mai-wa'azi ba a wani

wuri sam sam, ba tare da karban wani littafi dabam da Littafi Mai-tsarki ba,… Ba karya ba ce cewa ikon koyaswa yanzu ya fara hana Littafin daidaida yadda Rum ta yi, ko da shike a hankali ne."

Sa'anda amintattun mallamai suka bayana maganar Allah, wadansu masana, da pastoci masu cewa sun fahimci Littafin, da sukan yi sokar sahihiyar koyaswa cewa ridda ce, ta hakan kuma sukan hana bincike game da gaskiyar. Da ba don duniya ta yi maye da ruwan anab na Babila ba, da jama'a da yawa za su tuba tawurin bayananiyar maganar Allah. Amma addini ya rikice ta yadda mutane basu san abin da za su gaskata kuma ba, alhakin zunubin rashin tuban duniya yana kan ekklesiya ne.

An fara wa'azin sakon malaika na biyu na Ruya 14 da daminan 1844 ne, kuma lokacin ya fi cika kai tsaye ga ekklesiyoyin Amerika inda aka fi shelar gargadin game da hukumcin, aka kuma fi kin gargadin, inda kuma lalacewar ekklesiyoyin ya fi sauri. Amma sakon malaika na iyu din bai cika duka a 1844 ba. A lokacin, ekklesiyoyin sun sami faduwa na halayyan kirki, sakamakon kin hasken zuwan Kristi da suka yi, amma faduwar ba ta cika ba. Yayinda suke ci gaba da kin gaskiyar wannan zamani, suna ci gaba da faduwa ne. Amma har yanzu ba za a ce "Babila ta fadi,… ita wadda ta sa dukan al'ummai su sha ruwan anab na hasalar fasikanchinta" ba. Ba ta rigaya ta sa dukan al'ummai su yi haka ba. Ruhun dayantuwa da duniya da rashin kula da gaskiyar zamaninmu yana nan kuma yana ci gaba cikin ekklesiyoyi masu Kin ikon aparuma a dukan kasashen Kirista, kuma ekklesiyoyin nan suna cikin soka mai-tsanani da nauyin nan na malaika na biyu din. Amma aikin ridda bai rigaya ya kai cikar sa ba.

Littafin ya ce kafin zuwan Ubangiji, Shaitan zai yi aiki "da dukan iko da alamu da al'ajibai na karya, da dukan rudami na rashin adilchi," kuma wadanda "basu amsa kamnar gaskiya domin su tsira ba," za a barsu su karbi "aikawar sabo, har da za su gaskanta karya." Tassalunikawa II, 2:9-11. Sai an kai wannan yanayin, aka kuma kamala hadewar ekklesiya da duniya ko ina a kasashen Kirista, kafin faduwar Babila ta cika. Canjin yana ci gaba ne, kuma Ruya 14:8 bai gama cika ba tukuna, sai nan gaba.

Duk da duhun ruhaniya da rabuwa da Allah da ke cikin ekklesiyoyin da Babila ta kunsa, akwai babban akwai jama'ar Kristi, watau amintattu masu binsa a cikinsu. Da yawa cikin su basu taba ganin muhimman gaskiya na wannan zamani ba. Da yawa basu gamsu da yanayin su na yanzu ba, suna kuma begen karin haske. A banza suke neman ganin surar Kristi a cikin ekklesiyoyinsu da suke ciki. Yayin da ekklesiyoyin nan suke kara rabuwa da gaskiya, suna kuma kara hada kansu da duniya, bambanci tsakaninsu zai kara fadi, zai kuma kai ga rabuwa daga bisani. Lokaci na zuwa da masu kaunar Allah fiye da komi ba za su kara kasancewa tare da wadanda su ke "mafiya son annishuwa da Allah; suna rike da surar ibada, amma sun musunchi ikonta" ba.

Ruya 18 yana nuna lokacin da, sakamakon kin gargadin Ruya 14:6-12, ekklesiya za ta kai cikar yanayin da malaika na biyu din ya yi annabcinsa; kuma mutanen Allah da ke cikin Babila za a bukace su su rabu da ita. Sakon ne na karshe da za a taba ba duniya, zai kuma cim ma manufarsa. Sa'anda za a bar wadanda basu gaskata gaskiya ba, amma suka kaunaci rashin adalci (Tasalunikawa II, 2:12), su karbi rudami mai karfi, har su gaskata karya, sa'an nan ne hasken gaskiya zai haskaka dukan wadanda zukatan su ke bude domin karbanta, kuma dukan 'ya'yan Ubangiji da ke cikin Babila za su ji kiran: "Ku fito daga chikinta, ya al'ummata." (Ruya 18:4).

Babi na 22—Cikawar Annabci

Sa’anda lokacin da aka sa tsammani Ubangiji zai zo ya wuce - a bazarar 1844 - wadanda suka yi zaman bangaskiya don bayanuwarsa sun yi zaman shakka da rashin tabbaci. Yayin da duniya ta duaka cewa an ka da su, an kuma nuna cewa an rude su ne, abinda ya share masu hawaye shi ne maganar Allah din dai. Da yawa sun ci gaba suna nazarin Littafin, suna sake bincika shaidun bangaskiyarsu, suna kuma nazarin annabci a hankali don samun Karin haske. Shaidar Littafin da ta goyi bayan matsayinsu ta kasance a sarari, tabbataciya kuma. Allamu tabbatattu sun nuna cewa zuwan Kristi ya kusa. Albarkar Ubangiji, cikin tubar da masu zunubi da falkas da rayuwar ruhaniya cikin Kirista, ta nuna cewa sakon daga sama ne. Kuma ko da shike basu iya gane dalilin yankan burin su ba, sun tabbata cewa Allah ne ya bishe su kafin wannan lokacin.

Garwaye da annabce annabcen da suka dauka cewa sun shafi lokacin zuwan Kristi na biyu akwai magana da ya je daidai da yanayin rashin tabbacin su da jiran tsammanin su, wanda kuma ya karfafa su su jira da hakuri cikin bangaskiyar cewa abin da ya shiga masu duhu yanzu za a bayyana shi a daidai lokaci.

Cikin annabce annabcen akwai na Habakuk 2:1-4: “Zan tsaya wurin tsaro na, in tsaya a bisa hasumiya, in duba, in ga abinda za ya fada mani, da abinda zan amsa masa a kan karata. Ubangiji ya amsa mani, ya che, ka rubuta, ta fita a fili chikin alluna, domin mai-karantawa shi yi a guje. Gama ruyan har yanzu da ayanannen lokachinta, tana kwa gaggabta zuwa matukan, ba kwa za ta yi karya ba, ko ta jima, dakanta mata, gama lallai za ta zo, ba za ta yi jinkiri ba. Duba, ransa ya kumbura, ba daidai yake ba a chikinsa, amma adili ta wurin bangaskiyassa, za ya rayu.”

Tun 1842, umurnin da annabcin nan ya bayar, cewa “ka rubuta ru’yan ta fita a fili chikin al’uma, domin mai-karantawa shi yi a guje,” ya nuna ma Charles Fitch zancen shirya wata taswirar annabci da za ta bayana wahyin Daniel da Ruya. An dauka cewa wallafawar taswiran nan cikar annabcin Habakuk ne. Amma kuma ba wanda ya lura cewa annabci dayan ya nuna cewa za a sami jikiri kadan kafin a cika annabcin. Bayan yankan burin, muhimmancin nassin nan ya bayana: “Gama ru’yan har yanzu da ayanannen lokachinta, tana kwa gagabta zuwa matukan, ba kwa za ta yi karya ba, ko ta jima, dakanta mata, gama lallai za ta zo, baza ta yi jinkiri ba,… adali tawurin bangaskiyarsa za ya rayu.”

Wani sashin annabcin Ezekiel ma ya kasance abin karfafawa da ta’azantarwa ga masu bi. “Maganar Ubangiji kwa ta zo gareni chewa, Dan mutum, mi ne wannan karin magana da ku ke yi a kasar Israila, kuna chewa, kwanaki sun dade, kowache ru’ya kwa ta kan lalache? Ka fada masu fa, in ji Ubangiji Yahweh,… zan yi magana, magana da na fadi kwa za a chikata, ba za ta sake yin jinkiri ba.” “Mutanen gidan Israila suna cewa, Ru’ya da yake gani zanchen kwanakin gaba ne da nisa tukuna, yana annabcin zamani na nesa. Ka che

masu fa, ga abinda Ubangiji Yahweh ya fadi, ba za a kara jinkirtadda maganata ba ko daya, amma magana da na fadi za ta chika, in ji Ubangiji Yahweh." Ezekiel 12:21-25,27,28.

Masu jira suka yi farinciki, da sanin cewa shi wanda Ya san karshe daga farkon ya dubi dukan sararaki, da ya hangi cizon yatsan, sai ya ba su kalmomin na karfafawa da bege. Ba don irin nassosin nan da suka shawarce su su jira cikin hakuri su kuma rike amincewar su ga maganar Allah ba, da bangaskiyarsu ta kasa a lokacin gwajin nan.

Misalin budurwai goman nan na Matta 25 ma yana bayana abin da ya faru da 'yan Adventist din. Cikin Matta 24, cikin amsa tambayar almajiran game da alamar zuwansa da na karshen duniya, Kristi ya bayaan wadansu al'amura mafi hunimmanci cikin tarihin duniya da na ekklesiyarsa, daga zuwan sa na farko har zuwansa na biyu; su ne, hallakawar Urushalima, babban kuncin ekklesiya kalkashin tsanantawan kafirai da na paparuma, duhuntawar rana da wata da kuma faduwar taurari. Bayan wannan, ya yi maganar zuwan mulkinsa, ya kuma ba da misalin bayi iri biyu da ke sauraron bayanuwarsa. Sura 25 ya fara da kalmomin nan: "Sa'an nan za a iske mulkin sama yana kama da budurwai goma." A nan ana maganar ekklesiyar kwanakin karshe ne, wadda it ace aka ambata a karshen sura 24. A wannan misalin, an kwatanta yanayinsu da al'amuran aure na kasashen Gabas.

"Sa'an nan za a iske mulkin sama yana kama da budurwai goma, wadanda suka dauki fitillunsu, suka fita garin su tarbi ango. Biyar daga chikinsu marasa- azachi ne, biyar masu hikima ne. Gama marasa azanchin nan, da suka dauki fitillunsu, basu dauka duk da mai ba: amma masu-hikima suka dauki mai chikin santulansu tare da fitillunsu. Ana nan sa'anda ango ya yi jinkiri, dukansu suka yi rurrumi, suka yi barci. Amma da tsakiyar dare sai aka ji murya, Ga ango! Ku fito, ku tarbe shi."

An gane cewa zuwan angon yana misalta zuwan nan na Kristi da malaika na fari ya sanar ne. Canje canje masu yawa da aka yi a kalkashin shelar kusantowar zuwansa sun je dai dai da tafiyar budurwai din ne. A wannan misalin, kaman na Matta 24, mutane kashi biyu aka misalta. Dukansu sun dauki fitillunsu, Littafin, kuma tawurin haskensa sun tafi domin su tarbi angon. Amma, yayinda "marasa azancbin nan, da suka dauki fitillunsu, basu dauka duk da mai ba," "masu-hikima suka dauki mai chikin santulansu tare da fitillinsu." Kashi na biyu din sun karbi alherin Allah, ikon sakewa mai-haskakawa na Ruhu Mai-tsarki, wanda ke mai da maganarsa fitilla ga sawaye, haske kuma ga tafarki. Cikin tsoron Allah sun yi nazarin Littafin domin su san gaskiyar, suka kuma nemi tsabtar ziciya da ta rayuwa. Sun sami dandano dan kansu, bangaskiya ga Allah da maganarsa, wadda yankan buri da jinkiri ba za su iya hambararwa ba. Wadansu suka "dauki fitillinsu, basu dauka duk da mai ba." Ba cikin hankalinsu suka karbi sakon ba. Nauyin sakon ya ba su tsoro, amma kuma sun dogara ga bangaskiyar yanu-wansu ne, suka gamsu da yadda jikinsu ke ji kawai, ba tare da kwakwarar fahimtar gaskiyar ko ainihin aikin alheri cikin zuciyar ba. Wadannan sun fita domin su tarbi Ubangiji, cike da begen samun lada nan da nan, amma basu shirya

domin jinkiri da yankan buri ba. Sa'anda jarabobi suka shigo, bangaskiyarsu ta kasa, haskensu kuma ya ragu.

"Sa'anda ango ya yi jinkiri, dukansu suka yi rurrumi, suka yi barci." Jinkirin angon, yana misalta wucewar lokacin da aka yi tsammanin zuwan Ubangiji ne, da yakan burin da kuma jinkirin zuwan na sa. Cikin wannan lokaci na rashin tabbaci, sha'awar marasa zurfin bangaskiya ta fara kaduwa nan da nan, kokarinsu kuma ya ragu; amma wadanda bangaskiyarsu ta kafu bisa saninsu na Littafin ne suka kasance da kafafunsu a kan dutse wanda iskar yankan kauna ba ta iya kawarwa ba. "Dukansu suka yi rurrumi, suka yi barci," wani bangare cikin rashin kulawa da kuma rabuwa da bangaskiyarsu, daya bangaren kuma tana jira cikin hakuri, har sai an ba da Karin haske. Duk da haka, cikin daren gwajin, masu hakurin ma kamar sun fara rasa bangaskiyar basu iya dogara ga bangaskiyar 'yan-uwansu kuma ba. Dole kowa zai tsaya ko kuma ya fadi don kansa.

Wajen wannanlokacin, tsananin ra'ayi ya fara bayanuwa. Wadansu da suka ce sun karbi sakon da himma suka ki maganar Allah a matsayin sa na mai-bishewa shi kadai, mara kuskure, kuma da korafin samun bishewar Ruhu, suka mika kansu ga ikon tunanin kansu da ra'ayinsu, da ganin zuciyarsu. Akwai wadanda suka nuna makauniyar himma mara sassauci, suna sokar wadanda basu bi ra'ayin su ba. Babbar kungiyar Adventist ba ta goyi bayan matsanantan ra'ayoyinsu da ayukansu ba.

Shaitan ya so ta wurin wannan hanyar ya ja da aikin Allah ya kuma rushe shi ne. Mutanen sun rigaya sun motsu sosai tawurin aikin koyaswar zuwan Kristi, dubban masu-zunubi sun rigaya sun tuba, amintattun mutane kuma suna ba da kansu ga aikin shelar gaskiyar, ko a lokacin jinkirin ma. Shaitan yana hasarar masu binsa, kuma don kawo reni ga aikin Allah, ya yi kokarin rudin wadansu da suka ce su masu bangaskiya ne ya kuma tura su zuwa makura. Wakilansa kuma suka shirya anfani da kowane kuskure da kowace kasawa, da kowane abin da bai dace ba, su kuma bayana shi a gaban mutane har da karin gishiri, domin a ki jinin Adventist da imaninsu. Ta hakanan idan ya sami karin yawan wadanda zai sa su ce sun ba da gaskiya ga zuwan Kristi na biyu, alhali shi Shaitan ne ke mulki bisa zukatansu, zai sami karin riba ta wurin jan hankula zuwa ga mutanen nasa cewa haka ne dukan masu ba da gaskiya su ke.

Shaitan ne "mai-zargin yan'uwan," kuma ruhunsa ne ke motsa mutane su lura suna jira su ga kurakurai da kasawar mutanen Ubangiji, su kuma bayana su ga jama'a, yayin da ake kin ambaton kyawawan ayukansu. A kullum Shaitan yakan dinga aikin duk lokacin da Allah ke aikin ceton rayuka. Sa'anda 'ya'yan Allah suka zo domin gabatarda kansu gaban Ubangiji, Shaitan ma yakan zo a tsakaninsu. A kowace falkaswa, yana shirye ne ya kawo wadanda ba a tsarkake zukatan su ba, kuma tunaninsu bai daidaita ba. Sa'anda wadannan suka karbi wadansu fannonin gaskiya, suka kuma karbu ga ainihin masu ba da gaskiyar, yakan yi aki tawurinsu don kawo ra'ayoyi da za su rudi marasa kulawa. Ba a tabbatar da cewa mutum Kirista ne na kwarai wai don ana ganin shi tare da 'ya'yan Allah, ko a gidan

sujada da wajen cin jibin Ubangiji ma. A kullum Shaitan yana wuraren ibada cikin kamanin wadanda zai iya anfani da su a matsayin wakilansa.

Sarkin mugunta yana jayayya kowane inci inda mutanen Allah suka ci gaba cikin tafiyarsu zuwa birni na sama. Cikin dukan tarihin ekklesiya ba wani canjin da aka taba gudanarwa ba tare da samun manyan matsaloli ba. Haka ya kasance a zamanin Bulus. Duk inda manzon ya kafa ekklesiya, akwai wadanda suka ce sun karbi gaskiyar, amma suka kawo ridda dabam dabam da in aka karba za su shanye gaskiyar ma a kwana a tashi. Luther ma ya gamu da rikici da wahala a hannun masu tsananin ra'ayi da suka ce wai Allah Ya yi magana kai tsaye tawurinsu, saboda haka kuma suka aza ra'ayoyinsu bisa shaidar Littafin. Da yawa marasa bangaskiya da kwarewa, amma masu gamsuwa da isarsu, kuma masu son ji da kuma fadin sabobin ababa, aka yaudare su tawurin karyar sabobin mallaman, suka kuma hada hannu da wakilan Shaitan cikin aikinsu na rushe abinda Allah ya motsa Luther ya gina. 'Ya'yan Wesley kuma, da wadansu da suka albarkaci duniya da tasirinsu da bangaskiyarsu kuma, a kowane mataki sun gamu da dabarun Shaitan, inda ya rika tura masu-tsananin himma, marasa daidaituwa, marasa tsarki kuma, zuwa tsananin ra'ayi kowane iri.

William Miller bai goyi bayan halayyan da suka kai ga tsananin ra'ayin ba. Kamar Luther, ya ce ya kamata a gwada kowane ruhu da maganar Allah. Miller ya ce: "Iblis yana da iko mai-yawa kan zukatan wadansu yau. Kuma ta yaya za mu san irin ruhun da suke da shi? Littafin ya amsa: 'Bisa ga 'ya'yansu za ku sansanche su.' Akwai ruhohi da yawa da suka shigo duniya, kuma an umurce mu mu gwada ruhohin. Ruhun da ba ya sa mu yin rayuwar natsuwa da adalci da tsoron Allah a duniya ta yanzu ba, ba Ruhun Kristi ba ne. Na kara hakikancewa akwai hannun Shaitan a cikin al'amuran nan na rashin natsuwa. Da yawa cikin masu karyan cewa an tsarkake su gaba daya suna bin al'adun mutane, kuma bisa dukan alamu, basu san gaskiyar ba, daidai da wadanda ba sa ikirarin nan din."

"Ruhun kuskure zai kau da mu daga gaskiya; Ruhun Allah kuma zai kai mu ga gaskiya. Amma, in ji ku, mutum zai iya kasancewa cikin kuskure amma ya ga kaman yana da gaskiya. Don me? Mun amsa: 'Ruhun da maganar sun je daidai. Idan mutum ya gwada kansa ta wurin maganar Allah, ya kuma sami daidaituwa da dukan maganar, ashe kuwa dole ya ba da gaskiya cewa yana da gaskiyar; amma idan ya tarar cewa ruhun da ke bi da shi bai je daidai da dukan dokar Allah ko kuma Littafinsa ba, to sai shi yi taka-tsantsan ko da tarkon Iblis ya kama shi." "Sau da yawa ni kan fi samun shaidar ibadata cikin zuciya a wurin masu tsoro da masu kuka da masu magana da kyar, fiye da yawan surutun nan a cikin Kirista."

A kwanakin Canjin, magabta sun zargi 'yan canjin da suka yi himman jayayya da tsananin ra'ayi da laifin jawo matsalolin matsanantan ra'ayin. Irin abin da masu jayayya da masu shelar zuwan Yesu na biyu suka yi ke nan su ma. Ban da kara gishiri ma kurakuran masu matsanancin ra'ayin, magabtan sun dinga baza rahotanin karya. Son kai da kiyaya ne

kowa suka motsa mutanen nan. Shelar kusantowar Kristi ta girgiza salamarsu, sun ji tsoron cewa watakila gaskiya ne, suna kuma begen cewa ba gaskiyan ba ne, wannan ne kuwa asirin yakin da suka yi da Adventist da imaninsu.

Kasancewar masu matsanantan ra'ayin nan marasa yawa a cikin Adventist daidai yake da kasancewarsu masu rudu kuma cikin ekklesiya a zamanin Bulus da zamanin Luther, wannan kuma bai zama hujjar kushe aikinsu ba. Bari mutanen Allah su tashi daga barci su fara aikin tuba da canji, bari su bincika nassosin, su kuma koyi gaskiya wadda ke cikin Yesu, bari su kebe kansu dungum ga Allah, za a kuwa ga shaida cewa har yanzu Shaitan yana aiki, ba barci. Da kowane irin rudu, zai nuna ikonsa, yana anfani da dukan malaikunsa.

Ba shelar zuwan Yesu na biyu ne ya jawo matsanancin ra'ayi da kuma rabuwa ba. Wadannan sun bayana da daminan 1844 ne, lokacin da Adventist ke cikin yanayi na shakka da rudewa game da ainihin matsayinsu. Wa'azin sakon malaika fari da na kiran nan na tsakar dare ya danne matsanancin ra'ayi da tsatsaguwa. Wadanda suka yi aikin nan mai-saduda sun kasance cikin daidaituwa, zukatansu sun cika da kaunar juna da kuma Yesu, wanda suka yi begen ganinsa ba da jimawa ba. Bangaskiya dayan, bege mai-albarka dayan, sun daga su bisa mulkin kowane tasiri na mutum, suka kuma zama garkuwa daga haren haren Shaitan.

"Sa'an da ango ya yi jinkiri, dukansu sun yi rurrumi, suka yi barci. Amma da tsakiyar dare sai aka ji murya, Ga ango! Ku fito, ku tarbe shi. Sa'an nan dukan wadannan budurwai suka tashi, suka yi ta gyartan fitillinsu." Matta 25:5-7. A daminar 1844 a tsakanin lokacin da aka fara tsammanin cewa kwana 2300 din za su kare, da kakar shekara dayan, lokacin da daga baya aka gane cewa kwana 2300 din sun kare, an yi shelar sakon ainihin kalmomin nassin: "Ga ango!"

Abin da ya jawo wannan aikin shi ne ganowar cewa a 457 BC ne umurnin Artaxerxes don maida Urushalima, ya fara aiki, wanda shine farawan kwana 2300 din nan, da kakan 457 BC din, ba a farkon shekaran ba yadda aka zata da farko. Idan aka kirga daga kaka na 457, shekaru 2300 din sun kare a kakan 1844 ne.

Ra'ayoyi da ke da tushe daga alamu na Tsohon Alkawali ma sun nuna cewa al'amarin da tsarkakewar haikakin ya misalta zai faru da kaka ne. Wannan ya bayana a sarari sa'anda aka mai da hankali ga yadda alamu game da zuwan Kristi na farko suka cika.

Yankan Dan ragon paskan misali ne na mutuwar Kristi. Bulus ya ce: "Gama an yanke paskarmu, watau Kristi." Korinthiyawa I, 5:7. Damin nunan fari, wanda a lokacin paska akan mika a gaban Ubangiji, alama ce ta tashin Kristi. Bulus ya ce: "Kristi yayan fari; kana su da ken a Kristi, chikin zuwansa." Korinthiyawa I, 15:23. Kamar damin da ake mikawa, wanda shi ne hatsin da ya fara nuna, wanda akan tara kafin girbi, Kristi ne nunan fari na cikin runbun Allah.

An cika alamun nan, ba game da al'amarin kadai ba, har da lokacin ma. Rana ta sha hudu ga watan daya na Yahudawa, daidai rana da watan da aka rika yanka Dan ragon Paskar har karni na goma sha biyar, Kristi, bayan Ya ci Paskar tare da alamajiransa, Ya kafa hidiman nan da zai zama abin tunawa da mutuwarsa, "Dan rago na Allah wanda yana dauke da zunubin duniya!" A wannan daren ne miyagu suka dauke Shi domin a kashe shi ta wurin giciyewa. Kuma kamar cikar misalin damin nan, an ta da Ubangijinmu daga matattu akan rana ta uku, nunan fari na wadanda ke barci, misalin dukan masu nagarta da za a tashe su daga matattu, wadanda za a canja jikunan kaskantarsu "domin ya yi kama da jikin darajassa." Filibiyawa 3:21.

Hakanan kuma dole misalan da suka shafi zuwan Kristi na biyu za su cika daidai lokacin da aka ambata a hidimar misalan. A kalkashin tsarin Musa, tsarkakewar haikalin, ko kuma babban Ranar kafarar yakan faru ne a rana ta goma ga watan bakwai na Yahudawa (Leviticus 16:29-34). Saboda babban priest, bayan ya yi ma Israila kafara, ta haka kuma ya cire zunubansu daga haikalin, yakan fito ya yi ma mutanen albarka. Haka aka ba da gaskiya cewa Kristi, Babban Priest namu, zai bayana domin tsarkake duniya ta wurin hallaka zunubi da masu zunubi, ya kuma albarkaci masu jiransa da rashin mutuwa. Rana ta goma ga watan bakwai, rana mai girma ta kafara, lokacin tsarkakewar haikalin, wanda a 1844 ya fado daidaida ran ashirin da biyu ga Oktoba, aka dauka cewa lokacin zuwan Ubangiji ke nan. Wannan ya je daidai da tabbacin da aka rigaya aka samu cewa kwana 2300 din za su kare lokacin kaka ne.

Cikin misalin nan na Matta 25, zuwan angon ya biyo bayan lokacin jira da rurrumin ne. wannan ya je daidai da ra'ayoyin da aka bayana ne, daga annabci da kuma misali. Dubban mutane ne suka yi shelar kiran nan na "tsakiyar dare".

Aikin ya mamaye kasar kamar ambaliya. Daga birni zuwa birni, kauye zuwa kauye, ya shiga kowane lungu har sai da mutanen Allah suka falka duka. Saboda wannan aikin, matsanancin ra'ayi ya watse kamar yadda raban takan watse in rana ta fito. Shakka da rudewar masu bada gaskiya suka kare, bege da karfin zuciya kuma suka cika zukatansu. Aikin ya yantu daga halayyan nan da kan faru sa'anda hankulan mutane sun motsu ba tare da tasirin maganar Allah da Ruhunsa ba. Kamar Israilawan da ne da sukan dawo wurin Ubangiji bayan bayinsa sun kai masu sakonin tsautawa. Aikin bai jawo murna mai-tsanani ba, sai dai zurfin binciken zukata da furta zunubi da rabuwa da duniya. Shiri don saduwa da Ubangiji ne ya dami mutanen. Akwai naciyar addu'a da kebewa dungum ga aikin Ubangiji.

Game da aikin, Miller ya ce: "Ba a nuna farinciki sosai ba," an dakatar da wannan har sai nan gaba, sa'anda dukan sama da kasa za su yi murna da ta wuce misali, cike da daraja kuma. Babu ihu: wannan ma an bar ma ihun nan daga sama. Mawaka sun yi shuru: suna jira su hadu da rundunonin maliku; mawakan sama,… Babu sabanin ra'ayi; duka suna da zuciya daya da tunani daya."

Wani wanda shi ma ya yi aikin ya shaida cewa: “Aikin ya haifar da binciken zuciya da kaskantar da kai a gaban Allah na sama. Ya jawo yayewar sha’awar ababan duniyan nan, da warkaswa daga jayayya da kiyayya, furtawar laifofi, tuba a gaban Allah, da addu’a na tuba da gaske a gabansa domin a sami gafara da karbuwa. Ya jawo kaskantar da kai da durkusawar ruhu, irin da ba mu taba gani ba. Kamar yadda Allah Ya umurta ta wurin Joel, sa’anda babbar rana ta Allah ta kusa, ta haifar da yagewar zukata ba na tufafi ba, da kuma juyawa ga Ubangiji da azumi da kuka da bakinciki kamar yadda Allah ya fada ta bakin Zechariah, an zubo da ruhun alheri da addu’a ma yayansa; suka dube Shi, Shi wanda, suka suke Shi, an yi babban bakinciki a kasar,… kuma wadanda ke neman Ubangiji suka kaskantar da kansu a gaban shi.”

Cikin dukan aikace aikacen addini tun zamanin manzanin, ba wanda ya fi na kakan 1844 din nan rashin harbuwa da kumamancin mutuntaka da dabarun Shaitan. Ko yanzu ma bayan shekaru da dama, dukan wadanda suka sa hannu cikin aikin nan suna kuma tsaye kan gaskiya suna jin tasiri mai-tsarki na aikin nan mai-tsarkin, suna kuma shaida cewa daga Allah ne.

Sa’anda aka kira: “Ga ango! Ku fito ku tarbe shi.” Masu jira “suka tashi, suka yi ta gyartan fitillunsu;” sun yi nazarin maganar Allah da himman da ba a taba ganin irin sa ba. An aiko maliku daga sama su falkas da wadanda suka fid da zuciya, su kuma shirya su su karbi sakon. Aikin bai dogara ga hikimar mutane ne da iyawar u ba, ya dogara ga ikon Allah ne. Ba mafi baiwa ba, mafi tawli’u da himma ne suka fara ji suka kuma yi biyayya ga kiran. Manoma suka bar hatsinsu a gona, makanikai suka bar kayan aikinsu, da hawaye da farinciki kuma suka fito don ba da gargadin. Wadanda da farko suka shugabanci aikin suna cikin na karshen shiga aikin. Ekklesiyoyin, a kalla, sun hana sakon shiga cikinsu, kuma yawancin wadanda suka karbe shi sun janye daga ekklesiyoyin. Cikin alherin Allah shelan nan ya hadu da sakon malaika na biyu ya kuma karfafa aikin.

Sakon nan, “Ango ya zo!” ba abin mahawara ba ne, da shike tabbacin daga Littafin a bayane yake. Ya zo da wani iko mai-karfi da ya motsa ruhu. Ba shakka ba tambaya. Lokacin shigowar Kristi Urushalima, mutanen da suka taru daga dukan sassan kasar don kiyaye bukin sun taru a Dutsen Zaitun, kuma yayin da suka sadu da jama’an da ke rufa ma Yesu baya sun sami motsuwar al’amarin, su ma suka ta da murya suna cewa: “Mai-albarka ne shi wanda ke zuwa chikin sunan Ubangiji!” Matta 21:9. Hakanan ne kuma marasa ba da gaskiya da suka rika halartar taron Adventist - wadansu don neman sanin abin da ke faruwa, ko don ba’a kawai - suka ji ikon da ke cikin sakon nan: “Ga ango!”

A lokacin akwai bangaskiya da ta kawo amsar addu’a, kamar yayyafi a kan busashiyar kasa, Ruhun alheri ya sauko bisa masu nema da himma. Wadanda suka yarda su tsaya fuska da fuska da Mai-fansarsu sun ji murna mai-saduda da ya fi gaban bayanawa. Ikon tausawa na Ruhu Mai-tsarki ya narkar da zuciya yayin da ake zubo da albarka a yalwace bisa amintattu.

A hankali cikin natsuwa wadanda suka karbi sakon sun kai lokacin da suka yi begen saduwa da Ubangijinsu. Kowace safiya sun dauka cewa aikinsu na farko shi ne neman tabbaci cewa Allah Ya karbe su. Zukatansu sun zama daya, suka rika addu'a tare, suna ma juna addu'a kuma. Sau da yawa sukan sadu don sadarwa da Allah, suna addu'a gare Shi a gona ko daji. Tabbacin karbuwa ga Mai-ceton ya fi masu abincinsu; kuma idan basu fahimci wani abu ba, basu huta ba har sai da suka fahimta. Yayin da suka ji tabbacin gafara, suka yi marmarin ganin Shi wanda suke kauna.

Amma yankan buri na jiran su har wayau. Lokacin da suke bege ya wuce. Mai-cetonsu kuma bai bayana ba. Sun yi begen zuwansa da dukan bangaskiya, yanzu kuma suka ji yadda Maryamu ta ji sa'anda bayan ta je kabarin Mai-ceton, ta tarar ba gawansa, ta yi ihu da kuka ta ce: "Sun dauki Ubangiji na, kuma ban san inda sun ajiye shi ba." Yohanna 20:13

Da farko tsoron kada ya zamana cewa gaskiya ce sakon ya sa marasa ba da gaskiya, suka yi hankali. Bayan lokacin ya wuce, tsoron nan bai watse nan da nan ba; da farko basu iya yin murna kan yankan burin da ya sami masu bin ba, amma da shike ba a ga alamun fushin Allah ba, suka farfado daga tsoronsu, suka koma ga reninsu da ba'ansu. Da yawa da suka ce sun gaskata Ubangiji zai zo suka watsar da bangaskiyarsu. Wadansu da suka nuna tabbaci da farko, sun ji kunya sosai da yadda suka ji, kamar su gudu daga duniyar ma. Kamar Yunana suka yi ma Allah gunaguni suka gwammaci mutuwa maimakon rai. Wadanda da suka dangana bangaskiyarsu kan ra'ayin wadansu, ba maganar Allah ba, a yanzu suka so su kuma canja ra'ayinsu. Masu ba'a suka sha kan masu kumamanci da matsorata zuwa gefensu, dukansu kuma suka hada kai wajen shelar cewa ba dalilin tsoro ko bege kuma yanzu. Lokacin ya wuce, Ubangiji bai zo ba. Duniya kuma za ta iya kasancewa yadda take har dubban shakaru.

Masu ainihin bangaskiya sun rigaya sun sallamar da komi sabo da Kristi, suka kuma yi shelar kasancewarsa fiye da kowane lokaci. Sun gaskanta cewa sun rigaya sun ba duniya kashedi na karshe, kuma, da begen karbuwa ga Maigidansu da malaikun sama, sun riagaya sun janye daga tarayya da wadanda basu karbi sakon ba. Da murandi mai yawa suka yi addu'a cewa: "Ka zo Ubangiji Yesu, ka zo da sauri." Amma bai zo ba. Yanzu kuma sun sake daukan nauyin matsalolin duniya da rudewarta, su kuma jimre ba'a da zage zagen marada, babban gwaji ne na bangaskiyarsu da hakurinsu.

Duk da haka cizon yatsan nan bai yi girma kaman wanda almajiran suka sha lokacin zuwan Kristi na farko ba. Sa'anda Yesu ya shiga Urushalima da nasara, masu binsa sun dauka cewa zai hau gadon sarautan Dauda ke nan, ya kubutar da Israila daga masu zaluntarta. Da bege mai-yawa suka rika gasar nuna daukaka ga sarkinsu. Da yawa suka shimfida tufafinsu a kan hanyan da yake takawa, ko kuma su baza ganyen dabino a gabansa. Cikin tsananin murnarsu suka ta da murya tare suna cewa: "Hossana ga Dan Dauda." Sa'anda Farisawa cikin damuwa da haushin jin wannan murnar, suka ce ma Yesu ya tsauta ma almajiransa, Ya amsa Ya ce: "Da a che wadannan za su yi shuru, ko duwatsu

za su yi murya.” Luka 19:40. Dole a cika annabci. Almajiran sun cika nufin Allah ne; duk da haka yankan buri yana gabansu. Amma kwanaki kalilan sun wuce bayan sun ga mutuwa mai-zafi na Mai-ceton, suka kuma shimfida Shi a kabarin. Ko burinsu daya bai cika ba, begensu kuma ya mutu tare da Yesu. Sai da Ubangijinsu ya fito daga kabari da nasara kafin suka gane cewa annabci ya rigaya ya ce haka zai faru, kuma “wajibi ne ga Kristi Ya sha wahala, ya tashi kuma daga matattu.” Ayukan 17:3.

Shekaru dari biyar kafin nan, Ubangiji ya rigaya ya bayana ta bakin annabi Zechariah cewa; “Ki yi murna sarai, ya diyar Sihiyona: ki yi sowa, ya diyar Urushalima, ga sarkin ki, yana zuwa wurinki; mai-adilchi ne shi, mai-nasara kwa; mai-tawali’u, haye a kan jaki, akan aholakin jaki.” Zechariah 9:9. Da almajiran sun gane cewa Kristi za shi wurin hukumci ne da wurin mutuwa kuma, da basu cika annabcin nan ba.

Hakanan ne kuma Miller da abokansa suka cika annabci suka kuma ba da sakon da annabci ya rigaya ya ce za a ba duniya, amma wanda da basu bayar ba, in da sun sami cikakkiyar ganewar annabcin da ya nuna cewa za su yi cizon yatsa, ya kuma ba da wani sakon da za a yi wa’azin sa ga dukan al’ummai kafin zuwan Ubangiji. An ba da sakon malaika na fari da na biyu din daidai lokaci, aka kuma cika aikin da Ubangiji Ya shirya aiwatarwa.

Duniya tana kallo, tana begen cewa idan lokacin ya wuce Kristi kuma bai bayana ba, za a yi watsi da dukan tsarin nan na Adventist. Amma yayin da mutane da yawa suka rabu da bangaskiyarsu, akwai wadanda suka tsaya da karfi; sakamakon aikin Adventist din, ruhun tawali’u da bimbini, ruhun rabuwa da duniya da sakewar rayuwa, wadanda aikin ya kunsa, ya nuna cewa aikin na Allah ne. Basu isa su yi musun cewa ikon Ruhu Mai-tsarki ya shaida wa’azin zuwan Kristi na biyu din ba, kuma basu iya ganin wani kuskure game da lissafin annabce anabacen wokatai ba. Manyan masu jayayya da su basu yi nasaran hambarar da tsarin su na fassara annabci ba. Basu yarda su rabu da ra’ayiyoyin da masanan da Ruhu ya motsa suka amince da su tawurin binciken Littafin cikin himma da addu’a ba, ra’ayoyin da suka jimre soke soken sanannun mallaman addini da masu hikima irin ta duniya, ra’ayoyin da kuma suka tsaya daram, duk da jayayyar masana da masu-iya magana, da kuma ba’a da zage zagen masu martaba da talakawa.

Gaskiya kam al’amarin da aka yi begensa bai faru ba, amma ko wannan ma bai jijjiga bangaskiyarsu ga maganar Allah ba. Lokacin da Yunana ya yi shela a titunan Nineveh cewa cikin kwana arba’in za a hallaka birnin, Ubangiji ya karbi kaskantar zuciyar mutanen Nineveh, ya kara masu lokacin gwaji, duk da haka Allah ne ya aika ma Yunana sakon, kuma bisa ga nufin Allah ne aka gwada Nineveh. Adventist sun gaskata cewa hakanan ne ma Allah ya kai su ga ba da gargadin hukumcin, suka ce: “sakon ya gwada zukatan dukan wadanda suka ji shi, ya kuma ta da sha’awar bayanuwar Ubangiji; ko kuma ya jawo kiyayya ga zuwan Ubangiji. Ya ja layi,… ta yadda wadanda ke so su gwada zukatan su su san ko da sun kasance a wane bangare ne, in da Ubangiji ya zo a lakacin, ko da sun yi ihu

cewa: “Ga shi wannan Allahnmu ne; mun jirache shi, za ya cheche mu?”, ko kuma da sun kira duwatsu su fadi a kansu, su boye su daga fuskar Shi wanda ke zaune bisa kursiyin, daga fushin Dan ragon kuma? Ta hakanan Allah ya gwada mutanensa, Ya gwada bangaskiyarsu, ya gwada su, ya kuma ga ko za su janye a lokacin gwaji daga wurin da ya so ya ajiye su; ko kuma za su sallamar da duniyan nan, su kuma dogara ga maganar Allah kadai.”

William Miller ya bayana tunanin wadanda suka ba da gaskiya cewa Allah ne ya bi da su cikin abin da ya faru da su. Ya ce: “In da zan sake maimaita rayuwa ta kuma, da shaida dayan da na samu a lokacin tsakani na da Allah dole zanyi yadda na yi a lokacin can.” “Ina fata na tsarkake tufafi na daga jinin mutane. Ina ji kamar na yi iyakacin kokarina dai na wanke kaina daga duk wani alhakin laifinsu.” “Ko da shike an yanke mani buri sau biyu, ni ban karai ba, ban kuma yi sanyin gwiwa ba,… Bege na game da zuwan Kristi yana da karfi kamar kowane lokaci. Ni dai na yi abin da, bayan shakaru ina bimbini, na ga cewa ya zama wajibi ne gare ni in yi. Idan na yi kuskure, saboda kauna ne, kaunar yan’uwa na mutane da sanin cewa aikin Allah ni ke yi.” Abu daya da na sani shi ne cewa ban yi wa’azin komi ba sai na abin da na gaskata, Allah kuma yana tare da ni, ikonsa ya bayana a cikin aikin, an kuma sami anfani sosai.” “Ga ganin mutum, an sa dubbai sun yi nazarin Littafin ta wurin wa’azin lokacin; kuma ta hakanan, ta wurin bangaskiya da yayyafawar jinin Kristi, an sasanta su da Allah.” “Ban taba yi ma masu girman kai fadanci ba, ko kuma in ji tsoron fushin duniya ba. Yanzu kuma ba zan sayi soyayyarsu ba, ba kuwa zan bata lokaci na ina neman kiyayarsu ba. Ba zan taba neman rai na a hannunsu ba, ko kuma in ji shakkar rasa raina idan Allah cikin kaddararsa ya umurta hakan.”

Allah bai rabu da mutanensa ba; Ruhunsa ya ci gaba da kasancewa da wadanda basu ki hasken da sun rigaya sun samu suka kuma kushe aikin maganar zuwan Kristi din ba. Cikin wasika zuwa ga Ibraniyawa akwai kalmomi na karfafawa da fadaka ga masu jira da aka jarabace su a lokacin hargitsin nan. “Kada fa ku yasda gaba gadin ku, abin da ke da sakamako mai-girma. Gama kuna da bukatar hankuri, domin, bayan da kun aika nufin Allah, ku karbi alkawalin. Gama da sauran jimawa kadan, wanda ke zuwa za shi zo, ba kwa za shi yi jinkiri ba. Amma adilina da bangaskiya za shi rayu: idan kwa ya noke, raina ba shi jin dadinsa ba. Amma mu ba mu chikin masu-nokewa zuwa hallaka ba; amma chikin wadanda su ke da bangaskiya zuwa cheton rai.” Ibraniyawa 10:35-39.

Kalmomin da sun nuna kusatowar zuwan Ubangiji sun tabbatar da cewa ana ma ekklesiyar kwanakin karshe ne fadakan nan. Ya ce: “Gama da sauran jimawa kadan wanda ke zuwa za shi zo, ba kwa za shi yi jinkiri ba.” Ya kuma nuna a sarari cewa za a sami kamanin dakatawa, kuma za a ga kamar Ubangiji Ya yi jinkiri ne. Umurnin da aka bayar a nan ya je daidai da abin da ya faru da Adventist a wannan lokacin. Mutanen da ake magana da su a nan suna fuskantar yiwuwar rushe bangaskiyarsu. Sun bi nufin Allah tawurin bin bishewar Ruhu Mai-tsarki da maganarsa; duk da haka basu iya gane nufinsa a abin da ya

faru da su ba, basu kuma gane hanyar da ke gabansu ba, suka so su yi shakka ma ko Allah ne yake bishe su. A lokacin nan kalmomin na cewa, “Amma adili na da bangaskiya ne za shi rayu.” Sun je daidai. Da shike hasken kiran tsakiyar daren nan ya haskaka hanyarsu, suka kuma ga an bayana annabcin, kuma alamun da ke cika da wuri wuri suna nuna cewa zuwan Kristi Ya yi kusa, sun yi tafiya bisa ga ganin ido ne a lokacin. Amma yanzu, da shike begensu bai cika ba, za su tsaya tawurin bangaskiya ga Allah da maganarsa ne kadai. Masu ba’a sun rika cewa: “An rude ku.” Amma maganar Allah ta ce: “Idan kwa ya noke, raina ba shi jin dadinsa ba.” Idan suka shika bangaskiyarsu yanzu, suka kuma musunci ikon Ruhu Ma-tsarki wanda Ya kasance tare da sakon, wannan zai zama ja da baya ne zuwa hallaka. Kalmomin Bulus, sun karfafa su, cewa: “Kada fa ku yas da gaba gadin ku.” “Kuna da bukatar hankuri,” “Gama da sauran jimawa kadan, wanda ke zuwa za shi zo, ba kwa za shi yi jinkiri ba.” Abin da ya fi anfani gare su shi ne su kaunaci hasken da sun rigaya sun karba daga wurin Allah, su rike alkawuransa, su kuma ci gaba da nazarin Littafin, su kuma yi hakuri su jira, suna tsaro don karban Karin haske.

Babi na 23—Menene Haikalin?

Nassin da ya fi kowanne zama harsashe da kuma babbar madogarar imanin zuwan Yesu shi ne furcin nan cewa: “Y ache mani, Har yamma da sfiya guda alfin da dari uku: kana za a tsarkake wuri mai-tsarki.” Daniel 8:14. Dukan masu ba da gaskiya ga zuwan Ubangiji sun san kalmomin nan. Dubbai sun rika maimata kalmomin a matsayin ginshikin bangaskiyarsu. Kowa ya dauka cewa burinsu da begensu sun dangana ga al’amuran da aka yi annabcinsu a nassin ne. An nuna cewa kwanakin nan na annabci za su kare a bazarar 1844 ne. Tare da sauran Kirista, Adventist a lokacin sun dauka cewa duniya, ko kuma wani sashen sa ne haikalin. A ganewarsu, tsarkakewar haikalin shi ne tsabtatawar duniya tawurin wutar rana mai-girma ta karshe, kuma cewa wannan zai faru lokacin zuwan Kristi na biyu ne. Shi ya sa suka ce Yesu zai zo duniya a 1844.

Amma lokacin ya wuce, Ubangiji kuma bai bayana ba. Masu-bi sun san cewa maganar Allah ba za ta yi kuskure ba, tilas fasarar da suka wa annabcin ne akwai kuskure, amma ina kuskuren yake? Da yawa sun yi gaggawar kauce ma matsalar tawurin kin cewa kwana 2300 din sun kare a 1844 ne. Ba su da wani dalili kuwa sai dai wai don Kristi bai dawo a 1844 yadda suka zata ba. Sun matsa cewa, da kwanakin annabcin sun kure a 1844, da Kristi ya dawo domin ya tsarkake haikalin tawurin tsabtata duniya da wuta; kuma cewa da shike bai dawo ba, kwanakin ne basu kare ba.

Yarda da wannan ra’ayin zai zama kin yarda da lissafin annabcin wokatai da an rigaya an yi ne. An rigaya an gane cewa kwana 2300 din sun fara sa’an da umurnin Artaxerxes don mayaswa da gina Urushalima ya fara aiki ne a bazarar 457 BC. Idan aka fara a nan, akwai daidaituwa game da dukan al’amuran da aka yi annabcinsu a fasarar lokacin a cikin Daniel 9:25-27. Bakwai sittin da tara, shekaru 483 na farko daga cikin shekaru 2300 din, za su kai ga Masiya, Shafaffen, kuma baptismar Kristi da shafewar sa da Ruhu Mai-tsarki ya yi a A.D. 27 ya cika annabcin daidai. A tsakiyar bakwai na saba’in din, za a datse Masiya. Shekara uku da rabi bayan baptismar Kristi, an giciye Shi, a bazaran A.D. 31. Bakwai saba’in din, ko kuma shekara 490 na Yahudawa ne musamman. A karshen wannan lokacin al’ummar ta hatimce kin Kristi da ta yi, ta wurin tsananta ma almajiransa, manzamin kuma suka juya zuwa ga Al’ummai, a A.D. 34. Da shike shekaru 490 na farko na shekaru 2300 din sun kare, saura shekara 1810 kenan. Daga A.D 34, shekaru 1810 za su kai 1844. Malaikan ya ce: “Dukan al’amuran da annabcin ya ambata sun rigaya sun cika,” dai dai lokacin da aka ambata.

Da wannan lissafin, komi ya je daidai bau shakka kuma, sai dai ba a ga cewa wani abin da ya je dai dai da tsarkake haikalin ya faru a 1844 ba. Idan aka ce kwanakin basu kare a lokacin ba za a birkitar da dukan batun ke nan a kuma warware ababan da an rigaya an tabbatar da su tawurin cikar annabci.

Amma Allah Ya rigaya Ya jogaranci mutanensa a babban aikin nan na batun zuwan Yesu. Ikonsa da darajarsa sun kasance tare da aikin, kuma Shi ba zai bar aikin ya kare cikin duhu da cizon yatsa ba, har a rena shi cewa karya ce. Ba zai bar maganarsa cikin shakka da rashin tabbaci ba. Ko da shike da yawa sun rabu da lissafin su na da, game da lokaci na annabci, suka kuma musunci sahihancin aikin da aka yi bisa ga lissafin lokaci na annabcin, wadansu basu yarda su rabu da matsayi na bangaskiya da ayuka da aka tabbatar tawurin Littafin da kuma shaidar Ruhun Allah ba. Sun gaskata cewa sun yi anfani da nagargarun kaidodin fassara wajen yin nazarin annabcin, kuma cewa wajibi ne gare su su rike gaskiyan da sun rigaya sun samu, su kuma ci gaba da nazarin Littafin. Da naciya cikin addu'a suka sake duba ra'ayoyinsu suka kuma yi nazarin Littafin domin su gano kusurensu. Sa'an da basu ga kuskure game da lissafinsu na lokatan annabci ba, aka bishe su zuwa ga karin binciken haikalin.

Cikin bincikensu sun gane cewa babu shaida daga Littafni da ya nuna cewa duniya ce haikalin, amma a cikin Littafin sun iske cikakken bayanin haikalin, da yanayinsa, da inda yake da hidimominsa, shaidar Littafin kuma ya kasance bayananne, isashe kuma ta yadda bai bar wata alamar tambaya ba. Manzo Bulus cikin littafin Ibraniyawa ya ce: "Amma ko alkawali na fari yana da farillai na hidimar Allah, da wuri mai-tsarki nasa, na duniyan nan. Gama da akwai mazamai shiryayye, na farin ke nan, inda ke fitilla, da teble, da gurasa ta nunawa, ana kwa che da ita wuri mai-tsarki. Bayan labule na biyu kuma, sai mazamni wanda ana che da shi mai-tsarki na tsarkaka, yana da bagadin turare na zinariya, da sanduki na alkawali rufaffe ko ina da zinariya, inda akwai kasko na zinariya da manna a chiki, da sandar Haruna wadda ta yi tofu, da kuma alluna na akawali, a bisansa kuma cherubim na daraja suna inuwantadda mazamni na jinkai." Ibraniyawa 9:1-5.

Haikalin da Bulus ke magana akai wanda Musa ya gina ne, bisa ga umurnin Allah domin shi zama wurin zaman madaukaki a duniya. "Bari kuma su yi mani mazamni mai-tsarki domin in zauna a chikinsu." (Fitowa 25:8), umurnin da aka ba Musa ke nan yayin da yake kan Dutsen tare da Allah. Israilawa suna tafiya cikin jeji ne, aka kuma tsara haikalin ta yadda za a iya tafiya da shi daga wani wuri zuwa wani wuri, duk da haka gini ne mai-kyau sosai. Bangonsa shaifi-shafi ne da aka lulluba da zinariya aka kuma kama da azurfa, jinkan kuma jerin ababa ne misalin labule, waje fatu, ciki kuma linen mai-laushi da aka masa ado da zanen hotunan cherubin. Ban da haraba ta waje din da ta kunshi bagadin hadaya ta konawa, haikalin kansa yana da sassa biyu: wuri mai-tsarki da wuri mafi-tsarki, aka raba su da kyakyawan labule mai kauri sosai; irin labulen ne ma aka rufe kofar wuri na farin da shi.

A wuri mai-tsarkin akwai sandar kyendur a kudu, da fitilunsa bakwai masu haskaka haikalin dare da rana; arewa akwai tebur na gurasar nunawa; kafin labulen da ya raba tsakanin wuri mai-tsarki da mafi-tsarki kuma akwai bagadin zinariya na turare, daga inda girgijen kamshi, da addu'o'in Israila, ke hawa sama zuwa wurin Allah.

A wuri mai-tsarkin akwai sandukin, akwatin katako ne da aka lulluba da zinariya, inda aka ajiye alluna biyu na dutse da Allah ya rubuta Dokoki Goma akai ke nan. A bisa sandukin, abin da kuma ya zama marufin sandukin, shi ne mazamnin jinkai, gwanin kyau, wanda cherubim biyu ke tsaye a kansa, kowanne a kusurwarsa, kuma da zallan zinariya aka kera su. A wannan wurin, kasancewar Allah yana ganuwa ta girgijen daraja tsakanin cherubim din ne.

Bayan Ibraniyawa sun zauna a Kan'ana, an sanya wannan mazamnin da haikalin Solomon, wanda, ko da shike gini ne kafaffe, babba kuma, ya bi daidai gwajin mazamnin nan ne irin kayan da ke cikinsu kuma iri daya ne. Hakanan ne haikalin ya kasance, ban da lokacin da ya kasance kango a lokacin Daniel, har sa'an da Romawa suka rushe shi a A.D. 70.

Wannan ne kadai haikalin da ya taba kasancewa a duniya, bisa ga Littafin. Bulus ya ce da shi haikali na alkawalin fari. Amma ko sabon alkawalin bas hi da haikali ne?

Sa'anda suka koma littafin Ibraniyawa kuma, masu neman gaskiyan suka iske cewa zancen kasancewar haikali na biyu ko na sabon alkawali yana kunshe cikin maganan nan na Bulus, cewa: "Amma ko alkawali na fari yana da farillai na hidimar Allah, da wuri mai-tsarki nasa na duniyan nan." Ba shakka Bulus ya rigaya ya ambaci wannan haikalin, inda ya ce: "Kwayar magana chikin abinda muke fadi kenan: muna da wannan irin babban priest, wanda ya zamana ga hannun daman a al'arshen madaukaki chikin sammai, mai-hidiman wuri mai-tsarki da na mazamnai na gaske, wanda Ubangiji ya kafa, ba mutum ba." Ibraniyawa 8:1,2.

A nan an bayana haikali na sabon alkawali. Haikali na fari mutum ne ya kafa shi, Musa ne ya gina shi; wannan kuwa Ubangiji ne Ya kafa shi, ba mutum ba. A wancan haikalin, priestoci na duniya ne suka rika hidimarsu, a wannan kuwa Kristi, Babban priest namu ne yake hidima a hannun dama na Allah. Da can akwai haikali daya ne a duniya, dayan kuma yana sama ne.

Bayan haka, haikalin da Musa ya gina ya bi wani fasali ne. Ubangiji ya umurce shi: "Bisa ga fasalin abin da na nuna maka duka, fasalin mazamnin, da fasalin kayansa duka, hakanan za ku yi shi." An kuma ba da fadaka cewa: "Ku lura fa ka yi su bisa ga fasalinsu, wanda aka nuna maka chikin Dutsen." Fitowa 25:9, 40. Bulus kuma ya ce haikali na farin "misali ne domin wannan zamani; a tafarkinsa fa ana mika baye-baye da hadayu," watau wurare masu-tsarki "misalin ababan da ke chikin sama" ne; cewa priestocin da suka mika baye-baye bisa ga doka sun yi hidima "misalin abuabuwa na sama" ne; kuma cewa "Kristi ba ya shiga chikin wani wuri mai-tsarki wanda aka yi da hannuwa ba, mai-kama da gaskiya ga zanchen fasali; amma chikin sama kanta shi bayana a gaban fuskar Allah sabili da mu yanzu." Ibraniyawa 9:9, 23; 8:5; 9:24.

Haikalin da ke sama, inda Kristi ke hidima a madadinmu, shi ne babban asalin, wanda haikalin da Musa ya gina ya misalta. Allah Ya sa Ruhunsa a kan maginan haikali na duniyan. Kwarewan da aka nuna wajen gina shi ya nuna cewa hikima ne daga Allah. Kowane bango yana da kamanin zinariya ne, yana kuma walkiya da hasken kyandir na fitillu bakwai din nan na sandar kyandir din. Tebur na gurasa ta nunawa da bagadin turare ta rika walkiya kamar tsabar zinariya. Kyakyawan labulen nan da ya kasance silin, shafe da zanen hotunan malaiku cikin launi daban-dabam ya kara ma ginin ban sha'awa. Kuma bayan labule na biyu din akwai Shekinah mai- daraja wanda shi ne darajar Allah da ake gani, wanda babban priest ne kadai zai iya shiga wurinsa ya kuma ci gaba da rayuwa.

Yawan ban-sha'awan haikali na duniyan ya nuna ma 'yan Adam darajar haikalin nan na sama inda Kristi ke hidima dominmu a gaban haikalin Allah. Wurin kasancewar sarkin sarakuna, inda dubban dubbai ke masa hidima, zambar goma so zambar goma kuma suna tsaye a gabansa (Daniel 7:10), wancan haikalin, cike da darajar kursiyi na har abada, inda Seraphim, masu lura da shi, da fuskokinsu a rufe don bangirma, suka iske cewa gini mafi kyau da 'yan Adam suka taba yi, don kankanin hoto ne na girman haikalin sama da darajarsa. Dun da haka an kyoyar da muhimman gaskiya game da haikalin sama da babban aikin da ake yi a wurin domin fansar mutum tawurin haikali na duniyan ne, da hidimominsa.

Wurare masu-tsarki na haikalin sama an misalta su da wurare biyu na haikali na duniyan. Sa'anda cikin ruya aka nuna ma manzo Yohanna haikalin sama, ya ga "fitilla bakwai ta wuta kuma suna chi a gaban kursiyin," Ruya 4:5. Ya ga malaika "yana rike da kasko na zinariya; aka ba shi turare da yawa, domin ya zuba shi tare da addu'o'in tsarkaka a bisa bagadi na zinariya wanda ke gaban kursiyin." Ruya 8:3.

A nan an yarda ma annabin ya ga wurin farko na haikalin da ke sama, can kuma ya ga fitillu bakwai na wuta da bagadi na zinariya, wanda kyandir na zinariya da bagadin turare na haikalin duniya suka misalta. Kuma, "Aka bude haikalin Allah da ke chikin sama" (Ruya 11:19), sai ya duba cikin labulen da ke ciki ya dubi wuri mafi-tsarki. A nan ya ga "sandukin alkawalinsa," wanda akwati mai-tsarkin nan da Musa ya gyara domin a sa dokar Allah a ciki ya misalta.

Don haka, wadanda suka yi ta nazarin batun suka sami tabbaci ba shakka cewa akwai haikali a sama. Musa ya yi haikali na duniyan bisa ga kwatancin da aka nuna masa ne. Bulus ya koyar da cewa kwatancin shi ne ainihin haikalin da ke cikin sama, Yohanna kuma ya shaida cewa ya gan shi a sama.

A cikin haikali na sama, wurin kasancewar Allah, kursiyinsa yana kafe cikin adalci da shari'a. A wuri mai-tsarki akwai dokarsa, babban kaidar cancanta wada tawurin ta ake gwada dukan 'yan Adam. Sandukin da ya kunshi allunan dokan an rufe shi da mazamnin jinkai, wanda a gaban shi ne Kristi yake roko da jininsa a madadin mai-zunubi. Ta hakanan

aka bayana hadewar adalci da jinkai cikin shirin fansar ‘yan Adam. Wannan hadewar, hikima mara matuka kadai ya iya kirkirowa, kuma iko mara matuka kadai ya iya aiwatarwa; hadewa ne da ya cika dukan sama da mamaki da girmamawa kuma. Cherubim na haikali na duniya da suke duban mazamnin jin kai, da bangirma, suna misaltar sha’awan da rundunan sama ke kallon shirin fansa da shi ne. Wannan asirin jin kai ne da malaiku ke sha’awar kallo, cewa Allah yana iya yin adalci, yayin da yake kubutar da mai-zunubi da ya tuba, yana kuma sabonta dangantakarsu da fadadun ‘yan Adam, cewa Kristi zai iya sunkuyawa ya daga tulin jama’a daga rami mara matuka na hallaka, ya suturta su da sutura mara aibi na dalcin kansa, domin su hadu da malaiku da basu taba faduwa ba, su kuma kasance har abada tare da Allah.

An bayana aikin Kristi na matsakanci a cikin annabcin nan mai-ban sha’awa na Zechariah game da shi “wanda sunansa zuriya ne.” In ji annabcin: “Shi kansa za ya gina haikalin Ubangiji; za ya dauki daraja, ya zamna kuma ya yi mulki a bisa kursiyinsa; za ya zama priest a bisa kursiyinsa; shawarar salama kuma za ta zama tsakanin su biyu.” Zechariah 6:12,13.

“Za ya gina haikalin Ubangiji.” Ta wurin hadayarsa da tsakancinsa, Kristi ne harsashe da kuma maginin ekklesiyar Allah. Manzo Bulus ya nuna cewa Shi Kristi “babban dutse na kusurwa ne; a chikinsa kwa dukan gini, sassadadde ne, yana hawa yana zama haikali mai-tsarki chikin Ubangiji, a chikinsa kwa an gina ku tare domin ku zama mazamnin Allah chikin Ruhun.” Afisawa 2:20-22.

“Za ya dauki daraja.” Darajar fansar fadadiyar jinsin ‘yan Adam ta Kristi ce. Cikin dukan sararaki har abada wakar fansassu za ta kasance: “A gare shi wanda yake kamnarmu, ya kwanche mu kuma daga zunubanmu chikin jininsa,… a gare shi daukaka da mulki har zuwa zamanun zamanai.” Ruya 1:5,6.

Za “ya yi mulki a bisa kursiyinsa, za ya zama priest a bisa kursiyinsa. Yanzu dai ba bisa kursiyin darajarsa ba, mulki na daraja bai zo ba tukuna. Sai aikinsa na matsakanci, ya kare ne Allah ya “za ya ba shi kursiyi na Ubansa Dawuda,” mulki wanda ba shi da matuka. Luka 1:32,33. A matsayinsa na priest, yanzu Kristi yana zaune da Uban a kursiyinsa. Ruya 3:21. Tare da Allah a kan kursiyin akwai Shi wanda “ya dauki bakinchikinmu, da kayan chiwutanmu ya nawaita,” wanda “an jarabche shi a kowache fuska kamarmu, sai dai banda zunubi,” domin Ya sami “iko ya taimaki wadanda ake jarabtassu.” “Idan kowa ya yi zunubi, muna da mai-taimako wurin Uba.” Ishaya 53:4; Ibraniyawa 4:15; 2:18; 1Yohanna 2:1. Tsakancinsa na jikin da aka huda ne, na rayuwa mara aibi. Hudaddun hannayen da hudadden gefen da kafafun da aka kuje, suna roko a madadin fadadden mutum, wanda aka sayi fansarsa da tamani mara iyaka hakanan.

“Shawarar salama kuma za ta zama tsakaninsu biyu.” Kaunar Uban da ita Dan shi ce mabulbulan ceto domin batacen al’umma. Kafin tafiyarsa, Yesu ya ce ma almajiransa:

“Kuma ban che maku ni yi addu’a ga Uba domin ku ba; gama Uba da kansa yana kamnarku.” Yohanna 16:26,27. “Allah yana chikin Kristi yana sulhunta duniya zuwa kansa.” Korinthiyawa II, 5:19. Kuma cikin hidima a haikali na sama, “shawarar salama za ta zama tsakaninsu biyu.” “Allah ya yi kamnan duniya, har ya ba da Dansa haifaffe shi kadai domin dukan wanda yana ba da gaskiya gare shi kada ya lalache amma ya sami rain a har abada.” Yohanna 3:16.

Littafi ya amsa tambayan nan, Mene ne haikalin? sarai. Kalman nan haikali a Littafin da farko yana nufin wurin zaman nan na Allah da Musa ya gina ne, misalin ababa na sama; na biyu kuma ainihin mazamnin Allah a sama, wanda na duniyan ya misalta. A mutuwar Kristi hidimar farillai ya kare. Ainihin haikalin Allah a sama shi ne haikalin sabon alkawalin. Kuma da shike annabcin Daniel 8:14 ya cika a wannan yanayin ne, haikalin da yake magana akai shi ne haikali na sabon alkawali. A karshen kwana 2300 din nan a 1844, an yi daruruwan shekaru ba haikali a duniya. Saboda haka annabcin nan “Har yamma da safiya guda alfin da dari uku; kuma za a tsarkakar wuri mai-tsarki” yana magana game da haikali na sama ne.

Amma tambaya mafi-muhimmanci ba a amsa shi ba tukuna: Mene ne tsarkakewar haikalin? Tsohon Alkawali ya ambaci hidimar tsarkakewa game da haikali na duniya. Amma ko akwai wani abu a sama da ke bukatar tsarkakewa ahaikali na sama? Cikin Ibraniyawa 9 ana koyar da batun tsarkakewar haikalin duniya da na sama. Ya ce: “Saura kadan sai in che dukan abu, bisa ga shari’a da jini akan tsarkake shi, kuma im ba zubawar jini, babu gafara. Ya wajaba fa a tsarkake misalan al’amuran da ke chikin sama da wadannan abu; amma na sama da kansu da hadayu wadanda sun fi wadannan kyau. (Ibraniyawa 9:22,23), watau jinin Kristi.

Tsarkakewar, a hidimar alamu da na ainihin ma dole da jini ake yin sa: a hidimar alamun da jinin dabbobi, a hidimar ainihin kuwa da jinin Kristi. Bulus ya ce dalili shi ne cewa im ba zubawar jini babu kafara, kafara, ko kuma kawas da zunubi shi ne aikin da za a gudanar. Amma ta yaya za a danganta zunubi da haikali, ko na sama ko na duniya? Za a iya gane wannan ta wurin duba hidima ta alamun, gama priestoci da suka yi hidima a duniya sun yi hidimarsu “misalin abubuwa na sama da inuwassu” ne. Ibraniyawa 8:5.

Hidimar haikali na duniya ta kunshi fannoni biyu ne; priestocin sukan yi hidima kowace rana a wuri mai-tsarki, amma sau daya kwace shekara baban priest yakan yi aiki na musamman na tsarkakewar haikalin.Kowace rana mai-zunubi da ya tuba yakan kawo hadayarsa kofar haikalin, kuma sa’an da ya aza hannunsa bisa kan hadayar, yakan furta zunubansa, ta hakanan kuma ya dauke su daga wurinsa ya zuba kan hadaya mara laifin. Sa’an nan akan yanka hadayar. Manzon ya ce “im ba zubawan jini” babu kafarar zunubi. “Gama ran nama yana chikin jini.” Leviticus 17:11. Dokar Allah da aka karya ta bukaci ran mai-ketarewan. Priest yakan dauki jinin, alamar ran mai-zunubi da ya rasa, wanda hadayar ke daukan laifinsa, zuwa cikin wuri mai-tsarki ya yayyafa shi a gaban labulen,

wanda a bayan shi akwai sandukin da ke kunshe da dokan da mai-zunubin ya ketare. Ta wurin wannan hidimar akan dauke zunubin tawurin jinin, a zuba shi a haikalin a misalce. A wadansu lokuta ba a zuba jinin a wuri mai-tsarki, amma priest yakan ci naman ne kamar yadda Musa ya umurci 'ya'yan Haruna cewa Allah "ya kwa ba ku ita domin ku dauki zunubin jama'a," Leviticus 10:17. Bukukuwan biyu sun misalta daukewar zunubi daga mai-zunubi da ya tuba, zuwa haikalin.

Irin aikin da aka dinga yi kenan kowace rana duk shekara. Ta hakanan akan mayar da zunuban Israila ga haikalin, kuma ya zama wajibi a yi aiki na musamman don cire su. Allah Ya umutra cewa a yi kafara domin kowane sashi na wurare masu-tsarkin. "Za ya yi kafara domin wuri mai-tsarki, domin laifofinsu kuma, watau dukan zunubansu ke nan; hakanan kuma za ya yi domin tent na taruwa, wanda ke zamne tare da su a chikin tsakiyar kazamtarsu. An kuma bukaci yin kafara domin bagadin, domin a "tsabtadda shi, ya tsarkake shi kuma daga kazamta na yayan Israila." Leviticus 16:16, 19.

Sau daya a shekara, a babban Ranan Kafara, priest yakan shiga wuri mafi-tsarki don tsarkake haikalin. Aikin da akan yi a wurin ne yakan kamala hidimomin shekaran. A ranar kafara bunsuru guda biyu ne akan kawo kofar tent, a jefa kuri'a a kansu, "daya domin Ubangiji, dayan domin Azazel." Aya 8. Bunsurun da karu'ar Ubangiji ta fadi a kansa akan yanka shi a matsayin hadaya ta zunubi domin mutanen. Priest kuma zai kawo jininsa cikin labulen, ya yayyafa shi bisa kan bunsuru mai-rai, ya furta dukan muguntar 'ya'yan Israila a bisansa, da dukan laifofinsu, watau zunubansu duka; za ya sa su a bisa kan bunsurun, kana ya sallame shi zuwa jeji ta hannun wani mutum wanda aka sanya, bunsuru kuma za ya dauka ma kansa dukan muguntassu, ya kai zuwa chikin kasa inda babu kowa." Aya 21, 22. Bunsurun Azazel din ba ya dawowa sansanin Israila kuma, mutumin da ya kai shi jejin kuma yakan wanke kansa da tufafinsa da ruwa kafin ya koma cikin sansanin.

An shirya dukan hidimar ta yadda za a nuna ma Israilawa tsarkin Allah da yadda yake kyamar zunubi; kuma domin a nuna masu cewa ba za su iya saduwa da zunubi har su kasance ba aibi ba. Akan bukaci kowane, mutum ya auna rayuwarsa yayin da ake aikin kafaran. Akan dakatar da kowane aiki, kuma dukan Israilawa sukan uni kaskantar da kan u ne a gaban Allah, da addu'a da azumi, da bincikewar zuciya.

Hidimar farillai din tana koyar da muhimman gaskiya. Akan karbi wani a madadin mai-zunubi; amma jinin hadayan ba ya share zunubin. Saboda haka aka tanada hanyar zubar da zunubin a haikalin. Ta wurin hadayar jini mai-zunubi yakan amince da ikon dokan ya furta laifinsa na ketare dokar, ya kuma bayana bukatarsa ta gafara ta wurin bangaskiya ga Mai-fansa da ke zuwa; amma tukuna ba a kubutar da shi daga hukumcin shari'a ba. A ranar kafara, babban priest, bayan ya karbi hadaya daga jama'a yakan shiga wuri mafi-tsarki da jinin hadayan nan, ya kuma yayyafa shi a kan mazamni na jinkai, daidai kan dokan, domin shi gamsar da sharuddan dokar. Sa'an nan, a yanayinsa na matsakanci, yakan dauki zunuban a ransa ya fitar da su daga haikalin. Sa'anda ya aza hannuwansa bisa kan

bunsurun Azazel, yakan furta dukan zunuban a kansa, alamar mayar da su daga shi kansa zuwa bunsurun kenan. Sa'an nan bunsurun yakan tafi da su, akan kuma dauka cewa har abada an raba su da mutanen ke nan.

Haka ne aka rika hidimar "misalin abubuwa na sama da inuwassu." Kuma abin da aka yi cikin misali a hidimar haikali na duniya ana yinsa zahiri a hidimar haikalin sama. Bayan komawarsa sama, Mai-ceton mu Ya fara aikin sa na babban priest namu. In ji Bulus; "Kristi baya shiga wani wuri mai-tsarki wanda aka yi da hannuwa ba, mai-kama da na gaskiya ga zanchen fasali; amma chikin sama kan ta, shi bayana a gaban fuskar Allah sabili da mu yanzu." Ibraniyawa 9:24.

Hidimar priest cikin dukan shekaran a wuri na fari na haikalin a cikin labulen, wanda shi ne kofa, ya kuma raba tsakanin wuri mai-tsarki da harabar ta waje, yana misaltar aikin hidima da Kristi Ya shiga yi da zaran ya koma sama. Aikin priest ne a hidima ta kowace rana shi gabatar ma Allah jinin hadaya na zunubi, da kuma turare da yakan tashi zuwa sama tare da addu'o'in Israila. Hakanan ne Kristi ya yi anfai da jininsa a gaban Uban a madadin masu zunubi, ya kuma gabatar masa a gabansa, tare da turaren adalcin kansa, addu'o'in masu ba da gaskiya da suka tuba. Haka aikin hidima a wuri na fari na haikali na sama yake.

Zuwa wurin ne bangaskiyar almajiran Kristi ta bi su yayin da ya haura sama suna hallon tafiyarsa. Nan ne begensu ya kasance. "Wanda muna da shi kamar anchor na rai, tabbatachen bege mai-tsayawa, mai-shiga kuma chikin abin da ke chikin labulen; inda Yesu kamar shugaba ya shiga dominmu, da ya rigaya ya zama babban priest har abada." "Ba kwa ta wurin jinin awaki da yan maruka ba, amma tawurin jini nasa, ya shiga so daya dungum chikin wuri mai-tsarki, bayan da ya jawo pansa ta har abada." Ibraniyawa 6:19, 20; 9:12.

Har karni sha takwas aikin kafaran nan ya ci gaba wuri na farko a haikalin. Jinin Kristi ya rika roko a madadin masu bada gaskiya, yana samo masu gafara da karbuwar Uban, duk da haka zunubansu sun kasance a cikin littattafan da aka rubuta su. Kamar yadda a hidimar tshohon haikalin akan yi aikin kafara a karshen shekara, hakanan kafin kamalawar aikin Kristi na fansar mutane akwai aikin kafara domin kawas da zunubi daga haikalin. Hidiman da ya fara ke nan a karshen kwana 2300 din. A wancan lokacin, bisa ga annabcin Daniel, Babban Priest namu Ya shiga wuri mafi-tsarki domin aiwatar da sashin karshe na aikinsa mai-saduda, watau tsarkake haikalin.

Kamar yadda a da akan jibga zunuban mutanen a kan hadaya ta zunubin, tawurin bangaskiya, kuma tawurin jinin hadayan akan zubar da shi a haikalin, bisa ga alama, hakanan ne a sabon alkawalin, tawurin bangaskiya, ana jibga zunuban masu tuba a kan Kristi, a kuma zuba su zahiri a haikali na sama, kuma kamar yadda akan tsarkake haikali na duniya tawurun cire zunuban da suka kazamtar da shi, hakanan ne za a ainihin tsarkake na saman tawurin sharewan zunuban da aka rubuta a wurin. Amma kafin a yi wannan, sai

an bincika littattafan domin a sansance wadanda, ta wurin tuba daga zunubi da bangaskiya ga Kristi, sun cancanci moriyar kafararsa. Sabo da haka tsarkakewar haikalin ta kunshi bincike, wanda kuwa wani fanni ne na hukumci. Dole a yi wannan aikin kafin zuwan Kristi domin shi fanshi mutanensa, domin sa'an da zai zo, ladarsa na tare da shi da zai ba kowa gwalgwadon aikinsa. Ruya 22:12.

Saboda haka wadanda suka bi hasken kalmar annabcin suka ga cewa maimakon zuwa duniya a karshen kwana 2300 din a 1844, Kristi ya shiga wuri mafi-tsarki na haikalin sama ne domin shi aiwatar da aikin kamalawar kafara domin shirya zuwansa.

An kuma ga cewa, yayin da hadaya ta zunubin ta misalta Kristi a matsayin sa na hadaya, babban priest kuma ya misalta Kristi a matsayin matsakanci, bunsurun Azasel ya misalta Shaitan ne, tushen zunubi, wanda a kansa ne za a jibga zunuban masu ainihin tuba. Sa'anda babban priest, ta wurin yin hadaya ta zunubi, ya cire zunubai daga haikalin, yakan jibga su a kan bunsurun Azazel ne. Sa'anda Kristi, ta wurin jinin kansa, ya cire zunuban mutanensa daga hailaki na sama a karshen hidimarsa, za ya jibga su a kan Shaitan ne wanda a lokacin aiwatar da hukumcin, dole zai dauki dukan horon. Akan kai bunsurun Azazel din wata kasa inda ba kowa ne, ba kuwa zai sake dawowa cikin Israilawa ba. Hakanan ne za a kori Shaitan har abada daga wurin Allah da mutanensa, za a kuma share shi kwata kwata daga kasancewa. Sa'anda za a hallaka zunubi da masu-zunubi a karshe.

Babi na 24—Cikin Wuri Mafi-Tsarki

Batun haikalin ne mabudin da ya bude asirin yankan burin nan na 1844. Ya bayana cikakken tsarin gaskiya da ya nuna cewa hannun Allah ne ya jagoranci babban aikin nan game da zuwan Kristi ya kuma bayana aikin da ya kamata mutanensa su yi yanzu. Kamar yadda almajiran Yesu, bayan daren bakincikinsu da yankan burinsu, suka ga Ubangiji, haka wadanan yanzu suka yi farinciki, su wadanda sun yi begen zuwansa na biyu da bangaskiya. Sun yi begen bayanuwarsa cikin daukaka domin ba da lada ga bayinsa. Da shike burinsu bai cika ba, suka manta da Yesu, tare da Maryamu a kabarin kuma suka ce: “Sun dauki Ubangiji daga chikin kabarin, ba mu san inda sun ajiye shi ba.” Yanzu kuma sun gan shi a wuri mafi-tsarki, Shi Babban Priest nasu wanda jima kadan zai bayana a matsayinsa na sarkinsu mai-kubutar da su. Haske daga haikalin ya haskaka baya da yanzu da nan gaba. Sun san cewa Allah ya shugabance su tawurin kadararsa mara kuskure. Ko da shike, kamar almajiran farkon, su kansu basu fahimci sakon da suke dauke da shi ba, duk da haka sakon daidai ne ta kowace fuska. Shelarsa da suka yi sun cika nufin Allah ne, kuma aikinsu bai zama banza ba, ga Ubangiji. Da shike an sake samo su zuwa ga bege mai-rai, suka yi murna kwarai “da murna wadda ta fi gaban a fadi, chike da daukaka kuma.”

Annabcin Daniel 8:14 cewa: “Har yamma da safiya guda alfin da dari uku: kana za a tsarkake wuri mai-tsarki,” da sakon malaika na fari cewa: “Ku ji tsoron Allah, ku ba shi daraja; gama sa’ar hukunchinsa ta zo,” suna batun hidimar Kristi ne a wuri mafi-tsarki, game da shari’a ta bincike, amma ba zuwan Kristi domin fansar mutanensa da hallakawar miyagu ba. Kurskuren bai shafi lissafin zamanun annabcin ba, amma a kan abinda zai faru ne a karshen kwana 2300 din. Ta wurin kuskuren nan masu bi sun sha cizon yatsa, amma kuma duk abinda annabcin ya fada da dukan abin da suka yi bege, sun cika. Daidai lokacin da suke bakincikin yankan burinsu, al’amarin da aka yi annabcin sa ya cika, kuma dole ne a cika shi kafin Ubangiji ya bayana domin ba da lada ga bayinsa.

Kristi Ya zo, ba a duniya ba yadda suka zata, amma kamar yadda alamar ta nuna, Ya shiga wuri mafi-tsarki ne a haikalin Allah a sama. Annabi Daniel ya nuna cewa a wannan lokaci yana zuwa wurin mai-zamanin da ne. Ya ce: “A chikin ruyai na dare na gani, ga shi, tare da gizagizan sama, wani ya zo mai-kama da dan mutum; ya zo kuma har wurin mai-zamanin da, aka kawo shi a gabansa har ya yi kusa.” Daniel 7:13.

Annabi Malachi ma ya yi annabcin wannan zuwan. Ya ce: “Ubangiji ma wanda ku ke bidassa za ya zo a haikalinsa ba labari; malaikan alkawali kuma, wanda ku ke murna da shi, ga shi, yana zuwa, in ji Ubangiji mai-runduna.” Malachi 3:1. Zuwan Ubangiji haikalinsa faraf daya ne, ba tsammani ga mutanensa. Basu zata zai zo wurin ne ba. Sun zata zai zo duniya ne, “chikin wuta mai-huruwa, yana daukan ramako bisa wadanda ba su san Allah ba, da wadanda sun ki yin biyayya ga bisharar.” Tasalunikawa II, 1:8.

Amma mutanen ba su shirya saduwa da Ubangiji ba tukuna. Akwai aikin shiryawa da za a yi masu. Za a ba da haske da zai bi da tunaninsu zuwa haikalin Allah a sama, kuma yayin da tawurin bangaskiya za su bi Babban priest na su cikin hidimarsa a can, za a bayana masu sabon haske. An kuma shirya ba ekklesiya wani sakon gargadi da umurni kuma.

Annabcin ya ce: "Amma wane ne za ya daure da ranar zuwansa? Wane ne kwa za ya tsaya kadan ya bayana? Gama yana kama da wutar mai-gyaran karfe, kamar sabulun mai-gyaran tufa; za ya kwa zamna kamar mai-gyaran azurfa mai-tsarkakenwatta, kuma za ya tsarkake yayan Levi, yana sabtatadda su kamar zinariya da azurfa; har su mika ma Ubangiji hadayu chikin adilchi." Malachi 3:2,3. Wadanda ke raye a duniya sa'anda tsakancin Kristi a cikin haikali na sama za ya kare za su tsaya a gaban Allah Mai-tsarki ba matsakanci. Dole tufafinsu su kasance babu la'ani, a tsarkake halayensu daga zunubi ta wurin jinin yayyafawa. Ta wurin alherin Allah da kokarin kansu, dole su yi nasara cikin yaki da mugunta. Yayin da hukuncin binciken ke gudana a sama, yayin da ake cire zunuban masu bangaskiya daga haikalin, za a yi aiki na musamman, na kawas da zunubi daga mutanen Allah a duniya. An fi bayana wannan aikin a cikin sakonin Ruya 14.

Sa'anda an kamala aikin nan, masu bin Kristi za su kasance a shirye domin bayyanuwarsa. "Sa'an nan hadayar Yahuda da Urushalima za ta zama abu mai-dadi ga Ubangiji, kamar chikin kwanakin da, chikin shekaru na tuntuni." Malachi 3:4. Sa'anan ekklesiyar da Ubangijinmu za ya karba ma kansa zai kasance "ekklesiya mai-daraja, ba tare da aibi ko chira ko kowane abu misalin wadannan." Afisawa 5:27. Sa'an nan za ta kasance "mai-leke kamar safiya, kyakyawa che kamar wata, garai kamar rana, mai-ban tsoro kamar rundunar yaki da tutochi." Wakar Wakoki 6:10.

Ban da zuwan Ubangiji haikalinsa, Malachi ya kuma yi annabcin zuwansa na biyu, don zartas da hukuncin. Ya ce: "Zan zo kusa da ku domin shari'a; zan zama shaida mai-samri a bisa masu sihiri, da mazinata, da masu-natsuwa da karya, da wadanda ke yi ma mai-aikin lada zalumchi wajen zanchen hakinsa, suna aikin zalunchi ga gwamruwa, da maraya, suna hana ma bako wajibinsa, ba su kwa ji tsoro na ba, in ji Ubangiji mai-runduna." Malachi 3:5. Yahuda ya ambaci al'amri dayan inda ya ce: "Ku duba ga Ubangiji ya zo da rundunan tsarkakansa, garin ya huykumta shari'a bisa dukan mutane, domin shi kada dukan masu fajirchi kuma a kan dukan ayukansu na fajirchi da suka yi chikin fajirchinsu." Yahuda 14,15. Wannan zuwan da zuwan Ubangiji wurin haikalinsa abu biyu ne daban dabam.

Zuwan Kristi a matsayin Babban Priest namu a wuri mafi-tsarki don tsarkake haikalin da Daniel 8:14 ya ambata; zuwan Dan mutum wurin mai-zamanin da, wanda Daniel 7:13 ya ambata, da zuwan Ubangiji haikalinsa da Malachi ya yi annabcinsa suna bayana abu dayan ne, kuma an misalta wannan a wurin zuwan angon a wurin bukin auren, wanda Kristi ya bayana a cikin misalin nan na budurwai goma na Matta 25.

A cikin damina da kaka na 1844, an yi shelan nan cewa: “Angon ya zo!” Sassa biyu da budurwai masu azanci da marasa azancin suka misalta sun bayyana: sashi daya masu sauraron zuwan Ubangiji da farinciki, suna kuma shiri sosai don saduwa da shi, wani sashin kuma cike da tsoro suka gamsu da ganewar gaskiyar kawai, amma ba su da alherin Allah. Cikin misalin, sa’anda angon ya zo, wadanda suna nan a shirye suka shiga tare da shi wurin anganchi.” A nan an nuna cewa zuwan angon zai faru kafin auren ne. Auren yana misaltar karban mulkinsa da Kristi zai yi ne. Birni mai-tarkin, Sabuwar Urushalima wadda ita ce babban birni da wakiliyar mulkin, ana kiran ta “amarya, matar Dan rago.” Malaikan ya ce ma Yohanna: “Ka zo daganan, ni nuna maka amarya, matar dan rago.” “Ya dauke ni cikin ruhu,” in ji annabin, “ya nuna mani birni mai-tsarki Urushalima, tana sabkowa daga chikin sama wurin Allah.” Ruya 9-10.

A bayyane dai amaryar tana misaltar Birni Mai-tsarki ne, budurwai da suka fita domin su sadu da angon kuma misalin ekklesiya ne. Cikin littafin Ruya an ce mutanen Allah ne aka gayyace halartar bukin auren. Ruya 19:9. Idan gayyatattu ne, ba za a misalta su da amarya ba. Annabi Daniel ya ce Kristi zai karbi sarauta da daukaka da mulki daga wurin mai-zamanin da, za ya karbi Sabuwar Urushalima, babban birnin mulkinsa, “shiryayya kamar amarya da ado domin mijinta.” Daniel 7:14; Ruya 21:2. Sa’an da ya karbi mulkin, zai zo cikin darajarsa, Sarkin sarakuna da Ubangijin iyayengiji, domin fansar mutanensa, wadanda za su zauna tare da Ibrahim da Ishaku da Yakubu a tebur dinsa a cikin mulkinsa (Matta 8:11; Luka 22:30), don shiga bukin auren Dan ragon.

Shelar cewa “Ga Ango!” da aka yi cikin daminan 1844 ta sa dubbai suka yi tunanin zuwan Ubangiji nan da nan. Daidai lokacin, Angon ya zo, ba a duniya ba, yadda mutane suka zata, amma zuwa wurin Mai-zamanin da a sama, zuwa auren, watau bukin karban mulkinsa. “Wandanda suke shirye suka shiga tare da shi wurin anganchi: aka rufe kofa.” Ba a ce za su kasance a wurin angancin su kan su ba; domin a sama ne anganci ke gudana, su kuma suna duniya ne. Masu bin Kristi za su zama “masu duban hanyar Ubangijinsu, sa’anda za ya koma daga bukin anganchi.” Luka 12:36. Amma za su gane aikinsa, su kuma bi shi tawurin bangaskiya yayin da zai shiga wurin Allah. Ta hakanan ne ake cewa sun shiga wurin angancin.

Cikin misalin budurwai din, masu mai a cikin santulansu da fitilunsu ne suka shiga wurin angancin. Wadanda, hade da sanin gaskiya daga Littafin, suna kuma da Ruhun Allah da alherinsa, wadanda kuma cikin daren gwajinsu, suka yi hakurin jira, suna nazarin Littafin don Karin haske, su ne suka ga gaskiya game da haikali na sama, da kuma sakewar hidimar mai-ceton, ta wurin bangaskiya kuma suka bi Shi cikin aikinsa a haikali na sama. Kuma dukan wadanda tawurin shaidar Littafin su ke karban gaskiya dayan, suna bin Kristi ta wurin bangaskiya yayin da ya ke shigowa gaban Allah don aiwatar da aikin tsakanci na karshe, a karshensa kuma Shi karbi mulkinsa; dukan wadannan ana misalta cewa sun shiga wurin angancin ne.

Cikin misali na Matta 22 an gabatar da misalin nan na aure, an kuma misalta cewa shari'a ta binciken tana faruwa ne kafin angancin. Kafin angancin. Sarkin ya shigo domin ya ga wadanda aka gayyata, domin ya ga ko kowa ya sa rigar angancin, tufafi mara aibi na hali wanda aka wanke ya zama fari cikin jinin Dan ragon. Matta 22:11; Ruya 7:14. Wanda aka iske ba ya yafe da rigar, an fitar da shi, amma dukan wadanda an bincika an ga suna yafe da rigar angancin, Allah ya karbe su, an kuma tabbatar cewa sun cancanci rabo cikin mulkinsa, da wurin zama kuma a kursiyinsa. Wannan aiki na binciken hali, na sansance wadanda ke shirye domin mulkin Allah shi ne shari'ar bincike, aiki na karshe a haikali na sama.

Sa'anda aikin bincike ya kare, sa'anda aka kamala shari'ar dukan wadanda a dukan sarraki suka ce su masu bin Kristi ne, sa'an nan ne, ba kafin nan ba, za a rufe gafara, a kuma rufe kofar jin kai. Ta hakanan, cikin furcin nan, "Wadanda suna nan a shirye suka shiga tare da shi wurin anganchi: aka rufe kofa," ana kai mu ta wurin hidimar karshe ta mai-ceton, zuwa lokacin da za a kamala babban aikin nan na ceton dan Adam.

A hidimar haikali na duniya, wanda misali ne na hidimar haikali na sama, sa'an da Babban Priest a Ranar Kafara ya shiga wuri mai-tsarki, aiki a wuri na farin yakan tsaya. Allah Ya umurta cewa; "Babu mutum da za ya kasanche a chikin tent na taruwa sa'anda ya shiga garin ya yi kafara a wuri mai-tsarki, har lokacin da ya rigaya ya fito." Leviticus 16:17. Saboda haka sa'anda Kristi ya shiga wuri mai-tsarki don aiwatar da aikin karshe na kafara, ya dena hidimarsa a wuri na farkon. Amma sa'anda hidimar wuri na fari ta kare, hidimar wuri na biyu ta fara kuma. A hidimata misalai din, sa'anda babban priest ya bar wuri mai-tsarki a Ranar Kafara, ya kan shiga a gaban Allah ya mika jinin hadaya ta zunubi a madadin dukan Israilawa da suka tuba da gaske daga zunubansu. Sabo da haka Kristi ya kamala sashi daya na aikinsa ne a matsayinsa na matsakancinmu, domin shiga wani fannin aikin kuma, ya kuma nuna jinin sa a gaban Uban a madadin masu zunubi.

Adventist ba su fahimci batun ba a 1844. Bayan lokacin da aka zata Mai-ceton zai zo ya wuce, sun ci gaba da zaton cewa zuwansa ya kusa, suka aza cewa sun kai wani muhimmin hargitsi ne, kuma aikin Kristi na matsakancin mutum a gaban Allah ya kare, suka dauka cewa Littafin yana koyar da cewa za a rufe gafara jima kadan ne kafin ainihin zuwan Ubangiji cikin gizagizai na sama. An dauka cewa wannan a bayane yake daga nassosin da ke annabcin lokacin da mutane za su nema, su kwankwasa, su kuma yi kuka a kofar jin kai, kuma ba za a bude ba. Tambayar a gare su ita ce ko ranar da suka zata Kristi zai zo ba ita ce farkon lokacin nan da zai gabaci zuwansa ba? Sa'anda suka ba da gargadi cewa hukumcin ya kusa, suka ji kamar sun gama aikinsu ga duniya ke nan, suka rasa himmarsu ta ceton masu-zunubi, yayin da ba'a da sabon masu fajirci ya zama masu kamar wata shaida kuma cewa an rigaya an janye Ruhun Allah daga masu kin jin kansa. Dukan wannan ya karfafa su cikin zatonsu cewa an rufe gafara, ko kuma an rufe kofar jin kai.

Amma Karin haske ya samu sa'anda aka yi nazarin batun haikalin. Sai suka ga cewa daidai ne da suka gaskata cewa karshen kwana 2300 din nan a 1844 farkon wani muhimmin hargitsi ne. Amma yayin da gaskiya ne cewa wancan kofar bege da jinkai da mutane sun rika bi don saduwa da Allah har shekara 1800 ta rufu, an kuma bude wata kofar, aka kuma mika ma mutane gafarar zunubi ta wurin shiga tsakani na Kristi a wuri mafi-tsarki. An rufe wani sashi na hidimarsa, domin a fara wani sashen kuma. Akwai dai "budaddiyar kofa" zuwa haikali na sama inda Kristi ke hidima a madadin mai-zunubi.

Wannan lokacin ne aka ga cikar maganar Kristi zuwa ga ekklesiya a wannan lokacin, inda ya ce: "Ga magana da wannan ya fadi wanda yake mai-tsarki, shi wanda yake mai-gaskiya, wanda yake da makublin Dawuda, wanda ya bude, ba mai-rufewa, ya rufe, ba mai-budewa; na san ayukanka (ga shi, na sa kofa a gabanka budaddiya, wadda ba mai-rufewa)" Ruya 3:7,8.

Masu bin Yesu ta wurin bangaskiya cikin babban aikin kafaran nan ne su ke samun moriyar tsakancinsa a madaddinsu, yayin da masu kin hasken da ke bayana wannan aikin ba sa cin moriyarsa. Yahudawa da suka ki hasken da aka bayar a zuwan Kristi na farko, suka kuma ki karban shi a matsayin Mai-ceton duniya, basu iya samun gafara ta wurinsa ba. Sa'anda Yesu, lokacin komawarsa sama ya shiga ta wurin jinin kansa cikin haikalin sama domin shi zuba ma al'majiransa alabrkun tsakancinsa, aka bar Yahudawa cikin bakar duhu suna ci gaba da hadayunsu da baye bayensu marasa anfani. Hidimar misalai da alamu ta kare. Kofan nan da da ake bi don zuwa wurin Allah an rufe shi. Yahudawan sun ki nemansa ta hanyar kadai da za su iya samunsa a wancan lokacin ta wurin hidima ta haikali na sama, sabo da haka ba su sami sadarwa da Allah ba. A garesu an rufe kofar. Ba su da sanin cewa Kristi ne ainihin hadaya, kuma shi ne kadai matsakanci a gaban Allah, sabo da haka ba su iya samun moriyar tsakancinsa ba.

Yanayin Yahudawa marasa ba da gaskiyan nan yana misalta yanayin Kirista marasa ba da gaskiya ne, wadanda da gangan suka jahhilci aikin Babban Priest namu mai-jinkai. A hidimar alamu, sa'anda babban priest ya shiga wuri mafi tsarki, akan bukaci dukan Israila su taru a haikalin, cikin saduda kuma su kaskantar da kansu a gaban Allah, domin su karbi gafarar zunubansu, kada a yanke su daga taron jama'ar. Ashe kuwa wajibi ne gare mu a wannan Ranar kafara na ainihin mu fahimci aikin Babban Priest namu, mu kuma san aikin da ake bukata daga wurin mu.

Mutane ba za su iya kin kashedin da Allah cikin jin kai Ya ba su, ba tare da sakamako ba. An aika da sako daga sama a zamanin Nuhu, kuma cetonsu ya dangana ga yadda suka yi da wannan sakon. Da shike sun ki gargadin, aka janye Ruhun Allah daga garesu, suka hallaka a ruwan ambaliyar. A zamanin Ibrahim mazamman Sodom sun dena samun jin kai, kuma dukansu, ban da Lot da matar sa da 'ya'yan sa biyu suka kone cikin wutar da aka aika daga sama. Haka a zamanin Kristi ma. Dan Allah ya bayana ma Yahudawa marasa ba da gaskiya a cewa: "Ga shi am bar maku gidan ku kango." Matta 23:38. Game da kwanakin

karshe, Allah dayan Ya furta game da wadanda “ba su amsa kamnar gaskiya da za su tsira ba.” “sabili da wannan fa Allah yana aike masu da aikawar sabo har da za su gaskanta karya: domin a hukumta shari’a bisa dukan wadanda ba su gaskanta gaskiya ba, amma suka ji, dadin rashin adilchi.” Tasalunikawa II, 2:10-12. Yayin da su ke kin koyaswar Kalmarsa, Allah yana janye Ruhunsa, yana kuma barinsu ga rudun da suke so.

Amma Kristi da yana tsakanci a madadin mutum, kuma za a ba da haske ga masu bidarsa. Ko da shike da farko Adventist ba su gane wannan ba, daga baya an bayana shi sa’anda suka fara gane nassosin da suka bayana ainihin matsayinsu.

Bayan wucewar lokaci a 1844, wani lokaci na babban gwaji ga wadanda suka ci gaba da rike bangaskiyar zuwan Yesu ya biyo baya. Saukin su kadai, game da gane ainihin matsayinsu, shi ne haske da ya kai hankulansu haikali na sama. Wadansu suka janye bangaskiyarsu ga fassararsu ta annabcin lokaci, suka danganta tasirin Ruhu Mai-tsarki game da aikin, da akin Shaitan ko mutane. Wani sashe ya nace dai cewa Ubangiji ne ya bishesu can baya; kuma yayin da suka jira suna tsaro da addu’a don sanin nufin Allah, suka ga cewa Babban Priest na su Ya shiga wani aikin hidima ne, kuma da suka bi shi ta wurin bangaskiya, aka kuma nuna masu aikin karshe na ekklesiya. Suka sami karin ganewar sakon malaika na fari da na biyu, suka kuma kasance a shirye domin su karba su kuma ba duniya kashedin nan na malaika na uku na Ruya 14.

Babi na 25—Dokar Allah Ba Ta Sakewa

“Aka bude haikalin Allah da ke chiki sama, a chikin haikali na sa kuma aka ga sanduki na alkawalinsa.” Ruya 11:19. Sandukin alkawalin Allah yana cikin wuri mafi-tsarki ne. A hidimar haikali na duniya wadda alama ce da kwatancin al’amura na sama, akan bude wannan wuri na biyu a haikalin. Sabo da haka sanarwar cewa an bude haikalin Allah a sama, kuma an ga sandukinsa ya nuna cewa an bude wuri mafi-tsarki na haikalin sama ke nan a 1844, sa’anda Kristi ya shiga wurin domin aiwatar da aikin karshe na kafara. Wadanda ta wurin bangaskiya suka bi Babban Priest nasu yayin da ya shiga hidimarsa a wuri mafi-tsarkin sun ga sandukin alkawalinsa. Sa’anda suka yi nazarin batun haikalin, sun gane sakewar hidimar Mai-ceton, suka kuma ga cewa yanzu yana hidima a gaban sandukin Allah ne, yana anfani da jininsa a madadin masu zunubi.

Sandukin cikin haikali na duniya ya kunshi alluna biyu na dutse da aka rubuta dokokin Allah a kai. Sandukin dai wurin ajiya ne na allunan dokar, kuma kasancewar dokokin ya ba sandukin darajarsa da tsarkinsa. Sa’anda aka bude haikalin Allah a sama, an ga sandukin alkawalinsa. Cikin wuri mafi-tsarki, a cikin haikali na sama, an ajiye dokar Allah cikin tsarki-dokan nan dai da Allah kansa Ya furta cikin tsawa na Sinai ya kuma rubuta da yatsansa a allunan dutse.

Dokar Allah a haikali na sama shi ne asalin, wanda kuma dokokin da aka rubuta a allunan dutse, Musa kuma ya rubuta a cikin Littafin, hoton su ne. Wadanda suka kai ga fahimtar wannan muhimmin batun ta hakanan ne aka kai su ga ganin yanayin rashin sakewa na dokar Allah. Sun ga karfin kalmomin Mai-ceton cewa: “Har sama da duniya su shude, ko wasali daya ko digo daya ba za su shude daga Attaurat ba, sai dukan abu ya chika.” Matta 5:18. Da shike dokar Allah bayanin nufinsa ne, hoton halinsa kuma, dole zai dawama, amintacen shaida a sama. Ba a soke ko doka daya ba, ba a soke wasali daya ko digo daya ba. In ji mai-zabura: “Har abada ya Ubangiji maganarka ta kafu a sama.” “Dukan dokokinsa masu aminchi ne. Sun kafu har abada abadin.” Zabura 119:89; 111:7,8.

A tsakiyar dokoki goma akwai doka ta hudu, yadda aka furta ta tun farko: “Ka tuna da ranar assabbat, domin a kiyaye ta da tsarki. Kwana shidda za ka yi aiki, ka kwa gama dukan aikinka; amma rana ta bakwai assabat ne ga Ubangiji Allahnka: cikinta ba za ka yi kowane aiki ba, da kai, da danka, da diyarka, da bawanka, da baiwarka, da bisashenka, da bakonka wanda ke chikin kofofinka: gama chikin kwana shidda Ubangiji ya yi sama da kasa, da teku da abin da ke chikinsu duka, ya huta kuma a kan rana ta bakwai; domin wannan Ubangiji ya albarkachi ranar assabbat, ya tsarkake ta kuma.” Fitowa 20:8-11.

Ruhun Allah Ya shiga zukatan masu nazarin nan na maganarsa. Aka nuna masu cewa sun ketare dokan nan ta wurin rashin kulawa da ranar hutu ta Mahalicin. Suka fara binciken dalilan kiyaye rana ta fari ga mako maimakon ranan da Allah ya tsarkake. Ba su sami shaida a cikin littafin cewa an warware doka ta hudu ba, ko kuma an canja assabbat din ba,

albarkan da ya fara tsarkake rana ta bakwai ba a taba cire ta ba. Da gaske suka rika neman sanin nufin Allah da aikata shi kuma; yanzu da suka ga cewa su masu ketare dokarsa ne, bakinciki ya cika zukatansu, suka kuma nuna biyayyarsu ga Allah ta wurin kiyaye assabbat dinsa da tsarki.

An yi kokari sosai ta hanyoyi da bam dabam don kawas da bangaskiyarsu. Kowa ya gane cewa idan haikali na duniya hoto ne ko kwaikwayon haikali na sama, dokan da aka ajiye a cikin sanduki a duniya daidai hoton dokan da ke cikin sanduki na sama ne; cewa kuma an yarda da gaskiya game da cewa haikali na sama ya kunshi amincewa da dokar Allah da assabbat na doka ta hudu. Wannan ne asirin jayayya mai daci da aka yi game da fassarar nassosi da ta bayana hidimar Kristi a haikali na sama. Mutane suka so su rufe kofar da Allah Ya bude, su kuma bude kofan da Ya rufe. Amma Shi “wanda ya bude, ba mai-rufewa, ya rufe, ba mai-budewa,” Ya rigaya Ya ce, “Gashi na sa kofa a gabanka budaddiya, wadda ba mai-rufewa.” Ruya 3:7,8. Kristi Ya bude kofa ko kuma hidima ta wuri mai-tsarki, haske ya rika haskakawa ta wannan badaddiyar kofar haikali na saman, aka kuma nuna cewa doka ta hudu tana cikin kundin dokar; abin da Allah ya kafa ba wanda zai warware.

Wadanda suka rigaya suka karbi haske game da tsakancin Kristi da dawamar dokar Allah sun iske cewa gaskiyan da aka gabatar cikin Ruay 14 ke nan. Sakonin wannan sura sun kunshi gargadi mai-sassa uku da zai shirya mazamanan duniya domin zuwan Ubangiji na biyu. Sanarwan nan “sa’ar hukuncin sa ta zo,” tana magana game da aikin karshe na hidimar Kristi ne domin ceton mutane. Yana shelar wata gaskiya da dole a dinga shelar ta har sai tsakancin Mai-ceton ya kare, ya kuma dawo duniya domin daukan mutanensa zuwa wurin kansa. Dole aikin hukumcin da aka fara a 1844 ya ci gaba har sai an gama jukumcin dukan mutane, rayayyu da matattu; sabo da haka aikin zai kai har rufewar gafara. Domin mutane su shirya tsayawa gaban shariar, sakon yana umurtarsu, su “ji tsoron Allah (su) ba shi daraja.” Su “yi sujada ga wanda Ya yi sama da duniya da teku da mabulbulan ruwaye.” An nuna sakamakon karban sakonin nan kamar haka: “Nan ga hankurin sarkaka, su wadanda ke kiyaye dokokin Allah da; imanin Yesu.” Domin a shirya ma hukumcin, wajibi ne mutane su kiyaye dokar Allah. Wannan dokan ne za a yi anfani da shi don hukumcin. Manzo Bulus ya ce: “Kuma dukan wadanda sun yi zunubi chikin shari’a bisa ga shari’a za a hukumta masu;… chkin rana da Allah za ya shar’anta asiran mutane, bisa ga bisharata, ta wurin Yesu Kristi.” Ya kuma ce, “masu aika doka za su kubuta.” Romawa 2:12-16. Bangaskiya muhimmin ne ga kiyayewar dokar Allah, gama “ba shi yiwuwa a gamshe shi ba sai tare da bangaskiya.” Kuma “iyakar abinda ba na bangaskiya ba zunubi ne.” Ibraniyawa 11:6; Romawa 14:23.

Tawurin malaika na fari ana kiran mutane su “ji tsoron Allah (su) ba shi daraja” su kuma yi masa sujada a matsayinsa na mahalicin sama da duniya. Domin su yi hakan, dole su yi niyya ga dokar sa. In ji mai-hikimar: “Ji tsoron Allah, ka kiyaye dokokinsa; gama wannan kadai ne wajibin mutum.” Mai-wa’azi 12:13. Idan ba biyayya ga dokokinsa, ba

sujadar da za ta gamshi Allah. “Gama kamnar Allah kenan, mu kiyaye dokokinsa.” “Wanda ya kawasda kunnensa daga jin shari’a, ko addu’atasa abin kyama ce.” 1Yohanna 5:3; Misalai 28:9.

Dalilin sujada ga Allah shi ne cewa shi ne mahalici, kuma dukan sauran ababa ta dalilinsa suke kasancewa. Kuma ko ina, a Littafin, ana shaida bukatarsa ta cewa a yi masa sujada da bangirma, bisa allolin kafirai domin Shi kadai ne mai-ikon halitta. “Gama dukan alloli na alloli gumaka ne; amma Ubangiji ya yi sammai,” Zabura 96:5. “Ga wa fa za ku kamanta ni, da zan zama daidai da shi? in ji Mai-tsarki. Ku ta da idanunku sama, ku duba ko wane ne ya halichi wadannan.” “Gama hakanan Ubangiji ya fadi, shi wanda ya halichi sammai; shi ne Allah; mai-sifanta duniya. Mai yinta kuma, “Ni ne Ubangiji; babu wani kuma,” Ishaya 40:25,26; 45:18. In ji mai-zabura; “Ku sani Ubangiji shi ne Allah: shi ne ya yi mu, mu kwa nasa ne,” “Ku zo, mu yi sujada, mu yi ruku’u; mu durkusa a gaban Ubangiji mahalichinmu.” Zabura 100:3; 95:6. Kuma tsarkaka masu sujada ga Allah a sama suna cewa dalilin da suke masa sujada shi ne cewa “Kai ne mai-isa ka karbi daukaka da daraja da iko, ya Ubangijinmu da Allahnmu; gama kai ka halici dukan abu, saboda nufinka kuma suka kasanche, sabada nufinka aka haliche su.” Ruya 4:11.

Cikin Ruya 14, ana bidar mutane su yi sujada ga Mahalici; kuma annabcin yana ambaton wata kungiya da ke kiyaye dokokin Allah, sakamakon sakon nan mai ressa uku. Daya daga cikin dokokin nan yana nunawa kai tsaye cewa Allah ne mahalicin. Doka ta hudu tana cewa; “Rana ta bakwai ‘assabbat ne ga Ubangiji Allahnka;… gama chikin kwana shidda Ubangiji ya yi sama da kasa, da teku, da abinda kechikinsu duka, ya huta kuma a kan rana ta bakwai: domin wannan Ubangiji ya albarkachi ranar assabbat ya tsarkake ta” Fitowa 20:10,11. Game da assabbat Ubangiji ya kuma ce, “shaida che tsakanina da ku, domin ku sani ni ne Ubangiji Allahnku.” Exekiel 20:20. Dalilin kuma shi ne: “gama chikin kwana shidda Ubangiji ya yi sama da duniya, a chikin rana ta bakwai ya huta, ya lumfasa.” Fitowa 31:17.

“Muhimmancin assabbat a matsayin abin tunawa da halitta shi ne cewa yana tuna mana da ainihin dalilin da ya sa Allah ne ya kamata a yi sujada gare shi.” Domin shi ne mahallici, mu kuma halitunsa ne “sabo da haka Assabbat ne tushen sujada ga mahalici da shike yana koyar da wannan muhimmiyar gaskiyar ta hanya mafi kayatarwa, ba kuma wani abin da ke koyas da hakanan. Ainihin dalilin sujada ga Allah, ba na assabbat ba kawai, dukan sujada, yana kunshe cikin bambanchin nan ne tsakanin mahalici da halitunsa. Wannan ba zai taba zama tsohon abu ba, kuma kada a taba manta shi.” Domin a dinga sa wannan a zukatan mutane ne Allah ya kafa assabbat a Adnin, kuma muddan dai kasanchewarsa mahalicin mu ne dalilin sujadarmu gareshi, assabbat kuwa zai ci gaba kasancewa alamarsa da abin tunawansa. Da duk duniya ta kiyaye assabbat, da tunanin mutum da sha’awoyinsa sun fuskanci Allah a matsayin wanda za a girmama a kuma yi masa sujada, kuma da ba a taba samun wani kafiri ko mai-cewa ba Allah ba. Kiyayewar

assabbat alama ce ta biyayya ga Allah na gaskiya, “shi wanda ya yi sama, da duniya da teku, da mabulbulan ruwaye.” Saboda haka sakon da ke umurtar mutane su yi sujada ga Allah su kiyaye dokokinsa zai kira gare su musamman su kiyaye doka ta hudu.

Sabanin masu kiyaye dokokin Allah suna kuma da imanin Yesu, malaika na uku ya ambaci wata kungiya kuma wadda aka ba da kashedi mai-nauyi game da kurakuranta cewa: “Idan kowane mutum ya yi sujada ga bisan da gunkinsa, ya karbi shaida kuma a goshinsa, ko a hannunsa, shi kuma za ya sha ruwan anab na hasalar Allah? Ruya 14:9,10. Kafin a fahimci sakon nan dole sai an fasara alaman da ke ciki daidai. Mene ne bisan da gumkin, da shaidan ke misaltawa?

Jerin annabcin da ake iske alamun nan a ciki ya fara daga Ruya 12 ne, da dragon da ya so ya hallaka Kristi lokacin haifuwarsa. An ce Shaitan ne dargon din (Ruya 12:9) shi ne ya motsa Hirudus ya nemi kashe Mai-ceton. Amma babban wakilin Shaitan wajen yaki da Kristi da mutanensa a karnonin farko na kristanci mulkin Rum ne, inda kafirci ne addinin da ya mamaye ko ina. Sabo da haka ya yin da dragon ke misaltar Shaitan, a wata hanyar kuma alama ce ta Rum.

Cikin sura 13 (aya 1-10) an bayana wani bisan kuma, mai-kama da damisa, wanda “dragon kuma ya ba shi ikonsa, da kursiyinsa, da hukumchi mai-girma. Yawancin masu kin ikon paparuma sun gaskata cewa wannan alamar mulkin paparuma ne, wanda ya gaji iko da kursiyi da hukumcin da mulkin Rum na da ta taba mallaka. Game da bisa mai-kama da damisan an ce: “aka ba shi baki kuma mai-yin ruba da saba-sabe … ya bude bakinsa kuma domin shi yi sabon Allah, shi sabi sunansa, da mazamninsa, watau wadanda ke zamne a sama nan. Aka yarda masa kuma shi yi yaki da tsarkaka, shi yi nasara da su: aka ba shi kuma hukumchi bisa kowache kabila da al’umma.” Wannan annabci da ya yi kama sosai da kwatacin karamin kaho na Daniel 7, ba shakka yana maganar tsarin paparuma ne.

“Aka ba shi iko kuma da za shi dawama wata arba’in da biyu.” In ji annabin, Na ga dayan kawunansa sai ka che an yi masa bugun ajali.” Kuma: “Idan an kadara kowane mutum ga bauta ga bauta za shi: idan kowane mutum za ya yi kisa da takobi, da takobi za a kashe shi.” Wata arba’in da biyu din daidai suke da “wokachi da wokatai da rabin wokachi,” shekara uku da rabi ko kwana 1260 na Daniel 7, lokacin da mulkin paparuma zai dauka yana zaluntar mutanen Allah. Lokacin nan ya fara da samun fifikon paparuma ne a AD 538, wanda ya kare a 1798. A lokacin ne mayakan Faransa suka mai da paparuma kamame, ikonsa kuma ya karbi bugun ajalinsa, aka kuma cika annabcin nan cewa “Idan an kadara kowane mutum ga bauta, ga bauta za shi.”

A wannan lokaci an kuma fito da wata alama. Annabin ya ce: “Na ga wani bisa kuma yana fitowa daga chikin kasa; yana da kafo biyu kamar dan rago,” Aya11. Kamanin bisan nan da yanayin tasowarsa suna nuna cewa al’umman da ta ke misaltawa ba ta yi kama da wadanda aka bayana a alamun da suka gabata ba. An misalta ma Daniel mulkokin da suka

mallaki duniya da bisashe masu kisa ne da suka taso sa'an da "iskoki fudu na sama suka pasu daga bisa kan teku" Daniel 7:2. Cikin Ruya 17, malaika ya bayana cewa ruwaye suna misalta "al'ummai ne da taron jama'a, da dangogi da harsuna." Ruya 17:15. Iska alamar tashin hankali ne. Pasuwar iskoki hudu na sama a kan teku yana misalta munanan yakoki da manyan tawaye da suka sa wadansu mulkoki suka sami iko.

Amma an ga bisa mai kahoni irin na dan ragon "yana fitowa daga chikin kasa" ne. Maimakon hambare wadansu mulkoki domin ta kafa kanta wannan al'umma da aka misalta dole za ta taso daga wurin da mutane ba su taba zama a cikinta ba ne, ta kuma girma a hankali cikin salama. Ba za ta taso daga al'ummai masu jama'a masu fama kuma na Tshohuwar Duniya, watau tekun nan na "taron jama'a ne.

Wace al'ummar Sabuwar Duniya ce ta yi tashen samun iko a 1798, wadda ta nuna alamar karfi da girma, ta kuma jawo hankalin duniya? Al'umma daya ce kadai ta cika bayanin annabcin nan, watau Amerika. Akai-akai ana anfani da kalmomin Littafin cikin rubuce rubucen tarihi don bayana tasowa da girman al'umman nan. An ga bisan yana "fitowa daga chikin kasa" ne, kuma ma'anar kalmar da aka juya zuwa "fitowa" ita ce yin girma ko kuma tsirowa kamar tsiro, kuma dai dole al'ummar za ta taso daga wurin da ba a taba kasancewa ciki ba ne. Wani shahararren marubuci, game da tasowar Amerika ya yi zancen "asirin tasowarta daga wofi," ya kuma ce: "Kamar iri, shuru muka girma muka zama kasa mai-ikon kanta." Wata majallar Turai a 1850 ta yi magana game da Amerika inda ta ce kasa ce mai-ban mamaki da ke "tasowa" kuma a cikin shurun duniyan nan ta na kara ikonta da alfarmarta." Edward Everett, yayin da yake yabon wadanda suka kafa al'umman nan ya ce: "Sun nemi wuri ne a gefe inda ba hayanniya da shike ba sannanne ba ne, kuma mara hakuri sabo da nisan sa, inda karamar ekklesiyar Leyden din nan za ta mori 'yancin ta na addini? Dubi manyan sassan da cikin nasara cikin salama,… suka rike tutocin giciyen!"

"Yana da kafo biyu kamar dan rago." Kahonin nan suna nuna yarantaka ne, da rashin laifi da tawali'u, daidai yadda Amerika ta ke sa'anda aka nuna ma annabawa cewa tana tasowa a 1798. Cikin Kirista masu hijiran da suka fara gudu zuwa Amerika suka nemi mafaka daga danniyar sarauta da zazzafar ra'ayin priestoci akwai da yawa da suka dukufa wajen kafa gwamnati bisa harsashen 'yancin yangaranci da na addini. Ra'ayoyinsu sun sami shiga Furcin Mulkin-kai, wanda ya ambaci babban gaskiyan nan cewa "an halici dukan mutane daidai ne, kuma suna da 'yanci da ba za a kwace ba, na rai da walwala da neman farinciki." Kundin tsarin mulkin kuma ya na tabbatar ma mutane 'yancin mulkin kai, cewa wakilai ne da mutane masu rinjaye suka zaba zasu kafa dokoki su aiwatarda su kuma. An kuma ba da 'yancin addini, aka yarda kowane mutum shi yi sujada ga Allah bisa ga muradin lamirinsa. Jamhuriyanci da Kin ikon paparuma suka zama muhimman kaidodin al'ummar. Kaidodin nan ne asirin karfinta da ci gabanta. Wulakantattu da wadanda aka zalunce su cikin Kiristanci sukan zo wannan kasar cikin sha'awa da bege. Miliyoyi suna

neman zuwa kasar, Amerika kuwa ta girma ta zama daya daga cikin al'ummai mafi-karfi a duniya.

Amma bisan, mai-kaho irin na dan ragon, "yana kwa zanche kamar daragon. Dukan hukumchin bisa na fari kwa yana aiki da shi a gaban idon sa. Yana sa, duniya da mazamna a chiki su yi sujada ga bisa na fari wanda bugunsa na ajali ya warke,… yana che ma wadanda ke zamne a duniya, su yi gumki ga bisan wanda ya sha bugun takobi ya kwa yi rai." Ruya 13:11-14.

Alamun kaho irin na dan rago da murya kaman na dragon suna misalta sabanin da ke tsakanin da'awa da kuma ayukan al'umman da ake misaltawa ne: ayukan ta suna sabani da maganan ta. "Maganan" al'umman, abinda hukumomin majalisa da na shari'a ta ke yi ne. tawurin ababan da hukumomin nan biyu ke yi al'umman za ta karyata kyawawan kaidodin nan na 'yanci da salama da ta bayana a matsayin harsashen hanyar tafiyar da al'ummaranta. Annabcin cewa za ta yi "zanche kamar dragon," kuma "dukan hukumcin bisa na fari kwa yana aiki da shi," annabci ne kai tsaye na ruhun rashin hakuri da zalunci da al'ummomin da dragon da bisa mai-kama da damisan anan ke misaltawa suka nuna. Batun nan kuma cewa bisa mai kaho biyu "Yana sa duniya da mazamna a chiki su yi sujada ga bisa na fari" a fili yana nuna cewa za a yi anfani da ikon al'umman nan don tilasta ibada da za ta zama aikin mubaya'a ga paparuma.

Wannan abu zai saba ma kaidodin gwamnatin nan, da 'yancin hukumominta, da furcin 'yancin kanta da, da kuma kundin tsarin mulkinta. Wadanda suka kafa kasar sun yi kokarin hana yin amfani da ikon kasa a aikin ekklesiya, wanda dole zai jawo rashin hakuri da zalunci. Kundin tsarin mulkin ya ce "Majalisa ba za ta yi wata doka game da kafawar addini, ko hana 'yancin yin addini ba," kuma cewa "ba gwaji na addini da za a taba anfani da shi ya zama sharadin rike mukami na gwamnatin Amerika ba." Sai dai in an ketare shingayen nan na 'yancin al'umman ne za a iya anfani da ikon gwamnati don tilasta kiyayewar addini. Bisan nan mai-kaho kaman na dan rago, mai-tawali'u, mara cutaswa kuma, shi ne kuma yana magana kamar dragon.

"Yana che ma wadanda ke zamne a duniya, su yi gumki ga bisan." A nan, ana maganan wani tsarin gwamnati ne inda ikon yin doka yana wurin mutane ne, shaida cewa annabcin nan game da Amerika ne.

Amma menene "gumki ga bisan?" kuma yaya za a yi shi? Ana kuma ce da shi gumkin bisan. Idan sansance bisan da yadda za a yi shi dole mu nazarci halayyan bisan kan sa, watau tsarin paparuma.

Sa'anda ekklesiyar farko ta lalace ta wurin rabuwa da saukin kan bishara, ta kuma karbi al'adun kafirci, ta rasa Ruhun Allah da ikonsa, kuma domin ta mallaki lamirin mutane, sai ta nemi goyon bayan iko na duniya. Sakamakon shi ne tsarin paparuma, ekklesiya da ta mallaki ikon kasa da kuma yin anfani da shi don ci gaban manufofinta,

musamman don horon “ridda.” Domin Amerika ta yi gumki ga bisan dole hukumar addini ta mallaki gwamnati ta yadda ekklesiya za ta kuma yi anfani da ikon gwamnati don cim ma manufofinta.

Duk lokacin da ekklesiya ta sami ikon kasa, takan yi anfani da shi don horon masu jayayya da koyaswoyinta. Ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma da suka bi matakan Rum tawurin hada hannu da mulkokin duniya, sun nuna wannan irin hali na son takura ma ‘yancin addini. Misali shi ne zaluncin da Ekklesiyar Ingila ta yi ma masu kin yarda da ita, cikin karni na sha shida da na sha bakwai an tilasta dubban ma’aikatan ekklesiya masu kin yarda da ekklesiya suka gudu daga ekklesiyoyinsu, da yawa kuma, pastoci da sauran mutane, aka sa su biyan tara, ko zuwa kurkuku, ko shan zalunci ko kuma aka kashe su ma.

Ridda ce ta sa ekklesiyar farko ta bidi taimakon gwamnati, wannan kuma ya shirya hanyar haifar da tsarin paparuma, watau bisan. In ji Bulus, “Wannan sai riddan ta fara zuwa, mutamen zunubi kuma ya bayanu”. Tassalunikawa II, 2:3. Sabo da haka ridda cikin ekklesiya ne zai shirya hanya domin gumkin bisan.

Littafin ya bayana cewa kafin zuwan Ubangiji za a tarar da lalacewar addini irin na zamanai na farkon. “Amma sai ku san wannan, chikin kwanaki na karshe miyagun zamanu za su zo. Gama mutane za su zama masu-son kansu, masu-son kurdi, masu-ruba, masu-girman kai, masu-zagi, marasa bin iyaye, marasa-godiya, marasa-tsarki, marasa-kamna irin na tabi’a, masu-bakar zuchiya, masu-tsegumi, marasa-kamewa, masu-zafin hali, marasa-son nagarta, masu-chin amana, masu-taurin kai, masu-kumbura, mafiya-son annishuwa da Allah; suna rike da surar ibada, amma sun musunchi ikonta.” Timothawus II, 3:1-5. “Amma Ruhu yana fadi a sarari, chikin kwanaki na karse wadansu za su yi ridda daga imani, suna mai da hankali ga ruhohi na rudani da koyaswar aljannu.” 1 Timothawus 4:1. Shaitan zai yi aiki “da dukan iko da alamu da al’ajibai na karya, da dukan rudani na rashin adilchi.” Kuma dukan wadanda “basu amsa kamnar gaskiya da za su tsira ba,” za a bari su karbi “aikawar sabo, har da za su gaskanta karya.” Tassalunikawa II, 2:9-11. Sa’anda aka kai wannan mataki na rashin imani irin sakamakon zamanai na farko zai samu.

Da yawa suka gani kaman sabo da yawan bambance-bambancen koyaswoyi tsakanin ekklesiyoyi masu Kin tsarin paparuma ba za a taba yin yunkurin tilasta hadin kai ba. Amma shekaru da dama cikin ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma, ana kara goyon bayan hadewa bisa ga koyaswoyin da suka je daidai. Dan samun wannan hadin kan, dole a rabu da duk wani mahawara ko wata shawara game da al’amuran da aka bambanta akai.

Charles Beecher cikin wani wa’azi a 1846, ya ce hidimar dariku masu Kin ikon paparuma ba an kafa ta duka kalkashin matsin tsoro na mutuntaka ba ne, amma suna raye, suna tafiya, suna lumfashi cikin yanayin lalatuttun al’amura ne, suna kuma kokari kowace sa’a domin su rufe gaskiyar, su kuma rungumi ridda. Ya ce: “Ba hakanan ne ya faru da Rum ba? Ba maimaita rayuwarta muke yi ba? Kuma me mu ke gani a gabanmu? Wata

majalisa ta duka kuma! Taron duniya! Hadin kan dariku da koyaswa daya ta kowa da kowa!" Sa'anda wannan ya faru, domin kokarin samun cikakkiyar daidaituwa, jima kadan za a shiga anfani da karfi.

Sa'anda manyan ekklesiyoyin Amerika suka hada kai bisa ga koyaswoyin da dukansu suka amince da su, idan sun rinjayi gwamnati ta tilasta bin umurnin su ekklesiyoyin da karfafa tsare-tsarensu, Amerika ta kafa gumki ga tsarin Rum ke nan, kuma za a fara horon masu kin yarda ke nan.

Bisa mai-kaho biyu din "yana sa a ba dukan mutane kanana da manya, mawadata da matalauta, yaya da bayi, shaida chikin hannunsu na dama ko a bisa goshinsu; kada kowane mutum kuma shi sani iko kuma shi sayi ko sayas, sai wanda yana da shaidan, watau sunan bisan ko number na sunansa." Ruya 13:16,17. Kashedin malaika na uku din shi ne: "Idan kowane mutum ya yi sujada ga bisan da gunkinsa, ya karbi shaida kuma a goshinsa, ko a hannunsa, shi kuma za ya sha ruwan anab na hasalar Allah." Bisan da aka ambata a cikin sakon nan, wanda bisa mai-kaho biyu din ke tilastawa a yi masa sujada, shi ne bisa na fari, mai-kama da damisa, na Ruya 13 din nan, watau mulkin paparuma" Gunkin bisan yana misalta irin riddan kin ikon paparuma din nan ne da za a kafa sa'anda ekklesiyoyi masu kin ikon paparuma za su nemi taimakon gwamnati don tilasta biyayya ga koyaswoyinsu. Saura a fassara "lamban bisan."

Bayan gardadi kada a yi sujada ga bisan da gunkinsa, annabcin ya ce; "Nan ga su wadanda ke kiyaye dokokin Allah, da imanin Yesu." Da shike an bambanta masu kiyaye dokokin Allah daga masu sujada ga bisan da gumkinsa suna kuma karban lamban sa, ya nuna cewa kiyaye dokar Allah a gefe daya da ketarewarta a daya gefen ne zai bambanta tsakanin masu sujada ga Allah da masu sujada ga bisan.

Hali na musamman na bisan wanda shi ne gumkinsa, shi ne ketarewar dokokin Allah. Game da karamin kahon, watau tsarin paparuma, Daniel ya ce: "Za ya nufa ya sake zamanai da shari'a kuma." Daniel 7:25. Bulus kuma ya ba mulki dayan suna "mutumen zunubi" wanda zai daukaka kansa gaba da Allah. Tawurin sake dokar Allah ne kadai mulkin paparuma zai daukaka kansa gaba da Allah. Duk wanda zai kiyaye dokan da aka sake hakanan da sanin sa, yana ba da mafificin bangirma ga mulkin da ya yi canjin ne. Biyayyan nan ga dokokin mulkin paparuma biyayya ne ga paparuma maimakon Allah.

Mulkin paparuma ya yi yunkurin canja dokar Allah. An cire doka ta biyu da ta hana sujada ga gumaka daga dokar Allah, aka kuma sake doka ta hudu ta yadda ana umurta kiyaye rana ta fari maimakon ta bakwai a matsayin assabbat. Amma yan paparuma suna cewa dalilin cire doka ta biyu shi ne cewa ba ta zama lallai ba, da shike tana kunshe cikin ta fari, kuma cewa wai suna ba da dokar daidai yadda Allah Ya nufa a gane ta ne. Ba wannan ne sakewan da annabin ke magana akai ba. Yana magana game da canji ne gadan-gadan; wanda aka nufa a yi. "Za ya nufa ya sake zamanu da shari'a kuma." Sakewar doka

ta hudu ce ta cika annabcin daidai. An ce da ikon ekklesiya ne kadai aka yi sakewar. A nan mulkin paparuma kai tsaye ya aza kansa gaba da Allah.

Yayin da za a iya bambanta masu sujada ga Allah tawurin girmama assabbat da su ke yi da shike shi ne shaidar ikonsa na halitta, dalilin da ya sa ya cancanci bangirma da biyayya, masu sujada ga bisan za a sansance su ta wurin kokarinsu na rushe abin tunawa na Mahalicin, don daukaka abin da Rum ta kafa. Game da Lahadi ne mulkin paparuma ya fara nuna girman kansa; kuma anfanin sa na farko da ikon gwamnati don tilasta sujada ranan Lahadi ne a matsayin “rana ta Ubangiji”. Amma Littafin yana cewa rana ta bakwai, ba ta fari ba, it ace rana ta Ubangiji. In ji Kristi: “Dan mutum Ubangiji ne har na ran assabbachi.” Ta bakin annabi Ishaya kuma Ubangiji ya che da assabbat “rana ta mai-tsarki.” Markus 2:28; Ishaya 58:13.

Ikirarin da aka cika yi wai Kristi ya sake assabbat ya saba ma maganar Kristi da kansa. Cikin wa’azinsa a kan Dutsen ya ce: “Kada ku zache na zo domin in warware Attaurat da Annabawa; ban zo domin in warware ba, amma domin in chichika. Gaskiya fa ni ke fada maku, har sama da duniya su shude, ko wasali daya ko digo daya ba za ya shude daga, Attaurat ba sai dukan abu ya chika. Dukan fa wanda ya ketare guda daya ma-fi kakanta daga chikin dokokin nan, har ya koya ma mutane haka, za a che da shi mafi karamta a chikin mulkin sama, amma dukan wanda za ya aikata su har ma ya sanas, za a che da shi mai-girma a chikin mulkin sama.” Matta 5:17-19.

Masu Kin mulkin paparuma sun amince cewa Littafin bai ba da dama a canja assabbat ba. Kungiyar wallafa majallu na Amerika da kungiyar Hadin kan “Sunday School” na Amerika sun wallafa wannan a sarari. Dayansu ta amince da cewa Sabon Alkawali gaba daya yayi shuru game da Lahadi, rana ta fari ko kuma umurni game da kiyaye ta.

Wani kuma ya ce: “Har lokacin mutuwar Kristi, ba a canja ranan ba, kuma bisa ga abinda ke rubuce dai manzanin basu… ba da wani umurni cewa a yi watsi da Assabbat na rana ta bakwai, a kuma kiyaye ta a rana ta fari ga mako ba.”

Roman Katolika sun amince cewa ekklesiyarsu ce ta sake assabbat, suna kuma cewa masu Kin ikon paparuma, ta wurin kiyaye Lahadi suna amincewa da ikon paparuma ne. A wata majallar Katolika mai suna a turance “Catholic Catechism of Christian Religion,” garin amsa tambaya game da ranar da za a kiyaye, don yin biyayya ga doka ta hudu, an ce: “A zamanin tshohuwar dokar, Asabar ne ranan da aka tsarkake, amma ekklesiya, wadda Yesu Kristi ya umurce ta, Ruhun Allah kuma ya bishe ta, ta sanya Lahadi a maimakon Asabar, sabo da haka yanzu muna tsarkake rana ta fari, ba ta bakwai ba, Yanzu Lahadi ne rana ta Ubangiji.”

A matsayin shaidar ikon Ekklesiyar Katolika, marubutanta suna anfani da “canjawar Assabbat zuwa Lahadi, wanda masu Kin ikon paparuma suka yarda da shi,… domin ta wurin kiyaye Lahadi, sun amince da ikon ekklesiyar ta umurtawa a yi bukukuwa, wanda

bai yi ba kuma ya yi zunubi.” Kenan mene ne sake Asabbat din, in ba alama, ko lamba, na ikon ekklesiyar Rum ba, watau lamban bisan?”

Ekklesiyar Rum ba ta bar kirarinta na fifiko ba, kuma sa’an da duniya da ekklesiyoyi masu-kin ikon paparuma suka karbi assabbat din da ita ta kirkiro, suka ki Assabbat na Littafin, sun amince da wannan ikirarin ke nan. Suna iya cewa an yi canjin bisa ikon al’ada ne da na Ubanin ekklesiya, amma garin yin haka suna manta ainihin kaidar da ta raba su da Rum, cewa “Littafin, da Littafin kadai ne addinin masu-kin kon paparuma.” Dan paparuma ya gane cewa wadannan suna rudin kansu ne, suna rufe idonsu ga ganin gaskiyan. Yayin da aikin tilasta kiyaye Lahadi ke samun karbuwa, yana jin dadi, a ganin shi daga bisani aikin zai jawo dukan masu Kin ikon paparuma su zama a kalkashin tutar Rum.

Romawa suna cewa; “Kiyaye Lahadi da masu Kin ikon paparuma ke yi, mubaya’a suke yi ga ikon ekklesiyar (Katolika).” Tilasta kiyaye Lahadi da masu Kin ikon paparuma ke yi tilasta yin sujada ga mulkin paparuma ne, sujada ga bisan. Wadanda, ko da shike sun san bukatun doka ta hudu, suka zabi kiyaye jebu maimakon ainihin Assabbat suna mubaya’a ga wannan mulkin ne wanda ke umurta shi. Amma tawurin tilasta ibada tawurin ikon gwamnati, ekklesiyoyin da kansu za su kafa gumkin bisan, sabo da haka tilasta kiyaye Lahadi a Amerika zai zama tilasta sujada ga bisan da gumkinsa ne.

Amma Kiristan sararakin baya sun kiyaye Lahadi, suna gani kamar suna kiyaye Assabbat na Littafin ne, kuma yanzu ma akwai Kirista na kwarai a kowace ekklesiya, har da ekklesiyar Roman Katolika, da suke ba da gaskiya cewa Lahadi ne Assabbat da Allah ya kafa. Allah yana karban sahihancin manufarsu da amincinsu gare shi. Amma sa’anda kiyaye Lahadi ya zama tilas bisa ga doka, aka kuma wayar ma duniya da kai game da takalifin Assabbat na gaskiyan lokacin ne duk wanda ya ketare dokar Allah, ya kuma yi biyayya da dokan da an kafa bisa ikon Rum, yana girmama Rum fiye da Allah ke nan. Yana mubaya’a ga Rum da mulkin da ke tilasta yin abin da Rum ta umurta. Yana sujada ga bisan da gumkinsa. Yayin da mutane a lokacinsu ke kin abinda Allah ya bayana cewa shi ne alaman ikonsa, a maimakon shi kuma suna girmama abin da Rum ta zaba ya zama alaman daukakarta, tawurin wannan suna karban alamar biyayya ga Rum ke nan, watau “Lamban bisan.” Kuma sai an gabatar ma muane da batun a sarari hakanan, aka kuma bukace su su zaba tsakanin dokokin Allah da dokokin mutane, sa’an na wadanda suka ci gaba da ketarewa za su karbi “lamban bisan.”

Barazana ma-fi ban tsoro da aka taba yi ma ‘yan Adam tana kunshe cikin sakon malaika na ukun, ne. Zunubi mai munin gaske ne zai jawo fushin Allah wanda ba a surka da jinkai ba. Ba za a bar mutane cikin duhu ba game da wannan muhimmin batun, za a ba duniya gargadi game da zunubin nan kafin zubowar horon Allah, domin mutane su san dalilin da ake azabtar da su, su kuma sami damar tsere ma horon. Annabci ya ce malaika na fari zai yi sanarwarsa “ga kowane iri da kabila da harshe da al’umma” ne. Gargadin

malaika na ukun, wanda wani fanni ne na sako dayan, shi ma za a baza shi hakanan. Annabcin ya ce da babban murya za a yi shelarsa, ta bakin malaika mai-firiya a tsakiyar sararin sama, kuma za ya jawo hankalin duniya.

Cikin batun hamayyan dukan Kirista za su kasu kashi biyu: masu kiyaye dokokin Allah da imanin Yesu, da masu sujada ga bisan da gumkinsa suna kuma karban lambansa. Ko da shike ekklesiya da gwamnati za su hada kai su tilasta “kanana da manyua, mawadata da matalauta, yaya da bayi” (Ruya 13:16), su karbi “shaidar bisan,” duk da haka mutanen Allah ba za su karbe shi ba. Annabin Patmos yana kallon “wadanda suka fito masu-nasara da bisan, da gumkin, da numba na sunansa, suna tsaye a bisa teku na madubi, suna da girayu na Allah.” Suna kuma raira wakar Musa da wakar Dan rago. Ruya 15:2,3.

Babi na 26—Aikin Canji

Aikin canji na Assabbat da za a yi a kwanakin karshe an yi annabcinsa cikin annabcin Ishaya cewa: “Haka Ubangiji ya fadi, ku kiyaye sahri’a, ku yi adilchi; gama chetona ya kusa yana zuwa, adilchi na kuma shi bayana. Mai-albarka ne mutum wanda ya ke aika wannan, dan mutum kuma wanda ya lizimshe shi, wanda ya tsare assabbat, ba ya tozartadda ita ba, yana kwa tsare hannunsa ga barin yin mugunta.” “Baki kuma wadanda suka hadu ga Ubangiji, domin su yi masa hidima, su kaunachi sunan Ubangiji, su zama bayinsa, kowane wanda ya tsare assabbat, baya tozartadda ita ba, yana kwa rike da wa’adi na; su dai sai in kawo su wurin dutsena mai-tsarki, in faranta zuchiyassu a chikin gidana na addu’a.” Ishaya 56:1,2; 6,7.

Kalmomin nan sun shafi zamanin Kirista. Aya 8 ta ce: “Ubangiji Yahweh wanda yak e tattara warwatsatsu na Isaraila, ya che, Har wa yau, zan tattara masa wadansu, ban da nasa da an rigaya an tattara.” Wannan yana nuna tattarowar al’ummai tawurin bishara. Kuma bisa wadanda ke girmama Assabbat a lokacin an furta albarka. Ta haka bukatar kiyaye doka ta hudu ta zarce lokacin giciye, da tashi, da haurawan Yesu, har zuwa lokacin da bayinsa za su yi wa’azin sakon albishir ga dukan al’umma.

Ubangiji ya umurta ta wurin annabi dayan cewa; “Ka damre shaidan ka hatimche shari’a a wurin almajiraina.” Ishaya 8:16. Ana samun hatimin dokar Allah a cikin doka ta hudu ne. Shi ne kadai cikin dokoki goman ya kunshi suna da matsayin Mai-ba da dokar. Ya bayana cewa Allah ne Mahalicin sammai da duniya, ta haka kuma yana nuna cewa ya cancanci ban girma da sujada fiye da kowa. Ban da wannan dokar, ba komi cikin dokoki goma da ke nuna ko tawurin ikon wane ne aka ba da dokar. Sa’anda mulkin paparuma ya canja Assabbat an dauke hatimi daga dokar. Ana kira ga almajiran Yesu su mayar da hatimin ta wurin daukaka Assabbat na doka ta hudu zuwa matsayin da ya dace da shi na abin tunawa na Mahalici da alamar ikonsa kuma.

“A komo bisa shari’an da shaidan!” Yayin da koyaswoyi da ra’ayoyi masu sabani da juna suka yawaita, dokar Allah ce mizani madawami shi kadai da za a iya auna dukan ra’ayoyi da koyaswoyi da ita. Annabin ya ce: “Idan ba su fadi bisa ga wannan magana ba, hakika babu wayewan gari a gare sub a.” Aya 20.

An kuma ba da umurnin cewa; “Ta da murya, kada ka saukaka; daukaka muryarka kamar kafo, ka shaida ma jama’ata laifinsu, gidan Yakub kuma zunubansu.” Ba muguwar duniyar ba ce, amma wadanda Ubangiji ke kiransu “mutane na” ne za a tsauta masu sabo da laifofinsu. Ya kuma ce; “Lallai kwa suna nemana kowache rana, murnassu ne su san tafarkuna, sai kache al’umma mai-yin adilchi ne, wadda ba ta rabuwa da shari’ar Allahnsu ba.” Ishaya 58:1,2. A nan ana maganan wani sashin mutane ne masu ganin kansu kamar suna da adalci, suna kuma nuna marmarin hidimar Allah sosai; amma tsawa mai-tsanani na Mai-binciken zukata ya bayana cewa suna tattake umurnin Allah.

Saboda haka annabin ya bayana dokar da aka rabu da ita; ya ce: “Za ka sake ginin gindaye na sararaki da yawa; za a che da kai mai-gyaran kufai, mai-mayasda tafarkun da za a zamna a chiki. Idan ka kawas da kafa ga barin aikin garalin kanka a ranar assabbat, rana ta mai-tsarki, ka kuma che da assabbat, abin marmari ne; mai-tsarki na Ubangiji, abin girmamawa; idan kwa ka girmama ta, ba ka aika sha’anin kanka ba, ba ka bidi naka nishadi ba, ba ka kwa fadi zanchen kanka ba; sa’an nan za ka faranta zuchiyarka chikin Ubangiji.” Ishaya 58:12-14. Wannan annabcin yana aiki a zamaninmu. An ketare dokar Allah sa’anda mulkin Rum ta canja Assabbat ne, amma lokaci ya yi da za a mayasda wannan hutun Ubangijin. Za a gyara kufai din a kuma sake gina gindaye na sararakin.

Da shike Allah Ya tsarkake Assabbat ta wurin hutawarsa da albarkasa, Adamu ya kiyaye Assabbat din bayan an kore shi daga gidansa na farinciki. Ubani daga Habila har mai-tsarki Nuhu, zuwa Ibrahim, zuwa Yakubu sun kiyaye ta. Sa’an da zababun mutanen ke bauta a Masar, da yawa a tsakiyar rinjayen bautar gumaka, sun manta dokar Allah; amma sa’anda Ubangiji Ya kubutar da Israila, Ya bayana dokarsa da martaba mai-ban tsoro ga taron jama’ar, domin su san nufinsa, su kuma ji tsoronsa, su yi biyayya gare shi har abada.

Daga wancan ranan har yau an kiyaye sanin dokar Allah a duniya, kuma ana kiyaye dokana hudu. Ko da shike “mutumin zunubi” ya tatteka rana mai-tsarki na Allah, duk da haka har a lokacin daukakarsa akwai amintattu a boye da suka girmama ranar. Tun lokacin Canjin nan kowace sara akwai masu kiyaye ta. Kullum akwai masu shaida dawamar dokar Allah da takalifin kiyayae Assabat na halitta, sau da yawa ma ko cikin zalunci da reni.

Gaskiyan nan, yadda ake gabatardasu cikin Ruya 14 game da bisara ta har abada za su bambanta ekkesiyar Kristi a lokacin bayyanuwarsa. Gama sakamakon sakon nan mai sassa uku za a sanar da cewa: “Ga su wadanda ke kiyaye dikokin Allah, da imanin Yesu.” Kuma sakon nan ne na karshe da za a bayar kafin zuwan Ubangiji. Da zaran an yi shelarsa, annabin ya ga Dan mutum yana zuwa cikin daraja domin ya yi girbin duniya.

Wadanda suka karbi haske game da haikalin da rashin sakewar dokar Allah sun cika da farinciki da al’ajibi yayin da suka ga ban sha’awar tsarin gaskiya da ta bayyana garesu. Sun so a ba dukan Kirista hasken nan da suka samu. Suka kuma ba da gaskiya cewa za a karbi hasken da farinciki. Amma koyaswoyin gaskiya da za su sa mutane sabani da duniya ba su karbu ga mutane da yawa masu cewa su masu bin Kristi ne ba. Biyayya ga doka ta hudu ta bukaci hadaya wadda da yawa ba su so ba.

Sa’anda aka bayana batun Assabbat, mutane da yawa suka ce: “Mu Lahadi mu ke kiyayewa tun farko, iyayenmu sun kiyaye shi, kuma nagargaru da yawa masu ibada har sun mutu suna kiyaye shi. Idan daidai suka yi, mu ma daidai muke yi. Kiyayewar sabon Assabbat din nan zai sa mu rashin jituwa da duniya, kuma ba za mu yi tasiri bisan su ba. Mene ne ‘yar karamar kungiyar masu kiyaye rana ta bakwai za su samu sabanin dukan

duniya da ke kiyaye Lahadi?" Ta wurin wannan irin maganar ne Yahudawa suka so su ba da hujjar kin Kristi da su ka yi. Allah ya karbi ubaninsu da suka mika hadayu gareshi, don me su yaran ba za su sami ceto ta hanya dayan ba? Haka ma a zamanin Luther 'yan tsarin paparuma suka ce Kirista na kwarai sun mutu cikin imanin Katolika, sabo da haka wannan addinin ya isa ceto. Irin tunanin nan yakan hana ci gaban imani ko ibada.

Da yawa suka koyar da cewa kiyaye Lahadi dadaddiyar koyaswa ce, kuma ekklesiya ne na daruruwan shekaru. Amma sabanin wannan, an nuna masu cewa Assabbat ya fi dadewa da kuma yaduwa, tun kafuwar duniya kanta ne ma, kuma yana da hatimin malaiku da na Allah ma. Sa'anda aka kafa harsashen duniya, sa'anda tauraren safiya suka raira tare, dukan 'ya'yan Allah kuma suka ta da murya don murna, lokacin ne aka kafa harsashen Assabbat. Ayuba 38:6,7; Farawa 2:1-3. Wajibi ne Assabbat ya bukaci bangirman mu; ba mutum ne ya kafa shi ba, kuma bai dangana ga al'adun mutane ba; Mai-zamanin da ne ya kafa shi, maganarsa ta har abada kuma ta umurta shi.

Sa'anda ana jawo hankulan mutane ga batun sabontawar Assabbat, shahararrun ma'aikatan bishara suka kangare ma maganar Allah, suna ba ta fasarar da za ta hana binciken batun. Wadanda kuma ba su bincika ma kansu Littafin ba suka gamsu da ra'ayoyin da sun je daidai da abin da su ke so. Ta wurin musu da al'adun Ubanni, da ikon ekklesiya, da yawa suka so su hambarar da gaskiyar. Masu goyon bayan gaskiyar suka koma ga Littafin domin kare sahihancin doka ta hudun. Talakawa, tawurin maganar gaskiya kadai, suka yi nasara bisa hare haren masana wadanda, cikin mamaki da fushi, suka ga cewa duk da iya maganansu da wayon su, ba su iya yin nasara bisa magana mai-sauki kai tsaye na mutanen nan da suka san Littafin sosai ba.

Da shike ba su da goyon bayan Littafin, da yawa suka ce: "Don me manyan mutanen mu ba su gane batun Assabbat din nan ba? Ai kalilan ne sun gaskata wannan batun. Ba shi yiwuwa a ce ku ke da gaskiya sa'annan dukan masanan duniyan nan suna kuskure." Sun manta cewa irin maganar da aka yi ma Yesu da manzaninsa ke nan.

Don wofinta irin maganan nan, an bukaci anfani da koyaswoyin Littafin ne da tarihin yadda Allah yana aiki tawurin wadanda ke jin maganarsa suna kuma biyayya da ita ne, wadanda in ta kama za su fadi maganan da ba a so a ji, wadanda ba sa tsoron tsawata zunuban da ake yayinsu. Dalilin da ya sa bai cika zaben masana su shugabanci canje canje ba shi ne cewa su kan dogara ga koyaswoyinsu da ra'ayoyinsu da tsare-tsaren ekklesiyoyinsu ne, su kuma ji kamar ba sa bukatar Allah ya koya masu. Wadanda ke da alaka da Tushen hikima, kai tsaye ne kadai za su iya gane ko kuma su bayana Littafin. Wani lokaci akan kira masu kankantar sani na makaranta su bayana gaskiya, ba don basu da ilimi ba, amma domin ba su cika dogara ga iyawar kansu ta yadda za su ki Allah ya koya masu ba. Su kan koya a makarantar Kristi, tawali'unsu da biyayyar su kuma sukan sa su zama manya. Ta wurin ba su sanin gaskiyar, Allah yakan ba su girman da ya fi na duniya.

Yawancin Adventist da sun ki gaskiya game da haikali da dokar Allah, da yawa kuma sun rabu da bangaskiyarsu game da batun zuwan Kristi, suka rungumi ra'ayoyi masu sabani da juna game da annabce-annacben da suka shafi aikin. Wadansu sun shiga kuskuren tsai da takamammen ranar zuwan Kristi a kai a kai. Ya kamata da hasken da ke haskakawa game da batun haikalin a lokacin ya nuna masu cewa babu lokacin annabci da ya kai har lokacin zuwan Yesu na biyu; cewa ba a yi annabcin daidai lokacin zuwan ba. Amma da suka juya daga hasken, sai su ka yi ta tsaida lokaci bayan lokaci da Ubangiji zai zo, kuma sun rika gamuwa da yankan buri.

Sa'anda ekklesiyar Tassalunikawa ta sami ra'ayiyoyin da ba su dace ba game da zuwan Kristi, manzo Bulus ya shawarce su su gwada begensu da maganar Allah. Ya tuna masu da annabce annabcen da ke bayana al'amuran da za su faru kafin Kristi ya zo ya kuma nuna cewa ba su da hujjar yin tsammanin cewa zai zo a zamanin su. "Kada ku bari kowane mutum shi rude ku da ko kaka."(Tasalunikawa II, 2:3). Kalmominsa na fadaka ke nan. Idan suka yarda da zance-zance da littafi bai amince da su kam, za su kai ga rudun marasa ba da gaskiya, za su kuwa shiga hadarin katsewar hanzari su kuma jarabtu ga yin shakkar gaskiyan da suka wajibta domin cetonsu. Gargadin manzon zuwa ga Tassalunikawan ya kunshi wani muhimmin darasi domin wadanda ke raye a kwanakin karshe. Adventist da yawa sun dauka cewa in ba sun kafa bangaskiyarsu ga wani takamammen lokacin da Ubangiji zai zo ba, ba za su iya yin himma da kwazo cikin aikin shiryawa ba. Amma yayin da begensu yana tashi akai akai yana kuma yankewa, bangaskiyarsu tana gigicewa ta yadda yana zama masu da wahala su yi sha'awar muhimman gaskiya na annabci.

Allah ne Ya sa aka koyas da batun takamammen lokacin hukumci sa'anda aka ba da sakon malaika na farin. Lissafin lokutan annabcin da suka shafi sakon, wanda ya aza karshen kwana 2300 a kaka na 1844, babu kuskure a cikinsa. Kokarin da aka dinga yi don samun sabobin ranakun farawa da na karewan lokutan annabcin, da kurakuran dalilan da ake bayarwa don amincewa da wadannan ranakun suna janye tunanin mutane daga gaskiya ta yanzu, su kuma sa a rena duk wani kokari na bayyana annabce annabce. Manufofin Shaitan su kan cika idan ana yawan aza takamammen lokacin zuwan Kristi na biyu ana kuma koya ma mutane hakanan. Bayan lokacin ya wuce, yakan sa a rika rena masu wannan koyaswar ana yi masu ba'a kuma, ta hakanan kuma ya sa a rena babban aikin 1843 da 1844 din nan game da zuwan Kristi na biyu. Masu nacewa da kuskuren nan a karshe za su aza wani lokaci can gaba da nisa da a ganinsu Kristi za ya zo. Ta hakanan za su yi sake, za su rudi mutane da yawa kuma har lokaci ya kure.

Tarihin Israila ta da, kwatanci ne na abinda ya faru da Adventist. Allah ya shugabanci mutanensa cikin aikin nan game da zuwan Yesu na biyu, yadda ya shugabanci 'ya'yan Israila daga Masar. A babban yankan burin nan an gwada bangaskiyarsu yadda aka gwada na Ibraniyawa a Jan Teku. In da sun ci gaba da amincewa da hannun da Ya dinga bishe su cikin rayuwarsu can baya, da sun ga ceton Allah. Da dukan wadanda suka yi aiki tare a

1844 sun karbi sakon malaika na uku, suka kuma yi shelarsa cikin ikon Ruhu Mai-tsarki, da Ubangiji Ya yi aiki sosai cikin kokarinsu. Da ambaliyar haske ta mamaye duniya. Da tun shekaru da suka gabata mazamnan duniya sun sami gargadin, an kamala aikin karshen, Kristi kuma da Ya dawo don fansar mutanensa.

Ba nufin Allah ne Israila suka yi ta yawo a jeji har shekara arba'in ba; ya so ya jagorance su kai tsaye ne har kasar Kan'ana, ya kafa su a wurin, jama'a mai-tsarki, mai-farinciki kuma. Amma ba su iya shiga ba saboda rashin bangaskiya; Ibraniyawa 3:19. Saboda koma-bayansu da riddarsu, sun hallaka a hamadar, aka kuma ta da wadansu suka shiga kusar Alkawalin. Hakanan kuma, ba nufin Allah ne a jinkirta zuwan Kristi da yawa haka, mutanensa kuma su kasance shekaru da yawa hakanan a wannan duniya ta zunubi da bakinciki ba. Amma rashin bangaskiya ya raba su da Allah. Sa'anda suka ki yin aikin da ya ba su, sai aka ta da wadansu da su ka yi shelar sakon. Cikin jin kai ga duniya, Yesu yana jinkirta zuwansa, domin masu zunubi su sami zarafin jin gargadin, su kuma sami mafaka cikinsa kafin a zubo da fushin Allah.

Yanzu, kamar a sararraki na da, bayana gaskiyan da ke sokar zunubai da kurakuran zamanin yakan jawo jayayya. "Gama kowanne wanda ya ke aika mugunta kin haske ya ke yi, kuma ba shi zuwa wurin haske, domin kada ayukansa su tonu." Yohanna 3:20. Sa'anda mutane sun ga cewa ba za su iya tabbatar da ra'ayinsu daga Littafin ba, da yawa sukan nace da rikon ra'ayin dai ko ta halin kaka, da ruhun mugunta kuma su kan dinga zargin halaye da manufofin wadanda ke kare gaskiya. A dukan sararaki haka abin yake. An ce ma Iliya wai shi ne mai wahal da Israila, an kira Irmiya mai-cin amana, aka ce da Bulus mai-kazantar da haikalin. Daga zamanin can zuwa wannan, wadanda ke biyayya ga gaskiya akan zarge su cewa su masu cin amana ne, masu-ridda, ko masu kawo tsatsaguwa. Jama'a da yawa marasa ba da gaskiya ga maganar annabci tabbataciya nan da nan za su yarda da zargin da za a yi ma wadanda ke kwaban zunuban da ake yayinsu. Wannan ruhun zai dinga karuwa. Littafin kuma yana koyarwa a sarari cewa lokaci yana zuwa da dokokin kasa za su saba ma dokar Allah ta yadda dukan wanda zai yi biyayya ga dukan umurnin Allah dole ya shirya fuskantar zargi da horo cewa, shi mai-aikata mugunta ne.

Saboda haka, me ya kamata dan sakon gaskiya ya yi? Zai ce ne bai kamata a bayana gaskiya ba, da shike sau da yawa mutane suna kin ta? Babu; ba shi da dalilin barin yin shelar maganar Allah wai don tana jawo jayayya. An rubuta furcin bangaskyar tsarkaka domin anfanin sararrakin baya ne. Rayayyun masu kwatanta tsarki da aminci suna karfafa wadanda yanzu ake kira su tsaya a matsayin shaidun Allah. Sun karbi alheri da gaskiya, ba don kansu ba kadai, amma domin, ta wurinsu, sanin Allah ya haskaka duniya. Ko Allah Ya ba da haske ga bayinsa na wannan sarar? Sai su hakaka shi ga duniya.

Da can Ubangiji Ya ce ma wani mai-magana a cikin sunansa. "Amma gidan Israila ba za su kasa kunnne gare ka ba; gama ba za su kasa kunne gareni ba." Duk da haka Ya ce: "Za ka fada masu maganata, ko su a ji, ko su ki ji." Ezekiel 3:7; 2:7. Ga bawan Allah a

wannan zamani ana umurta cewa: “Ka ta da murya kamar kaho, ka nuna ma mutanen nan laifinsu, gidan Yakub kuma zunubansu.” Annabin Israilan nan da kalmar Allah ta ce masa: “Hakanan kai fa dan mutum, na sanya ka mai-tsaro ga gidan Israila; domin wannan ka ji Magana ga bakina, ka yi masu fadaka daga gareni. Kadan na che ma mugun mutum, Ya kai mugun mutum, lallai za ka mutu, kai kwa ba ka yi magana domin ka fadakadda mugun shi bar hanyassa; wannan mugun mutum za ya mutu domin laifinsa, amma zan bidi jininsa gareka. Amma idan ka fadakadda mugun mutum domin shi juyo ga barin hanyassa, shi kwa bai juya ga barin hanyassa ba, za ya mutu sabada laifinsa, amma ka chechi ranka.” Ezekiel 33:7-9.

Babban matsala ga karban gaskiya da shelarta it ace cewa ta kunshi rashin jin dadi da zargi. Amma wannan ba ya hana ainihin masu bin Kristi na gaskiya. Ba sa jira wai sai gaskiya ta karbu ga mutane. Sa’anda sun gane takalifin da ya rataya a wuyansu, sukan karbi giciyen, tare da manzo Bulus suna dauka cewa “kunchinmu mai-sauki, wanda ke na lokachi kadan, yana aika dominmu nauyin daraja madawami gaba gaba kwarai,” tare da wani na da suna “mai da zargi domin Kristi wadata ne mafi-girma bisa ga dukiyar Masar.” Korinthiyawa II, 4:17; Ibraniyawa 11:26.

Ko da menene suke fadi, masu son duniya a zuchiyarsu ne su ke bin sauki maimakon kaida da al’amuran addini. Ya kamata mu zabi abin da ke daidai domin shi daidai ne, mu bar abin da zai biyo baya a hannun Allah. Ga masu aminci da bangaskiya da karfin zuciya, dole duniya ta gode masu saboda manyan canje canjen da suka kawo. Wadannan mutanen ne za su ci gaba da aikin canji.

In ji Ubangiji: “Ku kasa kunne gareni, ku masanan adilchi, mutane wadanda shari’a ta tana chikin zuchiyarku; kada ku ji tsoron zargin mutane, kada ku yi fargaba domin zaga zagensu kuma. Gama asu za su chinye su kamar riga, tsutsa kuma za ta chi su kamar ulu; amma adkilchina za ya dawama har abada, chetona kuma har dukan tsararaki.” Ishaya 51:7,8.

Babi na 27—Falkaswa na Zamani

Duk inda aka yi wa'azin maganar Allah da aminci, sakamakon yakan hakikance cewa Allah ne tushen ta, Ruhun Allah ya kasance tare da sakon bayinsa, maganar kuma ta zama da iko. Masu zunubi suka ji an farfado da lamirinsu. Hasken da ke haskaka dukan wanda ya zo cikin duniya ya rika haskaka kowane lungun ransu aka kuma bayana boyayun ababa na duhu. Tunanin su da zukatansu suka tabu kwari. Suka amince cewa akwai zunubi da adalci da hukumci mai-zuwa. Suka sami dandanon adalcin Yahweh suka kuma ji tsoron bayanuwa cikin laifinsu da rashin tsabtarsu, a gaban mai binciken zukata. Cikin bakinciki suka yi kuka cewa, "Wa za ya kubutar da ni daga jikin nan mai-mutuwa?" Sa'an da aka bayana giciyen kalfari da hadayarsa domin zunuban mutane, suka ga cewa ban da halayan Kristi ba abin da ya isa ya yi kafara domin zunubansu; abin da kadai zai iya sasanta mutum da Allah kenan. Da bangaskiya tare da saukin kai suka karbi Dan rago na Allah, wanda ke dauke da zunubin duniya. Ta wurin jinin Yesu sun sami gafarar zunuban da suka wuce.

Wadannan mutane suka haifi 'ya'ya da suka cancanci tuba. Sun ba da gaskiya aka kuma yi masu baptisma, suka kuma taso domin yin tafiya cikin sabon rai, sabobin halitta cikin Kristi Yesu; ba domin sifanta kansu bisa ga sha'awoyi na da ba, amma bisa ga bangaskiya na Dan Allah su bi sawunsa, su kamanta halinsa, su kuma tsabtata kansu, kamar yadda Shi mai-tsabta ne. Ababan da suka ki da, yanzu suka so su, ababan da suka so da kuma, yanzu suka ki su. Masu-girman kai da nuna isa suka zama masu saukin-kai da taushin zuciya, marasa kunya, masu rashin hankuri suka zama natsatsu marasa gagara. Marasa tsarki suka zama masu bangirma, mashaya suka zama natsatsu, fasikai kuma suka zama masu tsabta. Ayukan banza na duniya aka kawar da su. Kirista suka dena bidar "ado na waje, watau su kitson gashi, da sa ado na zinariya, ko yafa tufafi masu kawa, amma, boyayyen mutum na zuchiya, chikin tufafi wadanda ba su lalachewa, na ruhu mai-ladabi mai-lafiya, abin da ke da tamani mai-girma a gaban Allah." 1Bitrus 3:3,4.

Hidimomin falkaswa sun rika jawo bimbini mai-zurfi da tawali'u, sun kunshi roko mai saduda da gaske ga mai-zunubi cikin tausayi saboda jinin Kristi da an saye su da shi. Maza da mata sun yi addu'o'i ga Allah domin ceton rayuka. An ga 'ya'yan wadannan falkaswan cikin rayukan da ba su tsaya kan musun-kai da hadaya kadai ba, amma suka yi farinciki cewa suma sun isa su sha reni da gwaji sabo da Kristi. Mutane sun ga sakewa a rayukan wadanda suka furta sunan Yesu. Jama'a suka anfana ta wurin tasirinsu. Suka tattaro tare da Yesu, suka kuma shuka ga Ruhu, domin su girbe rai madawami.

Game da su ana iya cewa: "Bachin zuchiya da aka yi ya kawo tuba." "Gama bachin zuchiya irin da Allah ke sa ya kan aika tuba zuwa cheto, tuba mara-ladama; amma bakin zuchiya na duniya yana aika mutuwa. Gama wannan abu kansa, bakinzuchiya da aka yi maku irin da Allah ke sa, duba irin kaifin hankali da ya aika a wurinku, i, duba, wache irin kariyar kai, i, wane irin haushi, i, wane irin tsaro, i, wane irin bege, i, wache irin himma, i,

wane irin daukar pansa! Ga kowane abu kuka nuna kanku kubutattu a chikin wannan matsala.” Korinthiyawa II, 7:9-11.

Wannan sakamakon aikin Ruhun Allah ne. Sakewa it ace kadai shaidar ainihin tuba. Idan ya mayar da jingina, ya mayar da abin da ya kwace, kuma, ya furta zunubansa, ya kuma kaunaci Allah da yanuwansa ‘yan Adam, mai-zunubin nan zai sami tabbaci cewa ya sami salama da Allah. Irin sakamakon da suka biyo bayan lokutan falkaswa na addini kenan a shekarun baya. Bisa ga ‘ya’yan da suka haifar aka sani cewa Allah Ya yi masu albarkacikin ceton mutane da kyautata yanayin ‘yan Adam.

Amma da yawa cikin hidimomin falkaswa na zamanin nan sun bambanta kwarai daga almun alherin Allah da suka biyo bayan aikin bayin Allah a zamanin da. Hakika akan ta da marmari sosai, da yawa sukan ce sun tuba, kuma akan zama membobibn ekklesiyoyi, duk da haka sakamakon ba wadanda za su sa a ga cewa karuwar rayuwar ruhaniya ba ne. Hasken da ya kan nuna na wani dan lokaci ya kan mutu nan da nan, ya bar duhun da ya fi na da.

An cika gudanar da falkaswa ta yadda an fi maida hankali ga ababa masu ban mamaki ko ban tsoro, ko ban tausayi. Wadanda suka tuba ta wurin wadannan ba sa sha’awar jin gaskiya ta Littafin, kuma ba su damu da shaidar annabawa da manzani ba. Idan hidima ta addini tana jawo hankali a yi tunani ne kawai, ba a kula ta. Ba sa jin gargadin maganar Allah game da rayuwarsu ta har abada.

Ga kowane mai-tuba na gaskya, dangantaka da Allah da ababa na har abada ne za su zama muhimman ababa gare shi. Amma a shaharrarun ekklesiyoyi yau, ina ake samun ruhun mannewa ga Allah? Tubabbun ba sa barin girman-kan su da son duniya. Ba sa shirye su yi musun kai, su dauki giciyensu, su bi Yesu mai-tawali’u yanzu. Addini ya zama abin wasan kafirai da masu shakka domin da yawa masu addinin ba su san kaidodinsa ba. Ikon ibada ya kusa batawa daga ekklesiyoyi da yawa. Cin guziri na shan iska, nishadi, kyawawan gidaje, da burgewa sun kawar da tunani game da Allah. Filaye da kayan duniya da aikace-aikace na duniya ne suka mallaki tunanin mutane, kuma ababa masu anfani na har abada ba a ko kulawa da su ma.

Ko da shike bangaskiya da ibada sun ragu sosai, akwai masu-bin Kristi na kwarai a cikin wadannan ekklesiyoyin. Kafin hukumcin Allah na karshe a akan duniya, za a iske falkaswar ibada irin ta da a cikin mutanen Ubangiji, irin da ba a taba gani ba tun zamanin manzani. Za a zubo da Ruhun Allah da ikonsa bisa ‘ya’yansa. A wancan lokacin mutane da yawa za su rabu da ekklesiyoyi inda kaunar duniyan nan ta dauki wurin kaunar Allah da maganarsa. Mutane da yawa za su karbi muhimman gaskiyan nan da Allah Ya sa a sanar a wannan lokacin domin shirya jama’a don zuwan Kristi na biyu. Magabcin yana so ya hana wannan aikin, kuma kafin lokacin wannan aikin ya zo, zai yi kokarin hana shi tuwurin fito da jabu. A ekklesiyoyin nan da zai iya kawowa kalkashin ikon sa, zai sa a ga kamar an

zubo da albarkar Allah ta musamman, za a ga kamanin babbar sha'awar addini. Jama'a da yawa za su yi farinciki cewa Allah yana aikata al'ajibai domin su, alhali aikin na wani ruhu ne dabam. Cikin kamanin addini, Shaitan zai so ya fadada aikinsa cikin Krista.

Cikin falkaswa da yawa da aka yi cikin shekaru hamsin da suka gabata, an iske irin ikokin nan da za su yi aiki cikin manyan ayukan da za a yi nan gaba. Akwai nuna murna da garwaya gaskiya da karya ta yadda za a rudi mutane. Duk da haka kada a yaudare ka. Bisa ga maganar Allah yana da sauki a gane yanayin kungiyoyin nan. Duk inda mutane suka rabu da shaidar Littafin, suka juya daga gaskiyan nan bayyanannu masu bidar musun kai da rabuwa da duniya, sai mu sani cewa ba albarkar Allah a wurin. Kuma tawurin ma'aunin da Kristi kansa Ya bayar, "Bisa ga yayansu za ku sansanche su" (Matta 7:16), a bayyane yake cewa wadanan hidimomin ba aikin Ruhun Allah ba ne.

Cikin gaskiyar maganarsa, Allah Ya bayana kansa ga mutane. Ga dukan wadanda suka karbe su, gaskiyan nan garkuwa ce daga rudun Shaitan. Rabuwa da gaskiyan nan ne ya bude kofa ga muguntan da ke yaduwa yanzu cikin addinai na duniyan nan. An manta da yanayin dokar Allah da muhimmancinta. Rashin fahimtar yanayi da dawama da wajibtar dokar Allah ya haifar da kura-kurai game da tuba da tsarkakewa, ya kuma kai ga rage darajar ibada cikin ekklesiya. Wannan ne asirin rashin Ruhun Allah da ikonsa cikin falkaswan zamanin mu.

Cikin dariku dabam dabam, akwai mutane sannanu cikin ibadarsu da suka amince da wannan batun. Shehun mallami Edwards A. Park, game da matsalolin addini yanzu ya ce: "Wani tushen damuwa shi ne kin aiwatar da dokar Allah da ake yi. A zamanun da, shugabannin addini ne suke bayana ainihin addini,… Shahararrun masu wa'azinmu sun dinga ba da martaba ga jawabansu ta wurin bin kwatancin mai-gidan, su na kuma girmama dokar da umurninta da gargadinta. Su kan kuma maimaita cewa dokan nan hoton rashin aibin Allah ne, kuma cewa mutumin da ba ya kaunar dokar, ba ya kaunar bishara ke nan; gama dokar, da bisharar ma, madubi ne mai-bayana ainihin halin Allah. Matsalan nan na rabuwa da dokar Allah tana jawo wata matsalar kuma, ta rena muguntar zunubi da girmansa da ikonsa. Girman dokar daidai yake da girman rashin biyayya gare shi, …

"Dangane da matsalolin da an rigaya an ambata akwai kuma hadarin rena adalcin Allah. Masu wa'azi yanzu sun cika son raba adalcin Allah da kaunarsa, a nutsar da kauna maimakon daukaka shi. Sabon yayin koyaswar addini yana raba abinda Allah ya hada ne. Dokar Allah nagarta ce ko mugunta? Nagarta ce. Ashe adalci nagarta ne, da shike shi adalci aiwatar da doka ne. Daga halin rena dokar Allah da adalcinsa, da rena girman da illar rashin biyayya, mutane nan da nan su kan shiga halin rena alherin da ya tanada kafara domin zunubi." Ta hakanan bishara ta kan rasa anfanin ta da muhimmancinta a zukatan mutane, jima kadan kuma za su so ma su kawar da Littafin kan sa.

Mallamai da yawa na addini suna koyar da cewa wai Kristi tawurin mutuwarsa ya warware dokar, kuma wai daga yanzu mutane suna da ‘yanci su dena boyayya gare ta. Akwai wadanda ke koyar da cewa dokan ma karkiya ce mai-tsanani, kuma sabanin bautar dokar, su na koyar da wani ‘yanci da ake samu kalkashin bisharar.

Amma ba haka manzani da annabawa suka mai da dokar Allah ba. In ji Dawuda: “Zan yi tafiya kuma a sake; gama na bidi shaidun ka.” Zabura 119:45. Manzo Yakub wanda ya yi rubutunsa bayan mutuwar Kristi, ya kira dokoki goman “shari’an nan basarauchiya” da kuma “cikakkiyar shari’a, sahri’a ta yanchi.” Yakub 2:8; 1:25, mai-ruya kuma, shekaru hamsin bayan giciyewar, ya furta albarka kansu wadanan da ke wankin tufafinsu, dominsu sami iko su zo wurin itachen rai, su shiga kuma ta kofofi chikin birni.” Ruya 22:14.

Zancen cewa Kristi tawurin mutuwarsa ya warware dokar Ubansa ba shi da tushe. Da zai yiwu a canja dokar ko kuma a warware shi, da bai zama wajibi ga Kristi ya mutu domin ya ceci mutum daga horon zunubi ba. Mutuwar Kristi, maimakon warware dokar, yana tabbatar da cewa ba za a iya sake ta ba ne, Don Allah ya zo domin “ya daukaka shari’a, ya maishe ta abin kwarjini” ne. Ishaya 42:21. Ya ce: “Kada ku zache na zo domin in warware Attaurat,” “Har sama da duniya su shude, ko wasali daya ko digo daya ba za su shude daga Attaurat ba.” Matta 5:17,18. Game da kansa kuma ya ce: “Murna ni ke yi in yi nufinka, ya Allahna, hakika shari’arka tana chikin zuchiya ta.” Zabura 40:8.

Dokar Allah, daga yanayinsa mara sakewa ne. Bayani ne na manufa da halin mai-ba da shi. Allah kauna ne, dokarsa kuma kauna ce. Muhimman kaidodinta biyu su ne kaunar Allah da kaunar mutane. “Kamna fa chikar shari’a che.” Romawa 13:10. Halin Allah adalci ne da gaskiya haka kuma yanayin dokar sa yake. Mai-zabura yace:“Shari’arka kuma gaskiya che.” “Dukan dokokin ka adilchi ne.” Zabura 119:172. Manzo Bulus kuma ya ce: “Shari’a tsatsarka che, doka kuma tsatsarka che mai-adilchi kwa, tagari che.” Romawa 7:12. Wannan dokar da ke bayana tunanin Allah da nufinsa dole za ta dawama kamar mai ba da ita.

Aikin tuba da tsarkakewa ne su sasanta mutane da Allah ta wurin kawo su ga daidaituwa da kaidodin dokarsa. A cikin farko an halici mutum cikin surar Allah. Ya kasance cikin cikakkiyar daidaituwa da yanayin Allah da dokarsa kuma; an rubuta kaidodin adalci a zuciyarsa. Amma zunubi ya raba shi da mahalicinsa. Bai sake kasancewa cikin surar Allah ba. Zuciyarsa ta dinga yaki da kaidodin dokar Allah. “Domin himmatuwar ji ki gaba che da Allah, gama ba ta chikin biyayya da shari’ar Allah ba, ba ta iya kwa.” Romawa 8:7. Amma “Allah ya yi kamnar duniya, har abada Dansa, haifaffe shi kadai” domin mutum ya sasanta ga Allah. Tawurin adalcin Kristi za a iya mayas da mutum ga daidaituwa da Mahallicinsa. Dole a sabonta zuciyarsa tawurin alherin Allah; dole ya mallaki sabon rai daga sama. Wnnan canjin ne sabuwar haihuwa, wanda idan ba shi, Yesu ya ce “ba za ya shiga mulkin Allah ba.”

Matakin farko don sasantawa da Allah shi ne amincewa an yi zunubi. “Zunubi shi ne ketaren shari’a” “Gama tawurin shair’a a ke sanin zunubi.” 1Yohanna 3:4; Romawa 3:20. Domin ya ga laifinsa, dole mai-zunubi ya gwada halinsa da babban ma’aunin adalci na Allah. Madubi ne da ke nuna cikar halin adalci ya kuma sa shi ya gane aibin na sa halin.

Dokar ta na bayana ma mutum zunubansa, amma ba ta tanada magani. Yayin da ta na alkawalin rai ga mai-biyayya, ta na bayana cewa mutuwa ce rabon mai-ketarewa. Bisharar Kristi ce kadai za ta iya kubutar da shi daga kazantarwar zunubi. Dole ya tuba ga Allah, wanda dokarsa ce na ketare; ga kuma bada gaskiya ga Kristi da hadayarsa ta kafara. Ta hakanan ya ke samun gafarar zunubai da suka wuce, ya kuma zama mai-yanayi irin na Allah. Sai yaron Allah ne, da shike ya karbi ruhun karbuwa ta yadda ya ke cewa: “Abba, Uba.”

Yanzu yana da ‘yanci ya ketare dokar Allah ke nan? Bulus ya ce: “Tawurin bangaskiya fa muna mai da shari’a wofi? Dadai! Ba haka ba, tabbatadda shari’a mu ke yi.” “Dadai! Mu da muka mutu ga zunubi, kaka za mu kara rayuwa a chiki?” Yohanna kuma ya ce: “Gama kamnar Allah ke nan, mu kiyaye dokokinsa: dokokinsa fa ba su da ban chiwo ba.” Romawa 3:31; 6:2; 1Yohanna 5:3. Chikin sabuwar haihuwar, ana kawo zuciya ga jituwa da Allah, yayin da ake sasanta ta da dokarsa. Sa’an da wannan babban canji ya faru cikin mai-zunubi, ya wuce daga zunubi zuwa cikin rai ke nan, daga zunubizuwa tsarki, daga ketare doka, da tawaye zuwa biyayya. Tsohuwar rayuwar rabuwa da Allah ta kare; sabuwar rayuwar sasantawa da bangaskiya da kauna ta fara. Sa’an nan “wajibin sharia” za “ya chika a wurinmu, mu wadanda ke tafiya ba bisa ga tabi’ar jiki ba, amma bisa ga ruhu.” Romawa 8:4. Sa’an nan maganar mutumin za ta zama: “Ina kamnar shari’arka ba misali! Abin tunawa ne a gareni dukan yini.” Zabura 119:97.

“Shari’a ta Ubangiji chikakkiya che, ta na mayas da rai.” Zabura 19:7. Idan ba doka mutane ba za su sami ganewar tsabta da tsarkin Allah ko ganewar laifinsu da rashin tsabtarsu ba. Ba su da ainihin sanin zunubi kuma ba sa jin bukatar tuba. Da shike ba sa ganin batawarsu na masu ketare dokar Allah, ba sa gane bukatarsu ta jinin kafara na Kristi. Ana karban begen ceto ba tare da sakewar zuciya ko rayuwa ba. Sabo da haka tuba mara zurfi ya yi yawa, kuma jama’a suna shiga ekklesiya alhali ba su taba haduwa da Kristi ba.

Koyaswoyin kuskure game da tsarkakewa da ke tasowa daga rabuwa da dokar Allah suna da tasiri mai yawa cikin ayukan addini na zamanin nan. Koyaswoyin nan karya ne, kuma sakamakonsu akwai hatsari sosai, kuma karbuwan da su ke samu ko ina ya sa ya zama wajibi ga kowa shi sami kyakyawar fahimtar abin da Littafin ke koyarwa game da wannan batun.

Ainihin tsakkakewa koyaswa ce ta Littafin. Manzo Bulus, cikin wasikarsa zuwa ga ekklesiyar Tasslunikawa ya ce: “Gama nufin Allah ke nan, tsarkakewar ku.” Sa’an nan ya yi addu’a cewa: “Allah kwa da kansa na salama, shi tsarkake ku sarai.” Tassalunikawa I,

4:3; 5:23. Littafin yana koyar da abin da ake nufi da tsarkakewa, a bayane da kuma yadda ake samunsa. Mai-ceton ya yi addu'a don almajiransa: "Ka tsarkake su chikin gaskiya: maganarka ita che gaskiya." Yohanna 17:17. Bulus kuma yana koyar da cewa masu-ba da gaskiya za a tsarkake su tawurin Ruhu Mai-tsarki: (Romawa 15:16). Mene ne aikin Ruhu Mai-tsarki? Yesu ya ce ma almajiran; "Amma sa'an da shi, Ruhu na gaskiya, ya tafo, za ya bishe ku chikin dukan gaskiya." Yohanna 16:13, Mai-zabura kuma ya ce: "shari'ar ka gaskiya ce." Ta wurin maganar Allah da Ruhunsa ne ake bude ma mutane muhimman kaidodin adalci da ke kunshe cikin dokarsa. Kuma da shike dokar Allah mai-tsarki ce, da adalci da nagarta, kuma hoton rashin aibin Allahtaka ne, ya nuna cewa halin da aka samu tawurin biyayya ga dokar zai zama hali mai-tsarki. Kristi cikakken kwatanci ne na irin wannan halin." Yace: "Na kiyaye dokokin Ubana." "Kullum ina aika abin da ya gamshe shi." Yohanna 15:10; 8:29. Ya kamata masu bin Kristi su zama kamarsa - tawurin alherin Allah su sami halaye da suka je daidai da kaidodin dokar sa mai-tsarki. Tsarkakewa bisa ga Littafin ke nan.

Za a iya aiwatar da aikin tawurin bangaskiya ga Kristi ne kadai, tawurin ikon Ruhun Allah a cikinmu. Bulus ya fadakar da masu ba da gaskiya cewa: "Ku yi aikin chetonku da tsoro da rawan jiki, gama Allah ne yana aiki a chikinku da za ku yi nufi har ku aika kuma, zuwa abinda ya gamshe shi." Filibiyawa 2:12,13. Kirista zai ji jarabar zunubi, amma zai yake shi kullum. Inda ake bukatar taimakon Kristi ke nan. Kumamacin mutuntaka yakan hadu da karfin Allahntaka, bangaskiya kuma ta kan ce: "Godiya ga Allah wanda ya ke ba mu nasara tawurin Ubangijinmu Yesu Kristi." Korinthiyawa I, 15:57.

Littafin yana nunawa a fili cewa aikin tsarkakewa ba na lokaci daya ba ne. Sa'anda a lokacin da ya tuba, mai-zunubi ya kan sami salama da Allah tawurin jinin kafarar, rayuwar Kiristancin ya fara ma ke nan kawai. Yanzu za ya ci gaba ne "zuwa chikakken mutum," ya girma "Zuwa misalin tsawon chikar Kristi." In ji Manzo Bulus: "Amma abu daya ni ke yi, ina manta abubuwan da ke baya, ina kutsawa zuwa wadanda ke gaba, ina nache bi har zuwa ga goni, ina kaiga ladan nasara na madaukakiyar kira ta Allah chikin Kristi Yesu." Filibiyawa 3:13,14. Bitrus kuma ya bayana mana matakan da tawurinsu ne ake samun tsarkakewa. Ya ce: "Sai ku kara ba da kokari, chikin bangaskiyarku kuma, ku kawo halin kirki; chikin halin kirki kuma ilimi; chikin ilimi kuma kamawa, chikin kamewa kuma hankuri, chikin son-yanuwa kuma kamna,… gama idan kun yi wadannan abu, ba za ku yi tuntube ba dadai." Bitrus II, 1:5-10.

Wadanda suka sami tsarkakewa bisa ga Littafin za su nuna ruhun tawali'u. Kamar Musa, sun hangi martabar tsarki mai ban tsoro, suna kuma ganin rashin cancantar kansu sabanin tsabta da mafificiyar cikar Allah mara iyaka.

Annabi Daniel kwatanci ne na tsarkakewa na kwarai. Rayuwarsa mai-tsawon nan ta cika da hidima ta kirki ga mai-gidansa. Shi "Kamnatache kwarai" ne (Daniel 10:11) na Allah. Duk da haka, cewa shi mai-tsarki ne mara-aibi kuma, annabin nan mai-tsarki ya

hada kansa da ainihin masu-zunubi na Israila ya yin da ya ke roko a gaban Allah a madadin mutanensa, ya ce: “Ba mu zuba maka godon mu sabili da adilchin kanmu ba, amma sabili da manyan jiyejiyenkanka.” “Mun yi zunubi, mun aika mugunta.” Ya ce kuma: “Ina nan ina chikin magana, ina addu’a, ina furta zunubi na da zunubin mutanena.” Kuma sa’anda daga baya Dan Allah ya bayana, domin ya ba shi umurni, Daniel ya ce: “Jamali na ya juya a chikina ya zama ruba, ba ni da ringin karfi.” Daniel 9:18, 15,20; 10:8.

Sa’anda Ayuba ya ji muryan Ubangiji daga cikin babban guguwa, ya ce: “Raina yana tagumi a chikina.” Ayuba 42:6. Sai lokacin da Ishaya ya ga darajar Ubangiji, ya kuma ji cherubim suna cewa “Mai-tsarki, Mai-tsarki ne, Ubangiji Mai-runduna” ne, ya ta da murya ya ce, “Kaitona! Gama na lalache.” Ishaya 6:3,5. Bulus bayan an fyauce shi zuwa sama ta uku ne, ya kuma ji ababan da bashi yiwuwa mutum shi furta, ya ce shi ne, “Koma bayan baya chikin tsarkaka duka.” Korinthiyawa II, 12:2-4, Afisawa 3:8. Yohanna kamnatacen nan da ya jingina a kirjin Yesu, ya ga darajarsa, shi ne ya fadi kamar matace a sawayen malaikan. Ruya 1:17.

Ba wani daukakan kai, babu fahariyar cewa an kubuta daga zunubi ga wadanda ke tafiya a inuwar giciyen Kalfari. Su kan san cewa zunubinsu ne ya jawo azabar da ta karya zuciyar Dan Allah, kuma wannan tunanin zai sa su rena kan su. Wadanda sun fi kusa da Yesu sun fi gane kumamanci da yawan zunubin ‘yan Adam, kuma begensu kadai shi ne adalcin mai-ceto wanda aka giciye ya kuma tashi.

Irin tsarkakewan da ke tashe a cikin addinin duniya yanzu yana tattare da ruhun girmama kai da rabuwa da dokar Allah, wanda ya nuna cewa tsarkakewan ya saba ma addini na Littafin. Masu wannan koyaswar suna koyar da cewa tsarkakewa abu ne na lokaci daya, farap daya, wanda tawurin bangaskiya kadai su ke samun cikakken tsarki. Su kan ce, “Kaba da gaskiya kawai, albarkar ta zama taka ke nan.” Wai ba a bidar wani kokari kuma daga wurin mai ba da gaskiyan.” A lokaci dayan kuma su na musun ikon dokar Allah, suna cewa wai an yantar da su daga takalifin kiyaye dokokin. Amma ko zai yiwu mutane su zama tsarkaka, bisa ga nufin Allah, da halinsa, ba tare da jituwa da kaidodin da ke bayana yanayinsa da nufinsa, suna kuma nuna bin da ke gamsar da shi ba?

Son addini mai-sauki wanda ba ya bukatar kokari, ko musun kai, ko rabuwa da wawutar duniya, ya mai da koyaswar bangaskiya da bangaskiya kadai ya zama koyaswa mai farinjini sosai, amma mene ne maganar Allah ke cewa? In ji manzo Yakub: “Yan’uwana, idan mutum ya che yana da bangaskiya, amma ba shi da ayuka, mi ya anfana? Ko wannan bangaskiya ta iya chetonsa?... Amma ko za ka sani ya mutumen wofi, bangaskiya ba tare da ayuka bakarariya che? Ko ba tawurin ayuka uban mu Ibrahim ya barata ba, yayinda ya mika Ishaku dansa bisa bagadi? Ka gani fa bangaskiya ta aika tare da ayukansa, ta wurin ayuka kuma bangaskiya ta chika,… Kun gani fa ta wurin ayuka mutum ya barata, ba ta wurin bangaskiya kadai ba.” Yakub 2:14-24.

Shaidar maganar Allah ba ta yarda da wannan koyaswa mai-kasada na bangaskiya ba tare da ayuka ba. Bangaskiya ba za ta sami karbuwar Allah ba, sai dai in ta cika sharuddan samun jinkai, in ba haka ba bangaskiyan nan ganganci ne, da shike ainihin bangaskiya yana da tushe a alkawura da tanade-tanaden Littafin ne.

Har kuma suna rudin kansu cewa za su iya zama masu-tsarki yayinda suke ketare daya daga cikin umurnin Allah da gangan. Aikata zunubi da gangan ya kan bice muryan Ruhu ya kuma raba mutum da Allah. “Zunubi shi ne ketaren shari’a,” Kuma “Dukan wanda yake aika zunubi (ketaren shari’a) ba ya taba ganinsa ba, ba ya sonshi kuma.” Yohanna I, 3:6. Ko da shike Yohanna cikin wasikunsa yana magana da yawa game da kauna, duk da haka bai yi jinkiri ba wajen bayana ainihin yanayin wadanda ke cewa an tsarkake su alhali suna rayuwar ketare dokar Allah. “Wanda ya che, Na san shi, amma ba ya kiyaye dokokinsa ba, makaryachi ne, gaskiya kwa ba ta chikinsa ba; amma wanda yana kiyaye maganarasa, a chikinsa lallai kamanr Allah ta chika.” 1Yohanna 2:4,5. Wannan shi ne ma’aunin da’awar kowane mutum. Ba za mu iya kiran wani ma-tsarki, ba tare da an auna shi da ma’auni mai-tsarkin nan daya kadai na Allah, a sama da duniya ba. Idan mutane ba sa jin nauyin dokar Allah; idan suka kankantadda da umurnin Allah suka wofinta shi, idan sun ketare daya daga mafi-kankantan dokokin nan, suka kuma koya ma mutane hakanan, za su zama marasa martaba a ganin Allah, za mu iya ganewa kuma cewa da’awansu ba su da tushe.

Kuma idan mutum ya ce bashi da zunubi kan shi ma wannan shaida ce cewa mutumin yana nesa da tsarki. Don ba shi da ainihin ganewar tsabta da tsarki mara matuka na Allah ne, ko kuma ganewar abin da ya wajibta masu son jituwa da halinsa su zama ne, domin mutumin fahimci ainihin tsabta da daukakar halin Yesu, da kuma tsananin muguntar zunubi ba ne, zai sa shi ya dauka cewa shi mai-tsarki ne. Yawan nisansa daga Kristi, da kuma yawan rashin ganewarsa na halin Allah da sharuddan sama suna daidai da yawan adalcinsa,.

Tsarkakewa da aka shimfida cikin Littafin ya kunshi mutum dungum din sa ne: ruhu da rai, da jiki. Bulus ya yi ma Tassalunikawa addu’a cewa “ruhunku da ran ku da jikinku su zama a kiyaye sarai, ba abin zargi lokachin zuwan Ubangijinmu Yesu Kristi.” Tassalunikawa I, 5:23, ya kuma rubuta ma masu bada gaskiya cewa: “Ina rokonku fa, yan’uwa bisa ga jiyejiyenkai na Allah, ku mika jikunanku hadaya mai-rai mai-tsarki, abin karba ga Allah, bautarku mai-ruhaniya ke nan.” Romawa 12:1. A zamanin Israila ta da, akan bincika kowane hadaya da aka kawo ma Allah, idan aka ga wani la’ani ko wata illa a jikin dabban, akan ki ta, domin Allah ya umurta cewa hadaya ta kasance mara aibi. Saboda haka ana umurta Kirista su mika jikunansu “hadaya mai-rai mai-tsarki abin karba ga Allah.” Domin yin wannan, dole su kiyaye kan su cikin yanayi mafi kyau. Duk wani abin da ke raunana karfin jiki ko karfin tunani ya kan hana mutum bautar mahalicinsa kuma ko Allah zai ji dadin wani abin da bai kai iyakar kokarinmu ba? Kristi ya ce: “Za ka kaunachi Ubangiji Allahnka da dukan zuchiyarka.” Wadanda ke kaunar Allah da dukan zuciya za su

so su ba shi hidima mafi kyau na rayuwarsu, kuma za su yi ta kokarin yin anfani da kowane yanayinsu ga jituwa da dokokin da za su taimaka masu iya yin nufinsa, ba za su raunana ko su kazantar da hadayan da za su mika ma Uban su na sama ta wurin kwadayi ko yawan son dadi ba.

Bitrus yace: “Ku hanu daga sha’awoyi na jiki wadanda ke yaki da rai.” Bitrus I, 2:11. Kowane zunubi da aka yi ya kan kangarar da tunani ya kashe ganewa na ruhaniya, kuma maganar Allah ko Ruhunsa ba za su yi tasiri sosai ga zuciyar ba. Bulus ya ce ma Korinthiyawa: “Bari mu tsarkake kanmu daga dukan kazamtar jiki da ta ruhu, muna kamala tsarki chikin tsoron Allah. Korinthiyawa II, 7:1. Kuma tare da diyan Ruhun — “Kamna (ne), farinchiki, salama, tsawon jimrewa, nasiha, nagarta, aminchi, tawali’u,” ya hada “kamewa” Galatiyawa 5:22,23.

Duk da hurarrun nassosin nan, dubi yawan Kirista da ke nakasa kan su cikin neman arziki ko bautar salo ko yayi, dubi yawan masu rage darajar mazantakansu irin na ibada, ta wurin zarin ci da shan giya, da haramtaceyar anishuwa. Kuma ekklesiya, maimakon tsawatarwa, sau da yawa ta kan karfafa muguntar, ta wurin anfani da kwadayi da son riba ko son jin dadi don nema ma baitulamalinta kurdi, maimakon yin anfani da kaunar Kristi. Da Yesu zai shiga ekklesiyoyi na yau ya ga bukukuwa da hidimomi marasa tsarki da ake yi a ciki da sunan addini, ko ba zai kori masu kazantarwan nan yadda ya kori masu canjin kurdi da haikalin ba?

Manzo Yakub ya ce hikima daga sama, “da fari dai mai-tsarki ne.” Da ya sadu da wadanda ke rike da sunan Yesu a lebuna, kazamtattu da taba da ta bata lumfashinsu, da jikunansu masu wari, suna kuma bata iskar sama, suna tilasta na kusa da su shaker gubar - da manzon ya sadu da halin nan da ke sabani da tsabtar bishara, ashe da bai ce halin nan na yan duniya ne, na rashin imani, halin iblisanci ba? Bayin taba ma su cewa an tsarkake su sarai, suna zancen begensu na zuwa sama, amma maganar Allah tana bayana cewa “ba kwa wani abu mara tsarki da za ya shiga ko kadan.” Ruya 21:27.

“Ko ba ku sani ba jikinku haikali ne na Ruhu Mai-tsarki wanda ke chikinku, wanda kun karba daga wurin Allah? Ku kwa ba na kan ku ba ne; gama aka saye ku da tamani; ku daukaka Allah fa chikin jikinku.” Korinthiyawa I, 6:19,20. Shi wanda jikinsa haikali ne na Ruhu Mai-tsarki ba zai zama bawan wani halin banza ba. Lafiyarsa ta Kristi ce, wanda ya saye shi da farashin jini. Dukiyarsa ta Ubangiji ce. Ta yaya zai kubuta daga laifi idan ya watsar da wannan jarin da aka ba shi amana? Kirista kowace shekara su na kashe kurdi mai-yawa wajen ababa marasa anfani, alhali rayuka suna hallaka saboda maganar rai. Ana yi ma Allah kwace wajen zakkoki da sadakoki, yayin da su ke kashe dukiya wajen biyan kwadayin jikunansu fiye da abinda su ke bayarwa don taimaka ma matalauta ko bishara. Da dukan masu cewa suna bin Kristi tsarkakakku ne, da maimakon kashe dukiyarsu akan jin dadi mara anfani ko mai cutarwa ma za su sa ta cikin baitulmalin Ubangiji, Kirista kuma

da sun kafa kwatancin kamewa, da musun-kai, da sadakar da kai. Sa'an nan ne za su zama hasken duniya.

Duniya ta nutse cikin son jin dadi. "Sha'awa ta jiki, da sha'awa ta ido," da fahariyar rai suna mallakar yawancin mutane. Amma masu-bin Kristi suna da kira mafi tsarki. "Ku fito daga chikinsu, ku ware, in ji Ubangiji, kada ku taba kowane abu mara-tsarki." Bisa ga maganar Allah muna da 'yanci mu ce tsarkakewa ba za ta kasance sahihiya ba, idan ba ta haifar da rabuwa da ayukan zunubi da sha'awoyin duniya ba.

Ga wadanda suka cika sharuddan nan, "Ku fito daga chikinsu ku ware,… kada ku taba kowane abu mara-tsarki," alkawalin Allah shi ne: "Ni ma in karbe ku, in zama Uba gareku, ku za ku zama 'ya'ya maza da mata gareni, in ji Ubangiji Mai-iko duka." Korinthiyawa II, 6:17,18. Zarafi da takalifin kowane Kirista ne ya sami mawadacin dandano mai-yawa cikin al'ammuran Allah. Yesu Ya ce: "Ni ne hasken duniya; wanda yana biyona ba za shi yi tafiya chikin dufu ba, amma za ya sami hasken rai." Yohanna 12:8. "Amma tafarkin mai-adilchi yana kama da hasken ketowar alfijir, wanda ya ke haskakawa gaba gaba har zuwa chikakkiyar rana." Misalai 4:18. Kowane matakin bangaskiya da biyayya yana kawo mutum zuwa dangantaka na kusa kusa da hasken duniya, wanda babu duhu a cikinsa ko kadan. Tsirkiyoyin hasken Ranar Adilchi suna haskaka bayin Allah, su kuma ya kamata su bayana tsirkiyoyin na sa. Kamar yadda taurari su ke fada mana cewa akwai babban haske a sama wanda darajarsa ce ta ke sa su haskakawa, hakanan ne ya kamata Kirista su sa a gane sarai cewa akwai Allah a bisa kursiyin dukan halitta wanda halin sa ya isa yabo da kwaikwayawa. Albarkun Ruhunsa, da tsarki da tsabtar halinsa za su bayana cikin shaidunsa.

Bulus cikin wasikarsa zuwa ga Kolosiyawa ya bayana manyan albarkun da ake ba 'ya'yan Allah. Ya ce: "Ba mu fasa yin addu'a da roko dominku ba, ku chika da sanin nufinsa chikin dukan hikima mai-ruhaniya da fahimi kuma, da za ku yi tafiya wadda ta chanchanta ga Ubangiji, kuna gamshe shi sarai, kuna ba da yaya chikin kowane kyakkyawan aiki, kuna karuwa kuma chikin sanin Allah; karfaffafu da dukan iko, bisa ga ikon daukakarsa, zuwa dukan hankuri da jimrewa tare da farinchiki." Kolosiyawa 1:9-11.

Ya kuma rubuta game da fatarsa cewa 'yan-uwa da ke Afisus su fahimci girman gatancin Kirista. Ya bayana masu iko da sani na ban mamaki da za su iya samu kamar 'ya'yan Madaukaki. Gatarsu ce "a karfafa (su) da iko tawurin Ruhunsa chikin mutum na chiki," su zama "dasassu ne kafaffu kuma chikin kamna," su "ruska tare da dukan tsarkaka, ko minene fadin da ratar da tsawon da zurfin kamnar Kristi, ku sani kuma kamnar Kristi wadda ta wuce gaban a san ta." Amma addu'ar manzon ta kai makurar gatar, inda ya yi addu'a cewa: "domin ku chika har zuwa dukan chikar Allah." Afisawa 3:16-19.

Nan an bayana girman matsayin da za mu iya kaiwa ta wurin bangaskiya cikin alkawuran Ubanmu na sama, sa'an da mun cika sharuddansa. Ta wurin cancantar Kristi,

muna da hanyar zuwa kursiyin iko Mara-iyaka. “Wanda baya kebe Da na sa ba, amma ya bashe shi domin mu duka, kaka za ya rasa ba mu abu duka kuma tare da shi a yalwache?” Romawa 8:32. Uban Ya bada Ruhunsa ga Dansa a yalwace, mu ma kuma za mu iya samun moriyar cikar Ruhun. Yesu ya ce: “Idan ku fa da kuke miyagu kun san yadda za ku ba yayanku alherai, balle fa Ubanku na sama za ya bada Ruhu Mai-tsarki ga wadanda su ke rokonsa?” Luka 11:13. “Idan kun roke ni komi a chikin sunana, ni yi wannan.” “Ku yi roko, za ku karba, domin farinchikinku ya chika.” Yohanna 14:14; 16:24.

Yayin da rayuwar Kirista za ta kasance ta tawali’u, bai kamata ta cika da bakinciki ba. Gatancin kowa ne ya yi rayuwa ta yadda Allah zai gamsu, Ya kuma yi masa albarka. Ba nufin Ubanmu na sama ne mu taba kasancewa kalkashin hukumci da duhu ba. Ba shaidar tawli’u idan ana tafiya da kai a sunkuye amma zuciya cike da tunanin son kanmu. Za mu iya zuwa wurin Yesu a tsarkake mu, mu kuwa tsaya gaban shari’a, ba kunya ko nadama. “Babu hukumci fa yanzu ga wadanda ke cikin Kristi Yesu, wadanda ke tafiya, ba bisa jiki ba, amma bisa ga Ruhu.” Romawa 8:1.

Tawurin Yesu, fadaddun ‘ya’yan Adamu suna zama ‘ya’yan Allah. “Gama shi mai-tsarkakewa da su wadanda aka tsarkake su duk daga mafari daya ne; domin wannan fa a gare shi ba wani abin kunya ba ne shi che da su yan’uwa.” Ibraniyawa 2:11. Ya kamata rayuwar Kirista ta zama ta bangaskiya, ta nasara, da murna cikin Allah. “Gama kowane haifaffe daga wurin Allah yana yin nasara da duniya; nasara wadda ta chi duniya ke nan, bangaskiyarmu.” 1Yohanna 5:4. Nehemiah bawan Allah ya ce: “Farinchiki na Ubangiji shi ne karfinku.” Nehemiah 8:10. Bulus kuma ya ce: “Ku yi farinchiki chikin Ubangiji kullayomi; sai in sake chewa, ku yi farinchiki.” “Ku yi murna kullum; ku yi addu’a ba fasawa; chikin kowane abu a ba da godiya; gama shi ne nufin Allah gareku chikin Kristi Yesu.” Filibiyawa 4:4; 1Tassalunikwa 5:16-18.

Irin ‘ya’yan tuba da tsarkakewa irin na Littafin ke nan; kuma don Kirista suna daukan muhimman kaidodin adalci da aka bayana cikin dokar Allah da rashin kulawa ne ya sa ba a cika ganin ‘ya’yan nan na tuba da tsarkakewa ba. Shi ya sa aikin nan mai-zurfi na Ruhun Allah da ya rika samuwa wajen falkaswa na shekarun da bai cika ganuwa sosai ba yanzu.

Tawurin dubawa muke sakewa. Kuma sa’anda ake rabuwa da umurnin nan masu-tsarki inda Allah ya bude ma mutane cika da tsarkin halinsa, zukatan mutane kuma suna jawuwa zuwa koyaswoyi da ra’ayoyin mutane, ba abin mamaki ba ne aka iske raguwar ainihin ibada cikin ekklesiya. Ubangiji ya ce: “Sun yashe ni, ni mabulbular ruwaye masu rai, sun gina ma kansu runduna hadaddu, wadanda ba su rike ruwa ba.” Irmiya 2:13.

“Mai-albarka ne mutum wanda ba ya bi ta shawarar miyagu ba,… Amma marmarinsa chikin shari’a ta Ubangiji yake, kuma a chikin shari’assa yakan rika tunani dare da rana. Za ya zamna kamar itachen da aka dasa a magudanar ruwaye wanda yana ba da yayansa a chikin kwanakinsa; ganyensa ba ya yi yaushi ba, kuma chikin iyakar abinda yake yi za shi

yi albarka.” Zabura 1:1-3. Sai an mayas da dokar Allah ga ainihin matsayinsa ne za a iya samun falkaswar bangaskiya da ibada na da cikin mutanensa. In ji Ubangiji, “Ku tsaya a chikin hanya sosai, ku gani, ku tambayi hanyoyi na da inda hanyar kirki ta ke, ku yi tafiya a chiki, za ku sami hutawa domin rayukanku.” Irmiya 6:16.

Babi na 28—Fuskantar Rahoton Rayuwa

Annabi Daniel yace: “Ina nan ina dubawa, har na ga an kafa kursiyai, wani kuma wanda shi ke Mai-zamanin da yana zamne: tufafinsa fari fat kamar snow suke: gashin kansa kuma kamar tsatsabtar ulu, kursiyinsa harsunan wuta ne mai-chi. Rafi mai-kamar wuta ya tasa ya fito kuma daga gabansa: dubban dubbai kuma sun a yi masa hidima; zambar goma kuma so zambar goma suna tsaye a gabansa; aka kafa shari’a aka bude littattafai.” Daniel 7:9,10.

Haka aka bayana ma annabin babban ranan nan mai-saduda da halayen mutane da rayuwarsu za su gurbana a gaban mai-shari’an dukan duniya, za a kuma ba kowane mutum gwalgwadon ayukansa. Mai-zamanin Da Allah Uba ne. Mai-zabura ya ce: “Tun ba a bullo da duwatsu, tun ba ka ko sifanta kasa da duniya, tun fil’azal kai ne Allah har abda.” Zabura 90:2. Shi tushen dukan kowane abu, mabulbulan kowace doka, Shi ne zai zama shugaban shari’ar. Malaiku masu tsarki kuma a matsayin ‘yan hidima da shaidu, da yawan su ya kai dubban dubbai da zambar goma so zambar goma, za su halarci zaman shari’ar.

“Ga shi tare da gizagizan sama wani ya zo mai-kama da dan mutum ya zo kuma, har wurin mai-zamanun da, aka kawo shi a gabansa har ya yi kusa. Aka ba shi sarauta da daraja, da mulki, domin dukan al’ummai, da dangogi, da harsuna su bauta masa; sarautassa madauwamiya che, wadda ba za ta shude ba.” Daniel 7:13,14. Zuwan Kristi da a ke magana a kai a nan ba zuwansa na biyu a duniya ba ne. Zai zo wurin mai-zamanin Da a sama ne domin shi karbi sarauta da mulki, wanda za a ba shi a karshen aikin sa na matsakanci. Wannan zuwan ne, ba zuwan sa na biyu a duniya ba da annabci ya ambata cewa zai faru a karshen kwane 2300 din nan a 1844. Tare da malaiku na sama, babban priest na mu zai shiga wuri mafi tsarki inda za ya bayana a gaban Allah domin shi yi aikin shari’a ta bincike ya kuma yi kafara domin dukan wadanda suka cancanci kafara.

A hidima ta misalin, wadanda suka zo gaban Allah da tuba da furta zunubi ne kadai wadanda aka gafarta zunuban su. Ta wurin jinin hadaya ta zunubi wanda aka yayafa a haikalin ne sukan shiga hidimar Ranar kafara. Hakanan a baban ranan nan na kafara ta karshe da shari’a ta bincike al’amuran da za a bincika na wadanda ke cewa su mutanen Allah ne kadai. “Shari’a za ta faru a kan gidan Allah; idan kwa a wajenmu ta faru, ina matukar wadanda basu bi bisharar Allah ba?” 1Bitrus 4:17.

Littattafan da ke sama, inda a ke, rubuta sunaye da ayukan mutane, su ne za su nuna hukumcin da shari’ar ta yanka. Annabi Daniel ya ce: “An bude wani littafi kuma, littafin rai ke nan: aka yi ma matattu shari’a kuma bisa ga abinda aka rubuta chikin litattafai, gwalgwadon ayukan su.” Ruya 20:12.

Littafin rai ya kunshi sunayen dukan wadanda su ka taba shiga bautar Allah, Yesu ya ce ma almajiransa: “Ku yi murna saboda an rubuta sunayenku chikin sama.” Luka 10:20.

Bulus yana magana game da amintattun abokan aikinsa “wadanda sunayensu ke chikin littafin rai.” Filibbiyawa 4:3. Daniel yayin da yake kallon “kwanakin wahala irin da ba a taba yi ba” ya ce za a ceci mutanen Allah, “kowane daya wanda aka iske shi a rubuche chikin littafin.” Mai-ruyan kuma ya ce wadanda “an rubuta su chikin litafin rai na Dan rago” ne kadai za su shiga birnin Allah. Daniel 12:1; Ruya 21:27.

Akwai littafin tunawa da aka rubuta a gaban Allah, inda aka rubuta, kyawawan ayukan “wadanda su ke jin tsoron Ubangiji, masu tunawa da sunansa.” Malachi 3:16. Kalmomin su na bangaskiya, ayukan su na kauna, suna rubuce a sama. Nehemiah ya yi magana game da wannan sa’an da ya ce: “Ka tuna da ni, ya Allahna,… kada kwa ka shafe aikin nagarta da na yi sabili da gidan Allahna.” Nehemiah 13:14. A chikin littafin tunawa na Allah ana rubuta kowane aikin nagarta. A cikinsa, kowace jaraba da aka yi nasara a kai, kowace mugunta da aka yi nasara da ita, kowace kalmar tausayi da aka furta, suna nan a rubuce, ba kuskure. Kuma kwane aikin sadakarwa, kowace wahala da bakinciki da aka jimre saboda Kristi yana nan a rubuce. Mai-zabura ya ce: “Kana lissafin yawache-yawachena; ka sa hawayena chikin garanka; ba a chikin litafinka su ke ba? Zabura 56:8.

Ana kuma rubuta zunuban mutane. “Gama Allah za ya kawo kowane aiki wurin shari’a, da dukan aisirin rai, domin shi raba, ko nagari ne, ko mugu.” “Kowace maganar banza da mutane ke fadi, a chikin ranar shari’a za su ba da lissafinta.” Mai-ceton ya ce: “Bisa ga zantattukanka za ka barata, bisa ga zantattukanka kuma za a kashe ka.” Mai-wa’azi 12:14; Matta 12:36,37. Tunani da manufofi da ke cikin zuciya ma suna cikin rajista; gama Allah “za ya tone boyayyun al’amura na dufu, ya bubbude shawarwarin zukata a sarari.” Korinthiyawa I, 4:5. “Ga shi, a gabana yake a rubuche:… naku laifofi da laifofin ubanninku tare, in ji Ubangiji.” Ishaya 65:6,7.

Aikin kowane mutum yana wucewa a gaban Allah mai-bincikewa kuma yana rubuce, ko aminci ne ko rashin aminci. A gefen kowace suna a litattafan sama ana rubuta kowace kalma mara dacewa, kowane aikin son kai, kowane aikin da aka ki yi, da kowane zunubi na boye. Ana rubuta kowace fadaka daga sama da aka kyale, lokaci da aka bata, zarafi da aka ki anfani da shi, tasiri da aka yi anfani da shi don alheri, ko mugnta, da dukan sakamakonsa, dukansu malaika yana rubutawa.

Dokar Allah ce ma’aunin da za a yi anfani da ita don auna halaye da rayuwar mutane lokacin shari’a. Mai-hikima ya ce: “Ji tsoron Allah, ka kiyaye dokokinsa; gama Allah za ya kawo kowane aiki wurin shari’a.” Mai-wa’azi 12:13.14. Manzo Yakub ya gargadi yan-uwansa: “Haka za ku yi Magana, haka za ku aika kuma, kamar mutane wadanda za a yi masu shari’a bisa ga shari’a ta yanchi.” Yakub 2:12.

Wadanda a lokacin shari’a aka iske sun cancanta za su kasance cikin masu tashin adilai. Yesu ya ce: “Amma su wadanda an maishe su sun isa su kai wanchan zamani da tashi kuma daga matattu,… sun zama daidai da malaiku; yayan Allah su ke kwa, da shi ke

yayan tashin matattu ne.” Luka 20:35,36. Ya kuma ce: “Wadanda sun yi nagarta za su fito zuwa tashi na rai.” Yohanna 5:29. Ba za a ta da matattun masu adalci ba sai bayan shari’a inda za a hukunta cewa sun isa tashi na rai. Sabo da haka ba za su kasance a wurin shari’an da kansu ba yayin da ake bincika halayensu daga litattafan, ana kuma hukumta su.

Yesu za ya bayyana a matayin lauyansu, domin Ya yi roko a madadinsu a gaban Allah. “Idan kowa ya yi zunubi, muna da mai-taimako wurin Uba, Yesu Kristi mai-adalchi.” 1Yohanna 2:1. “Gama Kristi ba ya shiga chikin wani wuri mai-tsarki wanda aka yi da hannuwa ba, mai-kama da gaskiya ga zanchen fasali, amma chikin sama kanta, shi bayana a gaban fuskar Allah sabili da mu yanzu.” “Domin wannan kwa yana da iko ya yiwo cheto ba iyaka domin wadanda ke kusantuwa ga Allah ta wurinsa, da shike kullum a raye yake domin yin roko sabili da su.” Ibraniyawa 9:24; 7:25.

Sa’anda an bude littattafan a lokacin shari’a rayuwan dukan wadanda suka ba da gaskiya ga Yesu zai zo gaban Allah domin bincike. Kuma daga wadanda suka fara rayuwa a duniya Mai-taimakonmu zai gabatar da maganar kowace sara bi da bi, zai kuma karasa da masu-rai. Zai ambaci kowane suna, a bincika kowace magana, da kyau. Za a karbi sunaye, za a ki sunaye kuma. Wadanda su ke da zunuban a littafin, wadanda ba su tuba sun bari an kuma gafarta ba, za a share sunayensu daga littafin rai, kuma za a share rubutattun nagargarun ayukansu daga littafin tunawa na Allah. Allah ya ce ma Musa: “Wanda ya yi zunubi gareni duka, shi ne zan shafe daga chikin litafina.” Fitowa 32:33. Annabi Ezekiel kuma ya ce: “Amma lokachin da adili ya juya ga barin adilchinsa, ya yi ta aikin mugunta,… ba za a tuna da ayukansa na adilchi da ya yi ko daya ba.” Ezekiel 18:24.

Dukan wadanda sun tuba da gaske daga zunubi, tawurin bangaskiya kuma suka amshi jinin Kristi ya zama hadayar kafararsu, an rubuta yafewa a sunansu a cikin litattafan sama, da shike sun zama masu cin moriyar adalcin Kristi, an kuma iske halayyansu sun je daidai da dokar Allah, za a shafe zunubansu, su kansu kuma za a ga sun isa samun rai na har abada. Ubangiji ta bakin annabi Ishaya Ya ce: “Ni, i, ni ne na shafe laifofinka sabili da kaina; ba ni kwa kara tuna da zunubanka ba.” Ishaya 43:25. Yesu ya ce: “wanda ya yi nasara za a yafa shi hakanan da fararen tufafi; ba ni kwa shafe sunansa daga chikin litafin rai ba dadai, zan kuma shaida sunansa a gaban Ubana, da gaban malaikunsa.” “Ko wanene fa da za ya shaida ni a gaban mutane, shi zan shaida a gaban Ubana wanda ke chikin sama kuma. Amma dukan wanda za ya yi musun sani na a gaban mutane, shi zan yi musunsa a gaban Ubana wanda ke chikin sama kuma.” Ruya 3:5; Matta 10:32,33.

Hankali mafi-zurfi da mutane kan ba hukumcin kotunan duniya dan kankanin alama ne na hankalin da kotunan sama za su jawo sa’anda sunayen da aka rubuta a littafin rai za su bayana gaban mai-shari’an duniya domin bincike. Matsakancin yana roko cewa a gafarta zunuban dukan wadanda su ka yi nasara ta wurin bangaskiya cikin jininsa, a mayas da su gidansu na Adnin, a kuma daura masu rawanin sarauta tare da shi. Mikah 4:8. Shaitan cikin kokarinsa na rudin ‘yan Adam da jarabtarsu ya so ya lalata shirin Allah don halitar mutum;

amma yanzu Kristi yana roko cewa a aiwatar da shirin kamar mutum bai taba faduwa ba. Yana roko ma mutanensa yafewa da barataswa cikakku, da rabo cikin darajarsa da kujera a kursiyinsa kuma.

Yayinda Yesu yake roko domin mutanensa, Shaitan yana zarginsu a gaban Allah cewa masu ketare doka ne su. Mai-rudun ya so ya ja su zuwa shakka, ya sa su dena amincewa da Allah, su raba kansu da kaunarsa, su kuma ketare dokarsa. Yanzu kuma yana nuna rayuwan da su ka yi da aibin halayensu, da rashin kamaninsu da Kristi, wanda ya rage darajar mai-fansarsu, da dukan zunuban da ya jarabce su su ka aikata, saboda wadannan kuma yana cewa su bayinsa ne.

Yesu bai bada hujja domin zunubansu ba, amma yana nuna hakurinsu da bangaskiyarsu, kuma yana rokon gafara dominsu, yana nuna ma Uban da malaiku masu-tsarki hannuwansa da aka huda, yana cewa; na san su da sunayensu. Na rubuta su a tafin hannuwana. “Hadayu na Allah karyayyen ruhu ne; karyayyar zuchiya mai-tuba ba za ka rena ta ba, ya Allah.” Zabura 51:17. Ga mai-zargin mutanensa kuma ya ce: “Ubangiji shi tsauta maka, ya Shaitan, i, Ubangiji wanda ya zabi Urushalima shi tsauta maka; wannan ba konannen itace ba ne da aka chiro daga chikin wuta?” Zakariya3:2. Kristi zai suturta zabbabunsa da adalchin kansa, domin ya gabatar da su ga Ubansa “ekklesiya mai-daraja, ba tare da aibi ko chira ko kowane abu misalin wadannan.” Afisawa 5:27. Sunayensu suna rubuce cikin littafi na rai, game da su kuma an ce: “Za su yi tafiya tare da ni a yafe da fari; gama sun isa.” Ruya 3:4.

Ta haka ne za a tabbatar da cikawar sabon alkawalin nan: “Zan gafarta muguntassu, bani kwa kara tuna da zunubinsu ba.” “A chikin wadannan kwanaki, a loton nan kuma, in ji Ubangiji, za a nemi a ga laifin Israila, a rasa; za a nemi a ga zunubban Yahuda, ba za a iske ba.” Irmiya 31:34; 50:20. “A chikin ranan nan dashe na Ubangiji za ya yi jamali ya yi daraja, anfanin kasa kuma za ya kasanche kyakyawa mai-ado domin wadanda su ke tsira na chikin Israila. Za ya zama kuma shi wanda ya rage chikin Sihiyona, da shi wanda ya wanzu chikin Urushalima, za a che da shi mai-tsarki, watau kowane dayan da aka rubuta shi chikin masu-rai na Urushalima.” Ishaya 4:2,3.

Aikin shari’a ta bincike da shafewar zunuban nan za a kamala shi kafin zuwan Ubangiji na biyu. Da shike za a sharanta matattu daga ababan da aka rubuta cikin litattafan ne, ba zai yiwu a shafe zunuban mutane ba sai bayan shari’ar, inda za a bincika rayuwarsu. Amma manzo Bitrus ya fada a fili cewa za a shafe zunuban masu ba da gaskiya “domin hakanan wokatan wartsakewa daga wurin Ubangiji su zo; domin kuma shi aiko Kristi.” Ayukan 3:19,20. Sa’an da shari’ar binciken ta kare, Kristi za ya zo, ladarsa kuma tana tare da shi da zai ba kowa gwalgwadon ayukansa.

A hidima ta kwatanci, babban priest, bayan ya yi kafara domin Israila, yakan fito ya albarkaci jama’a. Hakanan Kristi a karshen aikinsa na Matsakanci, za ya bayana kuma, ban

da zunubi, zuwa ceto (Ibraniyawa 9:28), domin Ya alabrkaci mutanensa da ke jira, da rai madawami. Kamar yadda priest yayin da yake cire zunubai daga haikalin yakan furta su a bisa kan bunsurun Azazel, hakanan Kristi zai jibga dukan zunuban nan a kan Shaitan tushen zunubi, mai-ingizawa a aikata shi kuma. A kan kai bunsurun Azazel, dauke da zunuban Israila, can cikin wata kasa inda babu kowa ne (Levitikus 16:22), hakanan Shaitan, dauke da laifin dukan zunuban da shi ya sa mutanen Allah su ka yi, za a kange shi har shekaru dubu a duniyan nan, wadda a lokacin kango ne, babu kowa a ciki, a karshe kuma zai sha cikakken horon zunubi cikin wutan da zai hallaka dukan miyagu. Ta hakanan babban shirin nan na fansa zai cika sa'anda aka kawar da zunubi aka kuma kubutar da dukan wadanda suka kasance a shirye su rabu da mugunta.

A lokacin da aka shirya domin hukuncin-karshen kwana 2300 din a 1844 aikin bincike da shafawar zunubai ya fara. Dukan wadanda suka taba dauka ma kansu sunan Kristi dole za a bincika su sosai. Za a hukunta mattattu da masu rai daga ababan da aka rubuta a cikin littattafan, bisa ga ayukansu.

Zunjuban da ba a tuba daga gare su aka rabu da su ba, ba za a yafe a kuma shafe su daga litattafan ba, amma za su zama shaida akan mai-zunubin a rana ta Allah. Ko da hasken rana ne, ko cikin duhun dare ne ya aikata, muggan ayukansa, a bayane suke a gaban mai-shari'an. Malaikun Allah sun shaida kowane zunubi, sun ka kuma rubuta shi ba kuskure. Ana iya boye zunubi, a rufe shi, a yi musun shi a luluba shi daga sanin uba ko kuwa mata, da yara, da abokai, watakila mai-zunubin ne kadai ya san ya aikata, amma a bayane yake a gaban mazamnan sama. Duhun dare, da sirrin kowace dabarar rudu, basu isa su lulluba ko tunani daya ba daga wurin Allah. Allah yana da cikakken rahoton kowane rashin adalci da kowane rashin gaskiya. Kamanin ibada ba ya rudinsa. Ba Ya kuskuren sansance halin mutum. Masu mugunta a zuciya za su iya rudin wadansu, amma Allah yana zarce kowane rudu Ya karanta rayuwa ta cikin mutum.

Wannan abin tsoro ne. Kowace rana tana da rahoton ta a littattafan sama. Kalmomin da aka taba fadi, ayukan da aka taba aikatawa, ba za a iya janye su ba. Malaiku sun yi rajistan nagarta da mugunta duka. Mayaki mafi shahara a duniya ba zai iya janye rahoto ko na rana daya ba. Ayukanmu da kalmominmu, har ma da manufofin zukatanmu suna da anfaninsu game da sansance matsayinmu, ko mai-kyau ko mara kyau.

Ko da mu mun manta ma za a yi anfani da su don kubutarwa ko hukuntawa. Halin kowa yana bayane a sarari da aminci cikin littattafan sama. Duk da haka ba a cika kula rahoton nan da mazamana sama za su duba ba. In da za a cire labulen da ke raba abinda ake gani da wanda ba a gani a duniyan nan, 'yan Adam kuma su ga malaika yana rubuta kowace kalma da al'amari da dole za su sake saduwa da su a lokacin shari'a, da ba a furta wadansu kalmomin, da kuma ba a aikata wadansu ayukan.

A lokacin shari'ar za a bincika anfanin da ake yi da kowane talent, yaya mu ka yi anfani da jarin da Allah Ya ba mu rance? Ko mun kyautata kwarewan da aka ba mu amana ta hannu da zuciya da kwakwalwa domin daukakar Allah da alabrka ga duniya? Yaya mu ka yi anfani da lokacinmu da alkalaminmu, da muryarmu, da kurdinmu, da tasirinmu? Me mu ka yi ma Kristi, a matsayin matalauci da wahalalle da maraya da gwamruwa? Allah Ya mai da mu masu rikon maganarsa mai-tsarki, me muka yi da haske da kuma gaskiyan da aka ba mu domin mu sa mutane su zama da hikima zuwa ceto? Furcin cewa muna da bangaskiya cikin Kristi kawai ba shi da wani anfani, kaunan da ake nunawa tawurin ayuka ne kadai ke da anfani. Duk da haka kauna ce kadai ke sa ayuka su zama da anfani a ganin Allah. Duk abinda aka yi saboda kauna, komi kankantansa a ganin mutane, Allah ya kan karba Ya ba da ladansa.

Boyayyen son kan mutane yana bayane a litattafan sama, a ciki ma an rubuta ababan da ya kamata a yi ma mutane amma ba a yi ba, da ababan da Mai-ceto Ya ce a yi amma aka manta. Can kuma za a ga yadda sau da yawa aka ba Shaitan lokaci da tunani da karfin da ya kamata a yi anfani da su domin Yesu. Abin bakinciki ne rahoton malaikun nan a sama. Masu tunani, masu cewa suna bin Kristi, sun dukufa neman kayan duniya ko jin dadin duniya. Ana kashe kurdi da lokaci da karfi domin jin dadi, da nuna isa; amma lokaci kadan a ke anfani da shi don addu'a da binciken Littafin da kaskantar da kai da furta zunubi.

Shaitan yana kirkiro dabaru da yawa don mallakar tunaninmu, domin kada mu yi binbinin aikin da ya kamata mu fi saninnsa. Ya ki jinin muhimman gaskiya da ke bayana hadaya ta kafara da matsakanci mai-cikakken iko. Ya san cewa a gareshi wajibi ne ya kawar da tunanin mutane daga Yesu da gaskiyarsa.

Wadanda ke so su mori anfanin tsakonin mai-ceton, kada su bar wani abu ya tsoma baki cikin kokarin su na cikakken tsarki a tsoron Allah. Maimakon bata lokaci wajen jin dadi da nuna isa da neman abin duniya, sai a yi anfani da lokacin don naciya wajen addu'a da nazarin maganar gaskiya. Ya kamata mutanen Allah su fahimci batun haikali da shari'a ta bincike da kyau. Kowa yana bukatar sanin matsayi da aikin Babban priest dinsa. In ba haka ba, ba zai yiwu masu su yi bangaskiyar da ya wajibta a wannan lokaci ko kuma su dauki matsayin da Allah ya shirya masu su dauka ba. Kowane mutum akwai rai da zai kawo ga ceto ko kuma ya batar. Kowa yana da shari'a a gaban Allah. Dole kowa ya fuskanci babban Mai-shari'an fuska da fuska. Don haka wajibi ne kowa ya dinga bimbinin lokacin nan da za a fara shari'ar a kuma bude litattafai, sa'anda tare da Daniel, dole kowane mutum shi tsaya a cikin rabonsa a karshen kwanaki.

Dukan wadanda sun sami haske game da batutuwan nan ya kamata su shaida gaskiyan da Allah Ya ba su. Haikali na sama shi ne cibiyar aikin Kristi a madadin mutane. Ya shafi kowane mai-rai da ke duniya, yana bayana shirin fansa, ya kawo mu har karshen lokaci, yana bayana batun nasaran nan game da jayayya tsakanin adalci da zunubi. Wajibi ne kowa

ya bincika ababan nan da kyau ya kuma iya ba da amsa ga duk wanda ya tambaye su dalilin begen da ke cikinsu.

Shiga tsakanin da Kristi ke yi a madadin mutum a haikalin sama wajibi ne ga shirin ceto daidai da mutuwarsa a kan giciye. Ta wurin mutuwarsa ya fara aikin nan da bayan tashinsa ya koma sama domin ya karasa. Dole ta wurin bangaskiya mu shiga bayan labulen, “inda Yesu kamar shugaba ya shiga dominmu” Ibraniyawa 6:20. Can ne haske daga Kalfari ke haskakawa. Can ne za mu sami karin haske game da asiran fansa. An aiwatar da ceton mutum da tamani mai-tsada mara matuka ga sama, hadayar da aka yi daidaita ke da fadin bukatun dokar Allah da aka ketare. Yesu ya bude hanya zuwa kursiyin Uban, kuma ta wurin tsakancinsa za a mika ma Allah ainihin burin dukan masu zuwa wurinsa cikin bangaskiya.

“Wanda ya rufe laifofinsa ba za ya y i albarka ba, amma dukan wanda ya fade su, ya kwa rabu da su za ya sami jinkai.” Misalai 28:13. Wadanda ke boye zunubansu, suna kuma ba da hujja game da zunuban nasu, in da sun san yadda Shaitan ke jin dadinsu, yana yi ma Krisit da malaiku masu tsarki ba’a saboda halin nan nasu, da za su hanzarta fadin zunubansu su kuma rabu da su. Ta wurin lahani a halin mutum Shaitan yakan yi kokarin mallakar dukan tunanin, kuma ya san cewa idan ana rike da lahanin nan, shi zai yi nasara. Saboda haka kullum yana kokarin rudin masu bin Kristi da dabarunsa da ba za su iya nasara da su ba. Amma Yesu yana roko a madadinsu da hannayensa da aka huda, da kujajjen jikinsa, kuma yana ce ma dukan wadanda za su bi shi: “Alherina ya ishe ka.” Korintiyawa II, 12:9. “Ku dauka ma kanku karkiyata, ku koya daga wurina; gama ni mai-tawali’u me. ,ao-kaskantar zuchiya; za ku sami hutawa ga rayukanku. Gama karkiyata mai-sauki che, kaya na kuma mara nauyi.” Matta 11:29,30. Don haka kada wani ya dauka cewa ba za a iya magance lahaninsa ba. Allah zai ba da bangaskiya da alheri don yin nasara da su.

Yanzu muna cikin babban ranar kafaran nan ne. A hidimar farillai, yayin da babban priest ke yin kafara don Israila, akan bukaci kowa ya wahal da ransa tawurin tuba daga zunubi da kaskantar da kai a gaban Ubangiji, domin kada a datse su daga jama’ar. Hakanan kuma dukan wadanda ke so a iske sunayensu cikin littafin rai, ya kamata tun yanzu, cikin yan kwanaki kalilan da sun rage masu, su wahal da rayukansu gaban Allah ta wurin bakinciki domin zunubi da tuba na gaskiya. Dole a yi binciken zuchiya cikin aminci sosai; dole a rabu da ruhun sakacin da Kirista da yawa ke yi. Akwai yaki sosai a gaban dukan masu so su danne miyagun halayyan da ke neman ka da su. Aikin shirin na kai da kai ne. Ba kungiya-kungiya ne za a cece mu ba. Tsabta da himmar wani ba za su cika ma wani mara halayyan nan gibinsa ba. Ko da shike dukan al’ummai za su gurbana a gaban Allah domin shari’a, za ya bincika rayuwar kowane mutum a natse dalla dalla kamar wannan mutumin ne kadai a duniya. Dole a gwada kowane mutum a tarar ba shi da aibi ko lahani, ko kuma wani abu hakanan.

Al’amran da su ka danganci aikin karshe na kafarar masu muhimminci ne sosai. Yanzu ana shari’an a haikali na sama. Shekaru da dama ana wannan aikin. Ba da jimawa ba, ba wanda ya san lokacin za a kai kan shari’ar masu rai. Rayuwar mu za ta zo wurin Allah domin bincike. A wannan lokacin fiye da kowane lokaci ya kamata kowane mutum a ji fadakar Mai-ceton cewa: “Ku yi lura ku yi tsaro, ku yi addu’a; gama ba ku san lokachin da sa’a take ba.” Markus 13:33. “Idan fa ba ka yi tsaro ba, ina zuwa da kamar barawo ba kwa za ka san sa’an da zan afko maka ba.” Ruya 3:3.

Sa’an da aikin shari’a ta binciken ya kare, an sansance rabon kowa ke nan, ko rai ko mutuwa. Za a rufe gafara gaf da bayanuwar Ubangiji cikin gizagizai, na sama. Kristi cikin Ruya, sa’an da Ya hangi wannan lokacin, Ya ce; “Wanda shi ke mara-adalchi, bari shi yi ta rashin adilchi; wanda shike mai-kazamta kuma, a kara kazamtadda shi; wanda shi ke mai-adilchi kuma, bari shi yi ta adilchi; wanda shi ke mai-tsarki kuma, a kara tsarkake shi. Ga shi, ina zuwa da samri; hakina yana tare da ni kuma, da zan saka ma kowane mutum gwalgwadon aikinsa.” Ruya 22:11,12.

Masu adalci da miyagu za su ci gaba da rayuwa cikin jiki mai-mutuwa suna shuka da gine-gine, suna ci suna sha, ba tare da sanin cewa a haikali na sama an rigaya an fadi hukumcin karshe wanda ba za a taba sakewa ba. Kafin ambaliyar, bayan Nuhu ya shiga jirgin, Allah ya rufe shi a ciki, ya kuma rufe masu fajirci a waje; amma har kwana bakwai, muanen ba da sanin cewa hallakarsu ta tabbata ba, su ka ci gaba da rayuwarsu ta rashin kulawa da son annishuwa, suna ba’a ga r hukumcin da ke zuwa. Mai-ceton Ya ce; “Hakanan kuma bayanuwar Dan mutum za ta zama.” Matta 24:39. Shuru dai, ba zato ba tsammani, kamar barawo da tsakar dare, sa’ar za ta zo da za a tabbatar da rabon kowane mutum, sa’anda za a janye tayin jinkai na masu laifi.

“Ku yi tsaro fa,… kada ya iske ku kuna barci da zuwansa ba labari.” Markus 13:35,36. Abin tausayi ne yanayin wadanda sun gaji jira su ka koma ga sha’awoyin duniya. Sa’anda mai-jari ya mai-da hankali ga neman riba, mai-kaunar jin dadi kuma yana neman nishadi, yayin da yar gaye ta ke kwalliyarta, watakila a wannan sa’ar ce Mai-shari’ar dukan duniya zai bayana hukumcin: “An auna ka chikin mizani, an iske ka ka gaza.” Daniel 5:27.

Babi na 29—Mafarin Mugunta

Ga mutane da dama, mafarin zunubi da dalilin kasancewarsa ababa ne masu wuyan ganewa ainun. Su na ganin ayukan mugunta da munanan sakamakonta na kaito da hallakaswa, suna kuwa tambayan yadda aka yi ababan nan ke faruwa a kalkashin ikon wanda ya ke da hikima da iko da kauna marasa iyaka. Wannan asiri ne da ba su da bayaninsa. Cikin rashin tabbacinsu da shakkarsu, sun kasa ganin gaskiya da a ka bayana sarai sarai cikin maganar Allah, muhimmai ga ceto kuma. Akwai wadanda, cikin bincikensu game da kasancewar zunubi, su na kokarin binciken abin da Allah bai taba bayanawa ba; saboda haka ba sa samun amsar tambayoyin su; masu yawan shakka da zargi ba dalili, kuma suna anfani da wannan a matsayin hujjar kin maganar littafi mai-tsarki. Wadansu kuwa sun kasa samun cikakkiyar fahimtar babban matsalan nan, watau mugunta, sabo da abada da bahaguwar fasara sun duhunta koyaswar Littafin game da halin Allah da yanayin gwamnatinsa, da kaidodinsa na magance zunubi.

Ba shi yiwuwa a bayana mafarin zunubi ta yadda za a ba da dalilin kasncewarsa. Duk da haka za a iya fahimtar abu da yawa game da mafarin zunubi da yadda a karshe za a gama da shi, a ba da cikakken bayanin adinin Allah da kaunarsa cikin magance mutunta da ya ke yi. Littafin yana koyar da cewa Allah ba Shi da hannu cikin shigowar zunubi; cewa ba a janye alherin Allah haka kawai ba, ba aibi a gwamnatin Allah da har za a ce ya janyo tasowar tawaye. Zunubi ya kutsa ne, kuma ba za a iya ba da hujjar kasancewarsa ba. Asiri ne, babu dalilinsa; idan aka ba da hujjar kasancearsa, an nuna cewa ba laifi ne ba ke nan. Idan aka sami hujjarsa ko a nuna sanadin kasancewarsa, ya dena zama zunubi ke nan. Ma'anar zunubi ita ce wadda aka bayar cikin maganar Allah: zunubi shi ne "ketaren shari'a, bayanuwar wata kaida ce mai-jayayya da babban dokan nan watau kauna, wadda ita ce tushen gwamnatin Allah.

Kafin shigowar zunubi, akwai salama da farinciki ko ina a dukan halitta. Komi yana cikakkiyar jituwa da nufin Mahalici, kaunar Allah ita ce gaba, kaunar juna kuma ba son kai a ciki. Kristi kalma, haifaffe kadai na Allah, daya yake da Uban, daya cikin yanayi, da hali da manufa, shi kadai ne cikin duka halitta ya isa ya shiga cikin dukan shawarwarin Allah da manufofinsa. Ta wurin Kristi, Uban Ya y i aikin halittar dukan mazamnan sama. Ta wurinsa aka halici dukan abu, wadanda ke sama, ko kursiyai ne, ko mulkoki ne, ko ikoki ne, kuma dukan sama ta nuna biyayya ga Kristi yadda aka nuna ma Uban.

Da shike dokar kauna ce harsashen gwamnatin Allah, farincikin dukan halitu ya danganta ga cikakkiyar jituwarsu da manyan kaidodinta na adalci ne. Allah yana bidar hidima ta kauna daga dukan halitunsa - biyayya da ta ke bulbulowa daga godiya sabo da halinsa. Ba Ya son biyayya dole, kuma yana ba kowa yancin zabi, domin su yi masa hidima ta yardar rai.

Amma akwai wani da ya zaba ya bata yancinsa. Zunubi ya sami asali a wurinsa ne, shi wanda, bayan Kristi, Allah Ya girmama shi fiye da kowa, wanda kuma ya fi kowa cikin mazamnan sama iko da daraja. Kafin faduwarsa, Lucifer ne na farko cikin cherubim, mai-tsarki mara kazanta. “Abinda Ubangiji Yahweh ya fadi ke nan: ba ka rage komi ba, chike da hikima, kamiltache ne ga wajen jamali. A chikin Eden ka ke, gonar Allah; kowane dutse mai-daraja ya zama marufinka,… kai ne cherub shafaffe, mai-rufewa; na kafa ka a bisa dutse mai-tsarki na Allah; tafiyarka, kai da kawowa, a tsakiyar duwatsun wuta. Tun ran da aka haliche ka kamiltache ne kai a chikin dukan al’amuranka, har ran da aka iske rashin gaskiya a chikinka.” Ezekiel 28:12-15.

Ya kamata Lucifer ya kasance cikin alherin Allah, kamnatace wadanda dukan rundunan malaiku za su girmama shi su kuma kaunace shi, yana anfani da kyawawan gwanintan shi don taimakon wadansu da daukakar Mahalicinsa. Amma, in ji annabin, “Zuchiyarka ta daukaka sabada jamalinka: hasken ranka ya bata hikimarka.” Aya 17. Kadan da kadan, Lucifer ya zama mai-son daukaka kansa. “Tun da ka mai da zuchiyarka sai ka che zuchiyar Allah.” “Ka che,… zan daukaka kursiyina, bisa tamrarin Allah; zan zamna bisa dutse na taron jama’a,… in hau chan bisa madaukakan hadura; in maida kai na kamar Mai-iko duka.” Aya 6; Ishaya 14:13,14. Maimakon kokarin daukaka Allah cikin soyayya da biyayyar halitunsa, kokarin Lucifa shi ne jawo su su bauta masa su kuma yi masa biyayya shi kansa. Kuma sabo da kiyashin darajan da Uban Ya ba dansa, wannan sarkin malaikun ya yi kokarin samun ikon da Kristi ne kadai ke da yancin mallakarsa.

Dukan sama ta yi murnar bayana darajar mahalicin da kjuma nuna yabonsa. Kuma sa’anda a ke girmama Allah hakanan ba komi sai salama da murna. Amma wata muryar sabani ta lalata jituwar saman. Bautar kai da daukakar kai, sabanin shirin Mahalicin, sun jawo alamun mugunta cikin zukatan da daukakar Allah ce ta ke da fifiko a ciki. Majalisun sama suka roki Lucifer. Dan Allah Ya bayana masa girma da nagarta da adalcin mahalicin, da kuma yanayin tsarki na dokarsa da rashin sakewarta. Allah da kansa ya rigaya ya kafa tsarin sama; kuma idan lucifa ya kance masa, zai ci mutumcin mahalicinsa ke nan ya kuma kawo ma kansa hallaka. Amma kashedin nan da aka bayar cikin kauna da jinkai marasa iyaka sun jawo ruhun tirjiya ne kawai. Lucifa ya bar kishin Kristi ya dawoma, har ya nace da sabaninsa.

Alfarman darajarsa ta haifar da son daukaka. Lucifer bai ga cewa manyan girmamawa da aka yi masa kyauta ne daga Allah ba, don haka bai ga dalilin da zai gode ma mahalicin ba. Ya yi alfahari da walkiyarsa da girmansa, har ya yi burin zama daidai da Allah. Mazamnan sama sun kaunace shi suka kuma girmama shi. Malaiku sun rika marmarin aiwatar da umurninsa, kuma an suturta shi da hikima da daraja fiye da dukansu. Duk da haka Dan Allah ne babban sarkin sama da aka amince da Shi, wanda ikonsa da iyawansa daya ne da na Uban. Duk wata shawara a sama, Kristi yana ciki, amma ba a yarda Lucifa

ya shiga shawarar Allah ba. Sai shi wannan babban malaikan ya tambaya: “Don me Kristi ke da fifikon? Don me a ke daukaka Shi hakanan gaba da Lucifer?”

Sa’anda ya bar wurinsa a gaban Allah, Lucifer ya ci gaba ya baza ruhun rashin gamsuwa a cikin malaikun. Ya yi aiki cikin sirri, da fako kuma ya boye ainihin manufarsa kalkashin kamanin girmamawa ga Allah, ya yi kokarin ta da kiyayya ga dokokin da ke aiki kan mazamna na sama, yana nuna cewa dokokin suna da takura ba dalili. Da shike yanayinsu masu-tsarki ne, ya roka cewa malaikun su bi muradin zukatan su. Ya so ya ja ma kansa tausayi tawurin nuna cewa wai Allah Ya yi masa rashin adalci tawurin ba Kristi mafificiyar daraja. Ya ce cikin neman karin iko da daraja ba firmama kansa ya ke so ba, amma yana neman ya tabbatar ma dukan mazamnan sama yanci ne, domin tawurin wannan su cimma yanayin rayuwa mafi-girma.

Allah cikin jinkansa Ya yi hakuri da Lucifer da dadewa. Ba a rage masa girma nan da nan ba lokacin da ya fara tunanin rashin gamsuwa, ko ma lokacin da ya fara bayana zarge zargen shi na karya ga malaiku masu biyayya. An bari ya kasanche a saman da dadewa dai. Akai akai an rika yi masa tayin yafewa idan ya tuba, ya yi biyayya. An yi duk wani kokari na kauna da hikima mara iyaka domin a nuna masa kuskurensa. Kafin nan ba a taba samun ruhun rashin gamsuwa ba a sama. Lucifer kansa da farko ma bai san inda ya nufa ba; bai gane ainihin yanayin tunaninsa ba. Amma sa’an da aka bayana cewa ba dalilin rashin gamsuwarsa, Lucifer ya gane cewa ba shi da gaskiya, cewa batutuwan Allah daidai ne, kuma ya kamata ya amince da hakan a gaban dukan sama. Da ya yi haka, da ya ceci kansa da malaiku da yawa. A lokacin bai rigaya ya janye biyayyarsa ga Allah kwata kwata ba. Ko da shike ya rabu da matsayinsa na cherub mai-rufewa, duk da haka da ya yarda ya koma ga Allah, ya amince da hikimar Allah, ya kuma gamsu da matsayin da an bar shi cikin babban shirin nan na Allah, da an mayar da shi matsayinsa. Amma girman kai ya hana shi amincewa. Ya nace yana kare matakinsa, cewa ba ya bukatar tuba, ya kuma dukufa wajen babban jayayyarsa sabanin Mahalicinsa.

Yanzu ya mai da dukan kwarewar tunanin son yin rudu, domin shi sami goyon bayan malaiku da ke kalkashin ikonsa. Ko kashedi da shawaran da Kristi ya ba shi ma ya tankware shi don taimaka ma dabarunsa. Ga wadanda kauna da amincinsu su ka manna su gare shi, Shaitan ya ce ba a yi masa adalci ba, ba a girmama matsayinsa ba, kuma ana so a takaita ‘yancinsa. Daga canja kalmomin Kristi ya kai ga canja tasa maganar da yin karya kai tsaye, yana zargin Dan Allah da shirin ci masa mutunci a gaban mazaunan sama. Ya kuma so ya yi karya cewa akwai wata damuwa tsakaninsa da malaiku masu biyayya ga Allah. Ya zargi dukan wadanda bai iya rudinsu su bi shi ba, da cewa wai basu damu da sha’anonin da suka shafi mazaunan sama ba. Ya zargi masu biyayya ga Allah da aikin da shi kansa ya ke yi. Don neman tabbatar da zarginsa na cewa Allah Ya yi masa rashin adalci, ya shiga canja kalmomin Mahalicin. Ya shiga rikitar da malaiku da rudu game da manufofin Allah. Ababa masu saukin ganewa ya mai da su na asiri, kuma ta wurin dabarunsa ya rikitar da maganar

Allah. Kasancewarsa tare da hukumar sama ta kara ma karyarsa da karfi ta yadda malaiku da yawa su ka hada kai da shi wajen yi ma Allah tawaye.

Allah cikin hikimarsa Ya bar Shaitan ya ci gaba da aikinsa, har sai da ruhun rashin gamsuwa ya kai ga tawaye kai tsaye. Wajibi ne tsare-tsarensa su cika, domin kowa ya ga yanayinsu da sakamakonsu. An daukaka Lucifer sosai; mazaunan sama sun kaunace shi sosai, tasirinsa a kansu kuma yana da karfi. Gwamnatin Allah ya kunshi mazaunan sama, har da na dukan duniyoyin da ya halitta; Shaitan kuma ya dauka cewa idan ya iya jawo malaikun sama suka yi tawaye tare da shi, zai iya daukan sauran duniyoyin ma. Ya yi anfani da dabaru da zamba wajen gabatar da ra'ayinsa ta yadda zai cimma burinsa. Gwanin rudi ne shi, kuma tawurin boye kansa cikin karya ya sami nasara. Har malaiku masu biyayya ga Allah ma ba su iya fahimtar halinsa gaba daya ko kuma su ga inda aikinsa ya nufa ba.

An girmama Shaitan sosai, dukan ayukansa kuma sun cika da asiri ta yadda ya zama da wahala a bayana ma malaiku ainihinyanahin aikinsa. Ba don an bar zunubi ya cika girmansa ba, da ba a gane cewa mugun abu ne ba. Kafin nan, ba zunubi a dukan halittar Allah, halittu masu tsarki kuma basu san yanayinsa da muguntarsa ba. Ba su iya gane muggan sakamakon kawar da dokar Allah ba. Da farko Shaitan ya boye aikinsa ta wurin nuna cewa yana biyayya ga Allah. Ya ce wai yana karfafa daukaka ga Allah ne, da karkon gwamnatinsa da jin dadin dukan mazaman sama. Yayin da ya ke cusa rashin gamsuwa cikin zukatan malaikun da ke tare da shi, ya yi yadda za a ga kaman yana kokarin kawar da rashin gamsuwan ne. Sa'anda ya yi canje canje cikin tsarin Allah da dokokin gwamnatinsa, ya yi da karyan cewa canje canjen nan wajibi ne don tabbatarda jituwa a sama.

Cikin aikinsa na magance zunubi, Allah ya na anfani da adalci da gaskiya ne. Shaitan ya na iya anfani da ababan da Allah ba zai iya anfani da su ba, watau balmar baka da rudi. Ya rigaya ya yi kokarin kayryata maganar Allah, ya kuma yi ma gwamnatin Allah batanci a gaban malaiku, ya na cewa wai Allah bai yi adalci ba da ya kafa ma mazaunan sama dokoki, cewa biyayya da Allah ke bida daga hallittunsa neman daukakan kansa ne kawai. Saboda haka, dole a nuna ma mazaunan sama da na dukan duniyoyi cewa gwamnatin Allah tana da adalci, dokarsa kuma mara-aibi ne. Shaitan ya nuna kamar shi kansa ya na nema ya karfafa ci gaban dukan halitta ne. dole kowa ya gane ainihin halin mai-kwacen nan. Aka ba shi lokaci domin ya bayana kansa ta wurin miyagun halayyansa.

Shaitan ya zargi dokar Allah da gwamnatinsa da laifin jawo rashin jituwa, wanda aikin shi Shaitan din ne ya jawo. Ya ce kowace mugunta sakamakon mulkin Allah ne. Dole a bar aikinsa ya hukumta shi, da farko Shaitan ya ce shi ba tawaye ya ke yi ba. Dole a bari dukan halittu su ga tonon asirin makaryacin.

Ko sa'an da aka ce ba zai iya ci gaba da kusancewa a sama ba, Allah bai hallaka Shaitan ba. Da shike Allah yana karban hidima ta kauna ce kadai, dole biyayyar halitunsa

ta kasance bisa ga yarda da adalcinsa da kaunarsa. Mazaunan sama da na sauran duniyoyi ai da basu iya ganin adalcin Allah da jinkansa ba, in da ya hallaka Shaitan a wancan lokacin. Da an shafe shi daga halitta nan take, da ana yi ma Allah hidima don tsoro ne, ba don kauna ba. Da ba a rushe tasirin mai-rudun gaba daya ko kuma a kawar da ruhun tawaye gaba daya ba. Dole a bar mugunta ta nuna. Domin dukan haitta ta anfana, dole Shaitan ya girmar da kaidodinsa har su nuna, domin dukan halita su ga ainihin yanayin zarge zargen da ya yi ma gwamantin Allah da jinkansa da rashin sakewar dokarsa kuma.

Tawayen Shaitan darasi ne ga dukan halitta na dukan sararaki, shaida ce kuma har abada ta yanayin zunubi da mumunan sakamakonsa. Sakamakon mulkin Shaitan kan mutane da malaiku zai nuna sakamakon kawar da mulkin Allah. Zai shaida cewa zaman lafiyan dukan halittun Allah da dokarsa ne, ta hakanan tarihin mumunan tawayen nan za ya zama madawamin tsaro ne ga dukan tsarkaka, domin kada a rude su game da yanayin zunubi, a kuma cece su daga aikata zunubi, da shan horonsa.

Har karshen jayayyan nan a sama, babban mai kwacen nan ya ci gaba da cewa yana da gaskiya. Sa'anda aka sanar da cewa dole za a kore shi da dukan masu-goyon bayansa daga sama, sai shugaban tawayen nan ya bayana reninsa ga dokar Mahalici, kai tsaye. Ya maimaita ra'ayinsa cewa malaiku ba sa bukatar a nuna iko a akansu, amma a bar su su bi nufin kansu, wanda kullum zai bishe su daidai. Ya soki dokokin Allah cewa suna rage masu 'yanci, ya kuma bayana cewa niyyarsa ce ya tabbatar da sokewar doka; cewa idan aka 'yantar da rundunan sama daga wannan kangin, za su shiga yanayin rayuwa mafi daukaka da daraja.

Ruhun nan da ya ta da tawaye a sama har yanzu yana ta da tawaye a duniya. Abin da Shaitan ya yi da malaiku, ya ci gaba da yinsa tare da mutane. Ruhunsa yana mulki yanzu cikin 'yan tawaye. Kamar Shaitan din, suna so su rushe shingayen dokar Allah suna kuma yi ma mutane alkawalin 'yanci ta wurin ketare sharuddan doka. Har yanzu tsautawa zunubi ya na ta da ruhun kiyayya da tirjiya. Sa'an da aka bayana sakonin fadaka na Allah, Shaitan ya kan sa mutane su ba da hujja ma kansu, su kuma nemi goyon bayan wadansu cikin tafarkinsu na zunubi. Maimakon gyarta kurkuransu, su kan ta da fushi ne kan mai-fadakarwan, sai ka ce shi ne kawai matsala. Daga kwanakin Habila zuwa lokacinmu, irin ruhun da a ke nunawa ke nan game da masu kokarin nuna munin zunubi.

Tawurin karya dayan da ya yi a sama game da halin Allah, wanda ya sa aka mai da shi azalumi mai-danniya, Shaitan ya koya ma mtum zunubi. Da shike ya yi nasara hakanan kuma, ya ce kuntatawa na rashin adalci da Allah ya yi ne ya kai ga faduwar mutum, kamar yadda ya kai ga tawyensa.

Amma Madauwamin kansa Ya bayana halinsa: "Ubangiji, Ubangiji Allah ne cike da juyayi, mai-adalchi kuma, mai-jinkirin fushi, mai-yalwar jin kai da gaskiya; yana tsaron

jin kai domin dubbai, yana gafarta laifi da sabo da zunubi; ba shi kubutadda mai-laifi ko kadan.” Fitowa 34:6,7.

Tawurin korar Shaitan daga sama Allah Ya bayana adalcinsa Ya kuma tabbatar da darajar kursiyinsa. Amma sa’anda mutun ya yi zunubi ta wurin amincewa da rudun mai-riddan nan, Allah Ya ba da shaidar kaunarsa ta wurin ba da Dansa haifaffe tilo domin ya mutu saboda fadaddun ‘yan Adam. Cikin kafarar an bayana halin Allah. Babban darasin giciyen yana koya ma dukan halitta cewa hanyar zunubi da Lucifer ya dauka ba laifin gwamnatin Allah ba ne ko kadan.

Cikin jayayya tsakanin Kristi da Shaitan, lokacin hidimar Mai-ceto a duniya, an bayana halin babban mai-yaudaran nan. Ba abinda ya iya tumbuke Shaitan daga soyayyar malaikun sama da dukan halitta kamar yadda yakinsa da Mai-fansar duniya ya yi. Sabon nan na sa, inda ya ce ma Kristi shi yi masa sujada, da gangancin karfin halinsa da ya kai Kristi kan wani dutse mai-tsawo kwarai da kan hasumiya ta haikali, da muguwar manufar da ta bayana sa’anda ya bukaci Yesu ya fadi daga makurar tsawon hasumiyar haikalin, da muguntan da ya dinga farautar Kristi da ita ko ina, ya na zuga zukatan priestoci da mutane domin su ki kaunar Kristi, a karshe kuma su ta da murya su na cewa. “A giciye shi! A giciye shi!” - dukan wannan ya sa dukan halitta ta yi mamaki da fushi.

Shaitan ne ya sa duniya ta ki Kristi. Sarkin mugunta ya yi anfani da dukan ikonsa da dabarunsa domin shi hallaka Yesu; domin ya ga cewa jinkan Mai-ceton da kaunarsa da tausayinsa da tawali’unsa suna bayana ma duniya halin Allah. Shaitan ya yi jayayya game da kowace magana da Yesu ya yi, ya kuma yi anfani da mutane su ka zama wakilansa don cika rayuwar Mai-ceton da wahala da bakinciki. Dabarunsa da karyan da ya yi anfani da su don hana aikin Yesu, da kiyayan da ya nuna tawurin yayan rashin biyayya, da zarge-zargen da ya yi kan Shi wanda rayuwarsa ta nagarta babu kamarta, duk sun taso ne daga son ramako. Wutan kiyashi da mugunta da kiyayya da ramako sun habaka a Kalfari kan Dan Allah, yayin da dukan sama ke kallo shuru da kyama.

Sa’anda aka kamala hadayar, Kristi ya je sama, ya ki soyayyar malaiku tukuna, har sai bayan da ya gabatar da rokon nan cewa: “Wadanda ka bani, ina so su zamna wurin da ni ke, tare da ni. Yohanna 17:24. Sa’an nan da matukar kauna da iko Uban ya amsa daga kursiyinsa cewa: “Bari dukan mallaiku na Allah su yi masa sujada.” Ibraniyawa 1:6. Cin mutuncin da aka yi ma Yesu ya kare, hadayarsa ta cika, aka ba shi suna da ta fi kowace suna.

Yanzu laifin Shaitan ya tabbata ba hujja. Ya rigaya ya bayana ainihin halinsa na makaryaci mai-kisa kuma. Aka ga cewa ruhun nan da ya yi mulkin ‘ya’yan mutane wadanda ke kalkashin ikonsa da shi, in da an ba shi damar mallakar mazaunan duniya da ya yi anfani da ruhu dayan ne. Ya yi ikirarin cewa ketare dokar Allah zai kawo yanci da girmammawa, amma aka ga cewa ya haifar da bauta ne da kaskanci.

Zarge zargen Shaitan na karya game da halin Allah da gwamnatinsa sun bayana da ainihin yanayinsu. Ya zargi Allah da neman daukaka kansa ne kawai da yake bidar biyayyar halitunsa, ya kuma ce yayin da Mahalicin ke bidar musun kai daga wurin halita, shi kansa Mahalicin ba ya musun kai, kuma ba ya sadakar da komi. Yanzu ga shi an ga cewa domin ceton duniya ta zunubi sarkin dukan halitta ya yi hadaya mafi girma da kamna kan iya yi, gama "Allah yana chikin Kristi yana sulhunta duniya zuwa kansa." Korintiyawa II, 5:19. An kuma ga cewa yayin da Lucifer ya bude kofa domin shigowar zunubi tawurin son girma da neman daukakarsa, Kristi Ya kaskantar da kansa, ya yi biyayya har mutuwa, domin shi hallaka zunubi.

Allah Ya bayana kyaman da yake ma halayyan tawaye. Dukan sama sun ga an bayana adalcinsa ta wurin hukumta Shaitan da kuma fansar mutum. Lucifer ya rigaya ya ce idan dokar Allah ba ta sakewa, kuma ba za a iya cire horonta ba, dole za a hana kowane mai-laifi samun alherin Mahalici ke nan. Ya ce an kai masu zunubi inda ba za su iya samun fansa ba, saboda haka kuma su abincinsa ne na halal. Amma mutuwar Kristi ta ba mutum goyon bayan da ba wanda zai iya kawarwa. Horon dokar ya fadi a kansa ne, Shi wanda yake daidai da Allah, sai mutum ya sami 'yancin karban adalcin Kristi, kuma tawurin rayuwar tuba ya yi nasara, yadda Dan Allah ya rigaya ya yinasara, bisa ikon Shaitan. Ta hakanan Allah mai-adalci ne, kuma mai-kubutar da dukan masu ba da gaskiya ga Yesu.

Amma ba domin fansar mutum ne kadai Kristi ya zo duniya ya sha wahala har ya mutu ba. Ya zo domin Ya "chichika" dokan ne ya kuma mai-da shi abind daraja. Ba kawai domin mazaunan duniyan nan su dauki dokar yadda ya kamata ba ne, amma domin Ya bayana ma dukan duniyoyin dukan halitta ne cewa dokar Allah ba ta sakewa. Da za a iya kawar da bukatun dokar, da Dan Allah bai bukaci ba da ransa domin kafarar ketarewar ta ba. Mutuwar Kristi ta na tabbatar da rashin sakewar dokar. Kuma hadayan da kaunar Uban da Dan ta sa suka yi, domin a fanshi mutum, ta na nuna ma dukan halitta cewa adalci da jinkai ne harsashen dokar Allah da gwamnatinsa.

Sa'an da a karshe za a zartas da hukumci za a ga cewa ba hujja domin zunubi. Sa'anda Mai-shari'an dukan duniya zai tambayi Shaitan, "Don me ka yi mani tawaye, ka kuma kwace mani 'ya'yan mulki na? Mai-kirkiro zunubin ba zai sami hujjan da zai bayar ba. Kowane baki zai rufu, kuma dukan rundunan tawaye za su rasa abin fadi.

Yayin da giciyen Kalfari ke bayana cewa dokar ba ta sakewa, yana kuma bayana ma duniya cewa hakin zunubi mutuwa ne. Cikin kalmomin karshe na Mai-ceton, cewa: "An gama," an kada kararrawar mutuwar Shaitan. Babban jayayyan da aka dade ana yi ya zo karshensa, aka kuma tabbatar da kawar da zunubi a karshe. Dan Allah Ya shiga kabari "domin tawurin mutuwa shi wofinta wanda yake da ikon mutuwa, watau Shaitan." Ibraniyawa 2:14. Burin Lucifer na daukakar kansa ya sa shi ya ce: "Zan daukaka kursiyina bisa tamrarin Allah,… in mai da kaina kamar Mai-iko duka." Allah ya ce: "Na maishe ka toka a kasa, ba ka da sauran zama ba dadai." Ishaya 14:13,14; Ezekiel 28:18,19. Sa'an da

“rana tana zuwa, tana kuna kamar tanderu; dukan masu girman kai, da dukan wadanda ke aikin mugunta za su zama tattaka, ranan da ke zuwa kuma za ta kokone su, in ji Ubangiji mai-runduna, har da ba za ta bar masu tushe ko reshe ba.” Malachi 4:1.

Dukan hailitta sun zama shaidu game da yanayin zunubi da sakamakonsa. Kuma hallakawarsa, wanda in da tun farko aka yi shi, da zai jawo ma malaiku tsoro ya kuma jawo ma Allah rashin daraja, yanzu kuwa zai bayana kaunarsa ne a gaban dukan halitta masu murnan yin nufinsa, wadanda kuma dokarsa tana cikinsu. Mugunta ba za ta kara bayanuwa ba kuma. Maganar Allah ta ce: “Wahala ba za ta taso so biyu ba.” Nahum 1:9. Dokar Allah da Shaitan ya ce karkiyar bauta ce, za a girmama ta a matsayin dokar ‘yanci. Halitta da an rigaya an gwada an kuma tabbatar, da za a sake juya ta daga biyayya ga Shi wanda an rigaya an bayana halinsa kwata kwata a gabansu, cewa kauna ce mara matuka da hikima mara iyaka ba.

Babi na 30—Kiyayya ta Jahannama

“Tsakaninka da machen kuma zan kafa magabataka, da tsakanin zuriyarka da zuriyatta kuma; shi za ya kuje kanka, kai kuma zaka kuje duddugensa. Farawa 3:15. Hukunchin da aka zartas ma Shaitan bayan faduwar mutum, annabci ne ma, wanda ya kunshi dukan sararaki har karshen lokaci, ya kuma bayana babban tashin hankalin da zai shafi dukan kabilun ‘yan Adam da za su taba rayuwa a duniya.

Allah ya ce, “Zan sa gaba.” Gaban nan bai je daidai da yanayin halitta ba. Sa’anda mutum ya ketare dokar Allah, yanayinsa ya zama mungu, ya kuma sami jituwa, ba sabani ba, da Shaitan.

Bisa yanayi, ba gaba tsakanin mutum mai-zunubi da wanda ya kago zunubin, dukansu sun zama miyagu ta wurin ridda. Mai-ridda ba ya taba hutawa, har sai ya sami tausayawa da goyon baya tawurin rudin wadansu su bi gurbinsa. Saboda wannan dalilin ne fadaddun malaiku da miyagun mutane ke hada kai cikin abota sosai. Da ba don Allah ya shiga tsakani ba, da Shaitan da mutum sun shiga wani hadin kai na sabani da Allah; kuma maimakon yin gaba da Shaitan, da dukan iyalin duniya sun hada kai wajen yin jayayya da Allah.

Shaitan ya jarabci mutum ya yi zunubi, yadda ya sa malaiku su ka yi tawaye, domin ta wurin wannan shi sami hadin kai cikin yakinsa da Allah. Babu mahawara tsakaninsa da fadaddun malaikun game da kiyayarsu ga Kristi, yayin da suka sami rashin jituwa game da dukan sauran ababa, sun hada kai sosai wajen jayayya da ikon shugaban dukan halitta. Amma sa’anda Shaitan ya ji cewa gaba za ta kasance tsakaninsa da macen, da kuma tsakanin zuriyarsa da zuriyan macen, ya san cewa kokarinsa na lalata yanayin mutum zai sami cikas; cewa ta wata hanya za a ba mutum ikon kin yarda da ikonsa.

Abin da ya ingiza magabtakan Shaitan da ‘yan Adam shi ne cewa tawurin Kristi, su masu cin moriyar kaunar Allah da jin kansa ne. Yana so ne ya rushe shirin nan na fansar dan Adam, ya jawo ma Allah rashin daraja, tawurin bata aikin hannunsa; zai jawo bakinciki a sama, ya kuma cika duniya da kaito da hallaka. Sa’an nan yana cewa dukan wannan sakamakon halitar mutum da Allah ya yi ne.

Alherin da Kristi ya shuka cikin mutum ne yake haifar da magabtaka tsakaninsa da Shaitan. Ba domin wannan alherin tubarwa da ikon sabontawa ba, da mutum zai ci gaba da kasancewa kamammen Shaitan, bawan da zai kasance a shirye kullum ya bi umurnin Shaitan. Amma sabuwar kaidar a cikin mutum ya iya kin azalumin nan mai-kwace. Duk wanda aka ga yana kin zunubi maimakon sonsa, duk wanda ya ke ki yana kuma nasara da muradan zuciya da su ka mallaki zuciya a da, yana nuna aikin kaida ne daga sama dungum.

Sabanin da ke tsakanin ruhun Kristi da ruhun Shaitan ya bayana a fili sa’anda duniya ta karbi Yesu. Ba lallai don ya bayana ba tare da arziki na duniya, ko fahariya, ko nuna isa

ne Yahudawa su ka ki shi ba. Sun ga cewa Ya na da iko da ya fi arzikin duniya da duk wani abin fahariya muhimmanci. Amma kuma tsarkin Kristi da tsabtarsa sun jawo masa kiyayyar kafirai. Rayuwarsa ta musun kai da himma mara zunubi ta kasance soka na dindindin ga mutane masu fahariya da masu fasikanci. Wannan ne ya jawo ma Dan Allah kiyaya. Shaitan da miyagun malaiku suka hada kai da miyagun mutane. Dukan masu ridda suka hada baki sabanin jagoran gaskiya.

Ana nuna ma masu bin Kristi daidai gaban da aka nuna ma Mai-gidan na su ne. Duk wanda ya ga munin zunubi, da taimako daga sama, kuma ya ki faduwa cikin jaraba, zai fuskanci fushin Shaitan da talakawansa lallai. Muddan akwai zunubi da masu aikata shi, kiyaya ga kaidodin gaskiya da tsananta ma masu gaskiya zai ci gaba. Masu bin Kristi da bayin Shaitan ba za su iya jituwa ba. Laifin giciyen nan bai kare ba. “I, kuma dukan wadanda su ke so su yi rai mai-ibada chikin Kristi Yesu za su sha tsanani.” Timothawus II, 3:12.

Wakilan Shaitan kullum suna aiki kalkashin umurninsa don tabbatar da ikonsa da gina mulkinsa sabanin gwamnatin Allah. Don haka suna kokarin rudin masu bin Kristi, su janye su daga biyayyarsu ga Kristi. Kamar mai-gidansu, suna tankware Littafin domin cimma manufarsu. Kamar yadda Shaitan ya yi kokarin jawo ma Allah reni, hakanan ne wakilansa su ke kokarin bata sunan mutanen Allah. Ruhun da ya kashe Kristi ne yana motsa miyagu su hallaka mutanensa. Dukan wannan yana kunshe cikin annabcin nan na farko cewa, “Tsakaninka da machen kuma zan kafa magabtaka, da tsakanin zuriyakka da zuriyatta kuma.” Wannan kuwa zai ci baga har karshen lokaci.

Shaitan ya na tara dukan mayakansa, yana sa dukan karfinsa cikin fadan. Don me ba ya gamuwa da jayayya da yawa? Don me mayakan Kristi ke barci da kuma rashin kulawa? Domin dangantakarsu da Kristi ba shi da yawa; domin ba Ruhunsa a cikinsu. Zunubi ba abin kyama ba ne garesu, kamar yadda Mai-gidansu ke kyamarshi. Ba sa fuskantarsa da kiyayya mai-tsanani yadda Kristi ke yi. Basu gane matukar muguntar zunubi, kuma ba su san yanayin sarkin duhu da ikonsa ba. Gaban da a ke yi da Shaitan da ayukansa ba ta da yawa sabo da akwai jahilci ne game da ikonsa da muguntarsa, da kuma girman yakin da ya ke yi da Kristi da ekklesiyarsa. Jama’a da yawa sun rude a nan. Ba su san cewa magabcinsu babban janar ne, wanda ke mallakar tunanin miyagun malaiku ba, kuma cewa da ingantattun tsare tsare da matakai na gwamninsa ya na yaki da Kristi domin hana ceton rayuka. Cikin Kirista, har ma cikin masu aikin bishara, ba a cika ambaton Shaitan ba, sai dai wani lokaci a kan ambace shi a bagadi. Ba a kula alamun ayukansa da nasarorinsa; ana sakaci da gargadi kan gargadi game da dabarunsa, ana yin biris da kasancewarsa ma.

Yayin da mutrane su ka jahilci dabrunsa, magabcin wand ba ya barci ya na binsu kowane lokaci. Yana tsoma baki cikin kowane fanni na iyali, a kowane titi na biranenmu, cikin ekklesiyoyinmu, a majalisun kasa, a kotunar, ya na rikitarwa da rudarwa, yana lalatarwa, ko ina ya na tatike rayuka da jikunan maza da mata da yara, ya na raba iyalai, ya

na shuka kiyayya da rikici da hargitsi da kisa. Kuma Kirista su na gani kamar Allah ne ya shirya ababan nan, kuma dole su kasance.

Kullum Shaitan ya na kokarin rinjayar mutanen Allah tawurin rushe shingayen da ke raba tsakaninsu da duniya. An rudi Israila ta da sa'an da suka shiga ma'amala da kafirai. Haka kuma a ke jawo Israila ta zamani ga batawa. "A chikinsu kwa allah na wannan zamani ya makantadda hankulan marasa-bada gaskiya, domin kada hasken bisharar darajar Kristi, wanda shi ke surar Allah, ya waye masu." Korintiyawa II, 4:4. Dukan wadanda ba tsayayyun masu-bin Kristi ba ne bayin Shaitan ne. Cikin zuciyan da bai tuba ba, akwai son zunubi da son ba da juhhar yin zunubin. Zuciyar da ta sake ta na adawa da zunubi, tana kuma kinshi. Sa'an da Kirista su ka za bi dangantaka da kafirai da marasa ba da gaskiya ga Allah, su na jawo ma kansu jaraba ne. Shaitan ya kan boye kansa ya rufe idanunsu a sace da rudunsa. Ba za su iya gani cewa ma'amalan nan za ta cuce su ba, kuma yayin da su ke kusantuwa da duniya cikin hali da magana da ayuka, suna kara makancewa ne.

Jituwa da halayyan duniya yakan tubar da ekklesiya ne zuwa duniya; ba ya taba tubar da duniya zuwa wurin Kristi. Sabuwa da zunubi yakan sa a dena ganin muninsa. Wanda ya zabi yin ma'amala da bayin Shaitan, ba da jimawa ba zai dena tsoron mai-gidansu. Sa'an da mu na cikin aikinmu idan aka jaracbe mu, kamar yadda a ka jarabci Daniel a fadar sarki, mu sani cewa Allah zai tsare mu, amma idan mu ka sa kanmu cikin jaraba, za mu fadi, ko a jima ko a dade.

Magabcin ya cika aiki da nasara tawurin wadanda ba a tsammanin cewa 'ya'yansa ne. Ana sha'awar masu gwaninta da masana, ana kuma girmama su, sai ka ce gwaninta da sani za su iya magance rashin tsoron Allah, ko su ba mutane 'yancin samun karbuwa ga Allah. Gwaninta da ilimi kansu baiwa ne na Allah, amma idan aka sa su sun dauki matsayin ibada, idan maimakon jawo mutum kusa da Allah sun janye mutun ne daga Allah, sun zama la'ana ke nan da tarko kuma. Da yaya su na da ra'ayin cewa duk wani abu mai-kaman ladabi ko wayewa daga Krsiti ne. Ba kuskuren da ya fi wannan. Ya kamata kowane Kirista ya mallaki halayyan nan domin za su yi tasiri sosai ga ainihin addini, amma dole a sadakar da su ga Allah in ba haka ba kuwa su ma za su jawo mugunta. Mutane da yawa masu ilimi da ladabi, wadanda, ba za su taba yin rashin kirki ba, 'ya'yan Shaitan ne. Tasirin halinsu mai-kama da nagarta ya sa sun zama magabta masu hatsarin gaske ga aikin Kristi, fiye da jahhilai marasa hankali. Ta wurin adu'a da naciya, da dagora ga Allah kuma, Solomon ya sami hikima da ta sa duniya ta yi mamaki da sha'awa. Amma sa'anda ya juya daga tushen karfinsa, ya shiga dogara ga kansa, ya fada cikin jaraba. Sa'anan gwanintan da aka ba sarkin nan mafi hikima su ka sa shi ya zama wakilin magabcin mutane.

Yayin da Shaitan kullum ya ke nema ya makantar da tunaninsu, kada Kirista su taba manta cewa "Kokuwar mu ba da nama da jini ta ke ba, amma da mulkoki, da ikoki, da mahukumtan wannan zamani mai-dufu, da rundunai masu-ruhaniya na mugunta chikin sammai." Afisawa 6:12. Fadakar ta na zuwa mana a zamaninmu cewa: "Ku yi hankali

shimfide, ku yi zaman tsaro; magabcinku Shaitan, kamar zaki mai-ruri, ya na yawo ya na neman wanda za ya chinye." Bitrus I, 5:8. "Ku yafa dukan makamai na Allah, domin ku sami ikon da za ku yi tsayayya da dabarun Shaitan." Afisawa 6:11.

Daga kwanakin Adamu zuwa na mu, zamanin, babban magabcinmu ya na amfani da ikonsa domin danniya da hallakaswa. Yanzu yana shiri domin harinsa na karshe a kan ekklesiya. Dukan masu so su bi Yesu za su fuskanci sabani da magabcin nan. Idan Kirista ya na kara kamanta halin Kristi, ya na kara jawo ma kansa hare-haren Shaitan ke nan. Dukan masu yin aikin Allah, su na kokarin bayana rudun mugun, su na kuma bayana Kristi ga mutane, za su iya hada kai da Bulus inda ya ke shaida batun bauta ma Ubangiji da dukan tawali'u na zuciya, da hawaye mai-yawa da jarabobi kuma.

Shaitan ya jarabci Kristi da jarabobinsa mai-tsanani, amma an ka da shi ta kowace fuska. An yi yakokin nan a madadin mu ne, nasarorin nan sun sa mu ma za mu iya yin nasara. Krsiti zai ba da karfi ga dukan masu neman karfi. Shaitan ba za ya iya rinjayar wanda bai yarda masu ba. Majarabcin ba shi da iko ya mallaki tunani ko kuma ya tilasta mutum ya yi zunubi. Zai iya yin fitina, amma ba zai iya kazamtarwa ba. Zai iya jawo wahala amma ba zai iya lalatarwa ba. Da shike Kristi Ya yi nasara, ya kamata wannan ya motsa masu binsa su sami karfin hali su yi yaki da gaske sabanin zunubi da Shaitan.

Babi na 31—Miyagun Ruhohi

Littafi ya bayana dangantaka tsakanin duniyan da a ke gani da wanda ba a gani, da hidimar malaikun Allah, da wakilcin miyagun ruhohi, kuma ba a iya raba ababan nan da tarihin ‘yan Adam. Kin gaskata cewa akwai miyagun ruhohi ya na karuwa ne, sa’an nan wadansu kuma su na koyar da cewa malaiku masu tsarkin nan masu “hidima sabili da wadanda zasu gaji cheto” (Ibraniyawa 1:14), wai ruhohin matattu ne. Amma Littafin ya na koyar da kasancewar malaiku, nagargaru da miyagu, yana kuma cikakken tabbaci cewa malaiku ba ruhohin matattu ba ne.

Kafin halittar mutum, akwai malaiku, domin lokacin da aka kafa harsashen duniya. “tamrarin safiya suka yi waka, dukan ‘ya’yan Allah kwa suka yi sowa don farinchiki.” Ayuba 38:7. Bayan faduwar mutum, an aiki malaiku su tsare itacen rai, tun kafin mutum da ya ya mutu. Bisa ga yanayi, malaiku sun fi mutane, gama mai-zabura ya ce mutum da kadan ya gaza malaiku. (Zabura 8:5).

Littafin ya fada mana yawa da iko da darajar mazamnan sama, da dangantakarsu da gwamnatin Allah, da kuma dangantakarsu da aikin fansa. “Ubangiji ya kafa kursiyinsa a chikin sammai; mulkinsa kwa ya na bisa kowa.” Annabin kuma ya ce: “Na ji murya malaiku da yawa kewaye da kursiyin.” Su na jira a dakin sarkin sarakuna, malaiku “karfafa masu-iko” “masu hidima na sa, wadanda ke aika yardassa,” suna “kasa kunne ga muryar maganatasa.” Zabura 103:19-21; Ruya 5:11. Masu hidiman da Daniel ya gani su dubban dubbai ne, zambar goma kuma so zambar goma. Manzo Bulus ya ce rundunarsu “ba ta kidayuwa,” Daniel 7:10; Ibraniyawa 12:22. A matsayin su na ‘yan sakon Allah su na kaiwa da komowa “sai ka che hasken walkiya.” (Ezekiel 1:14), darajarsu mai walkiya, firiyarsu da saurin gaske. Malaikan da ya bayana a kabarin Mai-ceton wanda “siffarsa tana kama da walkiya, tufassa kuma fara fat kamar snow.” Ya sa masu tsoron kabarin suka yi rawan jiki don tsoro,” su ka zama kamar matattu.” Matta 28:3.4. Sa’anda Sennacherib sarkin Assyria ya rena Allah, ya kuma yi masa sabo, ya kuma yi ma Israila barazanar hallaka, “A daren nan fa ya zama malaikan Ubangiji ya fita, ya buga mutum zambar dari da tamanin da biyar chikin sansanin Assyriyawa.” Ya datse dukan jarumawa, da manya da shugannin.” Daga mayakan Sennacherib. “Ya fa kama garinsa da kunya.” Sarakuna II, 19:35; Labarbaru II, 32:21.

Ana aikan malaiku ne da sakonin jinkai zuwa ga ‘ya’yan Allah. Zuwa ga Ibrahim, da alkawaran albarka, zuwa kofokin Sodom, domin su ceci Lot adali daga hallaka ta wuta; zuwa ga Iliya, yayin da yake gaf da hallaka sabo da yunwa da gajiya a jeji; zuwa ga Elisha, da karusai da dawaki na wuta, kewaye da kankanin garin nan inda magabta su ka kewaye shi, zuwa ga Daniel, yayin da ya ke bidar hikimar Allah a fadar kafirin sarki, ko kuma inda aka bar shi ya zama abincin zakuna; zuwa ga Bitrus, wanda ke jiran mutuwa a kurkukun Hirudus, zuwa ga fursunonin nan a Filibbi; zuwa ga Bulus da abokansa a daren guguwan

nan a kan teku; domin a bude tunanin Karnilius don karban bishara; domin a tura Bitrus da sakon ceto zuwa ga ba-al'umi, hakanan ne malaiku masu tsarki suka yi ma mutanen Allah hidima cikin dukan sararraki.

Akan ba kowane mai-bin Kristi malaika shi zama waliyinsa, masu-tsaron nan na sama suna tsaron masu-adalchi daga ikon mugun. Shaitan kansa ya gane hakan lokacin da ya ce: "A banza ne Ayuba yake tsoron Allah? Ba ka kewaye da shinge ba, da shi da gidansa, da dukan abin da ya ke da shi, a kowane sassa?" Ayuba 1:9,10. Mai-zabura ya bayana ta yadda Allah ke tsaron mutanensa, inda ya ce: "Malaikan Ubangiji ya na kafa sansani a kewaye da masu tsoronsa. Ya na tseradda su kuma," Zabura 34:7. Game da masu-ba da gaskiya gareshi, Mai-ceton Ya ce: "Ku yi hankali kada ku rena wani a chikin wadannan kankanana; gama ina che maku, chikin sama kullum malaikunsu suna duban fuskar Ubana." Matta 18:10. Malaikun da aka sa su yi hidima ma 'ya'yan Allah kullum su na da hanyar zuwa wurinsa.

Muggan ruhohi da aka halice su da farko ba zunubi, da yanayinsu da iko da darajarsu daidai ne da na malaiku masu tsarki da yanzu ke hidimar Allah. Amma da shike sun fadi tawurin zunubi sun hada kai don rena Allah da hallaka mutane, da shike sun hada kai don rena Allah da hallaka mutane. Da shike sun hada kai da Shaitan cikin tawayensa, aka kuma kore su tare daga sama, cikin dukan sararaki su na hada kai da shi cikin yakinsa da Allah. Littafi yana bayana mana gangaminsu da gwamnatinsu, da kungiyoyinsu, iri iri, da wayansu da dabarunsu, da kuma muggan shirye shiryensu sabanin salamar mutane da farincikinsu.

Tarihin Tsohon Alkawali ya kan ambaci kasancewarsu da wakilcinsu; amma lokacin da Kristi ke cikin duniya ne miyagun ruhohi su ka nuna ikonsu sarai sarai. Kristi ya zo domin shiga cikin shirin fansar mutum, Shaitan kuma ya kudurta nuna 'yancinsa na mallakar duniya. Ya yi nasarar kafa bautar gumaka ko ina a duniya ban da Palestine. Ga kasa da ya kadai da ba ta yarda da mulkin Shaitan duka ba, Kristi Ya zo domin ya ba mutanen hasken sama. A kasan nan ikoki biyu masu gaba da juna sun yi jayayya game da fifiko. Yesu Ya mika hannuwansa na kauna, yana gayyatan dukan masu so, su sami gafara da salama cikinsa. Rundunan duhu sun ga cewa ba su da iko mara-iyaka, suka gane kuma cewa idan aikin Kristi ya yi nasara, mulkinsu zai kare ba da jimawa ba. Shaitan ya yi ta fushi kamar zakin da aka daure da sarka ya kuma ci gaba da nuna ikonsa a kan jikunan mutane da rayukansu.

Sabon Alkawali ya bayana a fili cewa aljannu su kan shiga cikin mutane. Wadanda aka wahal da su hakanan ba azabar ciwon jikunansu kadai suke sha ba. Kristi Ya na da cikakkiyar ganewar abinda yake fuskanta, Ya kuma gane kasancewa kai tsaye da kuma wakilcin miyagun ruhohi.

Misalin yawansu da iko da muguntarsu, da kuma ikon jin kan Kristi shi ne labarin Littafin na warkar da masu alajannun nan na Gadara. Wahalallun mahaukatan nan da suka fi karfin kowane kangi, suna birgima, suna kumfa, da fushi, su ka cika wuri da kukansu, suna ji ma kansu raunuka, suka kuma zama hatsari ga duk wanda ya je kusa da su. Jikunansu lalatattu jina-jina, da tunaninsu da ya kauce, sun gamsar da Shaitan hakanan. Daya daga cikin aljannun da ke cikin mahaukatan ya ce: “Sunana Tuli ne; gama muna da yawa.” Markus 5:9. A sojan Romawa, tuli guda ya kan kunshi tsakanin sojoki dubu uku zuwa dubu biyar ne. Rundunonin Shaitan ya na kuma karkasa su kampani-kampani ne, kuma kampani dayan da aljannun nan ke ciki ba su kasa tuli guda ba.

Bisa ga umurnin Yesu miyagun ruhohin suka fice daga mutanen nan, suka bar su suna zaune a natse a sawayen Mai-ceton, rinjayayyu, cikin hankalinsu da ladabi kuma. Amma an yarda ma aljannun suka share zuwa cikin teku; kuma ga mazamanan Gadara, garken aladun ya fi masu albarkan da Kristi ya bayar, suka roki Mai-warkarwan ya tafi. Sakamakon da Shaitan ya so ya samu kenan. Ta wurin zargin Yesu da laifin jawo masu hasara, ya ta da tsoro na son kai cikin mutanen, ya kuma hana su sauraron maganarsa. Kullum Shaitan ya na zargin Kirista cewa su ne sanadin hasara da rashin sa’a da wahala, maimakon amincewa cewa shi da wakilansa ne sanadin.

Amma ba a kawar da manufofin Kristi ba. Ya bar miyagun ruhohin suka hallaka aladun don tsauta ma Yahudawan nan ne da su ke kiwon dabbobin nan marasa tsabta don neman kurdi. Ba don Kristi ya hana aljannun ba, da sun tsunduma makiyayan aladun da masu aladun cikin tekun, tare da aladun. Kiyaye makiyayan da masu aladun sabo da ikonsa da ya yi anfani da shi cikin jinkai ne domin kubutar da su. Ban da haka, an bar wannan al’amari ya faru domin almajiransu shaida muguntar ikon Shaitan kan mutum da dabba ne, Mai-ceton Ya so masu-binsa su sami sanin magabcin da za su sadu da shi, domin kada ya rude su ya kuma rinjaye su da dabarunsa. Nufinsa ne kuma cewa mutanen yankin nan su ga ikonsa na karye kangin Shaitan da kuma kubutar kamanun Shaitan din. Kuma ko da shike Yesu kansa Ya tafi, mutanen da ya kubutar da su ta wurin al’ajibin nan sun kasance a wurin domin su bayana jinkan wanda ya taimake su.

An kuma rubuta wadansu al’amura masu kama da wannan cikin Littafin. Diyar macen nan Ba-surofinikiya ta wahala sosai da aljani, Yesu kuwa ya fitar da shi tawurin kalmarsa. Markus 7:26-30. “Wani mai-aljan, makafo da bebe,” (Matta 12:22); wani saurayi mai-ruhu na bebanci, wanda “so da yawa kwa ya kan jefa shi chikin wuta, da chikin tapkunan ruwa kuma, domin ya hallaka shi,” (Markus 9:17-22); mahaukacin nan da cikin fama da “ruhun aljani mai-kazamta” (Luka 4:33-36), wanda ya rikitar da salamar Assabbat a haikali na Kafarunhum -dukansu Mai-ceton nan Mai-tausayi ya warkar da su. A kusan kowane al’amari, Kristi ya yi magana da aljanin kamar halitta mai-wayo. Mai-ceton nan mai-tausayi Ya yi magana da al’janin kamar wanda ke da ganewa, yana umurtarsa shi fito daga cikin mutumin, kuma kada ya sake hallaka shi. Sa’anda masu-sujada a Kafarnahum suka

ga ikonsa mai-girma, “mamaki ya abko masu duka, suka yi zanche da junansu, suka che: Wache magana che wannan? Gama da hukumchi da iko yana umurnin kazaman ruhohi, suna kwa fito.” Luka 4:36.

Wadanda aljannu ke cikinsu akan ce suna cikin yanayi na wahala sosai; amma ba kowanne ne haka ba. Domin a sami ikon da ya fi na mutum, wadansu sun nemi tasirin Shaitan. Irinsu basu sami damuwa da aljannun ba. Irin su sun hada da masu ruhun sihiri, kamar su Simon Magus, Alima mai-sihiri, da budurwan nan da ta rika bin Bulus da Sila a Fillibi.

Ba wadanda suka fi fuskantar hadarin tasirin muggan ruhohi kamar wadanda, duk da shaidu da yawa kai tsaye daga littafin, su ke musun kasancewar Iblis da malaikunsa. Muddan dai ba mu san dabarunsu ba, suna da riba a kanmu; mutane da yawa suna sauraron shawarwarinsu yayin da suka gani kamar su na bin hikimar kansu ne. Shi ya sa, yayin da muka kusanto karshen lokaci, sa’anda Shaitan ke aiki da dukan ikonsa domin rudu da hallaka, yana yayata ra’ayin nan ko ina cewa ba Shaitan din ma. Yana so ne ya boye kansa da hanyoyin da ya ke tafiyar da aikinsa.

Ba abin da mai-yaudaran nan ya fi tsoro kamar cewa mu gane dabarunsa. Ta wurin boye halinsa da manufofinsa ya sa ana daukansa da wasa ta yadda ana masa ba’a ne da reni kawai. Ya kan ji dadi idan ana nuna cewa shi abin dariya ne ko kyama, mumuna wanda rabinsa dabba ne, rabi kuma mutum. Yakan ji dadi in ya ji wadanda ke gani kamar su na da wayo da sani sosai su na wasa ko ba’a da sunansa.

Domin ya boye kansa da kyau ne ya sa ake tambaya ko ina cewa: “Ko akwai wani halitta hakanan?” Amincewa da masu addini ke yi da ra’ayoyin da ke karyata shaidar Littafin, shaida ce ta nasarar Shaitan. Kuma domin Shaitan zai iya mallakar wadanda ba su san da tasirinsa ba ne ya sa maganar Allah ta ba mu misalai da yawa na aikin muguntarsa, ta kuma bayana mana ikokin sana sirri, ta hakanan kuma ta sa mu cikin tsaro daga hare harensa.

Ikon Shaitan da muguntarsa da na rundunansa za su iya razana mu ba don za mu iya samun mafaka da kubuta cikin mafificin ikon mai-fansarmu ba. Mukan kulle gidajen mu da makullai don tsaron dukiyarmu da rayukanmu daga miyagun mutane, amma ba mu cika tunanin miyagun malaikun da kowane lokaci su ke neman hanyar zuwa wurinmu, wadanda kuma a cikin karfin kanmu ba mu da hanyar kariya daga hare harensu. Idan aka yarda masu za su iya kawar da zukatanmu, su lalata jikunanmu su kuma azabtar da su, su hallaka dukiyarmu da rayukanmu kuma. Abin da ke masu dadi kawai shine wahala da hallaka. Abin tsoro ne yanayin wadanda ke kin umurnin Allah su na yarda da jarabobin Shaitan, har lokacin da Allah zai ba da su ga ikon muggan ruhohi. Amma masu bin Kristi su na lafiya kullum a kalkashin tsaronsa. Ana aikawa da malaiku masu-matukar karfi domin su tsare su. Mugun ba zai iya kutsawa da shingen da Allah Ya kewaye mutanensa da shi ba.

Babi na 32—Tarkokin Shaitan

Babban jayayyan nan tsakanin Kristi da Shaitan da ake yi, yanzu wajen shekaru dubu shidda kenan, ya kusa karewa; mugun kuma yana kara kokarinsa na bata aikin da Kristi ke yi a madadin mutum, ya kuma daure rayuka cikin tarkokinsa. Manufarsa ita ce ya rike mutane cikin duhu da rashin tuba har sai tsakancin Mai-ceton ya kare, kuma babu sauran hadaya domin zunubi.

Idan ba a yi wani kokari na musamman don jayayya da ikonsa ba, sa'anda kyaliya ta mamaye ekklesiya da duniya, Shaitan ba ya damuwa; domin ba yiwuwar rasa wadanda yake rike su cikin bauta yadda ya ga dama. Amma sa'anda aka jawo hankula zuwa ababa na har abada, mutane kuma su na tambaya: "Menene zan yi domin in sami ceto?" ya kan nemi yadda zai gwada ikonsa da na Kristi, ya kuma rushe tasirin Ruhu Mai-tsarki.

Littafin ya ce a wani lokaci sa'anda malaikun Allah suka zo su gabatar da kansu a gaban Ubangiji, Shaitan ma ya zo cikin taron. (Ayuba 1:6), ba domin shi durkusa a gaban Madawamin Sarkin ba, amma domin shi ci gaba da miyagun manufofinsa kan adilai. Da manufa dayan yake kasancewa sa'anda mutane suka taru don sujada ga Allah. Ko da shike ba a ganinsa, ya na aiki da dukan himma domin shi mallaki zukatan masu-sujadar. Kamar kwararren janar ya kan shimfida tsare tsarensa kafin lokacin. Yayin da yake ganin dan sakon Allah ya na binciken Littafin, ya kan lura da batun da za a gabatar ma mutanen. Sa'an nan yakan yi anfani da dukan dabarunsa da iyawarsa don mallakar al'amurata yadda sakon ba zai kai wurin wadanda yake rudinsu game da wannan batun ba. Wanda ya fi bukatar sakon za a nuna mashi wani sha'ani da ke bukatar kasancewarsa, ko kuma ta wata hanya a hana shi jin kalmomin da za su iya zama masa dalilin samun rai. Kuma, Shaitan ya na ganin bayin Ubangiji su na damuwa saboda duhun ruhaniya da ke mammayar mutane. Ya na jin addu'o'insu domin alherin Allah da iko domin rushe kangin kyaliya da rashin kulawa da kiwuya. Sa'an nan da sabuwar himma ya kan shiga aikinsa. Ya kan jarabci mutane da kwadayi ko kuma wani irin jin dadi, ta hakan kuma ya kangarar da tunaninsu domin su kasa jin ainihin ababan da suka fi bukatar sani.

Shaitan ya sani sarai cewa dukan wanda zai iya sa shi ya bar yin addu'a da binciken Littafin zai rinjaye shi da hare harensa. Saboda haka yana kirkiro kowane irin abu da zai mallaki zuciya. A kullum akwai masu cewa su na bin Allah amma maimako su ci gaba domin su san gaskiyar, sai su yi himma wajen neman kuskuren bangaskiya ko aibin hali wajen wadanda ke da banbancin ra'ayi da su. Irinsu masu taimakon Shaitan ne sosai. Masu zargin yan-uwa su na da yawa, kuma kullum su na aiki sa'anda Allah ya na aiki, bayinsa kuma suna yi masa biyayya. Za su sa launin karya kan kalmomi da ayukan masu kaunar gaskiya da kuma biyayya gareta. Za su nuna cewa wai bayin Kristi mafi himma da kwazo da musunkai an rude su ne ko kuma masu yaudara ne su. Aikinsu ne bata manufofin kowane abin gaskiya da martaba, su labarta jitajita, su ta da zato cikin zukatan marasa

kwarewa. Ta kowace hanya za su so su sa a ga abinda ke da tsarki da tsabta kamar kazamtace ne mai yaudara.

Amma kada a rudi wani, game da su. Nan da nan za a iya gane ko ‘ya’yan wanene su, ko kwatancin wa suke bi, kuma ko aikin wa suke yi. “Bisa ga ‘ya’yansu za ku sansanche su.” Matta7:16. Tafarkinsu kama da na Shaitan, mugun makaryaci, “mai-saran yan-uwanmu.” Ruya 12:10.

Babban mai-rudin ya na da wakilai da yawa da ke shirye su gabatar da kowane irin kuskure domin su kama rayuka, ridda da aka shirya domin a gamsar da sha’awoyi da kwarewar wadanda ya ke so ya hallaka. Shirinsa ne ya kawo marasa gaskiya wadanda basu tuba ba cikin ekklesiya, domin su karfafa yin shakka da rashin ba da gaskiya, su kuma hana dukan masu marmarin ganin ci gaban aikin Allah su kuma ci gaba da shi. Da yawa da ba su da ainihin bangaskiya ga Allah ko maganarsa, suna amincewa da wadansu kaidodin gaskiya ana kuma ganin su kamar Kirista, ta hakanan kuma za su iya gabatar da kurakuransu kamar koyaswoyin Littafin.

Koyaswan da ke cewa ko da menene a mutum ya gaskata ba damuwa, rudu ne na Shaitan ya san cewa gaskiya idan aka karbe ta cikin kauna, takan tsarkake ran mai-karban; sabo da haka a kullum ya na kokarin sauya ta da karya da tatsuniyoyi da wata bishara. Tun farko bayin Allah su na hamayya da mallaman karya, miyagu masu shuka karyan da ke kashe rayuka. Iliya da Irmiya da Bunlus, ba tsoro suka yi hamayya da masu juyar da mutane daga maganar Allah. Karimcin nan da ke gani kamar sahihiyar bangaskiya ba ta da muhimmanci bai karbu ga tsarkakan nan masu-kare gaskiya ba.

Fassara mara inganci da ake yi ma Littafin, da ra’ayoyi masu karo da juna game da bangaskiya na addinin da ake samu cikin Kiristanci aikin babban magabcinmu ne domin ya rikita zukata don kada su gane gaskiya. Rashin jituwa da tsatsaguwa da ke tsakanin ekklesiyoyin Kirista kuma yawanci saboda an saba murda nassosi ne domin su goyi bayan ra’ayin da ake so. Maimakon binciken maganar Allah da zuciyar ladabi, domin a san nufinsa, da yawa suna neman sabon abu ne kawai, wanda babu kamarsa.

Domin a tabbatar da koyaswoyin kuskure ko halayyan da suka saba ma Kiristanci, wadansu sukan dauke nassosi daga mahallinsu, ko su dauki rabin aya don tabbatar da ra’ayin nasu. Tare da dabarun Shaitan suna nutsar da kansu cikin guntayen batutuwan da suke murdawa don gamsar da bukatunsu na mutuntaka. Ta hakanan wadansu suke lalatar da maganar Allah. Wadansu kuma masu zurfin tunani, sukan yi anfani da misali da alama na Littafin, su fasarta su ta yadda za su gamsar da sha’awoyinsu, ba tare da kulawa da shaidar Littafin a matsayinsa na mai-fasarta kansa ba, sa’an nan su kan koyar da ganin damansu a matsayin koyaswar Littafin.

Duk lokacin da aka shiga nazarin Littafin ba tare da ruhun addu’a da tawali’u da neman koyuwa ba, za a murda nassosi mafi sauki da mafi-wahala daga ainihin ma’anarsu.

Shugabannin; ‘yan paparuma sukan zabi sassan Littafin da suka je daidai da manufarsu ne, su fasarta su yadda su ke so, sa’an nan su bayana ma mutane hakanan, yayin da su ke hana su nazarin Littafin da gane ma kansu gaskiyansa. Ya kamata a ba mutane dukan Littafin daidai yadda yake. Da bahaguwar koyaswar Littafin gara ma ba a koya masu Littafin ba gaba daya.

An shirya Littafin ya zama mai-bishewa ne ga dukan masu son sanin nufin Mahalicinsu. Allah Ya ba mutane tabbataciyar kalmar annabci; malaiku har da Kristi kansa sun zo domin su sanar ma Daniel da Yohanna alamuran da dole za su faru jima kadan. Ba a bar ababan nan da suka shafi cetonmu cikin sirri ba. Ba a bayyana su ta yadda za su rudar da mai-neman gaskiya har su batar da ita ba. In ji Ubangiji ta bakin annabi Habakkuk: “Ka rubuta ruyan, ta fita a fili,… domin mai-karantawa shi yi a guje.” Hababuk 2:2. Maganar Allah a fili ta ke ga dukan masu-nazarinta da zuciyar addu’a. Kowane ainihin mai-gaskiya zai zo wurin hasken gaskiya. “Ana shibka haske domin masu adilchi.” Zabura 97:11. Kuma ba ekklesiyar da za ta ci gaba cikin adalci sai membobin ta suna neman gaskiya da himma kamar boyayyar dukiya.

Ta wurin zancen ‘yanci, ko karimci, mutane ba sa ganin dabarun magabcinsu, yayin da kowane lokaci shi ya na kokarin cim ma burinsa ne. Idan ya yi nasarar sauya Littafin da ra’ayin mutane, za a kawar da dokar Allah, ekklesiyoyi kuma za su shiga bautar zunubi yayin da su ke cewa su na da ‘yanci.

Ga mutane da yawa, binciken kimiyya ya zama la’ana. Aka ya yarda ambaliyar haske ta zubo ma duniya ta wurin sabobin ababa da kimiya da fasaha ke ganewa, amma ko manyan masana, in ba maganar Allah ke bishe su cikin bincikensu ba, sukan rikice cikin kokarinsu na bincika dangatakar kimiya da wahayi.

Sanin mutuntaka ba cikakke ba ne, saboda haka yawanci basu iya daidaita ra’ayinsu na kimiya da batutuwan Littafin ba. Yawanci su na amincewa da ra’ayoyi da tunaninsu a matsayin tabbatattun batutuwan kimiya, su na kuma gani kamar ya kamata a gwada maganar Allah da koyaswoyin “ilimin da ana che da shi hakanan a karyache” Timothawus I, 6:20. Mahalici da aikace aikacensa sun fi karfin ganewarsu, kuma da shike basu iya bayana wadannan ta wurin dokokin halitta ba, akan maida tarihin Littafin abin shakka. Masu shakkar sahihancin Tsohon Alkawali da Sabon Alkawali sau dayawa su kan ci gaba su yi shakka cewa akwai Allah, har su mai da ikon Allah wai al’amarin halitta ne kawai. Da shike sun rabu da madogaransu, sukan shiga yawo cikin duwatsun kafirci.

Ta hakanan yawanci su kan bata, Shaitan kuma ya rude su. Mutane su na kokarin fin Mahalicinsu hikima. Tunanin mutum ya na kokarin bincikawa da bayana asiran da ba za a taba bayanawa ba har abada. Da mutane za su iya bincikawa su gane abin da Allah ya sanar game da kansa da manufofinsa, da za su ga daraja da martaba da ikon Yahweh ta yadda za su gane kankantar kansu su kuma gamsu da abin da aka bayana masu da ‘ya’yansu.

Babban rudun Shaitan ya sa mutane tunani da bimbini game da abin da Allah bai bayana ba, kuma bai nufa mu gane ba. Ta hakanan ne Lucifer ya rasa matsayin sa a sama. Bai gamsu ba da shike ba a fada masa dukan asiran manufofin Allah ba, ya kuma yi banza da abin da aka bayana game da aikinsa a babban matsayin da aka ba shi. Tawurin ta da rashin gamsuwan nan cikin malaikun da ke kalkashinsa kuma, ya jawo faduwarsu. Yanzu yana so ya cika zukatan mutane da ruhu dayan ya kuma kai su ga kin kula da umurnin Allah.

Wadanda ba sa so su amince da bayanannun gaskiya na Littafin, kullum su na neman tatsuniyoyi masu dadi ne da za su kwantar da lamiri. Idan suka rage yawan ruhaniya da musun-kai da kaskantarwar koyaswoyinsu, karbuwarsu ga mutane takan karu. Da shike su na ji kaman hikimarsu ta wuci cewa su yi binciken Littafin da zukatan tuba da addu'a da naciya domin bishewar Allah, bas u da tsaro daga rudu. Shaitan yana shirye ya biya muradin zuciya ya na kuma sauya gaskiya da rudunsa. Ta hakanan ne mulkin paparuma ya sami iko kan zukatan mutane; kuma ta wurin kin gaskiya domin ta kunshi daukan giciye, masu Kin ikon paparuma suna bin hanya dayan. Dukan masu-kyale maganar Allah domin bin sauki, domin kada su saba ma duniya, za su karbi ridda a matsayin gaskiyar addini. Wadanda su ka ki gaskiya da gangan za su karbi kowane irin kuskure. Wanda ke kyamar rudi daya, nan da nan zai karbi wani rudin kuma. Manzo Bulus, yayin da yake magana game da wadanda "ba su amsa kamnar gaskiya da za su tsira ba," ya ce: "Sabili da wannan fa Allah ya na aika masu da aikawar sabo, har da za su gaskata karya; domin a hukumta shari'a bisa dukan wadanda ba su gaskata gaskiya ba, amma suka ji dadin rashin adilchi." Tassalunikaya II, 2:10-12. Da irin kashedin nan a gabanmu ya kamata mu yi hankali da irin koyaswoyin da mu ke karba.

Cikin dabarun Shaitan, mafi nasara shi ne koyasuwoyin karya da al'ajiban karya na ruhohi. Ya sake kama, ya zama kamar malaikan haske, ya na baza tarunsa inda ba a taba zato ba. Da mutane za su yi nazarin littafin Allah da himma cikin addu'a domin su gane shi, ba za a bar su cikin duhu su karbi koyaswoyin karya ba. Amma ya yin da su ke kin gaskiya, suna shiga farkon yaudara.

Wata koyaswa mai hatsari kuma ita ce wadda ke musun Allahntakan Kristi, ta na cewa bai kasance ba kafin zuwan sa duniyan nan. Mutane da yawa masu cewa sun gaskata Littafin sun yarda da koyaswan nan, amma kuma a koyaswar ta saba ma furcin Mai-cetonmu game da dangantakarsa da Uban, da yayayin Allahntakansa da kasancewarsa kafin zuwansa duniya. Koyaswa ce da ke murda nassosi. Ta na rage ganewar mutum game da aikin ceto, ta kuma rage bangaskiya ga Littafin, cewa wahayi ne daga Allah. Wannan ya kara munin ta da wahalar yiyuwa a yarda da ita. Idan mutane su ka ki shaidar Littafin game da Allantakan Kristi, aikin banza ne yin mahawara da su game da batun, domin ba abin da za a bayana masu har su amince. "Mutum mai tabi'ar jiki ba shi karba al'amura na Ruhun Allah ba, gama wauta su ke a gare shi, ba shi kwa da iko shi san su, gama ana

gwadassu chikin ruhaniya.” Korintiyawa I, 2:14. Duk mai wannan kuskuren ba zai iya samun sahihiyar fahimtar halin Kristi ko aikinsa ba, ko kuma babban shirin Allah domin fansar mutum.

Wani kuskure mai-zurfin wayo da keta kuma shi ne wai Shaitan ba wani takamammen halitta ba ne; cewa wai Littafin ya na anfani da sunan ne kawai don bayana guggan tunani da muradan mutane.

Koyaswan nan da a ke maimaitawa a manyan majami’u cewa zuwan Kristi na biyu zai zo ma kowane mutum shi kadai a lokacin mutuwarsa ne dabara ce ta kawar da tunanin mutane daga zuwansa zahiri cikin gizagizai na sama. Shekaru da dama Shaitan ya na cewa, “Ga shi, ya na chikin lolokai,” (Matta 24:23-26), rayuka da yawa kuma sun salwanta ta wurin yarda da rudanin nan.

`Kuma, hikimar duniya ta na koyar da cewa addu’a ba ta da muhimmanci. ‘Yan kimiyya suna cewa ba yadda za a sami sahihiyar amsar addu’a; cewa wannan zai zama ketarewar doka, cewa al’ajabi ne, kuma wai ba al’ajibai ma. Su na cewa akwai kafaffun dokoki da ke iko da dukan halitta, kuma Allah kansa ba ya yi wani abin da ya saba ma dokokin nan. Ta haka suna nuna cewa Allah kansa ya na kalkashin dokokinsa, sai ka ce Allah ba shi da ‘yanci game da yadda dokokin su ke aiki ke nan. Irin koyaswan nan ya na sabani da shaidar Littafin. Ko Kristi da almajiransa ba su aikata al’ajibai ba? Mai-ceton nan Mai-tausayi har yau ya na da rai, ya na shirye kuma ya ji addu’ar bangaskiya kamar yadda ya yi lokacin da ya ke duniya. Mutuntaka ya na hada kai da wanda ya wuci ikon dan Adam. Shirin Allah ne tawurin amsa addu’ar bangaskiya, Ya ba mu abin da in da ba mu roka ba, ba zai ba mu ba.

Koyaswoyin karya a cikin Kirista ba su lissaftuwa. Ba shi yiyuwa a kiyasta miyagun sakamakon cire daya daga cikin shaidun da maganar Allah ta kafa. Masu gwada yin haka ba gaskiya daya kadai su ke ki ba. Yawanci su kan ci gaba su na kawar da kaidodin gaskiyan, daya bayan daya, har sai sun zama ainihin kafirai.

Abinda da Shaitan ya ke so ya faru ke nan. Ba abin da ya ke so kamar bata amincewa da Allah, da maganarsa da a ke yi. Shaitan ne shugaban kungiyar dukarun masu shakka, kuma ya na aiki da matukar ikonsa don rudin mutane su bi bayansa. Shakka ya zama abin da a ke yayi. Jama’a da yawa su na ganin maganar Allah da rashin yarda domin ta na tsauta ma zunubi, ta na kuma hukumta shi. Wadanda ba sa so su yi biyayya da bukatunta su kan yi kokarin watsar da ikonta. Sukan kranta Littafin, ko kuma su saurari koyaswoyinsa kawai domin su sami aibi daga Littafin ko wa’azin ne. Da yawa su na zama kafirai domin su sami hujjar kin aikin da ya kamata su yi ne. Wadansu su kan yi ta zarge zarge sabo da girman kai ne da kiwuya. Da shike son jiki ya hana su yin fice tawurin gwanancewa kan wani abu mai-daraja da ke bukatar kokari da musun-kai, su so su yi suna cewa suna da mafificiyar hikima, tawurin zargi ga sakon Littafin. Akwai ababa da yawa da tunanin mutum ba zai

iya ganewa ba sai da taimakon hikimar Allah, don haka su kan soki irin ababan nan. Akwai wadanda ke gani kaman gwaninta ne a tsaya a gefen rashin ba da gaskiya da shakka da rashin aminci. Amma a kalkashin kamanin son gaskiya za a ga cewa irin mutanen nan amincewa da kai da kuma fahariya ne ke motsa su. Da yawa su na jin dadin neman wani abu daga Littafin da zai rudar da tunanin wadansu. Wadansu su kan yi soka da zargi su kuma bi ra'ayi da son jayayya kawai. Ba sa gane cewa tawurin haka su na rikitar da kansu ne cikin tarkon Shaitan. Amma da shike sun bayana rashin ba da gaskiyarsu a fili, suna ji kamar dole ne su ci gaba da rike wannan matsayin. Ta wurin wannan su kan hada kai da arna su kuma rufe ma kansu kofofin mulkin Allah.

Allah Ya ba da isashen shaidan cikin Littafin, cewa Littafin maganarsa ce. Muhimman gaskiya da suka shafi fansar mu a bayane su ke a fili. Ta wurin taimakon Ruhu Mai-tsarki da a ka yi ma masu nemansa da gaske alkawalinsa, kowane mutum zai iya gane ma kansa koyaswoyin gaskiyan nan. Allah Ya ba mutane kakarfan harsashe da za su kafa bangaskiyarsu akai.

Duk da haka zukatan ba su isa su sami cikakkiyar fahimtar shirye shiryen Allah da manufofinsa ba. Ba yadda za mu gane Allah tawurin nemansa. Bai kamata mu yi gaggawar bude labulen da ya boye martabarsa da shi ba. Manzon ya ce: "Ina misalin wuyan binchiken shari'unsa al'amuransa kuma sun fi gaban a bi sawu!" Romawa 11:33. Za mu iya fahimtar yadda ya ke bi da mu, da manufofin da ya ke da su, domin mu gane kaunarsa da jinkansa marasa matuka da ke hade da iko mara iyaka. Ubanmu na sama ya na bi da kowane abu cikin hikima da adalci ne, kuma bai kamata mu yi rashin gamsuwa da rashin amincewa ba, amma mu durkusa cikin yarda ta bangirma. Za ya bayana mana yawan manufofinsa da ya kamata mu sani ne, fiye da wannan kuma,mu amince da ikonsa mara iyaka, da zuciyarsa cike da kauna.

Yayin da Allah Ya ba da isashiyar shaidar bangaskiya, ba zai taba kawar da dukan hujjar rashin ba da gaskiya ba. Dukan masu neman hujjojin shakka za su samu, kuma wadanda su ka ki karban maganan Allah su kuma yi biyayya gareshi, wai har sai an kawar da kowace jayayya da shakka, ba za su taba samun haske ba.

Rashin amincewa da Allah ya na samuwa ne daga zuciyar da ba ta tuba ba, wadda ke gaba da Allah. Amma Ruhu Mai-tsarki ne Ya ke jawo bangaskiya, kuma za ta girma yadda ke sha'awarta ne. Ba wanda zai iya samun karfi cikin bangaskiya ba tare da yin kokari da himma ba, rashin bangaskiya ya kan yi karfi idan ana karfafa shi ne, kuma idan mutane, maimakon tunani kan shaidun da Allah Ya bayar don karfafa bangaskiyarsu, suka yarda suka shiga yin tambayoyi da soke soke ba dalili, za su ga shakkunsu kullum sun tabbata.

Amma masu shakkar alkawaran Allah, su na kuma kin yarda da tabbacin alherinsa, su na kin grimama Shi ne, kuma tasirinsu, maimakon jawo wadansu wurin Kristi, ya na koransu ne daga wurinsa, su itatuwa ne marasa ba da 'ya'ya da su ke baza ressansu masu

yabanya nesa, sun a rufe hasken rana daga sauran shuke shuke, suna kuma sa su yakwanewa su na mutuwa kalkashin sanyin inuwar. Aikin mutanen nan zai bayana a matsayin shaida mara karewa game da su. Su na shuka irin shakka da rashin yarda da za su haifar da girbi dole.

Akwai hanya daya tak da ya kamata masu so a kubutar da su daga shakka su bi. Maimakon zargi da soka ba dalili game da abinda ba su fahimta ba, bari su saurari hasken da ke haskaka su yanzu, za su kuwa sami karin haske. Bari su yi kowane aikin da aka bayana ga ganewarsu, za a kuwa sa su iya ganewa su kuma aikata ababan da su ke shakkarsu yanzu.

Shaitan zai iya kawo jabu wanda ya yi kama da ainihin sosai, ta yadda zai rudi wadanda su ka yarda a rude su, wadanda ke so su ki musun-kan nan da hadaya da gaskiyar ke bida; amma ba shi yiwuwa gare shi ya rike mutum daya kalkashin ikon sa, wanda da gaske ya ke marmari, ko ta halin kaka, ya san gaskiyar. Kristi ne gaskiya da “Haske mai-gaskiya wanda yana haskaka kowane mutun, yana zuwa chikin duniya.” Yohanna 1:9. An aiki Ruhu Mai-gaskiya Shi bishe mutane zuwa dukan gaskiya. Kuma bisa ikon Dan Allah an ce: “Ku nema, za ku samu.” “Idan kowane mutum yana da nufi shi aika nufin Allah, shi za ya sani ko abin da nike koyaswa na Allah ne.” Matta 7:7; Yohanna 7:17.

Masu bin Kristi sun san kadan ne daga shirye shiryen da Shaitan da rundunansa ke kagowa game da su. Amma shi wanda ke zaune a sammai zai warware dukan dabarun nan domin cika shirye shiryensa. Ubangiji yana barin mutanensa su shiga wahalar jaraba, ba don yana jin dadin wahalarsu da azabarsu ba, amma domin matakin nan muhimmin ne ga nasararsu a karshe. Ba zai iya, bisa ga darajarsa, ya kare su daga jaraba ba, gama ainihin manufar jarabarsu ita ce don shirya su ki dukan jarabobin mugunta.

Ko miyagun mutane ko aljannu ba za su iya hana aikin Allah ba, ko kuma su rufe shi daga kasanchewa da mutanensa, idan da zukatan tuba da saukin kai, za su furta su kuma rabu da zunubansu, cikin bangaskiya kuma su karbi alkawuransa. Kowace jaraba, kowane tasiri mai-hamayya, bayananne ko na sirri, za a iya kin sa, “Ba ta wurin karfi ba, ba kwa tawurin iko ba, amma tawurin ruhuna, in ji Ubangiji Mai-runduna.” Zakariya 4:6.

“Gama idanun Ubangiji suna bisa masu-adilchi, kunnuwansa kuma suna bude ga jin rokonsu:… Wanene shi da za ya yi maku ta’adda kuma, idan kuna da himma domin nagarta?” 1Bitrus 3:12,13. Sa’anda Balaam, don kwadahin arziki, ya yi duba game da Israila, kuma tawurin hadaya ga Allah ya so ya jawo la’ana kan mutanensa, Ruhun Allah Ya hana muguntan da ya so ya ambata, dole kuma Balaam ya ce: “Ya ya zan la’anta wadanda Allah ba Ya la’anta ba? Yaya zan yi kirarin reni ga wadanda Ubangiji ya yi ba?” “Bari in mutu irin mutuwar mai-adilchi, bari karshena ya zama kamar nasa!” Bayan an sake yin hadaya kuma annabin nan mara-biyayya ga Allah ya ce: “Ga shi na karbi umurni in sa albarka; shi ya albarkache, ni kwa ba ni da iko in juyas. Ba ya ga mugunta a chikin

Yakub ba, baya kwa ga shiririta chikin Israila ba; Ubangiji Allahnsa yana tare da shi, sowa su ke yi domin sarki." "Ba wani magani da za ya chiwuchi Yakub; ba wani dabo da za ya chiwuchi Israila; yanzu fa za a bayana ma Yakub da Israila abin da Allah ya aika!" Duk da haka an shirya wurin hadaya, so na uku, Balaam kuma ya sake kokarin la'antawa. Amma daga lebunan annabin, ba da sonsa ba, Allah Ya bayana ci gaban zababbunsa, ya kuma tsauta ma wauta da muguntar magabtansu. Ya ce: "Mai-albarka ne dukan wanda ya albarkace ka, la'antache ne dukan wanda ya la'antadda kai." Littafin Lissafi 23:8,10,20,21-23; 24:9.

Mutanen Israila a wannan lokacin suna biyayya ga Allah, kuma muddan sun ci gaba suna biyayya ga dokarsa, ba wani iko a duniya ko lahira da zai yi nasara bisan su. Amma la'anan da ba a ba Balaam damar furtawa kan mutanen Allah ba, a karshe ya yi nasara ya furta shi akansu ta wurin rinjayarsu zuwa cikin sunubi. Sa'anda suka ketare dokokin Allah, suka raba kansu da Shi, aka kuma bar su su ji ikon mai-hallakaswan.

Shaitan ya sani sarai cewa mutum mafi-kumamanci da ke cikin Kristi ya fi karfin rundunonin duhu, kuma ya san cewa idan ya bayana kansa a fili, za a tare shi, a ki shi. Saboda haka yakan nemi janye mayakan giciyen daga mafakarsu, yayinda yake boye yana jira tare da dakarunsa, suna jira su hallaka duk wanda ya shiga yankinsa. Ta wurin dogara ga Allah da biyayya ga dukan dokokinsa ne kadai za mu iya samun tsaro.

Ba wanda ke da rashin hatsari, na rana daya ko sa'a guda in ba addu'a. Musamman, ya kamata mu roki Ubangiji hikimar fahimtar maganarsa. A nan an bayana dabarun majarabcin da hanyoyin da za a iya nasaran kansa. Shaitan kwararre ne wajen fadin nassosi, yana ba da fasara ta sa garesu ta yadda ya ke so ya sa mu tuntube. Ya kamata mu yi nazarin Littafin da tawali'un zuciya, kada mu taba manta dogararmu ga Allah. Yayin da dole ne a kullum mu yi hankali da dabarun Shaitan, ya kamata mu yi addu'a cikin bangaskiya kowane lokaci cewa: "Kada ka kai mu chikin jaraba."

Babi na 33—Babban Rudi na Farko

Da tarihin farko na mutum, Shaitan ya fara kokarin sa na rudin yan Adam. Shi wanda ya ta da tawaye a sama ya so ya sa mazaunan duniya su hada hannu da shi cikin yakinsa da gwamnatin Allah. Adamu da Hauwa'u sun yi farinciki cikin biyayya da dokar Allah, wannan kuma ya zama shaida kullum sabanin zargin da Shaitan ya yi a sama, cewa dokar Allah ta danniya ce kuma tana sabani da jin dadin halittunsa. Bugu da kari, Shaitan ya yi kishin kyakyawan gidan da aka shirya ma Adamu da Hauwa'u, marasa zunubi. Ya kudurta zai jawo faduwarsu, domin bayan ya raba su da Allah ya kuma kawo su kalkashin ikonsa, zai iya samun mallakar duniya ya kuma kafa mulkinsa a nan, inda zai yi sabani da Madaukaki.

Da Shaitan ya bayana kansa da ainihin halinsa da an tare shi nan da nan, gama an rigaya an gargadi Adamu da Hauwa'u game da mugun magabcin nan; amma ya yi aiki cikin duhu ne, ya boye manufarsa, domin ya cimma burinsa. Sa'an da ya yi anfani da maciji, wanda a lokacin nan halitta ne mai-kyaun gani sosai, sai ya ce ma Hauwa'u: "Ko Allah ya che, baza ku chi daga dukan itatuwa na gona ba?" Farawa 3:1. Da Hawa'u ba ta shiga musu da majarabcin ba, da ba ta sami damuwa ba, amma ta shiga hira da shi ta kuwa shiga tarkon dabarunsa. Har yanzu ma haka ne ake rinjayar mutane da yawa. Su kan yi shakka suna musu game da umurnin Allah, kuma maimakon biyayya ga dokokin Allah, su kan karbi ra'ayoyin mutane, wadanda ke badda kaman dabarun Shaitan.

"Sai machen ta che ma machijin, daga 'ya'yan itatuwan gona an yarda mamu mu chi; amma daga 'ya'yan itache wanda ke chikin tsakiyar gona, Allah Ya che, ba za ku chi ba, ba kwa za ku taba ba, domin kada ku mutu. Sai machijin ya che ma machen, Ba lallai za ku mutu ba; gama Allah ya sani ran da kuka chi daga chiki, ran nan idanun ku za su bude, za ku zama kamar Allah, kuna sane da nagarta da mugunta." Aya 2-5. Ya ce za su zama kamar Allah, su sami hikimar da ta fi ta da, su kuma sami yanayin rayuwa da ya fi na da. Hawa'u ta amince da jaraba kuma ta wurin tasirinta, ta jawo Adamu cikin zunubi. Sun yarda da kalmomin macijin, cewa Allah bai nufi abinda ya fada ba; basu gaskata Mahalicinsu ba, suka ga kamar yana rage 'yancin su ne kuma cewa za su iya samun hikima mai-yawa da daukaka tawurin ketare dokarsa.

Amma mene ne Adamu, bayan zunubinsa, ya gane cewa kalmomin nan "chikin rana da ka chi, mutuwa zaka yi lallai" ke nufi? Ko ya ga cewa su na nufin abin da Shaitan ya ce masu ne, cewa za a kai shi cikin yanayin rayuwa mafi girma ne? In da haka ne, da ketare dokar Allah ya zama da riba sosai, da Shaitan kuma ya zama babban mai-taimakon zunubin mutum, za ya koma kasa daga inda aka ciro shi; "Gama turbaya ne kai, ga trubaya za ka koma." Aya 19. Kalmomin Shaitan "Idanunku za su bude," sun zama gaskiya ta hanya daya ne kawai; Bayan Adamu da Hawa'u sun yi ma Allah rashin biyayya, idanunsu sun

bude, suka gane wautarsu; sun san mugunta, sun kuma dandana dacin sakamakon rashin biyayya.

A tsakiyar Adnin ne itacen rai ya kasance, ‘ya’yansa kuma suna da ikon sa rai ya dawama. In da Adamu ya ci gaba da biyayya ga Allah, da ya ci gaba da cin yayan itacen rai, kuma da ya rayu har abada. Amma sa’an da ya yi zunubi, an raba shi da ci daga wannan itacen, ya kuma zama mai-mutuwa. Hukumcin Allah cewa, “turbaya ne kai, ga trubaya za ka koma,” yana Magana game da shudewar rai ne gaba daya.

Rashin mutuwa da aka yi ma mutum alkawalinsa bisa sharadin biyayya, an rasa shi ta wurin ketare doka. Adamu bai iya mika ma zuriyarsa abinda shi bai mallaka ba; kuma da ba bege domin jinsin nan na ‘yan Adam da ya fadi, ba don Allah, tawurin hadayar Dansa, ya kawo masu yiwuwar samun rashin mutuwa ba. Sa’anda “mutuwa ta bi kan dukan mutane, da shi ke duka sun yi zunubi,” Kristi “ya haskaka rai da dawama tawurin bishara.” Romawa 5:12; 2Timothawus 1:10. Kuma tawurin Kristi ne kadai ana iya samun dawama. In ji Yesu: “Wanda yana ba da gaskiya ga Dan yana da rain a har abada; amma wanda ba ya yi biyayya ga Dan ba, ba za shi ganin rai ba.” Yohanna 3:36. Kowa zai iya mallakar albarkan nan idan ya bi sharuddan. Dukan “wandada ke bidan daukaka da girma da wanzuwa ta wurin hankuri chikin aikin nagarta,” za su sami “rai na har abada.” Romawa 2:7.

Wanda kadai ya yi ma Adamu alkawalin rai cikin rashin biyayya babban mai-yaudaran nan ne. Kuma furcin da macijin ya yi ma Hauwa’u a Eden cewa: “Ba lallai za ku mutu ba.” Shi ne hudubar farko game da dawamar ran mutum. Duk da haka, wannan Magana wadda Shaitan ne tushenta, ana maimaita ta a majami’un Kirista, kuma yawancin yan Adam sun yarda da ita kamar yadda iyayen mu na farko suka yarda da ita. Hukumcin Allah cewa, “wanda ya yi zunubi shi za ya mutu” (Ezekiel 18:20), an mai da shi: Wanda ya yi zunubi ba za ya mutu ba, amma za ya rayu har abada. Abin mamaki ne yadda mutane ke maganar Shaitan suna kuma kin gaskata maganar Allah.

Da bayan faduwar mutum an ba shi damar zuwa wurin itacen rai da ya rayu har abada, ta haka kuma da zunubi ya dawama. Amma cherubim da takobi mai-hasken wuta “sun tsare hanyar itache na rai.” (Farawa 3:24), kuma ba a ba ko mutum daya daga iyalin Adamu izinin wuce shingen nan har ya ci daga ‘ya’yan itace mai-ba da rai din ba. Sabo da haka ba mai-zunibi mara mutuwa.

Amma bayan faduwar, Shaitan ya bukaci malaikunsa su yi kokari na musamman don koyar da cewa mutum mara mutuwa ne, kuma bayan an rudi mutane suka karbi karyan nan, sai su sa su su dauka cewa mai-zunubi zai rayu cikin wahala ta har abada. Yanzu sarkin duhu, ta wurin wakilansa, yana nuna cewa Allah azalumi ne mara gafara, cewa yana jefa dukan wadanda ba ya sonsu cikin lahira, yana kuma sa su dandana fushinsa har abada,

kuma cewa yayin da suke fama da azaba mai-tsanani suna kuma birgima cikin wuta ta har abada, Mahalici zai dinga jin dadin kallonsu.

Haka ne babban magabcin ke daukan halayyan da ya shafa ma Mahalici mai-kaunar ‘yan Adam. Mugunta shaidanci ne. Allah kauna ne, kuma dukan abin da ya halitta mai-tsabta ne, mai-tsarki, mai-ban sha’awa, har sai da babban dan tawaye na farko ya shigo da zunubi. Shaitan kansa ne magabcin da ke jarabtar mutum shi yi zunubi, sa’an nan ya hallaka shi in ya iya; sa’anda ya tabbatar da muguntarsa, sai ya yi murna da hallakan da ya jawo. In ya sami izni zai share dukan ‘yan Adam zuwa cikin kamarsa. Ba don shiga-tsakanin ikon Allah ba, ko dan Adam ko ‘yar Adam daya ba za su tsira ba.

Shaitan yana so ya rinjayi mutane yau, yadda ya rinjayi iyayenmu na farko, ta wurin girgiza amincewarsu da Allah da sa su yin shakkan hikimar gwamnatinsa da adalcin dokokinsa. Shaitan da ‘yan sakonsa suna nuna cewa wai Allah ya fi su mugunta ma, domin su bada hujjar muguntarsu da tawayensu. Babban mai-yaudaran yana kokarin tura ma Ubanmu na sama mumunan mugun halin nan nasa, domin ya sa a ga kamar an yi masa rashin adalci sosai da aka kore shi daga sama don bai yarda da mai-mulkin nan mara adalci ba. Yana nuna ma duniya irin ‘yancin da za su mora kalkashin mulkinsa na tawali’un sabanin bautan da matsanantan dokokin nan na Allah ke dorawa kan mutane. Ta haka yana nasara wajen rudin mutane su janye biyayyarsu ga Allah.

Ina yawan sabanin kauna da jinkai da adalci ma, da koyaswan nan cewa matattun miyagu suna shan azaba da wuta da kibritu a lahira mai-konawa har abada, cewa saboda zunuban gajerewar rayuwarsu a duniya, za su sha azaba duk tsawon rayuwar Allah. Duk da haka ana baza wannan koyaswar, kuma tana cikin kundin koyaswoyin Kirista da yawa. In ji wani masani; “Ganin azabar lahira zai kara farincikin tsarkaka har abada. Sa’an da suka ga wadansu masu yanayi iri daya da su, da aka kuma haife su ta hanya dayan, suna fama da irin wahalan nan, su kuma suka bambanta hakanan, za su gane yawan farincikin da su ke da shi.” Wani kuma ya ce: “Yayin da umurnin rashin gamsuwa ke cika har abada da fushi, hayakin azabarsu za ya yi ta hawa har abada, a idon wadanda aka yi masu jin kai, wadanda, maimakon bin tafarkin wahallalun nan za su ce, Amin, Halelluya! Yabo ga Ubangiji!”

A cikin magabar Allah, ina ne ake samun wannan koyaswar? Fansassu a sama za su rasa tausayi da jinkai ne, har ma da juyayi na mutuntaka? Za a sauya wadannan da rashin kulawa da mugunta irin na marasa mutunci ne? Babu, babu; wannan ba koyaswar Littafin Allah ba ne. Masu koyas da ra’ayoyin nan da suka gabata, ko da shi ke masana ne, watakila kuma masu fadin gaskiya ne su, amma kuma Shaitan ya rude su da dabarunsa. Yakan sa sun kasa gane Littafin, ya ba maganar Allah kamanin fushi da mugunta irin na shi Shaitan, amma ba na mahalicinmu ba. “In ji Ubangiji Yahweh, na rantse da raina, ba ni da wani jin dadi chikin mutuwar mugu ba, gwamma dai shi mugun ya juyo ga barin hanyassa, shi yi rai; ku juyo dai, ku bar miyagun halulukanku; don mi za ku mutu? Ezekiel 33:11.

Wace riba Allah zai samu in mun yarda cewa shi yana jin dadin kallon azaba mara karewa, cewa yana farinciki da ihu da birgima da zage zagen wahalalun halitun da Shi ya ke rike da su a cikin wutar jahannama? Ko munanan suruce surucen nan za su yi dadin ji a kunnen Mai-kauna mara-matuka? Ana koyar da cewa wahal da miyagu har abada zai nuna yadda Allah Ya ki jinin zunubi da shi ke mugunta ce mai-hallaka salama da odan dukan halitta. Wannan sabo ne mai-ban tsoro! Sai ka ce don Allah Ya ki jinin zunubi ne ya sa a ke yinsa. Bisa ga koyaswoyin masanan nan, ci gaba da azabatarwa ba tare da begen jin kai ba tana haukatar da masu zunubin kuma yayin da su ke bayana fushinsu ta wurin zage zage da sabo, suna kara yawan laifinsu ke nan har abada. Ba za a kara darajar Allah tawurin damuwa da ci gaba da karuwar zunubi hakanan har abada ba.

Tunanin mutum ba zai iya kiyasta yawan illan da koyaswan nan na azaba har abada ya jawo ba. Addinin Littafin, cike da kauna da nagarta, da yalwar tausayi ya kazamtu da camfi ya kuma yafa tsoro. Idan mun dubi kamanin karyan da Shaitan ya shashafa ma halin Allah, ko za mu yi mamakin yadda ake tsoron Mahalicinmu Mai-jin kai, har ma ana kinsa? Munanan ra'ayoyi da ake koyarwa a majami'u ko ina a duniya sun haifar da miliyoyin masu shakka da kafirai.

Koyaswar azaba ta har abada tana cikin koyasuyoyin da su ke cikin ruwan anab na fasikancin Babila da ta sa dukan al'ummai su sha. Ruya 14:8; 17:2. Abin mamaki ne cewa ma'aikatan Kristi sun yarda da riddan nan suna kuma koyar da shi a bagadi. Sun karbe ta daga Rum ne, yadda suka karbi Assabbat na karyan. Gaskiya kam, manyan nagargarun mutane sun koyar da ita, amma a lokacin, haske game da batun nan bai zo masu, kamar yadda ya zo mana ba. Alhakinsu game da hasken da su ke da shi ne kadai a zamaninsu; mu za mu ba da lissafin hasken zamanin mu. Idan mun juya daga shaidar maganar Allah, muka karbi koyaswoyin karya wai don iyayenmu sun koyar da su, za mu fadi cikin hukumcin Babila, muna sha daga ruwan anab na fasikancinta kenan.

Da yawa da basu yarda da koyaswar azaba ta har abada ba, suna wata kuskuren dabam kuma. Sun ga Littafin ya nuna cewa Allah mai-kauna da tausayi ne, kuma basu yarda cewa zai iya jefa halitunsa cikin wutar jahannama mai-konawa har abada ba. Amma da shike sun dauka cewa rai baya mutuwa, sai suka dauka cewa a karshe za a ceci dukan 'yan Adam kenan. Da yawa sun dauka cewa kowace barazanar Littafin an shirya ta ne domin ta razanar da mutane su yi biyayya; amma ba za a aiwatar da barazanar a zahiri ba. Don haka mai-zunubi zai iya rayuwar holewa, ya ki kulawa da umurnin Allah, duk da haka kuma ya dauka cewa Allah zai karbe shi. Irin koyaswar gangancin nan game da jin kan Allah ba tare da kula adalcinsa ba, takan gamsar da zuciyar jiki ta mutumtaka ta kuma karfafa miyagu cikin zunubansu.

Don nuna yadda masu cewa za a ceci dukan mutane su ke murda nassosi don tabbatar da koyaswoyinsu, furcinsu ma kawai ya isa. A wajen janaizan wani saurayi mara addini, wanda ya mutu nan take bayan ya gamu da hatsari, mai-wa'azin ya zabi nassin nan game

da Dauda ne, cewa: “Ya hankura domin Ammon da shi ke ya rigaya ya mutu.” Samaila II, 13:39.

Mai-maganan ya ce: “Sau da yawa ana tambaya ta, me zai faru da wadanda sukan bar duniya cikin zunubinsu, su mutu watakila ma da jinin zunibin da suka aikata a rigarsu, basu wanke ba ma, ko kuma suka mutu kamar yadda saurayin nan ya mutu bai taba furta bangaskiya ko ya dandana addini ba. Mun gamsu da nassosin; amsarsu za ta magance matsalar. Amnon mai-zunubi ne matuka; bai tuba ba, mashayi ne shi, kuma cikin buguwarsa aka kashe shi. Dawuda annabin Allah ne; ai ya san ko Amonon zai wahala ne ko zai ji dadi ne a duniya mai-zuwa. Mene ne zuciyarsa ta ce?” Ran sarki Dawuda kwa ya yi marmarin shi bi Absalom: gama ya hankura domin Amnon, da shi ke ya rigaya ya mutu.” Aya 39.

“Kuma me za a gano daga kalmomin nan? Bai nuna cewa ba zancen whala ta har abada ba cikin addininsa? Haka mu ke gani, nan kuma mun gano koyaswar da ke goyon bayan ra’ayin nan mai-gamsarwa, mai-wayewa, mafi-nuna kauna, cewa a karshe za a sami salama da tsabta ko ina. Ya hakura, ganin cewa, dansa ya mutu. Kuma don me? Domin ta wurin idon annabci ya hangi gaba ya ga dan nan nesa daga dukan jarabobi, an kubutar da shi daga bautar zunubi aka tsarkake shi daga dukan rubansa, kuma bayan an ba shi isashen tsarki, da wayewa, an karbe shi cikin taron ruhohi masu farinciki da ke can sama. Ta’aziyarsa kawai ita ce cewa tawurin cire kaunatacen dansa daga yanayin zunubi da wahala na yanzu, ya je inda za a zuba ma rayuwarsa ta duhu lumfashi mafi-daraje na Ruhu Mai-tsarki, inda za a bude ma tunaninsa hikimar sama da murna mai dadi na kauna mara matuka, ta hakanan kuma a shirya shi da yanayin tsatsarka, ya ji dadin hutu da gado na sama.

“Cikin batutuwan nan, za a gane cewa mun gaskata cewa ceton sama bai danganta ga wani abin da za mu iya yi a wannan rayuwar ba ne; kuma ba kan wata sakewar zuciya yanzu ba ce, ko kuma bangaskiya na yanzu, ko addinin da ake bi yanzu,”

Hakanan ne ma’aikacin Kristi din nan ya maimaita karyan da macijin ya furta a Adnin cewa “Ba lallai za ku mutu ba.” “Ran da kuka chi daga chiki, ran nan idanunku za su bude, za ku zama kamar Allah,” ya ce komi munin zunubin mutum: da mai-kisa, da barawo, da mazinaci, bayan mutuwa za a shirya su domin shiga salama mara-matuka.

Kuma daga mene ne mai-murda nassosin nan ya sami ra’ayinsa? Daga magana daya inda Dawuda ya bayana danganarsa ga nufin Ubangiji. Ransa “ya yi marmarin shi bi Absalom; gama ya hankura domin Amnon, da shi ke ya rigaya ya mutu.” Da shi ke zafin bakincikinsa ya ragu a hankali, tunaninsa ya koma daga wurin mamacin zuwa wurin rayayyen dan, wanda ya kori kansa don tsoron horo sabo da laifinsa. Kuma shaidar ke nan da ake anfani da ita cewa da zaran mashayi da mazinacin nan Amnon ya mutu nan da nan a ka kai shi mazamna na salama, inda za a tsarkake shi a shirya shi don ma’amala da

malaiku marasa zunubi! Wannan tatsuniya ce mai-gamsarwa kam, shiryayya da kyau domin gamsar da zuciya ta jiki na mutumtaka; wannan koyaswar Shaitan ce, kuma tana cika aikinsa da kyau. Ko ya kamata mu yi mamaki cewa mugunta tana yawaita sabo da wannan koyaswar?

Hanyar da mallamin karyan nan ya bi misali ne na wadansu da yawa. Akan raba wadansu kalmomin Littafin daga sauran nassin da yawanci yakan nuna cewa ainihin ma'anar ta saba ma fasarar da ake bayarwa; sa'an nan akan murda guntayen nassosin tabbatar da koyaswoyin da ba su da tushe cikin maganar Allah. Shaidar da aka yi anfani da ita don nuna cewa Amnon mashayi yana sama zance ne kawai da ya saba ma bayyananiyar koyaswar Littafin cewa mashayi ba zai gaji mulkin Allah ba. Korintiyawa I, 6:10. Hakanan ne masu shakka da marasa ba da gaskiya su kan juya gaskiya ta zama karya. Ann kuma rudin jama'a da yawa ta wurin dabarunsu, a lallaba su su yi barci cikin zaman lafiya irin na mutumtaka.

Da gaskiya ne cewa rayukan mutane su kan wuce kai tsaye ne zuwa sama da zaran an mutu, da za mu gwammaci mutuwa maimakon rai. Koyaswan nan ta sa mutane da yawa sun kashe kansu. Sa'anda kamuwa ko rikicewa ko yankan buri ya fi karfinsu, su kan ga kamar ya fi masu sauki su yanke rayuwarsu su tashi zuwa salamar duniya ta har abada kawai.

Allah Ya shaida cikin maganarsa cewa zai hori masu ketare dokarsa. Masu rudin kansu cewa jin kansa ya yi yawa ta yadda ba zai iya aiwatar da hukumci kan mai-zunubi ba, su dubi giciyen Kalfari ma kawai mana. Mutuwar Dan Allah shaida ce cewa "hakin zunubi mutuwa ne," cewa kowace ketarewar dokar Allah dole zai gamu da ramuwarsa. Kristi mara-zunubi ya zama zunubi sabo da mutum. Ya dauki laifin ketarewar, da boyewar fuskar Ubansa, har sai da zuciyarsa ta karye, ransa kuma ya fice. An yi dukan hadayan nan domin a fanshi masu zunubi ne. Ba wata hanya dabam kuma da za a iya kubutar da mutum daga horon zunubi. Kuma kowane mutumin da ya ki zama mai-hannu cikin kafaran da aka tanada da tsada hakanan dole zai dauki laifi da horon zunubi a jikinsa.

Bari mu dubi abin da Littafin ke koyarwa game da marasa imani da marasa tuba, wadanda masu cewa za a ceci kowane mutum ke cewa suna sama, a matsayin tsarkakan malaiku masu farinciki. "Ni ba shi daga chikin mabulbulan ruwa na rai kyauta." Ruya 21:6. Alkawalin nan ga masu kishi ne kawai-sai masu jin cewa suna bukatar ruwan rai, suna kuma neman shi fiye da dukan sauran ababa, za a ba su." "Wanda ya yi nasara za ya gada wadannan abu, in zama Allahnsa kuma, shi zama da na." Aya 7. Nan ma an ba da sharudda. Domin mu gaji dukan abu, dole sai mun ki zunubi mu ka yi nasara da shi kuma.

Tawurin annabi Ishaya, Ubangiji ya bayana cewa: "Ku ambaci mai-adilchi, ku che, Dadi za ya ji." "Kaiton mai-mugunta! Wuya za ya sha; gama aikin hannuwansa za a saka masa." Ishaya 3:10,11. Mai-hikiman yace: "Mai-zunubi ya yi mugunta sau dari, har ma ya

dade a duniya, duk da haka na sani lallai, wadanda ke tsoron Allah za su zama lafiya, masu-iabda ke nan; amma babu lafiya ga miyagu." Mai-wa'azi 8:12,13. Bulus kuma ya sahida cewa mai-zunubi yana tanada ma kansa "fushi chikin ranar fushi da bayannuwar hukumchi mai-adilchi na Allah, shi da za ya saka ma kowane mutum gwalgwadon ayukansa;" "tsanani da azaba a kan kowane ran mai-aika mugunta." Romawa 2:5,6,9.

"Da mai-fasikanchi, da mutum mai-kazamta, da mutum mai-sha'awa, watau mai-bautan gumaka ke nan, duk basu da gadon komi chikin mulkin Kristi na Allah." Afisawa 5:5, "Ku nemi salama da dukan mutane, da tsarkakewa wadda babu mutum da za shi ga Ubangiji im ba tare da ita ba: Ibraniyawa 12:14. "Masu-albarka ne wadannnan da ke wankin tufafinsu, domin su sami iko su zo wurin itachen rai, su shiga kuma ta kofofi chikin birni. Daga waje da karnuka, da masu-sihiri, da fasikai, da masu-kisan kai, da masu-bautan gumaka, da dukan wanda yana kamnar karya yana kwa aikata ta." Ruya 22:14,15.

Allah ya ba mutane bayanin halinsa da na hanyar da yake bi da zunubi. "Ubagiji, Allah ne chike da juyayi, mai-alheri kuma, mai-jinkirin fushi, mai-yalwar jinkai da gaskiya, yana tsaron jinkai domin dubbai, yana gafarta laifi da sabo da zunubi; ba shi kubutadda mai-laifi ko kadan." Fitowa 34:6,7. "Za ya hallaka dukan miyagu." "Masu-zunubi fa za a hallaka su gaba daya: za a datse karshen miyagu." Zabura 145:20; 37:38. Za a yi anfani da karfin gwamnatin Allah da ikonsa don kwantar da tawaye; duk da haka dukan nuna adalci tawurin ramuwa ba zai saba ma halin Allah na jin kai da tsawon jimrewa da kauna ba.

Allah baya tilasta mutuwa ba ya son biyayya irin na bayi. Yana so halitunsa su kaunace Shi domin ya cancanci kauna ne. Yana so su yi masa biyayya domin sun gane hikimarsa, da adalci da kaunarsa ne. Kuma wadanda ke da kyakyawar ganewar halayyan nan za su kaunace Shi domin suna sha'war halayyan nasa ne.

Halayyan alheri da jinkai da kauna da Mai-ceton mu Ya koyar Ya kuma kwatanta hoto ne na halin Allah da nufinsa. Kristi ya bayana cewa bai koyar da komi ba sai abinda ya karba daga wurin Ubansa. Kaidodin gwamnatin Allah suna da cikakkiyar jituwa da umurnin mai-ceton cewa "Ku yi kaunar magabtanku." Allah yana aiwatar da hukumci kan miyagu, domin dukan halitta ta anfana, har ma domin wadanda aka hukumta din su anfana ne. Zai ba su farinciki idan zai iya yin hakan bisa ga dokokin gwamnatinsa da adalcin halinsa ne. Yana kewaye su da alamun kaunarsu, yana ba su sanin dokarsa, ya kuma bi su da tayin jin kansa; amma suna rena kaunarsa, su wofinta dokarsa, su kuma ki jin kansa. Yayin da kullum suna karban baye bayensa, suna cin mutuncin mai-bayarwan; sun ki Allah domin sun san yana kyamar zambansu. Ubangiji yana tsawon jimrewa da zunubansu; amma sa'ar hukumcin za ta zo a karshe, sa'an da za a tabbatar da karshensu. Ko a lokacin shi zai daura 'yan tawayen nan a jikinsa ne? Zai tilasta su yin nufinsa ne?

Wadanda suka zabi Shaitan ya zama shugabansu, suka kuma kasance kalkashin ikonsa ba su shirya shiga wurin Allah ba. Girman kai, yaudara, anishuwa da zalunci sun kafu cikin

halayensu. Za su iya shiga sama su kasance tare da wadanda suka rena suka kuma ki jininsa a duniya? Gaskiya ba za ta taba burge makaryaci ba. Tawali'u ba zai gamsar da mai-daga kai da girman kai ba; tsabta ba za ta karbu ga mara-kirki ba. Kauna zalla ba ta burge mai-son kai. Wane irin jin dadi ne sama za ta iya ba wadanda sun dukufa cikin son kai da kayan duniya?

Da wadanda suna rayuwar tawaye ga Allah za su iske kansu a sama faraf daya, su ga yanayin cikakken tsarki da ke wurin, yadda kowa yana cike da kauna, kowace fuska tana walkiya da farinciki, ga muzika mai dadi yana daukaka Allah da Dan ragon, haske mara iyaka kuma yana zubowa kan fansassu daga fuskar shi wanda ke zaune kan kursiyin, ko su ga wadanda zukatansu ke cike da kiyayya ga Allah da gaskiya da tsarki, za su iya cudanya da taron mutanen da ke sama su kuma sa baki cikin wakokin yabon su? Za su iya jimre darajar Allah da Dan ragon? Babu, babu, an ba su shekaru na damar samun halayya irin na sama, amma basu taba horar da tunanin su ya kaunaci tsarki ba; basu taba koyon harshen sama ba, yanzu kuma lokaci ya kure. Rayuwar tawaye ga Allah ta sa ba su cancanci sama kuma ba. Tsabtar sama da tsarkinta da salamar ta za su zama wuta mai-cinyewa. Za su so su gudu daga wuri mai-tsakin nan. Za su gwammaci hallaka, domin su buya daga fuskar wanda ya mutu domin shi fanshe su. Karshen miyagu ya tabbata bisa ga sabon su ne. Rashin kasancewarsu ganin daman su ne, kuma adalci ne da jinkan Allah.

Kamar ruwan Tufana, wutar babban ranan tana bayana hukumcin Allah ne cewa miyagun ba su da magani. Ba sa so su ba da kai ga mulkin Allah. Sun zabi tawaye, kuma sa'anda rai ya kare, lokaci ya kure da za a juya tunaninsu, daga zunubi zuwa biyayya, daga kiyayya zuwa kauna.

Tawurin barin ran Kayinu mai-kisankai, Allah Ya ba duniya kwatancin sakamakon barin mai-zunubi ya rayu ya ci gaba da zunubi ba sassauci. Ta wurin tasirin koyaswar Kayinu da kwtancinsa, zuriyarsa da yawa chikin duniya, kuma kowache shawara ta tunanin zuchiyassa mugunta che kadai kullayaumi. "Duniya kwa ta bachi a gaban Allah, duniya kuma ta chika da zalumchi." Farawa 6:5, 11.

Cikin jin kai ga duniya, Allah Ya shafe miyagun mazamnanta a lokacin Nuhu. Cikin jin kai ya shafe mazamnan Sodom. Ta wurin ikon yaudarar Shaitan, masu aikata zunubi suna samun tausayawa da sha'awa, ta haka kuma kullyaumi suna kai wadansu ga tawaye. Haka ya kasance lokacin Kayinu da lokacin Nuhu, da kuma lokacin Ibrahim da Lot; inda yake a lokacin mu. Cikin jin kai ga dukan halitta ne a karshe Allah za ya hallaka masu kin alherinsa.

"Hakin zunubi mutuwa ne; amma kyautar Allah rai na har abada ce tawurin Kristi Yesu Ubangijin mu." Romawa 6:23. Yayin da da rai gadon masu adalci ne, mutuwa ladar miyagu ce. Musa ya bayana ma Israila cewa: "Duba a gabanku na sa rai da nagarta, mutuwa da mugunta." Kubawar Sharia 30:15. Mutuwa da ake magana a nassosin nan ba wadda a

ka furta ma Adamu ba ce, domin dukan ‘yan Adam suna shan horon zunubinsa. Mutuwa ta biyu ce a ke bambanta ta da rai madawami.

Sanadiyar zunubin Adamu mutuwa ta bi kan dukan ‘yan Adam. Kowa yana zuwa kabari. Kuma ta wurin tanadin shirin ceto, za a kawo kowa daga kabarinsa. “Za a yi tashin matattu na masu-adalci da na marasa-adilchi.” “Gama kamar yadda chikin Adamu duka suna mutuwa, hakanan chikin Kristi duka za su rayu.” Ayukan 24:15; Korintiyawa I, 15:22. Amma an bambanta tsakanin kashi biyu na masu tashin. “Dukan wadanda suna chikin kabarbaru za su ji muryatasa, su fito kuma; wadanda sun yi nagarta su fito zuwa tashi na rai, wadanda sun yi mugunta, zuwa tashi na shari’a.” Yohanna 5:28,29. Wadanda aka ga sun cancanci tashi na rai masu albarka ne, masu-tsarki. “Mutuwa ta biyu ba ta da iko bisansu.” Ruya 20:6. Amma wadanda basu sami gafara, ta wurin tuba da bangaskiya ba dole za su karbi horon zunubi, watau “hakin zunubi.” Za su sha horo, kowa da tsawon horonsa da zurfin horonsa kuma dabam, “gwalgwadon aikinsa,” amma za su karasa da mutuwa ta biyu. Da shi ke ba shi yiwuwa ma Allah, daidai da adalcinsa da jinkansa, ya ceci mai-zunubi cikin zunubinsa, zai hana shi kasancewarsa, wanda zunubansa suka hana shi, wanda kuma shi kansa ya nuna cewa bai cancance shi ba. Wani nassi ya ce: “Gama in an jima kadan, sa’an nan mai-mugunta ba shi; hakika da anniya za ka duba wurin zamansa, ba kwa za ya kasance ba.” Wani kuma ya ce za “su zama sai ka che basu taba kasanchewa ba.” Zabura 37:10; Obadiah 16. Yafe da rashin daraja, za su nutse zuwa cikin bata, ba bege har abada.

Hakanan ne za a kawo karshen zunubi da dukan hallaka da kaito da ya haifar, mai-zabura ya ce; “Ka hallakadda miyagu, ka shafe sunansu har abada abadin. Abokan gaba sun kare sarai, sun zama kango har abada.” Zabura 9:5,6. Yohanna cikin Ruya, sa’anda ya hangi gaba zuwa yanayi na har abdada ya ji wata wakar yabo ta dukan halitta, wadda ko kuskure daya babu. An ji kowace halitta sama da duniya tana ba Allah dukan daraja. Ruya 5:13. Lokacin babu batacen rai ko daya balle a yi ma sunan Allah sabo ma, yayin da batattu suke birgima cikin azaba mara karewa; ba wahallu a lahira da za su garwaye ihunsu da wakokin cetattu.

Koyaswar cewa matattu sun san abin da ke faruwa ta kafu kan babban kuskuren nan ne cewa rai ba ya mutuwa, koysawar da ke sabani da koyaswoyin Littafin da bisira da kuma tausayi da juyayinmu na ‘yan Adam. Bisa ga koyaswar, fansassu a sama sun san duk abin da ke faruwa a duniya, kuma musamman ma da abokansu da suka bari a duniya. Amma ta yaya matattu za su yi farincikin sanin matsalolin masu rai, su ga zunuban da kaunatattunsu ke aikatawa, su kuma gan su suna jimre dukan bakinciki da yankan buri da azabar rayuwa? Ina yawan salamar sama da wadanda ke famar zagayar ‘yan-uwansu a duniya za su ji? Kuma dubi munin koyaswan nan cewa da zaran lumfashi ya bar jiki a kan jefa ran mara tuba cikin wutar jahannama nan da nan! Wane irin zurfin bakin ciki za a jefa wadanda ke

ganin abokansu suna wucewa zuwa kabari ba shiri, su shiga madawamin kaito da zunubi! Da yawa sun shiga tabin hankali sabo da wannan tunanin.

Mene ne littafin ke fadi game da ababan nan? Dauda Ya ce mutum bai san komi ba in ya mutu: “Lumfashinsa ya kan fita, ya kan koma turbayassa kuma; a chikin wannan rana shawarwarinsa sukan lalache.” Zabura 146:4. Solomon ya ba da shaida dayan: “Gama masu-rai sun san za su mutu, amma matattu basu san komi ba.” “Kamnarsu duk da kiyayyarsu, da kishinsu, yanzu sun kare; basu kwa da wani rabo har abada a chikin komi da a ke yi a chikin duniya.” “Babu wani aiki, ko dabara, ko ilimi, ko hikima, chikin kabari inda za ka.” Mai-wa’azi 9:5,6,10.

Sa’anda aka amsa addu’ar Hezekiah ta wurin tsawaita ransa da shekara goma sha biyar, sarkin ya raira ma Allah wakar yabo sabo da girman jinkansa. Cikin wakar, ya ba da dalilin murnarsa; “Gama kabari ba shi da iko shi yi yabonka, mutuwa ba ta iya daukaka ba. Wadanda suna gangarwa chikin rami basu iya begen gaskiyarka ba. Mai-rai, mai-rai, shi ne za ya yi yabonka, kamar yadda ni ke yi yau.” Masana da yawa suna koyar da cewa matattun tsarkaka suna sama yanzu, cikin salama suna yabon Allah da harshe mara mutuwa, amma Hezekiah bai ga matattu da irin darajan nan ba. Mai-zabura ya yarda da maganarsa. Ya ce: “Gama chikin mutuwa babu tunawa da kai; a chikin lahira wa za ya yi maka godiya?” “Matattu ba su yabon Ubangiji ba, babu mai-yabonsa kuma chikin masu-gangarawa wurin shuru.” Zabura 6:5. 115:17.

A ranar Pentecost Bitrus ya ce Dawuda “ya mutu, aka bizne shi, kabarinsa kwa a wurin mu yake har wayau.” “Gama Dawuda ba ya hau zuwa chikin sammai ba.” Ayukan 2:29,34. Kasancewar Dawuda cikin kabari har sai tashin matattu ya tabbatar da cewa matattu ba sa zuwa sama da zaran sun mutu. Ta wurin tashin matattu ne kawai, da kuma cewa Kristi ya tashi, Dawuda zai iya zama a hannun daman Allah.

Bulus kuma ya ce: “Gama idan ba a ta da matattu, ba a ta da Kristi kuma: idan kwa ba a ta da Kristi ba, bangaskiyarku kuma banza che: har yanzu ku na chikin zunubanku. Har wadannan ma da sun yi barchi chikin Kristi sun lalache.” Korintiyawa I, 15:16-18. Idan an yi shekara dubu hudu matattun masu adalci suna zuwa sama kai tsaye da zaran sun mutu, ta yaya Bulus zai ce idan ba tashin matattu “wadannan ma da sun yi barchi chikin Kristi sun lalache”? Ba anfanin tashin matattu ke nan.

Game da yanayin matattu, Tyndale ya ce: “Na furta a sarari, cewa ban gamsu cewa sun rigaya sun sami cikakkiyar daraja da Kristi ke ciki ba, ko wadda malaikun Allah ke ciki ba; ba kuma bangaskiya ta ke nan ba, domin da haka ne, da wa’azin tashin matattu ya zama aikin banza.”

Hakika, begen albarka mara matuka da zaran an mutu ya kai ga rabuwa da koyaswar Littafin game da tashin matattu. Game da wannan Dr. Adam Clarke ya ce: “Kirista na da sun ba da muhimmanci ga koyaswar tashin matattu fiye da yanzu. Kaman yaya? Manzanin

sun dinga nanata shi, suna ingiza masu bin Allah su yi kwazo, da biyayya da fara'a, tawurin koyaswan nan. Magadansu a wannan zamani kuma ba su cika ambaton shi ba. Manzani sun yi wa'azinsa, Kirista na da kuma sun gaskanta; haka mu ke wa'azinsa, haka kuma masu sauraronmu su ke gaskatawa. Ba wata koyaswar bishara da aka fi karfafawa kamar wannan; kuma ba koyaswar da aka fi yi mata kyaliya a zamanin nan kamar wannan!

Wannan ya ci gaba har sai da gaskiyan nan na tashin matattu ta kusan shudewa Kirista kuma suka manta da ita. Don haka, wani shahararren mawallafi na addini cikin sharhinsa game da maganar Bulus cikin Tassalunikawa I, 4:13-18 ya ce: "Sabo da kowane dalili na ta'azantarwa, koyaswar rashin mutuwar masu-adalchi yana sauya mana duk wata koyaswa da ba a tabbatar ba game da zuwan Ubangijinmu na biyu. Da zaran mun mutu, Ubangiji ya zo mana. Abin da ya kamata mu yi tsaro mu jira ke nan. Matattu sun rigaya sun wuce zuwa daraja. Ba sa jiran haho kafin hukuncinsu da alabrkarsu."

Amma gaf da tafiyar a daga almajiransa, Yesu ba ya ce masu za su zo wurinsa jima kadan ba. "Gama zan tafi garin in shirya maku wuri" Ya che; "kadan na tafi na shirya maku wuri ni ma, sai in sake dawowa, in karbe ku wurin kaina." Yohanna 14:2,3. Bulus kuma ya kara fada mana cewa; "Ubangiji da kansa za ya sabko daga sama, da kira mai-karfi, da muryar sarkin malaiku, da kafon Allah kuma; matattun da ke chikin Kristi za su fara tashi; sa'an nan mu da mu ke da rai, mun wanzu, tare da su za a fyauche mu zuwa chikin gizagizai, mu tarbi Ubangiji a sararin sama; hakanan za mu zamna har abada tare da Ubangiji." Ya kara da cewa: "Domin wannan fa ku yi ma junanku ta'aziya da wadannan magana." Tassalunikawa I, 4:16-18. Dubi yawan bambanci tsakanin kalmomin ta'aziyan nan da na wani mai-wa'azin nan da mun rigaya mun karanta can baya! Shi ya ta'azantar da abokan mamacin da tabbacin cewa, komi munin zunubin mamacin, da zaran ya ja lumfashinsa na karshe a nan, za a karbe shi cikin malaikun. Bulus yana jan hakulan ya-uwan ga zuwan Ubangiji nan gaba, sa'anda za a bude kabarbura, matattun da ke cikin Kristi kuma za a tashe su zuwa rai madawami.

Kafin a shiga wuraren zaman tsarkaka, dole sai an bincika rayuwarsu, halayensu da ayukansu kuma za su bayana a gaban Allah domin bincike. Za a shar'anta kowa bisa ga ababan da aka rubuta cikin littattafan ne, a kuma ba su lada gwalgwadon ayukansu. Ba lokacin da an mutu a ke shari'an nan ba. Lura da maganar Bulus: "ya sanya rana, inda za ya yi ma duniya duka shari'a mai-adilchi ta wurin mutum wanda ya kadara; wannan fa ya ba da shaidassa ga mutane duka, yayinda ya tashe shi daga matattu." Ayukan 17:31. A nan manzon ya bayana a sarari cewa an ayyana lokaci musamman domin sha'anta duniya.

Yahuda ya yi zancen lokaci dayan. Yace: "Malaiku kuma wadanda ba su rike matsayi nasu ba, amma suka rabu da nasu wurin zama, ya tsare su chikin madawaman sarkoki a chikin dufu zuwa hukumchin babbar ranar." Ya kuma maimaita kalmomin Enock cewa: "Ku duba ga Ubanguji ya zo da rundunan tsarkakansa, garin ya hukumta shari'a bisa dukan mutane." Yohanna ya ce ya "ga matattu kuma, kanana da manya suna tsaye a gaban

kursiyin, aka bude litattafai,… aka yi ma matattu shari'a kuma bisa ga abinda aka rubuta chikin litattafai." Ruya 20:12.

Amma idan matattu suna morar dadin sama yanzu ko kuma, suna birgima cikin wutar jahannama, wane anfani ne hukumci zai yi kuma? Koyaswoyin maganar Allah game da muhimman batutuwan nan a bayane suke, kuma ba sabani tsakaninsu, kowane mutum zai iya fahimtarsu. Amma wane mai-fadin gaskiya ne zai ga adalci ko hikima cikin ra'ayin da ake bazawa yanzu? Ko masu-adalchi, bayan an bincika shari'arsu, za su sami amincewan nan cewa; "Madalla kai bawan kirki mai-aminchi,… ka shiga chikin farinzuchiyar Ubangijinka," alhali tuntuni ma suna kasancewa tare da shi, watakila ma har tsawon sararaki masu yawa? Ko za a kira miyagu daga wurin azaba domin su karbi hukumci daga wurin Mai-shari'an dukan duniya, cewa: "Ku rabu da ni ku la'antattu, zuwa chikin wuta ta har abada?" Matta 25:21,41. Wace irin ba'a ke nan! Wofinta hikimar Allah da adalcinsa kawai!

Koyaswar rashin mutuwar mai-rai ta na cikin koyaswoyin karya da Rum ta aro daga kafirci ta kawo cikin addinin Kirista. Martin Luther ya danganta ta da tatsuniyoyi miyagu da aka hada cikin dokokin Rum. Game da furcin Solomon cikin Mai-wa'azi cewa matattu basu san komi ba, Luther ya ce: "wani wuri ke nan da ya nuna cewa matattu basu san komi ba. Ya ce ba alhaki, ba kimiya, ba sani, ba hikima a wurin. Solomon ya ce matattu suna barci, kuma ba sa jin komi sam. Gama matattu suna kwance a wurin, ba sa kirga kwanaki ko shekaru, amma idan aka tashe su, za su ga kamar barcin minti daya kadai suka yi."

Ba inda Littafin ya ce masu adalci su kan je wurin ladarsu, ko kuma miyagu sukan je wurin horonsu lokacin mutuwa. Ubanin iyaye da annabawa basu ba da wannan tabbacin ba, Kristi da manzanin basu ba da alamar hakan ba. Littafin yana koyar da cewa matattu ba sa zuwa sama nan da nan. Yana nuna cewa suna barci ne har sai tashin mattattu. Tassalunikawa I, 4:14; Ayuba 14:10-12. Ranar da "igiyar azurfa ta katse, tasar zinariya kuma ta fashe" (Mai-wa'azi 12:6), tunanin mutum yakan lalace. Wadanda ke gangarawa kabari shuru su ke. Ba su san komi kuma game da abin da ake yi a duniya ba. Ayuba 14:21. Hutu mai-albarka don gajiyayyun adilai! A gare su lokaci komi tsawo ko gajartarsa dan guntun lokaci ne. "Gama kafo za shi yi kara, matattu kuma za su tashi marasa-rubuwa,… Amma sa'anda wannan mai-rabuwa ya rigaya ya yafa rashin ruba, wannan mai-mutuwa kuma ya yafa rashin mutuwa, sa'an nan wannan batun da aka rubuta za ya tabbata cewa an hadiye mutuwa a nasarche." Korintiyawa 15:52-54.

Yayinda aka kirawo su daga barcinsu mai-nauyi, za su fara tunani daga inda su ka tsaya ne. Abu na karshe da suka sani shi ne abin da ya kashe su; tunani na karshe shi ne cewa suna faduwa zuwa kalkashin ikon kabari. Sa'an da su ka tashi daga kabari, za a maimaita tunanin su na farko mai tarin murna cikin ihun nan na nasara cewa: "Ya mutuwa, ina nasarakki, ya mutuwa ina karinki?" Aya 55.

Babi na 34—Ko Mattatu Za Su Iya Magana da Mu?

Hidimar malaiku masu-tsarki, bisa ga Littafin, gaskiya ce mafi-ta'azantarwa mai-daraja kuma ga kowane mai-bin Kristi. Amma an duhunta koyaswar Littafin game da wannan batu aka kuma bata shi tawurin kura-kuran koyaswar yawancin masanan ilimin tauhidi. Koyaswar yanayin rashin mutuwa, wadda aka fara aronta daga kafirci, aka kuma shigar da ita cikin addinin Kirista a zamanin duhun nan na babban ridda, ya kawar da gaskiyanda Littafin ke koyarwa a bayane cewa "matattu ba su san komi ba." Jama'a da yawa sun ba da gaskiya cewa ruhohin matattu ne "ruhohi masu-hidima ne, aikakku domin su yi hidima sabili da wadanda za su gaji cheto." Wannan kuma duk da shaidar Littafin game da kasancewar malaiku na sama, da dangantakarsu da tarihin mutum, kafin ma mutuwar Habila.

Koyaswar cewa matattu sun san abin da ke faruwa, musamman zancen cewa wai ruhohin matattu su kan dawo su yi ma masu rai hidima, ta shirya hanya domin sihiri na zamani. Idan ana shigo da matattu wurin Allah da malaiku masu tsarki, suna kuma da sanin da ya zarce wanda su ke da shi da, don ma baza su dawo duniya su koyar da masu-rai su kuma gargade sub a? idan ruhohin matattu sun a zagaya abokan su a duniya, don me baza a basu izini suyi sadarwa da su, su gargade su game da mugunta, ko kuma su ka'azantar da su cikin bakinciki ba? Ta yaya wadanda sun gaskata cewa matattu suna sane da abinda ke faruwa za su ki abin da ke zuwa masu a sunan hasken Allah wanda ruhohi ke kawo masu? Wannan hanya ce da a ke gani kamar mai-tsarki ce, wadda Shaitan ke anfani da ita don cim ma manufofin sa. Fadaddun malaukuda su ke bin nufin sa sukan bayyana kamar yan sako ne daga duniyar ruhohi. Yayin da su ke kirarin cewa suna hada adarwa tsakanin masurai da matattu, sarkin mugunta yana aikin rudarwar sa a zukatan mutansu.

Yana da iko ya kawo ma mutane kamanin abokansu da suka mutu. Jabun yakan yi daidai da ainihin; kamanin da kalmomin, da muryarsu sukan yi daidai da na mamacin. Mutane da yawa su kan ta'azantu da cewa kaunatattun su suna jin dadin salamar sama, kuma su kan saurari "ruhohi na rudami da koyaswar aljannu."

Idan aka sa su sun gaskata cewa da gaske ne matattu suna dawowa su yi sadarwa da su, Shaitan yakan sa wadanda sun je kabari ba a shirye ba su bayana. Su kan ce suna murna a sama har ma suna da manyan matsayi a can, don haka ana koyar da kuskuren nan ko ina cewa ba a bambanta masu-adalci da miyagu. Bakin karyan nan daga duniyar ruhohi wani lokaci sukan yi kashedi da gargadi da kan kasance daidai. Sa'an nan, da sun sami karbuwa sai su gabatar da koyaswoyi da ke rage amincewan da ake yi ma Littafin. Da kamanin kulawa da lafiyar abokansu a duniya, su kan nuna kurakurai masu muni. Da shike su kan fadi abin da zai faru nan gaba daidai, wannan yakan sa a ga maganar su da kamanin gaskiya; jama'a kuma su kan yarda da koyaswoyinsu nan da nan; su kuma gaskata su gaba daya sai ka ce su ne gaskiya mafi-tsarki na Littafin. A kan kawar da dokar Allah, a rena Ruhun

alheri, a kuma mai da jinin alkawalin abu mara tsarki. Ruhohin suna musun Allahntakan Kristi su kuma sa Mahalicin ma a matsayi daya da su kan su. Ta hakanan ta wurin sabuwar sake kama babban dan tawayen yana kan yakinsa da Allah, wanda ya fara a sama ya kuma ci gabada shi a duniya yanzu samada shekara dubu shi da ke nan.

Wadansu sukan yi kokarin cewa ayukan ruhohin nan yaudara ce da dabo kawai. Amma ko da shi ke gaskiya ce cewa akan yi wani ba-duhu mai-kama da ayukan ruhohi, ana kuma nuna ainihin ikon da ya fi na mutum. Buge bugen ban mamaki da aka fara sihirin zamanin nan da shi ba sakamakon dabara ko wayon mutum ba ne, amma ayukan miyagun malaiku ne kai-tsaye, wadanda ta hakanan suka fito da rudi mafi-nasarar hallaka rayuka. Za a rudi mutane da yawa ta wurin gaskata cewa sihiri dabara ce ta mutane kawai; sa'anda suka sadu fuska da fuska da ayukan da dole su yarda cewa sun fi karfin mutum, sai a rude su, a kuma sa su karbe su a matsayin babban ikon Allah.

Mutanen nan suna manta maganar littafi game da al'ajiban da Shaitan da wakilan sa su ka aikata. Tawurin taimakon Shaitan ne 'yan dabon Fir'auna su ka iya yin kwaikwayon aikin Allah. Bulus ya shaida cewa kafin zuwan Kristi na biyu za a yi irin ayukan nan na nuna ikon Shaitan. Zuwan Ubangiji zai faru ne bayan "aikin Shaitan da dukan iko da alamu da al'ajibai na karya, da dukan rudami na rashin adalchi." 2Tasalanukiyawa 2:9,10. Manzo Yohanna kuma, yayin da yake bayana iko mai-aika al'ajiban da za a bayana a kwanakin karshe, ya ce: "yana aika alamu masu girma, har ma yana sa wuta daga sama ta sabko a duniya a gaban idanun mutane. Yana rudin mazamnan duniya kuma saboda alamun da aka ba shi shi aika." Ruya 13:13,14. Ba 'yan rudi ake maganarsu a nan ba. Za a rudi mutane ta wurin al'ajiban da wakilan Shaitan za su aikata ne ainihi, ba wanda za su yi karyan cewa za su aikata ba ne.

Sarkin duhu, wanda ya dade yana anfani da ikonsa don aikin yaudara, yana anfani da jarabobinsa kan mutane kowane iri kuma komi yanayinsu. Ga masana masu wayewa, yakan nuna sihiri cikin kamani mafi-haske da sani, ta haka kuma yakan yi nasara wajen jawo da yawa daga cikinsu zuwa cikin tarkon sa. Hakimar da sihiri ke bayarwa ita ce wadda manzo Yakub ya bayana cewa: "Ba hikima mai-sabkowa daga bisa ba, amma ta duniya che, ta jiki, ta Shaitan." Yakub 3:15. Amma babban mai-rudin yana boye wannan muddan boyewan zai fi biya masa bukata. Shi wanda ya iya bayyana saye da hasken malaikun sama a gaban Kristi a jejin da ya jarabce shi a ciki, yana zuwa ma mutane cikin yanayi mafi-ban sha'awa kamar malaikan haske. Ya kan ja hankali ta wurin kawo batututwa masu kayatarwa; yakan fito da yanayi na ban sha'awa; yakan jawo soyayya tawurin furcinsa mai-dadi da ke nuna kauna da nagarta. Yakan kai tunanin mutane wasu wurare can sama, ya sa mutane su yi fahariya da hikimarsu ta yadda har za su rena madawami, a cikin zukatansu. Babban halittan nan da har ya kai Mai-fansar duniya kan dutse mai matukar tsawo, ya kuma nuna masa dukan mulkikin duniya da darajarsu, zai gabatar da jarabobinsa ga mutane ta yadda zai dauke hankulan dukan wadanda ikon Allah bai yi masu garkuwa ba.

Shaitan yana rudin mutane yau yadda ya rudi Hawa'u a Adnin ta wurin balmar baka, ta wurin sa mata burin samun haramtacen sani, ta wurin burin daukaka kai. Son ababan nan ne ya jawo faduwarsa, tawurinsu kuma yana so ya jawo hallakar mutane. "Za ku zama kamar Allah," in ji shi, "kuna sane da nagarta da mugunta." Farawa 3:5. Sihiri yana koyar da "cewa mutum halitta mai-ci gaba ne; cewa an kadara shi ya ci gaba ne har ma zuwa har abada, zuwa wurin Allahntaka." Kuma, wai "kowace zuciya za ta shar'anta kanta ne ba wata zuciyar ba." "Hukumcin zai yi daidai, da shike hukumcin kai ne,… kursiyin yana cikin kai na." Wani mallamin sihiri ya ce: "Yan-uwa na mutane, duka da alloli ne, da basu fadi ba." Wani kuma ya ce: "Kowane adali mara kuskure Kristi ne."

Don haka, a madadin adalci da cikar Allah mara-iyaka, shi ainihin wanda ya kamata a so kwarai; a madadin cikakken adalcin dokarsa, ainihin ma'aunin mutum, Shaitan ya sa yanayin mutum na zunubi da kuskure a matsayin abu kadai da za a so kwarai, kaida na hukumci, ko misanin hali. Wannan shi ne ci gaba, ba sama-sama ba, amma kasa-kasa.

Doka ce ta yanayin tunani da ta ruhaniya kuma, cewa tawurin kallo mu kan canja. Zuciya ta kan rika daidaita kanta a hankali da ababanda aka bari ta yi binbini a kai. Takan shaku da abin da ta saba so tana kuma girmamawa. Mutum ba zai taba zarce mizaninsa na tsabta ko nagarta ko gaskiya ba. Idan son kansa ne ya fi darajantawa ba zai taba zama wani abin da ya fi hakan mughimmanci ba. Maimako, zai dinga nutsewa kasa-kasa ne. Alherin Allah ne kadai ke da ikon daukaka mutum. Idan aka bar shi shi kadai zai dinga nutsewa kasa-kasa ne kawai.

Ga mai-son anishuwa, mai-son jin dadi, mai-son sha'awa, sihiri yana nuna kansa a fili fiye da yadda yake nuna kan sag a wanda yafi wayewa, da tunani kuma. Cikin yanayin sa mafi-muni sukan sami abin da ya je daidai da ababan da su ke so. Shaitan ya kan yi nazarin kowace alamar gazawar yanayin mutum, yakan lura da zunuban da kowane mutum zai so ya aikata sa'an nan ya kan lura kada a rasa zarafin aikata zunubin. Yakan jarabci mutane su zarce kadada game da yin abinda ya halatta, ya sa su, tawurin rashin kamewa, su raunana karfin jiki da na ruhaniya. Ya hallaka, kuma yana kan hallaka dubbai ta wurin bin abin da zukatansu ke so kwarai, ta hakanan kuma yana wulakanta yanayin mutum dungum. Kuma domin shi cika aikinsa, ta wurin ruhohin cewa wai "sani na gaskiya yana aza mutum bisa kowace doka," cewa "duk abin da yana nan daidai ne," cewa "Allah ba ya hukuntawa," kuma cewa "dukan zunuban da ake yi, babu laifi." Idan aka sa mutane suka gaskata cewa marmari shi ne doka mafi-girma, cewa 'yanci dama ce, cewa kuma mutum zai-ba da lissafi ma kansa ne kawai, me zai sa a yi mamakin cewa rashawa da lalacewa sun mamaye kowace kasa? Jama'a da yawa suna karban koyaswoyin da ke ba su 'yancin biyayya ga muradan zukatansu ne. Ana makala linzamin kamewa a wuyar sha'awa, ana sa karfin tunani da na rayuwa a kalkashin halayya irin na dabbobi, Shaitan kuma yana tattara dubban masu bin Kristi cikin taronsa.

Amma bai kamata yaudarar sihiri ta rudi wani ba. Allah ya ba duniya isashen hasken da zai sa su iya gane tarkon. Kamar yadda mun rigaya mun nuna, dabarar da ta kasance harsashen sihiri ta na yaki da maganar Littafin. Littafin ya ce matattu basu san komi ba, cewa tunaninsu sun lalace; ba su da rabo cikin komi da ake yi a duniya; ba su san komi game da farinciki ko bakincikin masoyansu da ke duniya ba.

Bayan wannan, Allah Ya hana kowane irin kamanin sadarwa da ruhohi da suka tafi. A zamanin Ibraniyawa akwai wadansu irin mutane masu da'awa kamar masu sihiri na zamanin yau, cewa suna sadarwa da matattu. Amma Littafin yana kiran ruhohin nan ruhohin aljannu ne. (Dubi littafin Lisafi 25:1-3; Zabura 106:28; Korintiyawa I, 10:20; Ruya 16:14). Littafin ya ce yin zumunta da aljannu haram ne ga Ubangiji, an kuma haramta shi, da hukumcin kisa kan wanda ya aikata. Leviticus 19:31; 20:27. Sunan maita ma kawai abin kyama ne yanzu. Ana mai da zancen cewa mutane sukan iya yin ma'amala da aljannu, kamar tatsuniya ce ta zamanin Jahiliya. Amma zancen sihiri, wanda ke da miliyoyin mabiya, wadda kuma ta shiga cikin kimiya, ta kuma shiga cikin ekklesiyoyi, ta sami karbuwa kuma cikin majalisu, har ma a fadar sarakuna-wannan babban rudin falkasuwa ce, sabon bad da kma na maita da aka haramta tun da.

Ko da ba wata shaidar ainihin yanayin sihiri ma, sanin cewa ruhohin ba sa bambanta akalci da zunubi, tsakanin manzani mafi martaba da tsarki na Kristi da bayin Shaitan mafi muni. Tawurin cewa wai mutane mafi mugunta suna sama, ana kuma daukaka su a can, Shaitan ya na ce ma duniya ne: "Komi yawan muguntanka, ko ka ba da gaskiya ga Allah da Littafin ko babu, yi rayuwarka yadda ka ga dama, sama gidan ka ne." Mallaman sihirin suna cewa a takaice: "Kowane mai-aikata mugunta nagari ne a ganin Ubangiji, yana kuma farinciki da su; ko kuwa, ina Allahn hukunci?" Malachi 2:17. In ji maganar Allah: "Kaiton wadanda ke che da mugunta nagarta, nagarta kuma mugunta su ke che da ita, wadanda su kan sa dufu maimakon haske, haske kuma maimakon dufu." Ishaya 5:20.

Makaryatan ruhohin nan su kan shiga siffar manzani su karyata abin da manzanin su ka rubuta lokacin da su ke duniya. Su kan yi musun cewa Allah ne tushen Littafin, ta hakanan kuma su yaga harsashen begen Kirista su kuma bice hasken da ke bayana hanyar sama. Shaitan yana sa duniya ta gaskata cewa Littafin kage ne kawai, ko kuma dai Littafin da ya je daidai da mutanen da, amma yanzu ya kamata a rabu da shi a mai da shi tsohon yayi. Kuma yana sauya maganar Allah da maganganun ruhohinsa. Wannan hanyar ta na hannunsa ne; ta wurinta zai iya sa mutane su gasktata ba in da ya ga dama. Yana boye Littafin da ya kamata ya hukumta shi da masu bin sa; yana mai da Mai-ceton duniya kamar kowane mutum kawai. Kuma kamar yadda sojojin Romawa masu gadin nan su ka dinga b za karyan da priestoci da dattibai suka ce su baza don karyata tashin Kristi, hakanan ne masu gaskata zancen ruhohin nan ke kokarin nuna cewa babu wani abin al'ajibi game da rayuwar Mai-ceton mu. Bayan neman tura Yesu a gefe, suna jan hankula zuwa al'ajibansu, da cewa wai sun fi ababan da Kristi ke yi.

Gaskiya ce cewa yanzu sihiri yana sake kamaninsa, kuma, ta wurin boye ainihin munanan fuskokinsa, yana daukan kamanin Kiristanci. Amma zatattukansa su na gaban jama'a da dadewa, kuma suna bayana ainihin halinsa. Ba za a iya boye koyaswoyin nan ko a boye su ba.

Ko a kamaninsa a yanzu rudi ne mafi-mugunta domin da zurfin wayo a ke yinsa. Da dai, yana kayarta Kristi da Littafin, amma yanzu yana cewa wai ya amince da duka biyu din. Amma ana fassara Littafin da yadda masu zunubi ke so, ana kuma wofinta muhimman koyaswoyin sa. Ana nanata cewa kauna ce babban halin Allah, amma ana rage shi ta yadda ba a bambanta nagarta da mugunta kuma. A na boye adalcin Allah da yadda yake hukumta zunubi da sharuddan dokarsa mai-tsarki. Ana koya ma mutane su mai da dokoki goma kamar mataciyar doka. Tatsuniyoyi masu dadi, masu rudi suna jan hankula har su sa mutane su musunci cewa Littafin ne tushen bangaskiyarsu. Ana kin Kristi sosai kamar da, amma Shaitan ya makantar da idanun mutane ta yadda ba za a gane rudin ba.

Mutane kalilan ne suna da kyakyawar ganewar ikon rudi da sihiri ke da shi da hatsarin shiga kalkashin tasirinsa. Da yawa su kan shiga cikinsa domin su ga yadda yake ne kawai. Ba su yarda da shi ba, kuma zasu yi kyamar tunanin ba da kansu kalkashin mulkin ruhohin. Amma su kan sa kafa cikin haramtacen wurin, mai-hallakaswan kuma yakan yi anfani da ikonsa a kan su ba da sonsu ba. Da zaran sun ba da zukatansu gare shi sau daya, sai ya rike su cikin bauta. Ba zai yiwu, ta wurin karfin kansu, su fita daga hannunsa ba. Ikon Allah da ake samu tawurin addu'ar naciya da bangaskiya ne kadai zai iya kubutar da kamammun mutanen.

Dukan masu halayyan zunubi, ko masu sha'awar sanannen zunubi, suna neman jarabobin Shaitan ke nan. Suna raba kansu da Allah da kulawar malaikunsa, sa'an da mugun ya gabatar da jarabobinsa, ba su da kariya, kuma cikin sauki a kan kama su. Masu sa kansu cikin ikonsa hakanan ba sa gane inda za su karasa. Da zaran ya kama su, majarabcin ya kan yi amfani da su su jawo wadansu zuwa hallaka.

In ji annabi Ishaya, "Sa'anda su ka che maku, ku bidi ga masu-mabiya, ga bokaye kuma, wadanda su ke kashe murya, suna magana da dan murya kamar tsuntsu; ba ya kamata mutane su yi bida ga Allahnsu ba? A bidi ga matattu sabada masu rai? A komo bisa shari'an da shaidan! Idan basu fadi bisa ga wannan magana ba, hakika babu wayewan gari a gare su ba." Ishaya 8:19,20. Da mutane sun yarda su karbi gaskiyan da Littafin ya bayana a fili hakanan game da yanayin mutum da na matattu, da sun gane cewa sihiri aikin Shaitan ne da yake yi da kikonsa da alamu da al'ajiban karya. Amma maimakon rabuwa da zunuban da su ke so, mutane da yawa suka rufe idanunsu ga hasken su ci gaba, da sa kulawa da gargadi, yayin da Shaitan ke nannade su cikin takokinsa, har su zama nama gare shi. "Da shike ba su amsa kamnar gaskiya da za su tsira ba. Sabili da wannan fa Allah yana aike masu da aikawar sabo, har da za su gaskanta karya." Tassalunikawa II, 2:10,11.

Masu hamayya da koyaswoyin sihiri, ba da mutane kadai suke fada ba, har da Shaitan da malaikunsa ma. Sun shiga fada da mulkoki da ikoki da miyagun ruhohi a madaukakan wurare ne. Shaitan ba zai taba ba da kai ba sai dai idan ikon ‘yan sakon sama ya kore shi. Ya kamata mutanen Allah su iya tare shi yadda Mai-cetonmu Ya tare shi, da kalmomin nan: “An rubuta.” Shaitan zai iya maimaita Littafin yanzu kamar zamanin Kristi, kuma zai karkata koyaswoyinsa domin shi tabbatar da yaudararsa. Dole masu rai a wannan mawuyacin lokacin su gane shaidar Littafin domin kansu.

Da yawa za su fuskanci ruhohin aljannu cikin siffar kamnatattun yanuwa da abokansu da suka mutu, masu baza ridda mai-hadarin gaske. Aljannun za su yi mana fadanci sosai su kuma aikata al’ajibai don tabbatar da karyansu. Dole mu shirya tare su da gaskiyan nan na Littafin cewa matattu basu san komi ba, kuma cewa su din da suke bayanuwa ruhohin aljannu ne.

A gabanmu ga “Sa’ar jaraba, wannan da ke zuwa bisa ga dukan duniya, domin a jarabci mazamnan duniya.” Ruya 3:10. Dukan wadanda bangaskiyar su ba ta kafu sosai kan maganar Allah ba za a rude su a kuma rinjaye su. Shaitan yana aiki da dukan rudami na rashin adalci domin shi mallaki ‘ya’yan mutane, rudinsa kuma zai ci gaba. Amma ba zai cim ma burinsa ba sai dai in mutane sun amince da jarabobinsa. Wadanda da naciya suke neman sanin gaskiya, suna kuma kokarin tsarkake rayukansu ta wurin biyayya, ta hakanan kuma suna iyakar kokarinsu domin shiryawa don sabanin, Allah na gaskiya za ya zama tsaronsu. “Tun da ka kiyaye maganar hankuri na, ni ma zan kiyaye ka” (aya 10), alkawalin Mai-ceton ke nan. Zai iya aiko kowane malaika daga sama domin su tsari mutanensa, maimakon barin Shaitan ya rinjayi mutum daya mai-dogara gare shi.

Annabi Ishaya ya bayana yaudaran da za ta abko ma miyagu, wadda za ta sa su dauka cewa Allah bazai hukumta su ba. Suna cewa: “Mun yi alkawali da mutuwa, muna kwa amana da Sheol, sa’anda bala’i mai-rigyawa za ya ratsa, ba za ya zo wurinmu ba; gama mun mai da karya mafakarmu, mun buya kuma kalkashin karya.” Ishaya 28:15. Cikin masu maganan nan akwai wadanda cikin taurin kai da rashin tuba su ke ta’azantar da kansu da tabbacin da ake yi masu cewa babu horo don mai-zunubi, cewa wai dukan ‘yan Adam, komi lalacewa, za a daukaka su zuwa sama, su zama kamar malaikun Allah. Amma fiye da wannan ma akwai masu yin yarjejjeniya da mutuwa, suna alkawali da lahira, wadanda ke kin gaskiyan da Allah ya tanada domin tsaron masu adalci a ranar wahala, suna kuma karban garkuwar karya da Shaitan ke bayarwa a maimako, watau rudin nan na sihiri.

Abinda da ya fi ban mamaki shi ne makantar mutanen yanzu. Dubbai suna kin maganar Allah cewa bai kamata a gaskata shi ba, amma da marmari suna karban rudin Shaitan. Masu shakka da masu ba’a suna sokar masu goyon bayan imanin annabawa da manzani, suna kan cewa kuma su kansu ta wurin yin ba’a ga maganar Littafin game da Kristi da shirin ceto da horon da za a yi ma masu kin gaskiya. Suna cewa wai suna tausaya ma masu kankantan tunani mara karfi cike da camfi da ya sa har suna yarda da maganar

Allah har suna biyayya ga dokarsa. Suna nuna tabbaci sosai sai ka ce sun dai yi yarjejjeniya da mutuwa, suka yi alkawali da lahira kuma, kaman sun gina shingen da ba za a iya wucewa ba ne tsakaninsu da ramuwar Allah. Ba abinda zai iya ba su tsoro. Sun ba da kansu ga majarabcin gaba daya, suka hada kai da shi, sun kuma amshi ruhunsa sosai, ta yadda ba su da iko ko niyyar tserewa daga tarkonsa.

Shaitan ya dade yana shirya yunkurinsa na karshe don rudin duniya. Ya kafa harsashen aikinsa ta wurin tabbacin da ya ba Hawa'u a Adnin cewa, "Ba lallai za ku mutu ba." "Ran da kuka chi daga chiki, ran an idanunku za su bude, za ku zama kamar Allah, kuna sane da nagarta da mugunta." Farawa 3:4,5. Da kadan da kadan ya rigaya ya shirya hanya domin babban rudinsa mafi girma ta wurin tsarin sihiri. Bai rigaya ya kai karshen tsare tsarensa ba; amma zai kai a karshen ringin lokaci. In ji annabin: "Na ga kuma kazaman ruhohi uku, sai ka che kwadi,… gama ruhohin aljannu ne su, masu aika alamu; suna kwa fita zuwa wurin sarakunan duniya, garin su tattara su zuwa yakin babbar rana ta Allah mai-iko duka." Ruya 16:13,14. Ban da wadanda ikon Allah ta wurin bangaskiya zai kiyaye su, dukan duniya za ta rude ta runtuma zuwa cikin rudinsa. Da sauri a ke ta rudin mutane zuwa cikin tsaro na karya mai-hadarin gaske, inda zubowar fushin Allah ne kadai zai falkas da su.

In ji Ubangiji Allah: "Gaskiya kwa zan maishe ta igiya, adilchi kuma in maishe shi magwaji; kankara za ta share mafalkan karya, ruwaye kuma za su sha kan moboya. Za a warware alkawalinku da mutuwa, amanarku da Sheol ba za ta tsaya ba; lokacin da bala'i mai-rigyawa za ya ratsa, sa'an nan za ku sha takawa daga kalkashinsa." Ishaya 28:17,18.

Babi na 35—Barazana ga Yancin Lamiri.

Yanzu masu Kin mulkin paparuma suna girmama tsarin Romawa fiye da shekarun baya. A kasashen da tsarin Katolika ba ya ci gaba, ‘yan paparuma kuma suna taka tsantsan domin su sami tasiri, akwai karuwan kyaliya game da koyaswoyin da suka bambanta ekklesiyoyin da suka canja da tsarin paparuma din; ana kara baza ra’ayin nan cewa ai ba mu bambanta sosai ba game da muhimman ababa kamar yadda aka zata, kuma cewa sassauci kadan daga gefen mu zai kawo mu ga karin fahimtar juna da Rum. Akwai lokacin da masu Kin ikon paparuma suka daukaka ‘yancin lamiri kwarai. Sun koya ma ‘ya’yan su su guji tsarin paparuma, suka kuma gaskata cewa neman jituwa da Rum rashin biyayya ga Allah ne. Amma yanzu abin ya bambangta sosai!

Masu-goyon bayan ‘yan paparuma suna cewa wai an bata ma ekklesiyarsu suna, masu Kin ikon paparuma kuma suna kokarin amincewa da wannan maganar. Da yawa suna koyar da cewa ba daidai ba ne a zargi ekklesiya ta yau da haramtattun halayya da muguntan da ta aikata lokacin mulkinta a zamanin jahiliya da duhu. Sun ba da hujja cewa zaluncin da ta yi, sakamakon jahilcin zamanin ne, suna kuma cewa tasirin wayewan zamani ya sake tunaninsu.

Mutanen nan sun manta da’awar cewa wannan mulkin ta yi shekara dari takwas tana cewa ita ba ta kuskure? Maimakon dena wannan kirarinma, an karfafa shi ne a cikin karni na sha tara da himmar da ta fi ta da. Da shi ke Rum ta na cewa wai “ekklesiya ba ta taba yin kuskure ba, kuma ba za ta taba yin kuskure ba, bisa ga Littafin,” ta yaya za ta yi musun kaidodin da ta yi anfani da su a sarraki da suka gabata?

Ekklesiyar paparuma ba za ta taba rabuwa da ikirarin ta na cewa ba ta kuskure ba. Tana nacewa cewa duk abin da ta yi na tsananta ma wadanda su ke kin dokin ta daidai ne, kuma ashe ba za ta maimaita ayukan nan ba idan ta sami zarafi? Bari gwamnatocin yanzu su janye hali da suka yi, a kuma mayar da Rum ga ikon ta na da, nan da nan za a farfado da zaluncin ta.

Wani sannanen mawallafi ya yi Magana hakanan game da halin tsarin paparuma game da ‘yancin lamiri, da kuma hadaruka da ke barazana ga Amerika game da nasarar tsarin mulkinta. Ya ce:

“Akwai wadanda ke so su mai da tsoron ekklesiyar Roman Katolika a Amerika kamar tsatsauran ra’ayi ne ko kuma yarantaka. Ba sa ganin komi a yanayin Roman Katolika da hakinta da ke sabani da tsare tsarenmu, kuma ba sa ganin wani abin tsoro game da girman da ta ke yi. bari mu gwada wadansu muhimman kaidodin gwamanatin mu da na ekklesiyar Katolika.

“Kundin tsarin Amerika yana tabbatar da ‘yancin lamiri. Ba abin da ya fi wannan tamani muhimmanci. Paparuma Pius IX cikin wasikarsa ta 15 ga Agusta 1854 ya ce:

‘Munanan koyaswoyi ko suruce-surucen da ke goyon bayan ‘yancin lamiri kuskure ne cike da annoba, kwaro ne da ya kamata kowace kasa ta ji tsoronsa.’ A wasikarsa ta 8 ga Disamba, 1864 kuma paparuman nan dayan ya tsine ma wadanda ke goyon bayan ‘yancin lamiri da na addini,’ da kuma ‘dukan wadanda ke cewa bai kamata ekklesiya ta yi anfani da karfi ba.’

“Taushin muryar Rum a Amerika ba nuna cewa da ta sake hali ba ne. Tana saukin kai inda ba ta da yadda za ta yi ne. In ji Bishop Oconnor: ‘Ana jimre ‘yancin addini kawai har sai lokacin da za a iya aiwatar da akasinsa ba tare da wani hatsari ga ekklesiyar Katolika ba.’… Babban bishop na St. Louis ya taba cewa: ‘Ridda da rashin ba da gaskiya laifuka ne; kuma a kasashen Kirista, kamar a Italiya da Spain misali, inda dukan mutanen ‘yan Katolika ne, da kuma inda addinin Katolika muhimmin fanni ne na dokar kasar, akan hori laifukan nan kamar sauran lafiya’,…

“Kowane cardinal da archbishop, da bishop a Ekklesiyar Katolika yakan dauki rantsuwar biyayya ga paparuma, inda akwai kalmomin nan: “Masu ridda, da masu kawo rabuwa, da ‘yan tawaye ga Ubangijin namu (watau paparuma), ko kuma magadansa, ni zan yi iyakar kokari na in zalunce su in yi sabani da su.”

Gaskiya ce akwai Kiristan gaskiya a cikin ekklesiyar Katolika. Dubbai cikin wannan ekklesiyar suna bauta ma Allah iyakar hasken da suka samu ne. Ba a barinsu su karanta maganarsa, sabo da haka kuwa ba su san gaskiyan ba. Basu taba ganin bambaci tsakanin ibada mai-rai daga zuciya da bukukuwa da hidimomi kawai. Allah yana kallon irinsu da idon tauisayi, ko da shike suna da ilimi cikin addini mai-rudi da ba ya gamsarwa. Za ya sa tsirkiyoyin haske su ratsa duhun da ya kewayesu. Za ya bayana maishe gaskiya da ke cikin Yesu, kuma da yawa za su zabi kasancewa tare da mutanensa.

Amma tsarin Romawa bai kara jituwa da Kristi yanzu fiye da duk wani lokaci cikin tarihinsa ba. Ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma suna cikin bakin duhu sosai, ba don haka ba da sun gane alamun zamanun. Ekklesiyar Rum ta yi nisa cikin shirye shiryenta da matakan aikin ta. Tana anfani da kowace dabara don fadada tasirinta, ta kuma kara ikonta don shiryawa saboda mumunan yaki da fada mai-zafi domin mallakar duniya, a sake dawowa da zalunci, a kuma warware duk abinda Kin ikon paparuma ya yi. Katolika tana ci gaba ta kowace fuska. Duni karuwar yawan majami’unta a kasashe masu Kin ikon paparuma. Dubi farinjinin kolejojinta da makarantun addininta a Amerika, inda masu Kin ikon paparuma ke zuwa don samun ilimi. Dubi yaduwar tsafi a Ingila da yawan komawa ekklesiyar Katolika da a ke yi. Ya kamata ababan nan su ta da taraddadin dukan masu kishin kaidodin bishara.

Masu Kin ikon paparuma sun sa hannu cikin tsarin paparuma, sun kuma amince da wadansu ababa, suka yi sassauci kan wadansu al’amura, har ‘yan paparuman kansu suna mamaki, suka kuma kasa gane dalili. Mutane suna rufe idanunsu daga ainihin halin

ekklesiyar Rum da hatsarin da za a iya fuskanta daga samun fifikonta. Ya kamata a falkar da mutane domin su yaki ci gaban wannan babban magabcin ‘yancin addini da sauran ‘yanci.

Masu Kin ikon paparuma da yawa suna tsammanin cewa addinin Katolika ba shi da ban-sha’awa, kuma cewa sujadarta mara armashi ce, kuma bukukuwa marasa ma’ana. Wannan kuskure su ke yi. Ko da shike ekklesiyar Rum ta kafu kan rudi ne, ba wani kauyanci ne mara fasali ba. Hidimar addinin ekklesiyar Rum hidima ce mai-ban sha’awa. Adonta da hidimominta su kan ja hankulan mutanen su kuma rufe muryar hankali da lamiri. Ido yakan yi sha’awar kyawawan majami’u da jerin gwano masu-ban sha’awa da bagadin zinariya, da dakunan ibada masu ado, da kyawawan hotuna, da sassaka masu tamani; duka suna jan hankulan masu son abu mai-kayu. Kunne ma yakan ji abu mai-dadi. Muzikan na musamman ne, da sautin molon, da amon muryoyi da yawa sukan cika majami’un ekklesiyar, kuma baza su kasa cika zuciyar mutum da sha’awa da bangirma ba.

Wannan kyau da shagali da hidima masu ban sha’awa da ido ke gani alama ce ta lalacewa daga ciki. Addinin Kiristi baya bukatar irin ban sha’awan nan. Cikin hasken da ke haskakawa daga giciyen ainihin Kiristanci yana bayanuwa cikin tsabta da ban-sha’awa da babu ado daga waje da zai kamanta ainihin tamaninsa. Kyaun tsarki ne, ruhun tawali’u da natsuwa, su ke da tamani ga Allah.

Walkiyar salo ba lallai alamar kyakyawan tunani ba ne. Sau da yawa akan iske iya zane da yawan wayewa cikin ‘yan duniya masu mumunan sha’awa. Shaitan ya cika anfani da su don su mutane su manta wajibai na rai, su manta rayuwa ta rashin mutuwa da ke zuwa nan gaba, su juya da mai-taimakonsu mara-iyaka, su kuma yi rayuwa domin wannan duniyan kadai.

Addinin abin da ake gani kawai yana da ban sha’awa ga zuciyar da ba ta tuba ba. Shaguli da al’adar sujadar Katolika yana jan-hankali sosai ta yadda yana rudin mutane da yawa, har su ga kamar ekklesiyar Rum ce kofar sama. Ba wanda ke da kariya daga tasirinta sai wadanda suka dasa kafafunsu da karfi bisa tushen gaskiya, wadanda ruhun Allah ke sabonta zukatansu kuma. Dubbai da ba su da ainihin sanin Allah za su karbi kamanin ibada ba tare da ikonta ba. Irin addinin da yawancin mutane ke so ke nan.

Da’awar ekklesiya cewa tana da ‘yancin gafara ta kan sa Romawa su ji kamar suna da ‘yanci su yi zunubi, kuma hidimar furta laifi. Kafin ta yi gafarar ma tana ba da daman yin zunubi. Wanda ya durkusa a gaban mutum faddade kamarsa, ya kuma bayana masa asiran tunanin zuciyarsa, yana nakasa mutumtakansa da kuma kowane tunanin zuciyarsa ne. Ta wurin bayana zunuban ransa ga priest, wanda mai-kuskure ne, mai-zunubi, mai-mutuwa, wanda sau da yawa barasa da anishuwa sun rigaya sun lalata shi, matsayin halin mai-tuban yakan ragu, har ma ya kazamtu tawurin wannan. Tunaninsa game da Allah yakan ragu zuwa kamanin fadadden mutum, gama priest din yana matsayin wakilin Allah ne. Furta

laifin mutum ga mutum din nan ne mabulbular boye daga inda yawancin mugunta ne da ke kazamtar da duniya, tana kuma shirya ta don hallaka ke bulbulowa. Duk da haka ga mai-son jin dadi, ya fi masa dadi ya furta zunubinsa ga mai-mutuwa kamarsa da ya bude ransa ga Allah. Yanayin mutuntaka ya fi jin dadin shan wahala don samun gafara maimako rabuwa da zunubi; wahal da jiki da toka da kayayuwa da sarkoki ya fi giciyewar sha'awoyin jiki sauki. Kayan da zuciyar mutumtaka ke shirye ya dauka maimakon durkusa ma karkiyar Kristi, yana da nauyi.

Akwai kamani sosai tsakanin ekklesiyar Rum da ta Yahudawa ta lokacin zuwan Kristi na fari. Yayin da Yahudawa suka dinga tattake kowace kaidar dokar Allah a boye, sun dinga kiyaye umurninta a bayane, suna jibga mata sharudda da al'adu da suka sa biyayya ta zama da zafi da wahala kuma. Yadda Yahudawa su ka ce suna girmama dokar haka ne Romawan ke cewa suna girmama giciyen. Suna daukaka alamar wahalokin Kristi alhali cikin rayuwarsu suna kin Kristi din.

'Yan paparuma suna manna giciye a majami'unsu da bagadinsu da rigunansu. Ko ina ana ganin alamar giciyen. Ko ina ana girmama ta a daukaka ta. Amma ana bizne koyaswoyin Kristi kalkashin tulin al'adu marasa ma'ana da fassaran karya da yawan bukatu. Kalmomin mai-ceton game da Yahudawa sun fi cancantar shugabanin ekklesiyar Roman Katolika ma, cewa: "I, su kan damra kaya masu nauyi, masu-wuyan daukawa kuma, su dibiya ma mutane a kafadu; amma su da kansu basu yarda su ko motsa su da yatsansu ba." Matta 23:4. Ana rike masu bi cikin fargaba kullum suna tsoron Allahn da suka yi masa laifi, alhali da yawa cikin shugabannin ekklesiya suna rayuwa cikin jin dadi da sha'awa.

Sujada ga siffofi, rokon tsarkaka da daukaka paparuma, dabarun Shaitan ne don jawo hankulan mutane daga Allah da Dansa. Domin tabbatar da hallakarsu, yana, kokarin juya hankulansu daga wanda ta wurinsa ne kadai zasu iya samun ceto. Zai mai da hankulansu ga duk wani abin da za a iya sauyawa a madadin shi wanda ya ce: "Ku zo gareni, dukanku da ku ke wahala, masu-nauyin kaya kuma, ni kwa in ba ku hutawa." Matta 11:28.

Kokarin Shaitan kullum shi ne karyata halin Allah, da yanayin zunubi da ainihin batutuwan da babban jayayyan nan, ta kunsa. Karyarsa tana rage nauyin bukatar kiyaye dokar Allah ta ba mutane damar yin zunubi. A lokaci dayan, yana sa su sha'awar tunani mara kyau game da Allah, ta yadda suna daukan shi da tsoro da kiyayya maimakon kauna. Ana danganta Allah da muguntar da ke halin Shaitan ne, sai a kunsa shi cikin tsarin addini, a bayana shi tawurin salon sujada. Ta haka ana makantar da zukatan mutane, Shaitan kuma yakan rike su su zama wakilansa don yin yaki da Allah. Tawurin mumunan fahimtar halin Allah, an sa al'ummai na kafirai suka gaskata cewa wajibi ne a ba da hadayar mutane domin samun karbuwa ga Allah, kuma an aikata munanan zalunci kalkashin salo iri iri na bautar gumaka.

Ekklesiyar Roman Katolika da ta hada ayukan kafirci da Kiristanci, kuma kamar kafirin, ta na karyata halin Allah, ta shiga ayukan zalunci masu ban-kyama. A zamanin fifikon Rum akwai dabarun zalunci da suka tilasta amincewa da koyaswoyinta. Akwai itacen nan mai-tsini inda ake kashe wadanda suka ki yarda da ikonta. Akwai kashe kashe da ba za a iya sanin yawan su ba, sai sa'ar hukumci ta bayana su. Shugabannin ekklesiya kalkashin mai-gidansu Shaitan sun rika nazarin yadda za su kirkiro hanyoyin yin zalunci mafi girma ba tare da dauke ran mutunin ba. A lokata da yawa a kan dinga maimaita konawar, har iyakar inda mutumin zai iya jimrewa, har inda mai-faman yakan gwammaci mutuwa.

Abinda ya faru da masu jayayya da Rum ke nan. Ga membobin, takan ba da horo na bulala, ko yunwa mai tsanani, ko kuma wahalrwa ta jiki kowace iri. Don samun alherin Allah, masu tuba sukan ketare dokokin Allah tawurin ketare dokokin halitta. Aka koya masu su raba dangantakan da Allah ya hada domin ya kyautata bakuncin mutum a duniya. Makabarta tana cike da miliyoyin mutane da suka kashe rayuwarsu a banza wai suna kokarin danne soyayyar jikunansu, su kawar da kowane tunanin tausayin sauran halittatu, cewa Allah ba ya so.

Idan muna so mu fahimci zaluncin Shaitan, wanda ya yi daruruwan shekaru yana nunawa, ba cikin wadanda basu taba jin labarin Allah ba, amma a tsakiyar Kiristanci, kuma ko ina, sai mu dubi tarihin Romawa kawai. Tawurin tsarin nan na rudi sarkin muguntan yana cim ma manufarsa ta kawo reni ga Allah da bakinciki ga mutum. Kuma yayin da mu ke ganin yadda yake badda kamaninsa yana kuma cika aikinsa ta wurin shugabannin ekklesiya, ya kamata mu gane dalilin da ya sa yana kiyayya da Littafin. Idan aka karanta Littafin nan, jinkan Allah da kaunarsa za su bayana, za a ga cewa bai aza ma mutane wadannan manyan nauyin ba. Abin da yake bida kadai shi ne zuciyar tuba da ruhun tuba mai-tawali'u.

Kristi bai ba da kwatanci cikin rayuwarsa na cewa mutane su kulle kansu cikin gidajen zuhudu domin a cancanci sama ba. Bai taba koyar da cewa dole a danne kauna da tausayi ba. Zuciyar Mai-ceton ta cika da kauna.

Idan mutum yana kara kusantuwa da samun cikakken halin kirki, tunaninsa zai kara kaifi, kuma zai kara fahimtar zunubi, kuma zai kara tausaya ma wahallalu. Paparuma yana da'awar cewa shi ne wakilin Kristi, amma yaya halinsa yake idan aka gwada shi da na Mai-ceton? Ko an san Kristi da jefa mutane cikin kurkuku ko wurin kisa wai don basu yi masa biyayya a matsayin Sarkin sama ba? Ko an taba jin muryarsa yana hukumcin kisa ga wadanda basu karbe shi ba? Saboda mutanen wani kauyen Samariyawa su ka nuna masa reni, manzo Yohanna ya fusata sosai, har ya tambaya: "Ubangiji kana so mu umurchi wuta ta sabko daga sama ta chinye su?" Yesu Ya dubi almajiransa da tausayi, ya tsauta ma ruhun fushinsu Ya ce, "Dan mutum ba ya zo domin hallaka rayukan mutane ba, amma domin ya

cece su ne.” Luka 9:54,56. Dubi bambancin ruhun da Kristi ya nuna da ruhun mai-cewa wai shi ne wakilinsa.

Yanzu ekklesiyar Rum tana nuna ma duniya cewa tana da adalci, tana rufe zaluncin ta da neman gafara. Ta suturta kanta da riguna irin na Kristi, amma ba ta sake ba. Kowace kaidar tsarin paparuma ta sararaki na da, tana nan yanzu. Har yanzu ana rike da koyaswoyin da aka kago a zamanin jahiliya. Kada kowa ya rudi kansa. Tsarin paparuma da masu Kin ikon papruma ke shirye su girmama yanzu shi dayan ne wanda ya yi mulkin duniya a kwanakin canjin, lokacin da mutanen Allah suka tashi tsaye, suka sa kansu cikin hadari suka fallasa zunubin ta.

Tana da griman kai da zaton nan da suka aza ta bisa sarakuna da ‘ya’yan sarki ta kuma mallaka ma kanta ababa da Allah kadai Ya isa ya mallaka. Ruhunta na kama-karya da zalunci yana nan daidai da na lokacin da ta murkushe ‘yancin ‘yan Adam ta kuma kashe tsarkakan madaukaki.

Tsarin paparuma dai abin da annabci ya ce zai kasance ne, watau riddar kwanakin karshe. Tassalunikawa II, 2:3,4. Takan dauki yanayin da zai fi biya mata bukata ne, amma kalkashin canje-canjen kamaninsa kamar hawainiya tana boye dafin macijin nan mara sakewa. “Bai kamata a amince da masu ridda ba, ko ma wadanda a ke tsammanin sun yi ridda,” in ji ta. Ko ya kamata mulkin nan da ya yi shekaru dubu yana zubar da jinin tsarkaka ya karbu a matsayin wani sashe na ekklesiyar Kristi?

Ba kawai ba ne a kasashen da suka ki ikon paparuma ana cewa wai yanzu Katolika ba ta bambanta sosai da ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma ba kamar da. An sami canji kam, amma canjin ba na tsarin paparuman ba ne. Tsarin Katolika, hakika, ya yi kama da yawancin Kin ikon paparuma na zamanin nan, da shike Kin ikon paparuma ya lalace sosai daga na zamanin ‘yan Canjin.

Yayin da ekklesiyoyin masu Kin ikon paparuma ke neman goyon bayan duniya, kaunar karya ta makantar da idanunsu. Suna gani kamar daidai ne su gaskata cewa kowace mugunta nagarta ce, kuma ba shakka a karshe za su gaskanta cewa kowace nagarta mugunta ce, maimakon kare bangaskiyar da aka taba ba atsarkaka, yanzu suna tuba ma Rum saboda ra’ayinsu mara-kyau game da ita, suna rokon gafara sabo da matsanancin ra’ayinsu.

Da yawa har ma da masu goyon bayan Rum suna ganin karamin hatsari daga ikonta da tasirinta. Da yawa suna cewa duhun da ya mamaye tunani da halin kirki a zamanin jahaliya ya taimaka wajen baza koyaswoyinta da camfe canfenta da danniyarta, kuma cewa Karin tunani na wannan zamani, da yaduwan sani da karuwar ‘yanci a sha’anin addini suna hana tasowar rashin hakuri da zalunci. Tunanin ma cewa wannan abu zai kasance an mai da shi abin ba’a. Gaskiya ne, cewa haske mai-yawa ta fannin addini da halin kirki da tunani.

A cikin budadiyar maganar Allah haske daga sama yana haskaka duniya. Amma a tuna cewa yawan hasken da aka bayar, yawan duhun wadanda suka lalata shi suka kuma ki shi.

Nazarin Littafin tare da addu'a zai nuna ma masu-kin ikon Rum ainihin halin tsarin paparuma ya kuma sa su su ki shi, su kuma rabu da shi, amma da yawa suna gani kamar suna da wayo sosai ta yadda basa ji kamar suna bukatar bidar Allah domin a bishe su zuwa gaskiya. Ko da shike suna fahariya da wayewarsu, sun jahilci Littafni da ikon Allah ma. Dole su sami wata hanyar lallabar lamirinsu, sabo da haka suna bidar abin da ke da mafi-kankantar ruhaniya, abin da ke kaskantarwa kuma. Abin da suke nema shi ne hanyar mance Allah da za a ga kamar hanyar tunawa da shi ne. Tsarin paparuma tana shirye ta gamsar da dukan wadannan. Tana shirye don mutane kashi biyu da suka mamaye kusan dukan duniya, watau wadanda za a cece su bisa ga isar su, da wadanda za a cece su cikin zunubansu. Asirin ikonsu ke nan.

An rigaya an nuna cewa ranar duhun tunani yakan taimaka ma nasarar paparuma. Za a kuma nuna cewa ranar babban hasken tunani ma zai taimaka ma nasarar paparuman. A sararakin da suka gabata, lokacin da mutane ba su da maganar Allah, kuma ba su san gaskiya ba, an hyi masu rufa-ido, aka kuma kama dubbai da ba su ga tarkon da aka dana masu ba. A zamanin nan akwai da yawa da idanunsu sun rufu da walkiyar zato da kimiyyar karya, har ba sa iya ganin tarkon, suna kuwa shiga cikinsa sai ka ce an rufa masu ido. Allah ya shirya cewa mutum ya rike tunaninsa kamar kyauta daga wurin mahalicinsa da zai yi anfani da shi cikin hidimar gaskiya ta adalci, amma sa'anda girman kai da buri suka shirya zuciyan mutane kuma suka daukaka tunaninsu fiye da maganar Allah, a lokacin nan tunani zai yi ta'adi fiye da wanda jahilci zai yi. Ta hakanan kimiyar karya ta yau, wadda ke rage bangaskiya ga Littafin, zai yi nasara wajen shirya hanyar karban ikon paparuma da ayukansa kamar yadda hana sani ya yi nasara wajen bude mata hanyar biyan bukatunta a zamanin jahiliya.

Cikin al'amuran da ke gudana yanzu a Amerika don samo ma fannonin ekklesiya da ayukan ta goyon bayan kasa, masu Kin ikon paparuma suna bin matakan 'yan paparuma ne. Har ma suna bude kofa ne ma 'yan paparuma su sake samun fifikon da suka rasa a tsohuwar duniya. Abin da ke kara ma wannan yankuri muhimmanci kuma shi ne cewa babban burin da ake da shi shi ne tilasta kiyayewar Lahadi, al'ada da Rum ta fara, tana kuma cewa ita ce shaidar ikonta. Ruhun tsarin paparuma ne ruhun daidaituwa da al'adun duniya. Daukaka al'adun mutane fiye da dokokin Allah shi ne yake mamaye ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma, yana kuma kai su ga daukaka Lahadi wanda 'yan paparuma suka yi kafin su.

Idan mai-karatu zai gane dabarun da za a yi anfani da su cikin hayayyan da ke zuwa, zai bukaci tunawa ne kawai da dabarun da Rum ta yi anfani da su a sararakin da sun gabata. Idan mai-karatun yana so ya san yadda 'yan paparuma da hadin kan masu Kin mulkin

paparuma za su yi da masu-kin kayaswoyinta, ya dubi irin ruhun da Rum ta nuna game da Assabbat da masu kiyaye shi.

Dokokin sarakuna, da majalisu na bai daya, da haikalin ekklesiya da ake tabbatarwa tawurin ikon kasa, matakai ne ta inda bukin kafirai ya sami matsayin girmamawa cikin Kiristanci. Matakin farko da ya tabbatar da kiyaye Lahadi shi ne dokar da Constantine ya kafa a AD 321. Dokan nan ta bukaci 'yan alkarya su huta a "rana mai-tsarki ta rana," amma ya ba kauyawa dama su ci gaba da ayukan su na noma. Ko da shike dokar kafirci ce babban sarkin ya tabbatar da ita bayan ya karbi Kiristanci a suna kawai.

Da shike umurnin sarauta bai kai ikon Allahntaka ba, Eusebius, wani bishop mai-neman goyon bayan 'ya'yan sarauta, wanda kuma aboki na musamman ne mai-fadanci kuma ga Constantine, ya dinga baza wani ikirari cewa Yesu ya mayar da Assabbat zuwa Lahadi. Ba aya ko shaida ko daya daga Littafin da ya tabbatar da sabuwar koyaswar. Eusebius kansa ya amince cewa karya ce, ya kuma nuna ainihin masu kirkiro canjin. Ya ce: "Dukan ababan da suka wajibta a yi ran Assabbat, mu mun mayar da su ranar Ubangiji." Amma zancen Lahadin nan, ko da shi ke ba shi da tushe, ya karfafa mutane tattake Assabar na Ubangiji. Dukan masu son daukakar duniya sun amince da Lahadin.

Sa'anda tsarin paparuma ya kafu sosai, an ci gaba da aikin daukaka Lahadi. Da farko, mutanen sukan shiga aikin gona idan basu je masujada ba, aka kuma ci gaba da kiyaye rana ta bakwai a matsayinta na Assabbat. Amma a hankali an yi canji. Aka hana masu aikin ekklesiya yin hukumci game da kowace jayayyar da ba ta addini ba ce a ranan Lahadi. Ba da jimawa ba, aka umurci dukan mutane, komi matsayinsu, su dena aiki in ba haka ba su biya tara in ba barori bane, ko kuma su sha bulala in barori ne. Daga baya aka umurta cewa a hori masu-arziki ta wurin kwace rabin gidajensu. A karshe kuma idan duk da haka basu dena ba, sai a mai da su bayi. Talakawa kuma sai a kore su kwatakwata daga kasar.

An kuma yi anfani da al'ajibai. "Daya daga cikin al'ajiban shi ne cewa wai wani manomi da ya shirya nome gonarsa ran Lahadi ya share garmarsa da wani karfe, sai karfen ya manne cikin hannunsa, ya kuma yi shekaru biyu yana tafiya da karfen, yana fama da zafi da kunya masu yawa kuwa."

Daga baya paparuma ya ba da umurni cewa kowane priest na masujada ya gargadi masu-ketare Lahadi ya kuma koya masu su rika zuwa masujaida su yi addu'o'insu, kada su jawo ma kansu da makwabatansu mumunan bala'i.

Wata majalisar ekklesiya ta gabatar da zancen da har masu Kin ikon paparum ma sun yi anfani da shi, cewa wai da shike walkiya ta kashe wadansu yayin da su ke aiki ran Lahadi, wannan ya nuna cewa Lahadi din ne Assabbat. Priestocin suka ce: "Rashin jin dadin Allah game da yadda basu kula ranan nan ba a bayane yake." Sai aka roka cewa priestoci da pastoci da sarakuna da 'ya'yan sarakuna, da dukan amintattu su "yi anfani da

iyakar kokarinsu domin a dawo da darajar ranar, kuma, don anfanin Kiristanci, a kara himmar kiyaye ta saboda lokaci mai-zuwa.

Da shike umurnin majalisu sun kasa, aka bukaci hukumomin kasa su ba da doka da za ta razana zukatan mutane ta kuma tilasta su su dena aiki ran Lahadi. A wani taron Synod da aka yi a Rum aka jaddada dukan kudurorin da aka taba dauka, da karin karfi da bangirma. Aka kuma hada su cikin dokar ekklesiya, hukumomin kasa kuma suka zartas da su, kusan ko ina a cikin Kirista.

Har da haka dai rashin nassin da ya goyi bayan kiyaye Lahadi ya ci gaba yana jawo rudewa, sosai. Mutane suka yi shakkar ikon da mallamansu ke da shi na kawar da umurnin Yahweh cewa “Rana ta bakwai Assabbat ne ga Ubangiji Allahnka,” domin su girmama ranar rana. Don cika gibin nan na rashin shaidar Littafin, ya zama dole a nemi wadansu dalilai. Wani mai himmar goyon bayan Lahadi, wanda kusan karshen karni na sha biyu ya ziyarci ekklesiyoyin Ingila, ya gamu da jayayya daga amintattun shaidun gaskiya; kuma kokarin sa ya kasa haifar da komi ta yadda ya bar kasar na wani lokaci, ya nemi wadansu hanyoyin tabbatar da koyaswoyinsa kuma. Sa’anda ya dawo, an cika gibin, daga nan kokarinsa ya yi nasara. Ya zo da wata takarda da ya ce daga Allah kansa ne, wadda ta kunshi umurnin da a ke bukata don kiyaye Lahadi, da barazana masu-ban tsoro don razana marasa biyayya. Wannan takardar, mara daraja, aka ce ta fado daga sama ne, kuma wai an same ta a Urushalima ne, a kan bagadin Saint Simon a Golgotha. Amma, a gaskiya, fadar paparuma a Rum ce inda ta fito. Tsarin paparuma cikin dukan sararaki takan amince da yaudara don kawo ci gaban ikon ekklesiya.

Takardar ta hana aiki daga sa’a ta tara, watau karfe uku, ran Asabar da rana, har zuwa fitar rana ran Litinin; aka kuma ce al’ajibai da yawa sun tabbatar da ikonta. Aka ba da labari cewa mutanen da suka yi aiki har sun zarce lokacin da aka yarda masu an hore su da ciwon shan inna. Wani mai nika da ya yi kokarin nika masaransa, maimakon garin masara ya ga jini ne ke kwararowa, injin kuma ya tsaya ko da shike ruwan da ke juya injin ya ci gaba da zubowa. Wata mace da ta sa kullun burodi a tanderun wutan gasa burodin, ta iske shi danye lokacin da ta fitar da shi, ko da shike tanderun yana da zafi sosai. Wata da ta shirya kullum burodin domin gasawa a sa’a ta tara, amma ta ajiye shi sai ran Litinin, washegari ta iske cewa an mai da shi dunkule-dunkule, kuma ikon Allah ya gasa su. Wani mutum da ya gasa burodi bayan sa’a ta tara ranan Asabar, washegari ya iske cewa jini yana fita daga cikinsa. Ta wurin irin kulle-kullen nan ne masu goyon bayan Lahadi su ka yi kokarin tabbatar da tsarkinsa.

A Scotland, kamar Ingila, an sami karin goyon bayan Lahadi ta wurin hada shi da wani sashi na Assabbat. Amma lokacin da aka ce a kiyaye da tsarki ya bambanta. Wata doka daga sarkin Scotland ta ce “Asabar daga sha biyu na rana ya kamata a kiyaye shi da tsarki,” kuma wai daga wannan lokacin har Litinin da safe kada wani ya yi wani sha’ani da ba na addini ba.

Amma duk da kokarin tabbatar da tsarkin Assabbat, ‘yan paparuma kan su sun amince a fili da sahihancin Assabbat din. Cikin karni na sha shida, wata majalisar ‘yan paparuma a sarari ta ce; “Bari dukan Kirista su tuna cewa Allah ya tsarkake rana ta bakwai, kuma ba Yahudawa kadai ba, dukan masu-cewa suna sujada ga Allahsun karbe ta suna kuma kiyaye ta, ko da shi ke mu Kirista mun sake Assabbat din nasu zuwa Rana ta Ubangiji.” Wadanda suka taba dokar Allah b a u kasa sanin yanayin abin da su ke yi a lokacin ba. Da gangan suka aza kansu bisa Allah.

An ba da kyakyawan misalin manufar Rum game da wadanda basu yarda da ita ba a zalunci mai-tsawo da zub da jini da aka yi ma Walensiyawa, wadanda cikin su akwai masu kiyaye Assabbat. Wadansu ma sun wahala hakanan sabo da amincinsu ga doka ta hudu ne. Tarihin ekklesiyoyin Habasha da Abyssiniya abin tunawa ne musamman. A tsakiyar bakincikin Sarrarakin Duhun nan, duniya ta manta da Kiristan Afirka ta Tsakiya, kuma sun yi daruruwan shekaru suna morar ‘yancin addininsu. Amma a karshe, Rum ta sami labarin kasancewarsu, nan da nan kuwa aka rudi babban sarkin Abyssiniya ya amince cewa paparuma ne wakilin Kristi. Ya amince da wadansu ababan kuma. Aka ba da dokar hana kiyaye Assabbat, wanda bai yi biyayya ba kuwa ya sha horo mai-tsanani. Amma zaluncin paparuma nan da nan ya yi tsamanin da ya sa mutanen Abyssiniya suka yi himmar kubutar da kansu daga gare shi. Bayan mumunan yaki aka kori Romawan daga garuruwan Abyssiniya, aka kuma mayar da bangaskiya ta da. Ekklesiyoyin sun yi farinciki da ‘yancin su kuma basu taba manta darasin da suka koya game da rudi da matsanancin ra’ayi da ikon danniya na Rum ba. Suka gamsu da kasancewa su kadai, sauran Kirista basu san da su ba.

Ekklesiyoyin Afirka sun rike Assabbat kamar yadda ekklesiyar paparuma ta rike shi kafin ta cika riddar ta. Yayin da suka kiyaye rana ta bakwai don biyayya ga dokar Allah, suka bar yin aiki ranan Lahadi bisa ga al’adar ekklesiya. Sa’an da ta sami mafificin iko, Rum ta tattake Assabbat na Allah domin ta daukaka na ta, amma ekklesiyoin Afirka da ke boye har kusan shekaru dubu basu shiga wannan riddar ba. Sa’an da aka jawo su kalkashin ikon Rum, an tilasta su su kawar da Assabbat na gaskiya su daukaka na karyan, amma da zaran sun dawo da yancin su sai suka koma biyayya ga doka ta hudu.

Labarum nan suna bayana magabtakan Rum game da Assabbat na gaskiya da masu kiyaye shi, da hanyar da take anfani da ita don daukaka na ta assabbacin da ta kirkiro. Maganar Allah tana koyar da cewa za a maimaita al’amuran nan sa’anda yan Roman Katolika da masu Kin ikon paparuma za su hada kai don daukaka Lahadi.

Annabcin Ruya 13 ya bayana cewa mulkin da bisa mai-kahoni irin na dan rago ke misaltawa zai sa duniya da dukan mazamna cikinta su yi sujada ga tsarin paparuma, wanda nassin ya misalta da damisa. Bisa mai kahoni biyu din zai kuma “che ma wadanda ke zamne a duniya, su yi gunki ga bisan.” Kuma bugu da kari, za ya umurci kowa “kanana da manya, mawadata da matalauta, yaya da bayi,’ su karbi shaidar bisan. Ruya 13:11-16. An rigaya an nuna cewa Amerika ce mulkin da bisa mai-kahoni irin na dan ragon ke misaltawa, kuma

cewa za a cika annabcin nan ne lokacin da Amerika za ta tilasta kiyaye Lahadi, wanda Rum ke cewa amincewa ne da fifikon daukakanta. Amma ba Amerika ce kadai za ta yi biyayyan nan ga Rum ba. Tasirin Rum cikin kasashen da suka taba amincewa da mulkin ta har yanzu ba a rushe shi ba. Annabci kuma ya ce za a mayar mata da ikonta. “Na ga dayan kawunansa sai ka ce an yi masa bugun ajali; sai kuma bugunsa na ajali ya warke, dukan duniya fa tana mamaki da bisan.” Ruya 13:3. Bugun ajalin shi ne faduwar paparuwa a 1798. Bayan wannan, in ji annabin, “bugunsa na ajali ya warke.” Dukan duniya fa tana mamaki da bisan.” Bulus ya bayana a fili cewa “mutumin zunubin” zai ci gaba har sai zuwa na biyu din. Tassalunikawa II, 2:3-8. Har karshen lokaci zai ci gaba da aikin rudi. Mai-ruya kuma ya ce, game da tsarin paparuman dai: Dukan mazamanan duniya kuma za su yi masa sujada, kowane wanda ba a rubuta sunansa tun kafuwar duniya chikin Littafin rai,” Ruya 13:8. Cikin Tsohuwar Duniya da Sabuwar Duniya, paparuma zai sami mubaya’a cikin darajanta Lahadi da ake yi, wanda tushensa ikon Ekklesiyar Rum ne kadai.

Tun tsakiyar karni na goma sha tara, daliban annabci a Amerika suna ba da wannan shaida ga duniya. Cikin al’amuran da ke aukuwa yanzu ana ganin ci gaba da hamzari zuwa cikar annabcin nan. Ga mallamai masu Kin ikon paparuma akwai ikirari dayan game da goyon bayan Allah ga kiyayae Lahadi, da kuma rashin shaida daga Littafin, kaman na shugababbin tsarin paparuma da suka kirkiro al’ajibai don cika wurin umurni daga Allah. Kirarin cewa ana zubo da hukumcin Allah kan masu ketare Assabbat na Lahadi zai sake faruwa, yanzu ma an fara iza shi. Kuma yunkurin tilasta kiyaye Lahadi ya fara samun goyon baya.

Dabarun Ekklesiyar Rum da wayonta abin mamaki ne. Ta iya karanta abin da zai faru. Tana daukan lokacinta, da sanin cewa ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma yi mata mubaya’a tawurin amincewa da Assabbat na karyan nan, cewa kuma suna shirin tilasta ta ta hanyar da ita ma ta yi anfani da ita can baya. Wadanda suka ki hasken gaskiya za su bidi taimakon wannan mulkin mai-cewa ba ta kuskure, don daukaka abin da ita ta kirkiro. Nan da nan za ta taimaki masu Kin ikon paparuma cikin wannan aikin. Wa ya fi shugabannin ‘yan paparuma sanin yadda za a bi da marasa biyayya ga ekklesiya?

Ekklesiyar Roman Katolika ko ina a duniya wata babbar kungiya ce kalkashin mulkin paparuma, wadda kuma aka tsara ta don cimma manufofin paparuma. Miliyoyin membobinta a kowace kasa a duniya, ana umurta su su mika kansu don biyayya da paparuma ne. Ko da wace kasa suke, ko kuma wace irin gwamnati ke mulkinsu, ana bidar su da su, girmama ikon ekklesiya fiye da dukan sauran hukumomi; ko da sun yi rantsuwar yin biyayya ga kasa, duk da haka a bayan wannan akwai rantsuwar biyayya ga Rum da ke wanke su daga duk wani alkawali da ya saba ma burinta.

Tarihi yana shaida kokarinta na kutsa kanta cikin al’amuran kasashe; kuma idan ta sami wuri ta ci gaba da manufofinta, ko da ‘ya’yan sarakuna da sauran mutane za su hallaka ma. Cikin shekara ta 1204 paparuma Innocent III ya sa Peter II, sarkin Arragon rantsuwa

da ta ce: “Ni Peter, sarkin Arragonawa, na yi alkawali zan kasance da aminci kullum ga Ubangiji na paparuma Innocent III, da magadansa Katolikawa, da Ekklesiyar Rum, da aminci kuma in rike kasata cikin biyayya gare shi, ina kare Ekklesiyar Katolika, ina kuma tsananta ma masu ridda.” Wannan ya je daidai da korafin nan game da ikon paparuma “cewa doka ta ba shi dama ya saukar da sarakuna,” kuma “cewa zai iya kubutar da talakawa daga yin biyayya ga shugabanni marasa adalci.”

A tuna kuma, Rum tana alfaharin cewa ba ta taba canjawa. Kaidodin Gregory VII da na Innocent III har yanzu su ne kaidodin Ekklesiyar Roman Katolika. Kuma da tana da iko da ta yi aiki da su da tsanani kamar yadda ta yi cikin sararraki da suka wuce. Masu Kin ikon paparuma basu san abin da suke yi ba sosai sa’anda su ke so su karbi taimakon Rum cikin aikin daukaka Lahadi. Yayin da suke naciya wajen cimma burinsu, Rum tana kokarin sake tabbatar da ikonta, ta sake mayar da daukakanta da ta rasa. Bari a kafa kaida a Amerika cewa ekklesiya za ta iya yin anfani da ikon kasa, cewa za a iya tilasta ayukan ibada ta wurin dokokin kasa, a takaice dai, cewa ikon ekklesiya da na kasa zai mallaki lamiri, nasarar Rum kuwa za ta tabbata a wannan kasar.

Maganar Allah ta ba da kashedi game da hatsarin da ke zuwa; idan an ki ji, masu Kin ikon paparuma za su kuwa gane ainihin manufofin Rum, a kurerren lokaci kuwa, don ba za su iya kauce ma tarkon ba. Tana girma shuru zuwa samun iko. Koyaswoyinta suna tasirinsu a majalisun dokoki, cikin majami’u, da cikin zukatan mutane, tana tara manya manyan gine ginenta a wuraren sirri inda za a maimaita zaluncinta na da. A sace ba tsammani kuma tana karfafa dakarun ta don ci gaba da manufofinta, sa’an da lokaci ya yi da za ta kai hari. Abin da take bukata kawai shi ne zarafi mai-kyau, kuma yanzu ma an rigaya an fara ba ta. Ba da jimawa ba za mu gani mu kuma ji ko mene ne manufar Rum din. Dukan wanda zai gaskata ya kuma yi biyayya da maganar Allah zai sami zargi da zalunci.

Babi na 36—Yakin da Kɛ Zuwa.

Daga farkon babban jayayyar a sama nufin Shaitan ne ya rushe dokar Allah. Don cimma burin nan ne ya shiga tawayen sa ga Mahalici, kuma ko da shi ke an kore shi daga sama, ya ci gaba da yakin a nan duniya. Manufan da yake bi kulluin ita ce rudin mutane, ta hakanan kuma shi sa su ketare dokar Allah. Ko ya yi wannan ta wurin kawar da dokar gaba daya ne ko kuma tawurin kin doka daya ne, a karshe dai sakamakon daya ne. Wanda ya ketare doka daya, ya rena dukan dokan ke nan; tasirinsa da kwatancinsa na zunubi ne; “ya zama mai-laifi ga duka ke nan.” Yakub 2:10.

Don neman jawo reni ga dokar, Shaitan ya karkata koyaswoyin Littafin, kurakurai kuma sun shiga cikin ibadar dubbai masu cewa sun ba da gaskiya ga Littafin. Babban yaki na karshe tsakanin gaskiya da kuskure babban jayayyan nan da aka dade ana yi game da dokar Allah ne. Yanzu muna shiga wannan yakin ke nan, yaki tsakanin dokokin mutane da umurnin Yahweh, tsakanin addinin Littafin da addinin tatsuniya da al’ada.

Wakilan da za su hada hannu sabanin gaskiya da adalci a wannan yaki suna aiki yanzu sosai. Magana mai-tsarki na Allah wanda aka mika mana ta wurin wahala da zub da jini, ba a ma ba shi muhimmanci sosai. Kowa zai iya samun Littafin amma mutane kalilan ne su ke karban shi a matsayin mai-bishewar rayuwarsu. Rashin aminci ya dawama sosai, ba cikin duniya kadai ba, har cikin ekklesiya. Da yawa sun ki koyaswoyin da suka kasance madogarar addinin Kirista. Manyan batutuwa na halitta da horarrun marubuta suka bayana, da faduwar mutum, da kafara, da kuma dawowar dokar Allah, Kirista da yawa suna kin, ko dukan su, ko sassansu. Dubban masu takama da hikimarsu da ‘yancinsu suna gani kamar amincewa da Littafin gaba daya kumamanci ne, suna gani kamar tabbacin baiwa da ilimi ne idan ana ba’a da Littafin ana kuma wasa da muhimman koaswoyinsa. Masu aikin bishara da yawa suna koya ma mutanensu, shehunan mallamai da sauran mallamai kuma suna koya ma dalibansu, cewa an canza ko kuma an soke dokar Allah, kuma wadanda ke gani kamar dokar tana aiki har yanzu, cewa ya kamata a yi biyayya gare ta, ana gani kamar ya kamata a rena su ne ko a yi ba’a da su.

Tawurin kin gaskiya, ana kin tushen gaskiyan ne. Ta wurin tattake dokar Allah ana kin ikon mai-ba da dokan ne, mai da koyaswoyin karya gumki yana da sauki kamar sifanta gumki daga itace ko dutse ne. Ta wurin karyata halayyan Allah Shaitan yakan sa mutane su ga Allah da halin da ba nashi ba ne. Da yawa suna daukaka gumkin tunani a madadin Yahweh, yayin da kalilan ne su ke sujada ga Allah Mai-rai, yadda aka bayana shi cikin kalmarsa, cikin Kristi da cikin ayukansa na halitta. Dubbai suna mai da halitta allah, alhali suna kin Allahn halitta. Ko da shike ta wata hanya dabam ne, akwai bautar gumaka yau a cikin Kirista tabbas kamar yadda ta kasance cikin Israila ta da, a zamani Iliya. Allahn yawancin wadanda a ke gani masu hikima ne, da masu-zurfin tunani, da mawaka da ‘yan siyasa, da ‘yan jarida - allahn wayayyun ‘yan zamani, na kolejoji da jami’o’i da yawa, har

ma, na wadansu makarantun koyar da tauhidi, ba da yawa suka fi Baal allan rana na Phoenicia ba.

Babu kuskuren Kirista da ya fi saba ma ikon Allah, kuskuren da ya fi saba ma tunani kai tsaye, wanda sakamakonsa ya fi muni kamar koyaswar zamani da ke bazuwa da sauri, cewa wai dokar Allah ta dena aiki kan mutane. Kowace kasa tana da dokokinta da ke bidar biyayya da ban-girma; ba gwamnatin da za ta iya kasancewa in ba dokokin, kuma ko za a taba tunanin cewa Mahalicin sama da kasa ba shi da dokar da ke mulkin wadanda Ya halitta? Bari a ce manyan shugabannin ekklesiya suna koyarwa a fili cewa dokokin kasarsu da ke tabbatar da 'yancin yan kasa ba wajibi ba ne, cewa suna takaita 'yancin mutane, sabo da haka kuma bai kamata a yi biyayya gare su ba, ko za a bar shuganbannin nan su dade a aikinsu? Amma ko kyale dokokin kasashe ya fi tattake dokokin Allah, tushen gwamnati, muni?

Da zai fi dacewa ga alummomi su soke dokokinsu, su yarda ma mutane su yi abin da sun ga dama, maimakon shugaban dukan halitta ya soke dokarsa, Ya bar duniya ba ma'aunin da zai hukunta mai-laifi ya kuma baratar da mai-biyayya. Ko mun san sakamakon soke dokar Allah? An taba gwadawa. Ababan da suka faru a Faransa a lokacin kafircinta ba kyaun gani. Lokacin an nuna ma duniya cewa yin watsi da hanin da Allah Ya dora zai sa a karbi shugabancin azalumi mafi-mugunta. Idan aka kawar da ma'aunin adalci, an bude ma sarkin mugunta hanya ke nan ya kafa ikonsa a duniya.

Duk inda aka ki dokokin Allah, zunubi baya kama da zunubi, kuma adalci ba ya zama abin sha'awa. Wadanda suka ki mika kai ga gwamnatin Allah ba za su iya mulkin kansu ba sam. Ta wurin munanan koyaswoyinsu suna shuka ruhun rashin bangirma cikin zukatan yara da matasa, kuma sakamakon wannan shi ne jama'a marasa bin doka, masu son nishadi kawai. Yayin da ake dariyan wautar masu biyayya ga dokokin Allah, jama'a suna karban yaudarar Shaitan da marmari. Suna bin sha'awa, suna kuma aikata zunuban da suka jawo ma kafirai hukumci.

Masu koya ma mutane su rena dokokin Allah suna shuka rashin biyayya ne domin su girbe rashin biyayya. Bari a kawar da halin da dokar Allah ta dora gaba daya, nan da nan kuma za a rabu da dokokin mutane. Da shike Allah Ya hana rashin aminci, kiyashi, karya da yaudara, mutane suna shirye su tattake dokokinsa domin suna hana su ci gaba a duniya. Amma sakamakon watsar da umurnin nan zai zama abin da bas u zata ba. Idan dokar ba ta aiki,don me za a ji tsoron ketarewa? Duniya za ta kasane ba tsaro. Mutane za su kwace dukiyar makwabtansu da karfi, masu karfi ne kuma za su fi arziki. Ba za a girmama rai kansa ba ma. Alkawalin aure ba zai kasance garkuwa da zai tsari iyali ba kuma. Mai-karfi, in ya ga dama sai ya dauki matar makwabcinsa da karfi. Zai kawar da doka ta biyar tare da ta hudu. Yara ba za su yi shakkar dauke ran iyayensu ba, idan wannan zai sa su sami muradum zukatansu. Duniya da ta waye za ta zama matattarar mafasa da masu-kisan gilla, kuma salama da hutu da farinchiki za su watse daga duniya.

Yanzu ma koyaswar cewa an ‘yantar da mutane daga biyayya ga dokar Allah ta nakasa tunanin halin kirki ta kuma bude ambaliyar zunubi a duniya. Rashin bin doka da rashawa suna kwararo mana kamar igiyar ruwa mai-nutsarwa. Shaitan yana aiki cikin iyali. Tutarsa tana kadawa har cikin iyalan Kirista. Akwai kishi da mugun zato, riya, rashin jituwa, tashin hankali, cin amana, da biyan muradin sha’awa. Dukan tsarin kaidodi da koyaswoyin addini da ya kamata su zama harsashe da ginshikin rayuwar jama’a, yana kaduwa ne, ya kusan faduwa zuwa hallaka. Masu aikata munanan laifuka, sa’anda aka kai su kurkuku sabo da laifukansu, sau da yawa akan ba su kyautuka da kulawa sai ka ce sun yi wani fice. Ana labarta halayensu da laifofinsu. Masu watsa labarai sukan labarta muguntansu dalla-dalla, ta haka kuma su sa wadansu shiga aikata yaudara, fashi, da kisa; Shaitan kuma yakan ji dadin nasarar dabarunsa. Yawaitar mugunta, daukan rai barkatai, yawaitar rashin kamewa da kawane nau’in zunubi, ya kamata su falkas da dukan masu-tsaron Allah su nemi sanin abin da za a iya yi don tsayar da mugunta.

Kotuna suna rashawa da cin hanci. Shugabanni suna kwadayin abin da za su samu suna kuma son sha’awa da jin dadi. Rashin kamewa ya duhunta tunanin mutane da yawa, ta yadda Shaitan yana mallakarsu. Ana rudar da masu-shari’a ana kuma ba su cin hanci. Maye da holewa da kishi da kowane irin rashin gaskiya suna cikin wadanda ya kamata su tabbatar da kiyaye dokoki. “Adalchi yana tsaye daga nesa; gama gaskiya ta fadi a chikin hanya, adilchi kuma ba ya iya shigowa ba.” Ishaya 59:14.

Zunubi da duhun ruhaniya da suka kasancewa a kalkashin mulkin Rum sakamakon danne Littafin ne da ta yi; amma ina za a sami sanadin rashin aminci, da kin dokar Allah, da kuma lalacewa da aka samu a kalkashin hasken bishara a zamanin ‘yancin addini? Yanzu da Shaitan ba zai sake iya rike duniya kalkashin mulkinsa tawurin hana Littafin ba, ya koma ga wadansu dabaru don cim ma manufa dayan. Hana amincewa da Littafin yakan cika burinsa ya kuma bata Littafin kansa. Ta wurin koyar da cewa dokar Allah ba ta aiki yana sa mutane su ketare ta kamar ma basu san ta ba. Yanzu kuma, kamar da, ya yi aiki ta wurin ekklesiya domin ci gaba da nufinsa. Kungiyoyin addini na yau sun ki jin gaskiya mara dadi da ake gabatarwa cikin Littafin, kuma cikin yaki da gaskiyan sun amshi fasara suka kuma dauki matsayin da ke baza iri na shakka.

Da shi ke sun manne ma kuskuren paparuma na cewa matattu sun san abin da ke faruwa, sun ki abin da shi ne kadai garkuwa mai-kariya daga sihiri. Koyaswar azaba ta har abada ta sa mutane da yawa sun bar gaskata Littafin. Kuma yayin da a ke iza mutane su kiyaye doka ta hudu, akan tarar cewa tana umurta cewa a kiyaye Assabbat na rana ta bakwai ne, kuma don kwace kansu daga abin da ba sa so su yi, shahararrun malamai da yawa suna cewa dokar Allah ta dena aiki. Ta hakanan suna watsar da dokar da kuma Assabbat tare. Sa’anda aikin inganta Assabbat ke ci gaba, kin dokar Allahn nan don ana so a rabu da bukatun doka ta hudu zai kusan mamaye duniya. Koyaswoyin shugabannin addini sun bude kofa domin rashin aminci, da sihiri, da kuma rena doka mai-tsarki ta Allah, kuma kan

shugababbin nan ne nawaya mai-ban tsoro ta rataya sabo da zunubin da ake yi a cikin Kirista.

Duk da haka, mutanen nan suna cewa lalacewa da ke yaduwa da saurin nan sakamakon bata abinda suke kira “Assabbat na Kirista” ne, kuma wai tilasta kiyaye Lahadi zai inganta halayyan kirki cikin jama’a. Ana wannan zancen, musamman a Amerika, in da aka yi wa’azin Assabbat na gaskiyan. A nan, aikin kamewa, daya daga cikin canje canje mafi muhimminci, akan garwaya shi da koyaswar Lahadi, masu koyar da zancen Lahadin kuma sukan ce suna kokari ne su kara ci gaban jama’a, kuma wadanda suka ki hada kai da su akan zarge su da cewa magabtan shirin kamewa ne. Amma hada yunkurin tabbatar da kuskure da wani aikin wanda shi kansa yana da kyau, ba zai canja kuskuren ba. Za mu iya badda kamanin guba tawurin garwaya ta da abinci mai-kayu, amma ba za mu sake yanayinsa ba. Sabanin haka ma, dafin zai kara zama da hatsari da shike ana iya cinsa cikin rashin sani. Wata dabarar Shaitan ita ce garwaya karya da daidai gaskiyar da za ta sa a yarda da ita. Shugabannin inganta Lahadin za su iya koyar da canje canjen da mutgane ke bukata, kaidodi da suka je daidai da Littafin, duk da haka da shike tare da su akwai abin da ya saba ma dokar Allah, bayinsa ba za su hada kai da su ba. Ba abinda zai halatta masu soke dokokin Allah domin umurnin mutane.

Ta wurin kurakurai biyu din nan, rashin mutuwar mai-rai da tsarkin Lahadi, Shaitan zai kawo mutane kalkashin rudinsa. Yayin da na farkon yana kafa tushen sihiri, na biyu din yana hada dankon amincewa da Rum. Masu Kin mulkin paparuma a Amerika ne za su jagoranci mika hannu zuwa ketaren teku su kama hannun sihiri; za su ketare rami mara matuka su kama hannu da mulkin Rum, kuma kalkashin tasirin hadin kan nan na sassa uku, kasan nan za ta bi matakan Rum wajen tattake ‘yancin lamiri.

Da shi ke sihiri ya fi kwaikwayon Kiristanci a suna na zamanin nan, yana da karfin rudi da kuma jawowa cikin tarko. Shaitan kansa zai tuba, bisa ga yanayin al’amuran zamanin. Zai bayana da kamanin malaikan haske. Tawurin wakilcin sihiri, za a aikata al’ajibai, za a warkar da marasa lafiya, za a kuma yi ababa na ban mamaki zahiri. Kuma da shike ruhohin za su ce suna da bangaskiya ga Littafin suna kuma girmama ekklesiya, za a yarda da aikinsu a matsayin bayana ikon Allah.

Layin bambanci tsakanin masu cewa su Kirista ne da marasa addini yanzu ba shi da yawa. Membobin ekklesiya suna kaunar abin da duniya ke kuana, kuma suna shirye su hada hannu da su, Shaitan kuma ya kuduri aniyar hada su wuri daya, ta hakanan kuma shi karfafa shirinsa tawurin tura kowa cikin harkar sihiri. ‘Yan paparuma masu alfahari da al’ajibai a matsayin alamar ekklesiya ta gaskiya, nan da nan ikon nan mai-aikata al’ajibai zai rude su, masu-Kin ikon paparuma kuma, da shike sun rigaya sun yi watsi da garkuwar gaskiya, su ma za a rude su. ‘Yan paparuma da masu Kin ikon paparuma da ‘yan duniya duka za su karbi surar ibada ba tare da ikonta, za su kuma ga wannan hadin kan kamar

babban yunkuri ne na tubar da duniya da kuma shigo da shekaru dubun da suka dade suna jira.

Ta wurin sihiri Shaitan yana bayanuwa da kamanin mai-taimakon ‘yan Adam, yana warkar da cututtukan mutane, yana kuma cewa wai ya kawo wani sabon tsarin ibada ta addini, amma kuma yana aikin hallakaswa ne. Jarabobinsa suna kai jama’a da yawa ga hallaka. Rashin kamewa yana kawar da tunani; fasikanchi da tashin hankali da zub da jini sukan biyo baya. Shaitan yana jin dadin yaki, domin yana ta da fushi mafi-muni, ya kuma tura mutane zuwa mutuwa cikin zunubansu. Nufinsa ne ya zuga al’ummai zuwa yaki da juna, domin ta hakanan zai iya karkata tunanin mutanen daga shiryawa don rana ta Allah.

Shaitan yana kuma aiki ta wurin halitta don tara girbinsa na rayuka da basu shirya ba. Ya rigaya ya yi nazarin asiran dakunan gwajin halitta, yana kuma anfani da dukan ikonsa don mallakar halitta duk inda Allah ya yarda masa. Sa’anda aka bar shi ya jarabci Ayuba, nan da nan aka share garkunan shanu da na tumaki, bayi, gidaje da ‘ya’ya, damuwa daya bayan daya kamar kyaftar ido. Allah ne yake kare halitunsa yana kange su daga ikon mai-hallakaswan. Amma Kirista sun rena dokar Yahweh; kuma Ubangiji zai yi daidai abinda Ya ce zai yi - zai janye albarkunsa daga duniya ya kuma cire tsaronsa daga wadanda ke tawaye ga dokarsa suna kuma koya ma wadansu, suna tilasta su yin haka. Shaitan yana mulki kan dukan wadanda Allah bai tsare su mausamman ba. Zai taimaki wadansu, ya ba wadansu ci gaba domin ya ci gaba da manufofinsa, zai kuma kawo ma wadansu wahala ya kuma sa su ji kamar Allah ne yake wahal da su.

Yayin da yake bayanuwa ga ‘ya’yan mutane kamar babban mai-maganin da zai iya warkar da dukan cututtukansu, za ya kawo ciwo da bala’i, har sai an rushe manyan birane suka zama kango. Ko yanzu ma yana aiki. Cikin hatsaruka da masifu na teku da na kasa, cikin gobara, cikin guguwa masu karfi da mahaukatan iskoki tare da kankara, da ambaliya da munanan iskan ruwa masu barna, da igiyoyin ruwan teku masu fushi, da rawan duniya, ko ina, ta hanyoyi dubu kuma, Shaitan yana nuna ikonsa. Yakan share anfanin gona da ya fara nuna, sai yunwa da wahala su biyo. Yana zuba ma iska wani guba mai-kisa, dubbai kuma sukan hallaka saboda annobar. Ababan za su rika kara yawaita da halaka. Hallaka za ta abko ma mutane da dabbobi. “Kasa tana makoki tana yaushi,” “madaukaka na wajen jama’a suna kasala. Kasa kuma ta kazamtu kalkashin mazamnanta; saboda sun ketare dokokin, sun sake farilla, sun ta da madawamin alkawali.” Ishaya 24:4,5.

Sa’an nan babban mai-yaudaran zai so ya nuna ma mutane cewa masu bautar Allah ne su ke jawo wahalolin nan. Wadanda suka jawo fushin Allah za su zargi wadanda biyayyarsu ga dokokin Allah tana tsauta ma masu ketare dokokin, cewa su ne suka jawo masu masifun. Za a ce mutane suna yi ma Allah laifi ta wurin ketare assabbat na Lahadi, cewa zunubin nan ya jawo masifu da ba za su kare ba har sai an tilasta kiyaye doka ta hudu, wanda ke lalatar da kiyayewar Lahadi, su ne ke wahal da mutanen, suna hana su dawowa ga alherin Allah da ci gaba a duniya. Ta hakanan zargin da aka yi ma bawan Allah a da, za

a maimaita shi, kuma sabo da dalilai tabbatattu ma. “Ya zama kwa, sa’anda Ahab ya hangi Iliya, Ahab ya che masa, kai ne, kai mai-wahal da Israila? Ya amsa, Ba ni na wahalda Israila ba, amma kai ne da gidan ubanka, da shi ke kun rabu da dokokin Ubangiji, ka kwa bi Baalim.” 1Sarakuna 18:17,18. Sa’anda aka ta da fushin mutanen tawurin zarge zargen karya, za su dauki mataki game da jakadun Allah daidai irin wanda Israila mai-ridda ta dauka game da Iliya.

Ikon aikata al’ajibai da aka nuna tawurin sihiri zai yi tasiri sabanin wadanda suka zabi biyayya ga Allah maimakon mutane. Sadarwa daga ruhohi zai ce Allah ya aike su su nuna ma masu-kin Lahadi kuskurensu, su kuma tabbatarda cewa ana biyayya ga dokokin kasa kamar dokokin Allah. Za su yi bakincikin muguntar da ke cikin duniya su kuma goyi bayan shaidar mallaman addini cewa lalacewar halayen kirki sakamakon bata Lahadi ne. Fushin da za a zuga sababinin dukan wadanda suka ki shaidar su mai-yawa ne.

Hanyar Shaitan a fadan karshen nan da mutanen Allah daya take da wadda ya bi a farkon babban jayayyar a sama. Ya ce wai yana neman ci gaban zaman lafiyan gwamnatin Allah ne, alhali yana iyakar kokarinsa ne ya tabbatar da rushewarsa. Kuma wannan aikin ne ya ce malaiku masu biyayya ke yi. Hanyar rudin nan ne ta mamaye tarihin Ekklesiyar Rum. Ta ce ita ce ke wakiltar sama, alhali tana kokarin daukaka kanta fiye da Allah tana kuma so ta canja dokarsa. Kalkashin mulkin Rum wadanda suka mutu saboda amincinsu ga bishara an zarge su cewa masu-aikata mugunta ne, aka ce suna hada kai da Shaitan, aka kuma bi kowace hanya don rufa su da kunya, don a sa mutane da su kansu ma su ga kamar su ne masu-laifi mafi-muni. Haka zai kasance yanzu, yayin da Shaitan ke so ya hallaka masu girmama dokar Allah, za sa a zarge su da ketare doka, cewa su masu rena Allah ne suna kuma jawo hukumci ga duniya.

Allah ba ya taba tilasta lamiri ko zuciya, amma Shaitan kullum, domin neman mallakar wadanda ba zai iya rudinsu ba, yana tilastawa ne ta wurin zalunci. Ta wurin tsoro ko tilastawa yana kokarin mallakar lamiri, ya kuma samo ma kansa biyayya daga mutane. Don cimma wannan, yana aiki ta wurin hukumomin addini da na kasa, yana zuaga su su tabbatar da dokokin mutane maimakon dokar Allah.

Za a zargi masu girmama Assabbat na Littafin cewa magabtan doka da oda ne su, masu rushe halayyan kirki na jama’a, suna jawo hargitsi da lalacewa, da kuma hukumcin Allah bisa duniya. Za a ce da kyawawan halayensu matsanantan halaye, da taurin kai, da rena hukuma. Za a zarge su da rashin biyayya ga gwamnati. Masu wa’azi da suka ki biyayya ga dokar Allah za su bayana a bagadi cewa Allah ne ya umurta a yi biyayya ga hukumomin kasa. A majalisun dokoki da kotunan shari’a za a zargi masu-kiyaye doka a kuma hukumta su. Abinda basu fada ba za a ce sun fada; za a karkata manufofinsu a ba su ma’ana mafi muni.

Sa’anda ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma suka ki bayanai masu-goyon bayan dokar Alllah, za su so su rufe bakunan wadanda ba za su iya ka da su ta wurin Littafin ba. Ko da shike suna rufe idonsu daga batun, yanzu suna daukan wata hanya da za ta kai ga zaluntar wadanda suka ki yin abin da sauran Kiristan duniya ke yi, suna kuma amincewa da sharuddan Assabbat na paparuma.

Masu martaba na ekklesiya da na kasa za su hada hannu su ba da toshiya ko su rinjayar ko su tilasta dukan mutane su girmama Lahadi. Da shi ke babu goyon bayan Allah za a kafa dokoki na danniya. Toshiya ta siyasa tana lalata kaunar adalci da girmama gaskiya; kuma har a Amerika ma mai-‘yanci, shugabanni da masu-yin dokoki, don neman goyon bayan jama’a, za su amince da sabuwar dokar da za ta tilasta kiyaye Lahadi. ‘Yancin lamiri, wanda da wahala sosai aka samo shi, ba za a girmama shi kuma ba. A yakin da ba da jimwa ba za a yi, za mu ga kwatancin kalmomin annabin cewa: “Sai dragon ya hasala da gaske da machen, ya tafi kuma domin shi yi yaki da sauran zuriyanta, wadanda su ke kiyaye dokokin allah, suna rike da shaidar Yesu.” Ruya 12:17.

Babi na 37—Littafi, Mai-tsaro.

“A komo bisa shari’an da shaidan! Idan basu fadi bisa ga wannan magana ba, hakika babu wayewan gari a garesu ba.” Ishaya 8:20. Ana nuna ma mutanen Allah Littafin a matsayin tsaronsu daga tasirin mallaman karya da ikon rudi na ruhohin duhu. Shaitan yana anfani da kowace dabara don hana mutane sanin Littafin, da shi ke kalamansa suna bayana rudinsa. A kowace falkaswar aikin Allah sarkin mugunta yakan kara himmar ayukansa, yanzu yana tayar da iyakar kokarinsa domin fama ta karshe tsakaninsa da Kristi da masu binsa. Babban rudi na karshe zai bayana a gabanmu ba da jimawa ba. Antichrist zai aikata al’ajiban a gabanmu. Jabun zai yi kama da ainihin sosai ta yadda ba zai yiwu a bambanta su ba sai ta wurin Littafin. Dole a gwada kowace shaida da kowace magana da shaidar Littafin.

Za a yi hamayya da masu kokarin yin biyayya ga dukan dokokin Allah, a kuma yi masu ba’a. Za su iya tsayawa cikin Allah ne kadai. Dominsu jimre gwajin da ke gabansu, dole su gane nufin Allah yadda aka bayana cikin maganarsa, za su iya girmama Shi kawai idan sun sami kyakyawar fahimtar halinsa da gwamnatinsa da manufofinsa ne kadai, suka kuma yi anfani da su. Sai dai wadanda suka karfafa tunaninsu da gaskiya na Littafin ne kadai za su jimre babban fada na karshen. Ga kowane mai-rai gwajin zai zo: ko zan yi biyayya ga Allah maimakon mutane? Sa’ar hukumcin ma ta zo yanzu. Ko sawayenmu sun kafu bisa Dutsen maganar Allah da ba ta sakewa? Ko muna shirye mu tsaya da karfi mu kare dokokin Allah da imanin Yesu?

Kafin giciyewarsa Mai-ceton ya bayana ma al’majiransa cewa za a kashe shi ya kuma sake tashi daga kabarin, kuma malaiku suna wurin domin su fassara kalmominsa ga tunanin almajiran da zukatansu. Amma almajiran suna begen kubutarwa daga bautar Romawa ne, kuma ba su iya yarda da tunanin cewa shi wanda dukan begen su ke kan sa zai yi mutuwar wulakanci ba. Kalmomin da ya kamata su ji sun fice daga tunaninsu; sa’an da lokacin gwaji ya zo kuwa, ya tarar ba su shirya ba. Mutuwar Yesu ta rushe begensu kaman bai gargade su kafin lokacin ba. Haka ne cikin annabci an bude mana a bayane abin da ke zuwa kamar yadda maganar Kristi ta bayana ma almajiran. Al’amuran da ke da nasaba da rufewar gafara da aikin shiryawa domin lokacin wahala suna bayane sarai. Amma da yawa ba su fahimci muhimman gaskiyan nan ba sai ka ce ba a taba bayana su ba. Shaitan yana kallo domin ya dauke kowace ganewa da za ta sa su zama da hikima zuwa ga ceto, kuma lokacin wahala zai same sub a a shirye ba.

Sa’anda Allah Ya aika ma mutane fadaka masu muhimmincin da ya sa an nuna kamar malaiku masu firiya a tsakiyar sararin sama ne ke shelarsu, yana bidar kowane mai-tunani ya saurari sakon. Hukumci mai-ban tsoro da aka furta kan sujada ga bisan da gumkinsa (Ruya 14:9-11) ya kamata ya kai kowa ga nazarin annabci domin a san ko menene shaidar bisan, da yadda za a iya kin karban ta. Amma yawancin mutane suna kin sauraron gaskiya,

suna komawa ga tatsuniyoyi. Manzo Bulus da ya hangi kwanakin karshe ya ce: “Gama kwanaki za su zo da ba za su daure da koyaswa mai-lafiya ba.” Timothawus II, 4:3. Wannan lokacin ya zo. Yawanci ba sa son gaskiya ta Littafin, da shi ke ta na tsoma baki cikin muradan zuciya ta zunubi mai-kaunar duniya; Shaitan kuma yana tanada rudin da su ke kauna.

Amma Allah yana so ya sami mutane a duniya da za su rike Littafin kadai a matsayin ma’aunin dukan koyuaswoyi da ginshikin kowane canji. Ra’ayin masana, ra’ayin kimiyya, kaidodi ko matakai na majalisun ekklesiyoyi, da duk yawansu da bambance bambancensu kamar ekklesiyoyin, da muryar masu rinjaye ko dayan wadannan ko ma dukansu bai kamata su zama shaidar sahihancin wani batu na imanin addini ba. Kafin a amince da kowace koyaswa ko umurni bari mu tabbatar cewa “in ji Ubangiji” ya goyi bayanta.

Shaitan kowane lokaci yana kokarin jan hankali daga Allah zuwa mutum. Yana jan mutane su dubi bishops da pastoci da shehunan mallaman tauhidi a matsayin masu bishewarsu maimakon binciken Littafin domin gano ma kansu aikinsu. Sa’an nan tawurin mallakar zukatan shugabannin nan zai iya juya jama’a yadda ya ga dama.

Sa’anda Kristi ya zo domin ya fadi kalmomi na rai, talakawa sun saurare shi da farinchiki, kuma priestoci da shugabanni da yawa sun gaskata shi. Amma shugabannin priestocin da manyan kasa suka dukufa wajen kushe koyaswoyinsa da warware su kuma. Ko da shi ke an kasa yin nasara da dukan kokarinsu na neman dalilan zargi a kansa, ko da shi ke kuma sun ji tasirin ikon Allah da hikimarsa cikin kalmominsa, duk da haka suka kulle kansu cikin rashin adalci, suka ki bayananniyar shaidar Masiyanan sa, domin kada a tilasta su zama almajiransa. Masu adawan nan da Yesu mutane ne da an rigaya an koya ma sauran mutane, tun suna yara, su daukaka su, kuma sun saba amincewa da mulkinsu ba jayayya. Suka tambaya, “Yaya aka yi shugabanninmu da marubuta masana ba su gasktata Yesu ba? Da shi ne Kristi din da mutane masu ibadan nan basu karbe shi ba? Tasirin irin wadnnan mallaman ne ya jawo al’ummar Yahudawa ta ki Mai-fansarsu.

Har yanzu mutane da yawa masu nuna cewa su masu-ibada ne, suna nuna irin ruhun nan da ya motsa priestocin nan da shuganbannin nan. Suna kin binciken shaidar Littafin game da gaskiya na musamman domin zamanin nan. Su kan dubi yawansu da arziki da son da ake yi masu, sai su rena kalilan din nan matatalauta, marasa farinjini, masu imanin da ya raba su da sauran duniya.

Kristi ya hangi cewa ikon da marubuta da Farisawa suka ba kan su ba zai kare sa’anda Yahudawa sun warwatsu ba. Ya hangi aikin daukaka ikon mutum don mulkin lamiri, wanda ya kasance mumunan la’ana ga ekkesiya cikin dukan sararaki. Sokarsa ga marubuta da Farsawa, da gardadinsa ga mutane, cewa kada su bi makafin shugabbanin nan, an rubuta su don fadaka ne ga sararaki da ke zuwa.

Ekklesiyar Rum ta kebe ma priestocinta ne ‘yancin fassara Littafin. A kan cewa ma’aikatan bishara ne kadai sun iya bayana maganar Aallah, ana hana sauran mutane Littafin. Ko da shi ke canjin ya ba da Littafin ga kowa duk da haka kaidan nan da Rum ta rike tana hana jama’a da yawa a ekklesiyoyi masu Kin ikon paparuma bincika Littafin don kansu. Ana koya masu su karbi koyaswoyinta yadda ekklesiya ta fassara su; kuma akwai dubbai da ba su isa su karbi wani abu ba, komi yadda Littafin ya bayana shi, idan ya saba ma koyaswar ekklesiyarsu.

Duk da cewa Littafin ya cika da gardadi game da mallaman karya, mutane da yawa suna shirye su ba da kiyayewar rayukansu ga masu aikin bishara. Yau akwai dubban masu addini da ba za su iya ba da wata hujjar bangskiyan da su ke da ita ba sai da cewa shugabannin addininsu ne suka koya masu hakanan. Su kan wuce koyaswoyin Mai-ceton basu kula ba ma, su kuma ba da cikakkiyar amincewa ga maganar pastocinsu. Amma ko pastocin ba sa kuskure? Yaya za mu mika rayukanmu ga bishewarsu in ba mun sani ne daga maganar Allah cewa masu kai haske ne su ba? Rashin karfin halin rabuwa da hanyar da duniya ta saba da ita yakan sa mutane da yawa su bi matakan masana, kuma sabo da rashin son bincikawa da su ke da shi, suna kara dauruwa da sarkokin kuskure ne. Suna gani cewa gaskiya don zamanin nan tana bayane a Litafin, kuma su na jin ikon Ruhun Mai-tsarki cikin shelarta da a ke yi; duk da haka suna yarda hamayyar masu bishara ta juya su daga hasken. Ko da shi ke tunaninsu da lamirinsu sun yarda, rudaddun mutanen nan basu isa su yi tunani dabam da na paston ba, don haka ana sadakar da ra’ayin kansu da muradan zukatansu ga rashin ba da gaskiya da girman kai da kiyayyar wadansu.

Hanyoyin da Shaitan ke aiki ta wurin tasirin mutane don daure mutane suna da yawa. Yana rike jama’a da yawa wurinsa tawurin manna su da kirtanin soyayya ga masu gaba da giciyen Kristi. Ko da mene ne dangantakan nan, na iyaye ne, na ‘ya’ya ne, na aure ne, ko na zama da jama’a ne, sakamakon daya ne, masu hamayya da gaskiya su na anfani da ikonsu don mulki bisa lamiri, kuma rayukan da aka rike hakanan ba su da isashen karfin hali ko ‘yancin kai da za su yi bayayya ga bangaskiyar kansu.

Gaskiya da darajar Allah ba su rabuwa; ba shi yiwuwa garemu, da Littafin kusa da mu, mu girmama Allah tawurin ra’ayoyi na kuskure. Da yawa sun a cewa wai ba abin da ka gaskata ne muhimmin ba, muddan dai rayuwarka daidai ne. Amma abin da aka gaskata ne yake sifanta rayuwar. Idan muna iya samun haske da gaskiya, kuma muka ki anfani da zarafin ji da na ganin shi, mun ki shi ke nan, mun zabi duhu maimakon haske. “Akwai wata hanya wadda ta ke da alamar kirki ga mutum, amma matukatatta tafarkun mutuwa che.” Misalai 16:25. Rashin sani ba hujja ce don kuskure ko zunubi ba, idan akwai dukan zarafin sanin nufin Allah. Mutum yana tafiya sai ya kai wani wuri inda akwai hanyoyi da yawa da allo na bishewa da ke nuna inda kowace hanya ta nufa. Idan ya rabu da allon bishewan, ya bi hanyar da ya ga ta dace mashi, ko da gaske yake yi, ba mamaki ya iske cewa bai bi hanyar da ta dace ba.

Allah Ya ba mu maganarsa domin mu san koyaswoyinta mu sani ma kan mu abin da yake bukata daga gare mu. Sa'an da masanin Attaurat din nan ya tambayi Yesu cewa; "Mi zan yi domin in gaji rai na har abada?," Mai-ceton Ya kai hankalinsa wurin Littafin, Ya ce: "Mi ke a rubuche a chikin Attaurat?, yaya ka ke karantawa?" Rashin sani ba zai zama hujja ga matasa ko tsofoffi ba ko kuma ya 'yantar da su daga horon da ya cancanci masu ketare dokar Allah, da shike a hannunsu akwai amintaciyar gabatarwar dokan da kai'dodinta da sharuddanta. Manufofi masu kyau kadai basu isa ba, yin abin da mutum ke gani daidai ne ko abin da pasto ya ce daidai ne kadai bai isa ba. Batun ceton ransa ake, kuma ya kamata ya bincike Littafin da kansa, komi karfin ra'ayinsa, komi tabbacin da yake da shi cewa ma'aikacin bisharan ya san gaskiya, wannan ba tushe ba ne. Yana da taswira da ke nuna kowace alama cikin tafiya zuwa sama, kuma bai kamata ya yi bara-da-ka ko kame-kame game da wani abu ba.

Babban aiki kuma aiki mai-girma ga kowane mai-tunani shi ne ganowa daga Littafin ko mene ne gaskiya, sa'an nan ya yi tafiya cikin haske ya kuma karfafa saura su bi kwatancinsa. Ya kamata kowace rana mu yi nazarin Littafin a natse, muna auna kowace magana muna kuma gwada nassi da nassi. Da taimakon Allah ya kamata mu sifanta ra'ayinmu don kanmu domin za mu amsa ma kanmu a gaban Allah.

Gaskiyan da Littafin ya bayana a fili, an jawo su cikin shakka da duhu, ta hannun masana wadanda, da son nuna cewa suna da hikima sosai, suke koyar da cewa Littafin yana da ma'ana mai-wuyan ganewa, ma'ana na sirri na ruhaniya wanda ba a gani daga harshen da aka yi anfani da shi. Mutanen nan mallaman karya ne. Irinsu ne Yesu ya ce suna da "Rashin sanin litattafai da ikon Allah." Markus 12:24. Ya kamata a fassara harshen Littafin bisa ga ma'anarsa na bayane ne, sai dai in an yi anfani da alama ko kamani. Kristi ya yi alkawali cewa; "Idan kowane mutum yana da nufi shi aika nufin Allah, shi za ya sani ko abin da ni ke koyaswa na Allah ne." Yohanna 7:17. Da mutane za su dauki Littafin daidai yadda take rubuce, da dai ba mallaman karya masu batar da mutane suna rikita tunaninsu, da an yi aikin da zai sa malaiku su yi murna ya kuma kawo dabban dubbai da yanzu su ke yawo cikin kuskure zuwa garken Kristi.

Ya kamata mu yi anfani da dukan tunaninmu cikin nazarin Littafin mu kuma ingiza tunaninmu ya fahimci muhimman ababa na Allah, kuma ba za mu taba manta cewa ainihin ruhun mai-koyon irin ruhun yaro ne na saukin horuwa da biyayya. Ba za a iya magance matsalolin Littafin ta hanyoyin da ake anfani da su don magance matsalolin ilimi ba. Bai kamata mu shiga nazarin Littafin da irin dogara da kai da ake shiga fannin kimiyya da shi ba, amma da ruhun tawali'u da koyuwa don samun sani daga Allah. In ba haka ba miyagun malaiku za su mankantar da tunaninmu su kuma taurara zukatanmu ta yadda gaskiya ba za ta yi tasiri gare mu ba.

Yawancin sassan Littafin da masana ke cewa asiri ne, ko kuma su wuce su wai ba su da anfani, suna cike da gargadi ga wanda aka koya masa a makarantar Kristi. Wani abin da

ya sa da yawa masanan tauhidi ba su da ganewa sarai na maganar Allah shi ne, su kan rufe idonsu ga ababan da ba sa so su aikata. Ganewar gaskiya ta Littafin ta dangana, ba lallai kan yawa da kuma kwarin tunanin da aka yi anfani da shi cikin binciken ba ne kamar kyakyawar manufa da himmatuwa wajen neman adalci.

Bai kamata a taba in nazarin Littafin ba addu'a ba. Ruhu Mai-tsarki ne kadai zai iya sa mu mu ji muhimmancin ababan da ke da saukin fahimta, ko kuma ya hana mu fizgo gaskiya masu wuyan ganewa. Aikin malaikan sama ne su shirya zuciya ta yadda za ta fahimci maganar Allah ta yadda za mu yi sha'awar kyaunta, mu koyu daga gardadinta, ko kuma motsu mu kuma karfafa daga alkawuranta. Ya kamata mu mai da addu'ar mai-zabura addu'armu, cewa: "Ka bude mani idanu na, domin in duba al'ajibai daga chikin shari'arka." Zabura 119:18. Jarabobi su kan yi kaman ba za a iya yin nasara da su ba saboda, tawurin rashin yin addu'a da nazarin Littafin, wanda aka jarabce shi ba zai iya tuna alkawuran Allah ya kuma tare Shaitan da makamai na Littafin ba. Amma malaiku su na kewaye da wadanda ke shirye a koyar da su ababan ruhaniya; kuma lokacin bukata. Don haka "Sa'an da magabchi ya shigo kamar rigyawa, ruhun Ubangiji za ya kafa tuta, ya yi gaba da shi." Ishaya 59:19.

Yesu ya yi ma almajiransa alkawali cewa: "Amma mai-taimako, watau Ruhu mai-tsarki, wanda Uban za ya aiko a chikin sunana, za ya koya maku abu duka, ya tuna maku kuma dukan abin da nafada maku." Yohanna 14:26. Amma dole sai an rigaya an ajiye koyaswoyin Kristi a zuciya domin Ruhu Mai-tsarki ya tuna mana a lokacin wahala. Dawuda ya ce: "Na boye maganarka chikin zuchiyata, domin kada in yi maka zunubi." Zabura 119:11.

Dukan wadanda ke kaunar rai na har abada ya kamata su yi hankali da shigowar shakka. Za a kai hari ga ainihin madogaran gaskiyar. Ba zai yiwu a boye ma habaici da yaudarar miyagun koyaswoyin nan masifa na kafircin zamani ba. Shaitan yakan sifanta jarabobinsa daidai da kowane sashi. Yakan tinkari jahilai da ba'a ko reni, amma yakan gwada masu ilimi da musu na kimiyya ne da babu 'yancin zurfin tunani, wadanda ya shirya domin ta da rashin amincewa ko rena Littafin. Har matasa marasa kwarewa ma su kan yi kokarin ta da shakka game da muhimman kaidodin Kiristanci, kuma rashin imanin matasan nan duk da rashin zurfinsa, yana da tasirinsa. Ta hakanan ana sa mutane da yawa su yi ma imanin ubaninsu ba'a, su kuma rena Ruhun alheri. Ibraniyawa 10:29. Rayuka da yawa da suka yi alkawalin daukakar Allah da albarka ga duniya sun la'antu da warin rashin imani. Dukan masu amincewa da fahariyar matakan tunanin mutum suka kuma ga kamar za su iya fassara asiran Allah har su kai ga gaskiya ba tare da taimakon hikimar Allah ba, sun nannadu cikin tarkon Shaitan ke nan.

Muna raye a zamani mafi ban tsoro na tarihin duniyan nan. Kadarar yawancin jama'an duniya ya kusa tabbatuwa. Lafiyar mu nan gaba da kuma ceton sauran rayuka sun dangana ga abin da mu ke yi yanzu ne. Muna bukatar bishewar Ruhun gaskiyar. Ya kamata kowane

mai-bin Kristi ya tambaya da gaske; “Ubangiji, me ka ke so in yi?” Muna bukatar kaskantar da kanmu a gaban Ubangii da azumi da addu’a, mu kuma yi bimbini kan maganarsa, musamman kan batutuwan hukumcin. Ya kamata yanzu mu bidi rayayyen dandano mai-zurfi game da al’amuran Allah. Ba mu da lokacin da za mu bata. Al’amura muhimmai suna faruwa kewaye da mu, muna filin Shaitan ne. Kada ku yi barci, masu-tsaro na Allah; magabcin yana boye kusa, yana shirye a kowane lokaci, ko za ka shagala ka yi gyangyadi, domin ya tasam maka ya mai da kai abincinsa.

Da yawa suna kuskure game da ainihin yanayinsu a gaban Allah. Suna tafa ma kansu game da ababa marasa kyau da ba sa yi, su kuma manta nagargarun ababa masu kyau da Allah ke bukata daga gare su, amma ba su yi ba. Cewa su itatuwa ne a lambun Allah kawai bai isa ba. Ya kamata su cika bukatarsa ta wurin haihuwar ‘ya’ya. Yana bidar lissafi daga wurinsu sabo da kasawansu su yi dukan alheran da ya kamata su yi ta wurin karfafawar alherinsa. A litattafan sama an rubuta su a matsayin masu bata kasa. Duk da haka ko wadannan din ma begensu bai kare kwata kwata ba. Ga wadanda suka wofinta jin kan Allah suka kuma wulakanta alherinsa, zuciyarsa mai-kauna mai-jinkirin fushi yana roko dai. “Domin wannan an che, ka falka, kai da ka ke barchi, ka tashi daga chikin matattu, Kristi kwa za ya haskaka bisa gareka. Ku duba fa a hankali yadda ku ke yin tafiya,… kuna rifta zarafi, tun da shi ke miyagun kwanaki ne.” Afisawa 5:14-16.

Sa’an da lokacin gwajin zai zo, za a bayana wadanda suka mai da maganar Allah kaidar rayuwarsu. Da damina ba bayanannen bambanci tsakanin itatuwa masu ganye kowane lokaci da sauran itatuwan, amma sa’anda iskar rani ta hura, masu-ganye kowane lokacin ba sa sakewa, yayin da sauran itatuwan a kan kakkabe ganyensu. Hakanan ba za a iya bambanta mai-zuciya ta karya daga ainihin Kirista ba yanzu, amma lokaci ya kusa da bambancin zai bayyana. Bari sabani ya taso, bari matsanancin ra’ayi da rashin sassauci su sake yawaita, bari a fara zalunci, masu zuciya biyu-biyu da masu riya kuwa za su kadu su kuma bar imanin; amma ainihin Kirista zai tsaya da karfi kamar dutse, bangaskiyarsa ta kara karfi, begensa ya kara haske, fiye da lokacin ci gaba.

Mai-zaburan ya ce: “Shaidunka su ne abin tunawa gareni.” “Ta wurin dokokinka ni ke samun fahimi; domin wannan fa na ki kowache hanyar karya.” Zabura 119:99,104.

“Mai-farin zuchiya ne mutum wanda yake samun hikima.” “Gama za ya zama kamar itachen da aka dasa a bakin ruwaye, wanda yana mika sawayensa a wajen kogi, ba za ya ji tsoro sa’anda zafin rana ke zuwa ba, amma ganyayensa za su yi kore, babu abinda za ya dame shi a shekaran fari, ba kwa za ya dena ba da yaya ba.” Misalai 3:13; Irmiya 17:8.

Babi na 38—Gargadi na Karshe

“Na ga wani malaika yana sabkowa daga sama, yana da hukumci da yawa; duniya kuma a haskaka domin daukakassa. Ya ta da murya da karfi, ya che, Fadadiya che, fadadiya che Babila babba, ta zama gidan aljannu, da madaurar kowane kazamin tsuntsu mai-ban kyama.” “Na ji wata murya daga sama ta che, Ku fito daga chikinta, ya al’ummata, domin kada ku yi taraya da zunubanta.” Ruya 18:1,2,4.

Nassin nan yana magana game da lokacin da za a maimaita sanarwar fadduwar Babila ne, da kari game da lalacewa da ke shiga kungiyoyi dabam dabam da suka hadu suka zama Babila, tun da aka ba da babban sakon nan da farko, da daminan 1844. An bayana munin yanayin addini ne anan. Duk sa’an da aka ki gaskiya, tunanin mutane zai kara duhunta, zukatansu za su kara tauri, har sai sun nutse cikin kangarar kafirci. Cikin tumbe ga gargadin da Allah Ya bayar, za a ci gaba da tattake daya daga cikin dokoki goma, har sai sun kai inda za su tsananta ma masu girmama dokar. Cikin rennin da ake yi ma maganar Kristi da mutanensa, ana wofinta Shi Kristi. Sa’an da ekklesiyoyi ke karban koyaswoyin sihiri, ana kawar da hanin da aka sa ma zuciyar mutumtaka, sa’annan addini zai zama alkyabbar da za ta boye zunubi mafi muni. Bangaskiya ga bayanuwar ruhohi ta kan bude kofa ga ruhohin lalata da koyaswoyin aljannu, ta hakanan kuma za a ji tasirin miyagun malaiku a cikin ekklesiyoyi.

Game da Babila a lokacin da annabcin nan ke magana akai, an ce: “Zunubanta sun kawo har ga sama, Allah kwa Ya tuna da muguntanta.” Ruya 18:5. Ta cika ma’aunin laifinta, hallaka kuma ta kusa fadowa a kanta. Amma Allah har yanzu yana da mutane a cikin Babila; kuma kafin zubowar hukumcin, dole za a fito da su domin kada su sa hannu cikin zunubanta, su kuma “sha rabon alobanta.” Don haka ne za a yi aikin nan da aka misalta da malaika da ya sauko daga sama, ya haskaka duniya da daukakarsa, da babbar murya kuma yana shelar zunuban Babila. Dangane da sakonsa, an ji: “Ku fito daga chikinta, jama’ata.” Sanarwoyin nan hade da sakon malaika na uku ne gargadi na karshe da za a ba mazamnan duniya.

Batun da duniya za ta fuskanta abin tsoro ne. Hukumomin duniya da suka hada kai don yaki da dokokin Allah za su umurta cewa “dukan mutane, kanana da manya, mawadata da mawadata da mataluta, yaya da bayi” (Ruya 13:16) su yi biyayya ga al’adun ekklesiya ta wurin kiyaye Assabbat na karya. Dukan wadanda sun ki yin biyayya za su gamu da horo daga gwamnati, a karshe kuma za a furta cewa sun cancanci mutuwa. A daya gefen kuma, dokar Allah game da ranar hutu ta Allah tana bukatar biyayya, tana kuma barazanar fushi kan dukan wadanda sun ketare umurninta.

Sa’anda an bayana batun a fili haka, duk wanda ya tattake dokar Allah domin ya yi biyayya ga dokar mutum, ya karbi shaidaar bisan ke nan; ya karbi alamar biyayya ga mulkin da ya yi biyayya gareta, maimakon Allah. Fadaka daga sama ita ce: “Idan kowane

mutum ya yi sujada ga bisan da gumkinsa, ya karbi shaida kuma a goshinsa ko a hannunsa, shi kuma za ya sha rowan annab na hasalar Allah wanda an shirya chikin koko na fushinsa," Ruya 14:9, 10.

Amma ba wanda za a sa ya sha fushin Allah sai an bayana masa gaskiya ga tunanin sa da lamirinsa, ya kuma ki. Akwai da yawa da basu taba jin gaskiya ta musamman don wannan zamanin ba. Ba a taba bayana masu doka ta hudu yadda ya kamata ba. Shi mai karanta kowace zuciya, yana kuma auna kowace manufa, ba zai bari a rudi wani mai-son sanin gaskiya game da batutuwan jayayyan ba. Ba za a tilasta ma mutane umurnin a duhunce ba. Kowa zai sami isashen haske da zai dauki mataki sa, da hankalinsa.

Assabbat ne zai zama babban magwajin biyayya da shike shi ne babban gaskiya da ake jayayya akai musamman. Sa'an da za a kawo gwaji na karshe ga mutane, sa'annan ne za a bamnamta tsakanin masu bauta ma Allah da marasa bauta masa. Yayin da kiyaye Assabbat na karya don biyayya ga dokar kasa sabanin doka ta hudu, zai zama shaidar biyayya ga wani mulki da ke jayayya da Allah. Kiyaye Assabbat na gaskiyar don yin biyayya ga dokar Allah shaida ce ta biyayya ga Mahalici. Yayin da wani bangare, ta wurin karban alamar biyayya ga ikokin duniya, take karban shaidar bisan, wani bangaren kuwa da ya zabi alamar biyayya ga ikon Allah, yana karban hatimin Allah ne.

Kafin nan, akan dauka cewa masu shelar sakon malaika na ukun nan masu ta da hankali ne kawai. Akan ce fadin da suke yi cewa rashin hakuri game da addini zai sake mamaye Amerika, kuma ekklesiya da kasar za su hada kai su tsananta ma masu kiyaye dokokin Allah, ba shi da tushe, kuma wai wauta ce, ana cewa wai kasan nan ba za ta taba zama wani abu dabam da abin da take ba, watau kasa mai-kare yancin addini. Amma yayin da ake baza zancen kiyayewar Lahadi, za a ga cewa lamirin da an dade ana shakkarsa yana tahowa, sako na ukun kuma zai haifar da sakamakon da kafin nan bai iya haifarwa ba.

A kowace sara Allah yakan aiko bayinsa su tsauta ma zunubi cikin duniya da cikin ekklesiya. Amma mutane suna so a fada masu ababa masu dadi ne, amma tsabar gaskiya ba ta karbuwa. Yan Canji da yawa, sa'an da suka shiga aikinsu, sun himmatu wajen anfani da dabara wajen tinkarar zunuban al'umma da na ekklsiya. Sun yi begen cewa ta wurin kwatancin rayuwa mai-tsabta ta Kirista za su dawo da hankulan mutane ga koyaswoyin Littafin. Amma Ruhun Allah Ya sauko masu yadda Ya sauko ma Iliya, ya motsa shi ya tsauta ma zunuban mugun sarki da jama'a mai-ridda; basu iya rabuwa da wa'azin bayanawan koyaswoyin Littafin ba, koyaswoyin da, da farko, sun yi shakkar bayanawa. Sun motsu su yi himmar bayana gaskiya da hatsarin da ke barazana ga rayuka. Suka furta kalmomi da Ubangiji Ya ba su, babu tsoron sakamakon yin haka, dole kuma mutanen suka saurari gargadin.

Ta haka aka yi shelar sakon malaika na ukun. Yayin da lokaci ke zuwa da za a ba da sakon da iko mafi girma, Ubangiji zai yi aiki ta wurin mutane masu tawali'u, ya jawo

hankulan masu himmatuwa ga hidimarsa. Ikon Ruhunsa ne zai horar da masu aikin, ba koyaswar makarantu ba. Masu bangaskiya da addu'a za su motsu su tafi da himma mai-tsarki, suna shelar kalmomin da Allah ke ba su. Za a fallasa zunuban Babila. Sakamako masu ban tsoro na tilasta hidimomin ekklesiya ta wurin ikon gwamnatin kasa, da shigowar sihiri, da ci gaban ikon paparuma a sace, duka za a fallasa su. Ta wurin gargadin nan za a motsa mutane.

Dubban dubbai wadanda basu taba jin irin kalmomin nan ba za su ji. Da mamaki za su ji shaida cewa ekklesiya ce Babila fadaddiya sabo da kurakuranta da zunubanta, sabo da ta ki gaskiyan da aka aika mata daga sama. Sa'an da mutane ke zuwa wurin mallaman su na da, da tambaya cewa, Ababan nan haka ne? Shugabannin addinin su kan ba da tatsuniyoyi, su yi annabcin ababa masu dadi, domin su kwantar da tsoronsu da lamirinsu da aka falkas. Amma da shike da yawa sun ki amincewa da ikon mutane, suka bidi "In ji Ubangiji," sanannun shugabannin, kamar Farisawa na da, cike da fushi sabo da an rena ikonsu, za su ce sakon na Sahitan ne, su kuma ingiza masu son zunubi su rena su kuma tsananta ma masu shelar sakon.

Sa'an da jayayyar ta kai har kauyuka, ana kuma jan hanulan mutane zuwa ga dokar Allah da aka tattake, Shaitan zai motsa. Ikon da ke cikin sakon zai haukatar da masu hamayya da shi sakon ne. Ma'aikatan bishara za su yi iyakar kokarin su don su rufe hasken, domin kada ya haskaka tumakinsu. Ta kowace hanya, za su yi kokarin danne kowace magana game da muhimman batutuwan nan. Ekklesiya za ta bidi taimakon karfin gwamnati, kuma a wannan aiki, 'yan paparuma da masu Kin ikon paparuma za su hada hannu. Yayin da aikin tilasta kiyaye Lahadi ke kara karfi da hima, za a yi anfani da doka kan masu kiyaye dokar. Za a yi masu barazana da tara, da kurkuku, wadansu kuma za a yi masu tayin matsayi mai-tasiri da wadansu lada domin a sa su ki imaninsu. Amma amsarsu kullum ita ce: "Ku nuna mana kuskuren mu daga maganar Allah." Magana dayan ne Luther ya yi. Wadanda za a gurbanar da su gaban kotuna za su nuna sahihancin gaskiyaar, wadansu da ke sauraronsu kuma za su kai ga daukan kudurin kiyaye dukan dokokin Allah. Ta hakanan za a kawo ma dubbai haske.

Biyayya ga maganar Allah bisa ga lamiri za a mai da shi tawaye. Da shike Shaitan zai makantar da su, iyaye za su tsananta ma 'ya'yansu masu ba da gaskiya; mai-gida ko uwar gida za su muzguna ma bara mai-kiyaye dokar. Za a manta da soyayya; za a hana ma 'ya'ya gado a kuma kore su daga gida. Kalmomin Bulus za su cika zahiri cewa: "I, kuma dukan wadanda su ke so su yi rayuwa mai-ibada chikin Kristi Yesu za su sha tsanani." Timothawus II, 3:12. Sa'anda masu gaskiya suka ki girmama assbbat na Lahadi, za a jefa wadansu cikin kurkuku, a kori wadansu daga kasarsu, a kuma maida wadansu kamar bayi. Ga hikimar mutum duk wannan yanzu kamar ba abu ne mai yiwuwa ba; amma sa'an da an janye Ruhun Allah daga mutane, suka kasance kalkashin mulkin Shaitan makiyin dokokin

Allah, za a yi ababa da ba a saba gani ba. Zuciya za ta iya cika da keta idan aka cire kaunar Allah da tsoronsa.

Yayin da guguwar ke tahowa, jama'a da yawa da ke cewa sun gaskata sakon malaika na ukun, amma basu tsarkaku ta wurin biyayya ga gaskiya ba, za su rabu da matsayinsu, su shiga jerin 'yan adawa. Ta wurin hada kai da duniya da samun rabon ruhun duniya, yanzu suna ganin al'amuran kusan yadda duniya ke kalonsu; kuma sa'an da aka kawo gwaji, suna shirye su zabi gefenda yawanci suke. Masu baiwa da iya magana wadanda ke son gaskiya za su rudi mutane su batar da su. Za su zama magabtan 'yan'uwansu na da. Sa'an da aka kawo masu kiyaye Assabbat gaban kotuna sabo da bangaskiyarsu, 'yan riddan nan ne za su zama wakilai mafi anfani ga Shaitan da za su yi masu karya su zarge su kuma, tawurin rahotanin karya kuma su fusata shugabani game da su.

A lokacin zaluncin nan, za a gwada bangaskiyan bayin Ubangiji. Da aminci suka ba da gargadin, su na duban Allah da maganarsa kadai. Ruhun Allah Ya motsa zukatansu, suka yi magana. Sa'an da himma mai-tsarki ta motsa su, sun shiga aikinsu ba tare da lissafta skamakon furta ma mutanen maganan da Allah Ya ba su ba. Basu dubi anfanin kansu na duniya ba, ko kuma su yi kokarin kare sunansu ko rayukansu ba. Duk da haka, sa'an da guguwar hamayya da reni ta abko masu, wadansu za su firgita har su ce: "Da mun hangi sakamakon kalmominmu, da mun yi shuru." Matsaloli sun kewaye su. Shaitan ya na kai masu hari da jarabobi masu tsanani. Aikin da suka kama kaman ya fi karfin iyawarsu. Ana yi masu barazanar hallaka. Marmarin da su ke da shi a da, ya tafi; duk da haka ba za su iya juyawa baya ba. Sa'an nan, idan suka gane kasawarsu, za su gudu zuwa wurin Madaukaki domin neman karfi. Za su tuna cewa kalmomi da suka furta nasu ba ne, amma na Shi wanda Ya umurce su su ba da gargadin ne. Allah Ya sa gaskiya cikin zukatansu, kuma ba su iya kin shekar ta ba.

Mutanen Allah sun fuskanci gwaji dayan a sararrakin baya. Wycliffe, Huss, Luther, Tyndale, Baxter da Wesley, sun koyar da cewa a gwada kowace koyaswa da Littafin, suka bayana cewa za su rabu da duk wani abin da Littafin ya hana. An tsananta ma mutanen nan da fushi sosai; duk da haka basu dena bayana gaskiyar ba. Lokuta dabam dabam a tarihin eklesiya sun kasance da wata gaskiya ta musamman da aka shirya don bukatun mutanen Allah a lokacin. Kowace gaskiya ta yi nasara bisa kiyayya da adawa; wadanda suka karbi hasken gaskiyar, an jaarabce su, aka kuma tsananta masu. Ubangiji yakan ba da gaskiya ta musamman domin mutane a lokacin tashin hankali. Wa ya isa ya ki baza ta? Ya umurci bayinsa su bayana gayyatar jinkansa ta karshe ga duniya. Ba za su iya yin shuru ba, sai dai su rasa rayukansu. Jakadun Kristi basu damu da batun sakamako ba. Dole za su cika aikinsu, su bar sakamakon a hannun Allah.

Yayin da adawa ke kara tsanani, bayin Allah za su kara rudewa, domin za su ga kamar su suka jawo tasin hankalin. Amma lamiri da maganar Allah suna tabbatar masu cewa basu yi kuskure ba, kuma ko da shike wahalolinsu suna ci gaba, ana karfafa su su jimre.

Hammayyar ta na kara marmatsowa, ta na kara tsanani kuma, amma bangaskiyarsu da karfin halinsu, suna karuwa daidai da damuwar. Shaidarsu ita ce cewa: “Ba mu isa mu taba maganar Allah ba, mu raba dokarsa mai-tsarki, muna ce da wani bangare mai—muhimmanci, wani kima mara muhimmanci, domin mu sami karbuwa ga duniya. Ubangij da mu ke bauta masa Ya isa Ya kubutar da mu. Kristi Ya rigaya Ya yi nasara da duniya, kuma sai mu ji tsoron duniya da an rigaya an yi nasara da ita?”

Zalunci iri iri abu ne da zai ci gaba da kasancewa muddan akwai Shaitan, kuma Kiristanci yana da ikon sa na musamman. Ba wanda zai iya bauta ma Allah ba tare da jawo ma kansa adawar rundunonin duhu ba. Miyagun malaiku za su kai masa hari, da shike sun damu cewa yana kwace abinci daga hannunsu. Miyagun mutane wadanda kwatancinsa ke tsauta masu, za su hada kai da miyagun malaiku wajen kokarin raba shi da Allah ta wurin jarabobi. Sa’an da wadannan basu yi nasara ba, za a yi anfani da wani iko domin a tilasta lamirin. Amma muddan dai Yesu Ya kasance Matsakancin mutum a haikali na sama, za a ji tasirin hani na Ruhu Mai-tsarki kan shugabanni da mutane. Har yanzu yana mulki kan dokokin kasar. Da ba domin dokokin nan ba, da munin yanayin duniya ya fi yadda yake yanzu. Yayin da shugabannin mu da yawa wakilan Shaitan ne, Allah ma yana da wakilansa cikin shugabannin kasar. Magabcin yana motsa bayinsa su shawarta a dauki matakan da za su hana ci gaban aikin Allah, amma manyan kasar, masu tsoron Allah, malaikun Allah su kan motsa su su yi jayayya kan shawarwarin nan ta yadda ba za a iya kin maganarsu ba. Ta hakanan mutane kalilan za su iya tare babbar rigyawar mugunta. Za a hana adawar magabtan gaskiya domin sakon malaika na ukun ya yi aikinsa. Sa’an da an ba da fadaka ta karshen, za ta jawo hankulan shugabannin nan da Ubangiji ke aiki ta wurinsu, wadansunsu kuma za su karbe shi, su kuma tsaya da mutanen Allah a lokacin wahala.

Malaikan da ya hada kai cikin shelar sakon malaika na uku zai haskaka dukan duniya da darajarsa. Aikin da zai mamaye dukan duniya ake nunawa a nan. Aikin zuwan Yesu na 1840-1844 ya nuna ikon Allah da daraja; aka kai sakon malaika na farin kowace cibiyar mishan a duniya, kuma a wadansu kasashe an sami marmarin addini mafi yawa da aka taba gani a wata kasa tun Canjin karni na sha bakwai; amma marmarin babban himman nan an lokacin fadaka na malaika na ukun zai fi wannan.

Aikin zai yi kama da na Ranar Pentecost. Kamar yadda aka ba da “ruwan fari,” ta wurin zubowar Ruhu Mai-tsarki a farkon bisharar, domin kawo tohuwar irin, haka kuma za a ba da ruwan bayan a karshe domin nunar da girbin. “Bari mu sani fa, mu nache bi kuma garin mu san Ubangiji; fitarsa tabbataciya che kamar wayewar gari; za ya zo wurinmu kamar ruwan sama, kamar ruwan karshe mai-damsasa kasa.” Hosea 6:3. Ku yi murna fa ku ‘ya’yan Sihiyona, ku yi farin zuchiya chikin Ubangiji Allahnku: gama ya na ba ku ruwan fari daidai bukatarku, ya na sa ruwa ya sabko maku, da na fari har na karshe, kamar da.” Joel 2:23. “Za ya zama a chikin kwanakin karshe, in ji Allah, zan zuba maku

Ruhu na bisa mai-rai duka.” “Za ya zama kuwa dukan wanda ya kira da sunan Ubangiji za ya tsira.” Ayukan 2:17, 21.

Babban aikin bishara ba zai kare da bayanuwar ikon Allah a kasa wadda aka bude aikin da ita ba. Annabce annabcen da aka cika ta wurin zubowar ruwan farko a farkon bisahra za a kuma cika su lokacin ruwan karshen a karshen aikin. Lokutan warsakewan kenan da manzo Bitrus ke begen sa,lokacin day a ce: “Ku tuba fa ku juyo domin a shafe zunubanku domin hakanan wokatan wartsakewa daga wurin Ubangiji su zo; domin kuma Shi aiko Kristi.” Ayukan 3:19, 20.

Bayin Allah da fuskokin su sama, suna walkiya da tsarkakewa mai-tsarki, za su yi sauri nan da can su yi shelar sakon nan daga sama. Ta wurin dubban muryoyi, ko ina a duniya za a ba da gargadin. Za a aikata al’ajibai, za a warkar da marasa lafiya, kuma alamu da al’ajibai za su bi masu ba da gaskiya. Shaitan ma zai bi da al’ajiban karya, har ma zai kawo wuta daga sama, mutane suna gani. Ruya 13:13. Ta hakanan za a kai mazamnan duniya ga daukan matsayinsu.

Za a kai sakon, ba lallai ta wurin mahawara ba, kamar ta wurin aikin Ruhun Allah. An rigaya an gabatar da dalilan. An rigaya an shuka irin, yanzu kuma zai tohu ya haifi ‘ya’ya. Majallun da ma’aikatan bishara ke bazawa za su yi nasu tasirin, duk da haka da yawa da zukatansu suka motsu an hana su samun cikakiyar fahimtar gaskiyar, ko kuma yin biyayya. Yanzu tsirkiyoyin hasken suna shiga ko ina, ana ganin gaskiya cikin haskenta, amintattun ‘ya’yan Allah kuma su na yanke madauran da suka rikesu. Gaskiya ta fi dukan ababa daraja. Duk da akilan da su ka hada kai domin su yaki gaskiyar, mutane da yawa za su dauki matsayinsu a gefen Allah.

Babi na 39—Kwanakin Wahala

“A wannan lokacin fa Micahel za ya tashi tsaye, shi babban sarki mai-kariyar jama’arka; za a yi kwanakin wahala irin da ba a taba yi ba tun da aka yi al’umma har loton nan; a loton nan kwa za a chechi mutanenka, kowane daya wanda aka iske shi a rubuche chikin litafin.” Daniel 12:1.

Sa’anda sakon malaika na ukun ya rufe, babu sauran alheri kuma domin mazamnan duniya. Mutanen Allah sun kamala aikinsu. Sun rigaya sun karbi ruwan karshe, “wartsakewa daga wurin Ubangiji,” kuma su na shirye domin lokacin gwaji da ke gabansu. Malaiku su na kai da kawowa da hanzari a cikin sama. Wani malaika da ya dawo daga duniya ya sanar da cewa aikin sa ya kare; an rigaya an yi ma duniya gwaji na karshe, kuma dukan wadanda suka nuna cewa su na biyayya ga dokokin Allah sun rigaya sun karbi hatimin Allah Mai-rai. Sa’an nan Yesu zai dena tsakancin Sa a haikali na sama. Za ya daga hannuwansa, da babban murya kuma zai ce: “An gama,” dukan rundunan malaiku kuma za su ajiye rawaninsu yayin da zai yi sanarwan nan mai-nauyi cewa: “Wanda shi ke mara-adilchi, bari shi yi ta rashin adiklchi: wanda shi ke mai-kazanta kuma, a kara kazamtadda shi: wanda shi ke mai-adilchi kuma, bari shi yi ta adilchi: wanda shi ke mara tsarki kuma, a kara tsarkake shi.” Ruya 22: 11. An rigaya an yanka hukuncin rai ko mutuwa game da kowane mai-rai. Kristi Ya rigaya Ya yi kafara domin mutanensa, Ya kuma shafe zunubansu. Adadin talakawansa ya cika; mulkin da ikon da girman mulkin kalkashin dukan sama an kusa a ba da shi ga magadan ceto, Yesu kuma zai yi mulki a matsayin Shi na Sarkin sarakuna da Ubangijin iyayen giji.

Sa’an da Ya bar haikalin, duhu zai rufe mazamnan duniya. A wannan lokaci na ban tsoro, dole masu adalci su kasance a idon Alah Mai-tsaarki, babu matsakanci. An cire hanin da ke kan miyagu, Shaitan kuma ya na da cikaken iko kan wadanda a karshe dai sun zama marasa tuba. Tsawon jimrewan Allah ya kare. Duniya ta ki jinkansa, ta rena kaunarsa, ta kuma tattake dokarsa. Miyagu sun zarce kadadar gafararsu; a karshe an janye Ruhun Allah da suka dinga ki. Da shike ba su da kariyar alherin Allah, ba su da tsaro ke nan daga mugun. Sa’annan Shaitan zai jefa mazamnan duniya cikin wata wahala babba ta karshe. Sa’an da malaikun Allah sun dena tsayar da ikokin fushi mai-tsanani, za a sake dukan fannonin tashin hankali. Dukan duniya za ta shiga cikin hallaka da ta fi wadda ta fada ma Urushalima ta da muni.

Malaika daya ne ya hallaka dukan ‘ya’yan farin Masarawa ya kuma cika kasar da makoki. Lokacin da Dawuda ya yi ma Allah laifi ta wurin lissafta jama’a, malaika daya ne ya kawo hallakan da aka hori Dawudan da ita. Ikon hallakan nan da malaiku masu tsarki suka yi anfani da shi sa’an da Allah Ya umurce su, shi ne miyagu za su yi anfani da shi idan Allah Ya yarda masu. Akwai ikoki da ke shirye yanzu, su na jiran izinin Allah ne kawai, su mai da ko ina kango.

An zargi masu girmama dokar Allah da jawo ma duniya matsaloli, za a kuma zarge su da cewa su ne sanadin masifu da za su abko ma halitta da tashin hankali da zub da jini da ke cika duniya da kaito. Ikon da ke tattare da gargadi na karshen ya fusata miyagu: suna fushi da dukan wadanda suka karbi sakon, Shaitan kuma zai kara zuga ruhun kiyayya da zalunci.

Sa'an da a karshe dai aka janye kasancewar Allah daga al'aummar Yahudawa, prietoci da mutane basu sani ba. Ko da shike suna kalkashin mulkin Shaitan, kuma cikin zafin fushi mai-munin gaske, duk da haka sun dauka cewa su zababbu na Allah ne. Hidima ta ci gaba a cikin haikalin; an ci gaba da mika hadayu a kan kazamtattun bagadinta, kowace rana kuma an dinga rokon albarkar Allah kan mutanen nan da ke da laifin jinin Dan Allah a kansu, suna kuma so su kashe 'yan hidimansa da manzaninsa. Sabo da haka, sa'an da aka bayana hukumcin da ke kan haikalin, kuma kadadar duniya ta tabbata har abada, mazamnan duniya ba za su sani ba. Mutanen da an rigaya an janye Ruhun Allah daga wurinsu a karshe, za su ci gaba da surar addini, kuma himmar mugunta da sarkin muguntan zai motsa su da ita don cim ma miyagun kulle kullensa, za su dauki kamanin himma domin Allah.

Da shike Assabbat ya zama muhimmin batun jayayya tsakanin Kirista ko ina, kuma hukumomin addini da na kasa sun hada kai domin kiyaye Lahadi, naciyar wata karamar kungiya ta marasa rinjaye wajen kin amincewa da masu rinjayen zai mai da su abin zagin dukan duniya. Za a koyar da cewa marasa yawan nan da ke jayayya da abin da ekklesiya ta kafa da kuma dokar kasa, bai kamata a yi hakuri da su ba; ya fi kyau su din su wahala da a jefa al'ummomi dungum cikin rikici da rashin bin doka. Shekaru dubu da dari takwas da suka gabata, shugabannin sun yi irin maganan nan game da Kristi. Kayafa ya ce: "Yana da anfani a gare ku mutum daya shi mutu saba da jama'a, kada al'umma duka ta lalace." Yohanna 11:50. Za a amince da wannan maganar, daga baya kuma za a kafa doka game da masu tsarkake Assabbat na doka ta hudu, a zarge su da cewa sun cancanci horo mafi tsanani, a kuma ba mutane dama bayan wani lokaci, su kashe su. Romanci a Tsohuwar Duniya da ridda cikin Kin ikon paparuma a Sabuwar Duniya za su dauki mataki dayan game da masu girmama dukan dokokin Allah.

Sa'an nan za a jefa mutanen Allah cikin al'amuran nan na fitina da wahala da annabi ya kira lokacin wahalar Yakub. "Gama haka Ubangiji Ya fadi: mun ji murya ta rawan jiki, ta tsoro ba ta lafiya ba che.... Dukan fuskoki fa sun komo fari. Kaito! gama wannan rana mai-girma che, har babu kamatta: lokachin wahalar Yakub ke nan; amma za a cheche shi daga chiki." Irmiya 30:5-7.

Daren azabar Yakub, sa'an da ya yi kokuawa cikin addu'a domin kubuta daga hannun Isuwa (Farawa 32:24-30) ya na misalta abin da zai faru da mutanen Allah a lokacin wahala ne. Sabo da yaudaran da ya yi domin samun albakar ubansa, wadda kuwa ta Isuwa ce, Yakub ya gudu domin ransa, barazanar dan'uwansa ta razana shi. Bayan shekaru da dama na zaman korarre, ya kama hanya, bisa umurnin Allah, domin shi dawo tare da matansa da

‘ya’yansa, da garkunan dabbobinsa, zuwa kasarsa ta gado. Daga isowa kasar, ya cika da tsoro sabo da zuwan Isuwa da mayaka domin daukan fansa. Da alama Yakub da jama’ar a za su fuskanci gwada karfi da kuma kisa ke nan. Ban da taraddadi da tsoro, ga kuma zargin kansa, (tsarguwa) da shike zunubin shi ne ya jawo wannan hatsarin. Begen shi kadai jin kan Allah ne; dole addu’a ce kadai tsaronsa. Duk da haka ya yi iyakar kokarinsa don yin kafara domin laifin da ya yi ma dan-uwansa, ya kuma kawar da barazanar. Haka ya kamata masu bin Kristi su yi iyakar kokari su sa kansu cikin hasken da ya dace a gaban mutane domin su kawar da kiyayya da hatsarin da ke barazana ga ‘yancin lamiri.

Bayan ya tara iyalin sa, domin kada su ga wahalarsa, yakub ya kasance shi kadai domin ya roki Allah. Ya furta zunubinsa, ya kuma yi godiya sabo da jin kan Allah gare shi yayin da cikin tawali’u mai-zurfi ya ambaci alkawalin da aka yi da ubaninsa da alkawuran da aka yi masa cikin wahayinsa a Babel da kuma cikin kasa hijirarsa. Lokacin matukar tarzomar rayuwarsa ta zo. Cikin duhu da kadaici, ya ci gaba da addu’a da kaskantar da kansa a gaban Allah. Faraf daya, wani hannu ya dafe kafadarsa. Ya dauka wani magabci ne ke neman ransa, kuma da dukan karfinsa ya yi kokuwa da wanda ya dafe shi. Sa’an da gari ya fara wayewa, bakon ya fito da ikonsa da ya fi na mutum, kuma da ya taba shi, sai Yakub mai-karfin nan kamar ya gurgunce, sai kuma ya fadi, babu taimako, yana kuka da roko a wuyar mai kokuwa da shi.

Yanzu Yakub ya gane cewa malaikan alkawalin ne ya ke kokuwa da shi. Ko da shike ya gurgunce, ya na kuma fama da matukar azaba, bai rabu da aniyarsa ba, ya dade yana jimre rudami da nadama da wahala sabo da zunubinsa; yanzu dole a tabbatar masa cewa an gafarta masa. Bakon nan daga wurin Allah Ya kusa ya tafi; amma Yakub ya manne masa yana rokon albarka. Malaikan ya ce: “Ka bar ni in tafi, gama gari yana wayewa;” amma Yakub ya ce: “Ba zan bar ka ba, sai ka yi mani albarka.” Wannan shi ne rashin tsoro da naciya da jimrewa. Da Yakub ya yi fahariya ne ko tsageranci, da nan da nan an hallaka shi; amma nashi tabbaci ne na wanda ya furta kumamancinsa da rashin cancantarsa, amma don haka ya amince da jin kan Allah Mai-cika alkawali.

“Ya yi iko bisa malaikan, ya rinjaye shi.” Hosea 12:4. Ta wurin kaskantarwa da tuba da mika kai, mai-zunubin nan, mai-kuskure, mai-mutuwa, ya rinjaya da Sarkin sama. Ya rigaya ya manna begensa ga alkawuran Allah, kuma zuciyar Kauna Mara-iyaka ba ta iya koran rokon mai-zunubin ba. Domin shaidar nasararsa da karfafawa ga wadansu, domin su bi kwatancinsa, a ka sake sunansa daga wanda ke tunurwa da zunubinsa zuwa wanda ya kan sa a tuna da nasararsa. Kuma rinjayar da Yakub ya yi da Allah tabbaci ne cewa zai rinjaya da mutane. Bai sake jin tsoron saduwa da fushin dan-uwansa ba, da shike Ubangiji ne tsaronsa.

Da Shaitan ya rigaya ya zargi Yakub a gaban malaikun Allah, yana cewa yana da ‘yanci ya hallaka shi sabo da zunubinsa; ya motsa Isuwa ya kai masa hari; kuma a daren kokowar Yakub din nan, Shaitan ya yi kokarin danne shi da tunanin laifinsa domin shi

sanyaya masa gwiwa, shi karya masa dogararsa ga Allah. Yakub ya kusan fid da zuciya; amma ya san cewa idan babu taimako daga sama, zai hallaka. Ya rigaya ya tuba da gaske daga zunubinsa, ya kuma roki jinkan Allah. Bai bar manufarsa ba, amma ya manne ma Malaikan, ya kuma dinga add'uarsa da naciya, tare da kuka mai-zafi har sai da ya yi nasara.

Kamar yadda Shaitan ya zuga Isuwa ya kai ma Yakub hari, hakanan zai zuga miyagu su hallaka mutanen Allaha lokacin wahala. Kuma yadda ya zargi Yakub, haka ne zai zargi mutanen Allah. Yana gani kamar dukan duniya talakawansa ne, amma karamar kungiyan nan da ke kiyaye dokokin Allah suna kin mulkinsa. Da zai shafe su daga duniya da nasararsa za ta cika. Ya ga cewa malaiku masu-tsarki suna tsaronsu, ya kuma gane cewa an gafarta zunubbansu; amma bai san cewa an rigaya an kamala sahri'ar su a haikali na sama ba. Yana da cikakken sanin zunuban da ya jarabce su suka aikata, kuma yana gabatar da su a gaban Allah da karin gishiri ainun, ya na cewa su ma sun cancaci a hana su alherin Allah daidai da yadda aka hana shi. Yana cewa bisa adalci Ubangiji ba zai iya gafara zunubansu, sa'an nan Ya hallaka shi da malaikunsa ba. Yana kuma cewa su nasa ne, kuma ya kamata a ba shi su ya hallaka su.

Yayin da Shaitan ke zagin mutanen Allah sabo da zunubansu, Ubangiji yana barin shi Ya jarabce su matuka. Za a gwada amincewarsu ga Allah da bangaskiyarsu da naciyarsu kuma. Yayin da suke tuna baya, zukatansu su kan yi sanyi, domin a dukan rayuwarsu, ba nagarta da yawa. Suna da cikakken sanin rashin cancantarsu da kumamancinsu. Shaitan zai yi kokarin razana su da cewa wai ba su da bege, kuma ba za a taba wanke abin kazantarsu ba. Ta wurin wannan ya na begen lalata bangaskiyarsu domin su yarda da jarabobinsa, su kuma juya daga biyayyarsu ga Allah.

Ko da shike magabta masu son hallaka mutanen Allah za su kewaye su, duk da haka tsoron zalunci sabo da gaskiya ba shi ne ukuban da za su sha ba; suna tsoro ne cewa ba a tuba daga kowane zunubi ba, kuma cewa ta wurin wani laifinsu, za su kasa samun cikawar alkawalin Mai-ceton, cewa: "Ni ma zan kiyaye ka daga sa'ar jaraba, wannan da ke zuwa bisa dukan duniya." Ruya 3:10. Da za su sami tabbacin gafara, da ba za su ji tsoron azaba ko mutuwa ba; amma idan basu cancanta ba, har suka rasa rayukansu sabo da aibin halayensu, wannan zai jawo reni ga sunan Allah.

A kowane gefe suna jin shirye shiryen tawaye da tashin hankali; kuma a cikin zukatansu akwai bege da buri sosai na cewa riddan nan ta kare, muguntar miyagu kuma ta kare. Amma yayin da suke rokon Allah Ya tsayar da tawaye, suna zargin kansu kwarai cewa su kansu ba su da ikon tsayayya da mugunta da kuma rage karuwarta. Suna ji kamar da kullum sun dinga anfani da dukan iyawarsu don hidimar Kristi, su na ci gaba da kokarinsu, da mayakan Shaitan ba su da iko sosai da za su dawama a kansu.

Za su azabtar da kansu a gaban Allah, suna nuna tubarsu daga zunubansu, suna kuma rokon alkawalin Mai-ceton cewa: "Bari shi kama karfi na, domin shi yi amana da ni."

Ishaya 27:5. Bangaskiyarsu ba ta da fadi ba wai don ba a amsa addu'o'insu nan da nan ba. Ko da shike su na fama da masananan taraddadi da razana da wahala ba za su dena addu'o'insu ba. Za su rike karfin Allah yadda Yakub ya rike Malaikan, kuma maganar rayukansu ita ce: "Ba zan bar ka ka tafi ba, sai ka yi mani albarka."

Da Yakub bai rigaya ya tuba daga zunuubinsa na samun gado ta wurin yaudara ba, da Allah bai ji addu'arsa Ya kuma kiyaye ransa ta wurin jinkai ba. Hakanan a lokacin wahala, idan mutanen Allah sun tuna da zunuban da basu furta ba, yayin da suke fama da tsoro da ukuba, da za a fi karfinsu; rashin bege zai yanke bangaskiyarsu, kuma ba za su sami karfin zuciya da za su roki Allah Ya kubutar da su ba. Amma yayin da suke da kyakyawar sanin rashin isarsu, ba su da boyayyun zunubai da za su bayana. Zunubansu sun rigaya sun fuskanci hukumci an kuma shafe su, kuma ba za su iya kawo su a tuna da su ba.

Shaitan yana sa mutane da yawa su gaskata cewa Allah zai manta da rashin amincinsu game da kananan al'amuran rayuwa; amma Ubangiji yana nunawa cikin huldarsa da Yakub cewa ba zai taba amincewa ko kuma ya kyale mugunta ba. Dukan wadanda sun yi kokarin boye zunubansu ko kuma ba da hujja dominsu, suka kuma bar zunuban sun kasance a littattafan sama, ba su furta ba, ba a kuma gafarta su ba, Shaitan zai yi nasara bisan su. Yawan furcin bangaskiyansu da yawan darajar matsayin da su ke rike daidai yake da yawan fushin Allah game da laifinsu, da yawan farin cikin Shaitan babban magabcinsu. Masu jinkirta shiryawa don ranar Allah ba za su iya samun shirin a ranar wahala ba ko kuma wata rana daga baya. Dukan irin wadannan ba su da bege.

Kiristan da za su shiga ba shiri cikin yakin karshen nan mai-ban tsoro, cikin rashin bege za su furta zunubansu cikin kalmomi na azaba, yayin da miyagu za su yi murna game da wahalarsu. Furcin zunuban nan irin na Isuwa da Yahuda ne. Masu fadin zunuban suna bakincikin sakamakon zunuban su ne, amma ba laifin kansa ba. Ba sa jin tuba ta gaskiya, basa kyamar mugunta, suna amincewa da zunuban su, ta wurin tsoron horo; amma kamar Fir'auna na da, za su koma tumbensu ga Allah da zaran an kawar da horon.

Tarihin Yakub tabbaci ne kuma cewa Allah ba zai jefar da wadanda aka rude su, aka jarabce su, aka kuma yashe su zuwa cikin zunubi ba, idan sun dawo wurinsa da tuba ta gaskiya. Yayin da Shaitan ke kokarin hallaka wadannan, Allah zai aiko da malaikunsa, su tsare su, su ta'azanar da su a lokacin hadari. Hare haren Shaitan masu tsanani ne da himma kuma, rudinsa mumuna ne; amma idon Ubangiji yana kan mutanensa, kunnensa kuma yana sauraron kukarsu. Azabarsu mai-yawa ce, wutar tanderun kuma ta kusa ta cinye su; amma mai-tsarkakewan zai fito da su kamar zinariya da aka tsarkake da wuta; dole a cinye son duniyansu, domin a nuna halin Kristi cikakke.

Lokacin wahala da ukuba da ke gabanmu zai bukaci bangaskiya da za ta jimre gajiya da jinkiri da yunwa, bangaskiya da ba za ta kare ba ko da an jarabce ta sosai. An ba kowa lokacin gwajin hali domin a shirya don wancan lokacin. Yakub ya dawama domin ya yi

naciya da himma ne. Nasararsa shaida ce ta ikon addu'a da naciya, dukan wadanda za su kama alkawuran Allah yadda shi ya yi, su kuma yi himma da naciya yadda ya yi, za su yi nasara ma yadda shi ya yi. Wadanda ba sa so su yi musun kai, su yi kuka a Allah, su dade suna addu'a da naciya don albarkarsa, baza su same ta ba. Wadanda suka san kokowa da Allah ba su da yawa! Nawa suka taba sa rayukansu sun bi Allah da himmar bukata har sai an mika kowace gabar jikin? Sa'anda rashin bege ya yi yawa ta yadda harshe ba zai iya ambatawa ba game da mai-addu'ar, mutum nawa ne sukan nace da bangaskiya ga alkawuran Allah?

Masu kankantar bangaskiya yanzu, suna kalkashin babban hatsarin faduwa kalkashin ikon rudin Shaitan da dokan da za ta tilasta lamiri. Ko da sun jimre gwajin ma, za su kara nutsewa cikin wahala da ukuba ne lokacin wahala, da shike basu taba sabawa da dogara ga Allah ba. Zai zama masu dole su koya cikin matsi da sanyin gwiwa, darussan nan na bangaskiya da suka kyale.

Ya kamata mu fahimci Allah yanzu ta wurin gwada alkawuransa. Malaiku suna rubuta kowace addu'a ta naciya da gaskiya. Gara mu rabu da muradun kanmu da mu manta sadarwa da Allah. Talauci mafi zurfi, musun kai mafi girma, tare da yardar Allah, ya fi arziki da girmamawa da holewa da abota ba tare da yardar Allah ba. Dole mu sami lokaci mu yi addu'a. Idan mun bar zukatanmu sun shaku da ababan duniya, Ubangiji zai iya ba mu lokaci ta wurin cire mana gumakanmu na zinariya da gidaje da gonaki masu anfani.

Matasa ba za su jarabtu da zunubi ba idan sun ki shi ta duk wata hanya, sai dai wadda a ciki za su iya rokon albarkar Allah. Idan 'yan sakon da ke kai sakon gargadi na karshe ga duniya za su roki albarkar Allah, ba yamusai cikin kiwuya da rashin kuzari ba, amma da himma, cikin bangaskiya yadda Yakub ya yi, za su sami wurare da yawa inda zasu iya cewa: "Na ga Allah ido da ido, rai na kuma ya wanzu." Farawa 32: 30. Sama za ta lissafta su a matsayin 'ya'yan sarakuna, masu ikon yin nasara da Allah da kuma mutane.

Lokacin wahala "irin da ba a taba yi ba," ba da jimawa ba zai zo mana; kuma za mu bukaci kwarewan da ba mu da shi yanzu, wanda kuma da yawa sabo da yawan kiwuya ba za su samu ba. Sau da yawa wahala takan yi yawa a zato, fiye da zahiri; amma ba haka yake game da hargitsin da ke gabanmu ba. Komi yawan bayani ba za a iya nuna girman matsalar ba. A wancan lokacin gwajin, ole kowane mai-rai ya tsaya ma kan sa a gaban Allah. "Ko da a ce Nuhu, Daniel, da Ayuba suna cikinta [kasar], na rantse da raina, in ji Ubangiji Yahweh, ba za su chechi ko da ko daya ba, ransu kadai za su cheta ta wurin adilchinsu." Ezekiel 14:20.

Yanzu, yayin da Babban Priest na mu yake yin kafara domin mu, ya kamata mu bidi zama cikakku cikin Kristi. Ko ta wurin tunani ma ba a iya sa Mai-ceton ya amince da ikon jaraba ba. Shaitan yakan sami wani wuri da zai rike ne a cikin zukatan mutane inda zai sa kafa; ko ana sha'awar wani zunubi wanda ta wurinsa jarabobinsa za su nuna ikon su. Amma

Kristi Ya ce: “Sarkin duniya yana zuwa, ba shi da komi a chikina.” Yohanna 14:30. Shaitan bai iya samun wani abu a cikin Dan Allah ba da zai ba shi dammar yin nasara. Ya kiyaye dokokin Ubansa, kuma ba zunubi a cikinsa da Shaitan zai yi anfani da shi ya cuce Shi. Yanayin da dole a iske ga wadanda za su tsaya a kwanakin wahala ke nan.

A rayuwan nan ne za mu rabu da zunuubi, ta wurin bagaskiya cikin jinin kafara na Kristi. Mai-cetonmu yana gayyatar mu, mu hada kanmu da shi, mu hada kumamancinmu da karfinsa, jahilcinmu da hikimarsa, rashin isanmu da isarsa. Kadarar Allah ce makaranta, inda zamu koyi tawali’u da kaskantar da kai irin an Yesu. Ubangiji kullum yana nuna mana ainihin manufofin rayuwa ne, ba hanyar da muka zaba da ta fi kamar sauki da dadi gare mu ba. Ya rage namu mu hada kai da hanyoyin da Allah ke anfani da su cikin aikin sifanta haalayenmu daidai da gurbin sama. Ba wanda zai kyale aikin nan ko kuma ya dakatar da shi, ba tare da fuskantar hatsari mafi ban tsoro ga ransa ba.

Manzo Yohanna cikin ruya ya ji babbar murya a sama tana cewa: “Kaiton duniya da teku: domin Shaitan ya sabko wajenku, hasala mai-girma kwa gareshi, domin ya sani sauran zarafinsa kadan ne.” Ruya 12:12. Al’amuran da suka jawo wannan magana daga sama suna da ban tsoro. Fushin Shaita zai karu sa’an da ya ga lokacinsa yana karewa, kuma aikinsa na rudi da hallaka zai kai makuransa a kwanakin wahala ne.

Ba da jimawa ba za a bayana ababa masu ban tsoro a sammai, alamar ikon aljannu na aikata al’ajibai. Ruhohin aljannu za su shiga zukatan sarakunan duniya da cikin dukan duniya kuma, domin a rike su cikin rudi, a kuma zuga su su hada kai da Shaitan cikin fadan shi na karshe da gwamnatin sama. Ta wurin wadannan wakilan, za a rudi shugabanni da talakawa. Mutane za su taso suna karyan cewa su ne Kristi kansa, su kuma bidi suna, da sujada wadanda duka ‘yanci ne an Mai-fansarmu. Za su aikata al’ajibai na warkarwa, za su kuma ce suna da ruyai daga sama da ke sabani da shaidar Littafin.

A matsayin rudi mafi-girma, Shaitan kan shi zai ce shi ne Kristi. Ekklesiya ta dade tana cewa tana sauraron zuwan Mai-ceton a matsayin babban begenta. Yanzu babban mai-rudin zai sa a ga kamar Kristi Ya zo. A bangarorin duniya dabam dabam, Shaitan zai nuna kansa ga mutane kamar halitta mai-martaba da walkiya, kamar da Dan Allah yadda Yohanna ya bayana Shi cikin Ruya 1:13-15. Darajar da ta kewaye shi ta fi duk wadda idon dan Adam ya taba gani. Kuwwar nasara za ta cika wuri cewa: “Kristi Ya zo! Kristi Ya zo!” mutane za su durkusa a gabansa cikin bangirma, shi kuma zai daga hannuwansa, ya furta albarka a kansu, yadda Kristi Ya albarkaci almajiransa lokacin da yana duniya. Muryarsa tana da taushi, mai-dadin ji kuwa. Cikin amo cike da ladabi da tausayi zai gabatar da wadansu gaskiyan nan na sama da Mai-ceton ya furta; zai warkar da cututtuka, sa’an nan da kamanin halin Kristi, zai ce ya canja Assabbat zuwa Lahadi, ya kuma umurci kowa ya tsarkake ranan da shi ya yi mata albarka. Zai bayana cewa masu naciyar kiyaye rana ta bakwai da tsarki su na sabon sunansa ne ta wurin kin jin malaikunsa da ya aika da haske da gaskiya kuma. Rudi mai-karfi, maikusan tilastawa ke nan. Kamar Samriyawan da Simon

Magus ya rude su, jama'a, daga mafi-kankanta zuwa mafi-girma, za su saurari bokancin nan, su na cewa: "Wannan shi ne ikon Allah." Ayukan 8:10.

Amma ba za a yaudari mutanen Allah ba, koyaswoyin jabun Kristin nan basu je daidai da Littafin ba. Zai sa albarkarsa kan masu sujada ga bisan da gumkinsa ne, ainihin wadanda Littafin ya ce za a zuba fushin Allah wanda ba a surka ba a kansu.

Bugu da kari kuma, ba a yarda ma Shaitan ya yi kwaikwayon irin zuwan da Kristi zai yi ba. Mai-ceton Ya rigaya Ya gargadi mutanensa kan rudi game da wannan batun, Ya kuma bayana yadda zuwansa na biyu zai kasance. "Gama masu karyan Kristi za su tashi, da masu karyan annabchi, za su gwada alamu masu-girma da al'ajibai kuma; har su badda ko zababbu da kansu, da ya yiwu.... Idan fa sun che maku, Ga shi yana chikin jeji; kada ku fita: ko kwa, Ga shi yana chikin lolokai; kada ku gaskanta. Gama kamar yadda walkiya takan fito daga gabas, ana kwa ganinta har yamma; hakanan bayyanuwar Dan mutum za ta zama." Matta 24:24-27,31; Ruya 1:7; Tassalunikawa I, 4:16, 17. Ba za a iya yin jabun wannan zuwan ba. Ko ina za a sani, dukan duniya za ta shaida shi.

Wadanda da ma suna nazarin Littafin a natse, suka kuma karbi kaunar gaskiya ne kadai za a kare su daga kakarfan rudin da zai kama duniya. Ta wurin shaidar Littafin, masu binciken za su gane mai-rudin cikin sojan gonan na shi. Lokacin gwajin zai zo ma kowa. Ta wurin rairayar jarabobi za a bayana ainihin Kirista. Ko mutanen Allah yanzu sun kafu sosai cikin maganarsa ta yadda ba za su bi tunanin kansu ba ne? Ko a cikin wannan tashin hankalin za su manne ma Littafin da Littafin kadai ne? Shaitan, in ya yiwu, zai hana su shiryawa domin su tsaya a wannan ranar. Zai tsara al'amura ta yadda zai yi masu shinge, ya dabaibaye su da dukiyar duniya, ya sa su dauki kaya mai-nauyi da gajiyarwa, domin zukatansu su cika da damuwoyin rayuwan nan, har ranar gwaji ta zo masu kamar barawo.

Sa'an da dokan da shugabannin kashen Kirista dabam dabam za su bayar sabanin masu kiyaye dokokin Allah za ta janye tsaron gwamnati, ta bar su da wadanda ke so su hallaka su, mutanen Allah za su gudu daga birane da kauyuka, su hada kai a kungiyoyi, su na zama a wuraren da suka fi kadaici da kasancewa kango. Da yawa za su sami mafaka a kogunan duwatsu ne. Kamar Kiristan Kwarin Piedmont, za su mai da madaukakan wurare na duniya mafakansu, za su kuma gode ma Allah sabo da karfafan wurare na duwatsun, Ishaya 33: 16. Amma da yawa daga dukan al'ummai da dukan sassa, manya da kanana, mawadata da matalauta, bakake da farare, za a jefa su cikin muguwar bauta mafi rashin adalci. Kaunatattu na Allah za su yi kwanakin wahala, a daure da sarkoki, a kulle cikin kurkuku, da hukumcin kisa a kansu, wadansu kuma an bar su su mutu da yunwa cikin kurkuku masu duhu da ban kyama. Ba wanda ke jin kukansu; ba mutumin da ke shirye ya taimake su.

Ko Ubangiji zai manta da mutanensa a wannan lokacin jaraba? Ko Ya manta da Nuhu lokacin da aka hori duniyar zamaninsa? Ko Ya manta da Lot lokacin da wuta ta sauko daga

sama ta cinye biranen Sodom da Gomorrah? Ko Ya manta da Yusufu a tsakiyar masu bautar gumaka a Masar? Ko Ya manta da Iliya lokacin da rantsuwar Jezebel ta yi masa barazana da abin da ya faru da annabawan Baal? Ko Ya manta da Irmiya a cikin kurukun sa na ramin nan mai-ban kyama? Ko Ya manta da jarumawan nan uku a cikin tanderun wuta? Ko kuma Daniel a cikin ramin zakuna?

“Sihiyona ta che, Ubangiji Ya yashe ni, Ubangiji Ya manta da ni kuma. Ya yiwu mache ta manta da danta mai-shan mama, har da ba za ta yi juyayin dan chikinta ba? I, ya yiwu wadannan su manta amma ni ba ni manta da ke ba. Ga shi na zana ki a tafin hannu na” isahya 49:14-16. “Shi wanda ya taba ku, ya taba kwayar idonsa.” Zechariah 2:8.

Ko da shike magabta za su jefa su cikin kurkuku, duk da haka wannan ba zai yanke sadarwa tsakaninsu da Kristi ba. Wani wanda ke ganin kowane kumamancinsu, wanda Ya san kowane gwaji, Ya fi dukan ikokin duniya; malaiku kuma za su zo wurinsu cikin kurkukun, su ba su haske da salama daga sama. Kurkukun zai zama kamar fadar sarki, gama masu arzikin bnagaskiya su na zama a wurin, kuma za a haskaka wurin da hasken sama, yadda aka yi sa’anda Bulus da Sila su ka yi addu’a da wakokin yabo da tsakar dare cikin kurkukun Filibbi.

Hukumcin Allah zai abka kan masu neman danne mutanen Allah da hallaka su kuma. Tsawon hakurinsa da miyagu yana kara karfafa su cikin zunubansu, amma duk da haka horonsu tabbatace ne mai-tsanani kuma da shike ya yi jinkiri da yawa. “Gama Ubangiji za ya tashi kamar chikin dutsen Perazim, za ya hasala kamar yadda Ya yi chikin kwarin Gibeon; domin Shi yi aikinsa; aikinsa mai-ban al’ajibi, ya tabbatasda al’ajibinsa mai-ban al’ajibi.” Ga Allahnmu Mai-jinkai, horo abin al’ajibi ne. “In ji Ubangiji Yahweh, Na rantse da raina, ba ni da wani jin dadi chikin mutuwar mugu ba.” Ezekiel 33: 11. “Ubangiji yana chike da juyayi, mai-alheri kuma, mai-jinkirin fushi, mai-yalwar jin kai da gaskiya;... yana gafarta laifi da sabo da zunubi.” Duk da haka, “ba shi kubutadda mai-laifi ko kadan.” “Ubangiji mai-jinkirin fushi ne, mai-girma ne chikin iko, ba kwa za shi kubutadda masu laifi ba ko kadan.” Fitowa 34:6,7; Nahum 1:3. Ta wurin manyan al’amura, cikin adalci zai kunita ikon dokarsa da aka tattake. Zafin horon da ke jiran mai-laifi zai bayana ta wurin jinkirin Ubangiji wajen aiwatar da hukumcin. Al’amman da ya dade yana yi mata hakuri, wadda kuma ba zai buga ta ba har sai ta cika ma’aunin zunubinta a lissafin Allah, a karshe za ta sha kokon fushin da ba a surka da jinkai ba.

Sa’an da Kristi Ya dena tsakancinsa a haikalin, za a zubo fushin nan da ba a surka bad a za azuba ma wadanda suke sujada ga bisan da gumkinsa suka kuma karbi lambansa (Ruya 14:9, 10). Annoban Masar, a lokacin da Allah Ya kusa kubutar da Israila, sun yi kama da wadannan annoba mafi-muni da fadi da za su fado ma duniya gaf da kubutarwar mutanen Allah. In ji mai-ruyan, game da annoban nan, ya ce: “Sai ya zama mugun gyambo mai-azaba bisa mutane wadanda su ke da shaidar bisan, masu sujada ga gumkinsa kuma.” Teku ya zama jini irin na matachen mutum: kowane abu mai-rai “ya mutu kwa, watau abin da

ke chikin teku." Kuma "koguna da mabulbulan ruwaye ...ya zama jini kuma." Duk da munin annoban nan, adalcin Allah ya kunita. Malaikan Allah ya ce: "Mai-adilchi ne kai, ... domin ka hukumta hakanan: gama su suka zubasda jinin tsarkaka da annabawa, jini kuma ka ba su su sha: wannan ya dache da su." Ruya 16:2-6. Ta wurin hukumta mutanen Allah zuwa mutuwa, da gaske sun ja ma kansu laifin jinin na su kamar da hannunsu ne suka zubar da jinin. Hakanan ne kuma Kristi Ya ce Yahudawan zamaninsa ke da alhakin dukan jinin tsarkaka da aka zubar tun kwanakin Habila, da shike suna da ruhu iri dayan, sun kuma so su yi aiki iri dayan da masu kisan annabawan nan.

Cikin annoban da ke biye an ba rana iko "ta babbake mutane da wuta. Har mutane suka babbake domin tsananin zafi." Aya 8, 9. Annabawan sun bayana yanayin duniya a wannan lokaci na bantsoro kamar haka: "Kasa tana makoki, gama an banzantadda hatsi.... Dukan itatuwan gona sun bushe: gama farinchiki ya yi yaushi a zuchiyar yan Adam." "Iri ya ruba a kalkashin hoggan; an lalatadda rumbuna.... Ji dai nishin dabbobi! Garkunan shanu sun damu, domin babu wurin kiwo. Rafufukan ruwa sun kafe, wuta kwa ta chinye makiyaya na jeji." "Raira wakoki na haikali kuma za su zama kururuwa a chikin ranan nan, in ji Ubangiji Yahweh: gawaye za su yi yawa; a kowane wuri kwa za a zubas da su a shuru." Joel 1:10-12, 17-20; Amos 8:3.

Annoban nan ba za su mamaye duniya ko ina ba, in ba haka ba da mazamnan duniya za su hallaka gaba daya. Duk da haka za su zama annoba mafi-muni da 'yan Adam suka taba gani. Dukan annoban da mutane suka fuskanta kafin rufewar gafara akan surka su da jin kai. Jinin Kristi yakan tsare mai-zunubi daga karban cikakken mudun laifinsa, amma a hukumci na karshe, za a zubo fushi da ba a surka da jin kai ba.

A wancan ranar, jama'a da yawa za su yi marmarin mafakar jin kan Allah wanda sun dade suna ki. "Ga shi, in ji Ubangiji Yahweh, kwanaki suna zuwa inda zan aike yunwa a chikin kasan, ba yunwan gurasa ko kishin ruwa ba, amma na jin magnar Ubangiji. Za su kama yawo daga teku zuwa teku, daga arewa zuwa gabas; za su yi gudu nan da can garin neman magnar Ubangiji amma ba za su samu ba." Amos 8:11, 12.

Mutanen Allah ba za su rasa shan wahala ba; amma yayin da ake tsananta masu, ana wahal da su, yayin da suke jimre rashi, suna wahalar abinci kuma, ba za a bar su su hallaka ba. Allahn nan da Ya lura da Iliya ba zai kyale daya daga 'ya'yansa masu sadakar da kai ba. Shi wanda yake lissafta suman kansu zai lura da su, kuma a lokacin yunwa za a kosar da su. Yayin da miyagu ke mutuwa da yunwa da annoba, malaiku za su tsare masu adalci, su biya bukatunsu kuma. Alkawalin shi ne, "Shi wanda ke tafiya bisa adilchi" "za a rika ba shi abinchinsa; ruwansa na sha tabbatache ne..." "Fakirai da masu-mayata suka nemi ruwa, amma babu, harshen su kwa ya kasa domin kishin ruwa; ni Ubangiji, ni amsa masu, ni Allah na Israila ba ni yashe su ba." Ishaya 33:15, 16; 41:17.

“Gama ko da shike itachen baure ba za ya yi fure ba, ba kwa yaya a chikin kuringar anab ba; wahalar zaitun ta zama banza, gonaki basu ba da abinchi ba: ko da za a raba tumaki da wurin zamansu, ba a iske shanu a dangwalinsu ba;” duk da haka wadanda ke tsoronsa za su “yi murna chikin Ubangiji,” su yi farin ciki kuma cikin Allahn ceton su. Habakuk 3:17, 18.

“Ubangiji mai-tsaronka: Ubangiji Shi ne inuwarka ga hannun damanka. Rana ba za ta buge ka chikin yini ba, ko wuta da dare. Ubangiji za ya tsare ka daga dukan mugunta za ya kiyaye ranka.” “Gama za ya fishe ka daga tarkon mai-farauta, daga aloba mai-kawo mutuwa kuma. Za shi rufe ka da jawarkinsa, a kalkashin fukafukansa za ka sami kariya: gaskiyarsa garkuwa ne da kutufani. Ba za ka ji tsoron razanar dare ba; ko kwa kibiya wadda ke tashi da rana; ko aloban da ke yawo a chikin dufu, ko hallaka wadda ke lalataswa da tsakar rana. Mutum dubu za su fadi daura da kai, zambar goma kuma a hannun ka na dama; amma ba za su kusanche ka ba. Da idanun ka kadai za ka duba ka ga sakamakon miyagun mutane. Gama kai ne mafakata ya Ubangiji! Ka mai da Madaukaki wurin zamanka; babu mugunta da za ta same ka, babu wata aloba da za ta kusanchi tent naka.” Zabura 121:5-7; 91:3-10.

Duk da haka, ga ganin mutum, zai zama kaman ba da jimawa ba dole mutanen Allah za su hatimce shaidarsu da jinin su yadda jarumawan da aka kashe kafinsu suka yi. Su kansu sun fara tsoro cewa Ubangiji Ya bar su su fada hannun magabtansu. Lokaci ne na wahala mai-ban tsoro. Dare da rana su na kuka ga Allah domin kubutarwa. Miyagun za su yi takama, za a kuma ji ihun gorin cewa: “Yanzu ina bangaskiyar ta ku? Don me Allah bai kubutar da ku daga hannunmu, ba idan da gaske kumutanensa ne?” Amma masu jiran za su tuna Yesu yayin da yake mutuwa a giciyen Kalfari, da manyan priestoci da shugabanni da ke ihu suna ba’a cewa: “Ya ceci wadansu, ya kasa ceton kansa. Sarkin Israila ne shi; shi sabko yanzu daga gichiye, mu kwa mu ba da gaskiya gare shi.” Matta 27:42. Kamar Yakub, kowa yana kokowa da Allah. Fuskokinsu suna nuna faman da su ke yi a ciki. Kowace fuska ta nuna damuwa. Duk da haka basu dena addu’ar naciyarsu ba.

Da mutane sun iya gani da idon sama, da za su ga garkunan malaiku masu cikakken karfi kewaye da wadanda suka kiyaye Kalmar hakurin Kristi. Da tausayi mai-taushi sun shaida wahalarsu, suka kuma ji addu’o’insu. Su na jiran umurnin Kwamandan su ne domin su kubutar da su daga matsalarsu. Amma dole su kara jira kadan. Dole mutanen Allah su sha daga kokon, a kuma yi masu baptisma da baptismar. Jinkirin kansa da ke damun su, shi ne amsa mafi kyau ga addu’o’insu, yayin da suke jira da aminci dominUbangiji Ya yi aiki, wannan yana sa su yin bangaskiya da bege da hakuri da basu yi sosai ba lokacin rayuwarsu ta addini. Duk da haka sabo da zababbu za a takaita lokacin wahalar. “Allah fa ba za ya rama ma zababaunsa ba, da suke yi masa kuka dare da rana?... ina che maku, da samri za ya rama masu.” Luka 15:7-8. Karshen zai zo da sauri fiye da yadda mutane ke

zato. Za a tattara alkamar domin rumbun Allah; za a daure zawan kamar yayi domin wutar hallaka.

Masu gadin sama, cikin amincinsu, suna ci gaba da tsaro. Ko da shike wata doka ta bai daya ta ayana lokacin da za a karkashe masu kiyaye doka, magabtansu wasu lokuta kafin lokacin da aka aiyana, za su yi kokarin dauke rayukansu. Amma ba wanda zai iya wuce manyan masu tsaron da aka ajiye kewaye da kowane amintace. Za a abka ma wadansu lokacin da suke gudu daga birane da kauyuka ne; amma makamai da aka daga domin a kashe su da su za su karye su fadi kamar kara. Malaiku cikin kamanin mayaka za su kare wadansu.

Cikin dukan sararraki Allah Yakan yi aiki ta wurin malaiku masu tsarki domin taimako da kubutarwar mutanensa. Masu rai daga sama sukan sa hannu dumu dumu cikin harkokin ‘yan Adam. Sukan bayyana cikin tufafi masu kamar walkiya; su kan zo kamar mutane cikin tufafin matafiya. Malaiku sun sha bayanuwa cikin kamanin mutane ga mutanen Allah. Sukan huta kaman sun gaji, a gindin bishiyoyi da rana. Sun sha karban liyafa a gidajen mutane. Sukan zama masu bishewa ga matafiya cikin dare. Da hannunsu sun kunna wutar bagadi. Sun bude kofofin kurkuku suka ‘yantar da bayin Ubangiji. Yafe da makamai na sama sun sauko suka ture dutse daga kabarin Mai-ceton.

Cikin kamanin mutane malaiku su kan kasance cikin masu-adalci; sukan kuma ziyarci taron miyagu, yadda suka je Sodom, domin su rubuta ayukansu, domin a san ko sun wuce kadadar hakurin Allah. Ubangiji yana jin dadin jinkai; kuma sabo da kalilan da ke ainihin bauta masa, yakan hana bala’i, ya tsawaita salamar jama’a masu yawa. Da kadan masu zunubi zuka san cewa suna raye sabo da amintattu kalilan da suke wulakantawa suna kuma yi masu ba’a ne.

Ko da shike shugabannin duniyan nan basu sani ba, duk da haka cikin majalisunsu malaiku sukan yi magana a madadin wadansu. Idanun mutane sukan gan su, kunnuwan mutane sukan ji rokonsu, lebunan mutane sun sha hamayya da shawarwarinsu, suka kuma yi ba’a gare su, hannayen mutane sun sha zagin su, suka ci mutuncinsu. Cikin zauren majalisa da kotun shari’a ‘yan sakon nan na sama sun nuna sanin tarihin ‘yan Adam kwarai; sun nuna cewa sun fi kwararrun masu kare wulakantattun nan iya kare mutanen. Sun sha canja manufofi, suka hana mugunta da kan iya kawo cikas sosai ga aikin Allah, ya kuma jawo wahala mai-yawa ga mutanensa. A sa’ar hatsari da wahala, “Malaikan Ubangiji yana kafa sansani kewaye da masu-tsoronsa, yana tseradda su kuma.” Zabura 34:7.

Da bege mai-yawa, mutanen Allah suna jiran alamun Sarkinsu da ke zuwa. Sa’an da aka tambayi masu tsaron cewa, “Ina labarin daren?,” akan ba da amsa ba shakka cewa, “Safiya tana zuwa, dare kuma yana zuwa.” Ishaya 21:11,12. Haske yana haskakawa kan gizagizai da ke kan duwatsun. Ba da jimawa ba za a bayana darajarsa. Ranan adalci ya kusa

haskakawa. Safiya da dare duk sun kusa budewar rana mara karshe ga masu adalci, tabbatar dare mara matuka ga miyagu."

Yayin da masu kokowa suke addu'o'insu a gaban Allah, an kusan janye labulen da ya raba su da Shi. Sammai suna haskakawa da wayewar yini na har abada, kuma kamar dadin wakokin malaiku, kalmomin suna shiga kunne cewa: "Tsaya da karfi wurin biyayyarka. Taimako yana zuwa." Kristi babban Mai-nasara yana mika ma gajiyayyun mayakansa rawanin daraja mara mutuwa; muryarsa kuma tana fitowa daga budaddun kofofi cewa: "Ga shi ina tare da ku. Kada ku ji tsoro. Na san dukan bakincikinku; na dauki bakincikinku. Ba da magabtan da basu gogu ku ke yaki ba. Na rigaya na yi yakin a madadinku, kuma cikin sunana kun fi masu nasara ma."

Mai-ceton zai aiko taimako daidai sa'an da muke bukata ne. Hanyar sama tsarkakakkiya ce da tafin sawun kafafunsa. Kowace kaya da ke huda kafafunmu ta huda nasa. Kowane giciye da aka ce mu dauka Shi Ya rigaya Ya dauka kafin mu. Ubangiji yana barin rashin jituwa domin Ya shirya mai-rai don salama ne. Lokacin wahala ce mai-ban tsoro ga mutanen Allah; amma lokaci ne da kowane mai-ba da gaskiya na kwarai zai zabi sama, kuma ta wurin bangaskiya zai ga bakan gizon alkawalin kewaye da shi.

"Pansassu na Ubangiji kuma za su komo, da rairawa za su iso Sihiyona, farinchiki madawami za ya kasanche a bisa kansu; za su sami murna da farinchiki; bakinchiki da ajiyar zuchiya za su gudu. Ni dai ni ne mai-yi maku ta'aziya: Kai wane ne da kake jin tsoron mutum mai-mutuwa, dan mutum kuma da za a maishe shi kamar chiyawa; har ma ka manta da Ubangiji mahalichinka,.... kana jin tsoron hasalar azalumi tuttur sa'an da yana shirin hallakaswa? Ina take fa hasalar azalumi, da samri za a sake takurarre, ba za ya mutu chikin rami ba, abinchinsa kuma ba za ya sare ba. Gama ni ne Ubangiji Allahnka, wanda yakan dama teku, har da ambaliyunta su yi ruri: Ubangiji mai-runduna shi ne sunansa. Na kuma sa zantattukana a chikin bakinka, na boye ka kuma a chikin inuwar tafin hannuna." Ishaya 51:11-16.

"Domin wannan ki ji ya ke kuntachiya, ke mai-maye amma ba da ruwan anab ba: hakanan Ubangijinki Yahweh Ya fadi, allahnki kuma wanda ya ke taimakon da'awar mutanensa, Ga shi na amshe kokon tangadinki, kwariyar hasalata ke nan: ba za ki kara shanta ba; amma zan sa ta a chikin hannun wdanda ke kuntata ki, su wadanda sun che ma ranki, Ki duka domin mu taka mu wuche: har ma kin maid a bayanki kamar kasa, kamar hanya kuma, ga wanda ke bi ta kai." Aya 21-23.

Idon Allah, sa'anda ya dubi sararrakin da ke zuwa, ya kafu kan tashin hankalin da mutanensa za su fuskanta, sa'anda mulkokin duniya za su ja daga da su. Kamar kamamme a wata kasa, za su kasance cikin tsoron mutuwa ta wurin yunwa ko ta wurin anfani da karfi a kansu. Amma Mai-tsarkin nan da ya raba Jan Teku a gaban Israila, za ya nuna ikonsa Ya juya bautarsu. "Za su zama nawa, in ji Ubangiji Mai-runduna, a chikin wannan rana da ni

ke yin ajiya mai-daraja ke nan; zan kwa kebe su, kamar yadda mutum yakan kebe dansa da ke bauta masa.” Malachi 3:17. Da za a zubar da jinin amintattun shaidun Kristi a lokacin nan ne, da ba zai zama kamar iri da aka shuka domin ya kawo ma Allah girbi ba. Amincinsu ba zai zama shaida da zai sa wadansu su amince da gaskiyar ba, gama zuciyar da ta taurara ta rigaya ta tutture rakuman ruwan jin kai ta yadda ba za su sake komawa ba. Da yanzu za a bar masu adalci a hannun magabtansu, da sarkin duhu zai yi nasara. In ji mai-zabura: “Gama a chikin ranar wahala za shi boye ni a chikin maboyar tent nasa za ya suturche ni.” Zabura 27:5. Kristi Ya rigaya Ya yi magana, ya ce: “Ku zo, mutanena, ku shiga chikin dakunanku, ku rufe ma kanku kofofi: ku buya kadan, har fushin ya wuche. Gama ga shi Ubangiji yana fitowa daga wurinsa domin Shi yi ma mazamnan duniya hukmchi sabada muguntassu.” Ishaya 26:26, 21. Mai-daraja ce cetaswar wadanda suka yi hakuri suka jira zuwansa, wadanda kuma sunayensu suna rubuce cikin Littafi na rai.

Babi na 40—An Tsirar da Mutanen Allah

Sa'anda za a janye kariyar dokokin mutane daga masu girmama dokokin Allah a kasashe dabam dabam a lokaci daya, za a yi yunkurin hallaka su. Sa'an da lokacin da aka sa a cikin dokan ya kusa, mutane za su hada baki domin su kawar da kungiyoyin nan da aka ki jini. Za a shirya murkushe su a dare daya, bugu daya da zai rufe muryar adawa da tsautawa.

Mutanen Allah, wadansu a kurkuku, wadansu a boye cikin dazuzuka da duwatsu, suna da rokon tsaron Allah, yayin da a kowane gefe kungiyoyin mutane dauke da makamai, da zugin miyagun malaiku, suna shiryawa domin aikin kisa. Yanzu ne, a sa'a a karshe, Allahn Israila zai shiga tsakani domin tsiradda zababbunsa. In ji Ubangiji: "Ku kwa za ku yi waka kamar lokacin da ake yin idi mai-tsarki da dare: da murna kwa a zuchiya, kamar lokachin da akan tafi ... garin a zo da dutsen Ubangiji, watau dutsen Israila. Ubangiji kuma za ya sa a ji murya tasa mai-daraja, Ya nuna sabkowar hannunsa, tare da fushinsa mai-zafi, da harshen wuta mai-chinyewa; da tsawa da hadari, da duwatsun kankara." Ishaya 30:29, 30.

Da ihun nasara, da gori da zagi, garkuwan miyagun mutane suna gaf da rugawa kan masu adalci, sai ga duhu mai-nauyi da ya fi dare, ya sauko bisa duniya. Sa'an nan bakar gizo, mai-darajar kursiyin Allah, ta rufe sammai, kuma kaman ta kewaye kowace kungiyar addu'a. taron jama'an da suka fusata, nan da nan aka kama su ihun ba'arsu ya kare. Aka manta da wadanda su suka so su kashe. Da tsoro suka kalli alamar alkawalin Allah, suka kuma so da za a kare su daga haskensa.

Mutanen Allah za su ji murya tana cewa: "Dubi sama," kuma suna duban sama za su ga bakan gizon alkawalin. Za a raba bakaken gizagizai din nan da suka rufa sararin sama. Kuma kamar Istifanus, za su kalli sama da karfin hali har su ga darajar Allah da Dan mutum kuma yana zaune a kursiyinsa. A cikin yanayinsa na Allahntaka za su ga alamar kaskancinsa, daga lebunansu kuma za su ji rokon da zai gabatar a gaban Ubansa da malaiku masu-tsarki cewa: "Wadanda ka ba ni, ina so su zamna wurin da ni ke, tare da ni." Yohanna 17:24. Kuma za a ji wata murya mai-dadi cike da murna, tana cewa: "Suna zuwa! Suna zuwa! masu-tsarki, marasa mugunta, marasa kazamta kuma. Sun kiyaye kalmar hakurina; za su yi tafiya chikin malaikun;" sai kuma lebunan wadanda suka rike bangaskiyarsu da gaske za su ta da kuwwar nasara.

Da tsakar dare ne Allah zai bayana ikon Shi na tsirar da mutnensa. Rana za ta bayana, tana haskakawa cikin karfinta. Alamu da al'ajibai za su biyo bi da bi da hanzari. Miyagu za su kalli al'amarin da razana da mamaki kuma, yayin da masu adalci za su kalli alamar tsirarsu da murna. Kowane abu a halita, kaman ya kauce daga hanyarsa ne. Rafuka za su dena gudu. Manyan gizagizai masu kauri, masu duhu kuma, za su taso suna karo da juna. A tskiyar fushin sammai din akwai wani sarari mai-darajan gaske, ta inda muryar Allah kamar motsin ruwaye tana cewa: "An gama." Ruya 16:17.

Muryan nan za ta girgiza sammai da duniya. “Za a yi babban rawan duniya irin wanda ba a taba yi ba, tun kasancewar mutane a duniya, rawan duniya mai-girma, mai-karfi kuma.” Aya 17,18. Sararin sama kaman yana budewa yana rufewa kuma, daraja daga kursiyin Allah tana wucewa ciki. Duwatsu suna rawa kamar ciyawa a iska, kuma manya manyan duwatsu suna warwatsuwa ko ta ina. Akwai wani ruri kaman na guguwa da ke zuwa. Teku ya tuntsure, ya fusata. Za a ji karar mahaukaciyar guguwa kamar muryar aljannu da ke aikin hallaka. Dukan duniya za ta ja numfashi ta kumbura kamar rakuman ruwan teku. Fuskar duniyan tana tsagewa. Tussansa sai ka ce suna watsewa ne. Jerin duwatsu suna nutsewa. Tsibirai masu mazamna cikin su za su bata. Tashoshin jiragen ruwa da suka zama Kamar Sodom sabo da muguntarsu, za su nutse cikin ruwayen. An kuma tuna da Babila babba a gaban Allah, “domin a ba ta koko na ruwan anab na zafin hasalassa.” Manya manyan kankara, “kowane guda nauyinsa ya yi wajen talent daya,” su na aikinsu na hallaka. Aya 19,21. Biranen duniya masu alfarma za a rusar da su. Manyan gine ginen da mutanen duniya suka kashe arzikinsu domin su daukaka kansu akai su na rugujewa a idonsu, suna zama kango. Gidajen kaso su na rushewa, mutanen Allah kuma, wadanda aka kulle su sabo da sabo da imaninsu, za a yantar da su.

Za a bude kabarbaru, “Da yawa kwa daga chikin wadanda su ke barci chikin turbayar kasa a su falka , wadansu zuwa rai na har abada, wadansu kuma zuwa kunya da reni mara matuka.” Daniel 12: 2. Dukan wadanda suka mutu cikin bangaskiyar malaika na uku za su fito daga kabari da daraja, domin su ji alkawalin Allah na salama da wadanda suka kiyaye dokarsa. “Su kuma wadanda suka soke shi.” (Ruya 1:7), wadanda suka yi ba’a ga azabar mutuwar Kristi, da kuma masu mafi-yawan jayaya da gaskiyarsa da mutanensa, za a tashe su su ganshi cikin darajarsa su kuma ga girmamawa da za a yi ma masu biyayya.

Har yanzu dai, gizagizai suna rufe da sararin sama, amma rana takan ratsa loto loto, tana kama da idon ramuwa na Yahweh. Walkiya masu ban tsoro suna tsalle daga sammai, suna kunsa duniya cikin fallen wuta. A kan rurin tsawa, muryoyi da ba a gane su ba, masu ban tsoro kuma, suna bayana hallakar miyagu. Ba duka ne za su fahimce su sarai ba. Wadanda ba da dadewa ba, da garaje da fahariya da tumbe suka yi ta murnar zaluncin da suka yi ma mutanen Allah masu-kiyaye dokokinsa, yanzu mamaki ya cika su, suna rawan jiki sabo da tsoro. Ana jin ihunsu fiye da karar kasa da teku da iska. Aljannu za su yarda cewa Kristi Allah ne, su kuma yi rawan jiki a gaban ikonsa, yayin da mutane ke rokon karin jin kai, suna kuma damuwa game da jin kai, suna kuma fama cikin razana mai-tsanani.

In ji annabawa na da, sa’an da suka hangi ranar Allah cikin wahayi mai-tsarki: “Ku yi ihu gama ranar Ubangiji ta kusa: misalin hallaka daga wurin Mai-iko duka.” Ishaya 13:6. “Ka shiga chikin dutse, ka buya chikin turbaya, daga gaban razanar Ubangiji, da darajar daukakassa. Za a sunkuyadda duban rai na mutum, ta da hanci na mutane kuma za ya sha kaskanchi; Ubangiji kadai kwa za ya daukaka chikin wannan rana. Gama za a yi ranar Ubangiji mai-runduna, a kan kowane mai-girman kai da mai-ta da hanchi, a kan kowane

daukakakken abu kuma; za a kwa kaskantadda shi.” “A chikin ranan nan mutum za ya dauki gumakansa na azurfa, da gumakansa na zinariya, wadanda aka yi masa domin sujada ya yar ma jaba da jemage; domin ya shiga chikin ramummuka na duwatsu, da chikin tsatsaguwa na tsagaggun duwatsu kuma, daga gaban razanar Ubangiji da darajar daukakassa, sa’anda ya tashi garin girgiza duniya da karfi.” Isahaya 2:10 -12; 20, 21.

Ta wurin wani tsago a gizagizan, wani tauraro zai haskaka wanda walkiyarsa ta karu ribi hudu, sabo da duhun. Yana ba amintattu bege da murna, wahala da fushi kuma ga masu ketare dokar Allah. Wadanda suka sadakar da komi sabo da Kristi, yanzu za su kasance da tsaro, boyayyu kamar cikin sirrin rumfar Ubangiji. An rigaya an gwada su, kuma a gaban duniya da masu rena gaskiya sun nuna shaidar kaunarsu ga Shi wanda Ya mutu dominsu. Babban canji ya zo kan wadanda suka rike amincinsu har a bakin mutuwa ma. An tsirar da su faraf daya daga mugun zaluncin mutane da suka juya suka zama aljannu. Fuskokinsu da suka nuna taraddadi da damuwa yanzu sun haskaka da mamaki da bangaskiya da kauna. Muryoyinsu suna tashi da wakar nasara cewa: “Allah mafakanmu ne da karfinmu, taimako ne na kurkusa chikin wahala. Domin wannan ba za mu ji tsoro ba, ko da duniya ta juya, ko a duwatsu sun motsu a chikin zuchiyar tekuna; ko da duwatsunsu suna ruri suna hauka, duwatsu suna rawa da kumburinsu.” Zabura 46:1-3.

Yayin da kalmomin amincewan nan mai-tsarki ke hawa zuwa wurin Allah, gizagizan za su koma baya, za a kuma ga sammai cike da taurari, da mafificiyar daraja sabanin duhun sarari mai-fushin da ya kewaye su ta kowane gefe. Darajar birnin sama din tana kwararowa ta budaddun kofofin nan ne. Sa’an nan za a ga hannu rike da alluna biyu na dutse da aka rufe su tare. In ji annabin: “Sammai za su ba da labarin adilchinsa; gama Allah mai-shari’a ne da kansa.” Zabura 50:6. Doka mai-tsarkin nan, adalchin Allah, da aka yi shelarta cikin tsawa da wuta daga Sinai a matsayin maibishewar rayuwa, yanzu za a bayana shi ga mutane a matsayin kaidar hukumci. Hannun zai bude allunan, za a kuma ga umurnin dokoki goma din da aka rubuta kaman da alkalamin wuta. Kalmomin suna bayane ta yadda kowa zai iya karanta su. Tunani zai falka, za a shafe duhun camfi da ridda daga kowace zuciya, kuma kalmomi goman nan na Allah, gajejjeru, bayanannu, masu iko, za a gabatar da su ga ganin dukan mazamnan duniya.

Ba shi yiwuwa a bayana tsoro da bakincikin wadanda suka tattake dokoki masu-tsarki na Allah. Ubangiji Ya ba su dokarsa; da sun gwada halayensu da dokan nan su kuma sansance aibin halayensu tun da sauran zarafin tuba da canjin hali; amma domin a sami karbuwar duniya, suka kawar da umurnin dokokin, suka kuma koya ma wadansu su ketare su. Sun yi kokarin tilasta mutanen Allah su kazantar da Assabbat dinsa. Yanzu dokan nan da suka rena yana hukunta su. A fili sun gane cewa ba su da hujja. Su suka zabi wanda za su yi masa sujada. “Sa’an nan za ku komo, ku rarrabe tsakanin adili da mugu, tsakanin wanda yake bauta ma Allah da wanda ba ya bauta masa ba.” Malachi 3:18.

Magabtan dokar Allah, daga shugabannin addini har zuwa mafi kankana cikinsu, za su sami sabuwar fahimtar gaskiya da abin da ya kamata su yi. A makare za su ga cewa Asabbat na doka ta hudu ne hatimin Allah Mai-rai. A makare za su ga ainihin yanayin assabbat din nan nasu na karya da harsashen yashi da su ke ta gini a kai. Za su gane cewa suna ta fada da Allah ne. Mallamai na addini sun kai rayuka ga hallaka da sunan cewa suna bishe su zuwa paradise ne. Sai ranar karshe ta lissafi ne za a ga girman alhakin mutanen da ke aiki mai-tsarki da kuma munin sakamakon rashin amincinsu. Cikin rai na har abada ne kadai za mu iya kiyasta munin hasarar mai-rai daya. Abin tsoro ne abin da Allah za y ace masa: Rabu da ni, mugun bawa.

Za a ji muryar Allah daga sama ya na bayana rana da sa'ar zuwan Yesu, yana kuma mika ma mutanensa alkawali na har abada din. Kamar kuwwar tsawa mafi-karfi, kalmominsa za su gangaro duniya. Israila ta Allah tana ji, da idanunsu sama. Za a haskaka fuskokinsu da darajarsa, za su kuma haskaka kamar fuskar Musa lokacin da ya sauko daga Sinai. Miyagu ba za su iya kallonsu ba. Kuma sa'an da za a furta albarka bisa wadanda suka girmama Allah ta wurin kiyaye Assabbat nasa da tsarki, za a yi babban ihun nasara.

Ba da jimawa ba, karamin bakin girgije zai bayana ta gabas, girmansa kamar tafin hannun mutum. Girgijen da zai kewaye Mai-ceton ne, wanda kuma daga nesa za a ga kamar yana da duhu ne. Mutanen Allah za su san cewa wannan alaman Dan mutum ne. Cikin zama shuru za su kalle shi yayin da yake kusantowa duniya, yana kara haske da daraja, har sai ya zama babban farin girgije, gindinsa mai-daraja kamar wuta mai-konawa, samansa kuma bakan-gizon alkawalin. Yesu yana hawa a matsayin babban Mai-nasara. Yanzu ba mutum mai-bakinciki ba da zai sha koko mai-daci na kunya da kaito, zai zo, Mai-nasara a sama da kasa, domin ya hukumta masu rai da matattu. "Mai-aminchi da Mai-gaskiya," "chikin adilchi kwa yake yin shari'a da yaki kuma." Kuma, "Rundunan yaki kwa wadanda ke chikin sama" (Ruya 19:11, 14) suka bi Shi. Da wakoki masu amo na sama malaiku masu-tsarki da ba za a iya lissafta su ba, za su bi shi. Sararin sama dai kaman ya cika da masu hasken- "dubu goma sau dubu goma, da dubban dubbai." Babu alkawalin dan Adam da zai iya bayana wannan al'amarin; ba tunanin mutum da zai iya fahimtar ban-sha'awarsa. "Daraja tasa ta rufe sammai, duniya kwa ta chika da yabonsa. Shekinsa yana kama da haske." Habakuk 3:3. Sa'an da girgijen ya kara kusantowa, kowane ido zai ga Sarkin rai. Babu rawanin kaya a kan nan mai-tsarki, amma rawanin daraja ke zaune a kan nasa. Fuskarsa ta fi rana haskakawa. A bisa rigatasa da bisa chinyatasa kuma yana da suna a rubuche, SARKIN SARAKUNA DA UBANGIJIN IYAYENGIJI." Ruya 19:16.

A gabansa "dukan fuskoki fa sun komo fari;" tsoron bakin ciki na har abda zai fada ma masu kin jin kan Allah. "Zuchiya tana narkewa, guwawu suna bugun juna, ... fuskokin dukansu kwa suna fari." Irmiya 3:6; Nahum 2:10. Masu adalci za su yi kuka da rawan jiki suna cewa: "Wa zai iya tsayawa?" Wakar malaikun za ta tsaya, kuma wuri zai yi shuru na ban tsoro har wani lokaci. Sa'an nan za a ji muryar Yesu yana cewa: "Alherina ya ishe ku."

Za a haskaka fuskokin adilai, murna kuma za ta cika kowace zuciya. Malaiku kuma za su kara amo su yi waka kuma yayin da suje kara kusatowa duniya.

Sarkin sarakuna zai sauko a kan girigjen, yafe da harshen wuta mai-ci bal-bal. Za a nade sammai tare kamar walkar takarda, duniya za ta yi rawan jiki a gabansa, kuma za a gusar da kowane dutse da tsibiri daga wurinsa. “Allahnmu yana zuwa, ba kwa za ya yi shuru ba: wuta za ta chi a gabansa, za ta yi hauka kuma kwarai kewaye da Shi. Za ya kira sammai daga bisa, za Ya kira duniya kuma domin Ya yi ma mutanensa shari’a.” Zabura 50:3,4.

“Sarakunan duniya kuma, da hakimai, da jarumawa, da attajirai, da masu-karfi, da kowane bawa da da, suka buya chikin ramummuka da pannun duwatsu; suna che ma duwatsu da pannu, Ku fado mana, ku rufe mu daga fuskar wanda Ya zamna bisa kursiyin, daga hasalaar Dan ragon kuma: gama babban rana ta hasalassu ta zo, wa ke da iko shi tsaya kuma?” Ruya 6:15-17.

Ba’an reni zai tsaya. Lebuna masu-karya za su yi shuru. Surutun makamai, hayaniyar yaki “chikin rigimar yaki da tufafi mirginannu chikin jini (Ishaya 9:5), za su taya. Ba abin da ake ji yanzu sai muryar addu’a da karar kuka da makoki. Kukan zai fito daga lebunan da dazun nan ke ba’a ne. “Babban rana ta hasalassa ta zo; wa ke da iko shi tsaya kuma?” miyagu suna roko a bizne su a kalkashin duwatsu, maimako su sadu da fuskar Shi wanda suka rena suka kuma ki.

Muryar da ke shiga kunen matattu, sun sani. Sau da yawa amonta ya dinga kiran su zuwa tuba. Sau da yawa sun rika jinta cikin rokon wani aboki ko dan’uwa ko Mai-fansa ma. Ga masu kin alherinsa ba muryar da ta fi hukumtawa da tsautawa kamar muryar da ta dade ta na roko cewa: “Ku juyo dai ku bar miyagun halulukanku; don mi za ku mutu?” Ezekiel 33:11. In ji Yesu: “Da shike na yi kira, kun ki; na mika hannuna, ba wanda ya kula; amma kun wakala dukan shawarata, ba ku yarda da tsautawata ba ko kadan” Misalai 1: 24, 25. Muryan nan za ta tuna masu ababa da za su so da an shafe su - gargadin da suka rena, gayyatan da suka ki, zarafin da suka wofinta.

Akwai wadanda suka yi ma Kristi ba’a lokacin da aka wulkanta Shi. Da karfi mai-motsa zuciya za a tuna masu kalmomin nan na Kristi lokacin da babban priest ya yi masa tambaya, inda Ya ce: “Gaba nan za ku ga Dan mutum a zamne a hannun daman na iko, yana zuwa kuma bisa gizagizan sama.” Matta 26:64. Yanzu suna ganin Shi cikin darajarsa, amma basu rigaya sun gan Shi a hannun daman iko ba.

Wadanda suka rena furcinsa cewa Shi ne Dan Allah za su yi shuru yanzu. Akwai Hirudus mai-fahariyan nan da ya yi ma sarautar Kristi ba’a, ya kuma sa sojojin da ke masa ba’a suka sa masa rawanin sarauta. Akwai ainihin mutanen da suka sa masa wata riga da hannun su, suka sa masa rawanin kaya a goshinsa mai-tsarki, a hannunsa kuma suka sa sandar sarauta ta ba’a, suka kuma durkusa a gabansa cikin ba’a na sabo. Mutanen nan yanzu

za su kau da fuska daga kallon da yake yi masu, su kuma so su gudu daga darajar kasancewarsa. Wadanda suka buga kusoshi a hannuwansa da kafafunsa, da sojan da ya soki gefensa, za su dubi alamun nan da razana da juyayi kuma.

A sarari priestoci da sarakuna za su tuna al'amuran Kalfari. Cikin tsoro mai-yawa za su tuna yadda cikin murna irin na Shaitan suka ce: "Ya chechi wadansu, ya kasa cheton kansa. Sarkin Israila ne shi; shi sabko daga gichiye yanzu, mu kwa mu a ba da gaskiya gare shi. Yana dogara ga Allah; bari ya cheche shi yanzu, idan yana son sa." Matta 27: 42,43.

A bayane za su tuna misalin nan na Mai-ceton game da manoman da suka ki ba ubangijinsu anfanin gonansa, suka wulakanta bayinsa suka kuma kashe dansa. Za su kuma tuna hukumcin da su kansu suka furta cewa: Ubangijin gonan zai hallaka miyagun mutanen nan. Cikin zunubi da horon mutanen nan marasa aminci, priestoci da dattibai za su ga abin da su kansu suka yi da hallakar da ta cancance su. Wani ihun kuma zai taso yanzu. Fiye da ihun da aka cika titunan Urushalima da su, cewa: "A giciye shi, a gichiye shi," yanzu wata muryar tsoro da makoki ce za ta taso tana cewa: "Shi ne Dan Allah! Shi ne Masiya na gaskiyan!" za su so su gudu daga wurin Sarkin sarakunan. A banza za su so su buya a cikin kogunan kasa da ta tsatsage lokacin hargitsin.

Cikin rayuwar dukan masu kin gaskiya, wani lokaci lamiri yakan falkas da su, zuciya takan tuna masu da rayuwarsu ta riya, sai rayuwarsu ta cika da nadama ta banza. Amma wadannan ba komi ba ne idan aka gwada da nadamar wancan rana da "tsoro ya afka masu kamar hadari," sa'an da "masifarku ta chi maku kamar guguwa." Misalai 1:27. Wadanda suka so su hallaka Kristi da amintattunsa, yanzu za su ga darajan da ke kansu. A tsakiyar razanar su za su ji muryoyin tsarkaka cikin farin ciki suna cewa: "ga shi wannan Allahnmu ne; mun jirache shi, za ya cheche mu." Ishaya 25:9.

Cikin rawan duniya da walkiya, da rurin tsawa, muryar Dan Allah za ta kirawo tsarkaka da ke barci. Za Ya dubi kabarbarun adilai, sa'an nan, da hannayensa sama, zai ce: "Ku falka, ku falka, ku falka, ku da kuke barci cikin turbayar, ku tashi kuma!" Ko ina cikin duniya, matattu za su ji wannan muryar, kuma wadanda suka ji za su rayu. Dukan duniya kuma za ta amsa da takawar babban rundunar mayakan kowace al'umma, da dangi, da harshe, da jama'a. Daga kurukun mutuwa za su zo, yafe da daraja mara mutuwa, suna cewa: "Ya mutuwa ina nasarakki? Ya mutuwa, ina karinki? Korinthiyawa I, 15:55. Sa'an nan adilai da ke raye, da adilai da aka ta da su daga matattu za su hada muryoyinsu cikin dogon ihu na murnar nasarar."

Duka za su fito daga kabarbarun da kamaninsu, daidai yadda su ke lokacin da suka shiga kabarin. Adamu da zai kasance cikinsu dogo ne da surar martaba, amma a sura zai kasa Dan Allah da kadan. Zai bambanta sosai da mutanen sararakin baya; cikin wannan fanni za a nuna yawan lalacewar 'yan Adam. Amma duka za a tashi sabobi da kuzarin samartaka ta har abada. A cikin farko, an halici mutum da kamanin Allah ne, ba a hali kadai

ba, amma duk da siffa da kamani. Zunubi ya bata ya kuma so ya lalata suran nan na Allah gaba daya; amma Kristi Ya zo domin Shi mayas da abin nan da aka rasa. Za Ya canja jikunan nan namu kazamtattu Ya kuma sifanta su kamar jikinsa na daraja. Suran nan mai-mutuwa mai-lalacewa kuma, mara ban sha'awa, wanda zunubi ya kazamtar, zai zama mara aibi, kyakyawa mara mutuwa kuma. Za a bar dukan illoli da nakasa a cikin kabari. Sa'an da an mayas da su wurin itacen rai a Adnin tsarkaka za su fita (Malachi 4:2) zuwa siffar dan Adam cikin darajarta ta halitta. Za a cire burbushin zunubi da suka ragu, sa'an nan amintattu na Kristi za su bayana cikin kyau na Ubangiji Allahnmu, a tunani da ruhu da jiki za su zama da sura mara aibi irin na Ubangijinsu. Fansa ke nan mai-ban al'ajibi! wanda an dade ana zancensa, an dade ana begensa, an yi bimbininsa da bege mai- yawa, amma ba a taba fahimtarsa duka ba.

Za a canja tsarkaka masu-rai faraf daya, da kyaftar ido. Da muryar Allah za a darajanta su; yanzu za a ba su rashin mutuwa, kuma tare da tsarkaka da aka ta da su za su wanzu domin su sadu da Ubangijinsu a sararin sama. Malaiku za su kai kananan yara wurin uwayensu. Abokai da mutuwa ta raba su da dadewa za a sada su, babu rabuwa kuma, wakokin murna kuma za su hau zuwa birnin Allah.

A kowane gefen karusar girgijen akwai fukafukai, a kalkashinsa kuma akwai garegare masu rai, kuma yayin da karusar ke haurawa, garegaren suna cewa: "Mai-tsarki," fukafukin kuma, yayin da suke motsi, suna cewa, "Mai-tsarki, Mai-tsarki, Mai-tsarki, Ubangiji Allah Madaukaki." Fansassu kuma za su yi ihu su ce, "Haleluya!" yayin da karusar ke ci gaba zuwa sabuwar Urushalima.

Kafin shigowa Birnin Allah, Mai-ceton zai ba masu binsa shaidar nasara ya kuma nada su da lambobin sarautarsu. An jera su, siffar murabba'i ne kewaye da Sarkinsu wanda siffarsa, a martaba ta zarce ta tsarkaka da ta malaiku, fuskansa kuma yana haskaka su cike da kauna. Ko ina cikin rundunan fansassu da yawansu ba mai iya kirgawa, idanunsu suna kallon Shi ne. Kowane ido yana duban darajarsa, Shi wanda aka bata fuskarsa fiye da na kowane mutum, siffarsa kuma aka ba ta fiye da ta 'ya'yan mutane. Bisa kawunan masu nasaran, Yesu da hannun damansa zai aza rawanin daraja. Akwai rawani domin kowa da sabon sunansa a kai (Ruya 2:17), da rubutu mai-cewa "Tsarki ga Ubangiji." Za a sa ma kowa dabinon nasara da giraya mai-walkiya ahannunsa. Muzika mai-dadi kwarai. Dadi da ya wuce misali zai cika kowace zuciya, za a kuma ta da kowace murya cikin yabo da murna, cewa: "A gareshi wanda yake kamnarmu, ya kwanche mu kuma daga zunubanmu chikin jininsa, ya sa mu mu zama mulki, mu zama priest ga Allahnsa da Ubansa; a gareshi daukaka da mulki har zuwa zamanun zamanai." Ruya 1:5,6.

A gaban fansassu, ga birni mai-tsarkin. Yesu za ya bude kofofi masu adon, al'umman da suka kiyaye gaskiyar kuma za su shiga ciki can za su ga Paradise na Allah, da gidan Adamu kafin ya yi zunubi. Sa'an nan muryan nan da ya fi duk wata muzika da kunen masu

mutuwa sun taba ji, zai ce: “Yakinku ya kare,” “Ku zo, ku masu albarka na Ubana, ku gaji mulkin da an shirya dominku tun kafawar duniya.”

Yanzu addu’ar Mai-ceton domin almajiransa ta cika, cewa: “Wanda ka ba ni, ina so su kazance wurin da ni ke.” “Marasa aibi chikin mafifichin farin zuchiya a gaban bayanuwar darajassa” (Yahuda 24), Kristi za ya mika ma Uban wadanda aka saya da jininsa, yana cewa: “Ga ni nan, da yayan da ka ba ni.” “Wadanda kai ka ba ni, na kiyaye su.” Dubi dai al’ajiban kauna mai-fansa! Dadin wannan sa’ar sa’anda Uba mara iyaka, sa’an da Ya dubi fansassun, zai ga kamaninsa, an rigaya an kawar da illar zunubi, burtuntunansa kuma an cire, ‘yan Adam kuma sun sake jituwa da Allah!

Da kauna wadda ta wuce misali, Yesu zai marabci amintattun zuwa murnar Ubangiji. Murnar Mai-ceton ita ce ganin rayukan nan a mulkin, wadanda aka cetas ta wurin azabarsa da kaskancinsa yayin da suke gani cikn cetattun, wadanda aka kawo wurin Kristi ta wurin addu’o’insu da hadayarsu ta kauna. Yayin da su ke taruwa kewaye da babban farin kursiyin nan, murna da ta fi karfin bayanawa za ta cika zukatansu, sa’an da suka ga wadanda suka kawo ma Kristi, suka kuma ga daya ya samo wadansu, dukansu aka kawo su wurin hutawa, inda za su ajiye rawaninsu a sawayen Yesu, su kuma yabe Shi har abada.

Yayin da ake marabtar fansassu cikin birnin Allah, za a yi ihu na yabo sabo da nasara, Adamun nan biyu sun kusa saduwa. Don haka Allah yana tsaye, hannuwansa a mike domin karban uban zuriyar mu — mutumin da Shi Ya halitta, wanda ya yi ma Mahalicinsa zunubi, wanda sabo da zunubinsa kuma Mai-ceton ke dauke da alamun giciyewarsa. Sa’an da Adamu zai ga alamun kusoshin, ba zai fadi a kirjin Ubangijinsa ba, amma cikin kaskantar da kai, zai fadi a sawayensa ne, yana cewa; “Ka isa, ka isa, Dan rago da an kashe!” A hankali Mai-ceton zai daga shi, ya kuma ce mashi ya sake kallon gidan nan na Adnin daga inda da dadewa aka kore shi.

Bayan korarsa daga Adnin, rayuwar Adamu a duniya ta cika da bakinciki. Kowane ganye da ke bushewa, kowace dabbar hadaya, kowace burtuntuna a kyakyawar fuskar halitta, kowane la’ani ga tsarin mutum, yakan tuna ma Adamu da zunubinsa. Azabar nadama ta yi muni sa’an da ya ga zunubi yana karuwa, kuma akan amsa masa fadakarsa da zargin cewa shi din ne sanadin zunubi. Da tawali’u da hakuri, ya sha horon zunubi har kusan shekara dubu. Da aminci ya tuba daga zunubinsa, ya kuma mutu cikin begen tashin matattu. Dan Allah Ya fanshi kasawar mutum da faduwarsa; yanzu kuma ta wurin aikin kafara za a mayas da Adamu ga mulkinsa na fari.

Cikin farinciki zai dubi itatuwan da ya so da, ainihin itatuwan da shi kansa da yakan diba a lokacinsa na murna da rashin laifi. Zai ga anab din da hannuwansa suka gyara, ainihin furanin da yakan ji dadin lura da su. Zuciyarsa za ta tuna ainihin yanayin; zai gane cewa hakika wannan Adnin ne aka mayar, da kyau ma fiye da lokacin da aka kore shi daga ciki. Mai-ceton zai kai shi wurin itacen rai, Ya tsinka Ya ba shi ya ci. Zai duba kewaye da

shi ya ga taron iyalinsa fansassu suna tsaye a Paradise na Allah. Sa'an nan zai jefa rawaninsa mai-walkiya a sawayen Yesu ya fadi a kirjinsa ya rungumi Mai-fansar. Zai taba girayar zinariyar, sama kuma za ta amsa kuwwar wakar nasarar, cewa: "Na kirki ne, na kirki ne, na kirki ne Dan ragon da an kashe, yana raye kuma!" Iyalin Adamu za su amsa wakar, su kuma jefa rawaninsu a sawayen Mai-ceton yayin da suke durkusawa a gabansa cikin sujada.

Malaikun da suka yi kuka lokacin faduwar Adamu, suka kuma yi farinciki sa'an da Yesu bayan tashinsa ya hau sama, bayan ya bude kabarin domin dukan wadanda za su ba da gaskiya ga sunansa, za su kalli wannan sake saduwar. Yanzu za su ga cikawar aikin fansa, za su kuma hada muryoyinsu cikin wakar yabon.

A kan tekun madubi a gaban kursiyin, wanda yake kaman an garwaya shi da wuta, cike da darajar Allah, za a yi taruwar wadanda suka sami nasara kan bisan, da kan gumkinsa, da kan shaidarsa, da kan lamban sunansa. Tare da Dan ragon a kan Dutsen Sihiyona, rike molon Allah, zambar dari, da zambar arba'in da hudu din nan da aka fanshe su daga cikin mutane za su tsaya, a wurin kuma za a ji kamar muryar ruwaye masu- yawa, kamar rurin babbar tsawa kuma, za a ji "muryar masu molo suna kada molonsu." Za su kuma raira "Sabuwar waka" a gaban kursiyin, wakan da ba wanda zai iya koyonsa sai dai mutum zambar dari da zambar arba'in da hudun din. Wakan Musa da Dan ragon ne, wakar tsira. Ba wanda zai iya koyonsa sai mutum zambar dari da zambar arba'in da hudun nan; da shike wakar abin da ya faru da su ne, wanda bai taba faruwa da wadansu ba. "Su ne su kan bi Dan rago inda Ya tafi duka." Wadanda aka fyauce su daga duniya, daga cikin masu rai, ana ce da su "nunan fari ga Allah da Dan rago." Ruya 15:2,3; 14:1-5.

"Su ne wadanda suka fito daga chikin babban tsanani;" sun rigaya sun wuce lokacin wahala irin da ba a taba ji ba tun da aka yi al'umma; sun jimre azabar lokacin wahalar Yakub; sun rigaya sun tsaya ba matsakanci lokacin zubowar hukumcin Allah. Amma an tsiradda su, gama sun "wanke rigunansu, suka faranta su chikin jinin Dan ragon kuma." "A chikin bakinsu ba a iske karya ba: marasa aibi ne su" a gaban Allah. "domin wannan suna gaban kursiyin Allah; suna masa bauta kuma dare da rana cikin haikalinsa: shi kuma wanda Ya zamna bisa kursiyin za ya inuwantadda su." Sun rigaya sun ga duniya yadda yunwa da annoba sun lalatar da ita, rana kuma ta na da iko ta kone mutane da zafi mai-yawa, su kansu kuma sun jimre wahala da yunwa da kishirwa. Amma "Ba za su kara jin yunwa ba, ba kwa za su kara jin kishirwa ba; rana kuma ba za ta buge su ba, ko kowane irin zafi: gama Dan rago wanda ke chikin tsakiyar kursiyin za ya zama makiyayinsu, za ya bishe su kuma wurin mabulbulan ruwaye na rai: Allah kuma za ya share dukan hawaye daga idanunsu." Ruya 7:14-17.

Cikin dukan sararaki akan ilimantar da zababbu na Allah a kuma horar da su cikin makarantar gwaji. Sun yi tafiya cikin matsatsun hanyoyi a duniya; an tsarkake su cikin tanderun azaba. Sabo da Yesu sun jimre adawa da kiyayya da bata suna. Sun bi Shi cikin

yake yake munana; sun sha musun kai da yankan buri. Ta wurin abin da ya faru da su sun gane muguntar zunubi da ikonsa da laifinsa, da kaitonsa; kuma suna kallon shi da kyama. Sanin hadaya mara-matuka da aka yi domin magance zunubi zai ladabtar da su ga ganin kan su, ya kuma cika zukatansu da godiya da yabo da wadanda basu taba faduwa ba ba za su iya faimta ba. Suna kauna da yawa domin an gafarta masu da yawa. Da shike sun zama da rabo cikin wahalolin Kristi, sun cancanta su zama da rabo cikin darajarsu.

Magadan Allah sun zo daga kauyuka, daga kurukuku, daga wuraren horo, daga duwatsu, daga hamada, daga kogunan kasa, daga kogunan teku. A duniya sun sha talauci da azaba da zalunci. Miliyoyi sun je kabari a wulakance domin sun ki su amince da rudin Shaitan. Kotunan kasa suka hukaumta su cewa su masu-laifi mafi muni ne. Amma yanzu "Allah mai-shari'a ne da kansa." Zabura 50:6. Yanzu za a warware hukumcin duniya. "Za ya kuma kawasda zargin mutanensa" Ishaya 25:8. "Za a che da su Jama'a mai-tsarki, Pansassu na Ubangiji." Ya rigaya Ya umurta "a ba su dajiyar fure maimakon toka, mai na farin chiki maimakon makoki, mayafi na yabo maimakon ruhu na nauyi." Ishaya 62:12; 61:3.

Ba za su kasance kamammu masu shan azaba, a warwatse, wulakantattu kuma ba. Daga nan za su kasance tare da Ubangiji har abada. Za su tsaya a gaban kursiyin, yafe da tufafi masu —tamanin da mutane da aka fi girmamawa a duniya basu taba sa irinsu ba. Za a daura masu rawani masu daraja da ba a taba daura ma wani sarki a duniya ba. Kwanakin azaba da kuka sun kare har abada. Sarkin daraja Ya shafe hawaye daga dukan fuskoki; an cire kowane dalilin bakin ciki. Da ganyen dabino a hannuwan su za su raira wakar yabo mai-dadi; kowace murya za ta raira har sai wakar ta cika kowane wuri a sama, suna cewa: "Cheto ga Allahnmu ne, wanda ya zamna bisa kursiyin, ga Dan ragon kuma." Kuma dukan mazamnan sama za su amsa su ce: "Amin: albarka da daukaka da hikima, da godiya da daraja, da iko da karfi, ga Allahnmu har zuwa zamanun zamanai." Ruya 7: 10,12 .

Cikin rayuwarmu a duniyan nan, za mu iya fara gane batun fansa ne kawai. Da ganewar mu mai-iyaka, za mu iya bimbini kan kunya da darajar, rai da mutuwar, adalci da jinkan da suka sadu a giciyen ne; duk da haka, komi yawan tunanin mu baza mu iya fahimtar duk cikar ma'anar fansa ba. Kadan kawai ake fahimtar tsawo da fadi da zurfin kauna mai-kawo fansa. Ba za a sami cikakkiyar fahimtar shirin fansa ba, ko ma sa'anda fansassu sun ga yadda ake ganinsu, suka kuma san yadda aka sansu: amma har cikin dukan sarraki har abada sabobin gaskiya za su ci gaba da bayanuwa ga zukatan mutane. Ko da shike bakinciki da azaba da jarabobin duniya za su kare, za a kuma cire sanadinsu, mutanen Allah za su ci gaba da sanin farashin cetonsu.

Giciyen Kristi ne zai zama kimiyyar fansasssu da wakarsu har abada. Cikin darajar Kristi za su ga giciyewar Kristi. Ba za a taba manta cewa Shi wanda Ya halitta, Ya kuma rike dukan duniyoyi, Kaunatace na Allah, Martabar sama, Shi wanda malaiku suka yi murmnar girmama Shi, Ya kaskantar da kansa domin Shi daukaka mutum fadadde, cewa

Ya dauki laifin zunubi da kunyarsa, da boyewar fuskar Ubansa, har sai da kaiton bataciyar duniya suka karya zuciyarsa, suka kuma murkushe ransa a giciyen Kalfari. Cewa Mahalicin dukan duniyoyi, Mai-rike da dukan kadara, ya ajiye darajarsa, Ya kuma kaskantar da kansa sabo da kaunar mutum da yake yi zai ci gaba da ba dukan halitta mamaki da sha'awa har abada. Dukan al'ummomin cetattu za su dubi mai-cetonsu su kuma kalli daraja mara matuka ta Uban, suna haskakawa a fuskarsa, yayin da sue kallon kursiyinsa wanda daga har abada zuwa har abada ne, sun kuma san cewa mulkinsa ba zai kare ba, za su kuwa barke da wakar murna cewa: "Ya isa, Ya isa, Dan ragon da an kashe, Ya kuma fanshe mu zuwa ga Allah da jininsa mafi-daraja."

Asirin giciyen zai bayana dukan sauran asiri cikin hasken da ke kwararowa daga Kalfari za su zama da ban sha'awa gwanin kyau kuma. Jin kai da tausayi da kaunar iyaye za su hadu da tsarki da adalci da iko. Yayin da mu ke kalon martabar kursiyinsa, da daukakarsa za mu ga halinsa yadda Ya bayana shi da ban sha'awa, mu kuma gane ma'anar lakabin nan "Uban mu."

Za a ga cewa Shi wanda hikimarsa ba ta da iyaka, bai iya fito da wani shiri domin cetonmu ba, sai dai giciyewar Dansa. Diyyar hadayan nan ita ce murnar cika duniya da fansassun mutane masu-tsarki da murna, marasa mutuwa kuma. Sakamakon yakin Mai-ceton da ikokin duhu abin murna ce ga fansassu wadda ke kawo daukaka ga Allah har abada. Kuma hakanan ne tamanin rai har ma Uban Ya gamsu da farashin da aka biya; Kristi kansa kuma, sa'an da Ya kalli sakamakon babban hadayar tasa ya gamsu.

Babi na 41—Mayar da Duniya Kango

“Gama zunubanta sun kawo har sama, Allah kwa Ya tuna da muguntanta…. Chikin koko wanda ta dama, ku dama mata so biyu. Misalin da ta daukaka kanta duka, ta yi annishuwa kuma, daidai hakanan a ba ta azaba da kewa: gama chikin zuchiyatta tana chewa, Sarauniya ni ke zaune, ba gwamruwa ni ke ba, ba kwa zan ga kewa ba dadai. Domin wannan fa rana daya alobanta za su zo, mutuwa da kewa da yunwa; za a kone ta sarai da wuta; gama Ubangiji Allah Mai-tsarki ne wanda ya shar’anta mata. Sarakunan duniya kwa wadanda suka yi fasikanchi da ita, suka yi zaman annishuwa kuma tare da ita, za su yi kuka da kuwa bisanta,… suna cewa, kaito, kaito, babban birnin, Babila, birni mai-karfi! gama chikin sa’a daya hukumcinki za ya zo.” Ruya 18:5-10.

“Dillalan duniya kuma” da “suka wadata bisa ga ikon annishuwanta,” za su tsaya daga nesa domin tsoron azabatta, suna kuka suna bakinzuchiya, suna ta chewa, Kaito, kaito babban birni, ita wadda takan yafa da linen mai-labshi da shunaiya da mulufi,takan yi ado da zinariya da duwatsu masu tamani da lu’u lu’u gama chikin sa’a daya duniya mai-yawa haka ta lalache.” Ruya 18:11,3,15-17.

Irin hukumcin da za su fada ma Babila ke nan a ranar fushin Allah. Ita ta cika mudun zunubinta; lokacinta ya zo; ta isa hallakawa daidai.

Sa’an da muryan Allah zai juya bautar mutanensa, akwai falkaswa mai-ban tsoro ta wadanda suka yi hasarar komi cikin babban yakin nan na rai. Kafin a rufe gafara, rudin Shaitan ya makantar da su, suka ba da hujja domin halinsu na zunubi. Mawadata sun rika alfahari da fifikonsu kan matalauta, amma sun sami arzikinsu ta wurin ketare dokar Allah ne. Sun ki ciyar da mayunwata, suka ki suturta marasa sutura, su yi adalci su kuma so jin kai. Sun so su daukaka kansu su kuma sami ban girma daga sauran halitu, sai ga shi an raba su da duk ababan da suka yi takama da su, aka bar su a tsiyace ba tsaro kuma. Da razana suna kallo za a hallaka gumakan da suka girmama fiye da Mahalicinsu. Sun rigaya sun sayar da rayukansu domin wadata domin wadata da jin dadi na duniya, basu kuma bidi wadata game da Allah ba. Sakamakon shi ne cewa rayuwarsu ba ta da nasara; jin dadinsu ya zama da daci kamar matsarmama, dukiyarsu ta lalace. Cikin dakika daya za a share abin da suka tara duk tsawon rauwarsu. Mawadata za su yi bakincikin hallakar manyan gidajensu da watsarwar zinariyansu da azurfansu. Amma makokinsu zai tsaya domin tsoron cewa su kansu da gumakansu za su hallaka. Miyagu za su cika da nadama, ba domin rabuwarsu da Allah da yan’uwansu ‘yan Adam ba, amma domin Allah Ya yi nasara. Suna bakincikin yadda sakamakon ya kasance ne, amma ba za su tuba daga muguntarsu ba. Da akwai abin da za su iya yi don samun nasara da za su yi shi.

Duniya za ta ga cewa mutane da suka yi masu ba’a, suka rena su, suka kuma so su hallaka su, ga su suna wucewa cikin annoba da guguwa da rawan duniya, ba matsala. Shi wanda wuta ne mai-hallakaswa ga masu ketare dokarsa, rumfar tsaro ne ga mutanensa.

Mai-aikin bishara da ya sadakar da gaskiya domin ya sami karbuwar mutane, yanzu zai gane yanayi da tasirin koyaswoyinsa. A bayane yake cewa idon Allah yana bin shi a wurin aikinsa, a titi, yayin da yake ma'amala da mutane cikin fannoni dabam dabam na rayuwa. Kowane yanayi na rayuwarsa, kowane abin da aka rubuta, kowace kalma da aka furta, kowane abin da ya kai mutane ga amincewa da karya, yana shuka iri ne; yanzu kuma zai ga girbin wahalallun batattun rayukan da ke kewaye da shi ne.

In ji Ubangiji: "Sun warkar da chiwutar diyar mutanena bisa bisa kadai, sun che Lafiya, lafiya; ba kwa lafiya." "Tun da kun bata zuchiyar masu adilchi da karya, wadanda ni ban bata masu zuchiya ba; kun karfafa hannuwan mugu, da ba za shi juya ga barin muguntassa ba, shi tsira da ransa." Irmiya 8:11; Ezekiel 13:22.

"Kaiton makiyaya wadanda ke hallaka tumakin makiyayata…ga shi, zan jawo maku muguntar ayukanku, in ji Ubangiji." "Ku yi ihu, ku makiyaya, ku yi ta kuka; ku yi birgima chikin toka, ku shugabannan garke: gama lokachin kisanku ya yi sarai,… Makiyaya kuma za su rasa hanyar gudu, shugabannan garke kuma za su rasa hanyar tsira." Irmiya 233:1,2; 25:34,35.

Shugabannin addini da sauran mutane za su ga cewa basu rike dangantaka mai-dacewa da Allah ba. Za su ga cewa sun yi tawaye ga Mai-ba da dukan dokokin adalci. Kawar da umurnin Allah ya jawo babban mabulbulan mugunta da rashin jituwa da kiyayya da zunubi, har sai da duniya ta zama babban fili guda na tashin hankali da lalacewa. Abin da wadanda suka ki gaskiya suka kuma rungumi kuskure za su gani ke nan a wannan lokacin. Babu harshen da zai iya bayana irin sha'awan da marasa biyayya za su yi, na rai madawami da suka rasa har abada. Mutanen da duniya ta yi masu sujada sabo da baiwarsu da iya maganarsu, yanzu za su ga ainihin yanayin ababan nan. Za su gane abin da ta wurin zunubi suka rasa, za su kuma fadi a sawayen wadanda suka rena amincinsu, za su kuma furta cewa Allah Ya kaunace su.

Mutanen za su ga cewa an yaudare su. Za su zargi juna da cewa sun kai su ga hallaka; amma dukansu za su hada kai su jibga dukan zarginsu kan shugabannin addini. Pastoci marasa aminci sun yi annabcin ababa masu dadi, suka sa masu sauraronsu suka wofinta dokar Allah suka kuma tsananta ma masu son kiyaye ta da tsarki. Yanzu, cikin bakincikinsu, mallaman karyan nan za su furta a gaban duniya cewa sun rudi mutane. Taron jama'a za su cika da fushi. Za su ce: "Mun bata! Kuma ku ne sanadin hallakrmu," sa'an nan za su koma kan makiyayan karyan. Wadanda suka fi sha'awansu a da, za su furta la'ana mafi-muni a kansu. Hannuwan da suka taba manna masu lambobin girmamawa za a daga domin hallaka su. Za a yi anfani da makaman da aka so a hallaka mutanen Allah da su domin hallaka magabtansu yanzu. Ko ina akwai tashin hankali da zub da jini.

"Kara za ta kai har matukar duniya; gama Ubangiji yana shari'a da al'ummai, za ya kai dukan masu rai garin shari'a; don miyagu kwa, za ya bashe su ga takobi." Irmiya 25:31.

Har shekaru dubu shida babban jayayyar tana gudana; Dan Allah da ‘yan sakonsa na sama suna fada da ikon mugun, domin su fadakar, su mayar da kwana, su kuma ceci ‘ya’yan muatane. Yanzu kowa ya dauki matakinsa; miyagu sun hada kai da Shaitan gaba daya cikin yakinsa da Allah. Lokacin ya zo da Allah zai nuna ikon dokarsa da aka tattake. Yanzu jayayyar ba da Shaitan ne kadai ba, amma har da mutane ma. “Ubnagiji yana da jayayya da al’ummai;” “Za ya ba da wadanda ke miyagu ga takobi.”

Bayan an ba da shaidar cetaswa ga wadanda ke bakincikin dukan ban kyama da ake yi, yanzu malaikan mutuwa zai fita, wanda a wahayin Ezekiel aka misalta da mutanen da ke rike da makamai na yanka, wadanda aka ba su umurni cewa: “Ku karkashe sarai tsofo, da sarmayi da budurwa, kananan yara da mata; amma kada ku kusanto kowane mutum wanda shaida tana kansa; a sama kuma, a wuri mai-tsarki nawa.” Ezekiel 9:1-6.

Aikin hallakan zai fara cikin wadanda suka ce su ne masu kiwon ruhaniyar mutanen ne. Masu tsaro na karyan ne za su fara mutuwa. Ba wanda za a tausaya masa ko a kyale shi. Maza da mata da ‘yan mata da kananan yara duk za su hallaka.

“Ubangiji yana fitowa daga wurinsa domin shi yi ma mazamnan duniya hukumci sabada muguntassu: kasa kuma ta bude asirin jininta, ba kwa za ta kara rufe kisassunta ba.” Ishaya 26:21. “Amma aloba ke nan wadda Ubangiji za ya buga dukan al’ummai da ita, wadanda suka yi yaki da Urushalima; namansu za ya rube tun suna tsaye, idanunsu za su rube a chikin kwarinsu, harshensu kuma za shi rube a chikin bakinsu. Za ya zama kwa a chikin ranan nan, fargaba mai-yawa daga wurin Ubangiji za ta kama su; kowane dayansu kuma za ya kama hannun makwabcinsa, hannunsa kuma za ya shiga tasamma hannun makwabchinsa.” Zechariah 14:12,13. Cikin mahaukaciyar tarzumar fushinsu kansu, da kuma zubowar fushin Allah da ba a surka ba, miyagun mazamnan duniya: priestoci da shugabanni da mutane, mawadata da matalauta, manya da kanana za su mutu. “A ranan nan fa za a ga kisassun Ubangiji tun daga wannan iyakan duniya zuwa wannnan iyaka: ba za a yi makokinsu ba, ba za a tattara, ba kwa za a bizne su ba.” Irmiya 25:33.

Lokacin zuwan Kristi, za a shafe miyagu daga fuskar duniya, za ya cinye su da lumfashin bakinsa ya hallaka su kuma da hasken darajarsa. Kristi zai dauki mutanensa zuwa Birnin Allah, a dauke mazamnan duniya daga cikinta. “Duba, Ubangiji yana mai da duniya wofi, yana maishe ta kufai, yana kabantadda ita, yana matsadda mazamnanta.” “Kasa za ta wofinta sarai, ta bachi sarai: gama Ubangiji Ya fadi wannan magana.” “Sabada sun ketare dokokin sun sake farilla, suna ta da madawamin alkawali. Domin wannan la’ana ta cinye kasan, mazamna a chikinta kuma an iske su masu laifi ne: domin wannan mazamnan kasa sun kone.” Ishaya 24:1,3,5,6.

Dukan duniya ta zama kamar kangon jeji. Kufai na birane da kauyuka, wadanda rawan duniya ya hallaka, itatuwa da aka tumbuke, duwatsun da teku ya jefo, ko kuma aka yaga

daga kasa kanta, suna warwatse a fuskar kasa, yayin da manyan koguna suka zama alamun inda aka tumbuke duwatsun daga tushensu.

Yanzu al'amarin da hidimar karshe ta ranar kafara takan misalta zai faru. Sa'an da aka gama hidima a cikin wuri mafi-tsarki, aka kuma cire zunuban Israila daga haikalin ta wurin jinin hadaya ta zunubin, sa'an nan akan kawo bunsurun Azazel din da ransa gaban Ubangiji; a gaban taron jama'a kuma babban priest za "shi furta dukan muguntar 'ya'yan Isarila a bisansa, da dukan laifofinsu, watau zunubansu duka; za a sa su a bisa kan bunsurun." Leviticus 16:21. Hakanan kuma sa'an da aka kamala aikin kafara a haikalin sama, sa'an nan a gaban Allah da malaikun sama, da rundunan fansassun, za a aza zunuban mutanen Allah a kan Shaitan; za a kuma bayana cewa shi ne mai-laifin dukan muguntan da ya sa suka aikata. Kuma kamar yadda akan kori bunsurun Azazel din zuwa kasan da babu kowa a ciki, hakanan za a kori Shaitan zuwa kangon duniya inda ba kowa, jeji mara ban sha'awa."

Mai-ruyan ya yi annabcin korar Shaitan da yanayin rashin tsari da kango da duniya za ta kasance, ya kuma ce yanayin nan zai kasance har shekara dubu. Bayan ya bayana yadda zuwa Ubangiji na biyu da hallakar miyagu, annabcin ya ci gaba da cewa: "Na ga wani malaika kuma yana sabkowa daga sama, yana rike da makublin rami mara-matuka, yana kwa da babbar sarka a hanunsa. Sai ya damki dragon tsofon maciji, shi ne Ibelis da Shaitan, ya damre shi har zuwa shekara dubu, ya jefas da shi chikin rami mara-matuka, ya rufe bakin, ya sa masa hatimi a bakinsa, domin kada shi kara rudin al'ummmai, har shekara dubu suka chika: bayan wannan sai a kwanche shi domin kankanin lokachi." Ruya 20:1-3.

Batun cewa "rami mara —matuka" yana misalta duniya a yanayin ta na kango da duhu ne, a bayane yake cikin wadansu nassosi dabam. Game da yanayin duniya "a chikin farko," Littafin ya ce, "Kasa kwa sarari che wofi kuma; a kan fuskar zurfi kuma sai dufu." Farawa 1:2. Annabci yana koyar da cewa za a sake dawo da duniya wannan yanayin. Sa'an da ya hangi babban ranar Allah, annabi Irmiya y ace: "Na duba kasa, ga kufai, kango che: na duba sammai, ba su da haske, na duba duwatsu, ga su suna rawan jiki, dukan tuddai kuma suna makerketa. Na duba, ga shi, babu mutum; dukan tsuntsayen sama kuma sun tashi sun tafi. Na duba kuma, ga Karmel ta zama jeji, dukan biranen kuma sun rurrushe." Irmiya 4: 23-26.

Nan ne zai zama gidan Shaitan da miyagun malaikunsa har shekara dubu. Iyakar shi duniyan nan, ba zai iya zuwa wadansu duniyoyi ba har da zai jarabci wadanda basu taba faduwa ko kuma ya fitine su ba. Ta yadda za a daure shi kenan: babu sauran wadanda zai gwada ikon shi a kansu. An yanke shi gaba daya daga aikin rudi da hallaka da ya yi daruruwan shekaru yana jin dadin yi.

Annabi Ishaya da ya hangi lokacin da za a hambarar da Shaitan, ya ce: "Daga sama ga faduwarka, ya Lucifer, dan asubahi. Duba fa, aka datse ka har kasa, kai mai-kasadda

al'ummai! …Chikin zuchiyarka ka che, Har sama zan hau, zan daukaka kursiyi na bisa tamrarin Allah….in mai da kaina kamar Mai-iko duka. Amma dai har lahira za a gangaradda kai, har zuwa iyakar kurewar ramin. Wadanda suka ganka za su zuba maka ido, su yi bimbini a kanka, su che, Ko shi ne mutumin da ya sa duniya ta yi rawa, mai-girgiza mulkoki; wanda ya mayas da duniya kamar jeji, ya kabantadda biranenta; wanda ba yakan saki kamammunsa su koma gidansu ba?" Ishaya 14: 12-17.

Shekara dubu shida aikin tawayen Shaitan "ya sa duniya ta yi rawa." Ya "mayas da duniya kamar jeji, ya kabantadda biranenta;" kuma "ba yakan saki kamammunsa." Shekara dubu shida kurkukunsa yana tara mutanen Allah, kuma da ya rike su kamammu har abada, amma Kristi Ya yanke sarkokin, Ya saki fursunonin.

Ko miyagu ma za su kasance inda ikon Shaitan ba zai kai su ba, sa'an nan zai kasance daga shi sai miyagun malaikunsa domin su gane sakamakon la'anan da zunubi ya jawo. "Dukan sarakunan al'ummai, ai, dukansu, a chikin daraja su ke barchi, kowa chikin gidansa [kabari]. Amma kai an yas da kai chan bayan kushewar kamar reshe abin kyama,….Ba za ka tara zamanka da su chikin kabari ba, gama ka hallaka kasarka, ka kashe talakawanka." Ishaya 14:18-20.

Har shekara dubu, Shaitan zai yi ta yawon banza nan da can cikin kangon duniya domin ya ga sakamakon tawayen sa ga dokar Allah. A wannan lokacin wahalolinsa za su yi tsanani. Tun faduwarsa, rayuwarsa ta aiki ba tsayawa ta hana shi yin bimbini; amma yanzu za a hana shi ikonsa a kuma bar shi ya yi bimbini game da aikin da shi ya yi tun da ya yi tawayensa na farko ga gwamnatin Allah, ya kuma hangi gaba da rawan jiki da razana zuwa ga lokacin da dole zai sha wahala sabo da dukan muguntan da ya yi, a kuma hore shi sabo da zunuban da ya sa aka yi.

Ga mutanen allah, daurin Shaitan zai kawo murna da farin ciki. In ji annabi: "Za ya zama kuma a chikin ranan nan da Ubangiji za ya hutadda kai daga bakinchiki naka, da wahalarka, da bauta mai-wuya wadda aka sa maka, sa'an nan za a mai da wannan habaichi bisa sarkin Babila [watau Shaitan kenan], ka che, Ga yanda mai-wulakanchi ya kare!... Ubangij iYa karya sandar miyagu, kandirin masu-mulki; shi wanda ya dinga bugun dangogi chikin fushi, ya mallaki al'ummai da fushi, da tsanani wanda ba mai-hanawa." Aya 3-6.

Cikin shekaru dubu, tsakanin tashin matattu na fari da na biyu din, hukumcin miyagu za ya gudana. Manzo Bulus ya nuna cewa hukuncin nan zai biyo zuwan Kristi na biyu ne. "Kada ka shar'anta komi da garaje, kamin Ubangiji ya zo, wanda za ya tone boyayyun al'amura na dufu, ya bubbude shawarwarin zukata a sarari." Korinthiyawa I, 4:5. Daniel ya ce sa'anda Mai-zamanin da Ya zo, "aka ba da shari'a chikin hannuwan tsarkaka na Madaukaki." Daniel 7:22. A wannan lokacin, masu adalci za su yi mulki a matsayin sarakuna da priestoci ga Allah. Yohanna cikin Ruya ya ce: "Na ga kursiyin kuma, akwai

mazamna a bisansu kuma, aka ba da shari'a chikin hannunsu." "Za su zama priests na Allah da na Kristi, za su yi mulki kuma tare da shi shekara dubu." Ruya 20:4,6. A wannan lokacin ne kamar yadda Bulus ya ce, "trsarkaka za su yi ma duniya sahri'a." Korinthiyawa I, 6:2. Tare da Kristi, za su sahr'anta miyagu, suna gwada ayukansu da littafin dokokin, watau Littafi Mai-tsarki, suna hukumta kowane mutum bisa ga ayukan da aka yi cikin jiki. Sa'an nan za a bayana horon da za a ba miyagun, bisa ga gayukansu, sai a kuma rubuta shi daidai sunayensu a cikin littafin mutuwa.

Kristi da mutanensa za su kuma shar'anta Shaitan da miyagun malaikunsa. In ji Bulus: "Ba ku sani ba mu za mu yi ma malaiku shari'a?" Aya 3. Yahuda kuma ya bayana cewa: "Malaiku kuma wadanda basu rike matsayi nasu ba, amma suka rabu da nasu wurin zama, ya tsare su chikin madawaman sarkoki a chikin dufu zuwa hukumchin babban ranar." Yahuda 6.

A karshen shekara dubu din, tashi na biyu din zai gudana. Sa'an nan za a ta da miyagu daga matattu su bayana a gaban Allah domin aiwatar da rubutacen hukumcin. Ta hakanan, mai-ruyan, bayan ya bayana tashin matattu na masu adalci, ya ce: "Sauran matattu basu rayu ba sai shekara dubu din suka chika tukuna." Ruya 20:5. Ishaya kuma ya bayana, game da miyagu, cewa: "Za a tara su wuri daya kamar yadda ake tara 'yan sarka a rami, za a kuble su a chikin kurkuku, bayan kwana da yawa kuma za a ziyarche su da hukumchi." Ishaya 24:22.

Babi na 42—Karshen Jayayyar

A karhen shekara dubu din, Kristi zai sake dawowa duniya. Zai zo tare da rundunan fansassun da malaiku masu rufa masa baya. Yayin da yake saukowa da martaba mai-ban tsoro zai bukaci matattun miyagu su taso su karbi hallakarsu. Za su taso, babban runduna da ba mai-kirgawa, kamar yashin teku. Sun bambanta sosai da wadanda aka ta da su a tashin farko! An suturta masu- adalci da kuruciya, da kyau, mara mutuwa. Miyagu suna da burbushin ciwo da mutuwa.

Kowane ido a wancan taron jama'an zai juye domin ya kalli darajar Dan Allah. Da murya daya rundunar miyagun za su ce: "Mai-albarka ne shi wanda yake zuwa chikin sunan Ubangiji!" Ba don suna kaunar Yesu ne za su yi wanan furcin ba. Karfin gaskiya ne zai tilasta kalmomin su fito daga lebunansu. Yadda miyagun suka shiga kabarbarunsu, hakanan ne kuma za su fito da kiyayya ga Kristi da kuma ruhun nan nasu na tawaye. Ba za su sami wata damar gyarta kurakuran halayensu na rayuwarsu ta da ba. Damar ba za ta anfane su ba. Rayuwar ketare doka ba ta sake zukatansu ba. Da za a ba su wani zarafi kuma, da za su yi anfani da shi yadda suka yi anfani da na farin ne, wajen kauce ma umurnin Allah da ta tayar da tawaye gare Shi.

Kristi za ya sauko a kan Dutsen Zaitun ne, inda, bayan tashin Sa daga matattu, Ya hau, kuma inda malaiku suka maimaita alkawalin nan na dawowansa. Annabin ya ce: "Ubangiji Allahna, kuma za ya zo tare da dukan tsarkakansa." "A chikin wannan rana kwa sawunsa za su tsaya a bisa Dutsen Zaitun, wanda ke fuskanta Urushalima wajen gabas, Dutsen Zaitun kwa za ya rabu a tsaka,… da kwari mai-girma kuma a tsakani." "Ubangiji za ya zama sarki bisa dukan duniya; a chikin wannan rana Ubangiji daya ne, sunansa kuma daya ne." Zechariah 14:5, 4, 9. Sa'an da Sabuwar Urushalima ta fito daga cikin sama, da ban sha'awan ta, za ta sauka a wurin da aka tsarkake, aka kuma shirya dominta ne, kuma Kristi, tare da mutanensa da malaikun, zai shiga Birni Mai-tsarkin.

Yanzu Shaitan zai shirya babban yaki na karshe don neman daukaka. Sa'an da aka kwace ikonsa aka kuma yanke shi daga aikin sa na rudi, sarkin muguntan zai yi bakinciki, ya kuma damu; amma sa'an da aka ta da matattun miyagu, idan ya ga taron jama'a da ke gefensa, begen shi zai farfado, kuma zai yi himman cewa ba zai bar babban jayayyan ba. Zai tattara dukan mayakan batattu kalkashin tutarsa, ta wurin su kuma zai yi kokaarin aiwatar da shirye shiryensa. Miyagu kamammun Shaitan ne. Ta wurin kin Kristi, sun karbi shugabancin shugaban tawayen ke nan. Suna shirye su karbi shawrwarinsa, su yi abin da ya umurce su. Duk da haka bai yarda cewa shi ne Shaitan ba, sabo da rinto kawai. Yana ikirarin cewa shi ne sarki, ainihin mai-duniyar, wanda kuma aka kwace masa gadonsa ba bisa ga doka ba. Yana nuna kansa ga talakawansa rudaddu cewa shi mai-fansa ne, yana tabbatar masu cewa ikon shi ya fito da su daga kabarbaru, kuma ba da jimawa ba, zai kubutar da su daga zalunci mafi-muni. Da shike Kristi ba ya wurin, Shaitan zai aikata

al’ajibai don tabbatar da maganarsa. Zai karfafa kamamu, ya kuma motsa kowa da ruhunsa da karfin sa kuma. Zai yi masu tayin shugabantarsu zuwa ga yaki da tsarkaka don karban mallakar Birnin Allah kuma. Da murnar mugunta zai ja hankula zuwa ga miliyoyin nan da aka tayar daga matattu ya ce a matsayin shi na shugaban su shi zai hambarar da mulkin ya kuma sake karban kursiyansa da mulkinsa.

Cikin babban taron nan akwai tulin mutane da suka kasance kafin ruwan tufana; mutane masu girman jiki da tunani mai-kyau ainun, wadanda suka yarda da bishewar fadaddun malaiku, suka ba da dukan kwarewarsu da saninsu ga daukaka kansu; mutanen da al’ajiban aikin hannuwansu suka sa duniya ta mai da gwanintar tasu gumaka, amma kuma muguntarsu da miyagun kage kagensu sun kazantar da duniya suka kuma bata surar Allah, wanda ya sa Shi Ya shafe su daga fuskar halitta. Cikinsu akwai sarakuna da janar janar da suka yi nasara da al’aummai, jarumawa da basu taba kasa cin yaki ba, mayaka masu alfahari da buri, wadanda zuwansu kawai yakan sa al’aummai su yi rawan jiki. Sa’an da suka mutu kuma ai basu sake hali ba. Sa’an da suka fito daga kabari, za su ci aba da irin tunaninsu daidai inda suka tsaya. Za su ci gaba da son yakin da ya mallaki zukatansu lokacin da suka mutu.

Shaitan zai yi shawara da malaikunsa, sa’an nan sarakunan nan da jarumawa da mayakan nan za su dubi karfinsu da yawansu, sai su ce wai mayakan da ke cikin birnin ba su da yawa kamarsu, kuma za a iya yin nasar abisan su. Za su tsara shirye shiryensu na kwace wadata da darajar Sabuwar Urushalima. Nan take dukansu za su fara shiri domin yaki. Gwanayen masu aikin hannu za su kera makamai. Shahararrun shugabannin soja za su shirya kungiyoyin mayaka su karkasa su kamfani kamfani, sashi sashi.

Daga karshe za a ba da umurni cewa a fara yakin, rundunan nan da ba mai-kirgawa kuma za ta taso, mayaka irin da ba a taba hadawa ba a duniya, kuma taron dakarun dukan sararaki tun da aka fara yaki a duniya ba za su kai yawan wannan rundunan ba. Shaitan shugaban mayaka zai shugabance su, malaikunsa kuma za su hada dakarunsu domin fadan nan na karshe. Akwai sarakuna da mayaka cikin rundunarsa, sauran jama’a kuma za su bi bisa ga kamfanoninsu, kowane dayansu kalkashin shugabansu. Bisa tsari za su ci gaba, suna ketare kwari da tudu zuwa Birnin Allah. Bisa umurnin Yesu, za a rufe kofofin Sabuwar Urushalima, mayakan Shaitan kuma za su kewaye birnin su shirya kai hari.

Yanzu kuma Kristi zai bayana ga magabtansa. Can bisa birnin, a kan harsashe na zinariya, akwai kursiyi a sama da aka daga. A kan kursiyin nan Dan Allah yana zaune, kuma kewaye da Shi talakawan mulkinsa ne. Ikon Krisiti da martabansa, babu harshen da zai iya bayanawa, ba alkalami da zai iya kwatantawa. Darajar Uba Madawami za ta kewaye Dansa. Hasken kasancewarsa zai cika Birnin Allah ya kwarara, ya wuce kofofin, ya cika dukan duniya da walkiyarsa.

Mafi-kusa da kursiyin akwai wadanda a da suka yi himma cikin aikin Shaitan, amma, kamar itace daga cikin wuta, aka fizge su, suka kuma bi Mai-cetonsu da dukufa sosai. Biye da su akwai wadanda suka kasance da halayen Kirista, inda karya da rashin aminci suka dawama, wadanda suka girmama dokar Allah lokacin da Kiristan duniya suka rika cewa dokan nan wofi ne, da kuma miliyoyi na dukan sararaki da aka kashe sabo da imaninsu. Bayan wannan akwai "taro mai-girma wanda ba mai-kirgawa, daga chikin kowane iri da dukan kabilu, da al'ummai da harsuna,…gaban kursiyin da gaban Dan ragon, suna yafe da fararen riguna, da ganyayen dabino chikin hannuwansu." Ruya 7:9. Yakinsu ya kare, sun yi nasara. Sun yi tseren, sun kai wurin ladar. Ganyen dabinon da ke hannuwansu alama ce ta nasararsu, farar rigar kuma shaidaar adalci mara-aibi na Kristi wanda yanzu nasu ne.

Fansassun za su ta da wakar yabo da za ta dinga amsa kuwa ko ina a sama, suna cewa: "Cheto ga Allahnmu wanda Ya zamna bisa kursiyin, da Dan ragon kuma." Aya 10. Malaiku kuma za su hada muryoyinsu cikin yabo. Kamar yadda fansassu suka ga ikon Shaitan da muguntarsa, haka za su ga cewa ba wani ikon da ya isa ya ba su nasaran nan sai dai ikon Kristi. Cikin dukan rundunan nan mai-haskakawa, ba wanda ke gani Kaman da ikon kan shi ne ya yi nasara. Ba wanda ke maganar abin da suka yi ko wahalar da suka sha, amma kan maganar kowace waka ita ce ceto ga Allahnmu da Dan ragon kuma.

A gaban taron mazamnan duniya da sama za a yi nadin sarauta na karshe na Dan Allah. yanzu kuma yafe da martaba da iko fiye da na kowa, Sarkin sarakunan zai fadi hukumci kan masu tawaye ga gwamnatinsa, ya kuma zartas da adalci kan wadanda suka ketare dokarsa suka kuma wulakanta mutanensa. In ji annabin Allah: " Na ga kuma babban farin kursiyi da wanda ke zamne a bisansa, wanda duniya da sama suka guje ma fuskatasa; ba a kwa sami masu wuri ba. Na ga matattu kuma kanana da manya, suna tsaye a gaban kursiyin; aka bude littattafai: aka bude wani litafi kuma,litafin rai ke nan; aka yi ma matattu shari'a kuma bisa ga abin da aka rubuta chikin litatafai, gwalgwadon ayukansu." Ruya 20:11,12.

Da zaran an bude littattafan, idon Yesu kuma ya dubi miyagu, za su tuna kowane zunubi da suka taba yi. Za su ga daidai inda suka kauce daga hanyar tsabta da tsarki, nisan inda girman kai da tawaye suka kai su cikin ketarewar dokar Allah. Jarabobin da suka karfafa ta wurin aikata zunubi, albarkun da suka kawar, yan sakon Allah da aka rena, fadaka da aka ki ji, jiye jiyen kai da aka ki tawurin zukatan taurin kai da rashin tuba — duka za su bayana kamar an rubuta da harufofin wuta.

A bisa kursiyin, za a ga giciyen, kuma kamar majigi za a nuna jarabawa da faduwar Adamu da matakai bi da bi na babban shirin fansa. Haifuwar Mi-ceton, rayuwarsa ta saukin kai da biyayya, baptismarsa a Urdun, azuminsa da jarabawarsa a jeji, aikinsa cikin jama'a inda ya bayana ma mutane albarkun sama mafi muhimmanci; ayukansa na kauna da jinkai, daren da yakan kwana addu'a da tsaro shi kadai a kan duwatsu; shirye shiryen masu-kishi, da mugunta da kiyayya don ayukansa na nagarta, wahalarsa mai-tsanani a Gethsemani sabo

da zunuban duniya duka, bashewar shi a hannun masu-kisa, ababan ban tsoro na daren nan mai-ban-kyama, ga Shi fursuna mara-gardama, wanda almajiransa kaunatattu suka yashe Shi, da rashin ladabi aka bi da Shi titunan Urushalima, Dan Allah da aka kai Shi gaban Annas, aka gurbanar da Shi a fadar babban priest, a zauren shari'ar Bilatus, gaban matsoracin azalumin nan Hirudus, aka yi masa ba'a, aka zage Shi, aka zalunce Shi, sa'an nan aka yanka masa hukumcin kisa, za a nuna dukan wadannan.

Yanzu kuma za a bayana ma taron jama'ar ababan da suka faru a karshe: Mai-shan wahalan a hanyarsa zuwa Kalfari; Sarkin sama a rataye kan giciyen; priestoci masu-girman kai da jama'a masu ba'a game da wahalarsa; duhun nan na musamman; duniya mai-lumfashi, fansassu na duwatsu, budaddun kabarbaru da suke nuna lokacin da Mai-fansa Ya ba da ransa.

Al'amarin zai bayyana, daidai yadda al'amura suka kasance da. Shaitan da malaikunsa da talakawansa ba su da iko su kau da ido daga hoton aikinsu. Kowa zai tuna fannin da shi ya aikata. Hirudus, wanda ya karkashe yaran Baitalahmi, domin shi hallaka Sarkin Israila; yar banzan nan Herodiya wadda jinin Yohanna mai-baptisma ke kanta; Bilatus kumaman nan; sojoji masu-gori; prirestoci da shugabanni da taron jama'an nan da suka yi ihu cewa; "Jininsa a kan mu da 'ya'yanmu!" - dukan su za su ga yawa laifinsu. A banza za su so su buya daga martabar fuskarsa da ta fi rana haske, yayin da fansassu za su jefa rawaninsu a sawayen Mi-ceton, suna cewa: "Ya mutu domi na!"

A cikin fansassun akwai manzanin Kristi: jarumi Bulus, Bitrus mai-himma, Yohanna kaunatace mai-kauna, da amintattun yan'uwansu, tare da su kuma akwai babban rundunar wadanda aka kasha sabo da imaninsu, yayin da a bayan ganuwar, tare da kowane abu mai-ban kyama, wadanda suka tsananta masu ne, suka kai su kurkuku, suka kashe su kuma. Akwai Nero, mugun nan azalumi, yana kallon murna da farincikin wadanda ya taba azabta masu ya kuma ji dadin ganin azabarsu. Uwarsa za ta kasance a wurin domin ta ga sakamakon aikinta; ta ga yadda halin mugunta da ta ba dan ta, da fushin da tasirinta da kwatancinta suka karfafa, sun haifar da laifukan da suka sa duniya ta ji tsoro.

Akwai prietoci da sauran ma'aikatan 'yan paparuma da suka rika cewa su jakadun Kristi ne, amma suka yi anfani da zalunci don mallakar lamirin mutanen Kristi din. Akwai paparuma dabam dabam masu-girman kai da suka daukaka kansu fiye da Allah, suka kuma dauka cewa za su iya canja dokar Madaukaki. Su ma akwai lissafin da za su bayar ga Allah da ba za su so bayarwa ba. A kuraren lokaci za su ga cewa Shi Masanin komi yana kishin dokarsa, kuma babu yadda zai kubutar da mai-laifi. Za su sani yanzu cewa Kristi yana hada burinsa da na mutanensa da ke wahala, za su kuma ji karfin maganarsa cewa: "Da shike kuka yi wannan ga guda daya a chikin wadannan mafiya-kankanta ni kuka yi ma." Matta 25:40.

Dukan miyagun duniya sun gurbana a gaban shari'ar Allah, da zargin cin amanar gwamnatin sama. Ba su da mai-kare su, ba su da hujja; za a kuma furta hukumcin mutuwa ta har abada a kansu.

Yanzu zai bayana ga kowa cewa hakin zunubi ba 'yancin kai da rai madawami ba ne, amma bauta ce, da hallaka da mutuwa. Miyagu za su ga abin da suka ki ta wurin rayuwarsu ta tawaye. Sun rena nauyin daraja lokacin da aka yi masu tayinta, amma yanzu suna sha'awar ta. Batace zai ce: "Da na mallaki dukan wannan, amma na zaba in nisantar da shi daga wuri na…. Na sauya salama da murna da girma, da rashin kirki da wahala." Kowa zai ga cewa hana shi shiga sama daidai ne. Ta wurin rayuwarsu, sun rigaya sun bayana cewa: "ba ma son wannan mutumin [Yesu] ya yi mulki bisanmu."

Kaman a mafalki, miyagu za su kalli nadin sarautar Dan Allah. A hannuwansa za su ga allunan dokar Allah, umurnin da suka rena, suka ketare. Za su shaida ihun mamaki da murna da sha'awa daga cetattun; kuma yayin da amon sautin ke mamaye jama'a da ke bayan katangar birnin, duka, da murya daya za su ce: "Ayukanka masu girma ne, masu-ban al'ajibi, ya Ubangiji Allah Mai-iko duka; halullukanka kuma masu-adilchi ne, masu-gaskiya kuma, ya sarkin zamanai."(Ruya 15:3); kuma za su yi rub da ciki, su yi sujada ga Sarkin rai.

Shaitan zai shanye, yayin da yake kallon martraba da darajar Kristi. Shi wanda da can malaika ne, zai tuna daga inda ya fadi. Malaika mai-walkiya, "dan asubahi," dubi yadda ya canja, ya lalace! Daga majalisa inda ake girmama shi, yanzu ba dama ya shiga wurin, har abada. Zai ga wani yanzu kusa da Uban, yana rufe darajansa. Ya rigaya ya ga rawanin da malaika mai-kwarjini ya sa a kan Kristi, ya kuma san cewa babban matsayin malaikan nan da na shi Shaitan ne.

Zai tuna gidansa na lokacin rashin laifi, ga tsabta da salama da gamsuwa da yake da su kafin ya fara gunaguni kan Allah, da kuma kishin Kristi. Zarginsa da tawayensa da rudinsa don samun goyon bayan malaiku, taurin kansa wajen kin tuba lokacin da Allah zai iya gafarta masa, dukan wadannan za su bayana a gabansa. Zai tuna aikinsa cikin mutane, da sakamakonsa: kiyayyar mutane, hallakar rayuka, tasowa da faduwar mulkoki, hambarar da sarauta, tashe tashen hankula bi da bi, sabani, da canje canje. Zai tuna kokarinsa na hamayya da aikin Kristi, da kara nutsar da dan Adam kullum. Zai ga cewa kulle kullensa basu iya hallaka wadanda suka dogara ga Yesu ba. Sa'anda Shaitan ya dubi mulkinsa, da sakamakon famarsa, zai ga faduwa ne da lalacewa kadai. Ya sa jama'a sun gaskata cewa Birnin Allah zai yi saukin kamawa; amma kuma ya san cewa wannan karya ce. Akai akai, cikin babban jayayyar, an yi nasara da shi, aka kuma tilasta shi ya yarda da hakan. Ya san iko da martabar Madaukakin sosai.

Manufar babban dan tawayen kullum shi ne ya ba da hujjar ayukansa, ya kuma nuna cewa gwamantin Allah ne ya jawo tawayen. Inda ya mai da dukan hankalinsa ke nan. Ya

yi aiki da saninsa, bisa tsari kuma, ya kuma yi nasara sosai inda ya sa tulin jama'a suka yarda da labarinsa game da babban jayayyan da an dade ana yi. Shekaru dubbai, wannan sarkin laifin yana mai da karya gaskiya. Amma lokaci ya yi yanzu a karshe dai da za a yi nasara bisa karyar, a kuma bayana tarihin Shaitan da halinsa. Cikin babban kokarin shi na karshe don hambarar da Kristi, ya hallaka mutanensa, ya kuma karbi mallakar Birnin Allah, an fallasa babban mai-rudin gaba daya. Wadanda suka hada kai da shi za su ga faduwar aikinsa gaba daya. Masu-bin Kristi da malaiku masu biyayya, za su ga dukan iyakar kulle kullen Shaitan game da gwamnatin Allah. Shi ne dukan duniya za ta yi kyamarsa.

Shaitan zai ga cewa tawayen shi ya sa bai cancanci shiga sama ba. Ya rigaya ya horar da kansa cikin yaki da Allah; tsabta, da salama da jituwar sama a gare shi za su zama azaba ne. Zarge zargensa game da jinkan Allah da adalcinsa sun kare yanzu. Renin da ya yi kokarin kawo ma Yahweh ya koma kansa dungum. Yanzu kuma Shaitan zai durkusa ya furta cewa hukumcinsa daidai ne.

"Wane ne za ya rasa jin tsoro, ya rasa daukaka sunanka, ya Ubangiji." Gama kai kadai Mai-tsarki ne; gama dukan al'ummai za su zo su yi sujada a gabanka; gama ayukanka masu-adlichi sun bayanu." Aya 4. Yanzu kowane batu na gaskiya da karya cikin dadaddiyar jayayyan nan an rigaya an bayana shi. Sakamakon tawaye, da kawar da dokokin Allah sun rigaya sun bayyanu a gaban dukan halitu masu-tunani. An bayana ma dukan halitta bambanci da ke tsakanin yanayin mulkin Shaitan da gwamnatin Allah. Aikace aikacen Shaitan kansa sun rigaya sun yanka masa hukumci. Hikimar Allah da adalcinsa da nagartaarsa sun tabbata a bayyane. Za a ga cewa dukan ma'amalansa cikin babban jayayyan nan Ya yi su domin anfanin mutanensa har abada da kuma anfanin dukan duniyoyin da ya halitta. "Dukan ayukanka za su albarkacheka ya Ubangiji; tsarkakanka kuma za su albarkacheka." Zabura 145:10. Tarihin zunubi zai tsaya har abada a matsayin shaida cewa kasncewar dokar Allah wajibi ne don farincikin dukan wadanda Ya halita. Da sanin dukan baatuttuwan babban jayayyar, dukan halita masu-biyayya da masu-tawaye, tare gaba daya za su ce: "Tafarkunka adalchi da gaskiya ne, Ya Sarkin tsarkaka."

A gaban dukan halita, an rigaya an bayana babban hadayan da Uban da Dan suka yi a madadin mutum lokacin da Kristi Ya dauki matsayin Shi, aka kuma daukaka Shi fiye da ikoki da kowace suna. Sabo da murnan da ke gabansa ne, cewa zai kai mutane da yawa ga daraja, shi ya sa ya jimre giciyen, ya kuma yi watsi da kunyar. Kuma ko da shike bakincikin da kunyar sun fi karfin ganewa, duk da haka, murnar da darajar sun fi. Zai dubi fansassu da aka sabunta cikin siffarsa, kowace zuciya dauke da cikakkiyar shaidar Allah, kowace fuska tana nuna kamanin Sarkinsu. Cikinsu zai ga sakamakon wahalar ruhunsa, zai kuma gamsu, sa'an nan cikin murya da ta kai dukan taron masu-adalci da na miyagu, zai ce: "Duba ga wadanda jini na ya sayo! Domin sun a sha wahala, dominsu na mutu, domin su kasance tare da ni har dukan sararaki har abada." Sa'an nan wakar yabo za ta hau daga wurin masu fararen tufafin nan kewaye da kursiyin, cewa: "Dan rago wanda an kashe mai-

isa ne shi karbi iko, da wadata, da hikima, da karfi, da daraja, da daukaka, da albarka." Ruya 5:12.

Ko da shike an matsa ma Shaitan ya amnice da adalcin Allah, ya kuma durkusa ma fifikon Kristi, halinsa ba zai sake ba. Ruhun tawaye, kamar babban ambaliyar ruwa, zai sake kwararowa. Cike da garaje, zai dauki kudurin cewa ba zai bar babban jayayyar ba. Lokaci ya zo domin fada na karshe da Sarkin sama. Zai ruga zuwa tsakiyar talakawan shi, ya yi kokarin motsa su da fushinsa, ya kuma ingiza su domin yaki nan take. Amma cikin miliyoyin nan da ya rude su zuwa cikin tawaye, ba wadanda yanzu za su yarda da mulkin shi. Ikon shi ya kare.Miyagun suna cike da kiyayya dayan da ke motsa Shaitan; amma za su ga cewa ba su da bege, ba za su iya yin nasara bisa Yahweh ba. Fushin su zai koma kan Shaitan da wakilansa cikin rudi, sa'an nan da fushin aljannu, za su juya kansu.

In ji Ubangiji Yahweh: "Tun da ka mai da zuciyarka sai ka che zuchiyar Allah; ni ma ga shi sai in jawo maka baki masu ban tsoro na al'ummai: za su zare takobinsu su yi yaki da jamalin hikimarka, su kazantadda haskenka. Za su gangaradda kai har ramin." "Na kwa hallaka ka, ya cherub, mai-rufewa, na raba ka da duwatsun wuta… na fyade ka, na mike ka a gaban sarakuna, su zuba maka ido…ka zama abin tsoro ba ka da sauran zama ba dadai." Ezekiel 28:6-8, 16-19.

"Gama dukan kayan mayaki chikin rigimar yaki, da tufafi mirginannu chikin jini, za su zama na konewa, abinchin wuta." "Gama Ubangiji yana fushi da dukan al'ummai, yana hasala da da duka rundunassu: ya hallaka su sarai, ya bashe su ga kisa." "Za ya zubo da tarkuna bisa masu mugunta; wuta da kibiritu da iska mai-kuna su ne za su zama rabon kokon su." Ishaya 9:5; 34:2; Zabura 11:6. Wuta za ta sauko kasa daga wurin Allah cikin sama. Duniya za ta tsage. Makaman da aka boye cikinsu za a fitar. Harsunan wuta masu konewa za su bullo daga kowane kogo. Duwatsu kansu suna konewa da wuta. Ranar ta zo da za ta kuna kamar tanderu. Rundunan za su narke da kuna mai-zafi, duniya kuma da ayukan da ke cikin ta za su kone. Malachi 4:1; Bitrus II, 3:10. Fuskar duniya za ta zama kamar narkakkiyar dunkule guda, ta zama koramar wuta. Lokacin hukunci ne da hallakawar marasa biyayya ga Allah- "ranar daukan pansa ta Ubangiji ke nan, shekara ta sakaiya che chikin mahawara ta Sihiyona." Ishaya 34:8.

Miyagu za su karbi ladansu a duniya. Misalaii 11:31. "Za su zama tattaka; ranan da ke zuwa kuma za ta kokone su, in ji Ubangiji mai-rudauna." Malachi 4:1. Za a hallaka wadansu, kamar faraf daya ma, yayin da wadansu za su sha wahala kwanaki da yawa. Za a hori kowa "gwalgwadon ayukansu" ne. Da shike an rigaya an juye ma Shaitan zunuban masu-adalchi a kansa, za a sa Shi ya sha wahala ba domin tawayen shi kadai ba, amma domin dukan zunuban da ya sa mutanen Allah suka yi. Horon shi zai zarce na wadanda ya rude su. Bayan dukan wadanda sun fadi sabo da rudinsa sun mutu, shi zai ci gaba da rayuwa yana shan wahala. Cikin wutar tsarkakewar a karshe za a hallaka miyagu, tushe da reshe.

Shaitan ne tushen, masu- bin shi ne ressan. An kamala dukan horon duka; an cika dukan sharuddan adalci, sama da kasa kuma da suke kallo, zasu shaida adalcin Yahweh.

Aikin hallakan Shaitan ya kare. Shekara dubu shida yana yin abin da ya ga dama, yana cika duniya da kaito, yana jawo bakinciki ko ina cikin dukan halitta. Dukan halitta ta yi kishi ta kuma fama da azaba. Yanzu za a tsirar da halitar Allah har abada daga kasancewar Shaitan da jarabobinsa. “Dukan duniya tana zamne a huche; fashe da rairawa suke yi.” Ishaya 14:7. Kuma ihun yabo da nasara zai tashi daga dukan halittta masu biyayya. “Murya ta babban taro,” “kamar muryar ruwaye masu yawa kuma, kamar muryar tsawa mai-karfi kuma, suka che, Halellujah: gama Ubangiji Allahnmu Mai-iko duka yana mulki.” Ruya 19:6.

Yayin da duniya ke kunshe cikin wutar hallaka, masu-adalci suna zaune cikin Birni Mai-tsarkin. Mutuwa ba ta da iko kan wadanda suke cikin masu tashin matattu na fari. Ko da shike Allah wuta mai-cinyewa ne ga miyagu, ga mutanensa kuwa, Shi rana ne da garkuwa kuma. Ruya 20:6.; Zabura 84:11.

“Na ga sabuwar sama da sabuwar duniya kuma: gama sama ta fari da duniya ta fari sun shude.” Ruya 21:1. Wutar da za ta cinye miyagu za ta tsarkake duniya. Za a share kowane burbushin la’anar. Babu wata lahira mai-konawa har abada da za ta dinga tuna ma fansassu wannan sakamakon na zunubi.

Abin tunawa daya ne kadai ya rage: Mai-fansar mu zai kasance da alamun giciyewarsa har abada. A bisa kansa da aka kuje, a gefensa, da hannuwansa, da sawayensa ne kadai akwai alamun mugun aikin da zunubi ya yi. “Shekinsa yana kama da haske; kalkali suna fita daga hannunsa; ikonsa kwa a rufe yake.” Habakuk 3:4. A gefen nan nasa da jinin da ke sasanta Allah da mutum ke fitowa ne darajar Mai-ceton take, can ne ikonsa ke rufe. Da shike Mai-girma ne, wanda zai yi ceto, ta wurin hadayar fansa, domin wannan yana da ikon da zai zartas da adalci kan wadanda suka rena jinkan Allah. Kuma alamun kaskancinsa su ne bangirmansa mafi-yawa; har abada raunukan Kalfari za su nuna yabonsa, su bayana ikonsa.

“Ke fa ya hasumiyar garke, tudun diyar Sihiyona, a gare ki za ya zo; I, mulkin zamanin da za ya zo.” Mikah 4:8. Lokacin da tsarkaka suka yi begensa da marmari, tun da takobin wutan nan ya hana Adamu da Hawa’u shiga Adnin, lokacin ya zo, lokacin “pansar abin mulki na Allah.” Afisawa 1:14. Duniyan da aka fara ba mutum, cewa mulikin shi ne, ta bashe shi cikin hannuwan Shaitan, kuma duk da dadewa da ta yi a hannun Shaitan, an rigaya an dawo da ita ta wurin shirin fansa. Dukan abin da ka rasa ta wurin zunubi, an mayar. “Gama hakanan Ubangiji Ya fadi… mai-sifanta duniya, mai-yinta kuma; shi wanda ya kafa ta, ya haliche ta ba wofi ba, ya kamanta ta domin wurin zama.” Ishaya 45:18. Ainihin shirin Allah don halitar duniya ya cika, da shike duniyar ta zama wurin zaman

fansassu har abada. “Masu-adilchi za su gaji kasan, su zamna a chikinta har abda.” Zabura 37:20.

Tsoron kada a sa abin gadon ya zama kamar ba na ruhaniya ba, ya sa mutane da yawa sun mai da abin gadon da muke gani namu ne ya zama na cikin ruhaniya kadai. Kristi Ya tabbatar ma almajiransa cewa Ya je domin Ya shirya masu wurin zama ne a gidan Uban. Wadanda sun karbi koyaswoyin maganar Allah ba za su jahilci zancen wurin zama na sama ba. Duk da haka, “ido ba ya gani ba, kunne ba ya ji ba, ba ya shiga zuchiyar mutum ba, dukan iyakar abin da Allah Ya shirya ma wadanda ke kamnassa.” Korinthiyawa I, 2:9. Harshen mutumtaka bai isa ya bayana ladan masu- adalci ba. Wadanda za su gan shi ne kadai za su san shi. Tunanin mutum ba zai iya fahimtar darajar Paradise na Allah ba.

A cikin Littafin, ana ce da gadon cetattu “kasa” ne. Ibraniyawa 11:14-16. A can Makiyayi na sama zai kai tumakinsa mabulbulan ruwayen rai. Itacen rai zai ba da yayansa kowane wata, ganyen itacen kuma domin warkarwar al’ummai ne. akwai rafuka da ruwansu yana gudu kullum, mai-haske sarai, a gefensu kuma itatuwa masu ganyaye suna jefa inuwarsu kan hanyoyi da aka shirya domin fansassu na Ubangiji. A can budaddun filayen sukan zama tuddai masu-kyau a wadansu wurare, duwatsun Allah kuma sukan nuna bisansu masu ban-sha’awa. A wadannan filayen salaman, a gefen rayayyun rafukan nan, mutanen Allah da suka dade suna bakunci, suna kai da kawowa, za su sami gidansu.

“Mutane na za su zamna a chikin mazamni na salama, a chikin tabbatattun mazamnai, da chikin mazamnai na hutawa.” “Ba za a kara jin labarin kwache a kasarki ba, ko kisbewa, ko hallaka a chikin iyakanki: amma za ki kira ganuwarki cheto, kofofinki kuma yabo.” “Za su gina gidaje, kuma za su zamna a chiki, su yi gonakin annab kuma, su chi anfaninsu. Ba za su yi gini wani ya zamna ba: ba za su dasa, wani ya chi ba;… zababuna kuma za su dade suna jin dadin aikin hannuwansu.” Ishaya 32:15; 60:18; 65:21,22.

A can, “Jeji da kekadadiyar kasa za su yi farinchiki; hamada kuma za ta yi murna ta yi fure kamar rose.” “Maimakon kaya, itachen fir za ta tsiro; maimakon dakwara kuma myrtle za ya tsiro.” “Kerkechi za ya zamna tare da dan rago, damisa kuma za ta kwanta tare da dan akuya;… dan yaro kwa za ya bishe su.” “Ba za su yi chiwutaswa ba; ba kwa za su yi barna ko ina chikin dutsena mai-tsarki ba,” in ji Ubangiji. Ishaya 35:1; 55:13; 11:6,9.

Azaba ba za ta iya kasancewa a yanayin sama ba. Ba za a sake samun hawaye ko biso, ko makoki ba. “Mutuwa kwa ba za ta kara kasanchewa ba; ba kwa za a kara yin bakin-zuchiya, ko kuka, ko azaba: al’amura na fari sun shude.” “Wanda yake zaune a chiki ba zai che, Ina chiwo ba: mutanen da ke zaune a wurin za a gafarta masu zunubansu.” Ruya 21:4; Ishaya 33:24.

Akwai Sabuwar Urushalima, babban birnin sabuwaar duniyar da aka darajanta, “kambi jamali a chikin hannun Ubangiji, dajiyar sarauta kuma a chikin hannun Allahnki.” “Shekinta yana kama da dutse mai-tamani mafifici, sai ka che jasper, garai kamar crystal.”

“Al’aummai kuma za su yi yawo chikin haskenta; sarakunan duniya kuma suna kawo darajassu chikinta.” In ji Ubangiji: “Zan yi farin chiki domin Urushalima kuma, in yi murna domin mutanena.” “Mazamnin Allah yana wurin mutane, za ya zamna tare da su kuma, za su zama al’umma nasa, Allah kuma da kansa za ya zamna tare da su, ya zama Allahnsu.” Ishaya 62:3; Ruya 21:11,24; Ishaya 65:19; Ruya 21:3.

A birnin Allah babu dare. Ba wanda zai bukaci hutawa. Ba za a gaji da aikata nufin Allah da raira yabon sunansa ba. Kullum za mu rika jin sabontakar safiya ne, kullum kuma mu kasance nesa da karewar safiyar. “Ba su kwa da bukatar hasken fitilla, ko hasken rana ba; gama Ubangiji Allah za ya ba su haske.” Ruya 22:5. Wata walkiya mara-dauke ido za ta rufe hasken rana, haskenta kuwa zai fi na tsakar rana. Darajan Allah da na Dan ragon za su yi ma Birni Mai-tsarkin ambaliyar haske mara-shudewa. Fansassu za su rika tafiya cikin darajar yini mara matuka inda ba rana.

“Ban ga haikali a chiki ba: gama Ubangiji Allah Mai-iko duka da Dan rago su ne haikalinta.” Ruya 21:22. Mutanen Allah za su sami zarafin sadarwa da Uban da Dan. “Gama yanzu chikin madubi mu ke gani a zauranche.” Korinthiyawa I, 13:12. Muna ganin kamanin Allah da ke nunawa sai ka ce a madubi, cikin ayukan halita da dangantakarta da mutane, amma sa’an nan za mu gan shi fuska da fuska ba tare da wani labule a tsakani ba. Za mu tsaya a gabansa, mu ga daarajar fuskarsa.

Can fansassu za su sani kamar yadda su ma za a san su. Can ne kauna da tausayi da Allah da kan Shi ya shuka cikin mutm za su sami ainihi da mafi-dadin bayanuwarsu. Sadarwa mai-tsabta da rayuka masu-tsarki, rayuwar ma’amala mara sabani da malaiku masu —albarka da kuma amintattu na dukan sararaki wadanda suka wanke tufafinsu, suka mai da su fari cikin jinin Dan ragon, dangantaka na ruhaniya da suka hada “kowane iyali chikin sama da duniya” Afisawa 3:15 — wadannan duka za su taimaka wajen hada farincikin fansassun.

Can, zukata marasa mutuwa, masu murna kuma, za su yi bimbini game da al’ajiban ikon halita, da asiran kauna ta fansa. Ba za a iske mugun magabci mai-rudi da zai jarabci wani ya manta Allah ba. Kowane sani zai zama ingantace, kowace kwarewa za ta karu. Samun sani ba zai gajiyar da tunani ba, ko kuma ya kare kuzari ba. Can za a gudanar da al’amura mafi-girma, a cim ma manufofi mafiya-kyau, a cika buri mafi girma: duk da haka sabobin ababa za su taso da za a so a yi su, sabobin al’ajibai kuma da za a yi sha’awarsu, sabobin gaskiya da za a fahimta, sabobin manufofi da za su ingiza zuciya da ruhu da jiki.

Dukan halita ko ina za su kasance domin fansassu su yi nazarinsu. Da shike mutuwa ba za ta yi masu takunkumi ba, za su rika firiya babu gajiya zuwa duniyoyi nesa, duniyoyin da suka yi bakincikin wahalolin dan Adam, suka kuma ta da wakokin murna game da labarin rai da aka fansa. Da murnan da ba za a iya bayanawa ba, ‘ya’yan duniya za su shiga cikin murna da hikimar masu rai da basu fadi ba. Za su raba dukiyar sani da ganewa da

suka samu cikin zamanai bisa zamanai da suka yi suna bimbinin aikin hannun Allah. Da gani garai za su kalli darajar halita — rana da taurari, dukansu bisa ga matsayinsu, suna kewaye kursiyin Allah. Bisa kowane abu, daga mafi kankanta zuwa mafi girma, an rubuta sunan Mahalici a kai, kuma cikin dukansu an bayana wadatar ikonsa.

Kuma shekaru mara-matuka, yayin da suke wucewa, za su kawo ganewa mafi wadata da daraja game da Allah da Kristi. Kamar yadda sani ke karuwa, haka kauna da ban girma da farin ciki za su karu. Yawan sha'awar halin Allah zai zama daidai da yawan saninsa da mutane suka yi ne. Sa'an da Yesu zai bude masu wadatar fansa da muhimman nasarori cikin babban jayayya da Shaitan, zukatan fansassu za su motsu da Karin kuzari da himma, kuma da karin murna mai-yawa za su kada girayan zinariya, su hada kai, su kara babban wakar yabon.

"Kuma kowane halitacen abu wanda ke chikin sama, da bisa duniya, da kalkashin duniya, da bisa teku, da dukan abin da ke chikinsu, na ji su suna chewa, Ga wanda yake zamne bisa kursiyin, ga Dan rago kuma, albarka, da daraja, da daukaka, da mulki, har zuwa zamanun zamanai." Ruya 5:13.

Babban jayayyar ta kare. Zunubi da masu-zunubi babu su kuma. Dukan halitta tana da tsabta. Jituwa da murna daya ke cikin dukan halita. Daga wurin Shi wanda Ya halici duka, rai da haske da murna ke fitowa zuwa ko ina cikin sarari mara-iyaka. Daga kwayar halita mafi-kankanta zuwa duniya mafi-girma, dukan ababa, masu rai da marasa rai, cikin kyaunsu mara —duhu da murnarsu cikakkiya, suna cewa, Allah kauna ne.

Ana jiran karshen komai